BISHARA TA HANNUN

MATIYU

Gabatarwa

Marubucin wannan bishara shi ne Matiyu, shi Bayahude ne, daya daga cikin almajiran Yesu.

Bishara ta Hannun Matiyu ta nuna cewa Yesu shi ne Almasihun nan da aka yi alkawarinsa a cikin Tsohon Alkawari, wanda kuma Yahudawa suka sa zuciya cewa zai zo. Sau da yawa *Bishara ta Hannun Matiyu* ta maimaita ayoyin annabci daga cikin Tsohon Alkawari don ta nuna yadda Yesu ya cika su. Ta kuma nuna cewa Yesu mutumin zuriyar Ibrahim ne (1.1). Sau da yawa kuma ta ce da Yesu "Dan Dawuda". Wato, Yesu ya zo a matsayin Almasihu ke nan, daidai yadda Yahudawa da kansu suka ba da gaskiya. Amma ko da yake bisharar ta sami karɓuwa sosai ga Yahudawa, duk da haka ta ba da tabbaci cewa bisharar Yesu Almasihu saboda mutanen duniya duka ne, wato, Yahudawa da waɗanda ba Yahudawa ba. *Bishara ta Hannun Matiyu* ta nuna a fili cewa Yesu wani babban malami ne wanda koyarwarsa da maganarsa sun tabbatar cewa yana da iko sosai, har ma fiye da Musa.

An tsara *Bishara ta Hannun Matiyu* da kyau, an tsara koyarwar Yesu a manyan sashe-sashe guda biyar. Da farko akwai koyarwar Yesu a kan dutse, wadda ta bayyana yadda ya yi daidai 'ya'yan Allah su yi rayuwarsu (sura 5-7). Kuma akwai koyarwa game da yadda manzon Almasihu zai yi aikinsa (sura 10). Sa'an nan akwai misalai dabam-dabam a kan mulkin Allah (sura 13). Na huɗu kuma akwai koyarwa a kan irin halayen da mai bi ya kamata ya kasance da su (sura 18). A ƙarshe kuwa akwai koyarwa a kan zamanin ƙarshe da kuma abubuwan da za su faru a wannan lokaci (sura 24-25).

Abubuwan da Suke Ciki

Asalin Yesu da haihuwarsa 1.1—2.23
Wa'azin Yohanna Maibaftisma 3.1-12
Baftismar Yesu da gwadawarsa 3.13—4.11
Ayyukan Yesu a ƙasar Galili 4.12—18.35
Dawowar Yesu daga Galili zuwa Urushalima 19.1—20.34
Aikin Yesu na ƙarshe a Urushalima 21.1—27.31
Gicciyen Yesu da mutuwarsa 27.32-66
Tashin Yesu da bayyanuwarsa 28.1-20

Zuriyar Yesu Almasihu
(Luk 3.23-38)

1 [1] Littafin asalin Yesu Almasihu,[a] ɗan Dawuda wanda shi ma
ɗan Ibrahim ne.
2 Ibrahim ya haifi Ishaku, Ishaku ya haifi Yakubu, Yakubu ya
haifi Yahuda da 'yan'uwansa. [3] Yahuda kuwa ya haifi Feresa da
Zera, uwarsu Tamar. Feresa ya haifi Hesruna, Hesruna ya haifi
Aram, [4] Aram ya haifi Amminadab, Amminadab ya haifi Nashon,
Nashon ya haifi Salmon. [5] Salmon ya haifi Bo'aza, uwarsa Rahab,
Bo'aza ya haifi Obida, uwarsa Rut, Obida ya haifi Jesse. [6] Jesse
ya haifi sarki Dawuda.
Dawuda ya haifi Solomon wanda uwarsa dā matar Uriya ce.
[7] Solomon ya haifi Rehobowam, Rehobowam ya haifi Abija,
Abija ya haifi Asa, [8] Asa ya haifi Jehoshafat, Jehoshafat ya haifi
Yoram, Yoram ya haifi Azariya. [9] Azariya ya haifi Jotam, Jotam
ya haifi Ahaz, Ahaz ya haifi Hezekiya, [10] Hezekiya ya haifi
Manasse, Manasse ya haifi Aman, Aman ya haifi Josiya. [11] Josiya
ya haifi Jekoniya da 'yan'uwansa, wato a lokacin da aka kwashe
su zuwa bauta a ƙasar Babila.
12 Bayan da aka kai su Babila, sai Jekoniya ya haifi
Sheyaltiyel, Sheyaltiyel ya haifi Zarubabel, [13] Zarubabel ya haifi
Abihudu, Abihudu ya haifi Eliyakim, Eliyakim ya haifi Azuro.
[14] Azuro ya haifi Zadok, Zadok ya haifi Akim, Akim ya haifi
Aliyudu, [15] Aliyudu ya haifi Eliyaza, Eliyaza ya haifi Matana,
Matana kuwa ya haifi Yakubu. [16] Yakubu ya haifi Yusufu mijin
Maryamu wadda ta haifi Yesu wanda ake ce da shi Almasihu.
17 Wato dukan zuriyar daga kan Ibrahim zuwa Dawuda,
zuriya goma sha huɗu ce. Daga kan Dawuda zuwa lokacin da
an kwashe Isra'ilawa zuwa bauta a Babila, zuriya goma sha
huɗu ce, daga nan kuma zuwa kan Almasihu, zuriya goma sha
huɗu ce.

Haihuwar Yesu Almasihu
(Luk 2.1-7)

18 Ga yadda aka haifi Yesu Almasihu. Lokacin da Yusufu
yake neman Maryamu uwar Yesu da aure, tun ba a ɗaura musu
aure ba, sai ya zama tana da ciki daga Ruhu Mai Tsarki.
[19] Saurayinta Yusufu yana da kirki, kuma ba ya so yă ba ta kunya

---

1.11: 2 Sar 24.14-15; 2 Tar 36.10; Irm 27.20 1.18: Luk 1.27

[a] 1.1 **Almasihu**: Da Ibraniyanci "Masiha"; da Helenanci "Kiristi". Ma'anar Almasihu ita ce wanda aka shafe, aka kuma keɓe.

a cikin mutane, sai ya yi tunani yă sake ta shiru a ɓoye. 20 Amma
yana cikin wannan tunani sai ga wani mala'ikan Ubangiji ya
bayyana gare shi a mafarki, ya ce masa, "Yusufu ɗan Dawuda,
kada ka ji tsoron ɗaukar Maryamu ta zama matarka domin cikin
nan nata daga Ruhu Mai Tsarki ne. 21 Za ta haifi ɗa, za ka sa
masa suna Yesu[b] domin shi ne zai ceci mutanensa daga
zunubansu."

22 Dukan wannan ya faru ne domin a cika abin da Ubangiji
ya faɗa ta bakin annabi cewa,

23 "Budurwa za ta yi ciki, ta haifi ɗa
za a kuma sa masa suna Immanuwel."

Ma'anar Immanuwel ita ce, "Allah yana tare da mu."

24 Da Yusufu ya farka daga barci, sai ya bi umarnin mala'ikan
Ubangiji, ya ɗauki Maryamu ta zama matarsa. 25 Amma bai san
ta ba, sai bayan da ta haifi ɗanta, ya kuma sa masa suna Yesu.

Ziyarar Masu Ilimi daga Gabas

2 1 An haifi Yesu a garin Baitalami cikin Yahudiya a zamanin
sarki Hirudus. Bayan an haife shi sai waɗansu masu ilimin
gane taurari daga gabas suka zo Urushalima, suka yi tambaya
suka ce, 2 "Ina sabon sarkin Yahudawa da aka haifa? Domin
mun ga tauraronsa a gabas, kuma mun zo ne mu yi masa
sujada."

3 Da sarki Hirudus ya ji haka, sai hankalinsa ya tashi, haka
kuma dukan mutanen Urushalima. 4 Sai ya tara dukan manyan
firistoci da malaman dokoki, ya tambaye su inda za a haifi
Almasihu.

5 Suka ce masa, "A garin Baitalami ne, cikin Yahudiya, gama
haka annabin ya rubuta cewa,

6 'Ke ma Baitalami ta ƙasar Yahuda,
ke ba ƙarama ba ce a cikin masu mulkin Yahuda.
Gama daga cikinki wani mai mulki zai fito,
Wanda zai shugabanci mutanena Isra'ila.' "

7 Sai Hirudus ya kira masu ilimin nan a ɓoye don yă san daidai
lokacin da suka ga tauraron. 8 Sai ya aike su zuwa Baitalami ya
ce, "Ku je ku bincika mini game da ɗan yaron nan a hankali.
Idan kun same shi, sai ku zo ku faɗa mini don ni ma in je in yi
masa sujada."

1.21: Luk 1.31 **1.23:** Ish 7.14 **1.25:** Luk 2.21 **2.6:** Mika 5.2

[b] **1.21 Yesu:** Sunan "Yesu" a Helenanci, shi ne "Joshuwa" a Ibraniyanci. Ma'anar sunan kuwa ita ce "Allah yana ceto."

9 Su kuwa da suka gama jin maganar sarki, sai suka yi
tafiyarsu. Tauraron da suka gani a gabas kuwa yana gabansu suna
binsa har ya zo ya tsaya a kan inda ɗan yaron yake. 10 Da suka
ga tauraron sai suka cika da murna sosai. 11 Da suka shiga gidan
kuwa sai suka ga ɗan yaron da mamarsa Maryamu, suka durƙusa
a gabansa, suka yi masa sujada. Sa'an nan suka kunce kayansu
suka ba shi kyautar zinariya, da lubban, da mur.
12 Suka koma ƙasarsu ta wata hanya dabam, gama Allah ya
ja musu kunne a mafarki kada su koma wurin Hirudus.

Yusufu da Maryamu Sun Gudu zuwa Masar

13 Bayan da suka tafi sai wani mala'ikan Ubangiji ya
bayyana wa Yusufu a mafarki, ya ce, "Tashi, ka ɗauki ɗan
yaron nan da mamarsa ku gudu zuwa ƙasar Masar. Ku zauna a
can sai na faɗa muku ku dawo, gama Hirudus zai nemi ɗan
yaron don ya kashe shi."
14 Yusufu kuwa ya tashi ya ɗauki ɗan yaron da mamarsa da
daddaren, ya tafi ƙasar Masar, 15 ya zauna a can har sai da Hirudus
ya mutu. Wannan kuwa ya faru domin a cika abin da Ubangiji
ya faɗa ne ta bakin annabin cewa. "Daga Masar na kirawo Ɗana."

An Kashe 'Yan Yara a Yahudiya

16 Da Hirudus ya gane cewa masu ilimin nan sun yi masa
wayo ne, sai ya yi fushi sosai. Ya aika a kakkashe dukan 'yan
yara maza da suke Baitalami da kewayenta, daga masu shekara
biyu zuwa ƙasa, gwargwadon lokacin da masu ilimin nan suka
faɗa masa game da yaron.
17 A lokacin ne aka cika abin da aka faɗa ta bakin annabi
Irmiya cewa,

18 "An ji murya a Rama,
kuka ta baƙin ciki mai zafi,
Rahila ce take kuka domin 'ya'yanta,
Ta ƙi a ba ta haƙuri don sun mutu."

Dawowa daga Masar zuwa Nazarat

19 Bayan mutuwar Hirudus, sai mala'ikan Ubangiji ya
bayyana wa Yusufu a cikin mafarki a Masar, ya ce, 20 "Tashi ka
ɗauki ɗan yaron nan da mamarsa ka koma ƙasar Isra'ila, gama
masu nema su kashe yaron sun mutu." 21 Sai ya tashi ya ɗauki
ɗan yaron da mamarsa ya tafi ƙasar Isra'ila.

2.15: Hos 11.1 **2.18:** Irm 31.15

22 Amma da ya ji yaron Hirudus, wato, Arkilayus ya ci gādon
babansa, yana mulkin Yahudiya, sai ya ji tsoro ya kai can. Amma
da aka ja masa kunne a mafarki, sai ya ratse zuwa yankin Galili.
23 Ya je ya zauna a wani gari da ake ce da shi Nazarat, domin a
cika abin da aka faɗa ta bakin annabawa cewa, "Za a ce da shi
Banazare."

Wa'azin Yohanna Maibaftisma
(Mar 1.1-8; Luk 3.1-18; Yoh 1.19-28)

3 1 A wannan lokacin ne Yohanna Maibaftisma ya fito yana
wa'azi a cikin dajin Yahudiya, 2 yana cewa, "Ku tuba, gama
mulkin sama[6] ya kusa!" 3 Wannan shi ne wanda annabi Ishaya
ya yi maganarsa, ya ce,

"Muryar mai kira a daji tana cewa,
'Ku shirya wa Ubangiji inda zai bi,
Ku miƙe hanyoyinsa!' "

4 Rigar da Yohanna ya sa kuwa an yi ta da gashin raƙumi ne.
Yana kuwa ɗaure da bel na fata. Abincinsa kuwa fara ce da ruwan
zuma. 5 Sai mutanen Urushalima da na Yahudiya duka, da na
dukan ƙasashen yankin Kogin Urdun, suka yi ta zuwa wurinsa,
6 suna faɗin zunubansu, yana yi musu baftisma[c] a Kogin Urdun.

7 Amma da Yohanna ya ga Farisiyawa da Sadukiyawa da
yawa suna zuwa domin a yi musu baftisma, sai ya ce musu,
"Ku macizai! Wa ya gargaɗe ku ku guje wa hukuncin nan na
Allah mai zuwa? 8 Ku yi ayyukan da za su nuna cewa kun tuba.
9 Kada kuwa ku yi taƙama a ranku cewa, 'Ibrahim ne babanmu',
gama ina faɗa muku Allah yana da ikon yi wa Ibrahim 'ya'ya
da duwatsun nan. 10 An riga an sa bakin gatari a gindin itace.
Duk itacen da bai ba da 'ya'ya masu kyau ba, sai a sare shi a
jefa a wuta."

11 Ni dai da ruwa nake yi muku baftisma, don nuna kun
tuba, amma wanda ya fi ni girma zai zo a bayana, wanda ko
takalmansa ma ban isa in riƙe ba. Shi ne zai yi muku baftisma
da Ruhu Mai Tsarki, da wuta kuma. 12 Yana riƙe da
matankaɗinsa, zai tankaɗe hatsinsa, kuma yă tattara alkamarsa
ya sa cikin rumbunsa, amma zai ƙona yayin a wutar da ba a
iya kashewa.

2.23: Mar 1.24; Luk 2.39; Yoh 1.45 **3.2:** Mat 4.17; Mar 1.15 **3.3:** Ish 40.3
3.4: 2 Sar 1.8 **3.7:** Mat 12.34; 23.33 **3.9:** Yoh 8.33 **3.10:** Mat 7.19

[6] **3.2 Mulkin sama:** Shi ne mulkin da Allah yake yi a kan mutane.

[c] **3.6 Baftisma:** Ita ce wanka ko nutsewar da take nuna tuba.

An Yi wa Yesu Baftisma
(Mar 1.9-11; Luk 3.21-22)

13 A lokacin nan ne Yesu ya zo daga Galili, ya je Kogin Urdun
wurin Yohanna domin a yi masa baftisma. 14 Yohanna ya so ya
hana shi, ya ce, "Ni, da nake bukata ka yi mini baftisma, yaya
za ka zo wurina?"
15 Amma Yesu ya amsa masa ya ce, "Bari yă zama haka
yanzu, domin haka ne ya yi kyau mu cika dukan abin da Allah
yake so." Sa'an nan Yohanna ya yarda masa.
16 Da aka yi wa Yesu baftisma, ya fito daga ruwan ke nan,
sai nan da nan sama ya buɗe, ya ga Ruhun Allah yana saukowa
da kamannin kurciya, har ya sauka a kansa. 17 Sai aka ji wata
murya daga sama ta ce, "Wannan shi ne Ɗana da nake ƙauna,
wanda nake jin daɗinsa ƙwarai."

Shaiɗan Ya Gwada Yesu
(Mar 1.12-13; Luk 4.1-13)

4 1 Sa'an nan Ruhu Mai Tsarki ya kai Yesu cikin daji domin
Shaiɗan yă gwada shi. 2 Yesu ya yi azumi kwana arba'in dare
da rana. Daga baya kuwa yunwa ta kama shi. 3 Sai Shaiɗan ya
zo ya ce masa, "Idan kai Ɗan Allah ne, ka umarci duwatsun nan
su zama burodi."
4 Yesu ya amsa ya ce, "An rubuta a cikin Maganar Allah
cewa,

'Ba da abinci kaɗai mutum zai rayu ba,
sai dai da kowace magana da take fitowa daga wurin
Allah.' "

5 Sai Shaiɗan ya kai shi Urushalima birni mai tsarki ya kai
shi can bisa haikali. 6 Ya ce masa, "Idan kai Ɗan Allah ne, ka yi
tsalle ka fāɗi ƙasa, don a rubuce yake cewa,

'Zai ba da umarni ga mala'ikunsa su tsare ka.
Za su tare ka da hannayensu
don kada ka buga ƙafafunka a dutse.' "

7 Sai Yesu ya ce masa, "A rubuce yake kuma cewa, 'Kada ka
gwada Ubangiji Allahnka!' "
8 Sai Shaiɗan ya sāke kai shi kan wani dutse mai tsawo sosai,
ya nuna masa dukan mulkokin duniya da ɗaukakarsu. 9 Ya kuma
ce masa, "Dukan waɗannan zan ba ka idan ka durƙusa a gabana
ka yi mini sujada."

3.17: Far 22.2; Zab 2.7; Ish 42.1; Mat 12.18; 17.5; Mar 1.11; Luk 9.35
4.1: Ibr 2.18; 4.15 **4.4**: M. Sh 8.3 **4.6**: Zab 91.11-12 **4.7**: M. Sh 6.16

10 Sai Yesu ya ce masa, "Tafi daga nan kai Shaiɗan! Gama
a rubuce yake cewa,
'Ka yi wa Ubangiji Allahnka sujada,
kuma shi kaɗai za ka bauta masa.' "
11 Sa'an nan Shaiɗan ya bar shi. Sai mala'iku suka zo suka
yi masa hidima.

Yesu Ya Fara Hidimarsa a Galili
(Mar 1.14-15; Luk 4.14-15)

12 Da Yesu ya ji an kama Yohanna, sai ya tashi ya tafi Galili.
13 Ya kuma bar Nazarat ya koma Kafarnahum da zama, wadda
take can bakin teku, a kan iyakar ƙasar Zebulun da Naftali,
14 domin a cika abin da annabi Ishaya ya faɗa cewa,
15 "Ƙasar Zebulun da ƙasar Naftali,
ku da kuke a hanyar teku, da hayin Kogin Urdun,
Da kuma kasar Galili ta waɗanda ba Yahudawa ba,
16 Masu zama cikin duhu kuma sun ga babban haske,
masu zama a inuwar mutuwa kuwa rana ta ɓullo musu."
17 Tun daga lokacin nan, Yesu ya fara wa'azi, yana cewa,
"Ku tuba domin mulkin sama ya yi kusa."

Yesu Ya Kira Masu Kamun Kifi guda Huɗu
(Mar 1.16-20; Luk 5.1-11)

18 Yesu yana tafiya a gefen Tekun Galili ke nan, sai ya ga
waɗansu 'yan'uwa guda biyu, Siman da ake ce da shi Bitrus, da
ɗan'uwansa Andarawus, suna jefa abin kamun kifi a teku, don su
masu kamun kifi ne. 19 Sai Yesu ya ce musu, "Ku bi ni, zan mai
da ku masu jawon mutane zuwa wurina." 20 Nan da nan suka bar
kayansu na kama kifi suka bi shi.
21 Da ya ci gaba da tafiya, sai ya ga waɗansu 'yan'uwa guda
biyu kuma, Yakubu ɗan Zabadi, da ɗan'uwansa Yohanna. Suna
cikin jirgin ruwa tare da babansu Zabadi, suna gyaran abin kamun
kifi. Sai ya kira su. 22 Nan da nan suka bar jirgin duk da babansu,
suka bi shi.

Yesu Ya Taimaki Mutane da Yawa
(Luk 6.17-19)

23 Yesu ya yi ta zazzaga dukan Galili, yana koyarwa a
majami'unsu, yana wa'azin Labari Mai Daɗi na mulkin Allah. Yana
kuma warkar da kowane irin ciwo da rashin lafiya na mutane. 24 Ta

4.10: M. Sh 6.13 **4.12**: Mat 14.3; Mar 6.17; Luk 3.19-20 **4.13**: Yoh 2.12
4.15-16: Ish 8.23—9.1 **4.17**: Mat 3.2 **4.23**: Mat 9.35; Mar 1.39

haka kuwa aka san da shi a cikin ƙasar Suriya gaba ɗaya. Aka yi ta kawo masa dukan marasa lafiya, da masu fama da ciwo iri-iri, da masu shan wuya, da masu aljanu, da masu farfaɗiya, da shanyayyu, ya kuwa warkar da su duka. 25 Taron mutane da yawa suka bi shi daga Galili, da kuma daga yanki mai garuruwa goma, da Urushalima, da Yahudiya, har ma daga hayin Kogin Urdun.

Wa'azi a kan Dutse

5 1 Da Yesu ya ga mutane sun taru da yawa sai ya hau kan dutse ya zauna. Almajiransa kuma suka zo wurinsa, 2 sai ya fara koya musu.

Albarku
(Luk 6.20-23)

3 "Masu albarka ne waɗanda suka san kāsawarsu ta ruhu,
gama mulkin sama nasu ne.
4 Masu albarka ne masu ɓacin zuciya, gama za a yi musu
ta'aziyya.
5 Masu albarka ne masu tawali'u gama za su gāji duniya.
6 Masu albarka ne masu jin yunwa da ƙishin yin abin da
Allah yake so, gama za su ƙoshi.
7 Masu albarka ne masu jin tausayi,
gama za a ji tausayinsu su ma.
8 Masu albarka ne masu tsabtar zuciya,
gama za su ga Allah.
9 Masu albarka ne masu haɗa zumunci, gama za a
ce da su 'ya'yan Allah.
10 Masu albarka ne masu shan wahala saboda adalci,
gama mulkin sama nasu ne.
11 "Masu albarka ne ku, sa'ad da mutane suka zage ku, suka
ba ku wahala, suka kuma yi muku mugunta iri-iri saboda ni.
12 Ku yi murna da farin ciki sosai, domin za ku sami lada mai
yawa a sama, gama haka ma annabawan da suka riga ku suka
sha wahala.

Gishiri da Haske
(Mar 9.50; Luk 14.34-35)

13 "Ku ne gishirin duniya. Amma idan gishiri ya rabu da
daɗinsa, ta yaya za a mai da daɗinsa? Zai zama ba shi da sauran
amfani sai dai a zubar da shi, a tattaka shi.

5.4: Ish 61.2 **5.5:** Zab 37.11 **5.6:** Ish 55.1-2 **5.8:** Zab 24.3-4 **5.10:** 1 Bit 3.14 **5.11:** 1 Bit 4.14 **5.12:** 2 Tar 36.16; A. M. 7.52 **5.13:** Mat 9.50; Luk 14.34-35

14 "Ku ne hasken duniya. Ai, birnin da aka gina a kan tudu
ba a iya ɓoye shi. 15 Ba a kunna fitila a rufe ta da kwano, sai
dai a ajiye ta a kan tebur inda za ta ba wa dukan mutanen gidan
haske. 16 Haka kuma, bari ku zama masu haske ga mutane, domin
idan suka ga ayyuka masu kyau da kuke yi, za su ɗaukaka Ubanku
wanda yake cikin sama.

Koyarwa a kan Dokoki

17 "Kada ku yi tsammani na zo ne in rushe Dokar Musa da
koyarwar annabawa. Ban zo domin in rushe su ba, sai dai domin
in cika su. 18 Gaskiya ina gaya muku, kafin sama da ƙasa su ƙare,
ba wani layi ko ɗigo na Dokar da zai wuce, sai an cika kome
duka. 19 Saboda haka duk wanda ya karya ko da ɗaya daga cikin
ƙananan dokokin nan, ya kuma koya wa mutane su karya dokokin,
za a ce da shi mafi ƙanƙanta a cikin mulkin sama. Duk wanda
ya bi su kuwa har ya koyar da su, za a ce da shi mai girma a
mulkin sama. 20 Ina gaya muku idan ba ku fi malaman dokoki da
Farisiyawa adalci ba, ba za ku shiga mulkin sama ba, ko kaɗan.

Koyarwa a kan Fushi
(Luk 12.57-59)

21 "Kun dai ji an gaya wa kakanninmu cewa, 'Kada ka kashe
wani, wanda ya kashe wani kuma, za a hukunta shi.' 22 Amma
ina gaya muku, wanda yake fushi da ɗan'uwansa, za a hukunta
shi. Wanda ya kira ɗan'uwansa banza, za a kai shi kotu. Wanda
kuma ya kira ɗan'uwansa wawa, ya dace da gidan wuta. 23 Saboda
haka idan kana cikin ba da baiko a kan bagaden hadaya sai ka
tuna cewa ɗan'uwanka yana fushi da kai, 24 sai ka ajiye baikonka
a gaban bagaden tukuna, ka je ka shirya da ɗan'uwanka. Sa'an
nan ka zo ka ba da baikonka.

25 "Idan wani ya kai ƙararka, ka yi sauri ka shirya da shi tun
kuna kan hanya kafin ku isa kotu. Idan ba haka ba kuwa zai haɗa
ka da alƙali, alƙali kuma yă haɗa ka da ɗan sanda a kuma kulle
ka a kurkuku. 26 Gaskiya ina gaya maka, kafin a fitar da kai daga
nan, sai ka biya dukan kuɗin da ake binka.

Koyarwa a kan Zina

27 "Kun dai ji an faɗa musu cewa, 'Kada ka yi zina.' 28 Amma
abin da nake gaya muku shi ne, idan mutum ya yi wa mace kallon

5.14: Yoh 8.12; 9.5 **5.15:** Mar 4.21; Luk 8.16; 11.33 **5.16:** 1 Bit 2.12
5.18: Luk 16.17 **5.21:** Fit 20.13; M. Sh 5.17 **5.27:** Fit 20.14; M. Sh 5.18

sha'awa, ya riga ya yi zina ke nan da ita a zuciyarsa. 29 Idan idonka na dama yana sa ka ka yi zunubi, ka cire shi ka yar. Gara ka rasa wani gaɓa na jikinka da a jefa dukan jikinka a cikin wuta. 30 Idan hannunka na dama yana sa ka ka yi zunubi, ka cire shi ka yar. Gara ka rasa wani gaɓa na jikinka da dukan jikinka yă shiga cikin wuta.

Koyarwa a kan Kashen Aure
(Mat 19.9; Mar 10.11-12; Luk 16.18)

31 "An kuma gaya musu cewa, 'Wanda ya saki matarsa dole yă ba ta takardar saki.' 32 Amma abin da nake gaya muku shi ne, idan mutum ya saki matarsa ba domin laifin yin zina ba, ya sa ta a hanyar yin zina ke nan. Duk wanda ya aure ta kuma, ya yi zina.

Koyarwa a kan Rantsuwa

33 "Har yanzu dai kun ji an gaya wa kakanninmu cewa, 'Kada ka rantse kan ƙarya, sai dai ka cika alkawarin da ka yi wa Ubangiji.' 34 Amma abin da nake gaya muku shi ne, kada ku rantse sam, ko da sama, domin wurin zaman Allah ke nan. 35 Kada kuma ku rantse da ƙasa, domin nan ne Allah yake ajiye ƙafafunsa, ko kuma da Urushalima domin ita ce birnin Babban Sarki. 36 Kada kuwa ka rantse da kanka don ba za ka iya mai da ko gashi ɗaya yă zama fari ko baƙi ba. 37 Abin da ya kamata ku ce kawai, shi ne, 'I' ko 'A'a' abin da ya wuce haka kuwa daga wurin Mugun nan yake.

Koyarwa a kan Ramuwa
(Luk 6.29-30)

38 "Kun dai ji an gaya musu cewa, 'Ido domin ido, haƙori kuma domin haƙori.' 39 Amma abin da nake faɗa muku shi ne, kada ku ƙi wanda ya yi muku laifi. Idan wani ya mare ka a kumatun dama, ka juya masa ɗayan yă mara. 40 Idan wani ya kai ƙararka don yă ƙwace rigarka, to, ka ba shi har da mayafinka ma. 41 Idan wani mai iko ya matsa maka ku yi tafiyar kilomita ɗaya, to, ku yi tafiyar kilomita biyu. 42 Idan wani ya roƙe ka abu, ka ba shi. Wanda kuma ya zo neman aro daga wajenka, kada ka hana shi.

5.29: Mat 18.9; Mar 9.47 **5.30**: Mat 18.8; Mar 9.43
5.31: M. Sh 24.1-4; Mat 19.7; Mar 10.4 **5.32**: Mat 19.9; Mar 10.11-12; Luk 16.18; 1 Kor 7.10-11 **5.33**: L. Fir 19.12; L. Kid 30.2; M. Sh 23.21
5.34: Yak 5.12; Ish 66.1; Mat 23.22 **5.35**: Ish 66.1; Zab 48.2
5.38: Fit 21.24; L. Fir 24.20; M. Sh 19.21

A Kaunaci Abokan Gāba
(Luk 6.27-28, 32-36)

43 "Kun dai ji an gaya musu cewa, 'Ka ƙaunaci ɗan'uwanka,
ka ƙi wanda ba ya ƙaunarka.' 44 Amma abin da nake gaya muku
shi ne, ku ƙaunaci waɗanda ba sa ƙaunarku, ku yi wa masu ba
ku wahala addu'a. 45 Ta yin haka ne za ku zama 'ya'yan Ubanku
na sama, wanda yake sa rana ta yi haske a kan masu kirki da
marasa kirki ma, yă kuma aiko ruwan sama a kan masu adalci
da marasa adalci. 46 Idan waɗanda suke ƙaunarku kawai kuke
ƙauna, wane lada za ku samu? Ko masu karɓar haraji ma, ai, suna
yin haka. 47 Idan kuwa 'yan'uwanku kawai kuke gai da su, to, me
kuke yi da ya fi na waɗansu? Ai, ko waɗanda ba Yahudawa ba
ma suna yin haka. 48 Saboda haka sai ku zama cikakku kamar
yadda Ubanku na sama yake cikakke.

Koyarwa a kan Ba da Baiko

6 1 "Ku yi hankali kada hidimarku ta addini ta zama ta ganin
ido. Domin idan kuka yi haka, ba za ku sami lada a wurin
Ubanku na sama ba.

2 "Saboda haka, idan za ka ba da baiko, kada ka yi ta surutu
a kai, yadda munafukai suke yi a majami'u da kuma kan hanyoyi
domin mutane su yabe su. Gaskiya ina gaya muku, sun riga sun
sami ladansu ke nan. 3 Amma idan za ka yi wa wani mai bukata
taimako, kada ka bar wani ya san abin da kake yi. 4 Abubuwan
kirki da kake yi, ka yi su a ɓoye, Ubanka kuwa da yake ganin
dukan abin da ake yi a ɓoye, zai ba ka lada.

Koyarwa a kan Addu'a
(Luk 11.2-4)

5 "Kuma idan za ku yi addu'a, kada ku zama kamar
munafukai, masu son yin addu'a a tsaye a cikin majami'u da
kuma kan hanya don mutane su gan su. Gaskiya ina gaya muku,
sun riga sun sami ladansu. 6 Amma idan za ka yi addu'a, ka shiga
ɗaki ka rufe ƙofa, ka yi addu'a ga Ubanka wanda ba a gani,
Ubanka kuma da yake gani a ɓoye zai ba ka lada.

7 "Idan kuna addu'a, kada ku yi dogon surutu kamar waɗanda
ba su san Allah ba, waɗanda suke tsammani idan suka yi dogon
surutu ne za a ji su. 8 Kada ku yi kamarsu, gama Ubanku ya san

---

5.43: L. Fir 19.18. **5.48**: L. Fir 19.2; M. Sh 18.13 **6.1**: Mat 23.5
6.5: Luk 18.10-14

abin da kuke bukata kafin ma ku roƙe shi. 9 Sai ku yi addu'a
kamar haka:
Ubanmu wanda yake cikin sama,
a ɗaukaka sunanka mai tsarki.
10 Mulkinka yă zo,
a yi nufinka a cikin duniya,
kamar yadda ake yinsa a cikin sama.
11 Ka ba mu abincin yau da kullum.
12 Ka yafe mana laifofinmu,
kamar yadda muke yafe wa waɗanda suke yi mana laifi.
13 Kada ka kai mu cikin jaraba,
amma ka tsare mu daga Mugun nan.
14 "Gama idan kuka yafe wa waɗanda suka yi muku laifi,
Ubanku na sama ma zai yafe muku. 15 Amma idan kuwa ba ku yafe
wa mutane ba, haka ma Ubanku ba zai yafe muku laifofinku ba.

Koyarwa a kan Azumi

16 "Idan kuna azumi, kada ku ɓata fuska kamar yadda
munafukai suke yi. Su dai sukan ɓata fuskarsu don su nuna wa
mutane cewa suna azumi. Gaskiya ina gaya muku, sun riga sun
sami ladansu ke nan. 17 Amma idan kana azumi, ka wanke
fuskarka, ka shafa mai a kanka, 18 don kada a ga kana azumi.
Ubanka da ba a gani, wanda kuma yake ganin abin da ake yi a
ɓoye, zai ba ka lada.

Koyarwa a kan Tara Dukiya a Sama
(Luk 12.33-34)

19 "Kada ku tara wa kanku dukiya a duniya inda asu da tsatsa
za su ɓata, inda kuma ɓarayi za su iya shiga su yi sata. 20 Sai dai
ku tara wa kanku dukiya a sama, inda asu ko tsatsa ba za su ɓata
ba, inda kuma ɓarayi ba za su shiga su yi sata ba. 21 Gama inda
dukiyarka take nan tunaninka yake.

Fitilar Jiki
(Luk 11.34-36)

22 "Ido shi ne fitilar jiki, idan idonka yana da lafiya, dukan
jikinka ma zai cika da haske. 23 Amma idan idonka ba lafiya,
dukan jikinka zai rasa haske. Idan hasken jikinka ya zama duhu,
lallai duhun zai yi yawa.

6.14-15: Mar 11.25-26 **6.19:** Yak 5.2-3

Bautar Allah ko Bautar Dukiya
(Luk 16.13)

24 "Ba wanda zai iya bauta wa shugabanni biyu, ko dai ya ki
daya ya so daya, ko ya yi wa dayan aminci yă rena dayan. Ba dama
ku sa ranku ga bin Allah ku kuma sa ga kudi duk gaba daya.

Dogara ga Ubangiji
(Luk 12.22-31)

25 "Saboda haka ina gaya muku, kada ku damu da yadda za
ku rayu game da abin da za ku ci ko abin da za ku sha, ko kuma
yadda za ku sami riguna don jikinku. Rai bai fi abinci ba? Kuma
jiki bai fi kayan da za ku sa ba? 26 Ku dubi tsuntsaye mana, ba
sa shuka, ba sa girbi, ba sa tara a rumbuna. Duk da haka Ubanku
na sama ne yake ciyar da su. Ba ku fi su daraja ba? 27 Wane ne
a cikinku ta wurin damuwarsa zai iya kara wa kansa ko awa daya
ga kwanakin rayuwarsa? [d]
28 "Kuma don me kuke damuwa game da kayan da za ku sa?
Ku dubi su furen daji yadda suke girma mana, ba sa aiki ko saka
kome. 29 Duk da haka ina gaya muku, ko sarki Solomon da dukan
girmarsa, bai taba ado kamar daya daga cikinsu ba. 30 To, idan
har Allah zai yi wa ciyawar daji ado haka wadanda suke nan yau,
gobe kuwa a kone su, balle ku? Ya ku marasa bangaskiya!
31 "Saboda haka kada ku damu da cewa, 'Me za mu ci?' ko,
'Me za mu sha?' ko, 'Me za mu sa?' 32 Gama wadanda ba su san
Allah ba, su suke neman wadannan abubuwan. Ubanku na sama
kuwa ya san kuna bukatar duk wadannan abubuwan. 33 Muhimmin
abu na farko shi ne ku mika kanku ga al'amuran mulkinsa, da kuma
aikata nufinsa, za a ba ku har da wadannan abubuwan ma. 34 Saboda
haka kada ku damu don gobe, gama gobe yana zuwa da wahalolinsa,
wahalolin yau sun ishe ku don yau.

Kada ku Ba Kowa Laifi
(Luk 6.37-38, 41-42)

7 1 "Kada ku ba kowa laifi, don kada a ba ku. 2 Gama da irin
shari'ar da kuke yi wa mutane, da ita za a yi muku shari'a.
Mudun da kuke auna wa mutane da shi, da shi za a auna muku.
3 Don me kake ganin dan tsinken da yake cikin idon dan'uwanka,
amma ba ka kula da gungumen da yake cikin idonka ba? 4 Ko

6.29: 1 Sar 10.4-7; 2 Tar 9.3-6 **7.2**: Mar 4.24

[d] **6.27 kara wa kansa ko awa daya ga kwanakin rayuwarsa**: Wani juyi na wadannan kalmomin shi ne, "Kara wa kansa ko kafa daya ga tsawonsa."

kuma yaya za ka ce wa ɗan'uwanka, 'Bari in cire ɗan tsinken da yake cikin idonka,' bayan gungume yana cikin naka idon? 5 Kai munafuki, ka cire gungumen da yake cikin idonka tukuna, don ka iya gani sosai yadda za ka cire ɗan tsinken da yake cikin idon ɗan'uwanka.

6 "Kada ku ba karnuka abu mai tsarki, kada kuma ku ba aladu duwatsunku masu daraja wato, lu'ulu'unku. Don za su tattaka, su kuma juye su jiji muku ciwo.

Ku Roƙa, Ku Nema, Ku Kwanƙwasa
(Luk 11.9-13)

7 "Ku yi ta roƙo za a ba ku, ku yi ta nema za ku samu. Ku yi ta ƙwanƙwasa kuma za a buɗe muku. 8 Gama duk wanda ya roƙa za a ba shi, duk wanda ya nema zai samu, kuma duk wanda ya ƙwanƙwasa za a buɗe masa. 9 Ko akwai wani a cikinku ubanni, wanda idan ɗansa ya roƙe shi burodi, sai ya ba shi dutse? 10 Ko kuma idan ɗan ya roƙe shi kifi, sai ya ba shi maciji? 11 Idan ku da kuke mugaye kun san yadda za ku ba wa 'ya'yanku abubuwa masu kyau, balle fa Ubanku na sama, ai, zai ba da abubuwa masu kyau ga waɗanda suka roƙe shi!

12 "Duk abin da kuke so mutane su yi muku sai ku ma ku yi musu, gama wannan shi ne manufar koyarwar Dokar Musa da ta annabawa.

Karamar Kofa
(Luk 13.24)

13 "Ku shiga ta ƙaramar ƙofa, gama ƙofar zuwa halaka tana da fāɗi. Kuma hanyarta tana da saukin bi, masu shiga cikinta kuma suna da yawa. 14 Amma ƙofar zuwa rai, ƙarama ce. Hanyarta kuma da wuyar bi. Masu binta kuma ba su da yawa.

Akan Gane Itace ta Irin 'Ya'yansa
(Luk 6.43-44)

15 "Ku yi hankali da annabawan ƙarya waɗanda suke zuwa wurinku da kamannin tumaki amma a ainihi su kamar kuraye ne da suke cikin tsananin yunwa. 16 Za ku gane su ta irin aikinsu. Za a iya samun 'ya'yan inabi daga jikin ƙaya? Ko kuwa a sami ɓaure daga jikin sarƙaƙƙiya?

17 Haka kuma kowane itace mai kyau yakan ba da 'ya'ya masu kyau, itace marar kyau kuwa yakan ba da 'ya'ya marar

7.12: Luk 6.31

Hoton 'ya'yan inabi (7.16)

kyau. 18 Itace mai kyau ba zai iya ba da munanan 'ya'ya ba, haka
kuma mummunan itace ba zai iya ba da 'ya'ya masu kyau ba.
19 Duk itacen da baya ba da 'ya'ya masu kyau, sai a sare shi a
jefa a cikin wuta. 20 Saboda haka, da irin aikin annabawan ƙaryan
nan za ku gane su.

Ban Taɓa Saninku Ba
(Luk 13.25-27)

21 "Ba duk mai ce mini 'Ubangiji, Ubangiji' ne zai shiga
mulkin sama ba. Sai dai wanda ya yi abin da Ubana wanda yake
cikin sama yake so. 22 A Ranan nan mutane da yawa za su ce
mini 'Ubangiji, Ubangiji!' ba mun yi wa'azi cikin sunanka ba?
Ba mun kori aljanu cikin sunanka ba? Ba mun yi abubuwan ban
mamaki da yawa cikin sunanka ba? 23 Sa'an nan zan ce musu,
'Ni ban taɓa saninku ba. Ku rabu da ni, ku masu yin mugunta.'

Mutane Biyu Masu Gini
(Luk 6.47-49)

24 "Saboda haka duk wanda ya ji wannan maganar tawa, ya
kuma yi amfani da ita, zai zama kamar mai hikima wanda ya gina
gidansa a kan dutse. 25 Da ruwa ya sauko, koguna suka cika, iska

7.19: Mat 3.10; Luk 3.9 **7.20:** Mat 12.33 **7.23:** Zab 6.9

ta taso ta buga gidan, amma bai fãdî ba, domin an gina shi a kan dutse ne.

26 "Duk wanda ya ji maganan nan tawa kuma ya ƙi ya aikata, zai zama kamar wani wawa wanda ya gina gidansa a kan yashi. 27 Da ruwa ya sauko, koguna suka cika, iska ta taso ta buga gidan, sai gidan ya fãdî, mummunar faɗuwa kuwa."

28 Da Yesu ya gama faɗa waɗannan abubuwan, sai taron mutanen suka yi mamakin koyarwarsa, 29 domin ya koya musu kamar mutumin da yake da iko, ba kamar malaman dokokinsu ba.

Yesu Ya Warkar da Kuturu

(Mar 1.40-45; Luk 5.12-16)

8 1 Da Yesu ya sauko daga dutsen, mutane da yawa suka bi shi. 2 Sai wani kuturu wato, mai ciwon fatar jiki, ya zo wurinsa ya durƙusa a gabansa ya ce, "Ubangiji, idan ka yarda kana iya ka tsarkake ni." [d] 3 Sai Yesu ya miƙa hannunsa ya taɓa shi yana cewa, "Na yarda, ka warke." Nan da nan kuturtarsa ta warke. 4 Sai Yesu ya ce masa, "Ka lura fa, kada ka faɗa wa kowa abin da ya faru, amma ka je ka nuna kanka a wurin firist, ka kuma ba da baiko yadda Dokar Musa ta ce. Ka yi haka don ka tabbatar wa jama'a cewa ka warke."

Yesu Ya Warkar da Mai Hidimar wani Babban Sojan Roma

(Luk 7.1-10)

5 Da Yesu ya shiga Kafarnahum, sai wani babban sojan Roma ya zo wurinsa ya roƙe shi ya ce, 6 "Ubangiji, mai yin mini hidima yana kwance a gida, ba ya iya motsi ma, yana shan wahala sosai."

7 Yesu kuwa ya ce masa, "Zan zo in warkar da shi."

8 Sai babban sojan Roman ya amsa ya ce, "Ubangiji ban isa ka zo gidana ba, amma ka yi magana kawai, shi mai yin mini hidimar zai warke. 9 Gama ni ma a ƙarƙashin ikon wani nake, kuma ina da sojoji a ƙarƙashina, nakan ce wa wannan, 'Je ka,' sai yă je, wani kuwa in ce masa, 'Zo,' sai yă zo, in ce wa bawana, 'Yi abu kaza,' sai yă yi."

10 Da Yesu ya ji haka sai ya yi mamaki, sai ya ce wa masu binsa, "Gaskiya ina gaya muku, a cikin Isra'ila ban taɓa sami mai bangaskiya mai ƙarfi kamar wannan ba. 11 Ina gaya muku, da yawa cikin masu bangaskiya irin wannan za su zo daga gabas da

---

7.28-29: Mar 1.22; Luk 4.32 **8.4:** L. Fir 14.1-32

[d] **8.2 ka tsarkake ni:** Bisa ga addinin Yahudawa mai kuturta ba shi da tsarki.

yamma su zauna su ci biki tare da Ibrahim da Ishaku da Yakubu a mulkin sama. 12 Amma za a jefa waɗanda ya kamata su zama mutanen Allah amma suka ƙi a cikin baƙin duhu, inda za a yi kuka da cizon haƙora." 13 Sai Yesu ya ce wa babban sojan Roman, "Ka je, za a yi maka bisa ga bangaskiyarka." Nan da nan mai yin masa hidimar ya warke.

Yesu Ya Warkar da Mamar Matar Bitrus
(Mar 1.29-31; Luk 4.38-39)

14 Da Yesu ya shiga gidan Bitrus, sai ya ga mamar matar Bitrus a kwance, zazzaɓi yana damunta. 15 Sai ya taɓa hannunta, zazzaɓin kuwa ya bar ta, sai ta tashi ta yi masa hidima.

Yesu Ya Warkar da Mutane da Yawa
(Mar 1.32-34; Luk 4.40-41)

16 Da yamma ta yi, mutane suka kawo wa Yesu masu aljanu da yawa, ya kuwa fitar da aljanun ta yin magana kawai. Ya kuma warkar da duk marasa lafiya. 17 Ya yi wannan domin a cika abin da aka faɗa ta bakin annabi Ishaya cewa, "Ya ɗauke cututtukarmu, ya kawar da rashin lafiyarmu."

Masu cewa Za su Bi Yesu
(Luk 9.57-62)

18 Da Yesu ya ga babban taron mutane kewaye da shi, sai ya sa a haye zuwa wancan gefen. 19 Sai wani malamin dokoki ya zo ya ce masa, "Malam, zan bi ka duk inda za ka."

20 Sai Yesu ya ce masa, "Beraye suna da ramummukansu, tsuntsaye kuma suna da wurin kwanansu. Amma Dan Mutum ba shi da wurin kwana."

21 Wani daga cikin almajiransa ya ce masa, "Ubangiji bari in je in binne babana tukuna."

22 Amma Yesu ya ce masa, "Bi ni, bari waɗanda suka mutu su binne 'yan'uwansu matattu."

Yesu Ya Tsawata wa Hadari
(Mar 4.35-41; Luk 8.22-25)

23 Da ya shiga jirgin ruwa, sai almajiransa suka bi shi. 24 Sai iska mai ƙarfi ta taso a tekun har ruwan yana tashi yana shiga cikin jirgin, amma Yesu yana nan yana barci. 25 Sai suka je suka tashe shi suka ce, "Ubangiji, ka cece mu, za mu halaka!"

8.11: Luk 13.29 **8.12:** Mat 22.13; 25.30; Luk 13.28 **8.17:** Ish 53.4

26 Sai ya ce musu, "Don me kuka ji tsoro haka, ya ku masu ƙaramar bangaskiya?" Sai ya tashi ya tsawata wa iskar da kuma tekun, sai wurin duk ya yi shiru.

27 Mutane suka yi mamaki suka ce, "Wane irin mutum ne wannan, wanda har iska ma da teku suna yi masa biyayya?"

Yesu Ya Warkar da Masu Aljanu
(Mar 5.1-20; Luk 8.26-39)

28 Da ya kai ɗaya hayin, zuwa ƙasar Garasinawa,[e] mutum biyu masu aljanu suka fito daga wurin da ake binne mutane suka sadu da shi. Sun zama abin tsoro sosai har ma ba mai iya bin wannan hanyar. 29 Nan da nan sai suka yi ihu suka ce, "Ina ruwanka da mu, Dan Allah? Ko ka zo ne don ka ba mu wahala tun kafin lokacin yă yi?"

30 Gaba kaɗan kuma akwai wani babban garken aladu suna kiwo. 31 Aljanun suka roƙe shi suka ce, "Idan ka fitar da mu, ka sa mu shiga cikin garken aladun nan."

32 Sai ya ce musu, "To, ku tafi." Sai suka fita suka shiga cikin aladun, sai garken aladun gaba ɗaya suka tashi a guje suka gangara, suka fāɗi cikin tekun, suka mutu cikin ruwan.

33 Masu kiwon aladun kuwa suka gudu, da suka shiga gari sai suka ba da labarin abin da ya faru da masu aljanun. 34 Sai duk mutanen garin suka fito don su taryi Yesu. Da suka gan shi, sai suka roƙe shi yă tashi daga ƙasarsu.

Yesu Ya Warkar da Shanyayye
(Mar 2.1-12; Luk 5.17-26)

9 1 Sai Yesu ya shiga jirgin ruwa, ya haye ya je inda ya yi girma.[f] 2 Sai aka kawo masa wani shanyayye yana kwance a kan tabarma. Da Yesu ya ga bangaskiyarsu, sai ya ce wa shanyayyen, "Kada ka damu, ɗana, an yafe maka zunubanka." 3 Da jin wannan, waɗansu malaman dokoki suka ce wa junansu, "Wannan mutumin yana yi wa Allah reni"

4 Amma Yesu ya san abin da suke tunani a kai, sai ya ce musu, "Don me kuke yin mugun tunani a zuciyarku haka? 5 Wanne ya fi sauƙi, a ce, 'An gafarta maka zunubanka,' ko kuwa a ce, 'Tashi ka yi tafiya'? 6 Amma ina so ku sani cewa Ɗan Mutum yana da iko yă gafarta zunubai a duniya." Sai ya ce wa shanyayyen, "Tashi, ka ɗauki tabarmarka, ka tafi gida."

[e] **8.28 Garasinawa:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Gadara" ko "Gergesena" ne a nan.
[f] **9:1 inda ya yi girma:** Wato, Kafarnahum ke nan.

7 Mutumin kuwa ya tashi ya tafi gidansa. 8 Da taron mutanen
suka ga haka sai suka ji tsoro, suka ɗaukaka Allah wanda ya ba
mutane irin wannan iko.

Yesu Ya Kira Matiyu
(Mar 2.13-17; Luk 5.27-32)

9 Da Yesu ya ci gaba da tafiya, sai ya ga wani mutum wanda
ake ce da shi Matiyu, yana zaune a wurin karɓar haraji; sai Yesu
ya ce masa, "Bi ni." Sai ya tashi ya bi shi.

10 Daga baya da Yesu yana cin abinci a gidan Matiyu, sai
masu karɓar haraji da masu zunubi da yawa suka zo suka zauna
tare da shi da almajiransa.

11 Da Farisiyawa suka ga haka, sai suka ce wa almajiransa,
"Don me malaminku yake cin abinci da masu karɓar haraji, da
masu zunubi?"

12 Da Yesu ya ji wannan sai ya ce, "Masu lafiya ba sa bukatar
likita, sai dai marasa lafiya. 13 Ku je ku koyi abin da wannan yake
nufi, 'Jinƙai nake so a wurinku, ba hadaya ba.' Gama ban zo don
in kira masu adalci ba, sai dai domin masu zunubi."

Tambaya a kan Yin Azumi
(Mar 2.18-22; Luk 5.33-39)

14 Daga nan almajiran Yohanna suka zo wurin Yesu suka ce
masa, "Me ya sa mu da Farisiyawa mukan yi azumi amma
almajiranka ba sa yi?"

15 Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Abokan ango za su yi baƙin
ciki tun ango yana tare da su ne? Ai, lokaci yana zuwa da za a
ɗauke angon a bar su. A lokacin ne za su yi azumi.

16 "Ba wanda zai yi facin tsohuwar riga da sabon yadi, don
facin zai yage rigar, yagewar ma ta fi ta dā. 17 Ba wanda zai
zuba sabon ruwan inabi[g] a cikin tsofaffin salkuna. Idan ma an
zuba, salkunan za su fashe, ruwan inabin kuma yă zube,
salkunan kuma su lalace. Sabon ruwan inabi dai, sai a zuba shi
a cikin sababbin salkuna. Da haka ba za a rasa ko ruwan, ko
kuma salkunan ba."

9.10-11: Luk 15.1-2 **9.13**: Mat 12.7; Hos 6.6

[g] **9.17 ruwan inabi**: Akan samu wannan daga 'ya'yan inabin da aka matse. An cika yin amfani da ruwan inabi kamar ruwan sha a ƙasar Isra'ila.



Hoton salka (9.17)

'Yar Jayirus da Mace Mai Zub da Jini
(Mar 5.21-43; Luk 8.40-56)

18 Yesu yana kan gaya musu haka ke nan, sai ga wani shugaban majami'a ya zo ya durƙusa a gabansa ya ce, "'Yata ta mutu ba da jimawa ba, ka zo ka taɓa ta, za ta tashi."

19 Yesu kuwa ya tashi tare da almajiransa, suka bi mutumin.

20 Sai ga wata mata da ta yi shekara goma sha biyu tana fama da ciwon zubar da jini. Ta zo ta bayansa ta taɓa bakin rigarsa, 21 gama ta ce a ranta, "Idan na taɓa ko da rigarsa kawai, zan warke."

22 Da Yesu ya juya ya gan ta, sai ya ce, "Kada ki damu 'yata. Bangaskiyarki ta warkar da ke." Nan take matar ta warke.

23 Da Yesu ya zo gidan shugaban, ya ga masu busa da taron mutane ana ta hayaniya. 24 Sai ya ce, "Ku tashi daga nan! Yarinyar ba ta mutu ba, tana barci ne kawai." Sai suka yi masa dariyar reni. 25 Amma da aka kore su waje, sai ya shiga ya kama hannun yarinyar, sai ta tashi. 26 Labarin kuwa ya bazu duk cikin wannan ƙasar.

Yesu Ya Warkar da Makafi da Bebe

27 Yesu yana barin wurin ke nan, sai makafi biyu suka bi shi suna kira da ƙarfi suna cewa, "Ka ji tausayinmu, Ɗan Dawuda!"

28 Da Yesu ya shiga wani gida sai makafin suka zo wurinsa, ya ce musu, "Kun ba da gaskiya zan iya warkar da ku?"

Suka ce masa, "I, Ubangiji."

29 Sa'an nan ya taɓa idanunsu ya ce, "Bisa ga bangaskiyarku
za a warkar da ku." 30 Sai idanunsu suka buɗe. Sa'an nan kuma
Yesu ya ja musu kunne sosai ya ce, "Kada ku faɗa wa kowa
wannan."
31 Amma suka fita suka yi ta baza labarinsa ko'ina a ƙasar.
32 Da za su tafi, sai aka kawo wani da aljani ya hana shi
magana. 33 Da aka fitar da aljanin, wannan da ba ya iya magana
kuwa ya fara magana. Taron mutane kuwa suka yi mamaki suka
ce, "Ba a taɓa ganin wani abu kamar haka a Isra'ila ba."
34 Amma Farisiyawa suka ce, "Ai, da ikon shugaban aljanu
ne yake fitar da aljanun."

Yesu Ya Ji Tausayin Mutane

35 Daga nan Yesu ya bi dukan garuruwa da ƙauyuka, yana
koyarwa a majami'u, yana yin wa'azin Labari Mai Daɗi na
mulkin Allah, yana kuma warkar da mutane daga kowane irin
ciwo da rashin lafiya. 36 Da ya ga jama'a sun taru da yawa, sai
ya ji tausayinsu, gama suna shan wahala kuma ba mai taimako,
kamar tumakin da ba su da mai kiwo. 37 Sai ya ce wa almajiransa,
"Girbin yana da yawa, amma masu aikin kaɗan ne. 38 Saboda
haka ku roƙi mai gonar yă aiko da masu aiki su yi masa girbi."

Yesu Ya Kira Almajiransa
(Mar 3.13-19; Luk 6.12-16)

10 1 Sai Yesu ya kirawo almajiransa goma sha biyu, ya ba su
iko su fitar da aljanu, su warkar da kowane irin ciwo da
rashin lafiya. 2 Ga sunayen manzannin nan goma sha biyu. Da
farko, Siman wanda ake ce da shi Bitrus, da ɗan'uwansa
Andarawus; da Yakubu ɗan Zabadi; da ɗan'uwansa Yohanna; 3 da
Filibus; da Batilomi; da Toma; da Matiyu mai karɓar haraji; da
Yakubu ɗan Alfiyus; da Taddiyus; 4 da Siman mutumin Kan'ana;
da kuma Yahuda Iskariyoti wanda ya bashe shi.

Yesu Ya Aiki Sha Biyun
(Mar 6.7-13; Luk 9.1-6)

5 Yesu ya aiki sha biyun nan ya ce musu, "Kada ku je wurin
waɗanda ba Yahudawa ba, kuma kada ku shiga wani garin
Samariya, 6 sai dai ku je wurin tumakin da suka ɓata na jama'ar
Isra'ila. 7 Ku je ku yi musu wa'azi cewa, 'Mulkin sama ya kusan

---

9.34: Mat 10.25; 12.24; Mar 3.22; Luk 11.15 **9.35**: Mat 4.23; Mar 1.39; Luk 4.44
9.36: L. Kid 27.17; 1 Sar 22.17; 2 Tar 18.16; Ez 34.5; Mar 6.34 **9.37-38**: Luk 10.2

zuwa.' 8 Ku warkar da marasa lafiya, ku ta da waɗanda suka mutu,
ku tsarkake kutare, ku fitar da aljanu. Kun samu a kyauta, ku
kuma bayar kyauta. 9 Kada ku riƙe kuɗi ko wani abu kamar kuɗi
da za ku iya amfani da shi. 10 Kada kuma ku riƙe jaka, ko riga
guda biyu, ko takalma, ko sanda, don ma'aikaci ya cancanci
samun abin biyan bukatarsa.

11 "Duk gari ko ƙauyen da kuka shiga, ku nemi mutumin kirki
ku zauna da shi har sai lokacin da za ku tashi. 12 Idan kuka shiga
gidan ku gaishe su. 13 Idan gidan kirki ne, sai ku yi addu'a Allah
ya ba su salama, amma idan ba na kirki ba ne, to, kada su sami
salamar Allah. 14 Duk wanda bai karɓe ku ba, ko kuma ya ƙi jin
maganarku, ku kakkaɓe ƙurar ƙafafunku idan kuka fita daga gidan
ko garin. 15 Gaskiya ina gaya muku, za a fi jin tausayin mutanen
Sodom da Gomora fiye da mutanen garin nan a Ranar Shari'a.

Wahala mai Zuwa
(Mar 13.9-13; Luk 12.11-12, 21.12-19)

16 "Ga shi ina aikanku kamar tumaki cikin kuraye, saboda
haka ku zama masu wayo kamar macizai, kuma marasa ɓarna
kamar kurciya. 17 Ku yi hankali da mutane, gama za su kai ku
kotu, su kuma yi muku bulala a majami'unsu. 18 Saboda ni kuma,
za su kai ku gaban shugabanni da sarakuna, domin ku shaida
Labari Mai Daɗi a gabansu, da gaban waɗanda ba Yahudawa ba.
19 Lokacin da suka ba da ku, kada ku damu da abin da za ku faɗa,
gama za a ba ku abin da za ku ce a lokacin. 20 Domin ba ku ne
kuke magana ba, Ruhun Ubanku ne yake magana ta wurinku.

21 "Dan'uwa zai ba da ɗan'uwansa a kashe shi, baba kuma
yă ba da ɗansa, 'ya'ya kuma za su tayar wa iyayensu, har su sa
a kashe su. 22 Waɗanda ba Yahudawa ba kuma za su ƙi ku saboda
sunana. Amma wanda ya jimre har zuwa ƙarshe zai tsira. 23 Idan
suna ba ku wahala a wani gari, ku gudu zuwa gari na gaba, gama
gaskiya ina gaya muku, kafin ku gama zagaya dukan garuruwan
Isra'ila, Ɗan Mutum zai dawo.

24 "Ba ɗan makaranta da yi fi malaminsa, ko kuma bawa da
ya fi maigidansa. 25 Dan makaranta yana iya zama kamar
malaminsa, bawa kuma kamar maigidansa. Idan suka ce da
maigidan Ba'alzabul, me za su ce game da mutanen gidan?

10.10: 1 Kor 9.14; 1 Tim 5.18 **10.14:** A. M. 13.51
10.15: Mat 11.24; Far 19.24-28 **10.7-15:** Luk 10.4-12 **10.16:** Luk 10.3
10.17-20: Mar 13.9-11; Luk 12.11-12; 21.12-15 **10.21:** Mar 13.12; Luk 21.16
10.22: Mat 24.9,13; Mar 13.13; Luk 21.17 **10.24:** Luk 6.40; Yoh 13.16; 15.20
10.25: Mat 9.34; 12.24; Mar 3.22; Luk 11.15

Wanda Za a Ji Tsoro
(Luk 12.2-7)

26 "Saboda haka, kada ku ji tsoronsu, domin ba abin da yake
a rufe da ba za a buɗe ba, kuma ba abin da yake a ɓoye da ba
za a sani ba. 27 Abin da nake gaya muku a duhu, ku faɗa a haske.
Abin da na gaya muku a ɓoye kuwa, ku yi shelarsa a fili. 28 Kada
ku ji tsoron masu kashe mutum, amma ba sa iya kashe ransa. Sai
dai ku ji tsoron wanda zai iya halaka jiki duk da rai a gidan wuta.
29 Ba ana sayar da kanari guda biyu kobo ɗaya ba? To, ba ɗayansu
da zai fāɗi a ƙasa ba tare da sanin Ubanku ba. 30 Ai, gashin kanku
ma an ƙirga su. 31 Saboda haka, kada ku ji tsoro. Ai, kun fi kanari
daraja sau barkatai.

Nuna Yarda da Almasihu a Gaban Mutane
(Luk 12.8-9)

32 "Duk wanda ya nuna shi nawa ne a gaban mutane, ni ma
zan nuna shi nawa ne a gaban Ubana da yake a sama. 33 Amma
duk wanda ya yi mūsun sanina a gaban mutane, ni ma zan yi
mūsun saninsa a gaban Ubana da yake a sama.

Ban Kawo Salama ba Sai Faɗa
(Luk 12.51-53, 14.26-27)

34 "Kada ku yi tsammani na zo in kawo salama ne a duniya.
Ba don in kawo salama na zo ba, sai dai faɗa. 35 Gama na zo ne
in haɗa faɗa tsakanin ɗa da babansa, 'ya kuma da mamarta, mace
kuma da mamar mijinta. 36 Mutanen gidansa ne kuma za su zama
abokan gābansa.

37 "Duk wanda ya fi son mamarsa ko babansa fiye da ni,
bai isa yă zama nawa ba. Kuma duk wanda ya fi son ɗansa ko
'yarsa fiye da ni, bai isa yă zama nawa ba. 38 Duk wanda bai
ɗauki gicciyensa ya bi ni ba, bai isa yă zama nawa ba. 39 Wanda
ya so ransa, zai rasa shi. Wanda kuwa ya rasa ransa saboda ni,
zai same shi.

Ayyukan Lada
(Mar 9.41)

40 "Duk wanda ya karɓe ku, ya karɓe ni ne, duk wanda ya
karɓe ni kuwa ya karɓi wanda ya aiko ni ne. 41 Duk wanda ya

10.26: Mar 4.22; Luk 8.17 **10.33**: 2 Tim 2.12 **10.35-36**: Mika 7.6
10.38: Mat 16.24; Mar 8.34; Luk 9.23
10.39: Mat 16.25; Mar 8.35; Luk 9.24; 17.33; Yoh 12.25
10.40: Mar 9.37; Luk 9.48; 10.16; Yoh 13.20

karɓi annabi don shi annabi ne, zai sami ladan annabi. Kuma duk wanda ya karɓi mai adalci don shi mai adalci ne, zai sami ladan mai adalci. 42 Duk wanda ya ba wa ɗaya daga cikin yaran nan ko da kwaf ɗaya na ruwan sanyi don shi almajirina ne, gaskiya ina gaya muku, ba zai taɓa rasa ladansa ba."

'Yan Aika daga Wurin Yohanna Maibaftisma

(Luk 7.18-35)

11 1 Da Yesu ya gama ba wa almajiransa waɗannan umarnai, sai ya tashi daga wurin ya tafi yana koyarwa yana wa'azi a garuruwansu.

2 A lokacin Yohanna Maibaftisma yana cikin kurkuku, sai ya ji abubuwan da Almasihu yake yi, sai ya aiki almajiransa wurinsa 3 su ce masa, "Kai ne wanda zai zo, ko mu sa ido ga wani?"

4 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ku koma ku faɗa wa Yohanna abin da kuka gani kuka kuma ji: 5 makafi suna samun gani, guragu suna tafiya, kutare suna samun tsarkakewa, kurame suna jin magana, ana ta da waɗanda suka mutu, ana kuma ba wa talakawa Labari Mai Daɗi. 6 Allah zai albarkaci kowa da bai yi shakkar bangaskiyar da yake da ita a kaina ba."

7 Da suka tafi, sai Yesu ya fara yi wa taron mutanen magana a kan Yohanna ya ce, "Me kuka je gani a daji? Kun je ganin dogayen ciyawa da iska take kaɗawa ne? 8 To, me kuka je gani? Kuna tsammani za ku ga wani ya sa riguna masu kyau? Ai, mutanen gidan sarki ne suke sa riguna masu kyau. 9 To, me kuka je gani? Annabi? I, ina gaya muku, har ma ya fi annabi. 10 Wannan shi ne wanda aka rubuta a kansa cewa,

'Ga shi, na aiko manzona yă riga ka gaba,
wanda zai shirya maka hanya kafin ka zo.'

11 Gaskiya ina gaya muku, ba a taɓa haihuwar wani a duniyan nan wanda ya kai Yohanna Maibaftisma girma ba. Amma duk da haka, wanda yake ƙarami duka a mulkin sama ya fi shi. 12 Tun daga zamanin Yohanna Maibaftisma har zuwa yau mulkin Allah yana shan wuya, masu ba da wuyar kuma su suke so su ƙwace mulkin Allah da ƙarfi. 13 Gama Dokar Musa da littattafan annabawa duka sun yi magana a kan mulkin kafin Yohanna yă zo, 14 kuma idan za ku yarda da saƙonsu, Yohanna shi ne wanda aka yi magana a kai da aka ce Iliya zai dawo. 15 Bari mai kunnen ji, yă ji.

11.5: Ish 35.5-6; 61.1 **11.10:** Mal 3.1 **11.12-13:** Luk 16.16
11.14: Mal 3.23; Mat 17.10-13; Mar 9.11-13

16 "Amma da me zan kwatanta wannan zamanin? Kamar yara
ne da suke zaune a kasuwa suna kiran abokan wasansu suna cewa,
17 'Mun hura muku busa, kun ki ku yi rawa!
Mun rera waƙar mutuwa, kun ki ku yi kuka!'
18 Gama da Yohanna ya zo yana yawan azumi, ba ya shan ruwan
inabi, sai suka ce, 'Yana da aljanu.' 19 Da Dan Mutum ya zo yana
ci yana sha, suka ce, 'Ku gan shi, mai yawan ci da sha, abokin
masu karɓar haraji da masu zunubi!' Duk da haka, ana gane
hikimar Allah a ayyukanta."

Garuruwan da Ba su Tuba Ba
(Luk 10.13-15)

20 Sai ya fara tsawata wa garuruwan da ya yi yawancin
ayyukansa na ban mamaki, domin mutanen ba su tuba ba.
21 "Kaitonki, Korasin! Kaitonki, Betsaida! Gama da ayyukan ban
mamakin da aka yi a cikinku ne, aka yi a Taya da Sidon, da sun
tuba tun tuni, sun sa tsumma da toka a jikinsu. 22 Amma ina gaya
muku, a Ranar Shari'a za a fi jin tausayin mutanen Taya da Sidon
fiye da ku. 23 Ke kuma Kafarnahum, kina tsammani ɗaukaka ki
za a yi zuwa sama ne? A ina! Kaskantar da ke za a yi har wurin
zaman matattu. Ayyukan ban mamakin da aka yi a cikinki, da
su ne aka yi a Sodom, da tana nan har wa yau. 24 Amma ina
gaya muku, a Ranar Shari'a za a fi jin tausayin mutanen Sodom
fiye da ke."

Ku zo Wurina Don Ku Sami Hutu
(Luk 10.21-22)

25 A wannan lokacin ne Yesu ya ce, "Na gode maka, Uba,
Ubangijin sama da ƙasa, domin ka ɓoye waɗannan abubuwa ga
masu hikima da masu ilimi, ka kuma bayyana wa 'yan yara.
26 Haka ne ya Uba, gama wannan shi ne abin da ya yi maka kyau.
27 "Ubana ya ba ni dukan abu, kuma ba wanda ya san Dan
sai Uban, kuma ba wanda ya san Uban sai Dan, da kuma wanda
Dan ya so yă bayyana masa.
28 "Ku zo gare ni, dukanku da kuka gaji, kuma kuna fama da
kaya masu nauyi a kanku, zan ba ku hutawa. 29 Ku karɓi
umarnaina, ku kuma koya daga wurina, domin ni mai tawali'u
ne, marar girmankai, kuma za ku sami hutu a zuciyarku. 30 Gama
umarnaina suna da sauƙi, kuma kayana ba nauyi."

11.21: Ish 23.1-18; Ez 26.1—28.26; Jow 4.4-8; Amos 1.9-10; Zak 9.2-4
11.23: Ish 14.13-15; Far 19.24-28 11.24: Mat 10.15; Luk 10.12
11.27: Yoh 3.35; 1.18; 10.15 11.29: Irm 6.16

Tambaya a kan Kiyaye Ranar Hutun Yahudawa, wato, Asabar
(Mar 2.23-28; Luk 6.1-5)

12 [1] A lokacin nan a Ranar Hutun Yahudawa, wato, Asabar
Yesu ya bi ta gonakin alkama. Almajiransa kuwa suna jin
yunwa, sai suka fara cire tsabar alkamar suna ci. [2] Da Farisiyawa
suka ga haka, sai suka ce masa, "Ka gani, almajiranka suna yin
abin da Doka ta hana a yi a Ranar Hutu."
3 Sai ya ce musu, "Ashe, ba ku karanta abin da Dawuda ya
yi ba lokacin da shi da abokan tafiyarsa suke jin yunwa? [4] Yadda
ya shiga wurin da ake sujada ya ci burodin da aka keɓe, wanda
bai kamata ko shi ko abokan tafiyarsa su ci ba, sai dai firistoci
kawai. [5] Ko ba ku karanta a cikin Dokar Musa ba, yadda firistoci
suke karya dokar Ranar Hutu a haikali, kuma bai zama sun yi
laifi ba? [6] Ina gaya muku, ga wanda ya fi haikali a nan. [7] Amma
da kun san abin da wannan ayar take nufi wato, 'Jinkai nake so,
ba hadaya ba,' da ba ku ga marasa laifi da laifi ba. [8] Gama Dan
Mutum Ubangiji ne har ma da na Ranar Hutu."

Mai Shanyayyen Hannu
(Mar 3.1-6; Luk 6.6-11)

9 Sai Yesu ya bar wurin ya shiga majami'arsu. [10] Akwai wani
mutum a wurin mai shanyayyen hannu. Sai suka tambayi Yesu
suka ce, "Doka ta yarda a yi warkarwa a Ranar Hutu?" Sun yi
wannan tambayar ne don su same shi da laifi.
11 Sai ya ce musu, "A ce waninku yana da tunkiya ɗaya tak,
sai ta fāɗi cikin rami a Ranar Hutu, mai tunkiyar ba zai fitar da
ita ba? [12] Ai, mutum ya fi tunkiya daraja sosai. Saboda haka ba
a hana yin aikin kirki a Ranar Hutu ba." [13] Sai ya ce wa mutumin,
"Miƙo hannunka."
Sai ya miƙo, nan da nan sai hannun ya warke ya zama kamar
ɗayan hannun. [14] Amma Farisiyawa suka fita suka yi shawara
yadda za su kashe Yesu.

Cikawar Annabcin Ishaya

15 Da Yesu ya gane haka, sai ya bar wurin, mutane da yawa
suka bi shi, ya kuwa warkar da su duka. [16] Ya kuma ja musu
kunne cewa kada su ba da labarinsa. [17] Wannan kuwa don a cika
abin da aka faɗa ne ta bakin annabi Ishaya cewa,
[18] "Ga mai yin mini hidima, wanda na zaɓa,

12.1: M. Sh 23.26 **12.3-4:** 1 Sam 21.1-7 **12.4:** L. Fir 24.9
12.5: L. Kid 28.9-10 **12.7:** Mat 9.13; Hos 6.6 **12.11:** Luk 14.5

shi ne nake ƙauna, wanda nake jin daɗinsa sosai.
Zan cika shi da Ruhuna,
zai yi wa al'ummai hukunci.
19 Ba zai yi gardama, ko magana da ƙarfi ba,
ba za a ji muryarsa a titi ba.
20 Ba zai karya karan da ya yi kusan karyewa ba,
Fitilar da ta yi kusa mutuwa kuma, ba zai kashe ta ba
Sai ya sa gaskiya ta ci nasara.
21 Al'ummai kuma za su sa zuciya ga sunansa."

Yesu da Ba'alzabul
(Mar 3.20-30; Luk 11.14-23)

22 Sai aka kawo masa wani beben makaho mai aljani. Yesu kuwa ya warkar da shi, har mutumin ya yi magana ya kuma iya gani. 23 Mutanen duka suka yi mamaki suka ce, "Shin, ba wannan shi ne Ɗan Dawuda ba?"

24 Amma da Farisiyawa suka ji haka sai suka ce, "Ai, da ikon Ba'alzabul sarkin aljanu ne wannan mutumin yake fitar da aljanu."

25 Da yake Yesu ya san abin da suke tunani sai ya ce musu, "Duk mulkin da ya rabu kashi biyu suna gāba da junansu, mulkin ba zai tsaya ba. Kuma gari ko gidan da mutanen ba sa shiri da junansu ba zai tsaya ba. 26 Idan aljanu daga mulkin Shaiɗan suna fitar da juna, Shaiɗan yana faɗa da kansa ke nan. To, yaya mulkinsa zai tsaya? 27 Idan kuwa da ikon Ba'alzabul nake fitar da aljanu, to almajiranku fa? Da ikon wa suke fitarwa? Almajiranku ne za su yi muku shari'a a kan wannan. 28 Idan ni kuwa da ikon Ruhun Allah nake fitar da aljanu, ashe, mulkin Allah ya zo muku ke nan.

29 "Ba za a iya shiga gidan mutum mai ƙarfi a kwashe kayansa ba, sai dai idan an ɗaure shi tukuna, sa'an nan za a iya kwashe kayan gidansa.

30 "Wanda ba ya tare da ni, yana gāba da ni ke nan, wanda bai taimake ni tarawa ba kuwa, yana watsarwa ne. 31 Don haka ina gaya muku, za a yafe wa mutane kowane irin zunubi da maganar reni ga Allah, amma wanda ya yi maganar reni game da Ruhu Mai Tsarki, ba za a yafe masa ba. 32 Idan wani ya zagi Ɗan Mutum, za a yafe masa, amma duk wanda ya zagi Ruhu Mai Tsarki, ba za a taɓa yafe masa ba.

12.18-21: Ish 42.1-4 **12.24:** Mat 9.34; 10.25 **12.30:** Mar 9.40 **12.32:** Luk 12.10

Itace da 'Ya'yansa
(Luk 6.43-45)

33 "Itace mai kyau yakan ba da 'ya'ya masu kyau. Itace marar kyau kuma yakan ba da 'ya'ya marasa kyau. Itace dai, da irin 'ya'yansa ne ake ganesshi. 34 Ku mugayen macizai, yaya za ku iya faɗa abu mai kyau bayan ku mugaye ne? Ai, abin da yake cikin zuciya shi yake fitowa a baki. 35 Mutumin kirki yakan fitar da abu mai kyau daga wurin da yake ajiya. Mugun mutum kuma yakan fitar da mugun abu daga wurin da yake ajiya.

36 "Ina gaya muku, duk maganar banza da mutane suka yi, za su ba da lissafinta a Ranar Shari'a. 37 A kan maganarka ne za a yi maka shari'a, ko ta sa ka zama marar laifi ko mai laifi."

Malaman Dokoki da Farisiyawa Suna Neman Alama
(Mar 8.11-12; Luk 11.29-32)

38 Sai wasu daga cikin malaman dokoki da Farisiyawa suka ce masa, "Malam, muna so ka aikata wani abin ban mamaki da zai zama wata alama."

39 Sai ya amsa musu ya ce, "Mutanen zamanin nan mugaye ne waɗanda ba sa tsoron Allah. Suna so su ga alama, amma ba za a nuna musu wata alama ba, sai dai ta annabi Jona. 40 Gama yadda Jona ya yi kwana uku, dare da rana a cikin ciki na babban kifi, haka ma Ɗan Mutum zai yi kwana uku, dare da rana a cikin ƙasa. 41 A Ranar Shari'a mutanen Nineba za su tashi tare da mutanen zamanin nan, su nuna wa mutanen zamanin nan ba su yi daidai ba, don su sun tuba saboda wa'azin Jona. Ga shi kuwa wanda ya fi Jona a nan. 42 A Ranar Shari'a, sarauniyar Sheba za ta tashi tare da mutanen zamanin nan, ta nuna musu ba su yi daidai ba, don ta zo ne daga wuri mai nisa sosai, don ta ji koyarwar hikima ta sarki Solomon. Ga shi kuwa wanda ya fi Solomon a nan."

Dawowar Baƙin Aljani
(Luk 11.24-26)

43 "Idan baƙin aljani ya fita daga jikin mutum, yakan yi ta yawo a wuraren da ba ruwa don yă sami wurin hutawa. Amma idan bai samu ba, 44 sai yă ce, 'Zan koma gidana na dā inda na fito.' Idan ya zo ya sami ba kowa ya kuma ga an share, an gyara

12.33: Mat 7.20; Luk 6.44 **12.34:** Mat 3.7; 23.33; 15.18; Luk 3.7; 6.45
12.38: Mat 16.1; Mar 8.11; Luk 11.16 **12.39:** Mat 16.4; Mar 8.12 **12.40:** Joh 1.17
12.41: Jon 3.5 **12.42:** 1 Sar 10.1-10; 2 Tar 9.1-12

gidan, 45 sai yă koma yă kwaso ăljanu guda bakwai, waɗanda suka fi shi mugunta, su zo su shiga su zauna a wurin. A ƙarshe, zaman mutumin nan zai fi na farkon muni. Haka ma zai zama ga mutanen wannan zamani."

Mamar Yesu da 'Yan'uwansa
(Mar 3.31-35; Luk 8.19-21)

46 Yana kan magana da jama'a ke nan, sai ga mamarsa da 'yan'uwansa suna tsaye a waje suna so su yi magana da shi. 47 Sai aka ce masa, "Ga mamarka da 'yan'uwanka suna tsaye a waje suna so su yi magana da kai."[h]

48 Sai ya ce wa wannan da ya faɗa masa, "Wace ce mamata, kuma su wane ne 'yan'uwana?" 49 Sai ya nuna almajiransa da hannunsa ya ce, "Ga mamata da 'yan'uwana a nan. 50 Gama duk wanda ya yi abin da Ubana da yake cikin sama yake so, shi ne ɗan'uwana, da 'yar'uwata da kuma mamata."

Misali na Mai Shuka
(Mar 4.1-9; Luk 8.4-8)

13 1 A ranan nan Yesu ya fita daga gida, ya je ya zauna a bakin teku. 2 Taron mutane da yawa sosai suka taru kewaye da shi, har sai da ya shiga jirgin ruwa ya zauna, taron mutanen kuma suka tsaya a gefen tekun.

3 Sai ya gaya musu abubuwa da yawă ta wurin misalai, ya ce, "Wani manomi ya je gona don yă yi shuka. 4 Yana cikin yafa iri ke nan, sai waɗansu iri suka fāɗi a kan hanya, sai tsuntsaye suka zo suka cinye su. 5 Waɗansu kuma suka fāɗi a wuri mai duwatsu inda ba ƙasa sosai. Suka tsiro da sauri don ƙasar wurin ba zurfi. 6 Da rana ta yi zafi sai ta ƙone su, har suka bushe, don ba su da saiwa sosai. 7 Waɗansu kuma suka fāɗi a wurin da akwai ƙaya, sai ƙayar ta tashi ta hana su girma. 8 Waɗansu kuma suka fāɗi a wuri mai kyau, suka yi tsaba ɗari-ɗari, waɗansu sittin-sittin, waɗansu kuma talatin-talatin."

9 "Bari mai kunnen ji, yă ji."

Manufar Misali na Mai Shuka
(Mar 4.10-12; Luk 8.9-10)

10 Sai almajiran Yesu suka zo suka ce masa, "Don me kake yi musu magana da misalai?"

13.2: Luk 5.1-3
[h] 12.47 Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da ayar 47.

11 Ya amsa musu ya ce, "Ku dai an yarda muku ku gane asirin
mulkin sama, amma su ba a ba su ba. 12 Gama wanda yake da
abu za a ƙara masa har yă ishe shi sosai, amma wanda ba shi da
kome, za a karɓe ɗan kaɗan dîn da yake da shi. 13 Abin da ya sa
nake musu magana da misalai shi ne, don ko sun duba ba sa gani,
ko sun saurara ba sa ji. Ba sa kuma ganewa. 14 Lallai annabcin
Ishaya ya cika a kansu cewa,

'Za ku yi ta ji kam, amma ba za ku gane ba sam,
Za ku yi ta duba kuma, amma ba za ku gani ba sam,
15 Gama zuciyar mutanen nan ta yi tauri,
kunnuwansu kuma ba sa ji.
Sun kuma rufe idanunsu,
don kada su gani da idanunsu,
kada kuma su ji da kunnuwansu,
don kada su gane a zuciyarsu,
har su juyo wurina in warkar da su.'

16 "Idanunku masu albarka ne domin suna gani. Kunnuwanku
ma haka domin suna ji. 17 Gaskiya ina gaya muku, annabawa da
masu adalci da yawa sun so su ga abin da kuke gani, amma ba
su gani ba, su kuma ji abin da kuke ji, amma ba su ji ba.

Yesu Ya Ba da Bayanin Misalin Mai Shuka

(Mar 4.13-20; Luk 8.11-15)

18 "To, ga abin da misalin mai shuka yake nufi. 19 Idan mutum
ya ji maganar mulkin sa'an nan bai gane ba, Shaiɗan yakan zo
ya ƙwace abin da aka shuka a cikin zuciyar mutumin. Wannan
shi ne irin da ya fāɗî a kan hanya. 20 Wanda ya fāɗî a wuri mai
duwatsu kuwa, shi ne kwatancin wanda da jin maganar Allah sai
ya karɓa da murna. 21 Amma da yake ba shi da tushe, bai daɗe
sosai ba. Lokacin da wahala ko tsanani ya tashi domin wannan
maganar Allah, sai yă ja da baya. 22 Wanda aka shuka a wurin
da akwai ƙaya kuma, shi ne kwatancin wanda ya ji maganar Allah,
amma damuwar duniya da son arziki suka hana maganar girma,
har ta zama ba ta da amfani. 23 Wanda aka shuka a wuri mai kyau
kuma, shi ne kwatancin wanda yake jin maganar Allah ya kuma
gane ta, har ya ba da amfani, wani ɗari-ɗari, wani kuma
sittin-sittin, wani kuma talatin-talatin."

13.12: Mat 25.29; Mar 4.25; Luk 8.18; 19.26 **13.14-15:** Ish 6.9-10
13.16-17: Luk 10.23-24

Ciyawa cikin Alkama

24 Yesu ya sāke ba su wani misali ya ce, "Za a iya kwatanta
mulkin sama da mutumin da ya shuka iri mai kyau a gonarsa,
25 amma lokacin da kowa yake barci, sai abokin gābansa ya je ya
shuka wata irin ciyawa a gonar alkamar, ya tafi abinsa. 26 Da
shukar ta tashi ta yi tsaba, sai ciyawar ma ta tashi. 27 Bayin
maigidan suka zo suka ce masa, 'Maigida, ashe, ba iri mai kyau
ka shuka a gonarka ba? To, yaya duk ciyawa ta fito a wurin?'
28 Ya ce musu, 'Abokin gābana ne ya yi wannan.' Bayin suka ce,
'Kana so mu je mu cire ciyawar?' 29 Amma ya ce, 'A'a, kada
garin cire ciyawar ku cire da alkamar. 30 Bari dukansu su yi girma
tare har lokacin girbi, a lokacin girbin zan gaya wa masu girbin,
su fara cire ciyawar su tara, su ɗaɗɗaure, a ƙone, amma a tara
alkamar a zuba a rumbuna.' "

Misali na Kwayar Mastad
(Mar 4.30-32; Luk 13.18-19)

31 Yesu ya sāke ba su wani misali, ya ce, "Mulkin sama kamar
ƙwayar mastad ne wadda ta fi ƙankanta cikin iri duka da wani
mutum ya ɗauka ya shuka a gonarsa. 32 Shi ne ya fi ƙarami cikin
sauran iri, amma idan ya yi girma, sai yă fi duk sauran itatuwan,
yă zama babban itace, har ma tsuntsaye su yi gidansu a kan
rassansa."

Misali na Yisti
(Luk 13.20-21)

33 Yesu ya sāke ba su wani misali, ya ce, "Mulkin sama kamar
yisti yake, wanda wata mace ta kwaɓa da mudu uku na garin
alkama, har duk garin ya game da yistin."[i]

Yesu Ya Yi Amfani da Misalai
(Mar 4.33-34)

34 Yesu ya gaya wa taron mutanen duk waɗannan abubuwa
da misalai. Ba ya gaya musu wani abu sai tare da misali.
35 Wannan kuwa domin a cika abin da annabi Ishaya ya faɗa ne
cewa,

"Zan yi magana da misalai,
Abubuwan da dā mutane ba su sani ba tun farkon duniya
zan sa su sani."

[i] **13.33 Yisti:** Abu ne da ake sa a garin da ake yin burodi da shi domin burodin yă kumbura.

Yesu Ya Ba da Bayanin Misalin Ciyawa cikin Alkama

36 Sai Yesu ya bar taron mutanen ya shiga gida, almajiransa
kuma suka same shi suka ce masa, "Ka gaya mana abin da misalin
nan na ciyawa a gona yake nufi."
37 Sai ya amsa ya ce, "Wanda ya shuka iri mai kyau shi ne
Dan Mutum. 38 Gonar kuma ita ce duniya, iri mai kyau kuma shi
ne 'ya'yan mulkin, ciyawar kuma 'ya'yan Mugun ke nan. 39 Kuma
abokin gāban da ya shuka ciyawar, shi ne Shaiɗan. Lokacin girbin
kuwa, ƙarshen duniya ke nan. Masu girbin kuma su ne mala'iku.
40 Kamar yadda ake tara ciyawa a ƙone ta, haka zai zama a
ƙarshen duniya. 41 Dan Mutum zai aiko mala'ikunsa, za su tara
duk masu sa mutane su yi zunubi, da kuma duk masu yin mugayen
ayyuka, su fitar da su daga mulkinsa. 42 Su kuma jefa su a cikin
wuta mai zafi. A nan za su yi ta kuka suna cizon haƙoransu. 43 A
lokacin ne masu adalci za su yi haske kamar rana a cikin mulkin
Ubansu. Bari mai kunnen ji, yă ji.

Dukiyar da Take a Boye

44 "Mulkin sama kamar dukiya ne da aka ɓoye a gona, da
wani ya samu, ya sāke ɓoyewa. Saboda yawan murna ya je ya
sayar da dukan abubuwan da yake da su, ya sayi gonar.

Dutse mai Daraja wato Lu'ulu'u

45 "Har yanzu dai, mulkin sama kamar ɗan kasuwa yake mai
neman duwatsu masu daraja wato, lu'ulu'ai. 46 Da ya sami dutse
mai daraja wato, lu'ulu'u ɗaya mai daraja sosai, sai ya je ya sayar
da dukan abubuwan da yake da su, ya saye shi.

Abin Kamun Kifi

47 "Har yanzu dai, mulkin sama yana kama da abin kamun
kifi da aka jefa a teku ya kamo kifi iri dabam-dabam. 48 Da ya
cika, aka jawo shi gefen tekun, aka zauna, aka zaɓa kifi masu
kyau, aka sa a kwando, aka zubar da waɗanda ba su da kyau.
49 Haka zai zama a ƙarshen duniya, mala'iku za su zo su raba, su
cire mugaye daga masu adalci. 50 Su kuma jefa mugayen cikin
wuta mai zafi, inda za su yi kuka da cizon haƙora.

Sabuwa da Tsohuwar Dukiya

51 "Kun gane wannan duka?" Suka amsa suka ce, "I"

13.35: Zab 78.2.

52 Sai ya ce musu, "Saboda haka duk malamin da ya zama almajirin mulkin sama, kamar maigida yake wanda ya ɗebo sabuwa da tsohuwar dukiya daga wurin ajiyarsa."

An Ki Yesu a Nazarat
(Mar 6.1-6; Luk 4.16-30)

53 Da Yesu ya gama faɗa waɗannan misalan, sai ya bar wurin.
54 Yesu ya zo garinsa ya fara koya wa mutane a majami'unsu. Suka yi mamaki suka ce, "Ina wannan mutumin ya sami hikiman nan haka, da kuma ikon yin waɗannan ayyukan ban mamaki?
55 Wannan ba shi ne ɗan kafintan nan ba? Ba mamarsa ba ce ake ce da ita Maryamu? Ba 'yan'uwansa ba ne su Yakubu, da Yusufu, da Siman, da Yahuda?
56 Ba 'yan'uwansa mata duk tare da mu suke ba? To, daga ina ya samo duk waɗannan?"
57 Sai suka ji haushinsa. Amma Yesu ya ce musu, "Ai, kowa yana ba annabi girma amma ban da mutanen garinsa, da na gidansa."
58 Kuma bai yi abubuwan ban mamaki da yawa a can ba, saboda rashin bangaskiyarsu.

Mutuwar Yohanna Maibaftisma
(Mar 6.14-29; Luk 9.7-9)

14 1 A lokacin nan, sarki Hirudus ya ji labarin Yesu.
2 Sai ya ce wa masu yin masa aiki, "Ai wannan Yohanna Maibaftisma ne. An tashe shi daga matattu, shi ya sa yake da ikon yin waɗannan abubuwan ban mamaki."

3 Don dā ma Hirudus ya kama Yohanna ya ɗaure shi, ya sa shi a kurkuku saboda Hirudiya, matar ɗan'uwansa Filibus.
4 Don dā ma Yohanna ya yi ta gaya wa Hirudus cewa bai kamata yă zauna da ita Hirudiya ba.
5 Ko da yake Hirudus yana so yă kashe Yohanna, amma yana jin tsoron mutane, domin sun ɗauka Yohanna annabi ne.

6 To, da ranar da aka haifi Hirudus ta sāke zuwa, sai 'yar Hirudiya ta yi rawa a gaban baƙin da suka zo bikin. Ta sa Hirudus ya ji daɗi sosai
7 har ma ya yi mata alkawari tare da rantsuwa cewa, zai ba ta duk abin da ta roƙa.

8 Mamarta kuwa ta ba ta shawara game da abin da za ta ce, sai ta ce, "A ba ni kan Yohanna Maibaftisma yanzu a cikin kwano."

9 Sarki kuwa ya damu, amma saboda alkawarin da ya yi, da kuma baƙin, sai ya sa a ba ta.
10 Ya aika zuwa kurkuku aka yanke

13.57: Yoh 4.44 **14.3-4:** Luk 3.19-20 **14.4:** L. Fir 18.16; 20.21

wa Yohanna kai. 11 Aka kuwa kawo kan a cikin kwano, aka ba
yarinyar, sai ta kai wa mamarta. 12 Sai almajiran Yohanna suka
zo, suka ɗauki gawarsa suka binne. Sai suka je suka gaya wa Yesu.

Yesu Ya Ciyar da Mutum Dubu Biyar
(Mar 6.30-44; Luk 9.10-17; Yoh 6.1-14)

13 Da Yesu ya ji haka, sai ya tashi ya shiga jirgin ruwa ya
haye zuwa wani wuri inda ba kowa don yă kasance shi kaɗai.
Amma da taron mutanen suka ji haka, sai suka fito daga garuruwa
suka bi shi da ƙafa. 14 Da ya fita daga jirgin kuwa, ya ga mutane
sun taru da yawa. Sai ya ji tausayinsu, ya kuma warkar da marasa
lafiya a cikinsu.

15 Da yamma ta yi, sai almajiransa suka zo wurinsa suka ce,
"Wurin nan fa ba kowa, ga shi kuma yamma ta yi. Ka sallami
mutanen nan don su je ƙauyuka su saya wa kansu abinci."

16 Yesu ya ce musu, "Ba lallai su tafi ba, ku ba su wani abu
su ci."

17 Suka amsa suka ce, "Ba mu da kome a nan sai burodi guda
biyar da kifi guda biyu."

18 Sai ya ce, "Ku kawo mini." 19 Sai ya umarci mutanen su
zauna a kan ciyawa. Ya ɗauki burodin guda biyar da kifin biyu,
sai ya ɗaga kansa sama, ya yi godiya ga Allah. Sai ya rarraba
burodin ya ba almajiransa, almajiran kuma suka ba wa jama'a.
20 Kowa ya ci ya ƙoshi. Suka tattara duk abin da ya rage, har ya
cika kwanduna goma sha biyu. 21 Mutanen da suka ci kuwa sun
kai maza dubu biyar, ban da mata da yara.

Yesu Ya Yi Tafiya a kan Ruwa
(Mar 6.45-52; Yoh 6.15-21)

22 Suna gamawa ke nan, sai Yesu ya sa almajiransa su shiga
jirgin ruwa don su koma can gefen. Shi kuwa ya tsaya a wurin
don yă sallami jama'ar. 23 Bayan ya sallami mutanen sai ya hau
kan dutse shi kaɗai don yă yi addu'a. Har yamma ta yi sosai yana
can shi kaɗai.

24 A wannan lokacin kuwa jirgin yana tsakiyar teku, raƙuman
ruwa suna buga shi, kuma iska tana gāba da su.

25 Wajen ƙarfe uku na dare sai ga Yesu yana takawa a kan
teku zuwa wurin almajiransa. 26 Amma da almajiran suka gan shi
yana tafiya a kan teku, sai suka ji tsoro, suka ce, "Fatalwa ce!"
Suka yi ihu don tsoro.

27 Nan da nan sai Yesu ya yi musu magana ya ce, "Kada ku
damu! Ni ne, kada ku ji tsoro!"
28 Sai Bitrus ya amsa masa ya ce, "Ubangiji, idan kai ne, ka
sa in zo wurinka a kan ruwa."
29 Yesu ya ce, "Zo mana." Sa'an nan Bitrus ya fita daga jirgin,
ya fara tafiya a kan ruwa zai je wurin Yesu. 30 Amma da ya ga
iskar tana da ƙarfi, sai ya ji tsoro ya fara nutsewa. Sai ya yi ihu,
ya ce, "Ubangiji, ka cece ni!"
31 Nan da nan sai Yesu ya miƙa hannunsa ya kamo shi, ya ce
masa, "Kai mai ƙaramar bangaskiya, don me ka yi shakka?"
32 Da suka shiga jirgin sai iskar ta daina hurawa. 33 Waɗanda
suke cikin jirgin suka yi wa Yesu sujada, suna cewa, "Gaskiya,
kai Ɗan Allah ne."

Yesu Ya Warkar da Marasa Lafiya a Janisarat
(Mar 6.53-56)

34 Da suka ƙetare tekun, suka sauka a ƙasar Janisarat.
35 Mutanen garin kuwa suka gane shi, sai suka aika a faɗa wa
kowa da yake a wannan sashen ƙasar, suka kawo masa dukan
marasa lafiya. 36 Suka roƙe shi su taɓa ko da gefen rigarsa. Dukan
waɗanda suka taɓa kuwa suka warke.

Al'adar Shugabanni
(Mar 7.1-13)

15 1 Ana nan sai Farisiyawa da malaman dokoki suka zo
wurin Yesu daga Urushalima suka ce, 2 "Don me
almajiranka suke karya al'adar shugabanni? Gama ba sa wanke
hannu kafin su ci abinci."
3 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ku fa, don me kuke karya
dokokin Allah saboda al'adarku? 4 Ai, Allah ya ce, 'Ka ba wa
babanka da mamarka girma,' kuma 'Duk wanda ya zagi
babansa ko mamarsa lallai a kashe shi.' 5 Amma kukan koyar
cewa idan mutum yana da wani abu da zai taimaki babansa ko
mamarsa da shi, amma sai ya ce, 'Duk abin da dā za ku samu
a wurina, na keɓe wa Allah,' to, ba lallai ke nan yă ba wa
iyayensa girma ba. 6 Wato, saboda al'adarku, kun mai da
maganar Allah banza. 7 Ku munafukai! Daidai ne Ishaya ya yi
annabci a kanku da ya ce,
8 'Waɗannan mutane suna ba ni girma da bakinsu ne kawai,
amma zukatansu sun yi nesa da ni.

15.4: Fit 20.12; 21.17; M. Sh 5.16; L. Fir 20.9

9 A banza suke yi mini sujada;
suna koyar da dokokin mutane wai Maganar Allah ne.' "

Abubuwan da Suke Sa Mutum yă zama Marar Tsarki a gaban Allah
(Mar 7.14-23)

10 Yesu ya kira taron mutane ya ce musu, "Ku saurara ku
gane. 11 Ba abin da yake shiga bakin mutum ne yake sa shi yă
zama marar tsarki a gaban Allah ba, sai dai abin da yake fita daga
bakinsa."

12 Sai almajiran suka zo wurinsa suka ce masa, "Ka san
Farisiyawa sun ji haushi da suka ji maganan nan?"

13 Yesu ya amsa ya ce, "Duk shukin da ba Ubana na sama
ne ya shuka ba, za a tumɓuke shi. 14 Bar su kawai. Su makafi ne
masu yi wa makafi jagora. Idan kuwa makaho ya yi wa wani
makaho jagora, ai, dukansu za su fāɗi cikin rami."

15 Amma Bitrus ya ce masa, "Ka bayyana mana wannan
misalin."

16 Sai Yesu ya ce, "Ashe, har yanzu ba ku gane ba? 17 Ina
nufin duk abin da mutum ya ci, da farko zai shiga bakinsa,
sa'an nan zai shiga cikinsa, kuma daga ƙarshe zai fita daga
jikinsa. 18 Amma abin da yake fitowa daga baki, daga zuciya
yake fitowa. Shi ne kuwa yake sa mutum yă zama marar tsarki
a gaban Allah da mutum. 19 Gama daga zuciya ne mugayen
tunani suke fitowa. Wato, su kisankai, zina, lalata, sata, shaidar
ƙarya, da ɓata sunan waɗansu. 20 Waɗannan suke sa mutum yă
zama marar tsarki a gaban Allah, amma cin abinci da hannun
da ba a wanke ba ba ya sa mutum yă zama marar tsarki a gaban
Allah ba."

Bangaskiyar Wata Mace
(Mar 7.24-30)

21 Yesu ya bar wurin ke nan ya tafi yankin ƙasar Taya da
Sidon, 22 sai ga wata 'yar Kan'ana mutuniyar ƙasar, ta zo ta ɗaga
murya ta ce, "Ka ji tausayina, Ubangiji, Ɗan Dawuda. Wani aljani
yana ba 'yata wahala."

23 Yesu bai ce mata kome ba. Sai almajiransa suka zo suka
roƙe shi, suka ce, "Ka kore ta! Domin tana binmu tana damunmu
da ihu!"

15.8-9: Ish 29.13 **15.14:** Luk 6.39 **15.18:** Mat 12.34

24 Ya amsa ya ce, "An aiko ni ne domin tumakin Isra'ila da
suka ɓata ba don waɗansu ba."
25 Amma ta zo ta durƙusa a gabansa, ta ce, "Ubangiji, ka
taimake ni."
26 Ya amsa ya ce, "Ba zai yi kyau a ɗauki abincin yara a ba
karnuka ba."
27 Ta ce, "I, Ubangiji, amma ko karnuka[j] ma sukan lashe
sauran abinci da yake fāɗuwa daga teburin masu gidan."
28 Sai Yesu ya amsa mata ya ce, "Uwargida, bangaskiyarki
tana da yawa, bari bukatarki ta biya." Nan take 'yarta ta warke.

Yesu Ya Warkar da Mutane da Yawa

29 Daga wurin Yesu ya bi ta gefen Tekun Galili. Sa'an nan
ya hau dutse ya zauna. 30 Mutane da yawa suka zo wurinsa. Suka
zo da guragu, da makafi, da masu dungu, da bebaye, da waɗansu
da yawa, suka ajiye su a gabansa. Ya kuwa warkar da su. 31 Har
mutane suka yi mamaki da suka ga bebaye suna magana, masu
dungu kuma gaɓoɓinsu suna aiki, guragu suna tafiya, makafi
kuma suna gani. Sai duk suka yi wa Allah na Isra'ila yabo.

Yesu Ya Ciyar da Mutum Dubu Huɗu
(Mar 8.1-10)

32 Ana nan sai Yesu ya kira almajiransa ya ce, "Ina jin
tausayin jama'an nan, don yau kwana uku ke nan suna tare da
ni, kuma ba su da abinci. Ba na so in sallame su da yunwa, don
za su iya suma a hanya."
33 Sai almajiran suka ce masa, "A wannan wurin da ba kowa,
ina za mu sami burodi da zai isa mu ciyar da wannan jama'a?"
34 Yesu ya tambaye su ya ce, "Burodi nawa kuke da shi?"
Suka ce, "Guda bakwai da ƙananan kifaye kaɗan."
35 Sai ya sa taron mutanen su zauna a ƙasa, 36 ya ɗauki burodin
nan bakwai da kifayen. Da ya yi godiya ga Allah, sai ya rarraba
su, ya ba almajiran, almajiran suka ba wa taron mutanen. 37 Kowa
ya ci ya ƙoshi, almajiran kuwa suka tara ragowar abincin, cike
da kwanduna bakwai. 38 Mutanen da suka ci kuwa sun kai maza
dubu huɗu, ban da mata da yara. 39 Bayan ya sallami taron
mutanen sai ya shiga jirgin ruwa ya tafi ƙasar Magadan.

[j] **15.27 karnuka:** Duk wanda ba Bayahude ba, Yahudawa sukan ɗauke shi kamar kare.

Neman Alama
(Mar 8.11-13; Luk 12.54-56)

16 [1] Farisiyawa da Sadukiyawa suka zo wurin Yesu don su gwada shi, suka roƙe shi yă nuna musu wani abin ban mamaki da zai zama musu alama. [2] Ya amsa musu ya ce, "Idan yamma ta yi, kuka ga sama ta yi ja, sai ku ce, 'Yawwa, gari zai yi kyau gobe.' [3] Da safe kuma idan kuka ga sama ta yi ja, ta ɓata fuska, sai ku ce, 'Yau kam za a yi ruwan sama.' Kuna iya gane yanayin sararin sama, amma ba kwa iya gane alamun wannan zamanin.[k] [4] Mutanen zamanin nan mugaye ne, waɗanda ba sa tsoron Allah. Suna so su ga alama, amma ba za a nuna musu wata alama ba, sai dai ta Jona."

Sai ya bar su ya tafi.

Yistin Farisiyawa da Sadukiyawa
(Mar 8.14-21)

5 Da almajiran suka kai wancan gefen, ashe, sun manta ba su kawo burodi ba. [6] Sai Yesu ya ce musu, "Ku kula fa, kuma ku yi hankali da yistin Farisiyawa da Sadukiyawa."

7 Sai suka fara magana da junansu suna cewa, "Ko saboda ba mu kawo burodi ba ne?"

8 Da Yesu ya ga haka sai ya ce, "Ku masu ƙaramar bangaskiya, don me kuke cewa ba ku da burodi? [9] Har yanzu ba ku gane ba? Kun manta yadda na ciyar da mutum dubu biyar da burodi biyar? Kuma kwanduna nawa kuka tara? [10] Ko kuma lokacin da na ciyar da mutum dubu huɗu da burodi bakwai, kwanduna nawa kuka tara? [11] Yaya kuka kāsa gane cewa ba burodi nake magana a kai ba? Na ce ku yi hankali da yistin Farisiyawa da Sadukiyawa."

12 Sa'an nan ne almajiran suka gane cewa ba yana ce musu su yi hankali da yistin da ake sa a cikin burodi ba ne, amma yana nufin su yi hankali da koyarwar Farisiyawa da Sadukiyawa ne.

Bitrus Ya Shaida Yesu Shi Ne Almasihu
(Mar 8.27-30; Luk 9.18-21)

13 To, da Yesu ya zo ƙasar Kaisariya Filibi, sai ya tambayi almajiransa ya ce, "Wa mutane suke cewa Dan Mutum yake?"

16.1: Mat 12.38; Luk 11.16 **16.4:** Mat 12.39; Luk 11.29 **16.6:** Luk 12.1
16.9: Mat 14.17-21 **16.10:** Mat 15.34-38

[k] **16.2-3** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da aya biyu da kuma aya uku gaba ɗaya.

14 Sai suka ce, "Waɗansu suna cewa Yohanna Maibaftisma,
waɗansu kuma Iliya, waɗansu kuma Irmiya, ko kuma ɗaya daga
cikin annabawa."
15 Ya ce musu, "Amma ku fa, wane ne ni a ganinku?"
16 Sai Siman Bitrus ya amsa ya ce, "Kai ne Almasihu, Ɗan
Allah mai rai."
17 Sai Yesu ya amsa masa ya ce, "Kai mai albarka ne Siman,
ɗan Jona! Gama ba mutum ba ne ya nuna maka wannan, sai dai
Ubana da yake cikin sama. 18 Ina kuma gaya maka, kai Bitrus ne,
a kan wannan dutsen kuma zan gina jama'ar masu bina, wacce
mutuwa ma ba ta da iko a kanta. 19 Zan ba ka mabuɗan mulkin
sama. Kuma kome ka ɗaure a duniya, za a ɗaure shi a sama,
kome ka kunce a duniya, za a kunce shi a sama." 20 Sai ya ja wa
almajiransa kunne sosai kada su gaya wa kowa cewa shi ne
Almasihu.

Yesu Ya Faɗa Irin Mutuwar da Zai Yi

(Mar 8.31—9.1; Luk 9.22-27)

21 Tun daga wannan lokacin Yesu ya fara nuna wa almajiransa
cewa, dole ne yă je Urushalima, yă sha wuya iri-iri a hannun
shugabanni, da manyan firistoci, da malaman dokoki, a kuma
kashe shi, a rana ta uku kuma yă tashi.
22 Sai Bitrus ya ja shi gefe ɗaya ya fara tsawata masa yana
cewa, "Allah yă sawwaƙe, Ubangiji! Wannan ba zai taɓa faruwa
da kai ba."
23 Amma Yesu ya juya ya ce masa, "Ka rabu da ni, kai
Shaiɗan! Kai mai sa tuntuɓe ne a gare ni, gama kana tunani kamar
mutum ne, ba kamar Allah ba."
24 Sai Yesu ya ce wa almajiransa, "Duk mai so yă bi ni, sai
yă ƙi kansa, yă ɗauki gicciyensa yă bi ni. 25 Gama duk mai son
ajiyar ransa zai rasa shi. Amma duk wanda ya rasa ransa saboda
ni, zai same shi. 26 Wane amfani ne mutum zai samu, idan ya
sami duniya duka, amma ya rasa ransa? Ko kuwa me mutum zai
iya bayar a maimakon ransa? 27 Ɗan Mutum dai zai zo da
mala'ikunsa, cikin ɗaukakar Ubansa, sa'an nan ne zai biya
kowane mutum bisa ga aikinsa. 28 Gaskiya ina gaya muku, akwai
waɗansu a tsaye a nan da ba za su mutu ba, har sai sun ga zuwan
Ɗan Mutum cikin mulkinsa."

16.14: Mat 14.1-2; Mar 6.14-15; Luk 9.7-8 **16.16:** Yoh 6.68-69
16.19: Mat 18.18; Yoh 20.23 **16.24:** Mat 10.38; Luk 14.27
16.25: Mat 10.39; Luk 17.33; Yoh 12.25 **16.27:** Mat 25.31; Zab 62.13; Rom 2.6

Sākewar Kamannin Yesu
(Mar 9.2-13; Luk 9.28-36)

17 [1] Bayan kwana shida Yesu ya ɗauki Bitrus, da Yakubu, da ɗan'uwan Yakubu, wato Yohanna, ya kai su kan wani dutse mai tsawo, inda suka kasance su kaɗai. [2] Sai kamanninsa ya sāke a gabansu, fuskarsa ta yi haske kamar rana, sai rigunar da ya sa suka yi fari fat. [3] Nan da nan sai annabi Musa da annabi Iliya suka bayyana a gare su, suna magana da Yesu.

4 Sai Bitrus ya ce wa Yesu, "Ubangiji, ya yi kyau da muke a nan wurin. Idan kana so zan kafa bukkoki guda uku a nan, ɗaya dominka, ɗaya domin annabi Musa, ɗaya kuma domin annabi Iliya."

5 Yana magana ke nan sai ga wani girgije mai haske ya rufe su, aka kuma ji wata murya daga cikin girgijen ta ce, "Wannan shi ne Ɗana, wanda nake ƙauna; ina jin daɗinsa ƙwarai. Ku saurare shi!"

6 Da almajiran suka ji haka sai tsoro ya kama su sosai, har suka fāɗi ƙasa. [7] Sai Yesu ya zo ya taɓa su ya ce, "Ku tashi, kada ku ji tsoro." [8] Da suka ɗaga kai, ba su ga kowa ba sai Yesu shi kaɗai.

9 Da suke saukowa daga dutsen, Yesu ya ja musu kunne ya ce, "Kada ku gaya wa kowa abin da kuka gani, sai Ɗan Mutum ya tashi daga matattu."

10 Almajiran suka tambaye shi suka ce, "To, don me malaman dokoki suke cewa dole sai annabi Iliya ya fara zuwa?"

11 Ya amsa ya ce, "Lallai Iliya zai zo, zai kuma gyara kome. [12] Amma ina gaya muku, Iliya ya riga ya zo, ba su kuwa gane shi ba, har ma suka yi masa abin da suka ga dama. Haka kuma Ɗan Mutum zai sha wuya a hannunsu."

13 Sai almajiran suka gane cewa yana yi musu magana a kan Yohanna Maibaftisma ne.

Yesu Ya Warkar da Yaro mai Aljani
(Mar 9.14-29; Luk 9.37-43a)

14 Da suka ƙai wajen taron jama'a, sai wani mutum ya zo wurin Yesu ya durƙusa a gabansa ya ce, [15] "Ubangiji, ka ji tausayin ɗana, yana farfaɗiya, kuma yana shan wuya sosai. Sau

---

17.1-5: 2 Bit 1.17-18
17.5: Far 22.2; M. Sh 18.15; Zab 2.7; Ish 42.1; Mat 3.17; 12.18; Mar 1.11; Luk 3.22
17.10: Mal 2.23 **17.12:** Mat 11.14

da yawa yakan fādī cikin wuta, da kuma cikin ruwa. 16 Na kuwa
kai shi wurin almajiranka, amma ba su iya warkar da shi ba."
17 Sai Yesu ya amsa ya ce, "Ku mutanen zamanin nan,
marasa bangaskiya, masu taurin kai, har zuwa yaushe zan zauna
tare da ku? Har zuwa yaushe zan jimre muku? Ku kawo mini
shi nan." 18 Sai Yesu ya tsawata wa aljanin, aljanin kuwa ya
bar yaron. Nan take yaron ya warke.
19 Sai almajiran suka zo wurin Yesu a lokacin da ba kowa
tare da shi, suka ce masa, "Don me mu muka kāsa fitar da
aljanin?"
20 Yesu ya ce musu, "Saboda bangaskiyarku ƙarama ce.
Gaskiya ina gaya muku, idan kuna da bangaskiya da ta kai ko da
misalin ƙwayar mastad, wadda ta fi ƙankanta cikin iri duka, za
ku iya ce wa dutsen nan ya tashi daga nan zuwa can, kuma zai
tashi dīn. Ba kuwa abin da zai gagare ku."*l*

Yesu Ya Sāke Yin Magana game da Mutuwarsa
(Mar 9.30-32; Luk 9.43b-45)

22 Da almajiran suka sadu a ƙasar Galili, sai Yesu ya ce
musu, "Za a ba da Dan Mutum ga hannun mutane, 23 za su
kuma kashe shi. A rana ta uku kuma za a tashe shi." Sai
almajiran suka damu sosai.

Biyan Harajin Haikali

24 Da Yesu da almajiransa suka isa Kafarnahum, masu karɓar
haraji don haikali suka sami Bitrus suka ce masa, "Malaminku
ba ya biyan harajin haikali ne?"
25 Ya ce, "Yana biya mana." Da Bitrus ya dawo gida, sai
Yesu ya fara yi masa magana ya ce, "Me ka gani game da wannan
tambayar? Daga wurin wa sarakuna suke karɓar kudīn haraji,
daga wurin 'ya'yansu, ko daga wurin waɗansu?"
26 Da Bitrus ya ce, "Daga wurin waɗansu," sai Yesu ya ce,
"Wato, 'ya'yansu ba sa biya ke nan. 27 Duk da haka, don kada
mutanen nan su ji haushinmu, ka je teku ka jefa ƙugiya, ka buɗe
bakin kifin da ka fara kamawa, za ka sami azurfa da zai isa, sai
ka ɗauki azurfa dīn ka biya harajinka da nawa."

17.20: Mat 21.21; Mar 11.23; 1 Kor 13.2 **17.24**: Fit 30.13; 38.26
l **17.20** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya ta 21 haka: Ai, irin wannan baya fita sai da addu'a da azumi.

Wa Ya Fi Girma?
(Mar 9.33-37; Luk 9.46-48)

18 [1] A lokacin nan almajiran suka zo wurin Yesu, suka tambaye
shi, suka ce, "Wa ya fi girma duka a cikin mulkin sama?"
2 Sai ya kira wani ƙaramin yaro, ya sa shi a tsakiyarsu, [3] ya
ce, "Gaskiya ina gaya muku, idan ba kun sāke, kun zama kamar
ƙananan yara ba, ba za ku taɓa shiga mulkin sama ba. [4] Duk
wanda ya ɗauki kansa ba a bakin kome ba kamar ƙaramin yaron
nan, shi ne ya fi girma a mulkin sama. [5] Duk wanda ya karɓi
ƙaramin yaro kamar wannan saboda ni, ni ya karɓa.

Abubuwa Masu Sa Tuntuɓe
(Mar 9.42-48; Luk 17.1-2)

6 "Kuma duk wanda ya sa ɗaya daga cikin yaran nan da suka
gaskata da ni, ya yi zunubi, zai fi wa mutumin a rataya babban
dutsen niƙa a wuyansa, a kuma jefa shi a teku mai zurfi. [7] Kaiton
duniya saboda dalilan yin zunubi, dole ne dalilan yin zunubi su
zo, amma kaiton wanda shi ne dalilin.
8 "Idan kuwa hannunka, ko ƙafarka yana sa ka ka yi zunubi,
ka yanke shi ka yar. Zai fi maka ka shiga rai na har abada da
hannu ko ƙafa ɗaya, ko gurgu, da a jefa ka cikin wutar da ba ta
taɓa mutuwa, da hannaye biyu ko ƙafafu biyu. [9] Idan kuma idonka
yana sa ka ka yi zunubi, sai ka cire shi ka yar; zai fi maka ka
shiga rai na har abada da ido ɗaya, da a jefa ka cikin wutar da
ba ta taɓa mutuwa da idanu biyu.

Misali na Tunkiyar da Ta Bace
(Luk 15.3-7)

10 "Ku kula, kada ku rena ko ɗaya daga cikin waɗannan yaran,
gama ina faɗa muku, mala'ikunsu a sama kullum suna duban
fuskar Ubana da yake cikin sama. [m]
12 "Me kuke tsammani, idan makiyayi yana da tumaki guda
ɗari, sai ɗaya daga cikinsu ta ɓata, ba zai bar sauran casa'in da
taran a gindin dutse suna kiwo yă je neman ɗayarsu da ta ɓata
ba? [13] Kuma idan ya same ta, gaskiya ina faɗa muku, murnar da
yake yi a kanta, ya fi na casa'in da taran da ba su ɓata ba. [14] Haka
ma, ba nufin Ubanku da yake cikin sama ba ne ɗaya daga cikin
yaran nan yă ɓata.

18.1: Luk 22.24 **18.3:** Mar 10.15; Luk 18.17 **18.8:** Mat 5.30 **18.9:** Mat 5.29
[m] **18.10** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya ta 11 haka: Gama
ɗan Mutum ya zo ne yă ceci waɗanda suka ɓace (Luk 19.10).

Idan Ɗan'uwa Ya Yi Laifi
(Luk 17.3)

15 "Idan ɗan'uwanka ya yi maka[n] laifi, ka je ka nuna masa
ya yi maka laifi, kai da shi kaɗai. Idan ɗan'uwan ya saurare ka,
ka sāke maido da ɗan'uwanka ke nan. 16 Amma idan bai saurare
ka ba, sai ka sāke zuwa wurinsa tare da mutum ɗaya ko biyu don
a tabbatar da kowace magana daga bakin shaidu biyu ko uku.
17 Idan ɗan'uwan ya ƙi sauraronsu, sai ka faɗa wa jama'ar masu
bi, idan kuma har ya ƙi saurari jama'ar masu bi, ka mai da shi
kamar wanda bai san Allah ba, ko mai zunubi wanda ya ƙi tuba.

18 "Gaskiya ina gaya muku, duk abin da kuka ɗaure a duniya,
za a ɗaure shi a cikin sama. Kome kuma kuka kunce a duniya za
a kunce shi a cikin sama.

19 "Ina sāke gaya muku, idan mutum biyu daga cikinku a
duniya suka yarda su roƙi wani abu, Ubana wanda yake cikin
sama zai yi musu. 20 Gama duk inda mutum biyu ko uku suka
taru cikin sunana, ina tare da su."

Misali na Wakili wanda Ba Ya Yafewa

21 Ana nan sai Bitrus ya zo ya ce wa Yesu, "Ubangiji, sau
nawa ɗan'uwana zai yi mini laifi in yafe masa? Sau bakwai?"

22 Yesu ya ce masa, "Ba sau bakwai ba, amma dai bakwai
sau saba'in.[o] 23 Saboda haka, za a kwatanta mulkin sama da wani
sarkin da yake so ya ƙirga dukiyarsa da take hannun wakilansa.
24 Da sarkin ya fara ƙirgawa, sai aka kawo masa wani mutum
wanda yake bin bashin azurfa wanda mutumin ba zai iya biya a
duk rayuwarsa ba. 25 Da ya kāsa biya, sai sarkin ya sa a sayar da
shi da matarsa da 'ya'yansa da duk abin da yake da shi don a
biya kuɗin. 26 Sai wakilin ya durƙusa a gabansa yana roƙo ya ce,
'Ka yi haƙuri, zan biya ka kome.' 27 Sai sarkin ya ji tausayin
wakilin, ya sake shi, ya yafe masa bashin.

28 "Amma wannan wakilin daga fitarsa, sai ya tarar da wani
abokin aikinsa da yake bin bashin azurfa kaɗan kawai, ya shaƙe
masa wuya ya ce, 'Ka biya ni abin da nake binka.' 29 Sai abokin
aikinsa ya durƙusa ya roƙe shi ya ce, 'Ka yi mini haƙuri, zan biya
ka.' 30 Amma wakilin ya ƙi, ya kuma je ya sa shi a kurkuku, har

18.15: Luk 17.3 **18.16:** M. Sh 19.15 **18.18:** Mat 16.19; Yoh 20.23
18.21-22: Luk 17.3-4

[n] **18.15 maka:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da wannan kalmar.

[o] **18.22 bakwai sau saba'in:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "Sau saba'in da bakwai," wato, ba iyaka ke nan.

sai ya biya bashin. 31 Da abokan aikinsa suka ji abin da ya faru,
sai ba su ji dadî ba. Sai suka je suka faɗa wa sarkin duk abin da
ya faru. 32 Sai sarkin kuwa ya kira wakilin ya ce masa, 'Kai
mugun wakili ne. Na yafe maka duk bashin nan don ka roƙe ni.
33 Ashe, bai kamata ka ji tausayin abokin aikinka kamar yadda na
ji tausayinka ba?' 34 Sarkin ya ji haushi sosai, ya sa a ba shi wuya
har sai ya biya dukan bashin. 35 Haka kuwa Ubana da yake cikin
sama zai yi wa kowannenku da ya ƙi yafe wa ɗan'uwansa da
zuciya ɗaya."

Koyarwar Yesu a kan Kashen Aure
(Mar 10.1-12)

19 1 Da Yesu ya gama faɗin waɗannan abubuwa, ya bar ƙasar
Galili ya shiga yankin Yahudiya, wanda yake a ƙetaren
Kogin Urdun. 2 Mutane da yawa suka bi shi, ya kuwa warkar da
masu ciwo a can.

3 A nan, waɗansu Farisiyawa suka zo wurinsa don su gwada
shi, sai suka tambaye shi suka ce, "Bisa ga dokarmu daidai ne
mutum ya saki matarsa a kan kowane irin dalili?"

4 Ya amsa musu ya ce, "Ashe, ba ku karanta ba cewa, shi
Mahaliccin da ya yi su tun farko 'ya yi su ne namiji da ta
mace?' Ya kuma ce, 5 'Don haka fa, mutum zai bar babansa da
mamarsa ya manne wa matarsa, su biyun kuma su zama ɗaya.'
6 Har nan gaba ba za su zama mutum biyu ba, sai dai su zama
kamar mutum ɗaya. Saboda haka, abin da Allah ya haɗa, kada
wani yă raba."

7 Sai suka ce masa, "To, don me annabi Musa ya yi doka a
ba da takardar kashe aure, a kuma saki matar?"

8 Sai Yesu ya ce musu, "Don kuna da taurin zuciya shi ya sa
Musa ya yarda muku ku saki matanku, amma daga farko ba haka
ba ne. 9 Ina kuma gaya muku, duk wanda ya saki matarsa, idan
dai ba saboda an same ta da yin zina ba, ya kuma auri wata, ya
yi zina."

10 Sai almajiran suka ce masa, "Idan haka ne yake tsakanin
mutum da matarsa, ashe ma rashin aure ya fi."

11 Amma ya ce musu, "Ba kowa ne zai iya ɗauka maganan
nan ba sai dai waɗanda Allah ya yarda musu. 12 Akwai waɗanda
aka haifa da ba za su iya yin aure ba. Akwai waɗanda mutane ne
suka mai da su haka. Akwai kuma waɗanda suka yarda ba za su

19.4: Far 1.27; 5.2. 19.5: Far 2.24 19.7: M. Sh 24.1-4; Mat 5.31
19.9: Mat 5.32; 1 Kor 7.10-11

yi aure ba domin ƙaunar mulkin sama. Duk mai iya ɗaukar maganan nan yă ɗauka."

Yesu Ya Sa wa 'yan Yara Albarka
(Mar 10.13-16; Luk 18.15-17)

13 Sa'an nan aka kawo wa Yesu yara ƙanana don yă sa musu albarka, yă kuma yi musu addu'a, amma almajiransa suka tsawata wa waɗanda suka kawo yaran. 14 Amma Yesu ya ce musu, "Ku bar yara ƙanana su zo wurina. Kada ku hana su, gama mulkin sama na irinsu ne."

15 Sai ya sa musu hannu albarka, sa'an nan ya tafi.

Saurayi Mai Dukiya
(Mar 10.17-31; Luk 18.18-30)

16 Ana nan sai wani ya zo wurin Yesu ya ce, "Malam, wane abu mai kyau ne zan yi domin in sami rai na har abada?"

17 Yesu ya ce masa, "Don me kake tambayata a kan abin da yake da kyau? Ai, ba mai kyau sai Allah kaɗai. Idan kuwa kana so ka sami rai na har abada, sai ka kiyaye waɗannan dokoki."

18 Sai ya ce wa Yesu, "Waɗanne dokoki?" Sai Yesu ya ce, "Kada ka yi kisankai, kada ka yi zina, kada ka yi sata, kada ka yi shaidar ƙarya, 19 ka ba da girma ga babanka da mamarka. Ka kuma ƙaunaci abokin zamanka kamar yadda kake ƙaunar kanka."

20 Sai saurayin ya ce masa, "Ai, na kiyaye waɗannan duka, me ya rage mini?"

21 Yesu ya ce masa, "Idan kana so ka zama cikakke, ka je ka sayar da duk abin da kake da shi, ka ba talakawa kuɗin, za ka sami lada a sama. Sa'an nan ka zo ka bi ni."

22 Da saurayin ya ji haka, sai ya tafi yana baƙin ciki, don yana da arziki sosai.

23 Sai Yesu ya ce wa almajiransa, "Gaskiya ina gaya muku, zai zama da wuya mai arziki ya shiga mulkin sama. 24 Ina sāke gaya muku. Zai fi wa raƙumi sauƙi ya bi ta ramin allura, da mai arziki yă shiga mulkin Allah."

25 Da almajiran suka ji haka sai suka yi mamaki sosai, suka ce, "Idan haka ne, to, wa zai sami ceto?" 26 Amma Yesu ya dube su ya ce, "Ga mutane kam, ba zai yiwu ba, amma ga Allah kowane abu mai yiwuwa ne." 27 Sai Bitrus ya ce, "Ga shi mun bar kome mun bi ka, to, me za mu samu?" 28 Yesu ya ce musu,

19.18: Fit 20.13-16; M. Sh 5.17-20 19.19: Fit 20.12; M. Sh 5.16; L. Fir 19.18
19.18-19: Fit 20.13-16; M. Sh 5.17-20; Fit 20.12; M. Sh 5.16; L. Fir 19.18

"Gaskiya ina gaya muku, a zamani mai zuwa, lokacin da Ɗan Mutum zai zauna a mulkinsa mai girma, ku da kuka bi ni, ku ne kuma za ku zauna a kujerun mulki goma sha biyu. Za ku yi sarautar kabilu goma sha biyun nan na Isra'ila. 29 Kuma duk wanda ya bar gidaje, ko 'yan'uwa maza, ko 'yan'uwa mata, ko baba, ko mama, ko yara, ko gonaki, saboda sunana, zai sami fiye da haka sau ɗari, yă kuma gāji rai na har abada. 30 Amma mutane da yawa da suke na farko, za su zama na ƙarshe, na ƙarshe kuma za su zama na farko.

Ma'aikata a Gonar Inabi

20 1 "Mulkin sama kamar wani maigida ne da ya fita da sassafe don yă yi hayar waɗanda za su yi masa aiki a gonarsa ta itatuwan inabi. 2 Da suka shirya a kan kuɗin da ake biyan ma'aikata a yini, sai ya aika su gonarsa. 3 Wajen ƙarfe tara kuma da ya fita sai ya ga waɗansu suna zaman banza kawai a bakin kasuwa, 4 sai ya ce musu, 'Ku ma ku je gonata, zan biya ku abin da ya kamata.' Sai suka tafi. 5 Da ya sāke fita da rana, da kuma wajen ƙarfe uku, ya ɗauki masu aiki. 6 Har yanzu wajen ƙarfe biyar ya sāke fita ya ga waɗansu suna tsaye ba sa yin kome, sai ya ce musu, 'Don me kuke zaman banza duk yini?' 7 Suka ce masa, 'Don ba wanda ya ba mu aikin yi.' Sai ya ce musu, 'Ku ma ku je gonata.'

8 Da yamma ta yi, sai mai gonar ya ce wa mai taimakonsa lura da aikin gonar, 'Ka kira ma'aikatan ka biya su, ka fara daga na ƙarshe zuwa na farko.' 9 Waɗanda suka je wajen ƙarfe biyar suka zo, kowannensu ya karɓi abin da ya kamata a biya shi a yini. 10 To, waɗanda suka fara zuwa sun yi tsammani za a biya su fiye da sauran, amma su ma kowannensu ya karɓi abin da ya kamata a biya shi a yini. 11 Da suka karɓa, suka yi wa maigidan gunaguni, 12 suna cewa, 'Waɗanda suka zo daga ƙarshe, aikin awa ɗaya kawai suka yi, ka mai da su daidai da mu, mu da muka yini muna aiki, ga shan rana.'

13 "Sai ya amsa wa ɗaya daga cikinsu ya ce, 'Abokina, ai, ban cuce ka ba. Ba mun shirya a kan cewa zan biya ka abin da akan biya a yini ba? 14 Ka karɓi abin da yake naka ka tafi. Ni na ga damar in biya waɗanda suka zo daga baya daidai da abin da na biya ka. 15 Ba ni da iko in yi abin da na ga dama da abin da yake nawa? Ko kana jin kishi ne don ina da kirki?'

19.28: Mat 25.31; Luk 22.30 **19.30:** Mat 20.16; Luk 13.30
20.8: L. Fir 19.13; M. Sh 24.15

16 "Haka na ƙarshe za su zama na farko, na farko kuma za
su zama na ƙarshe."

Yesu Ya Sāke Yin Magana game da Mutuwarsa
(Mar 10.32-34; Luk 18.31-34)

17 Da Yesu da almajiransa suna haurawa zuwa Urushalima,
sai Yesu ya ja su gefen hanya ya ce musu, 18 "Ga shi za mu je
Urushalima. Za a ba da Dan Mutum a hannun manyan firistoci
da malaman dokoki, za su kuma yanke masa hukuncin kisa.
19 Sa'an nan su ba da shi ga waɗanda ba Yahudawa ba, su yi
masa ba'a, su yi masa bulala, su kuma gicciye shi, a rana ta uku
kuma zai tashi."

Roƙon da Mamar Yakubu da Yohanna Ta Yi
(Mar 10.35-45)

20 Sa'an nan sai mamar 'ya'yan Zabadi ta zo wurin Yesu da
'ya'yanta, ta durƙusa a gabansa ta roƙe shi wani abu.

21 Sai ya ce mata, "Me kike so?" Ta ce masa, "Ka sa
waɗannan 'ya'yana biyu su zauna, ɗaya a damarka, ɗaya a
hagunka, a cikin mulkinka."

22 Amma Yesu, ya ce wa 'ya'yan, "Ba ku san abin da kuke
roƙo ba, za ku iya sha daga kwaf nan na wahala da zan sha?"
Suka ce masa, "Za mu iya."

23 Ya ce musu, "Lallai za ku sha daga kwaf nawa, amma
zama a damana ko haguna ba ni nake da ikon bayarwa ba. Ubana
na sama ya shirya matsayin nan don waɗanda ya zaɓa."

24 Da sauran almajiran goma suka ji haka, sai suka ji haushin
'yan'uwan nan guda biyu. 25 Amma Yesu ya kira su duka ya ce,
"Kun san yadda sarakunan waɗanda ba Yahudawa ba sukan nuna
iko a kan mutanensu, manyansu ma suna nuna wa mutanensu iko.
26 Ba zai zama haka ba a cikinku, a maimakon haka duk wanda
yake so yă zama babba a cikinku dole ne yă bauta wa sauran.
27 Kuma wanda yake so yă zama shugaba a cikinku, dole ne yă
zama bawanku. 28 Haka kuma Dan Mutum bai zo domin a bauta
masa ba, sai dai domin yă yi bauta, yă kuma ba da ransa domin
ceton mutane da yawa."

20.16: Mat 19.30; Mar 10.31; Luk 13.30 **20.25-26:** Luk 22.25-26
20.26-27: Mat 23.11; Mar 9.35; Luk 22.26

Makafi Biyu Sun Sami Ganin Gari
(Mar 10.46-52; Luk 18.35-43)

29 Da Yesu da almajiransa za su bar Jeriko, mutane da yawa
suka bi shi. 30 Sai ga wadansu makafi biyu suna zaune a gefen
hanya. Da suka ji Yesu yana wucewa, sai suka daga murya suka
ce, "Mai girma,[s] Dan Dawuda! Ka ji tausayinmu!"
31 Mutane suka yi musu fada su yi shiru. Sai ma suka kara
daga murya suka ce, "Mai girma, Dan Dawuda! Ka ji
tausayinmu!"
32 Sai Yesu ya tsaya ya ce musu, "Me kuke so in yi muku?"
33 Suka ce masa, "Mai girma, bari mu sami ganin gari."
34 Don tausayi, sai Yesu ya taba idanunsu. Nan da nan kuwa
suka fara gani, suka bi shi.

Yesu Ya Shiga Urushalima
(Mar 11.1-11; Luk 19.28-40; Yoh 12.12-19)

21 1 Da Yesu da almajiransa suka kai kauyen Betafaji kusa
da Urushalima, wajen Dutsen Itatuwan Zaitun, sai ya aiki
almajirai biyu, 2 ya ce musu, "Ku shiga kauyen nan na gabanku.
Da shigarku za ku ga wata jaka a daure, da danta. Ku kunce su
ku kawo mini. 3 Idan wani ya yi muku magana ku ce, 'Ubangiji
ne yake bukatarsu.' Zai kuwa mai da su nan da nan."
4 Wannan ya faru ne don a cika abin da annabi ya fada cewa,
5 "Ku ce wa mutanen Urushalima,
'Ga sarkinku yana zuwa wurinku,
Mai tawali'u ne.
Yana kan dan aholaki, wato, dan jaki.' "
6 Sai almajiran suka je, suka yi yadda Yesu ya ce su yi. 7 Suka
kawo jakar da danta, suka shimfida musu rigunansu, shi kuwa ya
hau ya zauna. 8 Mutane da yawa suka shimfida rigunansu a kan
hanya, wadansu kuma suka karya ganye daga itatuwa suka
shimfida a kan hanya. 9 Mutanen da suke gabansa da wadanda
suke binsa a baya suka daga murya suna cewa,
"Yabo ya tabbata ga Dan Dawuda!
Mai albarka ne shi da yake zuwa cikin sunan Ubangiji!
Yabo ya tabbata ga Allah!"
10 Da Yesu ya shiga Urushalima, duk birnin ya rude, ana ta
tambaya ana cewa, "Wane ne wannan?"

21.5: Zak 9.9 **21.9**: Zab 118.25-26

[s] **20.30 Mai girma**: Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da wannan kalma.

11 Sai mutanen da suke bin Yesu suka ce, "Ai, wannan shi
ne annabi Yesu daga Nazarat na Galili."

Yesu Ya Tsabtace Haikali
(Mar 11.15-19; Luk 19.45-48; Yoh 2.13-22)

12 Sai Yesu ya shiga haikali ya kori duk masu saye da sayarwa
a ciki, ya tutture teburori masu canjin kudi, da kujerun masu sayar
da tattabaru. 13 Ya ce musu, "A rubuce yake,

'Za a ce da gidana gidan addu'a,'
amma kun mai da shi wurin ɓuyan 'yan fashi. "

14 Sai makafi da guragu suka zo wurinsa a haikalin, ya kuwa
warkar da su. 15 Amma da manyan firistoci da malaman dokoki
suka ga abubuwan ban mamaki da ya yi, har yara suna ihu cikin
haikalin suna cewa, "Yabo ya tabbata ga Ɗan Dawuda," sai suka
ji fushi. 16 Suka ce masa, "Kana jin abin da waɗannan suke cewa
kuwa?" Yesu ya amsa ya ce, "I, ashe, ba ku taɓa karanta cikin
Maganar Allah ba cewa,

'Kai ne ka shirya 'yan yara
da jarirai su yi maka yabo?' "

17 Daga nan sai ya bar su, ya fita daga birnin, ya tafi Betani,
ya kwana a can.

Yesu Ya La'anta Itacen Ɓaure
(Mar 11.12-14, 20-24)

18 Da gari ya waye yana dawowa, sai yunwa ta kama shi.
19 Da ya ga wani itacen ɓaure a gefen hanya, sai ya je wurin
itacen, amma bai sami kome ba sai ganye. Ya ce wa itacen, "Kada
ka ƙara yin 'ya'ya har abada." Nan take kuwa itacen ya bushe.

20 Da almajiran suka ga haka, suka yi mamaki sosai. Suka ce,
"Yaya itacen ya bushe haka nan take?"

21 Yesu ya amsa musu ya ce, "Gaskiya ina faɗa muku, idan
kuna da bangaskiya, kuma ba ku yi shakka ba ko kaɗan, za ku
iya yin fiye da abin da na yi wa wannan ɓauren, har ma idan
kuka ce wa dutsen nan, 'Tashi ka fāɗa cikin teku,' zai faru. 22 Idan
kun ba da gaskiya kome kuka roƙi Allah cikin addu'a, za ku
samu."

21.13: Ish 56.7; Irm 7.11 **21.16**: Zab 8.2 **21.21**: Mat 17.20; 1 Kor 13.2

Ana Shakkar Iznin Yesu
(Mar 11.27-33; Luk 20.1-8)

23 Da Yesu ya shiga haikali, yana cikin koyarwa, sai manyan firistoci da shugabannin jama'a suka zo wurinsa suka ce, "Da wane izni kake yin abubuwan nan, kuma wa ya ba ka wannan iznin?"

24 Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Ni ma zan yi muku wata tambaya. Idan kun ba ni amsa zan faɗa muku ko da wane iko nake yin abubuwan nan. 25 Ina Yohanna ya sami iznin baftismar da ya yi, Allah ne ya ba shi ko mutum?"

Sai suka fara gardama a tsakaninsu suna cewa, "Idan muka ce daga wurin Allah ne, zai ce mana, 'To, don me ba ku gaskata shi ba?' 26 Amma idan muka ce, 'Daga wurin mutum ne', muna jin tsoron abin da mutane za su yi mana, gama kowa ya ɗauki Yohanna annabi ne." 27 Sai suka amsa wa Yesu suka ce, "Ba mu sani ba."

Sai ya ce musu, "Ni ma ba zan faɗa muku ko da wane izni nake yin abubuwan nan ba.

Misali na Mai 'Ya'ya Biyu Maza

28 "To, me kuka gani? Akwai wani mutum yana da yara biyu maza, ya je wurin na farkon ya ce, 'Dana, yau ka je ka yi aiki a gonar inabi.' 29 Sai ɗan ya ce, 'Ba zan je ba,' amma daga baya ya sāke tunani ya je. 30 Sai baban ya je wurin na biyun, ya faɗa masa abin da ya faɗa wa na farkon. Sai ɗan ya amsa ya ce, 'To, zan je, baba,' amma bai je ba. 31 Cikinsu biyun nan, wane ne ya yi abin da babansa yake so?"

Sai suka ce, "Na farkon."

Yesu kuwa ya ce musu, "Gaskiya ina gaya muku masu karɓar haraji da karuwai suna riga ku shiga mulkin sama. 32 Gama Yohanna ya zo ya nuna muku hanyar gaskiya, ba ku ba da gaskiya ba. Amma masu karɓar haraji da karuwai sun ba da gaskiya gare shi. Duk da ganin haka ma, daga baya ba ku tuba kun gaskata shi ba.

Misali a kan Masu Noma da Suka Karɓi Hayar Gonar Inabi
(Mar 12.1-12; Luk 20.9-19)

33 "To, ga wani misali kuma. Akwai wani mutum da ya yi gonar inabi, ya kewaye ta da katanga, ya haka ramin matsin

21.32: Luk 3.12; 7.29-30



Hoton gonar inabi da rumfar gadi da kuma ramin matsin 'ya'yan inabi (21.33)

'ya'yan inabi a ciki, ya kuma gina rumfa mai tsayi don yin gadi. Ya ba waɗansu manoma hayar gonar, sa'an nan ya tafi wata ƙasa.

34 Da lokacin girbi ya yi, sai ya aiki bayinsa su je wurin waɗanda suka karɓi hayar gonar su karɓo masa nasa rabon amfanin gonar. 35 Amma masu hayar suka kama bayin, suka yi wa ɗaya dūka, suka kashe ɗaya, suka kuma jejjefe ɗaya. 36 Sai ya sāke aika waɗansu bayi fiye da na farko. Masu hayar gonar suka yi musu yadda suka yi wa na farkon. 37 Daga ƙarshe sai mai gonar ya aiki ɗansa zuwa wurinsu yana cewa, 'Ba shakka za su ba ɗana girma.' 38 Amma da masu hayar suka ga ɗan sai suka ce wa junansu, 'Yawwa! Ai, wannan shi ne zai gāji gonar. Mu kashe shi, gādonsa yă zama namu!' 39 Sai suka kama shi, suka jefa shi bayan katangar gonar, suka kashe shi.

40 "To, idan mai gonan nan ya zo, me zai yi wa masu hayan nan?" 41 Sai suka ce masa, "Ai, lallai zai kakkashe mugayen nan, ya ba waɗansu hayar gonar, waɗanda za su riƙa ba shi nasa rabon amfanin gonar."

42 Yesu ya ce musu, "Ashe, ba ku taɓa karantawa a Rubutattun Maganar Allah ba?

'Dutsen da masu gini suka ƙi,
shi ne ya zama dutsen da ya fi amfani duka cikin ginin.
Wannan yin Ubangiji ne,
abin mamaki ne kuwa a idanunmu.'

21.33: Ish 5.1-2 **21.42:** Zab 118.22-23

43 "Saboda haka ina gaya muku, za a karɓe mulkin Allah daga
wurinku, a ba wa masu ba da amfani mai kyau."[t]
45 Da manyan firistoci da Farisiyawa suka ji misalan nan da
ya bayar, sai suka gane cewa yana magana a kansu ne. 46 Sun
so su kama shi, amma suna tsoron jama'a, don jama'a sun ɗauka
shi annabi ne.

Misali na Bikin Aure
(Luk 14.15-24)

22 1 Sai Yesu ya sāke yi musu magana da misali ya ce, 2"Za
a iya kwatanta mulkin sama da wani sarki da ya yi wa ɗansa
bikin aure. 3Ya aiki bayinsa su kira mutanen da aka gayyace su
bikin, amma mutanen da aka gayyato ba su zo ba. 4Ya sāke aiken
waɗansu bayin ya ce, 'Ku faɗa wa mutanen da aka gayyata cewa,
"Ga shi na shirya abinci, an yanka shanu masu ƙiba da aka ciyar
da su musamman. Duk an gama shirya kome. Ku zo bikin mana!" '
5Amma ba su kula ba. Suka tafi abinsu, wani ya tafi gonarsa, wani
ya tafi kasuwancinsa, 6Waɗansu kuma suka kama bayin suka yi
musu dūka, har suka kashe su. 7Sarkin kuwa ya yi fushi sosai. Ya
aika sojojinsa suka kakkashe masu kisankan nan, har suka ƙone
garinsu tas. 8Sa'an nan ya ce wa bayinsa, 'An gama shirin bikin,
amma waɗanda aka gayyata ba su dace ba. 9Saboda haka ku bi
titi-titi ku ce wa duk waɗanda kuka samu, su zo bikin.' 10Bayin nan
kuwa suka bi titi-titi suka tattaro duk waɗanda suka samu, na kirki
da waɗanda ba na kirki ba, har wurin bikin ya cika da baƙi.
11 "Amma da sarkin ya shigo don yă ga baƙin, sai ya ga wani
mutum bai sa rigar biki ba. 12Sai ya ce wa mutumin, 'Aboki, yaya
aka yi ka shigo nan ba tare da ka sa rigar biki ba?' Amma mutumin
ya rasa abin da zai faɗa. 13Sai sarkin ya ce wa masu yin masa
hidima, 'Ku ɗaure hannayensa da ƙafafunsa, ku jefa shi cikin mugun
duhu, inda za a yi kuka da cizon haƙora.'
14 "Ai, an kira mutane da yawa, amma kaɗan ne aka zaɓa."

Tambaya game da Biyan Haraji ga Kaisar
(Mar 12.13-17; Luk 20.20-26)

15 Ana nan sai Farisiyawa suka je suka yi shawara yadda za su
yi masa tarko cikin abin da zai faɗa. 16Sai suka aiko da almajiransu
tare da waɗansu mutanen Hirudus suka ce, "Malam, mun san kai

22.13: Mat 8.12; 25.30; Luk 13.28
[t]**21.43** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā sun ƙara aya 44: "Wanda ya fāɗi
a kan wannan dutsen zai yi kucu-kucu, kuma wanda dutsen nan ya fāɗi masa,
zai nika shi kamar gari" (dubi Luk 20.18).

mai gaskiya ne, kana kuma koyar da maganar Allah cikin gaskiya,
don mutane duk ɗaya ne a gare ka, gama ba ka kula da darajar
wani fiye da wani. 17 To, ka gaya mana, kana gani daidai ne mu
biya Kaisar wato babban sarkin Roma haraji, ko a'a?"

18 Amma don Yesu ya gane mugun nufinsu sai ya ce, "Don
me kuke gwada ni, ku munafukai? 19 Ku nuna mini kuɗin da ake
biyan harajin da shi."

Sai suka kawo masa dinari. 20 Sai ya ce musu, "Hoton nan da
sunan nan na wane ne?"

21 Suka amsa suka ce, "Na Kaisar ne." Sai Yesu ya ce musu,
"To, sai ku ba Kaisar abin da yake na Kaisar, ku kuma ba Allah
abin da yake na Allah."

22 Da suka ji haka, sai suka kama baki suna mamaki, suka
bar shi, suka tafi.

Tambaya a kan Tashin Matattu
(Mar 12.18-27; Luk 20.27-40)

23 A ranan nan kuwa, waɗansu Sadukiyawa suka zo wurin Yesu.
Su ne suke cewa wai ba tashin matattu. Suka tambaye shi, 24 suka
ce, "Malam, Musa ya ce, 'Idan mutum ya mutu ba shi da ɗa,
ɗan'uwansa yă auri matar don yă haifa wa ɗan'uwansa 'ya'ya.'
25 To, akwai waɗansu 'yan'uwa guda bakwai a cikinmu. Na farkon
ya yi aure, ya mutu bai haihu ba, ya bar wa ɗan'uwansa matarsa.
26 Haka ya faru da na biyun, da na ukun, har ya kai kan na bakwai
ɗin. 27 Daga ƙarshe, sai matar ta mutu. 28 To, a tashin matattu, matar
wa za ta zama a cikinsu? Don dukansu sun aure ta."

29 Yesu ya amsa musu ya ce, "Tunaninku ba daidai ba ne,
don ba ku san Rubutattun Maganar Allah ba, kuma ba ku san
ikon Allah ba. 30 Ai, a tashin matattu, maza ba za su yi aure ba,
mata kuma ba za a ba da su ga aure ba, sai dai za su zama kamar
mala'ikun Allah. 31 Kuma game da tashin matattu, ba ku karanta
abin da Allah ya faɗa muku ba? An rubuta cewa, 32 'Ni ne Allah
na Ibrahim, Allah na Ishaku da kuma Allah na Yakubu.' Shi
Allahn masu rai ne, ba na matattu ba."

33 Da mutane suka ji haka, sai suka yi mamakin koyarwarsa.

Doka Mafi Girma
(Mar 12.28-34; Luk 10.25-28)

34 Da Farisiyawa suka ji ya ƙure Sadukiyawa, sai suka taru.
35 Wani malamin dokoki a cikinsu ya yi wa Yesu tambaya don ya

22.23: A. M. 23.8 **22.24**: M. Sh 25.5 **22.32**: Fit 3.6

gwada shi. 36 Ya ce, "Malam, wace doka ce ta fi girma a cikin
dokoki?"
37 Yesu ya amsa masa ya ce, " 'Ka ƙaunaci Ubangiji
Allahnka da dukan zuciyarka, da dukan ranka, da dukan
hankalinka.' 38 Wannan ita ce doka ta farko, kuma mafi girma.
39 Ta biyun ma kamar ta farkon take, 'Ka ƙaunaci abokin
zamanka kamar yadda kake ƙaunar kanka.' 40 Duk sauran
dokokin da koyarwar annabawa sun rataya a kan waɗannan
dokokin biyu."

Tambaya a kan Almasihu
(Mar 12.35-37; Luk 20.41-44)

41 Da Farisiyawa suka taru wuri ɗaya, sai Yesu ya tambaye
su 42 ya ce, "Mene ne tunaninku game da Almasihu? Dan wane
ne shi?"
Sai suka ce masa, "Dan Dawuda."
43 Sai Yesu ya ce musu, "To, yaya Dawuda ta ikon Ruhu yake
ce da shi 'Ubangiji'? Dawuda ya ce,
44 'Ubangiji ya ce wa Ubangijina,
"Zauna a damana sai na sa ka a kan abokan gābanka." '
45 Idan Dawuda yana ce da Almasihu 'Ubangiji', to, yaya
Almasihu ya zama ɗansa?"
46 Ba wanda ya iya ba shi amsa. Daga ranan nan kuwa ba
wanda ya sāke yi masa tambaya.

Yesu Ya Tona Asirin Malaman Dokoki da Farisiyawa
(Mar 12.38-39; Luk 11.43,46, 20.45-47)

23 1 Da mutane suka taru da yawa tare da almajiransa, sai
Yesu ya ce musu, 2 "Malaman dokoki da Farisiyawa su
ne aka ba su ikon koyar da Dokar Musa. 3 Saboda haka ku yi
duk abin da suke koya muku, ku kuma bi, amma kada ku yi
yadda suke yi, don ba sa yin abin da suke koyarwa. 4 Sukan
ɗaura kaya masu nauyi, masu wuyar ɗauka, su sa wa mutane a
baya, amma su kansu ba sa taimaka musu ko da ɗan yatsa.
5 Suna yin ayyukansu don mutane su gani ne, suna ɗaura
manya-manyan layu na ayoyin maganar Allah a goshinsu, bakin
rigunansu kuma suna kai har ƙasa.[u]

22.37: M. Sh 6.5 **22.39:** L. Fir 19.18 **22.35-40:** Luk 10.25-28 **22.44:** Zab 110.1
23.5: Mat 6.1; Num 15.38; M. Sh 6.8

[u] **23.5 bakin rigunansu kuma suna kai har ƙasa:** Isra'ilawa sukan ƙara tsawon rigunansu daga bakin rigar don yă zama alamar kebe kansu ga Allah (Dubi L. Kid 15.37-41).

Hoton Bafarisiye da laya a goshi (23.5)

6 "Sun cika so a ba su wurin zaman manya a wurin biki, da
kuma wuraren zama masu daraja a majami'u, 7 a kuma rika gaishe
su a kasuwa, a kuma rika ce musu, 'Malam'. 8 Amma ku dai,
kada a ce muku 'Malam', don malaminku daya ne, dukanku kuwa
'yan'uwa ne. 9 Kada ku ce da kowa 'Uba' a duniya, domin Uba
daya gare ku shi ne wanda yake cikin sama. 10 Kada kuma a ce
da ku 'Shugaba', domin Shugaba daya gare ku, wato, Almasihu.
11 Wanda yake babba a cikinku sai yă bauta muku. 12 Duk wanda
yake daga kai, za a mai da shi ba kome ba. Amma duk wanda
ya mai da kansa ba kome ba, za a ba shi girma.

13 "Amma kaitonku, ku malaman dokoki da Farisiyawa,
munafukai! Kun rufe wa mutane kofar shiga mulkin sama. Ku
kanku ba ku shiga ba, kuma kuna hana masu so su shiga, damar
shiga. [w]

15 "Kaitonku malaman dokoki da Farisiyawa, munafukai!
Gama kukan ketare teku, kukan kai kasashe masu nesa don samun

23.11: Mat 20.26-27; Mar 9.35; 10.43-44; Luk 22.26 **23.12**: Luk 14.11; 18.14

[w]**23.13** Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya ta 14 haka: Kaitonku malaman dokoki da Farisiyawa, munafukai! Kukan ci kayan matan da mazansu suka mutu, sa'an nan kukan yi doguwar addu'a don a ganku. Saboda haka za a yi muku hukuncin da ya fi tsanani.

mai tuba ɗaya. Idan kuwa kuka samu, sai ku mai da shi yă fi ku muni.

16 "Kaitonku, makafin jagora! Kukan ce, 'Duk wanda ya rantse da haikali, ba damuwa, amma duk wanda ya rantse da zinariyar haikalin, dole yă yi abin da ya rantse zai yi.' 17 Ku wawayen makafi! Wanne ya fi girma, zinariyar, ko haikalin da ya tsarkake zinariyar? 18 Kukan kuma ce, 'Duk wanda ya rantse da bagade, ba damuwa, amma duk wanda ya rantse da baikon da aka sa a kan bagaden, dole sai yă yi abin da ya rantse zai yi.' 19 Ku makafi! Wanne ya fi girma, baikon, ko bagaden hadaya da yake tsarkake baikon? 20 Saboda haka duk wanda ya rantse da bagaden hadaya, ya rantse da shi da duk abin da yake kansa ke nan. 21 Duk kuma wanda ya rantse da haikalin, ya rantse da shi, da kuma wanda yake zaune a cikinsa. 22 Duk wanda kuma ya rantse da sama, ya rantse da kursiyin Allah da kuma wanda yake zaune a kan kursiyin.

23 "Kaitonku, malaman dokoki da Farisiyawa, munafukai! Kukan ba da zakkar kayan yaji na ganye amma kun ƙyale abubuwan da suka fi muhimminci a cikin dokoki, wato, gaskiya, jinƙai, da bangaskiya. Waɗannan ne ya kamata ku yi ba tare da ƙyale sauran ba. 24 Ku makafin jagora, kukan tace ɗan ƙarami ƙwaro, amma kukan hadiye rakumi!

25 "Kaitonku, malaman dokoki da Farisiyawa, munafukai! Kukan wanke bayan kwaf da kwano, amma a ciki suna cike da ayyuka marasa kyau na cuce-cuce da sonkai. 26 Kai makahon Bafarisiye! Sai ka fara wanke cikin kwaf da kwano, don bayansu ma yă zama da tsabta.

27 "Kaitonku, malaman dokoki da Farisiyawa, munafukai! Kuna kamar kaburburan da aka shafa musu farin fenti, masu kyan gani daga waje, amma daga ciki sai ƙasusuwan matattu, da datti iri-iri. 28 Haka ku kuma kuke, a waje mutane sukan ga kamar ku masu adalci ne, amma daga ciki, cike kuke da munafunci da mugayen ayyuka.

29 "Kaitonku, malaman dokoki da Farisiyawa, munafukai! Gama kukan gina kaburbura masu kyau don annabawa, ku kuma yi wa kaburburan masu adalci ado. 30 Kukan ce, 'Da muna nan lokacin kakanninmu, da ba mu taimake su kashe annabawa ba.' 31 Ta haka kuka nuna cewa ku ne 'ya'yan waɗanda suka kashe annabawa. 32 To, sai ku ƙarasa mugayen ayyukan da kakanninku

23.22: Ish 66.1; Mat 5.34 **23.23:** L. Fir 27.30 **23.27:** A. M. 23.3

suka fara! 33 Ku macizai, ku 'ya'yan mugayen macizai! Yaya za
ku iya guje wa hukuncin gidan wuta? 34 Saboda haka ina aika
muku da annabawa, da masu hikima, da malaman dokoki. Za ku
kashe wadansu, ku gicciye wadansu, ku kuma yi wa wadansu
bulala a majami'unku, kuna binsu gari-gari kuna ba su wahala.
35 Zan aiko da wadannan mutane don alhakin jinin masu adalci
da aka kashe a duniya yă koma kanku, tun daga jinin Habila mai
adalci, har zuwa na Zakariya dan Berikiya, wanda kuka kashe
tsakanin Wurin Mai Tsarki da bagaden hadaya. 36 Gaskiya ina
gaya muku, duk wannan zai faru da mutanen wannan zamanin.

Yesu Ya Damu sosai a kan Urushalima
(Luk 13.34-35)

37 "Ayya Urushalima, Urushalima! Masu kashe annabawa,
masu jifar wadanda aka aiko gare ku! Sau nawa na so in tattara
ku kamar yadda kaza take tattara 'ya'yanta a cikin fukafukanta,
amma kun ki. 38 Ga shi yanzu, an bar muku gidanku ba kowa!
39 Gama ina gaya muku, ba za ku sāke ganina ba, sai ran da kuka
ce, 'Mai albarka ne wanda yake zuwa cikin sunan Ubangiji.' "

Yesu Ya Fada Irin Rushewar da Za ta Sami Haikalin
(Mar 13.1-2; Luk 21.5-6)

24 1 Da Yesu ya fita daga cikin haikali yana tafiya, sai
almajiransa suka nuna masa gine-ginen haikalin. 2 Sai ya
tambaye su ya ce, "Kun ga duk wadannan gine-ginen? Gaskiya
ina gaya muku, ba dutse ko daya da za a bari a kan wani. Duka
za a rushe."

Farkon Wahalā
(Mar 13.3-13; Luk 21.7-19)

3 Yesu yana zaune a kan Dutsen Itatuwan Zaitun sai
almajiransa suka zo wurinsa su kadai suka ce, "Fada mana,
yaushe ne wannan zai faru? Kuma mene ne alamar dawowarka,
da kuma ta karshen zamani?"

4 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ku lura fa, kada kowa yă rude
ku. 5 Gama mutane da yawa za su zo a cikin sunana, za su ce,
'Ni ne Almasihu', har su rudi mutane da yawa. 6 Za ku kuma ji
labarin yake-yake, da jita-jitarsu. Kada ku ji tsoro, don dole ne
haka yă faru, amma karshen bai zo ba tukuna. 7 Al'umma za ta

23.33: Mat 3.7; 12.34; Luk 3.7 **23.35:** Fit 4.8; 2 Tar 24.20-21 **23.38:** Irm 22.5
23.39: Zab 118.26

tasar wa al'umma, mulki yă tasar wa mulki. Za a kuma yi yunwa da girgizar ƙasa a wurare dabam-dabam. 8 Amma wannan duka masomin azaba ne kawai.

9 "Sa'an nan za su ba da ku, a ba ku wuya, su kuma kashe ku. Duniya duk za ta ƙi ku saboda sunana. 10 Sa'an nan mutane da yawa za su yi sanyi a cikin bangaskiyarsu, su ci amanar juna, su kuma ƙi juna. 11 Annabawan ƙarya kuma za su taso da yawa, su rudi mutane da yawa. 12 Saboda yawan mugunta, ƙaunar da yawancin mutane suke yi wa juna zai ragu. 13 Amma wanda ya jimre har zuwa ƙarshe, zai tsira. 14 Kuma za a ba da wannan Labari Mai Dadi na mulkin sama yă zama shaida ga dukan mutane, sa'an nan ƙarshen yă zo.

Muguwar Wahala
(Mar 13.14-23; Luk 21.20-24)

15 "Za ku ga mummunan aikin mai ban ƙyama, wanda annabi Daniyel ya faɗa, yana tsaye a Wuri Mai Tsarki (Bari mai karatu yă gane.) 16 To, sai waɗanda suke cikin Yahudiya su gudu zuwa cikin duwatsu. 17 Wanda yake kan rufin ɗaki kada ya sauko wai zai ɗauki abin da yake cikin gida. 18 Wanda yake gona kuma kada yă koma wai zai ɗauki mayafinsa. 19 Kaiton mata masu ciki, da masu goyo a wannan lokaci! 20 Ku yi addu'a kada gudun nan yă zo muku a lokacin sanyi ko Ranar Hutun Yahudawa, wato, Asabar. 21 Don a lokacin za a yi wata muguwar wahala irin wadda ba a taɓa yi ba tun farkon duniya har zuwa yanzu, ba kuwa za a sāke irinta ba. 22 Da ba don an rage kwanakin nan ba, da ba ɗan Adam da zai tsira. Amma domin waɗansu da aka zaɓa za a rage kwanakin.

23 "A lokacin nan, ko wani ya ce muku, 'Duba, ga Almasihu nan!' ko, 'Ga shi can!' Kada ku yarda. 24 Gama almasihan ƙarya, da annabawan ƙarya za su fiffito, su yi manyan alamu da abubuwan ban mamaki, don su rude mutane, har da waɗanda aka zaɓa in zai yiwu. 25 To, na dai gaya muku tun da wuri.

26 "Don haka idan aka ce muku, 'Ga shi can a daji,' kada ku fito. Idan aka ce muku, 'Yana can cikin ɗaki a ɓoye,' kada ku yarda. 27 Gama kamar yadda walƙiya take haskakawa daga gabas zuwa yamma, haka dawowar Ɗan Mutum za ta zama.

28 "Inda gawa take, ai, a nan ungulaye suke taruwa.

24.9: Mat 10.22 **24.13:** Mat 10.22 **24.15:** Dan 9.27; 11.31; 12.11
24.17-18: Luk 17.31 **24.21:** Dan 12.1; R. Yoh 7.14 **24.26-27:** Luk 17.23-24
24.28: Luk 17.37

Dawowar Dan Mutum
(Mar 13.24-27; Luk 21.25-28)

29 "Bayan tsananin wahalan nan, sai nan da nan rana ta yi
duhu, wata kuma ba zai yi haske ba. Taurari za su faffāɗi daga
sama, za a kuma girgiza manya-manyan abubuwan da suke
sararin sama. 30 Sa'an nan ne alamar Dan Mutum za ta bayyana
a sararin sama. Duk mutanen duniya kuma za su yi kuka don
tsoro. Za su ga Dan Mutum yana zuwa a cikin girgije da iko da
ɗaukaka mai yawa. 31 Zai kuwa aiko mala'ikunsa su busa ƙaho
mai ƙara sosai, su kuma tattaro waɗanda aka zaɓa daga gabas da
yamma da kudu da arewa, wato, daga wannan bangon duniya
zuwa wancan.

Koyarwa a kan Itacen Ɓaure
(Mar 13.28-31; Luk 21.29-33)

32 "Ku koyi wani abu daga itacen ɓaure. Idan rassansa sun
fara sākewa, suna fitar da sabon ganye, kun san damina ta yi kusa
ke nan. 33 Haka kuma idan kuka ga duk abubuwan nan da na gaya
muku, ku san cewa lokaci ya yi kusa, yana dab da bakin ƙofa.
34 Gaskiya ina gaya muku, mutanen zamanin nan ba za su mutu
ba, sai duk abubuwan nan sun faru. 35 Sama da ƙasa za su ƙare
amma maganata ba za ta ƙare ba ko kaɗan.

Ba Wanda Ya San Ranar zuwan Almasihu
(Mar 13.32-37; Luk 17.26-30, 34-36)

36 "Amma ba wanda ya san ranar, ko a ƙarfe nawa ne da
wannan zai faru, ko mala'ikun da suke sama, ko Ɗan,[y] sai dai
Uban kaɗai. 37 Kamar yadda aka yi a zamanin Nuhu, haka
dawowar Ɗan Mutum za ta zama. 38 Kamar a lokacin nan kafin
ruwan tsufana, ana ci, ana sha, maza suna aure, ana ba da mata
ga aure, har zuwa ranar da Nuhu ya shiga jirgin. 39 Kafin su san
abin da ake ciki, ruwan tsufana ya zo ya kwashe su duka. Haka
kuwa dawowar Ɗan Mutum za ta zama. 40 A lokacin nan, mutum
biyu za su kasance a gona; za a ɗauki ɗaya, a bar ɗaya. 41 Mata
biyu za su kasance suna niƙa tare; za a ɗauki ɗaya, a bar ɗaya.

42 "Don haka sai ku zauna da shiri, don ba ku san ranar da
Ubangijinku zai dawo ba. 43 Amma ku dai sani, da maigida zai

24.29: Ish 13.10; 34.4; Ez 32.7; Jow 2.10; 3.4; 4.15; R. Yoh 6.12-13
24.30: Dan 7.13; Zak 12.10-14; R. Yoh 1.7 **24.37:** Far 6.5-8 **24.38:** Far 6.14
24.39: Far 7.6-24

[y] **23.36 ko Ɗan:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da waɗannan kalmomin.

san ko a wane lokaci ne ɓarawo zai zo da dare, da ba zai yi barci ba, kuma ba zai bari a shigar masa gida ba. 44 Don haka ku ma sai ku zauna da shiri, don a lokacin da ba ku yi tsammani ba, shi ne Dan Mutum zai zo.

Bawa mai Aminci ko marar Aminci
(Luk 12.41-48)

45 "Wane ne bawan nan mai aminci, da hikima, wanda maigidansa ya sa shi yă lura da gidansa, yake kuma ba sauran bayi abincinsu a kan lokaci? 46 Mai albarka ne bawan da maigidansa zai zo yă same shi yana yin aikinsa. 47 Gaskiya ina gaya muku, zai sa wannan bawan yă lura masa da kayansa duka. 48 Amma idan bawan mugu ne, zai kuma ce wa kansa, 'Maigidana ba zai dawo da wuri ba.' 49 Sa'an nan kuwa yă fara dūkan abokan aikinsa, yana ci, yana sha tare da masu shaye-shaye. 50 Idan ya yi haka maigidansa zai zo a ranar da bai yi tsammani ba, a kuma lokacin da bai sani ba. 51 Maigidan zai yi masa mugun dūka, yă kuma hukunta shi tare da munafukai. Nan za a yi kuka da cizon haƙora.

Misali na 'Yan Mata Goma

25 1 "Sa'an nan za a kwatanta mulkin sama kamar 'yan mata goma da suka ɗauki fitilunsu suka tafi su karɓi ango. 2 Biyar daga cikinsu wawaye ne, biyar kuma masu hikima ne. 3 Lokacin da wawayen nan suka ɗauki fitilunsu ba su riƙe mai don ƙari ba. 4 Masu hikimar kuwa sun riƙe mai don ƙari. 5 Angon kuwa bai zo da wuri ba, sai dukansu suka yi ta jin barci har barci ya kwashe su.

6 "Can da dare sosai, sai aka ji kira ana cewa, 'Ga ango! Ku fito ku karɓe shi.' 7 Sai 'yan matan nan goma suka tashi suka gyaggyara fitilunsu. 8 Sai wawayen nan suka ce wa masu hikimar, 'Ku ɗan ba mu manku kaɗan mana. Fitilunmu suna mutuwa.' 9 Amma masu hikimar suka ce musu, 'A'a, ba zai ishe mu da ku ba. Gara ku je wurin masu sayarwa ku sayo naku.' 10 Da suka tafi don su sayo man, kafin su dawo sai angon ya iso. Waɗanda suke a shirye kuwa suka shiga wurin biki da shi, aka kuma rufe ƙofa.

11 "Daga baya sai sauran 'yan matan suka zo, suka ce, 'Mai girma, Mai girma, ka buɗe mana!' 12 Amma angon ya amsa musu ya ce, 'Gaskiya ina gaya muku, ban san ku ba.' "

24.43-44: Luk 12.39-40 **25.1:** Luk 12.35 **25.11-12:** Luk 13.25

13 Don haka sai ku zauna da shiri, don ba ku san ranar, ko awar ba.

Koyarwa a kan Rikon Amana
(Luk 19.11-27)

14 "Mulkin Allah zai zama kamar mutum ne da zai yi tafiya, sai ya kira ma'aikatansa, ya raba musu dukiyarsa. 15 Ya ba daya jaka[z] biyar, daya kuma jaka biyu, ya ba wani kuma jaka guda, kowa daidai da karfinsa. Sa'an nan ya tafi. 16 Wanda ya karɓi jaka biyar din nan, nan da nan ya je ya yi kasuwanci da kudin, har ya yi ribar jaka biyar. 17 Haka ma wanda ya karɓi jaka biyu din nan, ya yi ribar jaka biyu. 18 Amma wanda ya karɓi jaka guda din nan ya je ya tona rami ya ɓoye kudin maigidansa.

19 "Da aka dade, sai maigidan ma'aikatan nan ya dawo don su ba da lissafin abin da suka yi da kudin. 20 Sai wanda ya karɓi jaka biyar din ya zo gaba ya kawo wadansu jaka biyar ya ce, 'Maigida, ka ba ni jaka biyar. Ga shi kuma na yi ribar jaka biyar.' 21 Sai maigidansa ya ce masa, 'Madalla, ma'aikacin kirki, mai aminci! Ka yi aminci a kan karamin abu. Zan ba ka aikin da ya fi wannan. Ka zo ka yi murna tare da ni.'

22 "Sai wanda ya karɓi jaka biyun nan kuma ya zo gaba, ya ce, 'Maigida, ka ba ni jaka biyu. Ga shi kuma na yi ribar jaka biyu.' 23 Sai maigidansa ya ce masa, 'Madalla, ma'aikacin kirki, mai aminci! Ka yi aminci a kan karamin abu. Zan ba ka aikin da ya fi wannan. Ka zo ka yi murna tare da ni.'

24 "Sa'an nan wanda ya karɓi jaka guda shi ma ya zo gaba ya ce, 'Maigida, na san kai kana da wuyar sha'ani, kana girbi a inda ba ka yi shuki ba. Kai kuma mai son na banza ne. 25 Shi ya sa na ji tsoro na je na tona rami na ɓoye jakarka. Karɓi abinka.' 26 Sai maigidansa ya amsa masa ya ce, 'Kai mugun ma'aikaci, mai kyuya! Ashe, ka sani ina girbi inda ban shuka ba, ni kuma mai son na banza ne? 27 Ai, da ka sa mini kudina a banki da na dawo in karɓi abina har da riba! 28 Don haka sai ku karɓi jaka gudan nan daga wurinsa ku ba wa mai jaka goman nan. 29 Gama duk wanda yake da abu, za a kara masa, har yă samu da yawa. Wanda ba shi da abu kuwa, ko dan kadan din da yake da shi ma, sai an karɓe masa. 30 Ku kuma jefa banzan nan a bakin duhu. Nan za a yi kuka da cizon hakora.'

[z] **25.15 jaka:** Da Helenanci an rubuta "Talanti" ne a nan. Talanti daya ya fi albashin lebura daya a shekara goma sha biyar.

Shari'a ta Karshe

31 "Lokacin da Dan Mutum zai zo cikin ɗaukakarsa tare da
mala'iku duka, sa'an nan ne zai zauna a maɗaukakin kujerar
mulkinsa. 32 Za a tara duk mutanen duniya a gabansa, zai
rarraba su dabam-dabam, kamar yadda mai kiwo yake raba
tumaki da awaki. 33 Zai sa tumaki a hannun damansa, awaki
kuwa a hagunsa. 34 Sa'an nan ne Sarki zai ce wa waɗanda suke
damarsa, 'Ku zo, ku da Ubana ya yi muku albarka! Ku karɓi
mulkin da Allah ya shirya muku tun farkon duniya. 35 Don da
nake jin yunwa kun ba ni abinci. Da nake jin ƙishin ruwa, kun
ba ni ruwa na sha. Ina baƙo, kuka karɓe ni. 36 Ba ni da riga,
kuka ba ni riga. Ba ni da lafiya, kuka lura da ni. Ina kurkuku,
kuka ziyarce ni.'

37 "Sa'an nan ne waɗanda suka yi abin da Allah yake so za
su amsa masa su ce, 'Ubangiji, yaushe ne muka gan ka kana jin
yunwa muka ba ka abinci? Ko kuwa kana jin ƙishin ruwa muka
ba ka ruwa ka sha? 38 Kuma yaushe ne muka gan ka baƙo muka
karɓe ka? Ko kuwa ba ka da riga muka ba ka riga? 39 Kuma
yaushe ne muka ga ba ka da lafiya ko kana kurkuku muka ziyarce
ka?' 40 Sarkin zai amsa musu yă ce, 'Gaskiya ina gaya muku, tun
da yake kun yi wa ɗaya daga cikin waɗannan 'yan'uwana mafi
ƙanƙanta, ai, kun yi mini ke nan.'

41 "Sa'an nan zai ce wa na hagunsa, 'Ku rabu da ni, ku
la'antattu, ku shiga wutar da ba za ta taɓa mutuwa ba har abada,
wadda aka shirya wa Shaiɗan da mala'ikunsa. 42 Don da nake
jin yunwa, ba ku ba ni abinci ba. Ina jin ƙishin ruwa, ba ku ba
ni ruwa na sha ba. 43 Ina baƙo, ba ku karɓe ni ba. Ba ni da riga,
ba ku ba ni riga ba. Na yi rashin lafiya, kuma ina kurkuku ba
ku ziyarce ni ba.'

44 "Sa'an nan su ma za su amsa su ce, 'Ubangiji, yaushe
muka gan ka kana jin yunwa, ko ƙishin ruwa, ko kana baƙunci,
ko ba ka da riga, ko kana rashin lafiya, ko kana kurkuku, ba
mu kula da kai ba?' 45 Sa'an nan zai amsa musu yă ce, 'Gaskiya
ina gaya muku, tun da yake ba ku yi wa ɗaya daga cikin
waɗannan mafi ƙanƙanta ba, ai, ba ku yi mini ba ke nan.'
46 Waɗannan za su shiga azaba marar ƙarewa, masu adalci kuwa
su shiga rai na har abada."

25.29: Mat 13.12; Mar 4.25; Luk 8.18 **25.30:** Mat 8.12; 22.13; Luk 13.28
25.14-30: Luk 19.11-27 **25.31:** Mat 16.27; 19.28 **25.46:** Dan 12.2

Shugabanni Sun Yi Shawara Su Kashe Yesu
(Mar 14.1-2; Luk 22.1-2; Yoh 11.45-53)

26 [1] Da Yesu ya gama fadîn wadannan abubuwa duka, sai ya ce wa almajiransa, [2] "Kun san Bikin Ketarewa ya rage sauran kwana biyu, za a kuma ba da Ɗan Mutum a gicciye shi."

3 Sai manyan firistoci da shugabannin mutane suka taru a gidan babban firist, mai suna Kayafa. [4] Suka yi shawara su kama shi a ɓoye su kashe shi. [5] Amma suka ce, "Ba dai a lokacin bikin ba, don kada mutane su ta da rikici."

An Shafa wa Yesu Man Kamshi a Betani
(Mar 14.3-9; Luk 7.37-38; Yoh 12.1-8)

6 To, da Yesu yana Betani a gidan Siman, wanda dā kuturu ne, [7] sai wata mace ta zo wurin Yesu da 'yar kwalaba na man ƙamshi mai tsada sosai. A lokacin da yake cin abinci, sai ta juye masa man a kai. [8] Amma da almajiran suka ga haka, sai suka ji haushi suka ce wa junansu, "Ai, wannan ɓarna ce. [9] Gama da an sayar da man nan da an sami kudî mai yawa an ba talakawa."

10 Amma don Yesu ya san abin da suke faɗa sai ya ce musu, "Don me kuke damun macen nan? Ai, abu mai kyau ne ta yi mini. [11] Talakawa suna tare da ku kullum, amma ba kullum ne nake tare da ku ba. [12] Zuba mini man nan da ta yi kuwa tana shirya ni ne domin binnewa. [13] Gaskiya ina gaya muku, duk inda za a yi bisharan nan, a duniya duka, za a riƙa faɗin abin da macen nan ta yi don tunawa da ita."

Yahuda Ya Yarda Ya Ba da Yesu
(Mar 14.10-11; Luk 22.3-6)

14 Sai ɗaya daga cikin sha biyun, mai suna Yahuda Iskariyoti, ya je wurin manyan firistoci, [15] ya ce, "Me za ku ba ni, idan na ba ku shi?" Suka ba shi kudîn azurfa talatin. [16] Tun daga lokacin nan ya fara neman hanyar da zai ba da Yesu.

Yesu Ya Ci Abincin Bikin Ketarewa tare da Almajiransa
(Mar 14.12-21; Luk 22.7-13, 21-23; Yoh 13.21-30)

17 To, a ranar farko ta Bikin Burodi Marar Yisti, sai almajiran suka zo wurin Yesu suka ce masa, "Ina kake so mu shirya maka ka ci Bikin Ketarewa?"[a]

26.2: Fit 12.1-27 **26.7:** Luk 7.37-38 **26.11:** M. Sh 15.11 **26.15:** Zak 11.12
[a] **26.17 Bikin Ketarewa:** Dubi ma'anar wadansu kalmomi.

18 Ya ce, "Ku je cikin gari wurin wani mutum, ku ce masa,
'Malam ya ce, lokacinsa ya yi kusa, zai ci Bikin Ketarewa a
gidanka tare da almajiransa.' "
19 Almajiran kuwa suka yi yadda Yesu ya ce su yi, suka kuma
shirya abincin Bikin Ketarewa.
20 Da yamma ta yi, sai ya zauna domin yă ci abinci tare da
almajiransa sha biyu. 21 Suna cikin cin abincin ke nan sai Yesu
ya ce musu, "Gaskiya ina gaya muku, ɗaya daga cikinku zai
bashe ni."
22 Sai suka damu sosai, suka fara tambayarsa da ɗaya-ɗaya
suna cewa, "Anya, ni ne, Ubangiji?"
23 Sai ya amsa ya ce, "Wanda yake cin abinci a kwano ɗaya
tare da ni, shi ne zai ba da ni. 24 Dan Mutum zai mutu kamar
yadda aka rubuta game da shi. Amma kaiton wanda zai ba da
Dan Mutum! Zai fiye wa mutumin nan da ma ba a haife shi ba."
25 Sai Yahuda wanda ya bashe shi ya ce, "Malam, ko ni ne?"
Yesu ya ce masa, "Kai ma ka faɗa."

Jibin Ubangiji
(Mar 14.22-26; Luk 22.14-20; 1 Kor 11.23-25)

26 Suna cikin cin abinci, sai Yesu ya ɗauki burodi, ya yi
godiya ga Allah, ya kakkarya burodin ya ba almajiransa ya ce,
"Ku karɓa ku ci, wannan jikina ne."
27 Sai ya ɗauki kwaf ɗin na ruwan inabi. Bayan ya yi godiya
ga Allah, sai ya ba su ya ce, "Dukanku ku sha. 28 Gama wannan
jinina ne na cikar alkawari, wanda za a zubar saboda mutane da
yawa, don gafarar zunubansu. 29 Ina gaya muku, ba zan ƙara shan
ruwan inabin nan ba, sai dai a ranan nan da zan sha wani sabo
tare da ku a mulkin Ubana."
30 Da Yesu da almajiransa suka rera waƙa, sai suka fita, suka
tafi Dutsen Itatuwan Zaitun.

Bitrus Zai Yi Mūsun Sanin Yesu
(Mar 14.27-31; Luk 22.31-34; Yoh 13.36-38)

31 Sai Yesu ya ce musu, "Dukanku za ku gudu ku bar ni a
daren nan, don abin da zai faru da ni, gama a rubuce yake cewa,

'Zan bugi makiyayin,
tumakin garken kuma za su watse.'

32 Amma fa bayan an tashe ni daga matattu, zan riga ku zuwa
Galili."

26.23: Zab 41.10 **26.28**: Fit 24.8; Irm 31.31-34 **26.31**: Zak 13.7

33 Sai Bitrus ya ce masa, "Ko dukansu sun gudu domin abin
da zai faru da kai, ni ba zan gudu ba sam."
34 Sai Yesu ya ce masa, "Gaskiya ina gaya maka, a daren
nan, kafin zakara ya yi cara, za ka yi mūsun sanina har sau uku."
35 Bitrus ya ce masa, "Ko za a kashe ni, ba zan yi mūsun
saninka ba."
Haka ma dukan almajiran suka ce.

Yesu Ya Yi Addu'a a Getsemani
(Mar 14.32-42; Luk 22.39-46)

36 Sa'an nan Yesu da almajiransa suka je wani wuri da ake
ce da shi Getsemani, wato, wurin matsen 'ya'yan zaitun. Ya ce
wa almajiran, "Ku zauna a nan, zan je can in yi addu'a." 37 Sai
ya tafi da Bitrus da 'ya'yan nan na Zabadi guda biyu wato,
Yakubu da Yohanna, sai ya fara baƙin ciki da damuwa sosai,
38 ya kuma ce musu, "Baƙin cikin da yake a raina zai iya kashe
ni. Ku zauna a nan, ku yi tsaro tare da ni."
39 Da ya je gaba kaɗan sai ya fāɗi da fuskarsa a ƙasa ya yi
addu'a ya ce, "Ubana, idan zai yiwu, ka ɗauke mini kwaf dīn
wahalan nan. Duk da haka dai, ba abin da nake so za a yi ba, sai
dai abin da kake so."
40 Ya dawo wurin almajiran ya same su suna barci, sai ya ce
wa Bitrus, "Ashe, ba za ku iya yin tsaro tare da ni ba ko na awa
guda? 41 Ku yi tsaro, ku kuma yi addu'a don kada ku fāɗi cikin
jaraba. Lallai ruhu ya ɗauka, amma jikin ba ƙarfī."
42 Sai ya sāke komawa sau na biyu, ya je ya yi addu'a ya ce,
"Ubana, idan wannan wahalar ba za ta wuce ba sai na sha ta,
bari a aikata nufinka." 43 Ya sāke dawowa ya same su suna barci,
don idanunsu sun cika da barci.
44 Sai ya sāke barinsu, ya je ya yi addu'a sau na uku, ya sāke
faɗa maganar da ya yi a dā. 45 Sai ya dawo wurin almajiran ya
ce musu, "Har yanzu barci kuke yi kuna hutawa? To, ga shi lokaci
ya yi da za a ba da Ɗan Mutum ga hannun masu zunubi. 46 Ku
tashi mu tafi. Ga mai bashe ni nan, ya iso."

An Kama Yesu
(Mar 14.43-50; Luk 22.47-53; Yoh 18.3-12)

47 Kafin ya rufe baki sai ga Yahuda ɗaya daga cikin sha biyun
nan, tare da taron mutane da yawa, suna riƙe da takuba, da
sanduna. Manyan firistoci da shugabanni ne suka aiko su. 48 To,

26.32: Mat 28.16

dā ma shi mai bashe shi dĩn ya riga ya ba su alama cewa, "Wanda zan rungume shi, shi ne mutumin. Ku kama shi."

49 Da zuwansa sai ya miƙe zuwa wurin Yesu ya ce masa, "Sallama dai, malam!" Sai Yahuda ya rungume shi.

50 Yesu ya ce masa, "Abokina, yi abin da ya kawo ka."

Sai mutanen suka zo suka kama Yesu suka riƙe shi. 51 Da ganin haka sai ɗaya daga cikin waɗanda suke tare da Yesu, ya zare takobinsa, ya sari bawan babban firist, ya yanke kunnensa. 52 Sai Yesu ya ce masa, "Mai da takobinka, gama duk wanda ya ɗauki takobi, takobi ne zai kashe shi. 53 Kuna tsammani ba ni da iko in nemi taimako daga wurin Ubana, kuma nan da nan yă aiko mini da mala'iku fiye da ƙungiyar sojoji goma sha biyu? 54 To, ta yaya ke nan za a cika abin da Rubutattun Maganar Allah sun faɗa cewa lallai wannan abu yă faru?"

55 A lokacin nan Yesu ya ce wa mutanen, "Kun fito ne da takuba, da sanduna ku kama ni sai ka ce ɗan fashi? Kowace rana ina zama a haikali ina yin koyarwa ba ku kama ni ba. 56 Amma duk wannan ya faru ne don a cika abin da yake cikin Littattafan annabawa."

Da jin haka dukan almajiransa suka bar shi, suka gudu.

Yesu a gaban 'Yan Majalisa

(Mar 14.53-65; Luk 22.54-55, 63-71; Yoh 18.13-14, 19-24)

57 Sai waɗanda suka kama Yesu suka kai shi wurin Kayafa, babban firist, inda malaman dokoki da shugabanni sun riga sun haɗu. 58 Amma Bitrus ya bi su daga nesa-nesa, har zuwa filin gidan babban firist. Ya shiga ya zauna da dogarawan haikalin don yă ga yadda za a gama. 59 To, manyan firistoci da 'yan majalisa, duk suka nemi shaidar ƙarya da za a yi wa Yesu don su sami damar kashe shi. 60 Amma ba su samu ba, ko da yake waɗansu da yawa sun ba da shaidar ƙarya. Daga ƙarshe waɗansu mutum biyu suka fito 61 suka ce, "Wannan mutumin ya ce wai zai iya rushe haikalin Allah, yă kuma sāke gina shi cikin kwana uku."

62 Sai babban firist ya tashi ya ce, "Ba ka da wata amsa? Shaidar da suke bayar a kanka fa?" 63 Amma Yesu ya yi shiru. Sai babban firist ya ce masa, "Na haɗa ka da Allah mai rai, ka gaya mana ko kai ne Almasihu, Ɗan Allah."

26.55: Luk 19.47; 21.37 **26.61:** Yoh 2.19

64 Yesu ya ce masa, "Yadda ka faɗa. Amma ina gaya muku,
daga yanzu za ku ga Dan Mutum zaune a hannun damar Mai
Iko, yana kuma zuwa cikin girgije na sararin sama."
65 Sai babban firist ya yage rigunansa saboda ɓacin rai ya ce,
"Wace shaida ce kuma muke nema? Kun ji ya yi wa Allah reni.
66 Me kuka gani?"
Suka amsa suka ce, "Ya isa a kashe shi!"
67 Sai suka tottofa masa miyau a fuska, suka dudduke shi,
waɗansu kuma suka mare shi, 68 suna cewa, "Yi mana annabci,
in kai Almasihu ne! Faɗa wanda ya mare ka!"

Bitrus Ya Yi Mūsun Sanin Yesu
(Mar 14.66-72; Luk 22.56-62; Yoh 18.15-18, 25-27)

69 A lokacin nan Bitrus yana zaune a cikin filin gidan, sai
wata yarinya mai aiki a gidan ta zo wurinsa ta ce masa, "Kai ma,
ai, tare kake da Yesu mutumin Galilin nan!"
70 Amma Bitrus ya yi mūsu a gabansu duka ya ce, "Ni ban
san abin da kike magana a kai ba!" 71 Da ya fito zaure, sai wata
yarinya mai aiki a gidan kuma ta gan shi, ta ce wa waɗanda
suke tsaye a wurin, "Wannan mutumin yana tare da Yesu
Banazare!"
72 Bitrus ya sāke yin mūsu har da rantsuwa yana cewa, "Ban
ma san mutumin ba."
73 An jima kaɗan sai waɗanda suke tsaye a wurin suka zo
suka ce wa Bitrus, "Ba shakka kai ma ɗayansu ne. Yadda kake
magana ya tone ka."
74 Sai ya fara la'anta kansa, yana rantsuwa, yana cewa, "Ban
ma san mutumin ba!"
Nan take zakara ya yi cara. 75 Sai Bitrus ya tuna da maganar
da Yesu ya yi masa cewa, "Kafin zakara yă yi cara, za ka yi
mūsun sanina sau uku." Sai Bitrus ya fita waje ya yi kuka mai
zafi.

Yesu a gaban Gwamna Bilatus
(Mar 15.1; Luk 23.1-2; Yoh 18.28-32)

27 1 Da gari ya waye, sai dukan manyan firistoci da
shugabannin jama'a suka yi shawara su kashe Yesu. 2 Sai
suka ɗaure shi, suka tafi da shi, suka ba da shi ga gwamna
Bilatus.

26.64: Dan 7.13 **26.65-66**: L. Fir 24.16 **26.67**: Ish 50.6

Mutuwar Yahuda
(A. M. 1.18-19)

3 Sa'ad da Yahuda wanda ya bashe shi ya ga an yanke wa
Yesu hukuncin mutuwa, sai ya yi baƙin ciki, ya dawo wurin
manyan firistoci, da shugabanni, ya mayar musu da kuɗin azurfa
talatin ɗin nan. 4 Ya ce, "Na yi zunubi da na ba da marar laifi a
kashe shi."

Amma suka ce, "Ina ruwanmu? Wannan ruwanka ne."

5 Sai ya zubar da kuɗin azurfan nan a haikali, ya fita, ya je
ya rataye kansa.

6 Amma manyan firistoci suka kwashe kuɗin suka ce, "Bai
kamata a sa kuɗin nan a wurin ajiyar kuɗin haikali ba, don kuɗin
ladan kisankai ne." 7 Sai suka yi shawara, suka sayi wani fili da
kuɗin. Ana ce da filin, Fili Mai Yin Tukwane, don wurin yă zama
wurin binne baƙi in sun mutu. 8 Don haka har wa yau ana ce da
filin, Filin Jini.

9 Ta haka aka cika abin da annabi Irmiya ya faɗa cewa, "Aka
ɗauki kuɗin azurfa talatin, kuɗin da mutanen Isra'ila suka yarda
a biya a kansa ke nan. 10 Suka sayi filin mai yin tukwane da su,
yadda Ubangiji ya umarce ni."

Bilatus Ya Yi wa Yesu Tambayoyi
(Mar 15.2-5; Luk 23.3-5; Yoh 18.33-38)

11 To, Yesu yana nan tsaye a gaban gwamna ke nan, sai
gwamnan ya tambaye shi ya ce, "Kai ne sarkin Yahudawa?" Yesu
ya ce masa,

"Kai ne ka faɗa haka." 12 Amma da manyan firistoci da
shugabanni suka zarge shi, bai ce kome ba.

13 Sai Bilatus ya ce masa, "Ba ka ji abubuwan nan da suka
zarge ka a kai ba?"

14 Amma Yesu bai amsa masa ko tambaya ɗaya ba, har
gwamna ya yi mamaki sosai.

An Yanke wa Yesu Hukuncin Mutuwa
(Mar 15.6-15; Luk 23.13-25; Yoh 18.39—19.16)

15 To, a lokacin Bikin Ketarewa kuwa, gwamna ya saba sake
wa mutane mai laifi guda ɗaya da suke so. 16 A lokacin akwai
wani sananne mai laifi, mai suna Barabbas a kurkuku. 17 Da
Yahudawa suka taru sai Bilatus ya ce musu, "Wa kuke so in sake

27.3-8: A. M. 1.18-19 **27.9-10:** Zak 11.12-13

muku? Barabbas ko kuwa Yesu da ake ce da shi Almasihu?"
18 Gama Bilatus ya sani saboda kishi ne suka ba da Yesu.

19 Da Bilatus ya zauna wurin da yake shari'a, sai matarsa ta aiko a ce masa, "Ka fita sha'anin marar laifin nan, domin yau na sha wahala sosai a mafarki a kansa."

20 To, sai manyan firistoci suka zuga jama'a su ce a saki Barabbas, a kashe Yesu. 21 Gwamnan kuwa ya sāke ce musu, "Wane ne a cikin biyun nan kuke so in sake muku?"

Sai suka ce, "Barabbas."

22 Sai Bilatus ya ce musu, "To, me zan yi da Yesu da ake ce da shi Almasihu?" Duk sai suka ce, "A gicciye shi!"

23 Bilatus ya ce, "Saboda me? Wane mugun abu ne ya yi?" Amma mutanen sun ƙara ta da murya suna cewa, "A gicciye shi!"

24 Da Bilatus ya ga ba abin da zai iya yi, kuma mutanen suna shirin ta da hankali, sai ya dĩbi ruwa ya wanke hannayensa a gaban mutane, ya ce, "Ni dai, ba ruwana da alhakin jinin[b] marar laifin nan. Wannan ruwanku ne."

25 Sai mutanen duka suka amsa suka ce, "Alhakin jininsa yă zauna a wuyanmu, mu da 'ya'yanmu!"

26 Sa'an nan ya sake musu Barabbas. Bayan ya sa aka yi wa Yesu bulala, sai ya ba da shi a gicciye shi.

Sojoji Sun Yi wa Yesu Ba'a

(Mar 15.16-20; Yoh 19.2-3)

27 Daga nan sojojin gwamna suka kai Yesu cikin fadar gwamna, suka tara sauran sojojin a kansa, 28 suka tuɓe masa kaya, suka yafa masa wata jar riga irin ta sarakuna. 29 Suka yi wani rawani na ƙaya, suka sa masa a kai, suka sa ya riƙe sanda a hannunsa na dama, sa'an nan suka durƙusa a gabansa suna yi masa ba'a suna cewa, "Ranka yă daɗe, Sarkin Yahudawa!" 30 Suka tottofa masa miyau, suka karɓi sandan suka bubbuge shi da ita a kai. 31 Da suka gama yi masa ba'a, sai suka cire masa jar rigar, suka sa masa rigunansa, suka tafi da shi don su gicciye shi.

An Gicciye Yesu

(Mar 15.21-32; Luk 23.26-43; Yoh 19.17-27)

32 Suna tafiya ke nan, sai suka gamu da wani mutumin Sayirin, mai suna Siman, suka sa shi dole yă ɗauki gicciyen Yesu.

27.24: M. Sh 21.6-9

[b] **27.24 alhakin jinin:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "jini mai adalci" ko kuwa "jinin mutumin nan mai adalci".

33 Suka kai wurin da ake ce da shi Golgota, wato, wurin ƙoƙon kai. 34 Suka ba shi ruwan inabi haɗe da wani abu mai ɗaci don yă sha, amma da ya ɗanɗana sai ya ƙi sha.

35 Da suka gicciye shi, sai suka jefa kuri'a suka raba rigunansa. 36 Bayan haka sai suka zauna a nan suna gadinsa. 37 Daidai kansa aka kafa sanarwar laifinsa cewa, "Wannan Shi Ne Yesu, Sarkin Yahudawa." 38 Aka kuma gicciye waɗansu 'yan fashi guda biyu tare da shi, ɗaya a damarsa, ɗaya a hagunsa.

39 Mutane da suke wucewa suka riƙa zaginsa suna kaɗa kai, 40 suna cewa, "Kai da za ka rushe haikali, ka kuma gina shi cikin kwana uku, ka ceci kanka mana! Idan kai Ɗan Allah ne, ka sauko daga gicciyen mana!"

41 Haka kuma manyan firistoci, da malaman dokoki, da shugabanni suka riƙa yi masa ba'a, suna cewa, 42 "Ya ceci waɗansu, ya kāsa ceton kansa. Idan shi Sarkin Isra'ila ne, bari yă sauko daga gicciyen mana, sa'an nan za mu gaskata shi. 43 Ya dogara ga Allah. Bari Allah yă cece shi yanzu, idan yana so, don ya ce wai shi Ɗan Allah ne."

44 Haka ma 'yan fashin da aka gicciye su tare, su ma suka yi masa baƙar magana.

Mutuwar Yesu

(Mar 15.33-41; Luk 23.44-49; Yoh 19.28-30)

45 Tun daga tsakar rana, duhu ya rufe ƙasar duka, har zuwa wajen ƙarfe uku na yamma. 46 Wajen ƙarfe uku kuma Yesu ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, "Eloi, Eloi, lama sabaktani?" wato, "Ya Allahna, ya Allahna, don me ka yashe ni?"

47 Da waɗansu da suke tsaye a wurin suka ji haka, sai suka ce, "Mutumin nan yana kiran Iliya ne." 48 Sai nan da nan wani ya yi gudu, ya je ya ɗauki soso, ya jiƙa shi a cikin ruwan tsami, ya soka a sanda, ya miƙa masa yă sha.

49 Amma sauran suka ce, "Ku bari mu gani, ko Iliya zai zo yă cece shi."

50 Sai Yesu ya sāke ɗaga murya da ƙarfi, sa'an nan ya saki ransa.

51 Sai labulen da yake cikin haikali[6] ya yage kashi biyu, daga sama zuwa ƙasa. Aka yi girgizar ƙasa, duwatsu suka

27.34: Zab 69.22 **27.35:** Zab 22.18 **27.39:** Zab 22.8; 109.25
27.40: Mat 26.61; Yoh 2.19 **27.43:** Zab 22.9 **27.46:** Zab 22.1 **27.48:** Zab 69.22

[6] **27.51 labulen haikali:** Wato, yadin da aka rufe ƙofar Wuri Mafi Tsarki a cikin haikali.

faffashe. 52 Aka bubbuɗe kaburbura, tsarkaka da yawa da suka
mutu suka tashi da rai 53 suka fiffito daga kaburburansu. Bayan
Yesu ya tashi daga matattu, sai suka shiga birni mai tsarki,
mutane da yawa suka gansu.

54 A lokacin da babban sojan Roma da sauran waɗanda suke
gadin Yesu suka ga girgizar ƙasa da kuma duk abin da ya faru, sai
suka ji tsoro sosai, suka ce, "Lallai, wannan Ɗan Allah ne!"

55 Akwai kuma waɗansu mata da yawa da suka bi Yesu tun
daga Galili suna yi masa hidima. Suka tsaya daga nesa suna kallon
abin da yake faruwa. 56 Cikinsu akwai Maryamu daga Magadala,
da Maryamu mamar Yakubu da Yusufu, da kuma mamar 'ya'yan
Zabadi.

Jana'izar Yesu

(Mar 15.42-47; Luk 23.50-56; Yoh 19.38-42)

57 Da yamma ta yi, sai wani mai arziki, mutumin Arimatiya,
mai suna Yusufu ya zo; shi ma almajirin Yesu ne. 58 Ya je wurin
Bilatus ya roƙa a ba shi gawar Yesu. Bilatus kuwa ya ba da umarni
a ba shi. 59 Sai Yusufu ya ɗauki gawar Yesu ya naɗe a zanen lilin
mai tsabta. 60 Ya sa shi a cikin sabon kabari nasa, wanda ya haƙa
a jikin dutse. Sai ya tura babban dutse a baƙin kabarin, ya tafi.
61 Maryamu daga Magadala, da ɗaya Maryamun suna nan zaune a
gaban kabarin.

Masu Gadin Kabarin

62 Washegari, wato, bayan Ranar Shiri, [c] sai manyan firistoci da
Farisiyawa suka taru a gaban Bilatus, 63 suka ce, "Ranka yă daɗe!
Mun tuna abin da mai ruɗin mutanen nan ya ce tun yana da rai,
wai bayan kwana uku zai tashi daga matattu. 64 Saboda haka ka sa
a yi gadin kabarin nan sosai har zuwa rana ta uku, don kada
almajiransa su je su sace gawarsa, sa'an nan su ce wa mutane ya
tashi daga matattu. Ruɗin ƙarshe fa zai fi na farkon muni."

65 Bilatus ya ce musu, "Ku ɗebi sojoji, ku je ku yi gadin shi
duk yadda za ku iya."

66 Sai suka je suka tsare kabarin, suka buga hatimin sarki a
dutsen kabarin, suka kuma sa sojoji su yi gadin wurin.

27.51: Fit 26.31-33 **27.55-56:** Luk 8.2-3
27.63: Mat 16.21; 17.23; 20.19; Mar 8.31; 9.31; 10.33-34; Luk 9.22; 18.31-33
[c] **27.62 Ranar Sbiri:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

Tashin Yesu daga Matattu
(Mar 16.1-8; Luk 24.1-12; Yoh 20.1-10)

28 [1] Ranar Hutu ta Yahudawa ta wuce ke nan, a ranar Lahadi da sassafe sai Maryamu daga Magadala da ɗaya Maryamu suka je su duba kabarin. [2] Ba labari sai aka yi wata babbar girgizar ƙasa, don wani mala'ikan Allah ya sauko daga sama, ya ture dutsen da aka rufe kabarin, ya zauna a kai. [3] Yana haske kamar walƙiya, rigunansa kuma farare fat kamar auduga. [4] Da masu gadin suka gan shi, tsoro ya kama su sosai, suna rawar jiki, suka fāɗi a ƙasa kamar matattu.

5 Amma mala'ikan ya ce wa matan, "Kada ku ji tsoro, na sani kuna neman Yesu ne wanda aka gicciye. [6] Ba ya nan. Ya tashi yadda ya faɗa. Ku zo ku ga inda aka sa shi. [7] Ku je da sauri ku gaya wa almajiransa cewa, 'Ya tashi daga matattu. Ga shi kuma zai riga ku zuwa Galili, a can ne za ku gan shi.' Abin da na zo in gaya muku ke nan."

8 Sai suka bar kabarin da sauri cike da tsoro, tare da farin ciki mai yawa. Suna gudu don su je su faɗa wa almajiran Yesu ke nan, [9] sai Yesu da kansa ya gamu da su, ya ce musu, "Sallamarku dai!" Suka matso kusa suka rungume ƙafafunsa, suka yi masa sujada. [10] Sai Yesu ya ce musu, "Kada ku ji tsoro. Ku je ku faɗa wa 'yan'uwana su tafi Galili, a can ne za su gan ni."

Rahoton Masu Gadin Kabarin

11 Da matan suna cikin tafiya, sai waɗansu daga cikin masu gadin kabarin nan suka shiga gari, suka ba manyan firistoci labarin dukan abin da ya faru. [12] Sai firistocin da shugabannin mutane suka taru suka yi shawara, suka ba sojojin kuɗi mai yawa. [13] Suka ce, "Ku ce wa mutane, 'Almajiransa ne suka je da dare suka sace shi lokacin da kuke barci.' [14] Idan kuwa labarin ya kai kunnen gwamna, za mu yi masa magana, ba za ku shiga wahala ba."

15 Sai sojojin suka karɓi kuɗin suka yi yadda aka ce su yi. Wannan labarin kuwa har wa yau Yahudawa suna ba da shi.

Aikin da Yesu Ya Ba Almajiransa
(Mar 16.14-18; Luk 24.36-49; Yoh 20.19-23; A. M. 1.6-8)

16 To, almajirai goma sha ɗayan nan suka tafi Galili, suka je dutsen da Yesu ya ce su je. [17] Da suka gan shi sai suka yi masa sujada, amma waɗansunsu suka yi shakka. [18] Sai Yesu ya zo kusa

28.16: Mat 26.32; Mar 14.28

ya ce, "An ba ni dukan iko a sama da ƙasa. [19] Don haka ku je
ku faɗa wa dukkan al'umman duniya su bi ni, kuna yi musu
baftisma cikin sunan Uba, da na Ɗa, da na Ruhu Mai Tsarki.
[20] Ku kuma koya musu su yi biyayya da dukan abubuwan da na
umarce ku. Ku sani fa, ina tare da ku kullum har ƙarshen zamani."

28.19: A. M. 1.8

BISHARA TA HANNUN

MARKUS

Gabatarwa

Marubucin wannan bishara shi ne Markus wanda cikakken sunansa shi ne Yohanna Markus. Shi abokin manzo Bitrus ne na musamman (Dubi 1 Bit 5.13). Tarihi ya nuna cewa an rubuta *Bishara ta Hannun Markus* kafin rushewar Urushalima a shekara ta A.D. 70, a can yankin Roma, kuma an rubutata kafin sauran Littattafan Bisharar Yesu nan uku.

Bishara ta Hannun Markus ta yi ƙoƙari ta nuna mana cewa sakon nan na Yesu na mulkin Allah ta zo wurin mutane (1.14,15). Yesu da kansa kuma shi ne bisharan nan na Allah (1.1, 8.35, 10.25). Fiye da wadannan duka, *Bishara ta Hannun Markus* ta nuna cewa Yesu shi ne Dan Allah wanda aka aike shi yă ceci mutane ta wurin ba da ransa da ya yi a kan gicciye (10.45).

Ko da yake *Bishara ta Hannun Markus* ita ce gajeriya cikin dukan Littattafan Bisharar Yesu nan guda hudu, duk da haka ta ƙunshi dukan abin da yake a *Bishara ta Hannun Matiyu.* Amma *Bishara ta Hannun Markus* ta nanata ayyukan ban mamaki na Yesu.

Abubuwan da Suke Ciki

Shirin yin hidima na Yesu 1.1-13
Aikin Yesu a ƙasar Galili 1.14—9.50
Daga Galili zuwa Urushalima 10.1-52
Mako na ƙarshe na Yesu 11.1—15.47
Tashin Yesu daga matattu 16.1-20

Wa'azin Yohanna Maibaftisma

(Mat 3.1-12; Luk 3.1-9,15-17; Yoh 1.19-28)

1 [1] Wannan shi ne Labari Mai Dadi game da Yesu Almasihu,[a] Dan Allah.[b] [2] Ta fara kamar yadda aka rubuta a littafin annabi Ishaya cewa:

"Ga shi, na aiko manzona yă riga ka gaba,
wanda zai shirya maka hanya."

1.2: Mal 3.1

[a] **1.1 Almasihu:** Da Ibraniyanci, Masiha; da Helenanci, Kiristi. Ma'anar Almasihu ita ce wanda aka shafe aka kuma keɓe.

[b] **1.1 Dan Allah:** Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da wadannan kalmomi.

3 Muryar mai kira a daji tana cewa,
"Ku shirya wa Ubangiji inda zai bi,
Ku miƙe hanyoyinsa."

4 Yohanna Maibaftisma ya kuwa bayyana a daji yana wa'azi cewa mutane su tuba a yi musu baftisma[6] domin a yafe musu zunubansu. 5 Dukan mutanen yankin Yahudiya, da dukan mutanen Urushalima suka yi ta zuwa wurinsa suna faɗin zunubansu suna tuba. Ya kuwa yi musu baftisma a Kogin Urdun.

6 Rigar Yohanna kuwa an yi ta da gashin raƙumi ne. Yana kuwa ɗaure da bel na fata. Abincinsa kuwa fara ce da ruwan zuma. 7 Ya yi wa'azi, ya ce, "Wani yana zuwa a bayana wanda ya fi ni girma, wanda ban isa ko in sunkuya in kunce igiyar takalmansa ba. 8 Na yi muku baftisma da ruwa, amma shi dai, da Ruhu Mai Tsarki zai yi muku."

An Yi wa Yesu Baftisma
(Mat 3.13-17; Luk 3.21-22)

9 Ana nan a cikin wannan lokacin, sai Yesu ya zo daga Nazarat na yankin Galili, sai Yohanna ya yi masa baftisma a Kogin Urdun. 10 Da Yesu yana fitowa daga ruwa, sai ya ga sama ya buɗe, Ruhun Allah yana saukowa a kansa da kamannin kurciya. 11 Sai aka ji wata murya daga sama ta ce, "Kai ne Ɗana wanda nake ƙauna. Ina jin daɗinka ƙwarai."

Shaiɗan Ya Gwada Yesu
(Mat 4.1-11; Luk 4.1-13)

12 Nan da nan sai Ruhu ya kai Yesu cikin daji, 13 inda ya zauna har kwana arba'in. Shaiɗan yana gwada shi. Yesu yana tare da namomin daji, amma mala'iku suka yi masa hidima.

Yesu Ya Fara Hidimarsa a Galili
(Mat 4.12-17; Luk 4.14-15)

14 Bayan da aka sa Yohanna a kurkuku, Yesu ya shiga Galili yana shelar Labari Mai Daɗi da ya fito daga wurin Allah. 15 Yana cewa, "Lokaci ya yi! Mulkin Allah ya yi kusa! Ku tuba, ku gaskata da Labari Mai Daɗi."

1.3: Ish 40.3 1.6: 2 Sar 1.8
1.11: Far 22.2; Zab 2.7; Ish 42.1; Mat 3.17; 12.18; Mar 9.7; Luk 3.22
1.15: Mat 3.2
[6] **1.4 Baftisma:** Ita ce wankan da take nuna tuba.

Yesu Ya Kira Masu Kamun Kifi guda Huɗu
(Mat 4.18-22; Luk 5.1-11)

16 Da Yesu yana wucewa a gefen Tekun Galili, sai ya ga
Siman da ɗan'uwansa Andarawus, suna jefa abin kamun kifi a
teku don su masu kamun kifi ne. 17 Sai Yesu ya ce musu, "Ku
biyo ni, zan mai da ku masu jawo mutane zuwa wurina." 18 Nan
da nan sai suka bar kayansu na kama kifi, suka bi shi.

19 Da ya je gaba kaɗan, sai ya ga Yakubu ɗan Zabadi, da
ɗan'uwansa Yohanna, suna cikin jirgin ruwansu suna gyaran
abin kamun kifi. 20 Nan da nan ya kira su, suka kuwa bar
babansu Zabadi cikin jirgin tare da leburorin da suka ɗauka,
suka bi shi.

Mai Aljani
(Luk 4.31-37)

21 Yesu da masu binsa suka shiga Kafarnahum. Da Ranar Hutun
Yahudawa wato, Asabar ta yi sai ya shiga majami'a yana koyarwa.
22 Suka yi ta mamaki yadda yake koyarwa, domin ya koya musu
kamar mutumin da yake da iko, ba kamar malaman dokokinsu ba.

23 Ba labari sai ga wani mutum mai aljani a cikin majami'arsu,
24 yana ihu, yana cewa, "Ina ruwanka da mu, Yesu Banazare? Ko
ka zo ne ka halaka mu? Na san wane ne kai, kai ne Mai Tsarkin
nan na Allah!"

25 Sai Yesu ya tsawata wa aljanin, ya ce, "Ka yi shiru! Ka
fita daga cikin mutumin nan!"

26 Sai aljanin ya jijjiga mutumin. Ya yi ihu, ya fita daga
cikinsa. 27 Duk mutane suka yi mamaki, har suka yi ta tambayar
juna suna cewa, "Kai, mene ne haka? Tabɗi! Yau ga sabuwar
koyarwa! Wannan mutum yana da iko yă ba aljanu umarni, suna
kuwa yi masa biyayya!"

28 Nan da nan sai labarinsa ya bazu ko'ina a kewayen yankin
Galili.

Yesu Ya Warkar da Mamar Matar Bitrus
(Mat 8.14-15; Luk 4.38-39)

29 Da fitarsu daga majami'ar, sai suka shiga gidan su Bitrus
da Andarawus, tare da Yakubu da Yohanna. 30 Mamar matar
Bitrus kuwa tana kwance tana zazzaɓi. Da shigar Yesu, suka
ba shi labarinta. 31 Sai ya tafi wurinta, ya kama hannunta ya
ɗaga ta. Zazzaɓin kuwa ya bar ta, har ta tashi ta yi musu hidima.

1.22: Mat 7.28-29

Yesu Ya Warkar da Mutane da Yawa
(Mat 8.16-17; Luk 4.40-41)

32 Da yamma, bayan fāɗuwar rana, aka kawo wa Yesu dukan
marasa lafiya, da masu aljanu. 33 Sai dukan mutanen garin suka
taru a ƙofar gidan. 34 Ya warkar da marasa lafiya da yawa, masu
ciwo iri-iri, ya kuma fitar wa mutane aljanu da yawa. Bai ko
yarda aljanun su yi magana ba, domin sun san shi.

Yesu Ya Tafi Yin Addu'a Inda ba Kowa
(Luk 4.42-44)

35 Da sassafe, tun da sauran duhu, Yesu ya tashi ya fita, ya
tafi wani wuri inda ba kowa, yă yi addu'a a can. 36 Sai Siman da
waɗanda suke tare da shi suka je nemansa. 37 Da suka same shi,
suka ce masa, "Ai, dukan mutane suna nemanka."

38 Yesu ya amsa ya ce, "Mu je garuruwan da suke gaba, in
yi wa'azi a can kuma. Dalilin zuwana ke nan."

39 Ya zazzaga dukan Galili yana wa'azi a majami'unsu, yana
kuma fitar wa mutane aljanu.

Yesu Ya Warkar da Kuturu
(Mat 8.1-4; Luk 5.12-16)

40 Wani kuturu wato, mai ciwon fatar jiki ya zo wurin Yesu,
ya durƙusa[c] yana roƙo yana cewa, "Idan ka yarda, kana iya ka
tsarkake ni."

41 Sai tausayi ya kama Yesu, ya miƙa hannunsa ya taɓa shi,
ya ce masa, "Na yarda, ka warke!" 42 Nan da nan sai kuturtar ta
bar shi, ya kuwa warke.

43 Sa'an nan Yesu ya sallame shi da gargaɗi mai ƙarfi cewa,
44 "Ka lura fa kada ka gaya wa kowa. Amma ka je ka nuna kanka
a wurin firist, ka kuma yi hadaya kamar yadda Musa ya ce a yi
don tsarkakewa. Ka yi haka don ka tabbatar wa jama'a cewa ka
warke."

45 A maimakon haka, sai mutumin ya fita yana ta baza labarin
ko'ina. Wannan ya sa Yesu bai iya shiga wani gari a fili ba, sai
ya riƙa zama a waje a wuraren da ba kowa. Duk da haka, mutane
suka yi ta zuwa wurinsa daga ko'ina.

1.39: Mat 4.23; 9.35 1.44: L. Fir 14.1-32
[c] **1.40 ya durƙusa:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da waɗannan kalmomi.

Yesu Ya Warkar da Shanyayye
(Mat 9.1-8; Luk 5.17-26)

2 [1] Bayan 'yan kwanaki, Yesu ya sāke komawa Kafarnahum, sai mutane suka ji labari yana gida. [2] Mutane da yawa suka taru, har ba sauran wuri, ko a bakin ƙofa ma. Yesu yana yi musu wa'azin bishara. [3] Sai ga mutum huɗu suka zo, suna kuwa ɗauke da wani shanyayye. [4] Da suka kāsa shigar da shi zuwa wurin Yesu saboda yawan mutane, sai suka buɗe rufin gidan daidai inda Yesu yake. Da suka huda rufin, sai suka saukar da mutumin, duk da tabarmarsa.

Hoton rufin ɗaki da aka buɗe (2.4)

[5] Da Yesu ya ga bangaskiyarsu sai ya ce wa shanyayyen, "Dana, an yafe maka zunubanka."

6 To, waɗansu malaman dokoki suna zaune a wurin, suna ta tunani a cikin zuciyarsu, [7] suna cewa, "Don me mutumin nan yake magana haka? Ai, yana wa Allah reni ne! Wa yake da ikon yafewar zunubi in ba Allah kaɗai ba?"

8 Nan da nan Yesu ya gane abin da suke tunani a zuciyarsu, sai ya ce musu, "Me ya sa kuke yin irin waɗannan tunani? [9] Wanne ya fi sauƙi, a ce wa mai ciwon nan, 'An yafe maka zunubanka,' ko kuwa a ce, 'Tashi ka ɗauki tabarmarka ka yi tafiya?' [10] Amma ina so ku sani cewa Ɗan Mutum yana da iko

yă gafarta zunubai a duniya." Sai ya ce wa mai ciwon, 11 "Na ce maka, tashi, ka ɗauki tabarmarka ka tafi gida."

12 Nan da nan ya tashi, ya ɗauki tabarmarsa, ya fita. Dukan mutane kuma suna kallonsa, suna mamaki, suna ɗaukaka Allah suna cewa, "Ba mu taɓa ganin wani abu kamar haka ba."

Yesu Ya Kira Lawi
(Mat 9.9-13; Luk 5.27-32)

13 Yesu ya sāke fita ya je bakin Tekun Galili. Mutane da yawa suka taru kewaye da shi, ya kuwa koya musu. 14 Yana wucewa, sai ya ga Lawi ɗan Halfa yana zaune a wurin karɓar haraji. Sai Yesu ya ce masa, "Bi ni." Sai ya tashi ya bi shi.

15 Wata rana, Yesu da almajiransa suna cin abinci a gidan Lawi. Waɗansu masu karɓar haraji da waɗansu masu zunubi da yawa suna ci tare da shi da almajiransa, don mutane da yawa daga cikinsu ne suka bi shi. 16 Waɗansu malaman dokoki waɗanda su Farisiyawa ne, suka ga yana cin abinci tare da masu zunubin nan da masu karɓar haraji. Sai suka tambayi almajiransa suka ce, "Me ya sa yake ci tare da masu karɓar haraji da 'Masu zunubi?' "

17 Da jin haka, Yesu ya ce musu, "Masu lafiya ba sa bukatar likita, sai dai marasa lafiya. Ban zo don in kira masu adalci ba, sai dai masu zunubi."

Tambaya a kan Yin Azumi
(Mat 9.14-17; Luk 5.33-39)

18 To, almajiran Yohanna Maibaftisma da na Farisiyawa suna yin azumi, sai waɗansu mutane suka zo suka tambayi Yesu suka ce, "Me ya sa almajiran Yohanna da na Farisiyawa sukan yi azumi, amma naka ba sa yi?"

19 Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Abokan ango sukan yi azumi a lokacin da ango yake tare da su ne? Ai, sa'ad da ango yake tare da su ba za su yi azumi ba. 20 Lokaci yana zuwa da za a ɗauki angon a bar su. To, a lokacin ne za su yi azumi.

21 "Ba mai facin tsohuwar riga da sabon yadi. Idan kuwa ya yi, sai sabon yadin ya yage tsohuwar rigar, har yagewar ta fi ta dā muni. 22 Kuma ba wanda zai zuba sabon ruwan inabi[d] a cikin tsofaffin salkuna. Idan ya yi haka, sai ruwan inabin yă faffashe salkunan, a kuma yi hasarar salkunan duk da ruwan inabin. Ai, sabon ruwan inabi, sai sababbin salkuna."

[d] **2.22 ruwan inabi:** A kan samu wannan daga 'ya'yan inabin da aka matse. An cika yin amfani da ruwan inabi kamar ruwan sha a ƙasar Isra'ila.

Tambaya a Kan Kiyaye Ranar Hutu
(Mat 12.1-8; Luk 6.1-5)

23 Ana nan a Ranar Hutun Yahudawa Yesu da almajiransa
suna wucewa ta gonakin alkama. Suna cikin tafiya sai almajiransa
suka fara karya wadansu kan alkama. 24 Sai Farisiyawa suka ce
masa, "Duba abin da almajiranka suke yi. Don me suke yin abin
da Doka ta hana yi a Ranar Hutu?"

25 Yesu ya amsa ya ce, "Ashe, ba ku taba karanta abin da
Dawuda ya yi ba, a lokacin da yunwa ta dame shi kuma yana
cikin rashi, shi da abokan tafiyarsa? 26 A zamanin da Abiyata yake
babban firist ne, Dawuda ya shiga wurin sujada, ya ci burodin da
aka keɓe, wanda bai kamata kowa yă ci ba, sai dai firistoci kadai.
Har ma ya ba abokan tafiyarsa!"

27 Sai Yesu ya ce musu, "Ai, an yi Ranar Hutu domin mutum
ne, ba a yi mutum domin Ranar Hutu ba. 28 Saboda haka Dan
Mutum Ubangiji ne har ma da na Ranar Hutu."

Mai Shanyayyen Hannu a Kafarnahum
(Mat 12.9-14; Luk 6.6-11)

3 1 Da Yesu ya sāke shiga cikin majami'a, sai ga wani mutum
mai shanyayyen hannu a cikin majami'ar. 2 Wadansu
mutane kuwa suna neman hanya su sami Yesu da laifi, saboda
haka sai suka zuba ido su ga ko Yesu zai warkar da mutumin
a Ranar Hutu.

3 Sai Yesu ya ce wa mai shanyayyen hannun, "Fito ka tsaya
nan gaba." 4 Sa'an nan Yesu ya tambaye su ya ce, "Mene ne ya
dace a yi a Ranar Hutu? A yi alheri ko a yi mugunta? A ceci rai,
ko a kashe shi?"

Amma mutanen suka yi shiru. 5 Yesu ya duddube su cikin
fushi, yana kuma bakin ciki domin taurin zuciyarsu. Sai ya ce wa
mai shanyayyen hannun, "Ka miƙe hannunka." Sai ya miƙe,
hannunsa kuwa ya warke nan da nan. 6 Da ganin haka kuwa
Farisiyawa suka fita daga haikalin. Nan da nan suka yi shawara
da mutanen Hirudus a kan yadda za su kashe Yesu.

Babban Taro a Bakin Teku

7 Sai Yesu ya tashi tare da almajiransa, suka bar garin suka
je bakin Tekun Galili. Sai mutane da yawan gaske daga Galili
suka bi shi, har da mutanen Yahudiya, 8 da na Urushalima, da na
yankin Idumiya, da na hayin Kogin Urdun, da kuma mutanen

2.23: M. Sh 23.26 **2.25-26:** 1 Sam 21.2-7 **2.26:** L. Fir 24.9

wajen Taya da kuma Sidon. Da yawansu suka zo saboda sun ji dukan abin da yake yi. 9 Don gudun kada mutane su matse shi, sai Yesu ya faɗa wa almajiransa su kawo masa ƙaramin jirgin ruwa ɗaya. 10 Ya yi haka domin ya riga ya warkar da mutane da yawa, har ya kai ga duk masu ciwo suna ta zuwa kusa da shi don su taɓa shi. 11 Duk lokacin da aljanu suka gan shi, sai su fāɗi a gabansa suna ihu suna cewa, "Kai Ɗan Allah ne."

12 Amma ya kwaɓe su kada su gaya wa kowa wane ne shi.

Yesu Ya Zaɓi Almajirai Sha Biyu
(Mat 10.1-4; Luk 6.12-16)

13 Ana nan, sai Yesu ya hau dutse, ya kira waɗanda yake so, suka je wurinsa. 14 Sa'an nan ya zaɓi mutum sha biyu[d] daga cikinsu su kasance da shi. Yana so ya ɾika aikensu su yi wa'azi, 15 su kuma sami ikon fitar da aljanu. 16 Ga sha biyun da ya zaɓa: Siman, wanda Yesu ya sa masa suna Bitrus, 17 da Yakubu ɗan Zabadi, da ɗan'uwansa Yohanna, waɗanda ya sa musu suna Buwarnajis, wato 'ya'yan tsawa, 18 da kuma Andarawus, da Filibus, da Batilomi, da Matiyu, da Toma, da Yakubu ɗan Halfa, da Taddiyus, da Siman mutumin Kan'ana, 19 da Yahuda Iskariyoti wanda ya bashe shi.

Yesu da Ba'alzabul
(Mat 12.22-32; Luk 11.14-23; 12.10)

20 Sa'an nan Yesu ya shiga wani gida, mutane kuma suka sāke haɗuwa har shi da almajiransa ba su iya cin abinci ba. 21 Da 'yan'uwansa suka ji haka, sai suka je domin su kama shi, domin mutane suna cewa, "Ai, ya haukace!"

22 Malaman dokoki kuwa da suka zo daga Urushalima suka ce, "Ai, Ba'alzabul sarkin aljanu ne ya shiga cikinsa! Da ikonsa kuma yake fitar da aljanu."

23 Sai Yesu ya kira mutanen, ya yi musu misalai cewa: "Shaiɗan zai fitar da Shaiɗan kuma?" 24 Ai, idan mulki ya rabu, ɗaya gefen yana gāba da ɗayan, wannan mulki ba zai tsaya ba. 25 Haka kuma idan gida ya rabu biyu, ɗaya gefen yana gāba da ɗayan, wannan gidan ba zai tsaya ba. 26 Idan Shaiɗan kuma ya tayar wa kansa ya kuma rabu, ba zai tsaya ba. Karshensa ya zo ke nan.

3.9-10: Mar 4.1; Luk 5.1-3 **3.22:** Mat 9.34; 10.25

[d] **3.14 ya zaɓi mutum sha biyu:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā sun ƙara, "ya ce da su manzanni" ne a nan.

27 "Ba wanda zai iya shiga gidan mutum mai ƙarfi ya kwashe kayansa, sai dai ya fara kama mutumin, ya ɗaure. Sa'an nan zai iya kwashe kayan gidansa.

28 "Ina faɗa muku gaskiya, za a yafe wa mutane kowane irin zunubi, da maganar reni ga Allah da suka yi. 29 Amma fa, duk wanda ya yi maganar reni game da Ruhu Mai Tsarki ba za a taɓa yafe masa ba har abada. Ya yi zunubi na har abada ke nan." 30 Yesu ya faɗa wannan ne kuwa don sun ce, "Yana da aljanu ne."

Mamar Yesu da 'Yan'uwansa

(Mat 12.46-50; Luk 8.19-21)

31 Sai mamar Yesu da 'yan'uwansa suka zo. Suka tsaya a waje suka aika wani yă kira shi. 32 Mutane kuwa suna zaune kewaye da shi, sai suka ce masa, "Ga mamarka da 'yan'uwanka suna nemanka a waje."

33 Sai ya tambaye su ya ce, "Su wane ne mamata da 'yan'uwana?" 34 Ya duddubi waɗanda suke zaune kewaye da shi, sai ya ce, "Ga mamata da 'yan'uwana! 35 Ai, duk wanda ya yi abin da Allah yake so, shi ne ɗan'uwana, ita ce 'yar'uwata, ita ce kuma mamata."

Misali na Mai Shuka

(Mat 13.1-9; Luk 8.4-8)

4 1 Yesu ya kuma fara koyarwa a bakin Tekun Galili. Taron mutane da yawa sosai suka taru kewaye da shi, har sai da ya shiga jirgin ruwa ya zauna a cikin tekun. Taron mutanen kuwa suna a tudun bakin tekun. 2 Sai ya koya musu abubuwa da yawa ta wurin misalai. Ya ce musu: 3 "Ku kasa kunne! Wani manomi ya tafi gonarsa don yă yi shuka. 4 Yana cikin yafa irin ke nan, sai waɗansu iri suka fāɗi a kan hanya, sai tsuntsaye suka zo suka cinye su. 5 Waɗansu iri kuma suka fāɗi a wuri mai duwatsu inda ba ƙasa sosai. Sai suka tsiro da sauri don ƙasar wurin ba ta da zurfi. 6 Da rana ta yi zafi, sai ta ƙone su har suka bushe, don ba su da saiwa sosai. 7 Waɗansu kuma suka fāɗi a cikin ƙaya, sai ƙayar ta tashi ta hana su girma har ba su yi tsaba ba. 8 Waɗansu kuwa suka fāɗi a ƙasa mai kyau. Suka tsira suka yi girma, suka yi kai, waɗansu tsaba talatin-talatin, waɗansu sittin-sittin, waɗansu har ma ɗari-ɗari."

9 Sa'an nan ya ce, "Duk mai kunnen ji, bari yă ji."

3.29: Luk 12.10 **4.1:** Luk 5.1-3

Manufar Misali na Mai Shuka
(Mat 13.10-17; Luk 8.9-10)

10 Lokacin da Yesu yake zaune shi kaɗai, sai almajiransa sha
biyu da waɗansu masu bisa suka roƙe shi ya gaya musu abin da
misalin nan yake nufi. 11 Sai ya ce musu,
"Ku kam, an yarda muku ku san asirin mulkin Allah. Amma
waɗanda ba sa cikinku, kome sai cikin misalai. 12 Shi ya sa,
'Za su yi ta dubawa, amma ba za su taɓa gani ba,
Su yi ta ji kuma, amma ba za su gane ba.
Idan suka gane, za su tuba a kuma yafe musu.' "

Yesu Ya Ba da Bayanin Misali na Mai Shuka
(Mat 13.18-23; Luk 8.11-15)

13 Sai Yesu ya ce musu, "Ashe, ba ku gane misalin nan ba?
To, yaya za ku gane sauran? 14 Mai yafa irin nan fa maganar
Allah yake yafawa. 15 Irin da suka fāɗi a hanya, su ne kwatancin
mutanen da suka ji maganar Allah. Amma da zarar suka ji, nan
da nan sai Shaiɗan ya zo ya ɗauke maganar da aka shuka a
zuciyarsu. 16 Haka kuma irin da suka fāɗi a wurare masu duwatsu,
su ne kwatancin waɗanda da zarar suka ji maganar sai suka karɓa
da farin ciki. 17 Amma tun da ba su da tushe, ba su daɗe sosai
ba. Lokacin da wahala ko tsanani ya tashi domin wannan maganar
Allah, nan da nan sai su ja da baya. 18 Irin da suka fāɗi cikin
ƙaya, su ne kwatancin mutanen da suke jin maganar, 19 amma
damuwar duniya, da son arziki, da kuma kwaɗayin waɗansu
abubuwa, suka shiga suka hana maganar girma, har ta zama ba
ta da amfani. 20 Irin da suka fāɗi a ƙasa mai kyau kuwa, su ne
kwatancin waɗanda suke jin maganar Allah, suka karɓa, suka
kuma yi amfani da ita, har suka yi riba waɗansu talatin-talatin,
waɗansu sittin-sittin, waɗansu ma har ɗari-ɗari."

Misali a Kan Fitila
(Luk 8.16-18)

21 Yesu ya ci gaba da cewa, "Ko kukan kawo fitila ku rufe
ta da kwano ne? Ko kuma kukan ajiye ta a ƙarƙashin gado ne?
Ba kukan ajiye fitila a bisan tebur ba? 22 Abin da yake ɓoye yanzu,
za a tone shi; abin da ya zama asiri kuma, za a buɗe shi. 23 Duk
mai kunnen ji, bari yă ji."
24 Ya kuma ce musu, "Ku ji da kyau fa! Da mudun da ka
auna, da shi za a auna maka, har ma a ƙara. 25 Duk wanda yake

4.12: Ish 6.9-10 **4.21:** Mat 5.15 ; Luk 11.33 **4.22:** Mat 10.26; Luk 12.2

da abu, za a ƙara masa, wanda ba shi da abu kuma, ko ɗan abin da yake da shi ma za a karɓa a bar shi."

Misalin Irin da Ya Tsiro

26 Yesu ya kuma ce, "Ga yadda mulkin Allah yake. Mutum
ya yafa iri a gonarsa. 27 A kwana a tashi har irin ya tsira ya yi
girma, mutumin bai ma san yadda aka yi ba. 28 Kasa tana ba da
amfani da kanta, da farko takan fitar da kara, sa'an nan kai, sai
kuma kan ya fitar da ƙwaya. 29 Sa'ad da amfani ya nuna, sai yă
sa lauje yă yanke, domin lokacin girbi ya zo."

Misali na Kwayar Mastad

(Mat 13.31-32,34; Luk 13.18-19)

30 Yesu ya kuma ce, "Da me za mu kwatanta mulkin Allah?
Ko kuwa da wane misali ne za mu nuna yadda yake? 31 Yana
kama da ƙwaya iri na mastad wadda irinta ta fi ƙankanta a dukan
irin da ake shukawa a ƙasa. 32 Duk da haka, in an shuka ta, takan
yi girma ta fi duk sauran kayan lambu, takan yi manyan rassa,
har tsuntsaye su iya sauka a inuwarta."

33 Da irin waɗannan misalai da yawa Yesu ya faɗa musu
maganar Allah, daidai iyakar ganewarsu. 34 Bai faɗa musu kome
ba, sai tare da misali. Amma lokacin da yake tare da almajiransa
su kaɗai, yakan faɗa musu kome da kome a fili.

Yesu Ya Tsawata wa Hadari

(Mat 8.23-27; Luk 8.22-25)

35 A ranan nan, da rana ta kusan fāɗuwa, Yesu ya ce wa
almajiransa, "Mu haye zuwa wancan ƙetare." 36 Suka bar taron
mutane, suka ɗauke shi tare da su, cikin jirgin da yake zaune a
ciki. Akwai waɗansu jirage kuma tare da su. 37 Sai babban hadari
mai iska ya taso, har yana ta da ruwan tekun sama yana bubbuga
jirgin. Ruwa kuwa yana shiga cikin jirgin har jirgin ya kusan cika
da ruwa. 38 Yesu kuwa yana can bayan jirgin yana barci da kai a
matashi. Almajiransa suka tashe shi, suka ce, "Malam, za mu
halaka, ba ka kula ba ko?"

39 Sai Yesu ya farka, ya tsawata wa iskar, ya kuma ce wa
ruwan tekun, "Natsu! Ka yi shiru!" Sai iskar ta daina, wuri duk
ya yi tsit. 40 Ya ce wa almajiransa, "Me ya sa kuka ji tsoro haka?
Har yanzu ba ku da bangaskiya ne?"

4.24: Mat 7.2; Luk 6.38 **4.25:** Mat 13.12; 25.29; Luk 19.26 **4.29:** Jow 3.13

41 Sai suka ji tsoro sosai, suka ce wa juna, "Wane ne wannan?
Har iska da ruwan teku ma suna jinsa!"

Yesu Ya Warkar da Mai Aljanu
(Mat 8.28-34; Luk 8.36-39)

5 1 Yesu da almajiransa suka kai hayin teku da yake a ƙasar
Gadara.[e] 2 Da saukar Yesu daga jirgin ruwan, nan da nan sai
ga wani mai aljani, ya fito daga inda ake binne mutane, ya tarye
shi. 3 Mutumin kuwa, a wurin binne mutane ne yake kwana. Ba
mai iya ɗaure shi kuma, ko da sarƙa ma. 4 Don dā an sha ɗaure
hannayensa da ƙafafunsa da sarƙa, amma yakan tsintsinke su. Har
ba wanda yake da ƙarfi yă bi da shi. 5 Kullum kuwa dare da rana
yana yawo cikin inda ake binne mutane, da kan duwatsu, yana
ihu, yana tsatsage jikinsa da duwatsu.

6 Da ya ga Yesu daga nesa, sai ya tashi da gudu ya durƙusa
a gabansa. 7 Ya yi ihu da ƙarfi ya ce, "Ina ruwanka da ni, Yesu
Dan Allah Maɗaukaki? Na roƙe ka da sunan Allah, kada ka ba
ni wahala." 8 Ya faɗa haka ne don Yesu ya ce masa, "Rabu da
mutumin nan, kai aljani!"

9 Yesu ya tambaye shi ya ce, "Mene ne sunanka?"

Sai ya amsa ya ce, "Sunana Dubu Shida,[f] don muna da yawa."
10 Sai ya roƙi Yesu sosai kada yă kore su daga ungwar.

11 Kusa da wurin nan kuwa akwai wani babban garken aladu
da yake kiwo a gangaren dutsen. 12 Aljanun nan suka roƙi Yesu
suka ce, "Ka sa mu je wurin aladun nan, mu shiga cikinsu."
13 Yesu kuwa ya yarda. Sai aljanun suka fita suka shiga cikin
aladun. Wannan garken kuwa yana da aladu wajen dubu biyu,
suka kuwa tashi a guje, suka gangara suka fāɗi cikin tekun, suka
halaka a ruwa.

14 Da ganin haka, masu kiwon aladun suka gudu suka ba da
labarin a garinsu da karkararsu. Mutane suka fito don su ga abin
da ya faru. 15 Da suka zo wurin Yesu suka ga mutumin da dā
yake cike da aljanu, yana zaune da riguna a jikinsa, yana cikin
hankalinsa kuma, sai suka ji tsoro. 16 Waɗanda aka yi abin a
idonsu kuwa, suka yi ta ba da labarin abin da ya faru da mai
aljanun da kuma aladun.

17 Sai mutanen suka fara roƙi Yesu yă bar ƙasarsu.

---

[e] **5.1 Gadara:** A waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Garasinawa" ko kuwa "Gergesena" ne a nan.

[f] **5.9 Sunana dubu shida:** Da Helenanci, "Lijiyon", wato, ƙungiyar sojoji wadda ta kai mutum dubu huɗu zuwa dubu shida.

18 Yesu yana shiga cikin jirgin ruwa ke nan, sai wanda a dā
yake da aljanun nan ya roƙe shi yă yarda masa yă tafi tare da shi.
19 Amma Yesu bai yarda masa ba. Ya ce masa, "Tafi gida
wurin 'yan'uwanka, ka faɗa musu irin manyan abubuwan da
Ubangiji ya yi maka, da kuma yadda ya ji tausayinka."
20 Sai mutumin ya tafi, ya fara baza labari a yankin Mai
Garuruwa Goma a kan irin manyan abubuwan da Yesu ya yi
masa. Dukan mutane kuwa suka yi ta mamaki.

'Yar Jayirus da Mace Mai Zub da Jini
(Mat 9.18-26; Luk 8.40-56)

21 Da Yesu ya sāke hayewa zuwa wancan ƙetare cikin jirgin
ruwa, sai mutane da yawa suka taru wurinsa. Tun yana nan a
bakin tekun, 22 sai ɗaya daga cikin shugabannin majami'a mai
suna Jayirus, ya zo wurin. Da ganin Yesu kuwa, ya fāɗi a gabansa,
23 ya yi ta roƙonsa, yana cewa, "'Yata ƙarama tana bakin mutuwa.
Ina roƙonka ka zo ka taɓa ta don ta warke ta rayu."
24 Sai Yesu ya tafi tare da shi. Mutane da yawa suka bi shi
har suna matsa shi.

25 Akwai wata mace a wurin wadda ta yi shekara goma sha
biyu tana zub da jini. 26 Ta kuma sha wahala sosai a hannun masu
magani da yawa har ta kashe dukan kuɗinta. Amma maimakon ta
sami sauƙi, sai ciwon ya yi ta ƙaruwa. 27 Dā ma, ta ji labarin Yesu,
don haka, ta shiga cikin mutane ta bayansa, ta taɓa rigarsa, 28 tana
tunani a ranta cewa, "Ko da rigarsa ma na taɓa kawai, zan warke."
29 Nan da nan zubar da jininta ya tsaya, ta kuma ji a jikinta an
warkar da ita. 30 Nan da nan Yesu ya ji wani iko ya fita daga gare
shi, sai ya juye a cikin taron, ya ce, "Wa ya taɓa rigata?"
31 Sai almajiransa suka ce masa, "Haba! Kana ganin mutane
suna matsarka haka, ka ce, 'Wa ya taɓa ni?' "
32 Amma Yesu ya dudduba domin ya ga wanda ya yi wannan
abin. 33 Matar kuwa da ta san abin da aka yi mata, ta zo cikin
tsoro da rawar jiki, ta fāɗi a gabansa, ta faɗa masa dukan gaskiya.
34 Sai ya ce mata, "'Yata, bangaskiyarki ta warkar da ke. Ki sauka
lafiya, kin warke daga ciwonki."
35 Yana cikin magana, sai ga waɗansu mutane daga gidan
Jayirus suka ce, "Ai, 'yarka ta mutu, kada ka sa malam ya yi
wani wahala."
36 Amma Yesu bai kula da abin da suka faɗa ba, ya ce wa
shugaban majami'a, "Kada ka ji tsoro, ka dai ba da gaskiya."
37 Bai bar kowa yă bi shi ba sai Bitrus, da Yakubu, da kuma

Yohanna ɗan'uwan Yakubu. 38 Da suka kai gidan Jayirus, Yesu
ya ga mutane sun rikice suna ta kuka suna ihu. 39 Ya shiga ciki,
ya ce musu, "Don me kuke kuka kuna ihu haka? Ai, yarinyar ba
ta mutu ba, barci take yi." 40 Sai suka yi masa dariyar reni. Amma
ya fitar da dukan mutane waje, ya ɗauki baban yarinyar da
mamarta, da kuma almajiransa waɗanda suke tare da shi, ya shiga
inda yarinyar take. 41 Ya kama hannunta, ya ce mata, "Talita
kumi," wato "Yarinya, ki tashi."
42 Nan da nan yarinyar ta tashi ta yi tafiya (Shekarunta goma
sha biyu ne). Wannan kuwa ya sa suka yi mamaki sosai. 43 Amma
Yesu ya ja musu kunne sosai cewa kada kowa yă ji wannan labari.
Ya kuma ce musu su ba ta abinci.

An Ki Yesu a Nazarat
(Mat 13.53-58; Luk 4.16-30)

6 1 Yesu ya bar wurin ya koma garinsa, almajiransa kuwa suka
tafi tare da shi. 2 Da Ranar Hutun Yahudawa ta yi, sai ya fara
koyarwa a majami'a. Mutane da yawa da suka saurare shi, suka
yi mamaki suna cewa, "Ina mutumin nan ya sami waɗannan
abubuwa? Wace hikima ce aka ba shi haka har yana yi abubuwan
ban mamaki?



Hoton mai karatu a majami'a (6.2)

3 Wannan ba shi ne kafintan nan ba, ɗan Maryamu, ɗan'uwan
su Yakubu, da Yusufu, da Yahuda, da kuma Siman? 'Yan'uwansa
mata kuma ba ga su tare da mu ba?" Sai suka ji haushinsa.
4 Sai Yesu ya ce musu, "Ai, kowa yana ba annabi girma,
amma ban da mutanen garinsa, da 'yan'uwansa, da kuma mutanen
gidansa."
5 Yesu bai iya yin wani abin ban mamaki a can ba, sai dai ya
warkar da waɗansu marasa lafiya kaɗan, ta wurin taɓa su. 6 Ya
yi mamaki a kan ba su ba da gaskiya ba.

Yesu Ya Aiki Almajiransa
(Mat 10.5-15; Luk 9.1-6)

Sai Yesu ya zazzaga ƙauyuka yana koyarwa. 7 Sai ya kira sha
biyun nan, ya aike su biyu-biyu, ya kuma ba su iko a kan aljanu.
8 Ya umarce su cewa, "Kada ku ɗauki wani abu don tafiyar, ko
abinci, ko jaka, ko kuɗi ma a aljihunku; sanda kawai za ku riƙe.
9 Amma ku sa takalmi, kada kuma ku riƙe wata riga ban da wadda
take jikinku. 10 Duk gidan da kuka sauka, ku zauna a wurin har
lokacin da za ku bar wannan garin. 11 Duk inda ba a karɓe ku ba,
aka kuma ƙi jinku, in za ku tashi, sai ku kakkaɓe ƙurar ƙafafunku
don yă zama shaida a kansu."
12 Haka fa suka tashi, suna wa'azi cewa mutane su tuba.
13 Suka fitar da aljanu da yawa, suka kuma shafa wa marasa lafiya
da yawa mai, suka kuma warkar da su.

Mutuwar Yohanna Maibaftisma
(Mat 14.1-12; Luk 9.7-9)

14 Sai sarki Hirudus ya ji labarin, saboda sunan Yesu ya bazu
ko'ina. Har waɗansu suka ce, "Yohanna Maibaftisma ne aka ta
da shi daga matattu, shi ya sa yake da ikon yin waɗannan
abubuwan ban mamaki."
15 Amma waɗansu suka ce, "Annabi Iliya ne." Waɗansu kuwa
suka ce, "A'a, wani annabi ne dabam, daga cikin annabawan dā."
16 Da Hirudus ya ji maganar, sai ya ce, "Ai, Yohanna ne,
wanda na yanke masa kai, aka ta da shi daga matattu!" 17 Gama
dā Hirudus da kansa ya ba da umarni aka kamo Yohanna, ya
ɗaure shi a kurkuku. Hirudus ya yi haka saboda Hirudiya, matar
ɗan'uwansa Filibus, wadda shi Hirudus ya aura. 18 Don dā

6.4: Yoh 4.44 **6.8-11:** Luk 10.4-11 **6.11:** A. M. 13.51 **6.13:** Yak 5.14
6.14-15: Mat 16.14; Mar 8.28; Luk 9.19

Yohanna ya yi ta gaya wa Hirudus cewa, "Bai kamata ka auri matar ɗan'uwanka ba."

19 Ashe, ita Hirudiya kuwa tana jin fushin Yohanna a zuciyarta, har ta so ta kashe shi, amma ba ta sami dama ba, 20 don Hirudus yana tsoron Yohanna. Ya sani shi mutum mai adalci ne, mai tsarki kuma, shi ya sa Hirudus ya riƙe Yohanna da kyau. Yakan damu da yawa duk lokacin da Yohanna yake magana da shi, amma duk da haka yakan ji daɗin jin maganarsa.

21 A ƙarshe dai ta sami zarafi. A ranar haihuwar Hirudus, ya yi biki don hakimansa, da sarakunan yaƙinsa, da kuma manyan Galili. 22 Da 'yar Hirudiya[g] ta shigo ta yi rawa a gaban Hirudus da baƙinsa, suka ji daɗi ƙwarai. Sai ya ce, "Me kike so? Kome da kika roƙa, sai in ba ki". 23 Har da rantsuwa, sarki ya ce wa yarinyar, "Duk daɗ abin da kika roƙa zan ba ki, ko da rabin mulkina ne."

24 Sai ta fita ta ce wa mamarta, "Me zan roƙa?"

Mamar ta ce, "Kan Yohanna Maibaftisma."

25 Nan da nan ta gudu ta koma wurin sarki ta ce, "Ina so yanzu-yanzu ka ba ni kan Yohanna Maibaftisma a cikin kwano."

26 Da jin wannan, sarki ya damu ƙwarai, amma saboda rantsuwar da ya riga ya yi, da kuma baƙinsa, bai so yă hana mata ba. 27 Sai ya aiki dogarinsa da umarni yă kawo kan Yohanna. Mutumin kuwa ya tafi ya yanke kan Yohanna a kurkuku. 28 Ya kawo a cikin kwano, ya ba yarinyar, ita kuwa ta ba mamarta. 29 Da almajiran Yohanna suka ji labarin, sai suka zo suka ɗauki gawarsa, suka binne.

Yesu Ya Ciyar da Mutum Dubu Biyar

(Mat 14.13-21; Luk 9.10-17; Yoh 6.1-14)

30 Manzannin da Yesu ya aika a dā suka komo wurinsa, suka faɗa masa dukan abubuwan da suka yi, da abin da suka koyar. 31 Ga shi kuwa mutane da yawa suna ta kai da kawowa, har manzannin ba su sami damar cin abinci ba, sai ya ce musu, "Ku zo mu tafi wurin da ba kowa, don ku ɗan huta." 32 Sai suka shiga jirgin ruwa suka tafi wurin da ba kowa, sai su kaɗai.

33 Amma da suke barin wurin, waɗansu mutane da yawa suka gan su, suka kuma gane su. Sai suka bi tudu suna ta gudu da ƙafa daga garuruwa duka, suka riga su zuwa. 34 Da saukar Yesu sai

6.17-18: Luk 3.19-20

[g] **6.22 'Yar Hirudiya:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "'yar Hirudus" ne a nan.

ya ga taro mai yawa, ya kuma ji tausayinsu, domin suna kamar tumakin da ba su da mai kiwo. Sai ya fara koya musu abubuwa da yawa. 35 Kusan fāɗuwar rana sai almajiransa suka zo wurinsa, suka ce masa, "Wannan wuri fa ba kowa. Ga shi kuwa rana ta kusan fāɗuwa. 36 Ka sallami mutanen su shiga karkara da ƙauyuka na kurkusa, su saya wa kansu abin da za su ci."

37 Amma Yesu ya amsa musu ya ce, "Ku dai, ku ba su wani abu su ci mana."

Sai suka ce masa, "Wato mu je mu sayo abinci na kuɗin da ake biyan lebura yini ɗari biyu, mu ciyar da su?"

38 Ya ce musu, "Burodi nawa kuke da su? Ku je ku duba."

Da suka bincika suka ce, "Burodi biyar ne, da kifi biyu."

39 Sa'an nan Yesu ya sa almajiransa su sa mutanen su zauna ƙungiya-ƙungiya a ɗanyar ciyawa. 40 Sai suka zauna jeri-jeri, waɗansu ɗari-ɗari, waɗansu kuma hamsin-hamsin. 41 Da ya ɗauki burodi biyar ɗin da kifi biyun, sai ya ɗaga kai sama, ya yi godiya ga Allah, ya rarraba, ya yi ta ba almajiran, suna kai wa mutanen. Ya kuma raba wa dukan mutanen kifin nan biyu. 42 Duka kuwa suka ci suka ƙoshi, 43 har suka tattara gutsattsarin burodin da kifin, aka sami kwando goma sha biyu cike. 44 Yawan mutanen da suka ci wannan abinci kuwa maza dubu biyar ne.

Yesu Ya Yi Tafiya a kan Ruwa

(Mat 14.22-33; Yoh 6.16-21)

45 Nan da nan Yesu ya sa almajiransa su shiga jirgin ruwa su riga shi hayewa zuwa Betsaida, shi kuma yă sallami taron. 46 Bayan da ya sallame su, sai ya hau wani tudu domin yă yi addu'a. 47 Da rana ta fāɗī, jirgin yana tsakiyar teku, Yesu kuwa yana nan a kan tudu shi kaɗai. 48 Da ya ga suna fama da tuƙi, domin iska tana gāba da su, misalin ƙarfe uku na dare, sai ga shi yana zuwa wurinsu, yana takawa a kan ruwan teku. Ya yi kamar zai wuce su. 49 Amma da suka gan shi yana takawa a kan ruwan, sai suka yi tsammani fatalwa ce, suka yi ihu, 50 domin duk sun gan shi, suka firgita.

Sai nan da nan ya yi musu magana ya ce, "Kada ku damu! Ni ne, kada ku ji tsoro!" 51 Sa'an nan ya shiga cikin jirgin da su, iska kuma ta kwanta. Sai mamaki ya kama su ƙwarai, 52 don ba su san mene ne ma'anar ciyar da mutane dubu biyar nan ba, saboda zuciyarsu ba ta fahimci ma'anar ba.

6.34: Num 27.17; 1 Sar 22.17; 2 Tar 18.16; Ez 34.5; Mat 9.36

Yesu Ya Warkar da Marasa Lafiya a Janisarat
(Mat 14.34-36)

53 Da Yesu da almajiransa suka ƙetare tekun, suka sauka a ƙasar Janisarat, suka ɗaure jirgin a bakin tekun. 54 Da fitarsu daga jirgin ruwan, sai nan da nan mutane suka ga, ashe, Yesu ne. 55 Suka yi ta gudu daga ko'ina a cikin ƙasar, suka yi ta kawo marasa lafiya a kan abin kwanciyarsu zuwa duk inda suka ji Yesu yake. 56 Duk inda ya tafi kuma, birni ko ƙauye ko karkara, sukan kwantar da marasa lafiya a bakin kasuwa, su roƙe shi don marasa lafiyar su taɓa ko da gefen rigarsa ma. Dukan waɗanda suka taɓa shi kuwa suka warke.

Al'adar Shugabanni
(Mat 15.1-9)

7 1 Farisiyawa da waɗansu malaman dokoki daga Urushalima suka zo suka taru wurin Yesu. 2 Sai suka lura waɗansu almajiransa suna cin abinci da hannaye "marasa tsabta", wato, ba su wanke hannu bisa ga al'ada ba.

3 Ga shi Farisiyawa har da sauran Yahudawa ba sa cin abinci sai sun wanke hannu sarai tukuna, bisa ga al'adun dattibai. 4 In suka komo daga kasuwa kuwa, ba sa cin abinci sai sun yi wanka tukuna. Akwai kuma waɗansu al'adu da yawa da suka gāda, suke kiyayewa, kamar wanke-wanken ƙwarya, da tukwane, da tulunan ƙarfe.[h]

5 Sai Farisiyawa da malaman dokoki suka tambayi Yesu, "Don me almajiranka ba sa bin al'adun dattibai amma suna cin abinci da hannu marar tsabta?"

6 Sai ya amsa ya ce, "Daidai ne Ishaya ya yi annabci a kanku munafukai! Kamar yadda yake a rubuce cewa,

Allah ya ce, 'Waɗannan mutane suna girmama ni da
bakinsu ne kawai,
amma zukatansu sun yi nesa da ni.
7 A banza suke yi mini sujada;
Suna koyar da dokokin mutane,
wai maganar Allah ne.'

8 "Kun yar da abin da Allah ya ce a yi, kuna bin al'adun mutane."

9 Sai ya ce musu, "Lallai kam kun iya yar da umarnin Allah don ku bi al'adunku! 10 Gama Musa ya ce, 'Ka girmama babanka

---

7.6-7: Ish 29.13
[h] 7.4 **tulunan ƙarfe:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā sun ƙara "har da tabarma".

da mamarka,' kuma, 'Wanda ya zagi babansa ko mamarsa dole ne a kashe shi.' 11 Amma kukan bar mutum yă ƙyale iyayensa a lokacin da suke da bukata, yă ce, 'Duk abin da dā za ku samu a wurina na riga na keɓe wa Allah ko.' 12 Ta haka ku hana shi yă taimaki babansa ko mamarsa. 13 Ta haka kuna mai da maganar Allah wofi saboda al'adun da kuke koya wa yaranku. Haka kuma kuke yin abubuwa da yawa."

Abubuwan da Suke Sa Mutum yă zama Marar Tsarki a gaban Allah
(Mat 15.10-20)

14 Sai Yesu ya sāke kiran jama'a, ya ce musu, "Ku saurare ni dukanku, ku kuma gane da kyau. 15 Abin da yake shiga cikin mutum daga waje ba shi ne yake sa mutum yă zama marar tsarki a gaban Allah ba, abin da yake fitowa daga cikin mutum ne yake sa mutum yă zama marar tsarki a gaban Allah."[i]

17 Sa'ad da ya rabu da taron ya shiga gida, almajiransa suka tambaye shi ma'anar wannan koyarwa. 18 Ya amsa ya ce, "Ashe, ku ma ba ku gane ba? Ba ku gane cewa duk abin da ya shiga cikin mutum daga waje ba ya iya sa mutum yă zama marar tsarki a gaban Allah, 19 domin ba cikin zuciyarsa yake shiga ba, amma cikin cikinsa ne, sa'an nan yă kuma fita daga jikinsa?" (A wannan maganar Yesu ya nuna cewa ana iya cin kowane irin abinci.)

20 Ya ci gaba da cewa, "Abin da yake fitowa daga cikin mutum, shi ne yake sa mutum yă zama marar tsarki a gaban Allah. 21 Don daga cikin zuciyar mutum ne mugayen tunani suke fitowa, kamar su lalata, da sata, da kisankai, da zina, 22 da kwaɗayi, da mugunta, da rudi, da muguwar sha'awa, da kishi, da ɓata suna, da girmankai, da kuma rashin tunani. 23 Duk waɗannan mugayen abubuwa daga cikin zuciya suke fitowa, suna kuwa ƙazantar da mutum."

Bangaskiyar Wata Mace
(Mat 15.21-28)

24 Daga nan Yesu ya tashi ya tafi wajajen Taya da Sidon. Ya shiga wani gida, bai kuwa so kowa yă sani ba. Amma duk da haka ɓoyewansa bai yiwu ba. 25 Nan da nan sai wata mace wadda

7.10: Fit 20.12; 21.17; L. Fir 20.9; M. Sh 5.16
[i] 7.15 Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya 16 kamar haka "Duk mai kunnen ji, bari yă ji."

'yarta ƙarama take da aljani ta ji labarinsa. Ta zo ta fãdi a gabansa.
26 Matar kuwa Baheleniya ce. A yankin Finikiya aka haife ta, a
cikin ƙasar Suriya. Sai ta roƙi Yesu yă fitar wa 'yarta aljanin.
27 Yesu ya ce mata, "Bari 'ya'ya su ci su ƙoshi tukuna, ba daidai
ba ne a kwashe abincinsu a ba karnuka."[J]

28 Amma matar ta amsa ta ce, "I, haka ne, malam, amma ai,
karnuka sukan ci abin da yake fãɗuwa daga teburin yara."

29 Sai ya ce mata, "Saboda wannan amsa da kika bayar, ki
tafi gida, aljanin ya rabu da 'yarki."

30 Sai ta koma gida ta ga 'yarta a kwance a gado, aljanin kuwa
ya rabu da ita.

Yesu Ya Warkar da Bebe

31 Sai Yesu ya fita daga yankin Taya, ya bi ta Sidon ya je
Tekun Galili. A hanya, ya zo yankin ƙasar Mai Garuruwa Goma.
32 A can aka kawo masa wani kurma, wanda da kyar yakan yi
magana. Suka roƙe shi yă taɓa mutumin don yă warkar da shi.
33 Yesu ya ja kurman gefe inda ba kowa, sai ya sa yatsotsinsa a
kunnuwansa, ya tofa miyau, ya kuma taɓa harshensa da miyaun.
34 Sa'an nan ya ɗaga kai sama ya yi numfashi mai zurfi, ya ce
masa, "Iffata!" Wato "Buɗe!"

35 Da fadin haka sai kunnuwan mutumin suka buɗu, abin da
ya ɗaure harshensa kuma ya kunce, sai ya fara magana da kyau.
36 Yesu ya ja musu kunne kada su faɗa wa kowa, amma da yana
hana su, su kuma suna ƙara watsar da labarin. 37 Mutane suka
cika da mamaki, suka ce, "Kai, ya yi kome da kyau! Har ma ya
sa waɗanda dā suke kurma suna jin magana, waɗanda dā suke
bebe kuma suna yin magana."

Yesu Ya Ciyar da Mutum Dubu Huɗu
(Mat 15.32-39)

8 1 Ba a daɗe ba sai taro mai yawan gaske ya sāke haɗuwa.
Tun da ba su da abin da za su ci, Yesu ya kira almajiransa
wurinsa ya ce musu, 2 "Ina jin tausayin jama'an nan, don yau
kwana uku ke nan suna tare da ni, kuma ba su da abinci. 3 In
kuwa na sallame su su tafi gida da yunwa haka, ai, za su kāsa a
hanya. Ga shi kuwa, waɗansunsu sun zo daga nesa."

4 Almajiransa suka amsa, suka ce, "Ina za a sami abinci a
wannan daji da zai iya ciyar da mutanen nan?"

[J] **7.27 karnuka:** Duk wanda ba Bayahude ba Yahudawa sukan ɗauke shi kamar kare.

5 Yesu ya tambaye su cewa, "Burodi nawa ne kuke da su?"
Suka ce, "Bakwai."

6 Sai ya sa taron mutane su zauna a ƙasa. Da ya ɗauki burodin
nan bakwai, ya yi godiya ga Allah, ya rarraba, ya yi ta ba
almajiransa don su ba mutanen, suka kuwa rarraba musu. 7 Suna
kuma da ƙananan kifaye kaɗan. Ya yi godiya dominsu kuma, ya ce
su ma a raba wa taron. 8 Mutanen suka ci, suka ƙoshi, har suka
ɗauki raguwar cike da kwanduna bakwai. 9 Yawan waɗanda suka
ci kuwa sun kai wajen dubu huɗu. Sai ya sallame su. 10 Nan da nan
kuwa ya shiga jirgin ruwa da almajiransa, ya tafi ƙasar Dalmanuta.

Neman Alama
(Mat 12.38-42; 16.1-4; Luk 12.54-56)

11 Farisiyawa suka zo suka fara gardama da shi. Sun so su
gwada Yesu, sai suka roƙe shi yă nuna musu abin ban mamakin
da zai zama musu alama. 12 Sai ya yi numfashi mai zurfi, ya ce,
"Don me ku mutanen zamanin nan kuke neman ganin alama?
Gaskiya ina faɗa muku, ba wata alamar da za a nuna wa mutanen
wannan zamani." 13 Sa'an nan ya bar su, ya shiga jirgin ruwa, ya
ƙetare zuwa wancan hayen.

Yistin Farisiyawa da Hirudus
(Mat 16.5-12)

14 Almajiran Yesu sun manta ba su kawo burodi ba, sai guda
ɗaya kawai wanda suke da shi a jirgin ruwan. 15 Yesu ya ja musu
kunne, ya ce, "Ku kula fa, kuma ku yi hankali da yistin
Farisiyawa da na Hirudus."[k]

16 Sai almajiran suka fara tadi da juna suna cewa, "Ko saboda
ba mu da burodi ne ya faɗa haka?"

17 Da ya gane maganar da suke yi, sai Yesu ya tambaye su,
"Me ya sa kuke magana a kan ba ku da burodi? Ashe, har yanzu
ba ku gane ba? Ba ku kuma fahimta ba? Zuciyarku a taurare take?
18 Kuna da idanu, ba kwa gani ne? Kuna da kunnuwa, ba kwa ji
ne? Ba kwa tunawa ne? 19 A lokacin da na kakkarya wa mutum
dubu biyar burodin nan biyar fa? Kwanduna nawa kuka ɗauka
cike da abin da ya rage?"

Suka amsa cewa, "Sha biyu."

8.11: Mat 12.38; Luk 11.16 **8.12:** Mat 12.39; Luk 11.29 **8.15:** Luk 12.1
8.18: Irm 5.21; Ez 12.2; Mar 4.12

[k] **8.15 yistin:** Yisti abu ne da ake sa a garin da ake yin burodi da shi domin burodin yă kumbura.

20 "To, burodi bakwai ɗin nan da na kakkarya wa mutum
dubu huɗu fa? Manyan kwanduna nawa kuka tattara cike da
gutsattsarin?"
Suka ce masa, "Bakwai."
21 Sai Yesu ya ce musu, "To, har yanzu ba ku gane
maganata ba?"

Yesu Ya Warkar da Makaho a Betsaida

22 Suka zo Betsaida, sai aka kawo wa Yesu wani makaho,
aka roƙe shi yă taɓa makahon. 23 Ya kama hannun makahon, ya
kai shi bayan gari. Da ya tofa miyau a idanun mutumin, ya taɓa
shi don yă warkar da shi. Sai ya tambaye shi ya ce, "Kana iya
ganin wani abu?"
24 Sai makahon ya ɗaga kai, ya ce, "Ina ganin mutane kam,
amma kamar itatuwa nake ganinsu, suna yawo."
25 Sai Yesu ya sāke taɓa idanun mutumin. Mutumin ya zura
ido kwar, idanunsa kuwa suka warke, sai ya ga kome sosai.
26 Yesu ya sallame shi yă tafi gida, ya ce masa, "Kada ka koma
ta cikin gari, ko ƙauyen ma kada ka shiga."

Bitrus Ya Shaida Yesu Shi Ne Almasihu
(Mat 16.13-20; Luk 9.18-21)

27 Yesu da almajiransa suka tafi, suka shiga ƙauyukan
Kaisariya Filibi. A hanya kuwa ya tambayi almajiransa ya ce,
"Bisa ga faɗin mutane, ni wane ne?"
28 Suka amsa suka ce, "Waɗansu sun ce kai Yohanna
Maibaftisma ne, waɗansu kuwa suna cewa, kai ne annabi Iliya,
waɗansu kuwa sun ce kai wani ne daga cikin sauran annabawa."
29 Sai ya tambaye su, "Amma ku fa, wane ne ni a ganinku?"
Sai Bitrus ya amsa ya ce, "Kai ne Almasihu." 30 Yesu ya ja musu
kunne kada su gaya wa kowa wane ne shi.

Yesu Ya Faɗa Irin Mutuwar da Zai Yi
(Mat 16.21-28; Luk 9.22-27)

31 A lokacin nan, Yesu ya fara koya musu yadda Ɗan Mutum
zai sha wuya iri-iri. Shugabannin jama'a da manyan firistoci, da
malaman dokoki za su ƙi shi, har a kashe shi, bayan kwana uku
kuma zai tashi da rai. 32 Ya faɗa wannan magana a sarari.
Sai Bitrus ya ja shi gefe ɗaya, ya fara tsawata masa.

8.28: Mar 6.14-15; Luk 9.7-8 **8.29:** Yoh 6.68-69

33 Amma Yesu ya juya ya dubi sauran almajiran, ya tsawata
wa Bitrus ya ce, "Ka rabu da ni, kai Shaiɗan! Kana tunani kamar
mutum ne, ba kamar Allah ba."
34 Sa'an nan ya kira mutanen kusa, tare da almajiransa, ya
ce musu, "Duk mai so yă bi ni, sai yă ƙi kansa, yă ɗauki
gicciyensa, yă bi ni. 35 Gama duk mai son ajiyar ransa, zai rasa
shi. Amma duk wanda ya rasa ransa saboda ni, da kuma bishara,
ajiyarsa yake yi. 36 Ina amfani mutum yă sami dukan duniya,
sa'an nan yă rasa ransa? 37 Me kuma mutum zai iya bayarwa a
maimakon ransa? 38 Duk wanda yake jin kunyata da kunyar
maganata a wannan zamani marar aminci da kuma mai yawan
zunubi, Ɗan Mutum ma zai ji kunyarsa a lokacin da zai zo cikin
ɗaukakar Ubansa tare da mala'iku masu tsarki."
9 1 Ya kuma ce musu, "Gaskiya, ina gaya muku, akwai
waɗansu da suke tsaye a nan da ba za su mutu ba, sai sun
ga mulkin Allah ya bayyana da iko."

Sākewar Kamannin Yesu
(Mat 17.1-13; Luk 9.28-36)

2 Bayan kwana shida Yesu ya ɗauki Bitrus, da Yakubu, da
Yohanna, ya kai su kan wani dutse mai tsawo inda suka kasance
su kaɗai. Ana nan sai kamanninsa ya sāke a gabansu, 3 rigunansa
kuma suka yi fari fat suna ƙyalli, yadda ba mai wankin da zai
iya yinsu haka a duniya. 4 Sai ga annabi Iliya da annabi Musa
suka bayyana a gare su, suna magana da Yesu. 5 Sai Bitrus ya
ce wa Yesu, "Malam, ya yi kyau da muke nan, bari mu yi
bukkoki uku, ɗaya dominka, ɗaya domin annabi Musa, ɗaya
kuma domin annabi Iliya." 6 Ya rasa abin da zai faɗa ne, domin
shi da sauran almajiran sun ji tsoro ƙwarai.
7 Sai ga wani girgije ya zo ya rufe su, aka kuma ji wata murya
daga cikin girgijen, tana cewa, "Wannan shi ne Ɗana, wanda nake
ƙauna. Ku saurare shi!" 8 Ba labari, da suka dudduba, ba su ƙara
ganin kowa ba, sai Yesu kaɗai tare da su.
9 Da suna cikin gangarowa daga dutsen, sai Yesu ya ja musu
kunne kada su gaya wa kowa abin da suka gani, sai Ɗan Mutum
ya tashi daga matattu tukuna.
10 Don haka suka bar wannan maganar, suna tambayar juna
ko mene ne Yesu yake nufi da "tashi daga matattu". 11 A ƙarshe

---

8.34: Mat 10.38; Luk 14.27 **8.35:** Mat 10.39; Luk 17.33; Yoh 12.25
9.2-7: 2 Bit 1.17-18

suka tambaye shi suka ce, "To, don me malaman dokoki suke cewa sai annabi Iliya ya fara zuwa, sa'an nan Almasihu yă zo?"

12 Yesu ya amsa ya ce, "Gaskiya ne annabi Iliya zai fara zuwa don yă shirya kome. Amma an rubuta kuma cewa Dan Mutum zai sha wuya iri-iri, za a kuma wulaƙanta shi. Ko ba haka ba? 13 Ai, Iliya ya riga ya zo, mutane suka kuma yi masa duk abin da suka ga dama, kamar dai yadda aka rubuta zai faru."

Yesu Ya Warkar da Yaro Mai Aljani
(Mat 17.14-21; Luk 9.37-43a)

14 Da Yesu da almajiran nan uku suka koma wurin sauran almajiran, sai suka ga babban taro ya kewaye su. Malaman dokoki kuma suna gardama da su. 15 Da ganin Yesu sai duk taron suka yi mamaki ƙwarai da gaske, suka tashi da gudu suka je suka gaishe shi. 16 Yesu ya tambayi almajiransa ya ce, "Gardamar me kuke yi da su?"

17 Sai wani mutum daga cikin taron ya amsa masa, ya ce, "Malam, ga shi na kawo maka ɗana, wanda yake da aljani a cikinsa. Aljanin kuwa yana hana shi magana. 18 Duk lokacin da abin ya tashi, yakan jefar da shi a ƙasa. Yakan sa shi yă fid da kumfa a baki, yana kuma cizon haƙora, jikinsa kuma yă miƙe da ƙarfi. Na yi wa almajiranka magana su fitar da shi, amma sun kāsa."

19 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ku mutanen zamanin nan, marasa bangaskiya, har zuwa yaushe zan zauna tare da ku? Har zuwa yaushe kuma zan jimre da ku? Ku kawo mini yaron." 20 Sai suka kawo masa yaron.

Da aljanin ya ga Yesu, nan da nan sai ya bugi yaron, jikinsa yana rawa, ya fādi yana ta birgima, bakinsa kuma yana ta fid da kumfa. 21 Sai Yesu ya tambayi baban yaron, "Tun yaushe wannan abu ya same shi?"

Baban ya ce, "Tun yana ƙarami. 22 Yakan jefa shi a wuta da cikin ruwa, don dai ya kashe shi. Amma in za ka iya yin wani abu, ka ji tausayinmu ka taimake mu."

23 Yesu ya ce masa, "Don me kake tambaya ko zan iya? Ai, dukan abu mai yiwuwa ne ga wanda yake ba da gaskiya."

24 Nan da nan sai baban yaron ya ɗaga murya ya ce, "Na ba da gaskiya, ka taimake ni in ƙara gaskatawa!"

25 Da Yesu ya ga mutane suna ta zuwa da gudu, sai ya tsawata wa aljanin ya ce masa, "Kai beben aljani, na umarce ka ka fita daga cikinsa, kada ka sāke shiga cikinsa kuma."

9.11: Mal 3.23; Mat 11.14 **9.13**: Mat 17.13

26 Aljanin kuwa ya yi ihu, ya kuma jijjiga yaron sosai, sa'an
nan ya fita. Yaron kuma ya kwanta kamar gawa, har ma yawancin
mutane suka ce, "Ai, ya mutu." 27 Amma Yesu ya kama hannunsa
ya ɗaga shi, ya kuwa tashi a tsaye.
28 Da Yesu ya shiga cikin gida, almajiransa suka tambaye shi
a ɓoye, suka ce, "Don me mu muka kāsa fitar da aljanin?"
29 Yesu ya amsa, ya ce, "Ai, irin wannan aljanin ba ya fita
sai da addu'a."

Yesu Ya Sāke Yin Magana game da Mutuwarsa
(Mat 17.22-23; Luk 9.43-45)

30 Sai Yesu da almajiransa suka bar wurin, suka ci gaba da
tafiya, suka wuce ta cikin Galili. Yesu bai so wani yă san inda
suke ba, 31 domin yana koya wa almajiransa cewa, "Za a ba da
Dan Mutum ga hannun mutane, za su kuwa kashe shi. Bayan
kwana uku kuma zai tashi." 32 Amma ba su gane da abin da yake
nufi ba, suna kuma jin tsoro su tambaye shi.

Wa Ya Fi Girma?
(Mat 18.1-5; Luk 9.46-48)

33 Suka kai Kafarnahum. Da Yesu ya shiga gida sai ya
tambayi almajiransa ya ce, "A kan me kuke gardama a hanya?"
34 Amma suka yi shiru, don a hanya sun yi gardama a kan ko
wane ne mafi girma a cikinsu. 35 Sai Yesu ya zauna, ya kira sha
biyun nan, ya ce musu, "Duk wanda yake so yă zama na fari,
dole ne yă zama na ƙarshe duka, yă zama bawan kowa kuma."
36 Ya ɗauki wani ƙaramin yaro ya sa shi yă tsaya a tsakiyarsu.
Sa'an nan ya ɗauke shi ya rungume shi, ya ce musu, 37 "Duk
wanda ya karɓi ƙaramin yaro kamar wannan saboda sunana, ni
ne ya karɓa. Wanda ya karɓe ni kuma, ba ni ya karɓa ba, wanda
ya aiko ni ne ya karɓa."

Wanda Ba Ya Gāba da Mu, Namu Ne
(Luk 9.49-50)

38 Ana nan, sai Yohanna ya ce masa, "Malam, mun ga wani
yana fitar da aljanu da sunanka, muka kuwa hana shi, domin shi
ba ya cikinmu."
39 Amma Yesu ya ce, "Kada ku hana shi. Ai, ba wanda zai
yi wani abin ban mamaki a cikin sunana yă kuma yi baƙar magana

9.34: Luk 22.24 **9.35:** Mat 20.26-27; 23.11; Mar 10.43-44; Luk 22.26
9.37: Mat 10.40; Luk 10.16; Yoh 13.20

a kaina nan da nan. 40 Ai, duk wanda ba ya gāba da mu, namu ne. 41 Ina gaya muku gaskiya, duk wanda ya ba ku ruwan sha, ko kwaf ɗaya, domin ku na Almasihu ne, gaskiya ina gaya muku, ba zai rasa ladansa ba ko kaɗan.

Abubuwa Masu Sa Tuntuɓe
(Mat 18.6-9; Luk 17.1-2)

42 "Zai zama abin tausayi ga wanda ya sa ɗaya daga cikin waɗannan 'yan yara masu ba da gaskiya gare ni yă yi zunubi. Zai fi masa kyau a ɗaura masa babban dutsen niƙa a wuya, a jefa shi cikin teku. 43 Idan kuwa hannunka yana sa ka ka yi zunubi, sai ka yanke shi mana! Ya fi kyau ka shiga rai na har abada da hannu ɗaya, da ka bar dukan hannayenka ka shiga gidan wuta da hannu biyu. Wutar kuma ba za a iya kashe ta ba.[k] 45 Idan kuma ƙafarka tana sa ka ka yi zunubi, sai ka yanke ta mana! Ya fi kyau ka shiga rai na har abada da ƙafa ɗaya, da ka shiga gidan wuta da ƙafa biyu.[l] 47 Idan kuma idonka yana sa ka ka yi zunubi, sai ka cire shi. Ya fi kyau ka shiga mulkin Allah da ido ɗaya, da a jefa ka gidan wuta da ido biyu. 48 A wurin, tsutsotsin da suke cinsu ba sa mutuwa, wutar kuma ba za a iya kashe ta ba.

49 "Za a tsarkake kowa da wuta, kamar yadda ake tsarkake hadaya da gishiri.

50 "Gishiri abu ne mai kyau, amma idan gishiri ya rabu da daɗinsa, da me za ku gyara shi? Sai ku kasance da gishiri a cikinku, ku yi zaman lafiya da juna."

Koyarwa a kan Kashen Aure
(Mat 19.1-12; Luk 16.18)

10 1 Daga nan Yesu ya bar wannan wuri, ya tafi yankin Yahudiya, da kuma hayin Kogin Urdun. Mutane da yawa kuma suka sāke haɗuwa a wurinsa, ya kuma koya musu kamar yadda ya saba.

2 Sai waɗansu Farisiyawa suka zo wajensa don su gwada shi, suka tambaye shi suka ce, "Bisa ga Dokarmu, daidai ne mutum ya saki matarsa?"

3 Sai Yesu ya amsa ya ce, "Wane umarni ne Musa ya ba ku?"

9.40: Mat 12.30; Luk 11.23 **9.41:** Mat 10.42 **9.43:** Mat 5.30 **9.47:** Mat 5.29 **9.48:** Ish 66.24 **9.49:** L. Fir 2.13 **9.50:** Mat 5.13; Luk 14.34-35

[k] 9.43 Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya ta 44 haka "A wurin kuwa, tsutsotsin da suke cinsu ba sa mutuwa, wutar kuma ba za a iya kashe ta ba."

[l] 9.45 Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya ta 46 haka "A wurin dai tsutsotsin da suke cinsu ba sa mutuwa, wutar kuma ba za a iya kashe ta ba."

4 Suka amsa masa suka ce, "Musa ya ba da izni mutum yă
rubuta takardar kashen aure, yă kuma sallami matarsa."
5 Yesu ya ce musu, "Don taurinkanku ne Musa ya rubuta
muku wannan umarnin. 6 Amma tun farkon halitta 'Allah ya yi
mutane namiji da ta mace.' 7 Don haka fa, mutum zai bar babansa
da mamarsa, yă manne wa matarsa, 8 su biyun kuma su zama
ɗaya. Har nan gaba ba za su zama mutum biyu ba, sai dai su
zama kamar mutum ɗaya. 9 Saboda haka, abin da Allah ya haɗa,
kada wani yă raba."
10 Da suka sāke komawa cikin gida, sai almajiransa suka yi
wa Yesu tambaya a kan wannan magana. 11 Sai ya ce musu, "Duk
mutumin da ya saki matarsa, ya auri wata, yana cin amanar ta
farkon da laifin zina ke nan. 12 In kuma mace ta saki mijinta ta
auri wani, ta yi zina ke nan."

Yesu Ya Sa wa 'Yan Yara Albarka
(Mat 19.13-15; Luk 18.15-17)

13 Mutane suka yi ta kawo wa Yesu 'yan yara domin ya sa
musu albarka, amma almajiransa suka tsawata wa mutanen. 14 Da
Yesu ya ga haka, sai ya ji haushi, ya ce musu, "Ku bar yara
ƙanana su zo wurina, kada ku hana su. Gama mulkin Allah na
irinsu ne. 15 Gaskiya ina gaya muku, duk wanda bai karɓi mulkin
Allah kamar yadda ƙaramin yaro yake yi ba, ba zai taɓa shiga
cikinsa ba." 16 Sai ya ɗauki yaran ya rungume su yana tattaɓa su,
yana sa musu albarka.

Saurayi Mai Dukiya
(Mat 19.16-30; Luk 18.18-30)

17 Da Yesu zai tashi yă bar wurin ke nan, sai ga wani mutum
ya zo da gudu, ya durƙusa a gabansa, ya tambaye shi ya ce,
"Malam mai kirki, me zan yi in sami rai na har abada?"
18 Sai Yesu ya ce masa, "Don me kake ce da ni mai kirki?
Ai, ba wani mai kirki sai Allah kaɗai. 19 Ka dai san abin da dokoki
suka ce, 'Kada ka yi kisankai. Kada ka yi zina. Kada ka yi sata.
Kada ka yi shaidar ƙarya. Kada ka cuci mutum. Ka ba da girma
ga babanka da mamarka.' "
20 Sai saurayin ya ce, "Malam, ai, duk na kiyaye waɗannan
tun ina yaro."

10.4: M. Sh 24.1-4; Mat 5.31 **10.6**: Far 1.27; 5.2 **10.7-8**: Far 2.24
10.11-12: Mat 5.32; 1 Kor 7.10-11 **10.15**: Mat 18.3
10.19: Fit 20.12-16; M. Sh 5.16-21

21 Yesu ya dube shi da duban ƙauna, ya ce masa, "Abu ɗaya
ne tak ka rasa. Ka je ka sayar da duk abin da kake da shi, ka ba
talakawa, za ka sami dukiya mai yawa a sama. Sa'an nan ka zo
ka bi ni." 22 Da jin wannan magana sai saurayin ya ɓata fuska,
ya tafi yana baƙin ciki, don shi mai arziki ne sosai.

23 Sai Yesu ya dubi almajiransa, ya ce musu, "Zai zama da
wuya sosai masu arziki su shiga mulkin Allah!" 24 Almajiran
kuwa suka yi mamakin wannan magana. Sai Yesu ya sāke ce
musu, "Ku 'ya'yana, zai zama da wuya sosai fa, mutum[m] yă shiga
mulkin Allah! 25 Zai fi wa rakumi sauƙi yă bi ta ramin allura, da
mai arziki yă shiga mulkin Allah."

26 Da jin wannan, almajiran suka ƙara mamaki suna tambayar
juna cewa, "To, in haka ne, wa zai iya samun ceto?"

27 Yesu ya dube su ya ce, "A wurin mutane kam, ba zai yiwu
ba. Amma a wurin Allah zai yiwu. Domin kowane abu mai
yiwuwa ne a wurin Allah."

28 Sa'an nan Bitrus ya ta da magana ya ce, "Ga shi mu mun
bar dukan kome mun bi ka."

29 Yesu ya ce, gaskiya ina gaya muku, wanda ya bar gidansa,
ko 'yan'uwansa, ko mamarsa, ko babansa, ko 'ya'yansa, ko
gonakinsa, saboda ni da kuma bishara, 30 abin da zai samu a
zamanin nan ma, zai fi sau ɗari, na gidaje, da 'yan'uwa, da
iyaye, da 'ya'ya, da gonaki, amma tare da tsanani. Sa'an nan a
wurin zaman matattu, sai rai na har abada. 31 Mutane da yawa
da suke na farko, za su zama na ƙarshe. Na ƙarshe kuma, za su
zama na farko.

Yesu Ya Sāke Yin Magana Game da Mutuwarsa

(Mat 20.17-19, Luk 18.31-34)

32 Suna haurawa zuwa Urushalima ke nan, Yesu yana a gaba,
almajiran kuma suna binsa suna mamaki. Waɗanda suke binsu a
baya kuma suna tsoro. Sai Yesu ya ja su sha biyun nan gefe ya
sāke faɗa musu abin da zai faru da shi. Ya ce, 33 "Ga shi za mu
je Urushalima. Za a ba da Ɗan Mutum a hannun manyan firistoci
da malaman dokoki. Za su yanke masa hukuncin kisa, su ba da
shi ga waɗanda ba Yahudawa ba. 34 Za su yi masa ba'a, su tofa
masa miyau, su yi masa bulala, su kashe shi. Bayan kwana uku
zai tashi da rai."

10.31: Mat 20.16; Luk 13.30

[m] **10.24 mutum**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā sun ƙara, "mai arziki"
ko kuwa "wanda ya dogara ga arziki."

Yakubu da Yohanna Sun Yi Roƙo
(Mat 20.20-28)

35 Ana nan, sai 'ya'yan Zabadi, Yakubu da Yohanna, suka zo
wurin Yesu, suka ce, "Malam, muna so mu roƙe ka wani abu."
36 Sai ya ce, "Me kuke so in yi muku?"
37 Suka ce, "Muna roƙonka a ranar da za ka shiga ɗaukakar
mulkinka, ɗayanmu yă zauna a hannun damarka, ɗayan kuma yă
zauna a hannun hagunka."
38 Amma Yesu ya ce musu, "Ba ku san abin da kuke roƙo
ba. Za ku iya sha daga kwaf nan na wahala da zan sha? Ko kuwa
za ku iya a yi muku baftisma da baftisma da za a yi mini?"
39 Suka amsa suka ce, "I, za mu iya."
Yesu ya ce musu, "I, za ku sha kwaf da zan sha, za a yi muku
baftisma kuma da baftismar da za a yi mini. 40 Amma zama a
damana, ko a haguna, ba ni nake da ikon bayarwa ba. Waɗannan
wurare na waɗanda aka riga aka shirya musu ne."
41 Da sauran almajiran nan goma suka ji wannan, sai suka fara
jin haushin Yakubu da Yohanna. 42 Yesu ya kira su ya ce musu,
"Kun sani, a cikin waɗanda ba Yahudawa ba, waɗanda aka san su
da mulki, sukan nuna wa mutanensu iko, manyansu ma suna nuna
wa mutanensu iko. 43 Amma ba haka zai zama a tsakaninku ba. A
maimakon haka, duk wanda yake so yă zama babba a cikinku, dole
ne yă bauta wa sauran. 44 Kuma duk wanda yake so yă zama
shugaba a cikinku, lallai ne yă zama bawan kowa. 45 Gama Ɗan
Mutum ya zo ba domin a yi masa bauta ba, amma domin yă yi
bauta, yă kuma ba da ransa domin ceton mutane da yawa."

Makaho Ya Sami Ganin Gari
(Mat 20.29-34; Luk 18.35-43)

46 Sai suka kai Jeriko. Yana fita daga Jeriko ke nan, da shi,
da almajiransa, da mutane da yawa, sai ga wani makaho yana
zaune a gefen hanya yana bara. Sunansa kuwa Bartimawus ne,
wato, ɗan Timawus. 47 Da ya ji cewa Yesu Banazare ne yake
wucewa, ya fara ɗaga murya yana cewa, "Ya Yesu Ɗan
Dawuda,[n] ka ji tausayina!"

10.38: Luk 12.50 **10.42-43:** Luk 22.25-26
10.43-44: Mat 23.11; Mar 9.35; Luk 22.26
[n] **10.47 Ɗan Dawuda:** Yahudawa sun gaskata cewa Almasihu zai fita daga zuciyar sarki Dawuda.

48 Wadansu da yawa suka kwabe shi, cewa yă yi shiru. Amma sai ya ƙara ɗaga murya sosai yana cewa, "Ya Ɗan Dawuda, ka ji tausayina!"

49 Sai Yesu ya tsaya ya ce, "Ku kira mini shi."

Sai suka kirawo makahon, suka ce masa, "Ka yi murna! Tashi, yana kiranka."

50 Sai ya yar da mayafinsa, ya yi wuf! Ya tashi ya tafi wurin Yesu.

51 Yesu ya tambaye shi ya ce, "Me kake so in yi maka?"

Sai makahon ya amsa ya ce, "Maigida, ina so in sami ganin gari."

52 Sai Yesu ya ce masa, "Tafi, bangaskiyarka ta warkar da kai."

Nan da nan ya sami ganin gari, ya bi Yesu, suka tafi.

Yesu Ya Shiga Urushalima

(Mat 21.1-11; Luk 19.28-40; Yoh 12.12-19)

11 1 Da suka zo kusa da Urushalima, wato, a Betafaji da Betani, wajen Dutsen Itatuwan Zaitun, sai Yesu ya aiki almajiransa biyu, 2 ya ce musu, "Ku je ƙauyen can na gabanku. Da shigarku za ku ga wani ɗan jaki a ɗaure, wanda ba a taɓa hawa ba. Ku kunce shi ku kawo. 3 Idan wani ya tambaye ku, 'Don me kuke haka?' Sai ku ce masa, 'Ubangiji ne yake bukatarsa, zai kuma mai da shi nan da nan.' "

4 Sai suka tafi, suka ga ɗan jakin a ɗaure a ƙofar gida a bakin hanya. Suna kuncewa ke nan, 5 sai wadanda suke tsaye a wurin suka ce musu, "Yaya? Don me kuke kunce jakin nan?"

6 Suka ba da amsa daidai yadda Yesu ya faɗa musu, sai mutanen suka bar su su tafi da jakin. 7 Da suka kawo wa Yesu jakin, suka shimfiɗa rigunansu a kai, sai Yesu ya hau ya zauna. 8 Sai mutane da yawa suka shimfiɗa rigunansu a kan hanya, wadansu kuma suka baza ganyen da suka sare daga gonaki. 9 Wadanda suke gabansa da wadanda suke bayansa suka yi ta kururuwa suna cewa,

"Yabo ya tabbata ga Allah!
Albarka ta tabbata ga mai zuwa
a cikin sunan Ubangiji!
10 Albarka ta tabbata ga mulkin nan
mai zuwa na babanmu Dawuda.
Yabo ya tabbata ga Allah."

11.9: Zab 118.25-26 **11.10:** 2 Sam 7.11-14

11 Da Yesu ya shiga Urushalima, ya tafi haikali ya shiga ya dudduba dukan kome. Da yake rana ta fādi ko, sai ya fita ya koma Betani tare da almajiransa.

Yesu Ya La'anta Itacen Baure
(Mat 21.18-19)

12 Washegari da suka tashi daga Betani, sai Yesu ya ji yunwa.
13 Da ya hangi wani itacen ɓaure mai ganye, sai ya je yă ga ko
zai sami 'ya'ya. Amma da ya kai wurin, bai ga kome ba sai ganye
kawai, don ba lokacin 'ya'yan ɓaure ba ne. 14 Sai ya ce wa ɓauren,
"Kada kowa yă ƙara cin 'ya'yanka har abada!" Almajiransa kuwa
suka ji abin da ya faɗa.

Yesu Ya Tsabtace Haikali
(Mat 21.12-17; Luk 19.45-48; Yoh 2.13-22)

15 Da shigarsu Urushalima, Yesu ya shiga haikali ya fara korar
masu saye da sayarwa daga ciki. Ya kuma tutture teburorin masu
canjin kudi da kujerun masu sayar da tattabaru. 16 Ya kuma hana
kowa yă ɗauki wani abu yă wuce ta filin haikalin. 17 Sai ya koya
wa mutane ya ce, "A rubuce yake cewa, 'Za a ce da gidana gidan
addu'a na dukan al'ummai.' Ga shi kun mai da shi 'wurin ɓuyan
'yan fashi.' "

18 Manyan firistoci da malaman dokoki suka ji wannan
magana, suka fara neman hanyar da za su kashe shi, gama suna
jin tsoronsa, domin dukan taron suna mamakin koyarwarsa.

19 Da yamma kuwa, Yesu da almajiransa suka fita daga cikin
birnin.

Bauren da Yesu Ya La'anta Ya Bushe
(Mat 21.20-22)

20 Da safe suna wucewa, sai suka ga itacen ɓauren nan ya
bushe tun daga saiwarsa. 21 Bitrus ya tuna, sai ya ce wa Yesu,
"Malam, duba! Bauren nan da ka la'anta ya bushe!"

22 Yesu ya amsa ya ce, "Ku gaskata da Allah! 23 Gaskiya
ina gaya muku, idan mutum ya gaskata da Allah, zai iya faɗa
wa dutsen nan yă tashi yă jefa kansa cikin teku. In bai yi shakka
a zuciyarsa a kan abin da ya faɗa ba, za a yi masa. 24 Don haka
ina dai gaya muku, kome kuka roƙa da addu'a, ku gaskata cewa
kun riga kun samu, zai kuwa zama naku. 25 Kuma a kowane
lokacin da kuke tsayawa kuna addu'a, in akwai wanda kuke jin

11.17: Ish 56.7; Irm 7.11 **11.23**: Mat 17.20; 1 Cor 13.2

haushinsa, ku yafe masa, domin Ubanku wanda yake cikin sama shi ma yă yafe muku laifofinku."[o]

Ana Shakkar Iznin Yesu
(Mat 21.23-27; Luk 20.1-8)

27 Suka sāke shiga Urushalima. Yesu yana zagawa ke nan cikin haikalin, sai manyan firistoci, da malaman dokoki da shugabannin jama'a suka zo wurinsa. 28 Suka ce masa, "Da wane izni kake yin waɗannan abubuwa? Kuma wa ya ba ka iznin yin wannan?"

29 Yesu ya amsa ya ce, "Zan yi muku wata tambaya. Ku ba ni amsa, ni kuwa zan gaya muku ko da wane izni nake yin abubuwan nan. 30 Ku faɗa mini, iznin da Yohanna ya yi baftisma da shi, Allah ne ya ba shi, ko kuwa mutum?"

31 Sai suka fara gardama a tsakaninsu, suka ce, "Idan muka ce, 'Daga wurin Allah ne,' zai ce mana, 'To, don me ba ku gaskata shi ba?' 32 Amma za mu iya cewa daga wurin mutum ne kuwa?" (Suna jin tsoron abin da mutane za su yi musu, domin dukan mutane sun ɗauka cewa Yohanna annabi ne.) 33 Sai suka amsa wa Yesu suka ce, "Ba mu sani ba."

Yesu ya ce musu, "Ni ma, ba zan faɗa muku ko da wane izni nake yin abubuwan nan ba."

Misali a Kan Masu Noma da Suka Karɓi Hayar Gonar Inabi
(Mat 21.33-46; Luk 20.9-19)

12 1 Yesu ya ci gaba da magana yana ba su misalai. Ya ce, "Wani mutum ya yi gonar inabi, ya kewaye ta da katanga, ya haƙa ramin matsin 'ya'yan inabin, ya kuma gina wata rumfa mai tsayi don yin gadi. Ya ba waɗansu manoma hayar gonar, sa'an nan ya tafi wata ƙasa. 2 Da lokacin girbin inabin ya yi, sai ya aiki wani bawansa wurin waɗanda suka karɓi hayar gonar yă karɓo masa waɗansu 'ya'yan inabi daga gonar. 3 Amma 'yan hayar suka kama shi, suka yi masa dūka, suka sallame shi hannu wofi. 4 Sai ya sāke aika musu wani bawa. Suka bugi wannan mutum a kai, suka yi masa wulaƙanci. 5 Ya sāke aiken wani, wannan kuwa manoman suka kashe shi. Ya aika waɗansu kuma da yawa; manoman suka dūke waɗansu, suka kashe waɗansu. 6 Har yanzu dai yana da sauran mutum

11.25-26: Mat 6.14-15 **12.1**: Ish 5.1-2

[o] **11.25** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya ta 26 haka "Amma in ba kwa yafewa, haka Ubanku da yake cikin sama ma ba zai yafe muku laifofinku ba."

ɗaya, wato ɗansa, wanda yake ƙauna. A ƙarshe ya aike shi wurinsu, yana cewa, 'Ai, za su ba ɗana girma.' 7 Amma 'yan hayan nan suka ce wa juna, 'Yawwa! Ga wanda zai ci gādon gonar. Ku zo mu kashe shi, don gādonsa yă zama namu.' 8 Sai suka kama shi, suka kashe shi, suka jefar da gawar a bayan katangar gonar."

9 Yesu ya tambaye su, ya ce, "To, me mai gonan nan zai yi? Ai, zai zo yă halaka 'yan hayan nan, yă ba da gonar ga waɗansu.

10 Ashe, ba ku taɓa karanta wannan rubutaccen maganar Allah ba?
Don a rubuce yake cewa,

'Dutsen da masu gini suka ƙi,
Shi ne ya zama dutsen da ya fi amfani duka a cikin ginin.
11 Wannan yin Ubangiji ne,
abin mamaki ne kuwa a idanunmu.' "

12 Sai shugabannin Yahudawa suka nemi hanyar da za su kama shi, don sun gane a kansu ne ya yi misalin. Amma suka ji tsoron jama'a. Don haka suka bar shi, suka tafi.

Tambaya game da Biyan Haraji ga Kaisar

(Mat 22.15-22; Luk 20.20-26)

13 Ana nan, sai aka aika wasu daga cikin Farisiyawa da mutanen Hirudus, domin su sa wa Yesu tarko a cikin maganar da zai faɗa. 14 Da suka iso, suka ce masa, "Malam, mun sani kai mai gaskiya ne. Mutane duk ɗaya ne a gare ka, gama ba ka kula da darajar wani fiye da wani ba. Kuma kana koyar da hanyar Allah a cikin gaskiya. Kana gani daidai ne mu biya wa Kaisar wato, babban sarkin Roma haraji, ko a'a? 15 Mu biya, ko kada mu biya?" Amma Yesu ya gane munafuncinsu, ya ce musu, "Me ya sa kuke sa mini tarko? Ku kawo mini kuɗin da ake biyan haraji da shi."

16 Sai suka kawo masa, sai ya ce musu, "Hoton nan da sunan nan na wane ne?"

Suka ce masa, "Na Kaisar ne."

17 Sai Yesu ya ce musu, "To, ku ba Kaisar abin da yake na Kaisar; ku kuma ba Allah abin da yake na Allah." Sai suka yi mamakinsa ƙwarai.

12.10-11: Zab 118.22-23

Tambaya a kan Tashin Matattu
(Mat 22.23-33; Luk 20.27-40)

18 Waɗansu Sadukiyawa suka zo wurin Yesu. Su ne suke
cewa, wai ba tashin matattu. Suka tambaye shi suka ce,
19 "Malam, Musa ya rubuta mana cewa idan ɗan'uwan mutum
ya mutu, ya bar matarsa ba ɗa, dole ne mutumin yă auri matar,
yă haifa wa ɗan'uwansa 'ya'ya. 20 To, akwai waɗansu 'yan'uwa
maza guda bakwai. Na farkon ya yi aure, ya mutu bai bar ɗa
ba. 21 Na biyun kuma ya aure ta, shi ma ya mutu, ba ɗa. Na
ukun ma haka. 22 Haka dai duka bakwai dîn, ba wanda ya bar
ɗa. A ƙarshe kuma ita matar ta mutu. 23 To, a tashin matattu za
ta zama matar wane ne a cikinsu? Gama duk bakwai dîn sun
aure ta."

24 Sai Yesu ya amsa, ya ce musu, "Ai, tunaninku ba daidai
ba ne don ba ku san Rubutattun Maganar Allah ba, ba ku kuma
san ikon Allah ba. 25 Lokacin da matattu za su tashi, maza ba
za su yi aure ba, mata kuma ba za a ba da su ga aure ba, amma
za su zama kamar mala'ikun da suke cikin sama ne. 26 Game
da tashin matattu kuwa, ashe, ba ku taɓa karanta wannan a
littafin Musa ba, don an rubuta cikin labarin ɗanyen itace da
ya kama wuta, cewa, 'Ni ne Allah na Ibrahim, da na Ishaku,
da kuma na Yakubu?' 27 Shi ba Allah na matattu ba ne, amma
na masu rai. Kun yi babban kuskure."

Doka Mafi Girma
(Mat 22.34-40; Luk 10.25-28)

28 Wani malamin dokoki ya zo ya ji suna mahawara da juna.
Da ya lura cewa Yesu ya ba su amsa mai kyau, sai ya tambaye
shi ya ce, "Wace doka ce mafi girma duka?"

29 Yesu ya amsa, ya ce, "Mafi girma ita ce, 'Ku ji ni, ya
Isra'ila, Ubangiji Allahnmu, Ubangiji ɗaya ne. 30 Sai ka ƙaunaci
Ubangiji Allahnka da dukkan zuciyarka, da dukkan ranka, da
dukkan hankalinka, da kuma dukkan ƙarfinka.' 31 Mai biye da
ita ita ce, 'Ka ƙaunaci abokin zamanka kamar yadda kake
ƙaunar kanka.' Ba wata doka da ta fi waɗannan girma."

32 Sai malamin dokokin ya ce wa Yesu, "Daidai ne ka faɗa
malam, Ubangiji ɗaya ne, ba kuwa wani sai shi. 33 A ƙaunace shi
kuma da dukkan zuciya, da dukkan tunani, da dukkan ƙarfi, ka

12.18: A. M. 23.8 **12.19**: M. Sh 25.5 **12.26**: Fit 3.6 **12.29-30**: M. Sh 6.4-5
12.31: L. Fir 19.18 **12.32**: M. Sh 4.35

kuma ƙaunaci abokin zamanka kamar kanka, ai, ya fi dukkan hadayar ƙone-ƙone da yanke-yanke girma."

34 Da Yesu ya ga yadda ya yi masa magana da hikima, sai ya ce masa, "Kana kusa da mulkin Allah fa." Bayan wannan kuma ba wanda ya yi ƙarfin hali yă ƙara tambayarsa wani abu.

Tambaya a kan Almasihu
(Mat 22.41-46; Luk 20.41-44)

35 Sa'ad da Yesu yake koyarwa a haikali sai ya yi tambaya ya ce, "Yaya malaman dokoki suke cewa Almasihu ɗan Dawuda ne? 36 Dawuda da kansa, ta ikon Ruhu Mai Tsarki ya ce,

'Ubangiji ya ce wa Ubangijina,
zauna a damana,
Sai na sa ka a kan abokan gābanka.'

37 Dawuda da kansa ya ce da Almasihu 'Ubangiji'. To, yaya Almasihu zai zama ɗa a wurin Dawuda?"

Yesu Ya Tona Asirin Malaman Dokoki
(Mat 23.1-36; Luk 11.37-54, 20.45-47)

Da jin irin wannan magana a bakin Yesu, jama'a suka ji daɗi. 38 A cikin koyarwarsa, Yesu ya ce, "Ku yi hankali da malaman dokoki, su masu son sa manyan riguna suna yawo. Suna so a gaishe su a kasuwa. 39 Suna so kuma a ba su wuraren zama masu daraja a majami'u, da wuraren zama masu kyau a wurin biki. 40 Su ne masu cin kayan matan da mazansu suka mutu. Sa'an nan su yi doguwar addu'a don a gan su. Ai, su za a yi musu hukunci mafi tsanani."

Baikon Macen da Mijinta Ya Mutu
(Luk 21.1-4)

41 Yesu yana zaune a haikali wurin da ake zuba baiko, yana duban yadda jama'a suke zuba kuɗinsu a akwatin baiko. Waɗansu masu arziki da yawa suna zuba kuɗi mai yawa. 42 Sai ga wata matalauciya wadda mijinta ya mutu, ta zo ta zuba 'yan tagulla biyu, da ba su kai kobo ba. 43 Sai Yesu ya kira almajiransa, ya ce musu, "Gaskiya, ina gaya muku, abin da matalauciyan nan wadda mijinta ya mutu, ta zuba cikin akwatin, ya fi na sauransu duka. 44 Dukansu sun bayar daga yawan abin da suke da shi ne, amma ita kuwa daga cikin talaucinta ta ba da dukan kome, har ma dukan abin da take dogara da shi."

12.33: Hos 6.6 **12.28-34**: Luk 10.25-28 **12.36**: Zab 110.1

Yesu Ya Faɗa Irin Rushewar da Za Ta Sami Haikali
(Mat 24.1-2; Luk 21.5-6)

13 1 Yesu yana fitowa ke nan daga haikali, sai ɗaya daga cikin almajiransa ya ce masa, "Malam, dubi manyan duwatsun nan, da gine-ginen nan masu ban mamaki!"



Hoton haikali a lokacin Yesu (13.1-2)

2 Sai Yesu ya ce masa, "Ka ga dukan waɗannan manyan gine-gine? Za a rushe su duka. Ba za a bar ko dutse ɗaya a kan ɗan'uwansa ba."

Farkon Wahaloli
(Mat 24.3-14, 21.7-19)

3 Yesu yana zaune a kan Dutsen Itatuwan Zaitun wanda yake fuskantar haikalin, sai Bitrus, da Yohanna, da Andarawus suka tambaye shi a ɓoye, suka ce, 4 "Ka gaya mana, yaushe ne za a yi waɗannan abubuwa? Wace alama ce za a gani a lokacin da suke shirin faruwa?"

5 Sai Yesu ya ce musu, "Ku lura fa, kada wani yă ruɗe ku. 6 Mutane da yawa za su zo a cikin sunana, suna cewa su ne ni, har su rudî mutane da yawa. 7 Idan kuma kuka ji labarin yaƙe-yaƙe da jita-jitarsu, kada hankalinku yă tashi. Dole ne wannan yă faru, amma ƙarshen bai zo ba tukuna. 8 Al'umma za ta tasar wa al'umma, mulki yă tasar wa mulki. Za a yi ta girgizar ƙasa a wurare dabam-dabam, za a kuma yi yunwa. Amma duk waɗannan ba ainihin azabar ba ne. Masomin azaba ne kawai.

9 "Sai ku kula da kanku, don za su kai ku kotu a kuma yi
muku dūka a majami'u. Za a kai ku gaban shugabanni da
sarakuna saboda sunana, domin ku shaida Labari Mai Dadi a
gabansu. 10 Amma kafin ƙarshen yă zo, dole ne a yi wa dukan
al'ummai bishara tukuna. 11 Duk lokacin da suka kama ku suka
kai ku kotu, kada ku damu a kan abin da za ku faɗa. Ku dai
faɗa duk abin da ya zo muku a wannan lokaci, domin ba ku ne
kuke magana ba, Ruhu Mai Tsarki ne. 12 Dan'uwa zai ba da
ɗan'uwansa a kashe shi, baba kuma yă ba da ɗansa. 'Ya'ya
kuma za su tayar wa iyayensu har su sa a kashe su. 13 Kowa
zai ƙi ku saboda sunana. Amma duk wanda ya jimre har zuwa
ƙarshe, zai tsira.

Muguwar Wahala
(Mat 24.15-28; Luk 21.20-24)

14 "Za ku ga mummunar aiki mai ban ƙyama da yake kawo
rushewa yana tsaye a wurin da bai kamata ba (bari mai karatu fa
yă gane). To, sai waɗanda suke cikin Yahudiya su gudu zuwa
cikin duwatsu. 15 Wanda yake kan rufin ɗaki kuma kada yă sauko
yă shiga cikin gida wai zai ɗauki wani abu.



Hoton Kan Rufin Daki (13.15)

16 Wanda yake a gona kuma kada yă koma wai zai ɗauki
mayafinsa. 17 Kaiton mata masu ciki da masu goyo a wannan

13.9-11: Mat 10.17-20; Luk 12.11-12 **13.13**: Mat 10.22
13.14: Dan 9.27; 11.31; 12.11 **13.15-16**: Luk 17.31

lokaci! 18 Ku yi addu'a kada abubuwan nan su faru a lokacin
sanyi. 19 A lokacin nan za a yi wata wahala mai zafi sosai wadda
ba a taba yi ba tun farkon lokacin da Allah ya halicci duniya, har
zuwa yanzu. Ba kuwa za a kara yin irinta ba har abada. 20 Da ba
don Ubangiji ya rage kwanakin nan ba, da ba dan Adam da zai
tsira. Amma saboda tausayin wadanda ya zaba, sai ya rage tsawon
kwanakin.

21 "A lokacin nan duk wanda ya ce muku, 'Duba, ga Almasihu
nan!' ko, 'Duba, ga shi can!' kada ku yarda. 22 Almasihan karya
da annabawan karya za su fiffito, za su nuna alamu da abubuwan
ban mamaki, don su rudi mutane har ma da wadanda aka zaba,
idan zai yiwu. 23 Saboda haka, ku lura! Na gaya muku dukan
kome tun da wuri.

Dawowar Dan Mutum

(Mat 24.29-31; Luk 21.25-28)

24 "Amma a lokacin nan, wato, bayan wahalan nan mai zuwa,
za a sa rana ta yi duhu. Wata kuma ba zai yi haske ba. 25 Taurari
za su rika fadowa daga sararin sama. Za a kuma girgiza manyan
abubuwan da suke sararin sama.[s] 26 Sa'an nan za a ga Dan Mutum
yana zuwa a cikin girgije da iko mai girma da daukaka. 27 Sa'an
nan zai aiko mala'ikunsa su tattaro wadanda ya zaba daga gabas,
da yamma, da kudu, da arewa; wato daga wannan bangon duniya
zuwa wancan.

Koyarwa a kan Itacen Baure

(Mat 24.32-35)

28 "Ku koyi wani abu daga itacen baure. Idan rassansa sun
fara sākewa, suna fitar da sabon ganye, kun san damina ta yi kusa
ke nan. 29 Haka kuma idan kuka ga wadannan abubuwa suna
faruwa, ku san lokaci ya yi kusa, yana dab da bakin kofa.
30 Gaskiya ina gaya muku, mutanen zamanin nan ba za su mutu
ba, sai duk abubuwan nan sun faru. 31 Sama da kasa za su kare,
amma maganata ba za ta kare ba ko kadan.

13.19: Dan 12.1; A. M. 7.14
13.24: Ish 13.10; Ez 32.7; Jow 2.10; 3.4; 4.15; A. M. 6.12
13.25: Ish 34.4; Jow 2.10; A. M. 6.13 **13.26**: Dan 7.13; A. M. 1.7

[s] **13.25 manyan abubuwa da suke sararin sama:** A zamanin dā, mutane sun dauka cewa taurarin sama suna da iko a kan abin da yake faruwa a kasa. (Dubi Ish 13.10, 34.4).

Ba Wanda Ya San Ranar Zuwan Almasihu
(Mat 24.36-44; Luk 17.26-30,34-36)

32 "Amma ba wanda ya san ranar, ko a ƙarfe nawa ne da
wannan zai faru, ko mala'ikun da suke sama, ko Ɗan, sai dai
Uban kaɗai. 33 Ku lura, ku zauna da shiri,[f] domin ba ku san lokaci,
ko a ƙarfe nawa ne wannan zai faru ba. 34 Kamar mutum ne mai
tafiya, in ya tashi, yakan ba da gidan a hannun yaransa,
kowannensu da aikin da zai yi. Sa'an nan yă faɗa wa mai gadi
yă zauna a shirye. 35 Saboda haka, ku zauna da shiri, don ba ku
san lokacin da maigidan zai dawo ba. Gama zai iya dawowa ko
da yamma, ko da tsakar dare, ko da carar zakara, ko kuwa da
safe. 36 Kada yă zo ba labari, yă same ku kuna barci. 37 Abin da
nake gaya muku, ina gaya wa kowa ne, ku zauna da shiri!"

Shugabanni Sun Yi Shawara Su Kashe Yesu
(Mat 26.1-5; Luk 22.1-2; Yoh 11.45-53)

14 1 Sauran kwana biyu a yi Bikin Ketarewa da Bikin
Burodi Marar Yisti,[u] sai manyan Firistoci da malaman
dokoki suka nemi hanya su kama Yesu a ɓoye, su kashe shi.
2 Amma suna cewa, "Ba dai a lokacin biki ba, don kada mutane
su ta da rikici."

An Shafa wa Yesu Man Kamshi a Betani
(Mat 26.6-13; Yoh 12.1-8)

3 Yesu yana Betani a gidan wani mutum wanda ake ce da shi
Siman Maikuturta. Yana cin abinci ke nan, sai ga wata mace ta
zo da wata 'yar kwalabar da aka gina da dutsen alabasita cike da
man ƙamshi mai tsada sosai wanda aka yi da nardi zalla. Sai ta
fashe kwalabar ta zuba man a kan Yesu. 4 Wadansu kuwa da suke
wurin suka ji haushi, suka ce wa juna, "Yaya aka ɓata wannan
mai haka? 5 Da an sayar da shi kuwa, da an sami yawan kuɗin
da ake biyan lebura yini ɗari uku a ba talakawa, ai, da ya fi!"
Sai suka tsawata wa matar sosai.

6 Amma Yesu ya ce, "Ku bar ta mana. Don me kuke damunta?
Ai, abu mai kyau ne ta yi mini. 7 Talakawa suna tare da ku kullum.
Ko yaushe kuke so, kwa iya yi musu alheri, amma ba kullum ne
nake tare da ku ba. 8 Ta yi iyakacin ƙoƙarinta. Ta shafa jikina da

---

13.32: Mat 24.36 **13.34**: Luk 12.36-38 **14.1**: Fit 12.1-27 **14.3**: Luk 7.37-38
14.7: M. Sh 15.11

[f] **13.33 da shiri**: Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā sun ƙara "Kuna addu'a" a nan.

[u] **14.1 Bikin Ketarewa**: Dubi ma'anar wadansu kalmomi.

mai don shirin jana'izata. [9] Gaskiya ina gaya muku, duk inda za a yi bisharan nan a duniya duka, za a rika fadin abin da macen nan ta yi don tunawa da ita."

Yahuda Ya Yarda Yă Ba da Yesu
(Mat 26.14-16; Luk 22.3-6)

10 Ana nan, sai Yahuda Iskariyoti daya daga cikin almajirai sha biyun nan, ya je wurin manyan firistoci don yă bashe Yesu a gare su. [11] Da suka ji haka suka yi murna sosai, har suka yi alkawari za su ba shi kudi. Yahuda kuwa ya fara neman hanya yă bashe shi.

Yesu Ya Ci Abincin Bikin Ketarewa Tare da Almajiransa
(Mat 26.17-25; Luk 22.7-14,21-23; Yoh 13.21-30)

12 A ranar farko ta Bikin Burodi Marar Yisti, wato ran da akan yanka dan rago na Bikin Ketarewa, sai almajiran Yesu suka tambaye shi suka ce, "Ina kake so mu je mu shirya maka cin Bikin Ketarewa?"

13 Sai ya aika almajiransa guda biyu, ya ce musu, "Ku shiga gari. Can za ku gamu da wani mutum yana dauke da tulun ruwa. Ku bi shi. [14] Duk gidan da ya shiga, ku ce wa maigidan, 'Malam yana tambaya cewa ina dakin da zai ci Bikin Ketarewa da almajiransa?' [15] Shi kuwa zai nuna muku wani babban dakin sama wanda aka gama gyararsa don bikin. A wurin za ku shirya mana abinci."

16 Sai almajiran suka tashi, suka shiga cikin gari, suka kuwa samu abubuwa kamar yadda Yesu ya fada musu. Sai suka shirya abincin Bikin Ketarewa.

17 Da yamma ta yi, Yesu da almajiransa sha biyun nan suka zo gidan. [18] Suna cin abinci ke nan, sai Yesu ya ce, "Gaskiya ina gaya muku, daya daga cikinku zai bashe ni, wanda yanzu yake cin abinci tare da ni."

19 Sai almajiran suka fara bakin ciki, suna ce masa da daya-daya, "Ko ni ne?"

20 Yesu ya amsa, ya ce, "Daya daga cikinku sha biyun nan ne dai, wanda muke ci daga kwarya daya. [21] Dan Mutum zai mutu, kamar yadda yake a rubuce game da shi. Amma kaiton wanda zai ba da Dan mutum! Zai fiye wa mutumin nan da ma ba a haife shi ba."

14.18: Zab 41.9

Jibin Ubangiji
(Mat 26.26-30; Luk 22.14-23; I Kor 11.23-25)

22 Suna cikin cin abinci, sai Yesu ya ɗauki burodi, ya yi godiya ga Allah, ya kakkarya, ya ba almajiransa, ya ce, "Ku karɓa, wannan jikina ne."

23 Bayan wannan kuma, ya ɗauki kwaf na ruwan inabi ya yi godiya ga Allah, ya ba su. Dukansu kuwa suka sha daga ciki. 24 Sa'an nan ya ce musu, "Wannan jinina ne. Jini na cikar alkawari. Za a zubar da shi saboda mutane da yawa. 25 Ina gaya muku gaskiya, ba zan ɓara shan ruwan inabin nan ba, sai dai a ranar da zan sha wani sabon a mulkin Allah."

26 Bayan da suka rera waƙa, sai suka fita suka tafi Dutsen Itatuwan Zaitun.

Bitrus Zai Yi Mūsun Sanin Yesu
(Mat 26.31-35; Luk 22.31-34; Yoh 13.36-38)

27 Yesu ya ce wa almajiransa, "Dukanku za ku gudu ku bar ni, kamar yadda aka rubuta cewa,

'Zan bugi makiyayin,
tumakin kuma za su gudu.'

28 Amma bayan da na tashi daga matattu, zan riga ku zuwa Galili."

29 Sai Bitrus ya ce masa, "Ko dukansu sun gudu sun bar ka, ni kam, ba zan bar ka ba."

30 Yesu ya ce masa, "Gaskiya ina gaya maka, yau, a cikin daren nan, kafin zakara yă yi cara sau biyu, za ka yi mūsun sanina sau uku."

31 Amma Bitrus ya yi ta maimaitawa da ɓarfi yana cewa, "Ko da za a kashe ni tare da kai, ba zan yi mūsun saninka ba sam."

Dukan sauran almajiransa ma suka faɗa haka.

Yesu Ya Yi Addu'a a Getsemani
(Mat 26.36-46; Luk 22.39-46)

32 Suka tafi wani wurin da ake ce da shi Getsemani, wato wurin matsin 'ya'yan zaitun sai Yesu ya ce wa almajiransa, "Ku zauna a nan. Zan je in yi addu'a." 33 Sai ya ɗauki Bitrus, da Yakubu, da Yohanna tare da shi. Ana nan, sai ya fara damuwa ɓwarai, har jikinsa ya yi sanyi. 34 Sai ya ce musu, "Baƙin ciki da yake a raina zai iya kashe ni. Ku zauna a nan, ku yi tsaro."

14.24: Fit 24.8; Irm 31.31-34 **14.27**: Zak 13.7 **14.28**: Mat 28.16

35 Da ya je gaba kaɗan, sai ya fāɗi a ƙasa, ya yi addu'a ya
ce, idan ya yiwu, a ɗauke masa wannan lokacin wahala. 36 Ya ce,
"Abba,[w] Uba, kowane abu mai yiwuwa ne a gare ka. Ka ɗauke
mini wannan kwaf na wahala. Duk da haka dai, ka yi abin da
kake so, ba abin da ni nake so ba."

37 Bayan wannan, sai ya dawo ya sami almajiran nan uku suna
barci. Sai ya ce wa Bitrus, "Bitrus, kana barci ne? Ashe, ba za
ka iya tsaro ko da awa ɗaya ba? 38 Ku yi tsaro kuna kuma addu'a
don kada ku fāɗi cikin jaraba. Lallai ruhu ya ɗauka, amma jikin
ba ƙarfi."

39 Sai ya sāke komawa, ya yi addu'a, yana maimaita maganar
dā. 40 Sa'an nan ya sāke dawowa, ya same su suna barci don
idanunsu sun cika da barci sosai. Suka kuma rasa abin da za su
faɗa masa.

41 Sai ya je ya dawo, na uku ke nan, ya ce musu, "Har yanzu
barci kuke yi kuna hutawa? Shi ke nan! Lokaci ya yi da za a ba
da Ɗan Mutum ga hannun masu zunubi. 42 Ku tashi mu tafi! Ga
mai bashe ni nan ya iso!"

An Kama Yesu
(Mat 26.47-56; Luk 22.47-53; Yoh 18.3-12)

43 Yesu yana cikin magana ke nan, sai ga Yahuda, ɗaya daga
cikin almajiransa sha biyun nan, ya zo tare da mutane da yawa
suna rike da takuba da sanduna. Manyan firistoci, da malaman
dokoki, da shugabanni ne suka turo su. 44 Yahuda, wanda zai ba
da Yesu kuwa, ya riga ya shirya da su cewa, "Wanda zan
rungume shi, shi ne mutumin. Ku kama shi ku tafi. Ku rike shi
da kyau."

45 Da zuwan Yahuda, sai ya mike zuwa wurin Yesu, ya ce
masa, "Malam!" Sai ya rungume shi. 46 Sai mutanen kuwa suka
kama Yesu suka rike shi da ƙarfi. 47 Amma ɗaya daga cikin
almajiran Yesu wanda yake tsaye kusa, ya zare takobinsa, ya sari
bawan babban firist, ya yanke masa kunne. 48 Yesu ya ce musu,
"Kun fito da takuba da sanduna ku kama ni sai ka ce ɗan fashi?
49 Kowace rana ina tare da ku a haikali ina koyarwa, ba ku kama
ni ba. Ba kome. An yi haka ne fa domin annabcin Rubutattun
Maganar Allah yă cika."

50 Daga nan dukan almajiran suka bar shi, suka gudu.

14.49: Luk 19.47; 21.37

[w]**14.36 Abba:** Wannan kalmar da yaren Aramaya ce mai ma'ana "Baba".

51 Akwai wani saurayi tare da masu bin Yesu, ba shi da riga,
sai mayafi kawai. Da mutanen suka yi ƙoƙarin kama shi, 52 sai
ya bar mayafinsa a hannunsu ya gudu tsirara.

Yesu a Gaban 'Yan Majalisa
(Mat 26.57-68; Luk 22.54-55, 63-71; Yoh 18.13-14,19-24)

53 Suka kai Yesu wurin babban firist, sai manyan firistoci,
da shugabanni, da kuma malaman dokoki suka taru duk a wurin.
54 Bitrus kuma ya bi Yesu, amma daga nesa. Ya bi shi har cikin
filin gidan babban firist dîn. A wurin ya zauna tare da
dogarawan haikalin, yana jin ɗumin wuta. 55 Manyan firistoci
da sauran 'yan majalisa suna ta neman wani abu da za a yi
shaida a kan Yesu cewa ya yi laifi don su kashe shi, amma ba
su samu ba. 56 Mutane da yawa kam sun yi shaidar ƙarya, amma
bakinsu bai zo ɗaya ba.

57 Daga baya waɗansu suka tashi tsaye, suka yi wa Yesu
shaidar ƙarya suka ce, 58 "Mun ji ya ce, wai zai rushe haikalin nan
da mutane suka gina, yă gina wani cikin kwana uku, wanda ba
ginin mutum ba." 59 Duk da haka dai shaidarsu ba ta zo ɗaya ba.

60 Sai babban firist ya tashi ya tsaya a tsakiyarsu, ya tambayi
Yesu, ya ce, "Ba ka da wata amsa? Shaidar da suke bayar a
kanka fa?"

61 Amma Yesu ya yi shiru, bai ba shi ko amsa ba.

Sai babban firist dîn ya sāke tambayarsa, "Ko kai ne Almasihu
Ɗan Mai Albarka?"

62 Yesu ya amsa ya ce, "Ni ne. Kuma za ku ga Ɗan Mutum
zaune a hannun dama Mai Iko, yana kuma zuwa
cikin girgije na sararin sama."

63 Sai babban firist dîn ya yage rigunansa, ya ce, "Wace
shaida kuma muke bukata? 64 Kun dai ji renin da ya yi wa Allah!
Mene ne ra'ayinku?"

Sai dukan mutane suka yanke masa shari'a cewa a kashe shi.

65 Waɗansu ma suka fara tottofa masa miyau, suka ɗaure masa
idanu, suka kuma mammare shi, suna ce masa, "Faɗa wanda ya
mare ka!" Dogarawan haikalin kuma suka yi ta yin masa dūka.

Bitrus Ya Yi Mūsun Sanin Yesu
(Mat 26.69-75; Luk 22.56-62; Yoh 18.15-18,25-27)

66 Bitrus kuwa yana ƙasa a filin gidan, sai wata yarinya a
cikin ma'aikatan babban firist ta zo wurin. 67 Da ta ga Bitrus yana

14.58: Yoh 2.19 **14.62:** Dan 7.13 **14.64:** L. Fir 24.16

jin ɗumin wuta, sai ta dube shi da kyau, ta ce masa, "Ai, kai ma kana tare da Yesu Banazaren nan!"

68 Amma Bitrus ya yi mūsu, ya ce, "Ban san ma abin da kike magana ba. Ban gane ba sam!" Da faɗar haka, sai ya tashi ya je zauren gidan. Nan da nan sai zakara ya yi cara.[y]

69 Da yarinyar ta sāke gan shi a wurin, sai ta faɗa wa waɗanda suke tsaye a wurin, "Wannan ma ɗaya daga cikinsu ne." [70] Sai Bitrus ya sāke yin mūsu kuma.

Bayan ɗan lokaci kaɗan, waɗanda suke tsaye kusa da Bitrus suka ce masa, "Ba shakka, kai ma ɗaya daga cikinsu ne; kai ba mutumin Galili ba ne?"

71 Amma Bitrus ya fara zagi yana la'anta kansa, yana rantsuwa kuma a gabansu, yana cewa, "Ban ma san mutumin nan da kuke maganarsa ba."

72 Nan da nan sai zakara ya yi cara sau na biyu. Sai Bitrus ya tuna da maganar da Yesu ya faɗa masa cewa, "Kafin zakara yă yi cara sau biyu, za ka yi mūsun sanina sau uku." Da ya tuna wannan magana, sai ya fashe da kuka.

An Kai Yesu a Gaban Gwamna Bilatus

(Mat 27.1-2,11-14; Luk 23.1-5; Yoh 18.28-38)

15 [1] Da sassafe manyan firistoci da shugabanni, da malaman dokoki, da dukkan sauran 'yan majalisa suka yi shawara. Sai suka ɗaure Yesu, suka tafi da shi, gaban Bilatus. [2] Bilatus kuwa ya tambaye shi ya ce, "Kai ne sarkin Yahudawa?"

Yesu ya amsa masa ya ce, "Kai ne ka faɗa haka."

3 Sai manyan firistoci suka yi ta zarginsa a kan abubuwa da yawa. [4] Sai Bilatus ya sāke tambayarsa ya ce, "Ga shi fa, ana zarginka a kan abubuwa da yawa, ba za ka ba da amsa ba?"

5 Amma har yanzu, Yesu bai ƙara yi wata magana ba, har abin ya dami Bilatus.

An Yanke wa Yesu Hukuncin Mutuwa

(Mat 27.15-26; Luk 23.13-25; Yoh 18.39-19.16)

6 Abin da sarki ya saba yi a lokacin Bikin shi ne, yakan sakar musu ɗan kurkuku ɗaya wanda mutanen suka roƙa. [7] To, akwai wani mai suna Barabbas wanda yake a ɗaure a kurkuku, tare da 'yan tawaye da suka kashe mutum a lokacin da aka yi tawaye. [8] Sai taron jama'a suka zo suka fara roƙon Bilatus yă

[y] **14.68 sai zakara ya yi cara:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da waɗannan kalmomin.

yi musu abin da ya saba yi. 9 Bilatus ya amsa musu ya ce, "Kuna
so in sakar muku sarkin Yahudawa?" 10 Gama ya gane cewa
saboda kishi ne ya sa manyan firistoci suka ba da Yesu a
hannunsa.

11 Amma manyan firistoci suka zuga jama'a su ce yă saki
Barabbas a maimakon Yesu. 12 Sai Bilatus ya tambaye su ya ce,
"To, me zan yi da wanda kuke ce da shi sarkin Yahudawa?"

13 Suka ta da murya suka ce, "A gicciye shi!"

14 Bilatus kuwa ya ce musu, "Don me? Wane laifi ne ya yi?"
Sai suka ƙara ta da murya suna cewa, "A gicciye shi!"

15 Da yake Bilatus yana so yă faranta wa jama'a zuciya, sai
ya sake musu Barabbas. Bayan ya sa aka yi wa Yesu bulala, sai
ya ba da shi don a gicciye shi.

Sojoji Sun Yi wa Yesu Ba'a
(Mat 27.27-31; Yoh 19.2-3)

16 Sojojin suka tafi da Yesu a zauren bariki, wato fadar
gwamna wanda ake ce da shi "Firetoriyum". Suka tara dukan
sauran sojojin. 17 Suka sa masa wata jar riga irin ta sarakuna, suka
kuma yi wani rawani na ƙaya, suka sa masa a kai. 18 Sai suka
fara yi masa gaisuwa suna cewa, "Ranka yă daɗe, sarkin
Yahudawa!" 19 Suka kuma yi ta bubbuga shi a kai da sanda, suna
tottofa masa miyau. Sa'an nan suka durƙusa wai suna yi masa
ban girma.

20 Da suka gama yi masa ba'a haka, sai suka cire masa rigar
sarauta ɗin, suka sa masa nasa riguna. Sa'an nan suka kai shi
waje don a gicciye shi.

An Gicciye Yesu
(Mat 27.32-44; Luk 23.26-43; Yoh 19.17-27)

21 Suna cikin tafiya, sai ga wani mutum yana wucewa, mai
suna Siman, mutumin Sayirin, baban Alekzanda da Rufus, yana
zuwa daga ƙauye, suka sa shi dole yă ɗauki gicciyen Yesu. 22 Suka
kai Yesu wani wuri mai suna Golgota, wato wurin ƙoƙon kai.
23 A wurin suka miƙa masa ruwan inabi gauraye da mur,[z] amma
ya ƙi sha. 24 Sai suka gicciye shi. Suka kuma rarraba rigunansa a
tsakaninsu, suka yi kuri'a a kansu don su ga abin da kowa zai
samu. 25 Da ƙarfe tara na safe ne suka gicciye shi. 26 A gungumen
itacen kuwa an rubuta sanarwar zargin da aka yi masa cewa,

15.21: Rom 16.13 **15.24:** Zab 22.19
[z] **15.23 Mur:** Wani magani ne wanda yakan rage zafin ciwo a jikin mutum.

"Sarkin Yahudawa." 27 Suka kuma gicciye 'yan fashi biyu tare
da shi, ɗaya a hannun damarsa, ɗaya kuma a hannun hagunsa.[a]
29 Mutanen da suke wucewa suka yi ta zaginsa, suna kaɗa
kai, suna cewa, "Ahaf! Kai da za ka rushe haikali, za ka kuma
gina shi cikin kwana uku, 30 to, ka ceci kanka ka sauko mana!"
31 Haka kuma manyan firistoci da malaman dokoki suka yi ta
yi masa ba'a a tsakaninsu suna cewa, "Ya ceci waɗansu, amma
bai iya ceton kansa ba! 32 Bari wannan Almasihu, wai sarkin
Isra'ila, yă sauko yanzu daga gicciyen nan, don mu gani mu ba
da gaskiya!" 'Yan fashin da aka gicciye tare da shi ma suka yi
masa baƙar magana.

Mutuwar Yesu
(Mat 27.45-56; Luk 23.44-49; Yoh 19.28-30)

33 Da tsakar rana, sai duhu ya rufe dukan ƙasar, har zuwa
ƙarfe uku na yamma. 34 Sa'an nan da ƙarfe uku, Yesu ya ɗaga
murya da ƙarfi ya ce, *"Eloi, Eloi, lama sabaktani?"* Wato, "Ya
Allahna, ya Allahna, don me ka yashe ni?"
35 Da waɗanda suke tsaye a wurin suka ji haka, suka ce, "Ga
shi, yana kiran annabi Iliya." 36 Sai ɗayansu ya gudu, ya jiƙa soso
da ruwan tsami, ya soka a sanda ya miƙa wa Yesu don yă sha,
ya ce, "Ku tsaya dai! Bari mu gani ko annabi Iliya zai zo yă
sauko da shi."
37 Sai Yesu ya ɗaga murya da ƙarfi, sa'an nan ya mutu.
38 Sai labulen da yake cikin haikali[b] ya yage kashi biyu tun
daga sama har ƙasa.
39 Lokacin da soja wanda yake tsaye a gaban Yesu ya ga yadda
ya mutu, sai ya ce, "Ba shakka, wannan mutum Ɗan Allah ne!"
40 Waɗansu mata kuma suka tsaya can da nisa suna kallo.
Cikinsu kuwa akwai Maryamu daga Magadala, da Maryamu
mamar Yakubu ƙarami da Yusufu, da kuma Salomi. 41 Tun daga
Galili ne waɗannan matan suka biyo shi suna yi masa hidima.
Waɗansu mata kuma da yawa waɗanda suka zo tare da shi a
Urushalima suna wurin ma.

15.28: Ish 53.12 **15.29**: Zab 22.8; Zab 109.25; Mar 14.58; Yoh 2.19
15.34: Zab 22.1 **15.36**: Zab 69.22 **15.38**: Fit 26.31-33 **15.40-41**: Luk 8.2-3

[a] **15.28** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya ta 28 "Wannan shi ne cikar annabcin da ya ce, 'An lissafta shi a cikin masu laifi.' "

[b] **15.38 labulen . . . haikali**: Wato, yadin da aka rufe ƙofar Wurin Mafi Tsarki a haikali.



Hoton labulen da ya yage kashi biyu (15.38)

Jana'izar Yesu
(Mat 27.57-61; Luk 23.50-56; Yoh 19.38-42)

42 Da yamma ta yi, ana shiri[c] don gobe Ranar Hutawa ce.
43 Sai wani mutum mai suna Yusufu daga Arimatiya ya zo. Shi ɗan majalisa ne, mai daraja kuwa, wanda yake marmarin mulkin
Allah yă zo. Ya yi ƙarfin hali ya je wurin Bilatus, ya roƙa a ba
shi jikin Yesu. 44 Bilatus ya yi mamaki da ya ji cewa Yesu ya
riga ya mutu. Sai ya kira soja dîn ya tambaye shi ko gaskiya
ne Yesu ya riga ya mutu. 45 Da ya tabbatar daga bakin sojan
nan, sai ya ba Yusufu jikin.

46 Yusufu kuwa ya sayo yadin lilin, ya sauko da jikin Yesu,
ya nannaɗe shi a yadin lilin, ya sa shi a kabarin da aka haƙa a
jikin dutse. Sa'an nan ya gangaro da wani dutse ya rufe bakin
kabarin.

47 Maryamu daga Magadala da Maryamu mamar Yusufu suna
kallo, suka ga inda aka kwantar da jikin Yesu.

[c] **15.42 ana shiri:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

Tashin Yesu daga Matattu
(Mat 28.1-8; Luk 24.1-12; Yoh 20.1-10)

16 [1] Da Ranar Hutun Yahudawa ta wuce, Maryamu daga Magadala, da Maryamu mamar Yakubu, da kuma Salomi, suka sayo kayan ƙamshi domin su je su shafa wa jikin Yesu. [2] A ranar farko ta mako, da sassafe wajen fitowar rana suka tafi kabarin. [3] Da suke kan hanya, suka ce wa juna, "Wa zai ture mana dutsen daga bakin kabarin?" [4] Amma da suka kai wurin, suka ɗaga kai suka ga, ashe, an riga an ture dutsen. Babban dutse ne kuwa.

5 Da suka shiga kabarin, sai suka ga wani saurayi a zaune a gefen dama, da farar riga a jikinsa, sai suka ji tsoro.

6 Sai saurayin ya ce musu, "Kada ku yi mamaki. Kuna neman Yesu Banazare wanda aka gicciye? Ai, ya tashi. Ba ya nan. Ga inda aka kwantar da shi ma! [7] Yanzu sai ku tafi ku gaya wa almajiransa, har da Bitrus, cewa zai riga su zuwa Galili, a can ne za su gan shi kamar yadda ya faɗa musu."

8 Matan kuwa suka fita da gudu, sun ruɗe suna rawar jiki. Ba su kuma ce wa kowa kome ba, domin suna jin tsoro.

Yesu Ya Bayyana Kansa ga Maryamu
(Mat 28.9-10; Yoh 20.11-18)

[9] Da Yesu ya tashi daga matattu da sassafe a rana ta farko ta mako, ya fara nuna kansa ga Maryamu daga Magadala, wato macen nan da Yesu ya fitar mata da aljanu bakwai. [10] Ita kuwa ta tafi ta faɗa wa mutanen da suke tare da shi tun dā, waɗanda suke baƙin ciki suna ta kuka. [11] Amma da suka ji cewa Yesu yana da rai, har ma ta gan shi, ba su ba da gaskiya ba.

Yesu Ya Nuna Kansa ga Almajirai Biyu
(Luk 24.13-35)

12 Bayan haka Yesu ya canza kamanni ya nuna kansa ga waɗansu biyu daga cikin almajiran a lokacin da suke tafiya ƙauye. [13] Sai biyun nan suka koma suka faɗa wa sauran, amma har yanzu suka ƙi su yarda da labarin.

Aikin da Yesu Ya Ba Almajiransa
(Mat 28.16-20; Luk 24.36-49; Yoh 20.19-23; A. M. 1.6-8)

14 Daga baya Yesu ya nuna kansa ga sha ɗayan a daidai lokacin da suke cin abinci. Sai ya tsawata musu a kan rashin

---

16.7: Mat 26.32; Mar 14.28

bangaskiyarsu da taurinkansu, don ba su gaskata waɗanda suka gan shi bayan tashinsa ba.

15 Ya kuma ce musu, "Ku tafi ko'ina a dukkan duniya, ku yi wa dukkan 'yan Adam bishara. 16 Duk wanda ya ba da gaskiya, aka kuma yi masa baftisma, zai sami ceto. Amma duk wanda ya ƙi ba da gaskiya za a hukunta shi. 17 Ga abubuwan da masu bina za su yi don shaidar gaskiyarsu. A cikin sunana za su fitar da aljanu, za su kuma yi magana da sababbin harsuna. 18 Za su ɗauki macizai da hannayensu. Idan kuma suka sha dafi, ba zai yi musu kome ba. Za su kuma sa hannayensu a kan marasa lafiya, su warke."

An Ɗauke Yesu zuwa Sama
(Luk 24.50-53; A. M. 1.9-11)

19 Bayan da Ubangiji Yesu ya yi musu wannan jawabi, sai aka ɗauke shi aka kai shi cikin sama, ya zauna a hannun dama na Allah. 20 Almajiran kuwa suka fita, suka yi ta wa'azi ko'ina. Ubangiji kuwa ya yi aiki tare da su, yana nuna gaskiyar maganarsu ta wurin abubuwan ban mamakin da ya sa su suka yi tare da maganar.][d]

16.15: A. M. 1.8 **16.19**: A. M. 1.9-11
[d] **16.9-20** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da ayoyin nan.

BISHARA TA HANNUN

LUKA

Gabatarwa

Marubucin wannan bishara shi ne Luka. Shi ba Bayahude ba ne kuma shi likita ne. Shi kuma ba ɗaya ba ne cikin almajiran Yesu kamar sauran marubutan Littattafan Bisharar Yesu, ko da yake akwai alama ya sadu da waɗansu daga cikin almajiran Yesu (1.2). Ana zato an rubuta bisharan nan tsakanin A.D. 59-63, ko kuwa A.D. 70-80. Mai yiwuwa ne an rubuta ta a Roma. An rubuta Bisharan zuwa ga Tiyofilus ne ko da yake saƙon domin kowa da kowa ne.

Bishara ta Hannun Luka ta fara gabatar da Yesu cewa shi ne mai ceton Isra'ila da duniya duka. Bisharar ta fara da labari mai farin ciki na sanarwar haihuwar Yesu, ta kuma ƙare da labari mai farin ciki na tashin Yesu zuwa sama. A cikin bisharar, Luka ya nuna yadda Yesu ya damu sosai da mutanen da suke da damuwa.

Akwai labaru da bisharan nan ce kaɗai ta ba da su. Misalin irin waɗannan labaru su ne: Haihuwar Yohanna mai baftisma (1.5-25, 57-80), da na zuwan mala'ika wajen Maryamu (1.26-38). Da kuma yabo da mala'iku suka yi da ziyarar masu kiwo lokacin haihuwar Yesu (2.8-20), da kuma addu'ar Simiyon da ta Anna a haikali (2.25-38). Waɗansu labarun kuma su ne: Miƙawar Yesu a haikali (2.41-52), ta da yaron macen da mijinta ya mutu (7.11-17), ziyarar Yesu ga Maryamu da Marta (10.38-42), ziyarar gidan Zakka da Yesu ya yi (19.1-10). Har yanzu akwai misalin Basamariyen da ya nuna tausayi (10.29-39), mai arziki da Li'azaru (16.19-31), Bafarisiyi da mai karɓar haraji (18.9-14), da kuma bayyanuwarsa ga almajiran nan biyu da suke tafiya a hanya zuwa Imawus.

A cikin wannan *Bishara ta Hannun Luka* an yi magana sosai a kan addu'a, da Ruhu Mai Tsarki, da hidimar da mata suka yi wa Yesu cikin aikinsa, da kuma irin tausayin da Allah ya nuna wa 'yan Adam har ya yafe zunubansu.

Marubucin wannan Bishara ya ci gaba da ba da labarin a littafin *Ayyukan Manzanni* yadda masu bin Yesu sun ƙaru sun kuma bazu.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-4
Haihuwa da girmar Yohanna Maibaftisma da ta Yesu
1.5—2.52
Aikin Yohanna Maibaftisma 3.1-20
Baftismar Yesu da gwajinsa a daji 3.21—4.13
Aikin Yesu a Galili 4.14—9.50

Yesu ya bar Galili zuwa Urushalima 9.51—19.27
Ayyukan Yesu na ƙarshe, da hukuncinsa da mutuwarsa 19.28—23.56
Tashin Yesu daga matattu, da bayyanuwarsa, da kuma tashinsa zuwa sama 24.1-53

Gabatarwa

1 [1] Mutane da yawa sun yi ƙoƙari su rubuta labarin abubuwan
da suka faru a tsakaninmu. [2] Sun rubuta abin nan da muka ji
daga bakin waɗanda suka ga waɗannan abubuwa da idanunsu tun
farko, suka kuma yi shelar maganar Allah. [3] Saboda haka, mai
girma Tiyofilus, da yake na bincika abubuwan nan duka a hankali
tun daga farkonsu, na ga ya yi kyau in rubuta maka su bi da bi,
[4] domin ka san gaskiyar abubuwan nan kamar yadda aka koyar
maka da su.

An Ba da labarin Haihuwar Yohanna Maibaftisma

5 A lokacin da Hirudus yake sarautar Yahudiya, akwai wani
firist mai suna Zakariya, na sashin firistoci na gidan Abija. Sunan
uwargidansa kuma Alisabatu; ita kuma ta fito daga zuriyar gidan
Haruna ne. [6] Dukansu biyu, sun yi zama mai kyau a gaban Allah,
sun kuma bi dokoki da umarnan Ubangiji duka kamar yadda ya
ce a yi. [7] Amma ba su da 'ya'ya domin Alisabatu ba ta haihuwa,
kuma da Zakariya da ita duk sun tsufa.

8 Wata rana, Zakariya yana aikinsa na firistoci a cikin haikali,[a]
bisa ga tsarin da aka yi don hidima ta kowace rana. [9] Bisa ga
al'ada wadda aka kafa don firistoci su bi, aka zaɓe shi domin yă
shiga cikin haikalin Ubangiji yă ƙone turare mai ƙamshi. Saboda
haka sai ya shiga haikalin, [10] mutane kuma suna waje, suna addu'a
a lokacin da yake ƙone turare mai ƙamshi.

11 Ba labari, sai ga mala'ikan Ubangiji ya bayyana masa, ya
tsaya a gefen dama na bagade, inda ake ƙone turare. [12] Da ganin
mala'ikan, sai gaban Zakariya ya fāɗi, tsoro kuma ya kama shi.
[13] Amma mala'ikan ya ce masa, "Kada ka ji tsoro, Zakariya; Allah
ya karɓi addu'arka, kuma uwargidanka Alisabatu za ta haifa maka
ɗa. Za ka sa masa suna Yohanna. [14] In an haife shi, za ka yi farin
ciki da murna sosai, mutane da yawa kuma za ku yi murna.
[15] Yaron nan zai zama babban mutum a gaban Ubangiji. Ba zai

1.5: 1 Tar 24.10
[a] **1.8 haikali:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.



Hoton Firist (1.8-9)

sha ruwan inabi ko wani abu mai sa buguwa ba. Za a cika shi da Ruhu Mai Tsarki tun kafin a haife shi. 16 Shi ne zai dawo da mutanen Isra'ila da yawa zuwa wurin Ubangiji Allahnsu. 17 Zai ja gaban Ubangiji, yă kuma yi aikinsa da dukan ƙarfinsa da kuma ƙarfin zuciya kamar annabi Iliya. Zai kawo zaman lafiya tsakanin iyaye da 'ya'yansu. Zai juyo da mutane masu rashin biyayya su zama mutane masu halin kirki, ta haka zai shirya wa Ubangiji mutanensa."

18 Sai Zakariya ya ce wa mala'ikan, "Yaya zan san cewa abin nan da ka faɗa haka zai kasance? Ga ni wani tsoho ne, uwargidana kuma haka."

19 Mala'ikan ya ce, "Ni ne Jibra'ilu da yake tsaya a gaban Allah. Allah ya aiko ni in zo in faɗa maka wannan Labari Mai Daɗi. 20 Amma ga shi ka ƙi ka yarda da sakon, wanda zai zama gaskiya idan kwanakin suka cika. Saboda haka, tun da ka ƙi ka

1.15: L. Kid 6.3 **1.17**: Mal 4.5-6 **1.19**: Dan 8.16; 9.21

yarda, ba za ka ƙara iya yin magana ba, sai ranar da alkawarin nan ya cika."

21 Mutane sun zauna suna jiran fitowar Zakariya, suna ta tunani komene ne ya sa ya daɗe haka a cikin haikalin. 22 Da ya fito bai iya yin magana da baki ba, sai sun gane cewa ya ga ru'uya a cikin haikalin. Sai ya riƙa yin musu magana da hannu, amma bai iya yin magana da bakinsa ba.

23 Da lokacin hidimarsa ya ƙare, sai ya koma gida. 24 Bayan 'yan kwanaki, sai uwargidansa Alisabatu ta yi ciki, sai ta ɓoye kanta har wata biyar. 25 Alisabatu ta ce, "A ƙarshe Ubangiji ya ji tausayina, ya cire mini kunya a cikin jama'a."

An Ba da Labarin Haihuwar Yesu

26 Alisabatu tana cikin wata shida ke nan da samun ciki, sai Allah ya aiki mala'ika Jibra'ilu zuwa wani gari a cikin Galili, da ake ce da shi Nazarat. 27 Ya aike shi yă kai saƙo wurin wata yarinyar da aka yi alkawari za ta auri wani mutum mai suna Yusufu, daga zuriyar sarki Dawuda. Sunan yarinyar kuwa Maryamu ne. 28 Da mala'ikan ya zo wurinta sai ya ce, "A gaishe ki! Ubangiji yana tare da ke, ya kuma sa miki albarkarsa!" [b]

29 Da Maryamu ta ji gaisuwan nan, sai ta damu ƙwarai, tana tunani ko wacce irin gaisuwa ce haka. 30 Sai mala'ikan ya ce mata, "Kada ki ji tsoro, Maryamu. Allah ya nuna miki alherinsa. 31 Ga shi za ki yi ciki, za ki kuma haifi ɗa, wanda za ki ba shi suna Yesu. [6] 32 Zai zama babban mutum, kuma za a ce da shi Ɗan Allah Maɗaukaki. Ubangiji Allah zai ba shi kujerar mulkin kakansa Dawuda. 33 Zai yi mulkin gidan Yakubu har abada, mulkinsa kuma ba zai ƙare ba!"

34 Maryamu ta ce wa mala'ikan, "Yaya wannan zai faru, tun da yake ban taɓa sanin namiji ba?"

35 Mala'ikan ya amsa ya ce, "Ruhu Mai Tsarki zai sauko a kanki, ikon Allah kuma zai rufe ki. Saboda haka yaron nan mai tsarki da za a haifa, za a ce da shi Ɗan Allah. 36 Ga shi Alisabatu 'yar'uwarki, wadda ake ce ba za ta haihu ba, yanzu ɗin nan, tana da ciki wata shida, duk da tsufanta. 37 Ai, ba abin da zai gagari Allah yi."

1.27: Mat 1.18 **1.31**: Mat 1.21 **1.32-33**: 2 Sam 7.12,13,16; Ish 9.7
1.33: Dan 2.44, 7.14, 7.27; Mik 4.7 **1.37**: Far 18.14

[b] **1.28 albarkarsa**: Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā sun ƙara, "Mai albarka kike a cikin mata".

[6] **1.31 Yesu**: Sunan "Yesu" a Helenanci shi ne "Joshuwa" a Ibraniyanci. Ma'anar sunan kuwa ita ce, "Allah yana ceto".

38 Maryamu ta ce, "To, ni baiwar Allah ce, bari yă zama mini
kamar yadda ka faɗa." Sai mala'ikan ya tafi.

Maryamu Ta Ziyarci Alisabatu

39 A kwanakin nan Maryamu ta yi shiri ta tafi da sauri zuwa
wani gari cikin duwatsun Yahudiya. 40 Ta shiga gidan Zakariya,
ta gai da Alisabatu. 41 Da jin gaisuwar, sai Alisabatu ta ji yaron
da yake cikinta ya yi motsi. Aka kuma cika Alisabatu da Ruhu
Mai Tsarki. 42 Sai ta ɗaga murya da ƙarfi ta ce, "Ke mai albarka
ce a cikin mata, yaron nan na cikinki kuma mai albarka ne!
43 Yaya wannan alheri ya zo kaina, har da mamar Ubangijina za
ta zo wurina? 44 Da na ji gaisuwarki, sai yaron da yake cikina ya
yi motsi sosai saboda murna. 45 Mai albarka ce ke da kika gaskata
cewa saƙon nan da Ubangiji ya aika miki zai zama gaskiya!"

Waƙar da Maryamu Ta Yi don Yabo

46 Maryamu ta ce,
"Zuciyata tana yabon Ubangiji.
47 Raina yana murna saboda Allah mai cetona,
48 domin ya tuna da ni, ko da yake ni baiwarsa ce wadda ba
kome ba!
Daga yanzu dukan mutane za su ce da ni mai albarka,
49 saboda manyan abubuwan da Allah Maɗaukaki ya yi mini.
Sunansa mai tsarki ne.
50 Daga zamani zuwa zamani yana jin tausayin waɗanda
suke ba shi girma.
51 Da hannunsa mai ƙarfi ya aikata manyan abubuwa. Ya
watsar da masu ɗaga kai da dukan abin da suke
taƙama da shi a zuciyarsu.
52 Ya sauko da sarakuna daga sarautarsu,
ya ɗaukaka waɗanda ba kome ba.
53 Ya ba wa masu yunwa abubuwan masu kyau, ya sallami
masu arziki hannu wofi.
54 Ya tuna da alkawarin da ya yi wa kakanninmu a dā,
na cewa, zai taimaki mutanensa Isra'ila masu yin masa
hidima.
55 ya cika alkawarinsa ga kakanninmu, da kuma ga Ibrahim
da 'ya'yansa har abada!"
56 Maryamu ta zauna da Alisabatu kamar wata uku, sa'an nan
ta koma gida.

1.48: 1 Sam 1.11 **1.52**: Ayu 5.11; 12.19 **1.46-55**: 1 Sam 2.1-10 **1.55**: Far 17.7

An Haifi Yohanna Maibaftisma

57 Da kwanakin haihuwarta suka cika, sai Alisabatu ta haifi ɗa. 58 Abokan zamanta da 'yan'uwanta suka yi murna sosai da suka ji ta haihu, suka taya ta farin ciki saboda wannan albarkar da Ubangiji ya yi mata.

59 Da yaron ya cika kwana takwas, sai suka zo domin su yi masa kaciya.[c] Dā ma sun so ne su sa masa sunan babansa, Zakariya, 60 amma mamar yaron ta ce, "A'a! Za a ce da shi Yohanna."

61 Sai suka ce, "Wane ne a danginku mai wannan suna?" 62 Sai suka tambayi baban yaron da hannu yă faɗa sunan da za a kira yaron da shi.

63 Sai ya sa a kawo masa allo, sai ya rubuta, "Sunansa Yohanna." Sai dukan mutanen da suke wurin suka yi mamaki! 64 Nan take Zakariya ya sami bakin magana kuma, ya fara yabon Allah. 65 Tsoro ya kama dukan abokan zamansu. Mutane suka ba da labarin abin nan da ya faru a ko'ina a ƙasa mai duwatsu ta Yahudiya. 66 Duka wanda ya ji wannan labarin, sai yă yi ta tunani, yana cewa, "Me yaron nan zai zama?" Domin an gane cewa Ubangiji yana tare da shi.

Zakariya Ya Yabi Allah

67 Ana nan sai Ruhu Mai Tsarki ya cika Zakariya, baban Yohanna, sai ya yi annabci cewa,

68 "Mu yabi Ubangiji, Allah na Isra'ila.
Ya zo yă taimaki mutanensa, yă kuma ba su 'yanci.
69 Ya ba mu Mai Ceto mai iko
daga gidan mai hidimarsa Dawuda.
70 Ya yi alkawari tun tuni
ta bakin annabawansa masu tsarki cewa,
71 zai cece mu daga hannun masu gāba da mu,
da dukan waɗanda ba sa son ganinmu.
72 Ya ce zai nuna wa iyayenmu jinƙai,
zai tuna da alkawarinsa mai tsarki,
73 alkawarin da ya yi tare da rantsuwa wa babanmu Ibrahim.
74 Ya ce zai cece mu daga hannun masu gāba da mu,
don mu bauta masa ba tsoro,
75 mu kasance da tsarki da kuma ayyuka masu kyau a
gaban Allah dukan kwanakinmu.
76 Kai kuma ɗan yaron nan,

1.59: L. Fir 12.3 **1.73**: Far 22.16-18

[c] **1.59 kaciya**: Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

za a ce da kai annabi na Allah Maɗaukaki.
Za ka riga Ubangiji zuwa,
don ka shirya masa hanya.
77 Za ka kawo wa mutanensa labari
cewa za su sami ceto ta wurin yafewar zunubansu.
78 Ta wurin yawan jinƙan nan na Allahnmu,
hasken nan na ceto zai ɓullo daga sama,
yă haskaka mu.
79 Za a haskaka masu zama a duhu,
da masu zama a inuwar mutuwa.
Za a bi da mu a hanyar salama."

80 Sai Yohanna ya yi girma, ya yi ƙarfi a cikin ruhaniya. Ya yi zamansa a daji sai lokacin da ya fito domin yin wa'azi ga mutanen Isra'ila.

Haihuwar Yesu
(Mat 1.18-25)

2 1 A kwanakin nan, Kaisar Augustas ya ba da umarni a ƙirga dukan mutanen da suke a ƙarƙashin mulkin Roma. 2 Wannan shi ne ƙirga na farko wanda aka yi lokacin da Kiriniyus yake mulkin ƙasar Suriya. 3 Dukan mutane suka koma garuruwansu domin a ƙirga su.

4 Yusufu ma ya bar garin Nazarat a cikin Galili ya je birnin Baitalami a cikin Yahudiya, wato, garin da aka haifi sarki Dawuda ke nan. Yusufu ya je can domin shi daga dangin Dawuda ne. 5 Ya tafi tare da Maryamu da aka yi alkawari zai aura, domin a ƙirga su tare. Lokacin nan kuwa tana da ciki. 6 Da suna can Baitalami, sai kwanakin haihuwarta suka yi. 7 Ta haifi ɗanta na fari, ta rufe shi da zanen goyo, ta kuma kwantar da shi a abin da ake ba wa dabbobi abinci a ciki, domin ba su sami ɗaki a masauki ba.

Masu Kiwo da Mala'iku

8 A wannan gefen ƙasar kuwa, akwai waɗansu masu kiwo suna kwana a fili, suna lura da dabbobinsu da dare. 9 Ba labari sai ga mala'ikan Ubangiji ya bayyana gare su, kuma ɗaukakar Allah ta haskaka su. Sai suka ji tsoro sosai. 10 Amma mala'ikan ya ce musu, "Kada ku ji tsoro! Gama na zo muku da Labari Mai Daɗi, wanda zai sa dukan mutane su yi farin ciki sosai. 11 A yau ɗin nan, a cikin birnin Dawuda, an haifa muku Mai Ceto,

---

1.76: Mal 3.1 **1.78:** Mal 4.2 **1.79:** Ish 9.2

Almasihu[d] Ubangiji! 12 Wannan ne zai zama muku alama, za ku
samu an rufe yaron da zanen goyo, an kuma kwantar da shi a
abin da ake ba wa dabbobi abinci a ciki."
13 Ba labari sai ga ƙungiyar mala'iku daga sama sun bayyana
tare da mala'ika na farin, suna yabon Allah suna cewa,
14 "Daukaka ga Allah a can cikin sama!
A duniya bari salama ta kasance tare da waɗanda
Allah yake jin daɗinsu!"
15 Da mala'ikun suka rabu da su suka koma sama, sai masu
kiwon suka ce wa junansu, "Bari mu je Baitalami mu ga abin
nan da ya faru, da Ubangiji ya gaya mana."
16 Sai suka tafi da sauri, suka ga Maryamu da Yusufu, suka
kuma ga yaron yana kwance a abin da ake ba wa dabbobi abinci
a ciki. 17 Da masu kiwon suka gan shi sai suka ba da labarin abin
da mala'ikan ya faɗa musu a kan yaron. 18 Dukan mutanen da
suka ji wannan labari, sai suka yi ta rińe baki suna mamakin abin
da masu kiwon nan suka ce. 19 Maryamu kuwa ta rińe dukan
waɗannan abubuwa, tana tunaninsu a zuciyarta. 20 Masu kiwon
kuma suka koma, suna ta yin waƙoƙin yabon Allah, saboda dukan
abin da suka ji, suka kuma gani. Kome ya faru kuwa kamar dai
yadda mala'ikan ya faɗa musu.

An Sa wa Yesu Suna

21 Da yaron ya yi kwana takwas, sai aka yi masa kaciya, aka
kuma ba shi suna Yesu, sunan da mala'ika ya bayar tun kafin a
yi cikinsa.

An Kai Yesu Haikali don Miƙawa

22 Da lokaci ya kai da Maryamu da Yusufu za su yi abin da
Dokar Musa ta ce a yi don tsabtacewa, sai suka ɗauki Yesu zuwa
Urushalima don su miƙa shi ga Ubangiji. 23 Haka yake a rubuce
a Dokar Ubangiji, "Duk ɗa na fari da aka haifa, za a ce da shi
mai tsarki na Ubangiji." 24 Suka kuma yi hadaya kamar yadda
Dokar Ubangiji ta faɗa cewa, "Kurciyoyi biyu ko 'yan tattabaru
biyu ne za a yanka."
25 To, a wannan lokaci kuwa akwai wani mutumin da yake
zama a Urushalima, da ake ce da shi Simiyon. Shi mutumin kirki
ne, mai bautar Allah, kuma yana jiran ranar da za a ceci Isra'ila.

2.21: L. Fir 12.3; Luk 1.31 **2.23:** Fit 12.2,12 **2.22-24**: L. Fir 12.6-8

[d] **2.11 Almasihu:** Da Ibraniyanci "Masiha" da helenanci "Kiristi". Ma'anar Almasihu ita ce wanda aka shafe, aka kuma keɓe.

Ruhu Mai Tsarki kuwa yana tare da shi. 26 Ruhu Mai Tsarki ya
faɗa masa cewa ba zai mutu ba sai ya ga Almasihun da Ubangiji
ya yi alkawari zai aiko. 27 Da Ruhu yana iza shi sai ya shiga
haikalin a lokacin da iyayen suka kawo Yesu haikali domin su yi
kamar yadda Dokar ta ce a yi, 28 sai Simiyon ya karɓi yaron a
hannunsa ya yi wa Allah godiya ya ce,

29 "Yanzu, ya Ubangiji, ka sallami bawanka lafiya,
kamar yadda ka yi alkawari,
30 gama idanuna sun ga cetonka,
31 ceton da ka shirya a gaban dukan mutane,
32 Hasken da zai bayyana ka ga waɗanda ba Yahudawa ba,
yă kuma kawo ɗaukaka ga mutanenka Isra'ila."

33 Baban yaron da mamarsa suka riƙe baki, suna mamakin
abubuwan nan da Simiyon ya faɗa a kansa. 34 Simiyon ya sa musu
albarka, ya ce wa Maryamu, mamar yaron, "Allah ya zaɓi yaron
nan domin yă zama dalilin faɗuwar waɗansu, da tashiwar
waɗansu da yawa a cikin Isra'ila. Zai zama alama daga wurin
Allah wadda mutane da yawa ba za su so ba. 35 Ta haka asirin
zukatansu zai tonu. Abin nan kuwa zai yi miki zafi kamar takobi
ne ya soki zuciyarki."

36 Akwai wata tsohuwar annabiya mai suna Hannatu, 'yar
Fanuwel na kabilar Ashiru. Ta yi zaman aure na shekara bakwai
ne kawai, 37 sai mijinta ya mutu. Yanzu shekarunta tamanin da hudu
ne.[d] Ba ta barin haikali, tana yin wa Allah sujada dare da rana ta
wurin, addu'a da azumi. 38 Daidai wannan lokaci, sai ta shigo, tana
yi wa Allah godiya, ta kuma yi magana a kan yaron nan ga dukan
waɗanda suke jiran Allah yă ba wa Urushalima 'yanci.

Yusufu da Maryamu Sun Koma Gidansu a Nazarat

39 Da Yusufu da Maryamu suka gama yin dukan abubuwan
da Dokar Ubangiji ta ce a yi, sai suka koma garinsu Nazarat a
Galili. 40 Yaron ya yi girma, ya kuma yi ƙarfi, yana cike da
hikima. Alherin Allah kuma yana tare da shi.

Yesu, Ɗan Yaro, a cikin Haikali

41 Kowace shekara iyayen Yesu sukan je Urushalima don
Bikin Ketarewa.[e] 42 Da Yesu ya cika shekaru goma sha biyu da

2.32: Ish 42.6; 49.6; 52.10 **2.39**: Mat 2.23 **2.41**: Fit 12.1-27; M. Sh 16.1-8

[d] **2.37 Yanzu shekarunta tamanin da hudu ne**: Wani juyi na waɗannan kalmomin shi ne, "Ta yi shekaru tamanin da hudu da take zama ba tare da mijinta ba."

[e] **2.41 Bikin Ketarewa**: Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

haihuwa, sai suka je bikin kamar yadda suka saba. 43 Da bikin ya ƙare, suka kama hanya don su koma gida, amma Yesu, ɗan yaron nan, ya tsaya a baya a Urushalima, ba da sanin iyayensa ba. 44 Su kuma suna tsammani yana cikin jama'a, saboda haka suka yi ta tafiya har yini guda. Sa'an nan suka fara nemansa cikin 'yan'uwansu da kuma abokansu, 45 amma ba su gan shi ba. Saboda haka suka koma Urushalima domin su neme shi a can. 46 A rana ta uku suka same shi yana zama a cikin haikali tare da malamai. Yana jinsu, yana kuma yi musu tambayoyi. 47 Dukan waɗanda suka ji shi, suka riƙe baki, suna mamakin ganewarsa da yadda yake ba da amsoshi. 48 Iyayensa suka yi mamakin ganinsa a nan, sai mamarsa ta ce masa, "Dana, don me ka yi mana haka? Ni da babanka mun damu sosai, da ba mu gan ka ba."

49 Ya amsa musu ya ce, "Don me kuke nemana? Ba ku sani cewa ya kamata in kasance a gidan Ubana[f] ba?" 50 Amma ba su gane komene ne yake nufi da maganarsa nan ba.

51 Sai ya tashi ya bi su, suka koma Nazarat tare, inda ya riƙa biyayya ga iyayensa. Mamarsa kuma ta riƙe dukan waɗannan abubuwa a zuciyarta. 52 Yesu ya yi ta ƙaruwa da hikima da tsayi, ya kuma sami farin jini daga wurin Allah da mutane kuma.

Wa'azin Yohanna Maibaftisma

(Mat 3.1-12; Mar 1.1-8; Yoh 1.19-28)

3 1 A cikin shekara ta goma sha biyar na mulkin Kaisar Tibariya ne; Buntus Bilatus yana mulkin Yahudiya; Hirudus yana sarautar Galili; ɗan'uwansa Filibus yana mulkin Ituriya da Tarakunitas; Lisaniyas yana sarautar Abiliya; 2 kuma Hanana da Kayafa su ne manyan firistoci. A wannan lokacin kuwa sai maganar Allah ta zo wa Yohanna ɗan Zakariya a daji. 3 Sai Yohanna ya je ko'ina a duk sashin Kogin Urdun, yana wa'azi mutane su tuba, a yi musu baftisma domin a yafe musu zunubansu. 4 Kamar yadda yake a rubuce a cikin littafin annabi Ishaya cewa, "Muryar mai kira a daji tana cewa,

'Ku shirya wa Ubangiji inda zai bi,
ku miƙe hanyoyinsa.
5 A ciccika kowane kwari,
a faffashe kowane dutse da kowane tudu.
A miƙe hanyar da take da kwana-kwana,

2.52: 1 Sam 2.26; K. Mag. 3.4

[f] **2.49 Kasance a gidan Ubana:** Wani juyi na waɗannan kalmomin shi ne "yi aikin da Ubana ya ba ni."

a gyara mummunar hanya don ta yi kyau.
6 Dukan mutane za su ga ceton Allah!' "

7 Saboda haka ne, Yohanna ya ce wa taron jama'ar da suka zo domin yă yi musu baftisma,[g] "Ku macizai! Wa ya gargaɗe ku ku guje wa hukuncin nan mai zuwa? 8 Ku yi ayyukan da za su nuna cewa kun tuba. Kada ku yi tunani a zuciyarku cewa, 'Ibrahim ne babanmu.' Gama ina faɗa muku, Allah yana da iko yi wa Ibrahim 'ya'ya da duwatsun nan. 9 An riga an sa bakin gatari a gindin itace. Duk itacen da bai ba da 'ya'ya masu kyau ba, sai a sare shi a jefa a wuta."

10 Sai mutane suka tambaye shi, "Me za mu yi ke nan?"

11 Ya amsa musu ya ce, "Duk wanda yake da riguna biyu, yă raba da wanda ba shi da ko ɗaya, wanda yake da abinci shi ma yă yi haka."

12 Masu karɓar haraji suka zo domin a yi musu baftisma, suka tambaye shi suka ce, "Malam, me za mu yi?"

13 Ya ce musu, "Kada ku karɓa fiye da abin da aka ce a karɓa."

14 Sojoji ma suka tambaye shi, "Mu fa? Me za mu yi?"

Sai ya ce musu, "Kada ku sa wa mutane dole su ba ku kuɗi, kuma kada ku yi ƙarya a kansu don sun ƙi su ba ku. Ku gode da abin da ake biyanku."

15 Da yake mutane suna jiran zuwan Almasihu, sai dukansu suka yi tunani a zuciya ko Yohanna shi ne Almasihu ɗin. 16 Sai Yohanna ya ce wa dukansu, "Ni, ina muku baftisma da ruwa ne, amma akwai wani yana zuwa wanda ya fi ni girma. Ban isa in kunce igiyar takalmansa ba. Shi ne zai yi muku baftisma da Ruhu Mai Tsarki da wuta kuma. 17 Yana riƙe da matankaɗinsa, zai tankaɗe hatsinsa, kuma yă tattara alkamarsa yă sa cikin rumbunsa. Amma zai ƙona yayin da wuta da ba a iya kashewa."

18 Da waɗansu gargaɗi masu yawa, Yohanna ya yi wa mutane wa'azin Labari Mai Daɗi. 19 Amma Yohanna ya tsawata wa gwamna Hirudus, domin shi Hirudus ya auri Hirudiya, matar ɗan'uwansa Filibus, ya kuma yi waɗansu mugayen abubuwa. 20 A ƙarshe, Hirudus ya ƙara ɓata al'amarin da iznin nan da ya bayar na cewa a kama Yohanna a kulle.

3.4-6: Ish 40.3-5 **3.7:** Mat 12.34; 23.33 **3.8:** Yoh 8.33 **3.9:** Mat 7.19
3.12: Luk 7.29 **3.19-20:** Mat 14.3-4; Mar 6.17-18
[g] **3.7 Baftisma:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

An Yi wa Yesu Baftisma
(Mat 3.13-17; Mar 1.9-11)

21 Bayan da aka yi wa dukan mutane baftisma, sai aka yi wa
Yesu shi ma. Da yana addu'a, sai sama ya buɗe, 22 Ruhu Mai
Tsarki ya sauko a kansa da wani kamanni kamar kurciya. Sai aka
ji wata murya daga sama ta ce, "Kai ne Ɗana, wanda nake ƙauna.
Ina jin daɗinka ƙwarai." [h]

Asalin Yesu
(Mat 1.1-17)

23 Lokacin da Yesu ya fara aikinsa na koyarwa, yana da
shekara talatin ne a duniya. Mutane sun ɗauke shi a kan shi ɗan
Yusufu ne, wanda yake ɗan Heli, 24 Heli ɗan Matat, Matat ɗan
Lawi, Lawi ɗan Malki, Malki ɗan Yanna, Yanna ɗan Yusufu,
25 Yusufu ɗan Matatiya, Matatiya ɗan Amos, Amos ɗan Nahum,
Nahum ɗan Azaliya, Azaliya ɗan Najaya, 26 Najaya ɗan Ma'ata,
Ma'ata ɗan Matatiya, Matatiya ɗan Shimeya, Shimeya ɗan Josek,
Josek ɗan Yahuda.

27 Yahuda ɗan Yowanan, Yowanan ɗan Refaya, Refaya ɗan
Zarubabel, Zarubabel ɗan Sheyaltiyel, Sheyaltiyel ɗan Niri, 28 Niri
ɗan Malki, Malki ɗan Addi, Addi ɗan Kosama, Kosama ɗan
Almadama, Almadama ɗan Er, 29 Er ɗan Joshuwa, Joshuwa ɗan
Eliyezer, Eliyezer ɗan Yorim, Yorim ɗan Matat, Matat ɗan Lawi,

30 Lawi ɗan Simiyon, Simiyon ɗan Yahuda, Yahuda ɗan
Yusufu, Yusufu ɗan Yonana, Yonana ɗan Eliyakim. 31 Eliyakim
ɗan Malaya, Malaya ɗan Mainana, Mainana ɗan Matata, Matata
ɗan Natan, Natan ɗan Dawuda. 32 Dawuda ɗan Jesse, Jesse ɗan
Obida, Obida ɗan Bo'aza, Bo'aza ɗan Salmon, Salmon ɗan
Nashon.

33 Nashon ɗan Amminadab, Amminadab ɗan Aram, Aram ɗan
Hesruna, Hesruna ɗan Feresa, Feresa ɗan Yahuda. 34 Yahuda ɗan
Yakubu, Yakubu ɗan Ishaku, Ishaku ɗan Ibrahim, Ibrahim ɗan
Tera, Tera ɗan Nahor, 35 Nahor ɗan Serug, Serug ɗan Reyu, Reyu
ɗan Feleg, Feleg ɗan Eber, Eber ɗan Shela.

36 Shela ɗan Kenan, Kenan ɗan Arfakshad, Arfakshad ɗan
Shem, Shem ɗan Nuhu, Nuhu ɗan Lamek, 37 Lamek ɗan
Metusela, Metusela ɗan Enok, Enok ɗan Yared, Yared ɗan

3.22: Far 22.2; Zab 2.7; Ish 42.1; Mat 3.17; Mar 1.11; Luk 9.35
[h] **3.22 Kai ne Ɗana . . . ina jin daɗinka ƙwarai:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da, "Kai Ɗana ne, yau na zama ubanka" ne a nan.

Mahalalel, Mahalalel ɗan Kenan, 38 Kenan ɗan Enosh, Enosh ɗan Shitu, Shitu ɗan Adamu, Adamu kuma ɗan Allah.

Shaiɗan Ya Gwada Yesu
(Mat 4.1-11; Mar 1.12-13)

4 1 Yesu ya dawo daga Kogin Urdun cike da Ruhu Mai Tsarki. Ruhu kuwa ya iza shi zuwa cikin daji, 2 inda Shaiɗan ya gwada shi na kwana arba'in. A ƙarshen wannan lokacin sai yunwa ta kama shi, don bai ci kome ba.

3 Sai Shaiɗan ya ce masa, "Idan kai Ɗan Allah ne, ka umarci wannan dutse yă zama burodi."

4 Yesu ya amsa masa ya ce, "An rubuta a cikin Maganar Allah cewa, 'Ba da abinci kaɗai mutum zai rayu ba.' " 5 Daga nan, Shaiɗan ya kai shi wani wuri mai tsayi sosai, ya nuna masa dukan mulkokin duniya a cikin ɗan lokaci. 6 Shaiɗan ya ce masa, "Zan ba ka iko a kan dukan waɗannan da duk ɗaukakarsu, domin dukan waɗannan an ba ni. Kuma zan iya ba wa duk wanda nake so in ba shi. 7 Dukan wannan zai zama naka idan dai ka yi mini sujada."

8 Yesu ya ce masa, "Gama a rubuce yake cewa,
'Ka yi wa Ubangiji Allahnka sujada,
kuma shi kaɗai za ka bauta masa!' "

9 Sai Shaiɗan ya ɗauke shi zuwa Urushalima, ya kai shi can bisa haikali, ya ce masa, "Idan kai Ɗan Allah ne, ka yi tsalle daga nan ka fāɗi ƙasa. 10 Don a rubuce yake cewa, 'Zai ba da umarni ga mala'ikunsa su lura da kai, su tsare ka.' 11 Da kuma, 'Za su tare ka da hannayensu don kada ka buga ƙafafunka a dutse.' "

12 Amma Yesu ya ce masa, "A rubuce yake kuma cewa, 'Kada ka gwada Ubangiji Allahnka.' "

13 Da Shaiɗan ya gama gwada Yesu a ta kowane gefe, sai ya bar shi na ɗan lokaci.

Yesu Ya Fara Hidimarsa a Galili
(Mat 4.12-17; Mar 1.14-15)

14 Sai Yesu ya koma Galili, ikon Ruhu Mai Tsarki kuma yana tare da shi. Labarinsa ya kai ko'ina a kewayen. 15 Ya yi ta koyarwa a majami'unsu,[i] kowa yana ta yabonsa.

4.4: M. Sh 8.3 **4.8:** M. Sh 6.13 **4.10:** Zab 91.11 **4.11:** Zab 91.11-12
4.12: M. Sh 6.16
[i] **4.15 majami'a:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

An Ki Yesu a Nazarat
(Mat 13.53-58; Mar 6.1-6)

16 Daga nan sai Yesu ya zo Nazarat, inda ya yi girma. Ya shiga majami'a a Ranar Hutun Yahudawa wato, Asabar kamar yadda ya saba. Ya tashi zai yi karatu ke nan, 17 sai aka miƙa masa littafin annabi Ishaya. Ya kunce littafin ya nemi, ya kuma sami wurin da aka rubuta cewa,



Hoton littafi (4.17)

18 "Ruhun Ubangiji yana tare da ni,
Domin ya zaɓe ni in kawo wa talakawa Labari Mai Daɗi.
Ya aike ni in yi shelar 'yanci ga waɗanda suke a ɗaure.
In kuma buɗe idanun makafi.
In kuma ba da 'yanci ga waɗanda aka danne.
19 In kuma faɗa wa kowa cewa lokaci ya yi da Ubangiji zai ceci mutanensa."

20 Da ya gama karatun, sai ya naɗe littafin ya ba wa mai lura da majami'ar, ya zauna. Dukan mutanen da suke majami'ar, suka zuba masa ido, 21 sai ya ce musu, "Wannan Rubutaccen Maganar Allah, ya cika a kunnenku a yau."

22 Dukansu da suke wurin suka ji daɗinsa suna ta mamakin kalmomi masu kyau da suke fitowa daga bakinsa, suna ta tambaya, suna cewa, "Anya, wannan ba ɗan Yusufu ba ne?"

4.18-19: Ish 61.1-2

23 Yesu ya ce musu, "Na sani za ku gaya mini karin maganan
nan, 'Likita, ka warkar da kanka.' Za ku kuma ce mini, 'Ka yi
abubuwan da muka ji ka yi a Kafarnahum a nan garinka mana.' "
24 Ya sāke ce musu, "Ina faɗa muku gaskiya, ba annabin da a kan
yarda da shi a garinsa".

25 "Amma gaskiya ina gaya muku, a zamanin annabi Iliya,
akwai matan da mazansu suka mutu da yawa a Isra'ila. A wannan
lokacin ne ruwan sama ya ƙi zuwa har shekara uku da wata shida,
aka kuma yi muguwar yunwa ko'ina a ƙasar. 26 Amma ba a aiko
da annabi Iliya zuwa wurin ko ɗaya daga cikinsu ba. Ai, zuwa
wurin wata macen da mijinta ya mutu, a Zarifat da yake a yankin
Sidon ne aka aike shi. 27 A lokacin annabi Elisha kuma akwai
kutare wato, masu ciwon fatar jiki da yawa a Isra'ila, amma ba
a warkar da ko ɗaya a cikinsu ba, sai Na'aman mutumin ƙasar
Suriya ne kaɗai aka warkar."

28 Da mutanen da suke cikin majami'a suka ji wannan
magana, sai haushi ya kama su duka. 29 Suka tashi suka fitar da
Yesu bayan gari, har suka kai shi kan dutse da aka gina garinsu
a kai. Sun so su ture shi yă fāɗī daga kan dutsen, 30 amma sai ya
bi ta cikinsu ya yi tafiyarsa.

Mai Aljani
(Mar 1.21-28)

31 Sai ya tafi Kafarnahum, wani gari a cikin Galili. A nan ya
shiga majami'a a Ranar Hutun Yahudawa yana koyar da su.
32 Suka yi ta mamakin koyarwarsa, domin maganarsa tana da iko.
33 A cikin majami'ar, akwai wani mutum mai aljani. Sai ya ta da
murya da ƙarfi ya ce, 34 "Wayyo! Ina ruwanka da mu, Yesu
mutumin Nazarat? Ko ka zo ne ka halaka mu? Na san wane ne
kai, kai ne Mai Tsarkin nan na Allah!"

35 Yesu ya tsawata wa aljanin ya ce, "Ka yi shiru, ka fita daga
jikin mutumin nan!" Sai aljanin ya ɗaga mutumin, ya buga shi a
ƙasa a gabansu, sa'an nan ya fita, ya bar mutumin ba wani ciwo.

36 Sai dukan mutane suka kama baki kawai, suna ce wa
junansu, "Wane irin abu ne haka? Da ƙarfi da iko wannan mutum
ya umarci aljanu har sun fita!" 37 Wannan abin da Yesu ya yi, ya
sa an dinga maganarsa ko'ina a ƙasar.

4.24: Yoh 4.44 **4.25:** 1 Sar 17.1 **4.26:** 1 Sar 17.8-16 **4.27:** 2 Sar 5.1-14
4.32: Mat 7.28-29

Yesu Ya Warkar da Mutane da Yawa
(Mat 8.14-17; Mar 1.29-34)

38 Yesu ya fita daga majami'a, ya tafi gidan Siman. Mamar matar Siman kuma ba ta da lafiya, zazzaɓi ya dame ta sosai. Sai aka yi wa Yesu maganar rashin lafiyarta. 39 Ya je ya tsaya kusa da gadonta ya umarci zazzaɓin yă bar ta. Nan take zazzaɓin ya bar ta, ta kuma tashi, ta yi musu hidima.

40 Da rana ta fāɗi, kowa da yake da aboki mai rashin lafiya da kowane irin ciwo, suka kawo su wurin Yesu; shi kuma ya taɓa kowannensu da hannu ya warkar da su duka. 41 Aljanu suka fita daga jikin mutane da yawa suna ihu suna cewa, "Kai Ɗan Allah ne!"

Amma Yesu ya tsawata musu, ya hana su magana, don sun san cewa shi ne Almasihu.

Yesu Ya Yi Wa'azi a Majami'u
(Mar 1.35-39)

42 Da gari ya waye sai Yesu ya bar garin ya je inda ba kowa. Mutane suka yi ta nemansa, har suka same shi. Suka yi ƙoƙari su hana shi zuwa wani wuri kuma, 43 amma ya ce musu, "Ya kamata in kai Labarin Mai Daɗi na mulkin Allah ga waɗansu garuruwa, gama saboda wannan dalilin ne aka aiko ni."

44 Sai ya yi ta yin wa'azi a majami'un Yahudiya.[j]

Yesu Ya Kira Almajiransa na Farko
(Mat 4.18-22; Mar 1.16-20)

5 1 Wata rana Yesu yana tsaye a gefen Tekun Janisarat. Mutane suka yi ta matsawa kusa da shi domin su ji maganar Allah. 2 Yesu ya ga jirage biyu a ajiye a bakin tekun. Masu kamun kifin kuwa sun fita suna wanke kayansu na kaman kifi. 3 Sai Yesu ya shiga ɗaya daga cikin jiragen, wanda yake na Bitrus, ya kuma roƙe shi yă tura jirgin zuwa cikin ruwa kaɗan. Sai ya zauna a ciki yana koya wa mutane.

4 Da ya gama magana, sai ya ce wa Bitrus, "Ka ƙara tura jirgin zuwa inda akwai zurfi, ku saki abin kamun kifinku, ku jawo kifi."

5 Bitrus ya ce masa, "Mai girma, ai, tun da daddare muna a nan muna fama ba mu kama kome ba, amma in ka ce haka,

---

5.1-3: Mat 13.1-2; Mar 3.9-10; **4.1**

[j] **4.44 Yahudiya:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Galili" ne a nan.

to, zan yi." 6 Da suka sa abin kamun kifin, sai suka kama kifi
da yawa har abin kamun kifin ya fara tsintsinkewa. 7 Ganin
haka, sai suka kira abokansu na ɗayan jirgin su zo su taimake
su. Suka zo suka ciccika jiragen biyu da kifi, har jiragen suka
kusa nutsewa saboda nauyi. 8 Da Bitrus ya ga abin da ya faru,
sai ya durƙusa a gaban Yesu ya ce, "Rabu da ni, Ubangiji!
Gama ni mai zunubi ne!"

9 Domin shi da waɗanda suke tare da shi duka, mamaki ya
kama su sosai saboda yawan kifin nan da suka kama; 10 haka ma
Yakubu da Yohanna, 'ya'yan Zabadi, abokan aikin Bitrus. Sai
Yesu ya ce wa Bitrus, "Kada ka ji tsoro; daga yanzu mutane ne
za ka riƙa jawowa, ba kifi ba."

11 Sai suka jawo jiragensu zuwa gefen tekun, suka bar kome
da kome, suka bi Yesu.

Yesu Ya Warkar da Kuturu

(Mat 8.1-4; Mar 1.40-45)

12 Wata rana Yesu yana a wani gari, sai ga wani mutumin da
ciwon kuturta ya ci ƙarfinsa, ya zo. Da ganin Yesu, sai ya durƙusa,
ya roƙe shi, yana cewa, "Mai girma, idan ka yarda, kana iya ka
tsarkake ni!"

13 Yesu ya miƙa hannunsa ya taɓa shi, yana cewa, "Na yarda,
ka warke!" Nan da nan, sai kuturtar ta bar shi. 14 Sai Yesu ya
umarce shi ya ce, "Kada ka gaya wa kowa, amma ka je ka nuna
kanka a wurin firist, ka kuma yi hadaya kamar yadda Musa ya
ce a yi don tsarkakewa. Ka yi haka don ka tabbatar wa jama'a
cewa ka warke."

15 Amma duk da haka sai gaba-gaba labarin Yesu yake ta yi,
mutane da yawa suka riƙa zuwa don jinsa, suna neman warkarwa
daga dukan cututtukansu. 16 Amma Yesu yakan tafi wani wurin
da babu kowa, domin yin addu'a.

Yesu Ya Warkar da Shanyayye

(Mat 9.1-8; Mar 2.1-12)

17 Wata rana Yesu yana koyarwa sai waɗansu Farisiyawa[k] da
malaman dokoki[ƙ] waɗanda suka zo daga kowane ƙauye da yake
a Galili, da Yahudiya, da kuma daga birnin Urushalima, suna
zaune a wurin.

5.5: Yoh 21.3 **5.6**: Yoh 21.6 **5.12**: L. Fir 14.1-32 **5.14**: L. Fir 14.1-32

[k] **5.17 Farisiyawa**: Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

[ƙ] **5.17 Malaman dokoki**: Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

Ikon Ubangiji kuwa yana tare da shi domin yă warkar da masu ciwo. 18 Ana nan sai ga waɗansu mutane sun kawo wani shanyayye kwance a kan tabarma. Suna ƙoƙari su kai shi cikin gida domin su kwantar da shi a gaban Yesu, 19 amma ba su sami hanya ba saboda yawan mutane. Da suka ga babu dama, sai suka hau kan rufin ɗakin, suka ɓalle marufin suka saukar da shi ɗuk da tabarmar da yake kwance a kai, suka ajiye shi a tsakiyar mutane a gaban Yesu. 20 Da Yesu ya ga bangaskiyarsu, sai ya ce wa mutumin da yake kwance, "An gafarta maka zunubanka, abokina."

21 Malaman dokoki tare da Farisiyawa suka fara ce wa junansu, "Wane ne wannan da yake yin maganar reni wa Allah haka! Allah ne kaɗai yake da ikon gafarta zunubai!"

22 Da Yesu ya gane abin da suke tunani, sai ya ce musu, "Don me kuke wannan tunani? 23 Wanne ya fi sauƙi, a ce, 'An gafarta maka zunubanka,' ko kuwa a ce, 'Tashi, ka yi tafiya'? 24 Amma ina so ku sani cewa Ɗan mutum yana da iko yă gafarta zunubai a duniya." Sai ya ce wa shanyayyen, "Na ce maka, tashi, ka ɗauki tabarmarka ka tafi gida!"

25 Nan da nan mutumin nan ya tashi a idon kowa, ya ɗauki tabarmar da dā yake kwance a kai, ya tafi gida, yana yabon Allah. 26 Dukansu suka kama baki suna mamaki! Cike da tsoro, suka yabi Allah, suna cewa, "Yau mun ga abin mamaki!"

Yesu Ya Kira Lawi

(Mat 9.9-13; Mar 2.13-17)

27 Bayan haka, Yesu ya fita, ya ga wani mai karɓar haraji mai suna Lawi, yana zaune a wurin karɓar haraji. Sai Yesu ya ce masa, "Bi ni!" 28 Sai Lawi, ya bar kome da kome, ya tashi, ya bi shi.

29 Sai Lawi ya shirya babban biki a gidansa, ya kuma gayyaci Yesu. Masu karɓar haraji da yawa tare da waɗansu mutane suna nan suna cin abinci tare da su. 30 Amma Farisiyawa da malamansu da malaman dokoki suka fara gunaguni, suna ce wa almajiran Yesu, "Don me kuke ci, kuke kuma sha tare da masu karɓar haraji da masu zunubi?"

31 Yesu ya amsa musu ya ce, "Masu lafiyar jiki ba sa bukatar likita, sai dai marasa lafiya. 32 Ban zo don in kira masu adalci ba, sai dai don masu zunubi su tuba, su kuma canza rayuwarsu."

5.30: Luk 15.1-2

Tambaya a kan Yin Azumi
(Mat 9.14-17; Mar 2.18-22)

33 Waɗansu suka ce wa Yesu, "Almajiran Yohanna sukan yi azumi a kai a kai sukan kuma yi addu'a, haka ma na Farisiyawa; amma naka sai ci da sha suke yi kullum."

34 Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Kuna tsammani za ku iya hana abokan ango abinci, in suna tare da angon? 35 Lokaci yana zuwa da za a ɗauki angon a bar su. To, a lokacin ne za su yi azumi."

36 Sai Yesu ya ba su wani misali ya ce, "Ba wanda zai yage ƙyalle daga sabuwar riga yă yi wa tsohuwar riga faci da shi. Idan ya yi haka, sai yă zama ya yage sabuwar rigarsa, kuma facin ba zai yi wa tsohuwar rigar kyau ba. 37 Kuma ba wanda zai zuba sabon ruwan inabi[1] a cikin tsofaffin salkuna. Idan ya yi haka, sai sabon ruwan inabi yă faffashe salkunan ruwan inabin yă zube salkuna kuma su lalace. 38 Sabon ruwan inabi dai sai a zuba shi a cikin sababbin salkuna! 39 Ba wanda zai so shan sabon ruwan inabi bayan ya sha tsohon. Ai, yakan ce tsohon, ya fi daɗi!"

Tambaya a kan Kiyaye Ranar Hutu
(Mat 12.1-8; Mar 2.23-28)

6 1 Wata Ranar Hutun Yahudawa Yesu da almajiransa suka bi ta gonakin alkama; sai almajiran suka karya waɗansu kan alkama suna murjewa suna ci. 2 Sai waɗansu Farisiyawa suka ce, "Me ya sa kuke yin abin da Doka ta hana a yi a Ranar Hutu?"

3 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ashe, ba ku karanta abin da Dawuda ya yi ba sa'ad da shi tare da mutanensa suka ji yunwa? 4 Yadda Dawuda ya shiga wurin sujada, ya ɗauki burodin da aka keɓe, ya ci, har ma ya ba abokan tafiyarsa wanda bai kamata kowa yă ci ba, sai firistoci kaɗai?"

5 Sai ya gama maganan nan da cewa, "Ai, Ɗan Mutum Ubangiji ne har ma da na Ranar Hutu."

Mai Shanyayyen Hannu
(Mat 12.9-14; Mar 3.1-6)

6 A wata Ranar Hutun Yahudawa kuma, Yesu ya shiga majami'a yana koyarwa. Akwai wani mutum a wurin da hannun damarsa ya shanye. 7 Sai malaman dokoki da Farisiyawa suka

---

6.1: M. Sh 23.26 **6.3-4**: 1 Sam 21.1-6 **6.4**: L. Fir 24.9

[1] **5.37 ruwan inabi**: A kan sami wannan daga 'ya'yan inabin da aka matse. An cika yin amfani da ruwan inabi kamar ruwan sha a ƙasar Isra'ila.

zuba ido, su ga ko Yesu zai yi warkarwa a Ranar Hutu, domin su same shi da laifi. 8 Amma Yesu ya san abin da suke tunani. Sai ya ce wa mutumin nan, "Tashi ka zo ka tsaya a nan." Sai mutumin ya tashi ya zo ya tsaya a wurin. 9 Yesu ya ce musu, "Ina tambayarku, mene ne ya dace a yi a Ranar Hutu? A yi alheri ko a yi mugunta? A ceci rai, ko a halaka shi?" 10 Sai ya duddube su duka; sa'an nan ya ce wa mutumin, "Ka miƙa hannunka." Shi kuwa ya miƙe hannun, sai hannunsa ya warke.

11 Sai haushi ya kama Farisiyawa da malaman dokoki sosai, suka fara magana da junansu a kan abin da za su yi da Yesu.

Yesu Ya Zaɓi Almajirai Sha Biyu
(Mat 10.1-4; Mar 3.13-19)

12 A kwanakin nan, Yesu ya je ya hau dutse domin yă yi addu'a. Ya kwana yana addu'a ga Allah. 13 Da gari ya waye, sai ya kira almajiransa, ya zaɓi guda goma sha biyu daga cikinsu, waɗanda ya ce da su manzanni. 14 Su ne Siman, wanda Yesu ya sa masa suna Bitrus, da ɗan'uwansa Andarawus, da Yakubu, da Yohanna, da Filibus, da Batilomi, 15 da Matiyu, da Toma, da Yakubu ɗan Halfa, da Siman wanda ake ce da shi mai kishin ƙasarsu, 16 da Yahuda ɗan Yakubu, da kuma Yahuda Iskariyoti, wanda ya zama mai cin amana.

Yesu Ya Koyar da Mutane, Ya kuma Warkar da Su
(Mat 4.23-25)

17 Sai Yesu ya sauko tare da manzanninsa, ya tsaya a wani wuri mai fili sosai, tare da mutane da yawa waɗanda suke almajiransa. A nan kuma ga mutane da yawa da suka zo daga ko'ina a Yahudiya, da Urushalima, da kuma yankin ƙasar Taya da Sidon waɗanda suke a bakin babban teku. 18 Sun zo domin su ji shi, su kuma sami warkarwa daga dukan cututtukansu. Aka kuma warkar da mutanen da aljanu suke damunsu. 19 Kowa ya yi ƙoƙari yă taɓa shi, domin iko yana fitowa daga gare shi, ya kuwa warkar da su duka.

Jin Daɗi da kuma Wahala
(Mat 5.1-12)

20 Yesu ya dubi almajiransa ya ce,
"Masu albarka ne, ku talakawa;
gama mulkin Allah naku ne!
21 Masu albarka ne ku da kuke jin yunwa yanzu;
gama za ku ƙoshi!

Masu albarka ne ku da kuke kuka yanzu;
gama za ku yi dariya!

22 "Ku masu albarka ne idan mutane sun ƙi ku, sun ware ku,
suna zaginku, suna cewa, ku mugaye ne, saboda Dan Mutum!
23 Ku yi farin ciki in wannan ya faru, ku kuma yi rawa don farin
ciki, domin ladanku yana da yawa a sama. Gama haka kakanninsu
ma suka yi wa annabawan da suka riga ku.
24 "Amma zai zama abin tausayi gare ku, ku da kuke da
arziki yanzu,
gama kun riga kun ji dadîinku ko!
25 Zai zama abin tausayi gare ku, ku da kuka ƙoshi yanzu,
gama za ku zauna da yunwa!
Zai zama abin tausayi gare ku, ku da kuke dariya yanzu,
gama za ku yi bakin ciki, kuna kuka!
26 "Zai zama abin tausayi gare ku, ku da mutane suke
yabonku; gama haka kakanninsu ma suka yi wa annabawan
ƙarya."

Ku Nuna Kauna ga Masu Gãba da Ku

(Mat 5.38-48, 7.12a)

27 "Ina gaya muku, ku da kuke jina: Ku ƙaunace masu gãba
da ku, ku yi wa waɗanda ba sa son ganinku alheri. 28 Ku sa wa
masu zaginku albarka, ku kuma yi wa masu ba ku wahala addu'a.
29 Idan wani ya mare ka a wannan kumatu, ka juye masa ɗayan
ma; idan wani ya ƙwace maka babbar riga, ka cire rigar cikin ma
ka ba shi. 30 Duk wanda ya roƙe ka abu, ka ba shi. Wanda kuma
ya yi maka ƙwace, kada ma ka nemi a mayar maka. 31 Ku yi wa
mutane abin da kuke so su yi muku.

32 "Idan kuna ƙaunar waɗanda suke ƙaunarku ne kawai, yaya
za ku sami albarka? Ko masu zunubi ma suna ƙaunar waɗanda
suke ƙaunarsu ne! 33 Idan kuma kuna yin alheri ga masu yi muku
ne kawai, yaya za ku sami albarka? Ko masu zunubi ma suna yin
haka. 34 In kuma mutanen da za su iya biyanku ne kuke ba su
bashi, yaya za ku sami albarka? Ko masu zunubi ma suna ba da
bashi ga masu zunubi don a biya su daidai! 35 Amma ku, ku
ƙaunaci masu gãba da ku, ku kuma yi musu alheri; ku ba da bashi
ba da nufi sai an biya ku ba. Ta yin haka ne za ku sami lada mai
yawa, ku kuma zama 'ya'yan Allah Maɗaukaki. Gama shi mai
alheri ne ga mutanen da ba sa godiya da kuma mugaye. 36 Ku
zama masu tausayi kamar yadda Ubanku yake mai tausayi.

6.22: 1 Bit 4.14 **6.23**: 2 Tar 36.16; A. M. 7.52 **6.31**: Mat 7.12

Kada Ku Ba Kowa Laifi
(Mat 7.1-5)

37 "Kada ku ba kowa laifi, ku kuma ba za a ba ku ba. Kada
ku hukunta kowa, ku kuma ba za a hukunta ku ba. Ku yafe wa
kowa, ku kuma za a yafe muku. 38 Ku bayar, ku ma za a ba ku
mudu a cike, a cika har yă yi tudu yana zuba, har a juye muku
sauran a hannun riga. Mudun da kuke auna wa mutane da shi, da
shi za a auna muku."

39 Yesu ya kuma ba su wani misali ya ce, "Makaho zai iya
yin wa wani makaho jagora? Idan ya yi haka, to, dukansu za su
fãdi a rami. 40 Ba ɗan makarantan da ya fi malaminsa; amma
kowane ɗan makaranta wanda ya gama karatunsa, zai zama kamar
malaminsa.

41 "Don me kake ganin ɗan tsinken da yake a idon
ɗan'uwanka, amma ba ka kula da gungumen da yake cikin idonka
ba? 42 Yaya kuma za ka iya ce wa ɗan'uwanka, 'Kai, ɗan'uwana,
bari in cire maka ɗan tsinken nan da yake idonka,' bayan kuma
ba ka iya ganin gungumen da yake a naka idon ba? Kai munafuki!
Ka fara cire gungumen da yake cikin idonka tukuna, don ka iya
gani sosai yadda za ka iya cire ɗan tsinken da yake cikin idon
ɗan'uwanka.

Akan Gane Itace ta Irin 'Ya'yansa
(Mat 7.16-20, 12.33-35)

43 "Itace mai kyau ba ya yin 'ya'ya marasa kyau, kuma
mummunan itace ba ya yin 'ya'ya masu kyau. 44 Ana sanin
kowane itace ta irin 'ya'yansa. Ba yadda za a tsinke ɓaure a jikin
ƙaya, ko kuwa inabi a jikin sarƙaƙƙiya. 45 Mutumin kirki, yana
yin abubuwa masu kyau, domin abubuwa masu kyau ne suke
zuciyarsa; amma mugun mutum yana yin abubuwan da ba su da
kyau domin abubuwan da suke zuciyarsa ba su da kyau. Ai, abin
da yake cikin zuciya shi yake fitowa a baki.

Mutane Biyu Masu Gini
(Mat 7.24-27)

46 "Don me kuke ce da ni 'Ubangiji, Ubangiji,' amma kun ƙi
yin abin da na ce ku yi? 47 Duk wanda ya zo wurina ya saurare
ni, ya kuma yi abin da na ce yă yi, zan faɗa muku irin mutum
da yake. 48 Shi kamar mutum ne wanda, da zai gina gidansa, sai

6.39: Mat 15.14 **6.40:** Mat 10.24-25; Yoh 13.16; 15.20 **6.44:** Mat 12.33
6.45: Mat 12.35

ya haƙa ƙasa da zurfi, ya kuma kafa tushen ginin a kan dutse. Da kogi ya cika, ruwan ya zo ya bugi gidan, amma bai iya girgiza gidan ba, saboda an kafa tushensa a kan fā. 49 Amma duk wanda ya ji maganata bai kuma yi abin da na ce yă yi ba, daidai yake da mutumin da ya gina gidansa ba tare da ya yi wa gidan nan tushe mai kyau ba. Da kogi ya cika, ruwan ya zo ya bugi gidan, sai ya fāɗi gaba ɗaya. Fāɗuwar gidan nan kuwa ta yi muni sosai."

Yesu Ya Warkar da Bawan Wani Babban Sojan Roma

(Mat 8.5-13)

7 1 Da Yesu ya gama gaya wa mutane dukan waɗannan abubuwa, sai ya tafi Kafarnahum. 2 A can dîn, akwai wani babban sojan Roma wanda bawansa yana ciwo sosai har ya kusa mutuwa. Wannan babban sojan Roma kuwa yana ƙaunar bawan nan sosai. 3 Da ya ji labarin Yesu, sai ya aiki waɗansu shugabannin Yahudawa don su roƙe shi yă zo yă warkar da bawansa. 4 Shugabannin suka je wurin Yesu, suka roƙe shi sosai, suna cewa, "Wannan mutum ai, ya cancanci ka taimake shi! 5 Yana ƙaunar mutanenmu, har ya gina mana majami'a." 6 Sai Yesu ya tafi tare da su. Da ya yi kusa da gidan, babban sojan Roman nan ya aika da waɗansu abokansa su gaya wa Yesu, "Mai girma, kada ka dame kanka saboda ni! Ban ma isa har da za ka zo gidana ba. 7 Shi ya sa ban ma ga na isa in zo wurinka ba, amma ka yi magana kawai, yarona kuwa zai warke. 8 Gama ni ma a ƙarƙashin ikon wani nake, kuma da sojoji a ƙarƙashina, nakan ce wa wannan, 'Je ka,' sai yă je; wani kuwa in ce masa, 'Zo,' sai yă zo; in na ce wa bawana, 'Yi abu kaza,' sai yă yi."

9 Da Yesu ya ji haka, sai mamaki ya kama shi. Sai ya juye ya ce wa mutanen da suke binsa, "Ina gaya muku, a cikin Isra'ila ban taɓa sami mai bangaskiya mai ƙarfi kamar wannan ba!"

10 Da waɗanda aka aika suka koma gidan babban sojan Roma, sai suka sami bawan ya warke.

Yesu Ya Ta da Dan Wata Macen da Mijinta Ya Mutu

11 Ba da daɗewa ba,[m] sai Yesu ya tafi wani garin da ake ce da shi Nayin, almajiransa da mutane da yawa suka tafi tare da shi. 12 Da suka yi kusa da ƙofar shigar garin, sai ga waɗansu mutane suna fitowa da gawar wani saurayi, wanda shi kaɗai mamarsa ta haifa, mijinta kuma ya mutu. Mutane da yawa daga

[m] **7.11 Ba da daɗewa ba:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Washegari" ne a nan.

garin suna mata rakiya. 13 Da Ubangiji ya ga matar, sai ya ji tausayinta, sai ya ce mata, "Kada ki yi kuka!" 14 Sai ya je ya taɓa akwatin gawar, sai mutanen da suke riƙe da shi suka tsaya. Yesu ya ce, "Saurayi, na ce maka ka tashi!" 15 Sai wannan da ya mutu ya tashi ya zauna, ya fara magana. Yesu kuma ya miƙa shi ga mamarsa.

16 Sai tsoro ya kama su duka, suka ɗaukaka Allah suna cewa, "Lallai, wani babban annabi ya zo cikinmu! Allah ya zo domin yă ceci mutanensa!"

17 Labarin abin nan da Yesu ya yi, ya kai ko'ina a cikin Yahudiya da kewayenta.

'Yan Aika daga Wurin Yohanna Maibaftisma
(Mat 11.2-19)

18 Da almajiran Yohanna maibaftisma suka gaya masa dukan abubuwan nan, sai ya kira biyu daga cikinsu, 19 ya aike su wurin Ubangiji, su tambaye shi, "Kai ne wanda zai zo, ko mu sa ido ga wani?"

20 Da suka kai wurin Yesu, sai suka ce, "Yohanna Maibaftisma ne ya aike mu, mu tambaye ka, 'Ko kai ne mai zuwan nan, ko kuma mu sa ido ga wani?' "

21 A daidai lokacin nan kuwa, Yesu ya warkar da mutane da yawa daga rashin lafiyarsu da cututtukansu, da kuma daga aljanu. Makafi da yawa kuma suka sami ganin gari. 22 Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Ku koma ku gaya wa Yohanna abin da kuka ji, kuka kuma gani; makafi suna samun gani, guragu suna tafiya, kutare suna samun warkarwa, kurame suna jin magana, ana ta da waɗanda suka mutu, ana kuma ba wa talakawa Labari Mai Daɗi. 23 Allah zai albarkaci kowa da bai yi shakkar bangaskiyar da yake da ita a kaina ba!"

24 Bayan waɗanda Yohanna ya aika suka tafi, sai Yesu ya fara yi wa taron mutane magana game da Yohanna, yana cewa, "Me kuka je gani a daji? Kun je ganin dogayen ciyawa da iska take kaɗawa ne? 25 To, kallon me ya kai ku? Wani da ya ci ado ne? Masu sa kayan tsada suna kuma zaman jin daɗi ai, a gidan sarki suke. 26 To, wai kallon me kuka je yi? Annabi? I, ina gaya muku, ya ma fi annabi. 27 Gama Yohanna ne Maganar Allah ta ce a kansa, 'Ga shi, na aiko manzona yă riga ka gaba, wanda zai shirya maka hanya, kafin ka zo.' 28 Ina gaya muku, a cikin dukan

7.22: Ish 35.5-6; 61.1 **7.22**: Ish 29.18-19; 35.5-6; 61.1-2 **7.27**: Mal 3.1

waɗanda mata suka haifa, ba wanda ya fi Yohanna girma. Amma duk da haka wanda yake ƙarami duka a mulkin Allah ya fi shi."

29 Duka wanda ya ji wannan, har da masu karɓar haraji, suka tabbata cewa hanyar Allah ita ce daidai saboda su ne aka yi musu baftisma ta Yohanna. 30 Amma Farisiyawa da malaman dokoki suka ƙi yin biyayya da abin da Allah ya nufe su da shi, suka kuma ƙi Yohanna yă yi musu baftisma.

31 Yesu ya ci gaba da cewa, "To, da me zan kwatanta mutanen zamanin nan? Yaya suke? 32 Su kamar yara ne da suke zama a kasuwa, suna kiran juna, suna cewa, 'Mun hura muku busa, kun ƙi ku yi rawa! Mun rera waƙar mutuwa, kun ƙi ku yi kuka!' 33 Yohanna Maibaftisma ya zo, ba ya cin abinci, ba ya shan ruwan inabi, amma kuna cewa, 'Ai, yana da aljani!' 34 Dan Mutum ya zo, yana ci, yana sha, kuna cewa, 'Kun gan shi mai yawan ci da sha, abokin masu karɓar haraji da masu zunubi!' 35 Duk da haka waɗanda suka yarda da hikimar Allah, suna nuna cewa tana da gaskiya."

Yesu a Gidan Siman Bafarisiye

36 Wani Bafarisiye ya gayyaci Yesu cin abinci a gidansa, sai Yesu ya je ya zauna don cin abinci. 37 A wannan garin, akwai wata mace wadda ta yi rayuwa marar kyau. Da ta ji cewa Yesu yana cin abinci a gidan Bafarisiyen, sai ta kawo wata 'yar kwalabar man ƙamshi mai tsada. 38 Ta zo ta tsaya a bayansa,

Hoton yadda dā ake zama a ci abinci (7.38)

7.27: Mal 3.1 **7.29-30:** Mat 21.32; Luk 3.12

wajen ƙafafunsa, tana kuka. Da hawayenta ya fara zuba a ƙafafunsa, sai ta goge ƙafafun da gashinta, ta yi ta sumbatarsu, sa'an nan ta shafa musu man ƙamshin nan.

39 Da Bafarisiyen nan ya ga abin da macen nan take yi, sai ya ce a ransa, "Da mutumin nan annabi ne, da ya san kowace ce macen nan da take taɓa shi! Kuma da ya san cewa ita mai zunubi ce."

40 Yesu ya ce wa Bafarisiyen nan, "Siman, ina da abin da zan faɗa maka." Shi kuma ya ce, "Faɗa, malam."

41 Yesu ya ce, "An yi wani mutumin da yake bin waɗansu mutane biyu bashi, ɗaya ana binsa yawan kuɗin da lebura zai samu cikin shekara ɗaya da rabi, ɗayan kuma yawan kuɗin da lebura zai samu cikin kwana hamsin. 42 Da suka gagara biya, sai ya yafe musu dukansu biyu. To, a ganinka wa zai fi ƙaunarsa?"

43 Siman ya ce masa, "A ganina, wanda aka yafe masa mai yawan ne." Sai Yesu ya ce masa,

"Yawwa! Ka faɗa daidai." 44 Sai ya dubi macen, ya ce wa Siman, "Ka ga macen nan? Na shigo gidanka, ba ka ba ni ruwa in wanke ƙafafuna ba, amma ta wanke ƙafafuna da hawayenta, ta kuma goge su da gashin kanta. 45 Ba ka rungume ni da na shigo gidanka ba, amma tun shigowata a nan macen nan ba ta daina sumbar ƙafafuna ba. 46 Ba ka shafa mai a kaina ba, amma ita ta shafa man ƙamshi a ƙafafuna. 47 Saboda haka ina gaya maka, zunuban nan nata masu yawa an yafe mata su, gama ta yi ƙauna mai yawa. Wanda aka yafe wa kaɗan kuwa, ƙauna kaɗan yake nunawa."

48 Sai ya ce wa macen, "An gafarta miki zunubanki."

49 Mutanen da suke cin abinci tare da shi suka fara ce wa junansu, "Wane ne wannan, wanda har yana yafe zunubai?"

50 Sai Yesu ya ce wa macen, "Bangaskiyarki ta cece ki, ki sauka lafiya."

Waɗansu Mata Sun Tafi tare da Yesu

8 1 An jima kaɗan sai Yesu ya zazzaga birane da ƙauyuka, yana wa'azin Labari Mai Daɗi na mulkin Allah. Almajiransa sha biyun nan kuwa suna tare da shi, 2 da waɗansu mata waɗanda aka raba su da aljanu aka kuma warkar da su daga rashin lafiyarsu. A cikinsu kuwa akwai Maryamu daga Magadala, wadda aka fitar da aljanu bakwai daga gare ta. 3 Akwai kuma Yowana matar

---

7.37-38: Mat 26.7; Mar 14.3; Yoh 12.3

Kuza, wani wakili a gidan Hirudus, tare da Suzana, da waɗansu mata da yawa waɗanda suke yi musu hidima da kayansu.

Misali na Mai Shuka
(Mat 13.1-9; Mar 4.1-9)

4 Da mutane da yawa suna ta taruwa daga garuruwa dabam-dabam suna ta zuwa wurin Yesu, sai ya ba su wannan misali:

5 "An taɓa yin wani mutumin da ya je yă shuka iri a gonarsa. Yana cikin yafa iri ke nan, sai waɗansu suka fāɗi a kan hanya, aka tattaka su, sai tsuntsaye kuma suka cinye su. 6 Waɗansu suka fāɗi a kan dutse; da suka tsira sai suka bushe don babu ruwa a wurin. 7 Waɗansu kuma suka fāɗi a cikin ƙaya, suka yi girma tare, har ƙaya suka hana su girma. 8 Waɗansu irin kuma suka fāɗi a ƙasa mai kyau, suka yi girma, suka yi tsaba ɗari-ɗari."

Da Yesu ya gama faɗin haka sai ya ɗaga murya ya ce, "Bari mai kunnen ji, yă ji!"

Manufar Misalin na Mai Shuka
(Mat 13.10-17; Mar 4.10-12)

9 Sai almajiran Yesu suka tambaye shi abin da misalin nan yake nufi. 10 Ya ce, "An yarda muku ku san asirin mulkin Allah, amma ga sauran mutane ina magana da misalai ne domin, 'Ko sun duba ba za su gani ba, ko sun ji ba za su gane ba.'

Yesu Ya Ba da Bayanin Misali na Mai Shuka
(Mat 13.18-23; Mar 4.13-20)

11 "Ga ma'anar misalin nan: Irin shi ne maganar Allah. 12 Waɗanda suka fāɗi a kan hanya su ne kwatancin mutanen da suka ji, amma Shaiɗan ya zo ya ƙwace maganar daga zuciyarsu, don kada su ba da gaskiya su kuma sami ceto. 13 Irin da suka fāɗi a kan dutsen kuwa, su ne kwatancin mutanen nan da suka ji maganar, suka kuma karɓe ta da murna. Amma ba ta yi tushe a cikinsu ba; sun ba da gaskiya na ɗan lokaci, amma da wahala ta zo musu, sai suka watsar da bangaskiyarsu. 14 Irin da suka fāɗi a cikin ƙaya kuwa, su ne kwatancin mutanen da suka ji, amma a kwana a tashi, tunanin kayan duniya da neman arziki, da son jin daɗi, ya sa sun kāsa amfani. 15 Irin da suka fāɗi a ƙasa mai kyau kuwa, su ne kwatancin mutanen da suka ji maganar, suka kuma karɓa da zuciya ɗaya suka riƙe, suka jimre har suka yi amfani.

8.2-3: Mat 27.55-56; Mar 15.40-41; Luk 23.49 **8.10:** Ish 6.9-10

Misali A Kan Fitila
(Mar 4.21-25)

16 "Ba wanda zai kunna fitila yă ɗauka kwano yă rufe ko kuwa yă sa ta a ƙarƙashin gado. A maimakon haka, zai sa ta a kan tebur domin mutanen da za su shiga su ga haske.

17 "Gama duk abin da yake a ɓoye za a tone shi, kuma dukan abin da yake a rufe za a bayyana shi a fili.

18 "Ku yi hankali fa da yadda kuke ji, domin idan wani yana da abu, za a ƙara masa, amma wanda ba shi da wani abu, abin da yake tsammani yana da shi ma, za a karɓa a bar shi."

Mamar Yesu tare da 'Yan'uwansa
(Mat 12.46-50; Mar 3.31-35)

19 Sa'an nan mamar Yesu da 'yan'uwansa suka je wurinsa, amma ba su iya kai wurinsa ba saboda yawan mutane. 20 Sai wani mutum ya gaya wa Yesu cewa, "Ga mamarka da 'yan'uwanka suna tsaye a waje suna so su gan ka."

21 Yesu ya ce wa dukan mutanen da suke wurin, "Waɗanda suka ji maganar Allah, suka kuma aikata, su ne mamata da 'yan'uwana."

Yesu Ya Tsawata wa Hadari
(Mat 8.23-27; Mar 4.35-41)

22 Wata rana Yesu da almajiransa suka shiga jirgin ruwa, sai ya ce musu, "Mu haye zuwa wancan gefen tekun." Sai suka fara tafiya. 23 Da suna cikin tafiya, sai barci ya kwashe shi. Ba labari sai wata babbar iska ta taso, tana hurawa zuwa tekun. Suka shiga wani hatsari, saboda ruwa ya fara shiga cikin jirgin. 24 Almajiran suka je, suka ta da Yesu, suka ce, "Mai girma! Mai girma! Za mu halaka!"

Yesu ya tashi, ya tsawata wa iskar da kuma ruwan da suke hauka, sai suka yi tsit. 25 Sai ya ce wa almajiran, "Ina bangaskiyarku?"

Amma suka ji tsoro sosai, suka kuma yi mamaki, suna ce wa juna, "Wane ne wannan wanda yake wa iska da raƙuman ruwa umarni har suna masa biyayya?"

8.16: Mat 5.15; Luk 11.33 **8.17**: Mat 10.26; Luk 12.2 **8.18**: Mat 25.29; Luk 19.26

Yesu Ya Warkar da Mai Aljanu
(Mat 8.28-34; Mar 5.1-20)

26 Yesu da almajiransa suka yi ta tafiya a cikin jirgin ruwa
har suka kai sashin ƙasar Garasinawa,[n] da yake a hayen Tekun
Galili. 27 Yesu yana sauka daga jirgin ke nan sai ga wani mutumin
garin wanda yake da aljanu. Mutumin ya daɗe yana yawo ba riga,
kuma ba ya iya zama a gida, kullum yana wurin da ake binne
mutane. 28 Da ganin Yesu, sai mutumin ya ta da murya da ƙarfi,
ya fāɗi a gaban Yesu yana ihu yana cewa, "Ina ruwanka da ni,
Yesu Ɗan Allah Maɗaukaki? Ina roƙonka, kada ka ba ni wahala!"
29 Ya faɗa haka ne don Yesu ya riga ya tsawata wa aljanun su
bar shi. Domin sau da yawa aljanun sukan buge shi, akan kuma
tsare shi a ɗaure da sarƙa, amma yakan tsintsinke sarƙan, aljanun
kuma sukan kore shi zuwa daji.

30 Yesu ya tambaye shi, "Mene ne sunanka?"

Sai mutumin ya amsa, "Dubu Shida,"[o] domin aljanun suna da
yawa a cikinsa. 31 Suka yi ta roƙonsa kada yă tura su a ramin da
ake tsare aljanu a ciki.

32 Kusa da wurin nan kuwa, akwai wani babban garken aladu
da yake kiwo a gangaren dutsen, sai aljanun suka roƙi Yesu yă
bar su su shiga cikin aladun. Shi kuwa ya yarda musu. 33 Suka
fita daga cikin mutumin suka shiga cikin aladun. Sai dukan aladun
suka tashi a guje suka gangara cikin tekun, suka mutu a ciki.

34 Da masu lura da aladun suka ga abin da ya faru, sai suka
gudu zuwa gari da karkara don su kai labari. 35 Mutane suka fito
don su ga abin da ya faru. Da suka kai wurin Yesu, suka ga
mutumin da aljanun suka fito daga cikinsa yana zama kusa da
Yesu, ya sa riga kuma hankalinsa ɗaya. Sai tsoro ya kama su
duka. 36 Waɗanda suke nan lokacin da abin ya faru, suka yi ta
gaggaya wa mutane yadda aka warkar da mutumin. 37 Sai dukan
mutanen kewayen ƙasar Garasinawa suka roƙi Yesu yă bar
garinsu, don sun ji tsoro sosai. Da Yesu zai shiga jirgi yă tafi ke
nan, 38 sai mutumin da aka fitar da aljanu daga cikinsa ya zo, ya
roƙi Yesu yana cewa, "Bari in tafi tare da kai."

Amma Yesu ya sallame shi ya ce, 39 "Koma gida, ka faɗa abin
da Allah ya yi maka."

---

[n] **8.26 Kasar Garasinawa:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Gadarinas," waɗansu kuma "Gagasina" ne a nan.

[o] **8.30 dubu shida:** Da Helenanci "Lijiyon", wato, ƙungiyar sojoji wadda ta kai mutum dubu huɗu zuwa dubu shida.

Sai mutumin ya tafi ya bi ta cikin birnin, yana fadîn abin da Yesu ya yi masa.

'Yar Jayirus da Mace Mai Zub da Jini

(Mat 9.18-26; Mar 5.21-43)

40 Da komawar Yesu daga wancan gefen tekun, mutane suka yi masa maraba don dā ma suna jiransa ne. 41 Sai ga wani mutum mai suna Jayirus, wanda yake shugaban majami'a ya zo ya durkusa a gaban Yesu. Ya roke shi yă je gidansa, 42 don wadda take 'yarsa kadai, wadda ta kai shekara goma sha biyu, tana bakin mutuwa.

Da Yesu ya kama hanya, mutane suka yi ta binsa suna matsa shi ta kowane gefe. 43 A cikinsu kuwa akwai wata mace wadda ta sha wahala da ciwon zub da jini, na tsawon shekara goma sha biyu. Ta kashe duk abin da take da shi wurin neman magani,[r] amma ba wanda ya iya warkar da ita. 44 Sai ta bi ta cikin yawan mutanen nan ta zo ta bayansa, ta taba bakin rigarsa, sai zub da jinin nan nata ya tsaya cik. 45 Yesu ya ce, "Wa ya taba ni?"

Kowa ya ce ba shi ba ne, sai Bitrus ya ce, "Mai girma, ai, mutane sun kewaye ka ta kowane gefe, suna tutture ka."

46 Amma Yesu ya ce, "Ni dai, wani ya taba ni, domin na ji iko ya fita daga gare ni." 47 Da matar ta ga dai an gane ta, sai ta fita, jikinta yana rawa, ta durkusa a gaban Yesu. Ta kuma bayyana masa a gaban kowa dalilin da ya sa ta taba shi, da yadda ta warke nan take. 48 Yesu ya ce mata, "'Yata, bangaskiyarki ta warkar da ke. Ki sauka lafiya."

49 Bai ma kare maganar ba, sai ga dan aika daga gidan Jayirus, ya zo, yana gaya wa Jayirus cewa, "Kada ma ka sa malam ya yi wata wahala, ai, 'yarka ta mutu ko."

50 Da Yesu ya ji haka, sai ya ce wa Jayirus, "Kada ka ji tsoro; ka dai ba da gaskiya, za ta sāke rayuwa."

51 Da suka kai gidan, bai yarda kowa yă shiga tare da shi ba sai Bitrus da Yohanna da Yakubu, da kuma baban yarinyar da mamarta. 52 Dukan mutanen da suke gidan, sai kuka suke yi suna ihu domin yarinyar. Yesu ya ce musu, "Kada ku yi kuka, yarinyar ba ta mutu ba, tana barci ne kawai!"

53 Sai suka yi masa dariyar reni, domin sun sani ta mutu. 54 Yesu kuwa da ya kama hannunta sai ya ta da murya ya ce,

[r] **8.43 Ta kashe duk abin . . . neman magani:** Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da wadannan kalmomin.

"Yarinya, ki tashi!" 55 Ranta kuma ya dawo, ta tashi tsab, sai Yesu ya umarta a ba ta abinci ta ci. 56 Iyayenta suka kama baki suna mamaki, amma Yesu ya ja musu kunne cewa kada su faɗa wa kowa abin da ya faru.

Yesu Ya Aiki Almajiransa
(Mat 10.5-15; Mar 6.7-13)

9 1 Sai Yesu ya kira sha biyun nan wuri ɗaya, ya ba su iko da kuma izni a kan dukan aljanu, su kuma warkar da cututtuka. 2 Ya kuma aike su su je su yi wa'azin mulkin Allah, su kuma warkar da marasa lafiya. 3 Ya ce musu, "Kada ku ɗauki kome don tafiyarku, kada ma ku riƙe sanda, ko jaka, ko abinci, ko kuɗi. Kada kuma ku ɗauki wata riga ban da wadda kuka sa. 4 Duk gidan da aka karɓe ku, ku zauna nan sai lokacin da za ku bar garin. 5 Duk inda aka ƙi karɓarku, in za ku bar garin sai ku kakkaɓe ƙurar ƙafafunku don yă zama shaida a kansu."

6 Sai suka tashi suka zazzaga ƙauyuka suna wa'azin Labari Mai Daɗi, suna warkar da marasa lafiya a ko'ina.

Hirudus Ya Rikice
(Mat 14.1-12; Mar 6.14-29)

7 Da Hirudus mai mulkin Galili ya ji labarin dukan abubuwan nan da suke faruwa, sai ya rikice sosai, don waɗansu mutane suna cewa Yohanna Maibaftisma ne ya tashi daga matattu. 8 Waɗansu kuma suna cewa annabi Iliya ne ya sāke bayyana. Waɗansu kuma har wa yau, suna cewa ɗaya daga cikin annabawa na dā ne ya tashi. 9 Sai Hirudus ya ce, "Yohanna dai, na sa aka yanke kansa; to, wane mutum ne nake ji abubuwan nan a kansa?" Sai ya yi ta ƙoƙari yă ga Yesu.

Yesu Ya Ciyar da Mutum Dubu Biyar
(Mat 14.13-21; Mar 6.30-44; Yoh 6.1-14)

10 Da manzannin suka dawo, sai suka faɗa wa Yesu kome da suka yi. Sai ya ɗauke su su kaɗai suka tafi wani garin da ake ce da shi Betsaida. 11 Da mutane suka ji yana can, sai suka bi shi. Ya kuwa yi musu maraba, ya yi musu magana a kan mulkin Allah, ya kuma warkar da dukan masu bukata a warkar da su.

12 Da rana ta kusa fāɗuwa, sai sha biyun suka zo wurinsa suka ce, "Ka sallami mutane su shiga ƙauyuka da karkara don su nemi abinci da wurin kwana; don inda muke ba mutane."

9.3-5: Luk 10.4-11; A. M. 13.51 **9.7-8:** Mat 16.14; Mar 8.28; Luk 9.19

13 Amma Yesu ya ce musu, "Ku, ku ba su wani abu su ci
mana."
Sai suka ce masa, "Duk abin da muke da shi a nan bai wuce
burodi biyar da kifi biyu ba. Sai dai in za mu je mu saya wa
dukan jama'an nan abinci." 14 Gama maza kaɗai sun kai wajen
dubu biyar.
Yesu ya ce wa almajiransa, "Ku gaya wa mutanen su zazzauna
a ƙungiyoyi hamsin-hamsin."
15 Sai almajiran suka bi umarnin, suka sa dukan mutane suka
zazzauna. 16 Sai Yesu ya ɗauki burodi biyar da kifi biyu ɗin nan,
ya ɗaga kansa sama ya yi wa Allah godiya, sa'an nan ya kakkarya
su, ya ba wa almajiransa, su rarraba wa mutanen. 17 Duka kuwa
suka ci suka ƙoshi. Almajiran suka kwashe sauran da ya rage har
suka cika kwanduna goma sha biyu.

Bitrus Ya Shaida Yesu Shi Ne Almasihu
(Mat 16.13-19; Mar 8.27-29)

18 Wata rana Yesu yana addu'a shi kaɗai, almajiransa kuma
suka zo wurinsa. Sai ya tambaye su ya ce, "Wa mutane suke ce
da ni?"
19 Almajiransa suka ce masa, "Waɗansu suna cewa, kai ne
Yohanna Maibaftisma, waɗansu kuma suna cewa, kai ne annabi
Iliya; har wa yau waɗansu suna cewa, ɗaya daga cikin annabawan
dā ne ya tashi."
20 Sai Yesu ya ce musu, "Amma ku fa, wane ne ni a
ganinku?"
Bitrus ya amsa ya ce, "Kai ne Almasihu na Allah."

Yesu Ya Faɗa Irin Mutuwar da Zai Yi
(Mat 16.20-28; Mar 8.31-9.1)

21 Sai Yesu ya ja musu kunne sosai kada su gaya wa kowa
wannan magana. 22 Ya sāke gaya musu cewa, "Lallai ne Ɗan
Mutum yă sha wuya iri-iri, shugabannin jama'a da manyan
firistoci da malaman dokoki su ƙi shi, har a kashe shi, amma rana
ta uku a tashe shi kuma."
23 Sai ya ce wa dukansu, "Duk mai so yă bi ni, sai yă ƙi
kansa, yă ɗauki gicciyensa kowace rana, yă bi ni. 24 Gama duk
mai son ajiyar ransa, zai rasa shi. Amma duk wanda ya rasa ransa
saboda ni, ajiyarsa yake yi. 25 Wane amfani ne mutum zai samu,

9.19: Mat 14.1-2; Mar 6.14-15; Luk 9.7-8 **9.20**: Yoh 6.68-69
9.23: Mat 10.38; Luk 14.27 **9.24**: Mat 10.39; Luk 7.33; Yoh 12.25

in ya sami duniya duka, sa'an nan ya rasa ransa? 26 Gama duk wanda yake jin kunyata da kuma kunyar maganata, Dan mutum ma zai ji kunyarsa, lokacin da zai zo a cikin ɗaukakarsa, da kuma ɗaukakar Ubansa, da ta mala'iku masu tsarki. 27 Hakika ina gaya muku, akwai waɗansu a nan tsaye da ba za su mutu ba sai sun ga mulkin Allah."

Sākewar Kamannin Yesu
(Mat 17.1-8; Mar 9.2-8)

28 Bayan kamar kwana takwas da yin wannan magana, sai Yesu ya ɗauki Bitrus, da Yohanna da kuma Yakubu, suka hau kan dutse tare don su yi addu'a. 29 Da yana cikin addu'a, sai fuskarsa ta canza kamanni, rigunarsa kuma suka yi fari fat, har suna kashen ido. 30 Ba labari sai ga waɗansu mutum biyu suna magana da shi. Waɗannan mutum biyu kuwa annabi Musa ne da annabi Iliya. 31 Sun bayyana da ɗaukaka, suna magana da Yesu a kan yadda zai cika nufin Allah ta mutuwa da zai yi a Urushalima. 32 Bitrus tare da abokan tafiyarsa kuwa suna barci. Da suka farka sai suka ga ɗaukakar Yesu da kuma mutum biyun nan da suke tsaye tare da shi. 33 Da mutanen nan za su bar Yesu ke nan, sai Bitrus ya ce masa, "Mai girma, ya yi kyau da muke a nan! Bari mu yi bukkoki uku, ɗaya dominka, ɗaya domin annabi Musa, ɗaya kuma domin annabi Iliya." Bai ma san abin da yake faɗa ba.

34 Bai rufe baki ba sai ga girgije ya rufe su; da girgijen ya rufe su, sai almajiran suka ji tsoro. 35 Sai murya ta fito daga cikin girgijen tana cewa, "Wannan Dana ne, wanda na zaɓa. Ku saurare shi!"

36 Da muryar ta yi shiru, sai aka ga Yesu shi kaɗai. Almajiran kuwa suka yi shiru da bakinsu. A kwanakin nan kuwa ba su faɗa wa kowa abin da suka gani ba.

Yesu Ya Warkar da Yaro Mai Aljani
(Mat 17.14-18; Mar 9.14-27)

37 Washegari, Yesu da almajiran nan guda uku suka sauka daga kan dutsen. Sai ga wani babban taro ya zo ya same shi. 38 Sai wani daga taron ya yi kira da ƙarfi, ya ce, "Malam! Ina roƙonka ka ji tausayin ɗan nan nawa, shi ne kaɗai nake da shi! 39 Ga shi, aljani yakan hau shi, yakan sa shi yă yi ihu kawai ba dalili. Aljanin kuma yakan buge shi, jikinsa yana rawa, har

9.28-35: 2 Bit 1.17-18 9.35: Ish 42.1; Mat 3.17; 12.18; Mar 1.11; Luk 3.22

bakinsa yă yi kumfa. Ba ya barinsa sai ya ji masa ciwo sosai.
40 To, na roƙi almajiranka su fitar da shi, amma ba su iya ba."

41 Sai Yesu ya amsa, ya ce, "Ku mutanen zamanin nan marasa bangaskiya, masu yin mugunta! Har zuwa yaushe zan zauna da ku, ina jimre muku? Kawo yaronka a nan."

42 Yaron yana zuwa ke nan sai aljanin ya ɗaga shi ya buga a ƙasa, jikinsa ya fara rawa. Amma Yesu ya tsawata wa aljanin, ya warkar da yaron, ya mai da shi ga babansa. 43 Dukan mutanen da suke wurin suka kama baki suna mamakin ikon Allah.

Yesu Ya Sāke Yin Magana game da Mutuwarsa
(Mat 17.22-23; Mar 9.30-32)

Mutane suna cikin mamakin abubuwan da Yesu yake yi, sai ya ce wa almajiransa, 44 "Kada fa ku manta da abin da zan faɗa muku! Za a ɓa da Ɗan Mutum ga hannun mutane." 45 Amma almajiran ba su gane abin da yake nufi da wannan magana ba, an ɓoye musu ita ne don kada su gane. Su kuma suka ji tsoro su tambaye shi game da wannan magana.

Wa Ya Fi Girma?
(Mat 18.1-5; Mar 9.33-37)

46 Sai mūsu ya tashi a tsakanin almajiran, a kan ko wane ne a cikinsu ya fi girma. 47 Yesu ya gane tunaninsu, sai ya ɗauki wani ɗan ƙaramin yaro, ya sa shi yă tsaya kusa da shi, 48 ya ce musu, "Duk wanda ya karɓi wannan ɗan yaro saboda ni, ya karɓe ni ne; kuma duk wanda ya karɓe ni, ya karɓi wanda ya aiko ni ne. Domin wanda ya fi ƙanƙanta a cikinku duka, shi ne ya fi girma."

Duk Wanda Ba Ya Gāba da Ku, Naku Ne
(Mar 9.38-40)

49 Sai Yohanna ya ce, "Mai girma, mun ga wani yana fitar da aljanu a cikin sunanka, muka hana shi, don ba ya cikinmu."

50 Yesu ya amsa, ya ce, "Kada ku hana shi, ai, duk wanda ba ya gāba da ku, naku ne."

Samariyawan Wani Kauye Sun Ki Su Karɓi Yesu

51 Da lokaci ya yi kusa da Yesu zai koma zuwa sama, ya yi niyya sosai yă tafi Urushalima. 52 Sai ya aiki 'yan aika su yi gaba, su kuwa suka je cikin wani ƙauye na Samariya, don su shishirya

9.46: Luk 22.24 **9.48:** Mat 10.40; Luk 10.16; Yoh 13.20

masa abubuwa. 53 Amma mutanen ƙauyen suka ƙi su karɓe shi,
don sun gane ya yi niyyar zuwa Urushalima ne. 54 Da almajiransa
Yakubu da Yohanna suka ga haka, sai suka ce, "Ubangiji, kana
so mu sa wuta yă sauka daga sama yă cinye su?"[s]
55 Amma Yesu ya juya, ya tsawata musu.[t] 56 Sai suka je wani
ƙauye.

Masu Cewa Za Su Bi Yesu

(Mat 8.19-22)

57 Da suna kan hanya, sai wani mutum ya ce wa Yesu, "Zan
bi ka duk inda za ka."
58 Yesu ya amsa masa ya ce, "Beraye suna da
ramummukansu, tsuntsaye kuma suna da wurin kwanansu, amma
Dan Mutum ba shi da wurin kwana."
59 Ya kuma ce wa wani, "Bi ni." Amma mutumin nan ya ce,
"Mai girma, bari in je in binne babana tukuna."
60 Yesu ya amsa masa ya ce, "Bari waɗanda suka mutu su
binne 'yan'uwansu matattu. Amma kai, ka je ka yi shelar mulkin
Allah."
61 Wani mutum kuma ya ce, "Ni zan bi ka, mai girma, amma
ka bar ni in je in yi bankwana da mutanen gidana tukuna."
62 Yesu ya ce masa, "Duk wanda ya fara noma da keken
noma, yana kuma duban baya, bai dace da mulkin Allah ba."

Yesu Ya Aiki Mutum Saba'in da Biyu

10 1 Bayan haka, Ubangiji ya kuma zaɓi waɗansu mutum
saba'in da biyu,[u] ya aike su biyu-biyu su yi gaba zuwa
garuruwa da wuraren da shi kansa ya shirya zai je. 2 Sai ya ce
musu, "Girbin yana da yawa, amma masu aikin kaɗan ne. Saboda
haka, ku roƙi mai gonar yă aiko da masu aiki su yi masa girbi.
3 Sai ku tafi. Ga shi, ina aikanku kamar tumaki cikin kuraye.
4 Kada ku ɗauki kudi, ko abinci, ko takalma. Kada ku yi doguwar
gaisuwa a kan hanya. 5 Duk gidan da kuka shiga, ku fara cewa,
'Salamarku mutanen gida!' 6 Idan da ɗan salama a gidan, to, bari
gaisuwarku ta salama ta kasance tare da shi; in kuwa babu, sai

---

9.54: 2 Sar 1.9-16 **9.61**: 1 Sar 19.20 **10.2**: Mat 9.37-38 **10.3**: Mat 10.16

[s] **9.54** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā sun ƙara, "Kamar yadda annabi Iliya ya yi."

[t] **9.56** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā sun ƙara da cewa "Ba ku san irin Ruhun da kuke da shi ba. Dan Mutum bai zo domin yă halaka rayukan mutane ba ne, amma yă cece su."

[u] **10.1 saba'in da biyu**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "saba'in" ne a nan.

gaisuwarku ta salama ta komo muku. 7 Ku zauna a wannan gida,
ku ci, ku sha duk irin abin da aka ba ku, domin ya kamata a biya
wa mai yin aiki hakkinsa. Ku daina bin gida-gida. 8 Duk garin da
kuka shiga, in an karɓe ku, ku ci duk irin abin da aka kawo muku.
9 Ku warkar da marasa lafiya da suke a garin, ku kuma faɗa wa
mutanen cewa, 'Mulkin Allah ya zo kusa da ku.' 10 Amma duk
garin da kuka shiga, aka ƙi karɓarku, ku bi titi-titi, kuna cewa,
11 'Ko ƙurar garinku da ta manne mana a ƙafafu ma, mun kakkaɓe
muku. Amma ku sani cewa mulkin Allah ya zo kusa da ku!' 12 Ina
dai gaya muku, a Ranar Karshe, Allah zai ji tausayin Sodom fiye
da wannan gari.

Garuruwan da ba Su Tuba Ba
(Mat 11.20-24)

13 "Kaitonki, Korasin! Kaitonki, Betsaida! Gama, da ayyukan
ban mamaki da aka yi a cikinku ne, aka yi a Taya da Sidon, da
sun tuba tun tuni, sun sa tsummoki, sun zauna, suna zuba wa
kansu toka. 14 A Ranar Karshe, Allah zai ji tausayin Taya da Sidon
fiye da ku. 15 Ke kuma Kafarnahum! Kina tsammani ɗaukaka ki
za a yi zuwa sama ne? A ina! Kaskantar da ke za a yi har zuwa
wurin zaman matattu!

16 "Duk wanda ya ji ku, ni ne ya ji. Duk wanda kuma ya ƙi
ku, ni ne ya ƙi. Duk wanda ya ƙi ni kuwa, ya ƙi wanda ya aiko
ni ne."

Saba'in da Biyun Sun Dawo

17 Mutum saba'in da biyun nan suka dawo da murna, suka
ce, "Ubangiji, har aljanu ma suna jinmu idan mun umarce su
cikin sunanka!"

18 Yesu ya amsa musu, ya ce, "Na ga Shaiɗan ya fāɗo daga
sama kamar walƙiya. 19 Ku ji nan! Na ba ku iko da za ku taka
macizai da kunamai, ku kuma shawo kan dukan ikon masu gāba,
babu kuma abin da zai faru da ku. 20 Duk da haka kada ku yi
murna don aljanu sun ji ku; ku yi murna dai domin an rubuta
sunayenku a sama."

10.7: 1 Kor 9.14; 1 Tim 5.18 **10.4-11:** Mat 10.7-14; Mar 6.8-11; Luk 9.3-5
10.10-11: A. M. 13.51 **10.12:** Far 19.24-28; Mat 11.24; 10.15
10.13: Ish 23.1-18; Ez 26.1—28.26; Jow 4.4-8; Amos 1.9-10; Zak 9.2-4
10.15: Ish 14.13-15 **10.16:** Mat 10.40; Mar 9.37; Luk 9.48; Yoh 13.20
10.19: Zab 91.13

Yesu Ya Yi Farin Ciki
(Mat 11.25-27; 13.16-17)

21 A wannan lokaci, Yesu cike da farin ciki ta wurin Ruhu
Mai Tsarki, ya ce, "Na gode maka, Uba, Ubangijin sama da ƙasa,
domin ka ɓoye waɗannan abubuwa ga masu hikima da masu ilimi,
ka kuma bayyana su ga 'yan yara. Haka ne ya Uba, gama wannan
shi ne abin da ya yi maka kyau.

22 "Ubana ya ba ni abu duka. Ba wanda ya san ko wane ne
Ɗan sai dai Uban kaɗai, ko kuma ya san ko wane ne Uban sai
dai shi Ɗan, da kuma wanda Ɗan ya so yă bayyana masa."

23 Sai ya juya wurin almajiran, ya ce musu a ɓoye, "Ku masu
albarka ne da waɗannan abubuwa suka faru a idanunku! 24 Ina
gaya muku, annabawa da sarakuna da yawa, sun so su ga abin
nan da kuke gani amma ba su sami dama ba. Sun so su ji abin
da kuke ji, amma ba su ji ba!"

Misalin Basamariyen da Ya Nuna Jinƙai

25 Sai ga wani malamin dokoki ya miƙe tsaye don yă gwada
Yesu. Ya tambaye shi ya ce, "Malam, me zan yi don in sami rai
na har abada?"

26 Yesu ya amsa masa ya ce, "Me Maganar Allah ta ce? Yaya
kuma kake fassarta ta?"

27 Mutumin ya ce, "An ce, 'Ka ƙaunaci Ubangiji Allahnka da
dukan zuciyarka, da dukan ranka, da dukan ƙarfinka, da kuma
dukan hankalinka; ka kuma ƙaunaci abokin zamanka kamar yadda
kake ƙaunar kanka'."

28 Yesu ya ce masa, "Ka faɗa daidai. To, ka yi haka, za ka
rayu."

29 Amma malamin dokokin ya so yă nuna cewa ba shi da laifi.
Saboda haka sai ya tambayi Yesu ya ce, "Shin, wane ne abokin
zamana?"

30 Yesu ya amsa masa ya ce, "An taɓa yin wani mutum
wanda ya tashi daga Urushalima yana gangara zuwa Jeriko. Sai
ya haɗu da 'yan fashi, suka ƙwace masa kayansa, suka yi masa
mugun dūka, suka bar shi a wurin bakin rai da mutuwa. 31 Ana
nan sai ga shi wani firist ya biyo kan wannan hanyar. Da ya
ga mutumin nan a kwance, sai ya bi gefe ya wuce abinsa.
32 Haka ma wani Balawe, da ya zo wurin ya gan shi a kwance,
shi ma ya yi gefe, ya wuce abinsa. 33 Ana nan dai, sai hanya ta

10.22: Yoh 3.35; 10.15 **10.27:** L. Fir 19.18; M. Sh 6.5
10.25-28: Mat 22.35-40; Mar 12.28-34 **10.28:** L. Fir 18.5

kawo wani mutumin Samariya inda yake. Da ya ga mutumin
nan, sai tausayi ya kama shi. 34 Ya je wurinsa, ya zuba mai da
ruwan inabi wato, magani a mikinsa, sa'an nan ya ɗaɗɗaura su;
ya ɗauke shi, ya sa a kan jakinsa, ya kai shi wani masauki, ya
yi jinyarsa. 35 Washegari, sai ya ɗauki yawan kudîn da lebura
zai samu a kwana biyu ya ba mai masaukin, ya ce, 'Ka lura
mini da wannan mutum, idan na dawo, zan biya ka duk abin
da ka kashe a kansa bayan wannan.' "

36 A ƙarshe, sai Yesu ya tambayi malamin dokokin nan ya
ce, "A ganinka wane ne a cikin mutanen nan uku ya nuna halin
abokin zama ga mutumin nan da ya fāɗi a hannun 'yan fashi?"

37 Malamin dokokin ya ce, "Wannan da ya ji tausayinsa."

Yesu ya ce masa, "Sai kai ma ka tafi ka yi haka."

Yesu Ya Ziyarci Marta da Maryamu

38 Yesu da almajiransa suna cikin tafiya ke nan, sai ya kai
wani ƙauye inda wata mace mai suna Marta ta karɓe shi a
gidanta. 39 Ita Marta tana da 'yar'uwa mai suna Maryamu,
wadda ta zauna kurkusa da Ubangiji tana jin maganarsa.
40 Marta kuwa aikin abinci ya ɗauke mata hankali, sai ta je
wurin Yesu, ta ce, "Ubangiji, ba ka damu da yadda 'yar'uwata
ta bar mini yin abinci ni kaɗai ba? Faɗa mata ta zo ta taimake
ni mana."

41 Amma Ubangiji ya amsa mata ya ce, "Marta, Marta,
hankalinki ya tashi, kin kuma damu a kan abubuwa da yawa.
42 Abu ɗaya tak ake bukata.[w] Maryamu ta riga ta zaɓi abu mai
kyau, wanda ba za a iya karɓe mata ba."

Koyarwar Yesu a kan Addu'a

(Mat 6.9-13; 7.7-11)

11 1 Wata rana Yesu yana addu'a a wani wuri. Da ya gama,
sai ɗaya daga cikin almajiransa ya ce masa, "Ubangiji, ka
koya mana yadda za mu yi addu'a, kamar yadda Yohanna ya
koya wa almajiransa mana."

2 Yesu ya ce musu, "In za ku yi addu'a, ku ce,
'Ya Uba,[y] a kiyaye sunanka da tsarki,
mulkinka yă zo.

10.33-34: 2 Tar 28.15 **10.38-39**: Yoh 11.1

[w] **10.42 Abu ɗaya tak ake bukata**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna
da, "Abubuwa kaɗan ne na musamman" ne a nan.

[y] **11.2 Ya Uba**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Ubanmu wanda
yake cikin sama" ne a nan.

3 Ka ba mu abinci na yau da na kowace[z] rana.
4 Ka gafarta mana zunubanmu, gama mu ma muna
gafarta wa duk wanda ya yi mana laifi.
Kada ka kai mu cikin jaraba.' "[a]

5 Yesu ya sāke ce wa almajiransa, "A ce, ɗayanku yana da aboki, ya je wurinsa da tsakar dare ya ce masa, 'Wāni, ka ba ni bashin burodi guda uku mana. 6 Ga shi wani abokina wanda ya fito tafiya ya sauka a wurina yanzu-yanzun nan. Kuma ba ni da abincin da zan ba shi.' 7 Sa'an nan a ce abokin nan da an je neman bashi a wurinsa yă amsa daga cikin ɗaki yă ce, 'Kada ka dame ni! Ai, na riga na kulle ƙofa, da ni da yarana duk mun kwanta, ba zan iya tashi in ba ka wani abu ba.' 8 Ina gaya muku, ko da ba zai tashi yă ba shi wani abu don shi abokinsa ba ne, zai tashi yă ba shi ko nawa yake so domin abokin bai ji kunya yă yi ta roƙo ba.

9 "Ina dai gaya muku, ku yi ta roƙo za a ba ku. Ku yi ta nema za ku samu. Ku yi ta ƙwanƙwasawa, za a buɗe muku. 10 Gama duk wanda ya roƙa, za a ba shi, duk wanda ya nema zai samu, kuma duk wanda ya ƙwanƙwasa za a buɗe masa. 11 Akwai wani a cikinku wanda in yaronsa ya roƙe shi[b] kifi sai yă ba shi maciji? 12 Ko kuwa yaron yă roƙi ƙwai sai a ba shi kunama? 13 Idan ku da kuke mugaye kun san yadda za ku ba 'ya'yanku abubuwa masu kyau, balle Ubanku na sama, zai ba da Ruhu Mai Tsarki ga masu roƙonsa."

Yesu da Ba'alzabul

(Mat 12.22-30; Mar 3.20-27)

14 Yesu yana fitar da beben aljani daga wani mutum; da aljanin ya fita, sai mutumin ya yi magana, taron kuwa suka yi mamaki. 15 Amma waɗansu mutane suka ce, "A hab! Ai, Ba'alzabul,[6] sarkin aljanu ne ya ba shi wannan iko na fitar da aljanu."

16 Waɗansu suna so su gwada Yesu, sai suka ce masa yă yi wani abin ban mamaki domin yă nuna Allah yana tare da shi. 17 Amma Yesu ya gane tunanin da suke ciki, sai ya ce musu,

---

11.15: Mat 9.34; 10.25 11.16: Mat 12.38; 16.1; Mar 8.11

[z] **11.3 na kowace rana:** Wani juyi na waɗannan kalmomin shi ne, "Abincinmu na gobe."

[a] **11.4 Kada ka kai mu cikin jaraba:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā sun ƙara, "Amma ka cece mu daga mai mugunta."

[b] **11.11 roƙe shi:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā sun ƙara, "Burodi, yă ba shi dutse, ko kuma in yaro ya tambaya . . ."

[6] **11.15 Ba'alzabul:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

"Duk mulkin da ya rabu kashi biyu suna gāba da juna, mulkin ba zai tsaya ba. Haka ma in gida ya rabu kashi biyu, suna gāba da juna, zai rushe. 18 In kuma Shaiɗan ya rabu kashi biyu yana gāba da kansa, yaya mulkinsa zai yi ƙarfi? Kun ce da ikon Ba'alzabul nake fitar da aljanu. 19 Idan da ikon Ba'alzabul nake fitar da aljanu, to, almajiranku fa? Da ikon wa suke fitarwa? Almajiranku ne za su yi muku shari'a a kan wannan. 20 Amma, idan da ikon Allah nake fitar da aljanu, ashe, mulkin Allah ya zo muku ke nan.

21 "Idan mutum mai ƙarfi ya yi shiri sosai, yana gadin gidansa, kayan gidansa za su zauna lafiya lau. 22 Amma idan wanda ya fi shi ƙarfi ya zo ya hau shi da faɗa ya kuma sha ƙarfinsa, sai yă ƙwace duk makaman da mutumin ya dogara da su, yă kuma rarraba kayayyakin da ya ƙwace.

23 "Wanda ba ya tare da ni, yana gāba da ni ke nan; wanda bai taimake ni tarawa ba kuwa, yana watsarwa ne."

Dawowar Baƙin Aljani

(Mat 12.43-45)

24 "Idan baƙin aljani ya fita daga jikin mutum, yakan yi ta yawo a wuraren da ba ruwa, don yă sami wurin hutawa. Idan bai samu ba, sai yă ce, 'Zan koma gidana da na fito.' 25 Idan ya zo ya samu an share, an kuma gyara gidan, 26 sai yă koma yă kwaso waɗansu aljanu bakwai waɗanda suka fi shi mugunta, su zo su zauna a wurin. A ƙarshe, zaman mutumin nan zai fi na farkon muni."

Albarka ta Gaskiya

27 Da Yesu ya faɗa haka, sai wata mace daga cikin jama'a ta ɗaga murya ta ce masa, "Allah yă albarkaci matar da ta haife ka, ta kuma goya ka har ka yi girma !"

28 Yesu ya amsa ya ce, "I, amma albarka ta fi tabbata ga waɗanda suke jin maganar Allah, suke kuma kiyaye ta!"

Neman Alama

(Mat 12.38-42)

29 Da mutane suka riƙa ƙaruwa wurin Yesu, sai ya fara cewa, "Wannan zamani mugun zamani ne. Suna nema a nuna musu wata alama, amma babu wata alamar da za a nuna musu sai ta Jona. 30 Kamar yadda Jona ya zama alama ga mutanen Nineba,

11.23: Mar 9.40 **11.29:** Mat 16.4; Mar 8.12

haka ma Dan Mutum zai zama ga mutanen zamanin nan. 31 A
Ranar Ƙarshe, Sarauniyar Kudu za ta tashi tare da mutanen
zamanin nan ta nuna musu ba su yi daidai ba, ta zo ne daga wuri
mai nisa sosai don ta ji koyarwar hikimar Solomon. Amma ga
wanda ya fi Solomon a nan. 32 A Rana Ƙarshe, mutanen Nineba
za su tashi tare da mutanen zamanin nan, su nuna musu ba su yi
daidai ba, don su sun tuba saboda wa'azin Jona. Ga shi kuwa
wanda ya fi Jona a nan!

Fitilar Jiki
(Mat 5.15; 6.22-23)

33 "Ba wanda zai kunna fitila sa'an nan yă ɓoye ta, ko kuma
yă rufe ta da kwano.[c] A'a, sai dai yă ajiye ta a kan tebur, inda
kowa da ya shiga zai ga hasken. 34 Ido shi ne fitilar jiki. In idonka
yana da lafiya, dukan jikinka zai cika da haske; amma idan idonka
ba lafiya, sai dukan jikinka yă rasa haske. 35 Ka lura fa, ko hasken
da kake da shi duhu ne. 36 In dukan jikinka yana da haske, ba
inda yake da duhu, ai, duk sai yă haskaka gaba ɗaya, kamar yadda
hasken fitila yake ba ka haske."

Yesu Ya Tona Asirin Farisiyawa da Malaman Dokoki
(Mat 23.1-36; Mar 12.38-40)

37 Da Yesu ya gama magana, sai wani Bafarisiye ya gayyaci
Yesu gidansa su ci abinci. Sai Yesu ya je ya zauna don cin abinci.
38 Da Bafarisiyen ya ga cewa Yesu bai wanke hannu kafin yă fara
cin abincin ba, sai mamaki ya kama shi. 39 Ubangiji ya ce masa,
"Ku Farisiyawa kukan wanke bayan kwaf da ƙwarya, amma
cikinku kuna cike da cuce-cuce da mugunta. 40 Wawaye kawai!
Ashe, ba Allahn da ya yi wajen ne ya yi cikin ma ba? 41 Da za
ku ba wa talakawa abin da kuke da shi, da kome zai zama da
tsabta a gare ku.

42 "Kaitonku, Farisiyawa! Kuna ba wa Allah zakkar kayan
yaji na ganye, da kuma sauran ganyen miya duka. Amma kun ƙi
kula da aikata gaskiya da ƙaunar Allah. Waɗannan ne ya kamata
ku yi, ba tare da kun ƙyale sauran ba.

43 "Kaitonku, Farisiyawa! Kun cika so a ba ku wuraren zama
masu daraja a majami'u, a kuma riƙa gaishe ku a kasuwa.

11.30: Yun 3.4 **11.31**: 1 Sar 10.1-10; 2 Tar 9.1-12 **11.32**: Yun 3.5
11.33: Mat 5.15; Mar 4.21; Luk 8.16 **11.42**: L. Fir 27.30

[c] **11.33 yă rufe ta da kwano**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da waɗannan kalmomin.

44 Kaitonku! Kun yi kama da kaburburan da ba a gani, waɗanda
mutane suke tafiya a kai don rashin sani."

45 Sai ɗaya daga cikin malaman dokoki ya ce wa Yesu,
"Malam, in ka faɗa haka, ai, mu ma, ka zage mu!" 46 Yesu ya
amsa, ya ce, "Kaitonku, ku ma malaman dokoki! Kun jibga wa
mutane kaya wato, dokoki masu nauyi su ɗauka, amma ku
kanku ba kwa taɓa kayan ko da yatsa ɗaya, don ku taimake su.
47 Kaitonku! Kun gina kaburbura masu kyau wa annabawan
Allah waɗanda kakanninku suka kashe. 48 Wato ku da kanku
kun shaida kun kuma yarda da yadda kakanninku suka yi. Sun
kashe annabawan, ku kuma kuka gina kaburburan. 49 Shi ya sa
hikimar Allah ta ce, 'Zan aika musu da annabawa da manzanni.
Za su kashe waɗansu, su ba wa waɗansu wahala.' 50 Saboda
haka za a hukunta mutanen zamanin nan saboda kashe-kashe
da aka yi wa dukan annabawa, tun kafawar duniya, 51 wato, tun
daga jinin Habila, har zuwa na Zakariya, wanda aka kashe
tsakanin bagaden hadaya da Wuri Mai Tsarki cikin haikali. I,
ina gaya muku, za a hukunta mutanen zamanin nan don
waɗannan duka!

52 "Kaitonku malaman dokoki! Kun rɓe mabuɗin gidan
ilimi, ku kanku ba ku shiga ba, ba ku kuma bar masu son shiga
su shiga ba."

53 Da Yesu ya bar wurin, sai malaman dokoki da Farisiyawa
suka fara matsa masa, suna tsokanarsa da tambayoyi a kan
abubuwa da yawa, 54 suna ƙoƙari su sa masa tarko don yă faɗa
wani abin da ba daidai ba.

Gargaɗi game da Munafunci

(Mat 10.26-27)

12 1 Sa'an da dubban mutane suka taru har suna tattaka juna,
sai Yesu ya yi wa almajiransa magana da farko ya ce, "Ku
yi hankali da yistin[d] Farisiyawa, wato munafuncinsu. 2 Ba abin
da yake a rufe da ba za a buɗe ba, kuma ba abin da yake a ɓoye
da ba za a sani ba. 3 Saboda haka, duk abin da kuka faɗa a ɓoye,
za a ji shi a fili. Abin da kuka kuma faɗa a asirce, ko a cikin
ɗaki da kuka rufe ƙofofinsa ma, za a yi shelarsa a kan rufin
ɗakuna.

11.51: Far 4.8; 2 Tar 24.20-21 **12.1**: Mat 16.6; Mar 8.15
12.2: Mar 4.22; Luk 8.17

[d] **12.1 Yisti**: Abu ne da ake sa a garin da ake yin burodi da shi domin burodin yă kumbura.

Wanda Za a Ji Tsoro
(Mat 10.28-31)

4 "Ku abokaina, ina gaya muku, kada ku ji tsoron masu kashen
jiki amma bayan sun kashe shi ba abin da za su iya yi kuma.
5 Zan faɗa muku wanda za ku ji tsoronsa. Ku ji tsoron Allah,
wanda bayan ya kashe, yana da iko yă jefa a cikin wuta kuma.
Gaskiya ina gaya muku, shi ne wanda za ku ji tsoronsa!
6 "Ba akan sayar da kanari biyar kobo biyu ba? Duk da haka
Allah bai manta da ko ɗayansu ba. 7 Kai! Har gashin kanku ma
an ƙirga su duka. Saboda haka, kada ma ku ji tsoro, don kun fi
kanari daraja sau barkatai!

Nuna Yarda da Almasihu a Gaban Mutane
(Mat 10.32-33, 12.32; 10.19-20)

8 "Ina kuma faɗa muku, duk wanda ya shaida a gaban mutane
cewa ya yarda da ni, Ɗan Mutum ma zai shaida ya yarda da shi
a gaban mala'ikun Allah. 9 Wanda kuma ya yi mūsu sanina a
gaban mutane, ni ma zan yi mūsu saninsa a gaban mala'ikun
Allah.
10 "Duk wanda ya yi maganar reni game da Ɗan Mutum, za
a yafe masa, amma duk wanda ya yi maganar reni game da Ruhu
Mai Tsarki, ba za a yafe masa ba.
11 "Idan kuma an kawo ku a gaban majami'u, ko gaban masu
hukunci, ko kuma gaban shugabanni, kada ku damu da yadda za
ku fitar da kanku, ko kuma abin da za ku ce, 12 domin Ruhu Mai
Tsarki zai koya muku abin da ya kamata ku faɗa a lokacin."

Misali a kan Wani Wawa Mai Arziki

13 Sai wani mutum daga cikin jama'a ya ce wa Yesu, "Malam,
ka ce wa ɗan'uwana yă ba ni rabona na kayan da babanmu ya
mutu ya bar mana."
14 Yesu ya amsa masa ya ce, "Kai! Wa ya mai da ni alƙali
ko in zama mai raba muku kayan da babanku ya mutu ya bar
muku?" 15 Ya ci gaba da yi wa mutane magana, ya ce musu, "Ku
lura fa, ku yi nesa da kowane irin kwaɗayi, don yawan kaya ba
shi ne samun rai ba."
16 Sai ya ba su wani misali ya ce, "An taɓa yin wani mai
arziki wanda gonarsa ta yi amfani sosai. 17 Ya fara tunani a
ransa, ya ce, 'Ba ni da inda zan sa amfanin gonata duka. Me
zan yi ke nan?'

12.10: Mat 12.32; Mar 3.29 **12.11-12:** Mat 10.19-20; Mar 13.11; Luk 21.14-15

18 "Ya ce wa kansa, 'Yawwa! Na san abin da zan yi. Zan
rushe wadannan rumbunana, in gina wadansu manya, in zuba
dukan amfanin gonata da kayana a ciki. 19 Zan kuma ce wa raina,
"Haba! Kana da kaya masu yawa wanda za ka more a shekaru
masu yawa. Bari ka huta, ka yi ta ci, ka yi ta sha, kana jin
dadinka." ' 20 Amma Allah ya ce masa, 'Kai wawa! A wannan
dare za ka mutu; sa'an nan in ga ko wane ne zai ci duk kayan
nan da ka tara wa kanka.' "

21 Yesu ya gama maganan nan da cewa, "Haka zai zama ga
duk wanda ya tara wa kansa dukiya, amma a gaban Allah ba shi
da arziki."

Ku Daina Damuwa
(Mat 6.25-34)

22 Sai Yesu ya ce wa almajiransa, "Don haka ina gaya
muku, kada ku damu da yadda za ku rayu, ko kuma yadda za
ku sami riguna don jikinku. 23 Domin rai ya fi abinci, jiki kuma
ya fi riguna. 24 Ku dubi tsuntsaye mana! Ai, ba sa shuka, ba sa
girbi, ba su da dakunan ajiyar abinci ko rumbuna, amma duk
da haka Allah yana ba su abinci. Darajarku kuwa ta fi ta
tsuntsaye sau barkatai! 25 Wane ne a cikinku ta wurin
damuwarsa, zai iya kara wa kansa ko awa daya ga kwanakin
rayuwarsa?[d] 26 To, idan ba za ku iya yin kankanin abu irin
wannan ba, don me kuke damuwa a kan sauran? 27 Ku dubi
yadda su fure suke girma mana. Ba sa aiki, ko sakan kome, ba
sa yi wa kansu riguna, duk da haka ina gaya muku ko sarki
Solomon da dukan girmarsa bai taba ado kamar daya daga
cikinsu ba. 28 To, idan har Allah zai yi wa ciyawar daji ado
haka, ciyawa wadanda suke nan yau, gobe kuwa a kone su,
balle ku? Ya ku marasa bangaskiya!

29 "Kada ku rika tunani a kan abin da za ku ci, ko abin da
za ku sha, kada ma ku damu. 30 Ai, mutanen duniya wadanda
ba su san Allah ba suna ta neman duk irin wadannan abubuwa.
Ku kuwa, Ubanku ya san kuna bukatarsu. 31 Ku dai sa ranku
ga mulkin Allah, zai ba ku dukan wadannan abubuwa kuma.

12.27: 1 Sar 10.4-7; 2 Tar 9.3-6
[d] **12.25 kara wa kansa ko awa daya ga kwanakin rayuwarsa:** Wani juyi na wadannan kalmomin shi ne, "Kara wa kansa kafa daya ga tsawonsa."

Koyarwa a kan Tara Dukiya a Sama
(Mat 6.19-21)

32 "Ya ku ƙaramin garkena, kada ku ji tsoro, domin Ubanku
yana jin dadî yă ba ku mulkinsa. 33 Ku sayar da dukan abin da
kuke da shi, ku ba wa talakawa kudîn. Ku yi wa kanku ajiyar da
ba za ta tsufa ba, wato, dukiyar da ba za ta lalace ba ke nan a
sama, inda ba ɓarawo da zai sace su, ba kuma asu da zai ɓata su.
34 Gama inda dukiyar mutum take, a nan ne tunaninsa ma yake.

Bayin da Suke a Shirye

35 "Ku zauna a shirye, fitilunku a kunne. 36 Ku zama kamar
bayin da suke jiran maigidansu yă dawo daga bikin aure. Da ya
dawo ya buga ƙofa, nan da nan sai su buɗe masa. 37 Zai zama
abin farin ciki ga bayin nan in har maigidan ya dawo ya same su
ba su yi barci ba. Ina gaya muku, zai cire babbar rigar da ya sa,
yă ce musu su zazzauna, su ci abinci, sa'an nan yă bi kan kowane
ɗayansu yă kawo masa abinci. 38 Bayin nan masu albarka ne in
ya dawo ko da tsakar dare, ko kuma da asuba, ya same su a
shirye. 39 Ku dai sani cewa in maigida ya san lokacin da ɓarawo
zai zo masa, ba zai bar shi yă shiga yă yi masa ɓarna a gida ba.
40 Sai ku zauna da shiri, domin Ɗan Mutum zai zo a lokacin da
ba ku yi tsammani zai zo ba."

Bawa Mai Aminci ko Marar Aminci
(Mat 24.45-51)

41 Bitrus ya ce, "Ubangiji, wannan misali a kanmu aka yi ko
kuwa ya shafi kowa?"

42 Ubangiji ya amsa masa ya ce, "Wane ne bawan nan mai
aminci da hikima? Shi ne wanda maigidansa zai sa shi yă lura
da gidansa, yake kuma ba wa sauran bayi abinci a daidai lokaci.
43 Mai albarka ne bawan da maigidansa zai zo yă same shi yana
yin aikinsa. 44 Gaskiya ina gaya muku, zai sa wannan bawa yă
lura masa da kayansa duka. 45 Amma idan bawan nan ya ce a
ransa, 'Ai, maigidana ya yi letin zuwa,' sa'an nan ya fara dūkan
sauran bayin, mata da maza, ya kuma shiga ci da sha, har yana
buguwa, 46 maigidan wannan bawa zai dawo a ranar da bawan
bai yi tsammani ba, kuma a lokacin da bai sani ba. Maigidan
nan zai yi masa mugun dūka yă kuma hukunta shi tare da
marasa aminci.

12.35: Mat 25.1-13 **12.36:** Mar 13.34-36 **12.39-40:** Mat 24.43-44

47 "Bawan da ya san abin da maigidansa yake so yă yi, amma
bai yi shiri ba, bai kuma yi abin da ake so yă yi ba, za a yi masa
bulala sosai. 48 Wanda kuwa bai san abin da maigidansa yake so
yă yi ba, ya kuma yi abin da ya isa a dūke shi, za a dūke shi
kaɗan. Duk wanda aka ba shi abu mai yawa, za a nemi abu mai
yawa daga gare shi. Wanda kuma aka ba shi abu mai yawa sosai,
za a nemi abu mai yawa sosai daga gare shi.

Yesu Ya Kawo Rabuwa Ne
(Mat 10.34-36)

49 "Wuta ce na zo in sa wa duniya. Da so na ne, a ce ta huru
ko! 50 Ina da baftismar da za a yi mini, na kuwa matsu a zuciya
sosai har sai an yi mini ita! 51 Kuna tsammani zaman lafiya ne
na kawo wa duniya? A ina! Ina gaya muku, rabuwa ce na kawo.
52 Daga yanzu, a gida ɗaya, mutum biyar za su rabu kashi biyu,
uku suna gāba da biyu, biyu kuma suna gāba da uku. 53 Baba zai
yi gāba da ɗansa, ɗan kuma yă yi gāba da babansa. Mama za ta
yi gāba da 'yarta, 'yar kuma ta yi gāba da mamarta. Mamar miji
za ta yi gāba da matar ɗanta, matar ɗan kuma ta yi gāba da mamar
mijinta."

Gane Yanayin Lokaci
(Mat 16.2-3)

54 Yesu ya kuma ce wa mutane, "In kun ga hadari ya taso
daga yamma, kukan ce ai, za a yi ruwan sama; sai kuwa a yi.
55 Idan kuma kun ji iska tana hurawa daga kudu, sai ku ce za
a yi zafi; sai kuma a yi. 56 Munafukai! Kun iya gane yanayin
ƙasa da na sararin sama, amma ganewar alamun zamanin nan
ya gagare ku.

Shirya da Mai Kararka
(Mat 5.25-26)

57 "Me ya sa ku kanku ba kwa iya tunani ku gane abin da ya
fi kyau ku yi? 58 Idan wani ya kai ƙararka a kotu, ka yi ƙoƙari
ku shirya tun kuna a kan hanya. In ka ƙi, zai kai ka gaban alƙali.
Alƙali kuma yă miƙa ka ga ɗan sanda. Dan sanda kuma yă sa ka
a kurkuku. 59 Ina gaya maka, ba za ka fita a wurin ba sai ka biya
dukan abin da aka yanka maka, ba ko sauran kobo."

12.50: Mar 10.38 **12.53**: Mika 7.6

Tuba ko Halaka

13 [1] A daidai wannan lokacin waɗansu mutanen da suke
wurin suka gaya wa Yesu labarin Galilawan da Bilatus
ya sa aka kashe lokacin da suke miƙa wa Allah hadayarsu.
[2] Yesu ya amsa musu ya ce, "Don an kashe Galilawan nan haka,
kuna tsammani sun fi kowa zunubi ke nan a Galili? [3] Sam! Ina
gaya muku, idan ba ku tuba a kan laifofinku ba, dukanku za ku
mutu kamarsu. [4] Ko kuwa mutane sha takwas dîn nan da gini
ya fādî a kansu a Siluwam, ya kashe su, kuna tsammani sun fi
duk sauran mutanen Urushalima zunubi ne? [5] Sam! Ina gaya
muku, in ba kun tuba ba, za ku mutu kamarsu."

Misali na Baure Marar 'Ya'ya

6 Sai Yesu ya ba su misali ya ce, "An taɓa yin wani mutum
wanda yake da itacen ɓaure a gonar inabinsa. Sai ya zo don yă
tsinka 'ya'yan, amma bai sami ko ɗaya ba.

Hoton ɓaure (13.6)

7 Sai ya ce wa mutumin da yake lura da gonar, 'Duba, yau
shekara uku ke nan ina zuwa neman 'ya'yan ɓauren nan, amma
kullum ba na samun kome a kansa. Sare shi! Don me za a bar
shi yă tare wuri a banza?' [8] Amma mai lura da gonar ya amsa ya
ce, 'Mai girma, a bar shi dai, in yi masa bankasa, in kuma zuba
masa taki a wannan shekara. [9] Idan ya yi 'ya'ya nan gaba, to, in
kuma bai yi ba, sai a sare shi.' "

Yesu Ya Warkar da Mace a Ranar Hutu

10 Wata rana Yesu yana koyarwa a wata majami'a a Ranar
Hutu, 11 sai ga wata mace wadda aljani ya sa ciwo ya shanye ta
na tsawon shekaru goma sha takwas. Duk ta tanƙware, ba ta ma
iya miƙewa. 12 Da Yesu ya gan ta, sai ya kira ta ya ce, "Uwargida,
an warkar da ke daga rashin lafiyarki." 13 Sai ya sa hannunsa a
kanta, nan da nan sai ta miƙe tsab, ta yabi Allah.

14 Amma shugaban majami'ar ya ji haushi yadda Yesu ya
warkar da ita a Ranar Hutu. Sai ya ce wa mutanen da suke nan,
"Akwai ranaku har shida da ya kamata a yi aiki, ku zo a ranakun
nan a warkar da ku, ba Ranar Hutu ba."

15 Amma Ubangiji ya ce masa, "Munafukai kawai! Ashe,
kowannenku ba ya kunce saniyarsa ko jakinsa, yă kai shi wurin
da zai sha ruwa a Ranar Hutu? 16 Macen nan, 'yar dangin Ibrahim,
wadda Shaiɗan ya ɗaure, yau shekara goma sha takwas. Ashe,
bai yi daidai a warkar da ita a Ranar Hutu ba?" 17 Wannan
maganarsa da ya yi, ta sa duk masu ƙin ganinsa suka ji kunya.
Sauran mutane kuwa, duk suka yi ta murna saboda abubuwan ban
mamaki da yake yi.

Misali na Kwayar Mastad
(Mat 13.31-32; Mar 4.30-32)

18 Sai Yesu ya ce, "Yaya mulkin Allah yake? Da me kuma
zan kwatanta shi? 19 Mulkin sama kamar ƙwayar mastad ne wadda
ta fi ƙanƙanta cikin iri duka, wadda wani mutum ya ɗauka ya
shuka a lambunsa, sai ta yi girma har ta zama itace, tsuntsaye
suka yi gida a rassanta."

Misali na Yisti
(Mat 13.33)

20 Yesu ya sāke tambaya, "Da me zan kwatanta mulkin Allah?
21 Kamar yisti yake wanda wata mace ta kwaɓa da mudu uku na
garin alkama, har duk garin ya game da yistin."

Karamar Kofa
(Mat 7.13-14, 21-23)

22 Da Yesu ya kama hanya zai tafi Urushalima, sai ya bi
birane da ƙauyuka yana koya wa mutane. 23 Sai wani ya tambaye
shi ya ce, "Malam, shin, wai mutane kaɗan ne kawai za su sami
ceto?"

13.14: Fit 20.9-10; M. Sh 5.13-14

Yesu ya ce musu, 24 "Ku yi ƙoƙari ku shiga ta ƙaramar ƙofa,
domin mutane da yawa za su yi ƙoƙarin shiga amma ba za su iya
ba. 25 In dai maigidan ya riga ya tashi ya rufe ƙofar gidan, ku
kuwa za ku tsaya a waje kuna bugan ƙofar, kuna cewa, 'Maigida,
a buɗe mana ƙofa!' Shi kuma zai amsa muku yă ce, 'Ban san
inda kuka fito ba!' 26 Sa'an nan za ku fara kuka kuna cewa, 'Haba,
mu da muka ci, muka sha tare da kai, har ka koyar a
garuruwanmu.' 27 Amma zai ce, 'Ban san inda kuka fito ba. Ku
rabu da ni, mugaye kawai!' 28 Sa'ad da kuka ga Ibrahim, da
Ishaku, da Yakubu, da dukan annabawa a mulkin Allah, ku kuwa
ana korarku, a nan ne za ku yi kuka da cizon haƙora. 29 Mutane
za su zo daga gabas da yamma, kudu da arewa, su zauna cin biki
a mulkin Allah. 30 A nan ne fa waɗanda suke na ƙarshe za su
zama na farko, na farko kuma su zama na ƙarshe."

Yesu Ya Damu sosai a kan Urushalima
(Mat 23.37-39)

31 A wannan lokaci sai waɗansu Farisiyawa suka zo suka ce
wa Yesu, "Ka tashi daga nan fa, domin Hirudus yana so yă kashe
ka."

32 Sai ya ce musu, "Ku je ku gaya wa mai makircin nan cewa,
'Yau ina fitar da aljanu, ina kuma warkar da mutane, gobe ma
haka, jibi ne zan gama aikina. 33 Duk da haka lallai ne in ci gaba
da tafiyata yau da gobe, da kuma jibi, don kuwa bai yi kyau a ce
annabi ya mutu ba, in ba a Urushalima ne aka kashe shi ba.'

34 "Ayya, Urushalima! Urushalima! Masu kashen annabawa,
masu jifar waɗanda aka aiko gare ku! Sau nawa na so in tattara
ku kamar yadda kaza take tattara 'yan yaranta cikin fikafikanta,
amma kun ƙi! 35 Ga shi an bar muku gidanku, ba kowa! Ina kuwa
gaya muku, ba za ku ƙara ganina ba, sai ranar da kuka ce, 'Mai
albarka ne, wanda yake zuwa cikin sunan Ubangiji!' "

Yesu Ya Warkar da Mai Ciwo

14 1 Wata Ranar Hutun Yahudawa, Yesu ya shiga gidan wani
shugaban Farisiyawa don yă ci abinci. Mutane suka zuba
masa ido. 2 Sai ga wani da ƙafafunsa da hannayensa sun
kumbura ya zo wurin Yesu. 3 Sai Yesu ya tambayi malaman
dokoki da Farisiyawa ya ce, "Dokarmu ta yarda a yi warkarwa
a Ranar Hutu, ko babu?"

13.27: Zab 6.9 **13.28**: Mat 22.13; 25.30 **13.28-29**: Mat 8.11-12
13.30: Mat 19.30; 20.16; Mar 10.31 **13.35**: Zab 118.26; Irm 22.5

4 Amma ba su ce kome ba. Yesu kuwa ya kama mutumin dîn,
ya warkar da shi, sa'an nan ya ce masa yă tafi abinsa. 5 Sa'an
nan Yesu ya tambayi mutanen, ya ce, "Idan jakinku[e] ko saniyarku
ya fādî a rijiya Ranar Hutu, ba za ku cire shi nan da nan ba wai
don Ranar Hutu ne?" 6 Suka rasa amsar wannan tambaya.

Dauki Kanka Kamar ba Kome ba Ne

7 Da Yesu ya ga wadansu a cikin mutanen da aka gayyata don
cin abinci suna ɓoɓarin zaɓan kujeru masu daraja, sai Yesu ya
faɗa musu wannan misali. 8 "Idan wani ya kira ka bikin aure,
kada ka je ka fara zauna a wurin zaman manya, don watakila an
kira wani da ya fi ka daraja. 9 Shi wanda ya kira ku duka biyu
kuwa zai zo yă ce maka, 'Tashi, ka ba ma wannan wuri.' Ka ga,
za ka ji kunya, don za ka koma kan wurin zama marar daraja.
10 Amma idan an kira ka biki, ka je ka nemi wurin zama marar
daraja ka zauna, don in wanda ya kira ka ya zo, sai yă ce maka,
'Zo nan, abokina, ka zauna a wannan kujera mai daraja.' Wannan
zai sa sauran mutanen da aka kira, su ba ka girma. 11 Gama duk
wanda ya ɗaga kansa za a mai da shi ba kome ba, amma duk
wanda ya mai da kansa ba kome ba ne, za a ba shi girma."

Yin Alheri

12 Sai Yesu ya ce wa wanda ya kira shi, "Idan ka kira wani
don cin abinci, ko ka shirya biki, kada ka kira abokanka ne
kawai, ko 'yan'uwanka, ko danginka, ko abokan zamanka masu
arziki, don wata rana za su kira ka, su ma. Ta haka za su biya
ka abin da ka yi musu. 13 Amma in za ka kira mutane biki, ka
kira talakawa, da guragu, da shanyayyu da makafi. 14 Ta haka
za ka sami albarka, domin wadannan dai ba za su iya biyanka
ba. Allah ne zai biya ka a ranar da masu halin kirki za su tashi
daga matattu."

Misalin Babban Biki

(Mat 22.1-10)

15 Da jin haka, sai wani da yake tare da shi a tebur dîn ya ce
wa Yesu, "Mai albarka ne duk wanda zai ci abinci a bikin nan
na mulkin Allah!"

14.5: Mat 12.11 **14.8-10:** K. Mag. 25.6-7 **14.11:** Mat 23.12; Luk 18.14

[e] **14.5 jakinku:** Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "yaronku" ne a nan.

16 Yesu ya ce masa, "An taɓa yin wani mutumin da ya shirya
babban biki, ya kuma kira mutane da yawa. 17 Da lokacin bikin
ya yi, sai ya aiki bawansa yă je yă ce wa waɗanda aka kira, 'Ku
zo, gama an gama shirya kome!' 18 Amma sai dukansu suka fara
ba da hujjoji. Na farko ya ce, 'Na sayi gona, dole ne in je in gani
yadda take, ina roƙonka, ka yi mini haƙuri.' 19 Dayan kuma ya
ce, 'Na sayi shanun noma guda goma, ina hanyata ke nan in
gwada su, ina roƙonka, ka yi mini haƙuri.' 20 Wani kuma ya ce,
'Kwana-kwanan nan ne na yi aure, saboda haka ba zan sami
damar zuwa ba.'

21 "Bawan ya koma ya gaya wa maigidansa dukan abin da
aka gaya masa. Haushi ya kama maigidan, sai ya ce wa bawan,
'Yi maza, ka bi titi-titi da lungu-lungu na birni, ka tattara
talakawa, da guragu, da makafi, da shanyayyu ka kawo su nan.'
22 Nan da nan, bawan ya dawo ya ce, 'Ranka yă daɗe, an yi
abin da ka faɗa, amma da sauran wuri har yanzu.' 23 Maigidan
ya ce wa bawan, 'Ka je kan manyan hanyoyi da ƙanana, ka turo
mutane su zo, don gidana yă cika. 24 Ina gaya muku, babu ko
ɗaya daga cikin mutanen nan da dā aka kira da zai ɗanɗana
abincin bikin nan da na shirya.' "

Wuyar Rayuwar Bin Almasihu
(Mat 10.37-38)

25 Wata rana, mutane da yawa suna bin Yesu, sai ya juya ya
ce musu, 26 "Duk mai son bina, in bai fi ƙaunata fiye da babansa,
ko mamarsa, ko matarsa, ko 'ya'yansa, ko 'yan'uwansa maza
da mata, har ma ransa ba, ba zai iya zama almajirina ba. 27 Duk
wanda bai ɗauki gicciyensa ya bi ni ba, ba zai iya zama
almajirina ba.

28 "Misali: Idan wani daga cikinku yana so yă yi gini, zai fara
zauna, yă yi lissafin abin da ginin zai ci tukuna yă gani ko yana
da isasshen kuɗin da zai gama ginin. 29 In bai yi haka ba, ba zai
iya gama ginin ba bayan ya fara, kuma dukan mutanen da suka
ga wannan aikin za su yi masa dariya, 30 za su ce, 'Wannan mutum
ya fara gini amma ya kāsa gamawa.'

31 "Idan wani sarki zai fita da sojoji dubu goma, don yă yi yaƙi
da wani da yake da sojoji dubu ashirin, ai, zai zauna tukuna yă
duba ko yana da isasshen ƙarfin da zai yaƙi wancan sarkin. 32 Idan
ba zai iya ba, to, tun suna da nisa sai yă aika da 'yan-aika su je

14.26: Mat 10.37 **14.27**: Mat 10.38; 16.24; Mar 8.34; Luk 9.23

su nemi hanyar zaman lafiya. 33 Haka ma kowannenku in bai bar
duk abin da yake da shi ba, ba zai iya zama almajirina ba."

Misali a kan Gishiri
(Mat 5.13; Mar 9.50)

34 "Gishiri abu ne mai kyau, amma idan ya rabu da dadinsa, ta
yaya za a mai da dadinsa? 35 Ba shi da wani amfani a gona, ko a
taki, sai dai a zubar da shi kawai. Bari mai kunnen ji, yă ji."

Misali na Tunkiyar da Ta Bace
(Mat 18.12-14)

15 1 Wata rana masu karɓar haraji da "masu zunubi" suka zo
don su ji koyarwar Yesu. 2 Sai Farisiyawa da malaman
dokoki suka fara gunaguni suna cewa, "Haba! Wannan mutum
ya mai da kansa abokin masu zunubi, har ma yana cin abinci da
su." 3 Sai Yesu ya ba su wannan misali:

4 "A ce ɗayanku yana da tumaki ɗari, sai ɗayansu ta ɓace, to,
ai, zai bar casa'in da taran a inda suke kiwo, yă je neman wannan
da ta ɓace. 5 Idan ya same ta, zai yi murna, yă ɗauke ta a kafaɗa
6 yă kai ta gida. Sa'an nan yă kira abokansa da kuma waɗanda
suke zama tare da shi, yă ce musu, 'Ku taya ni murna gama na
sami wannan tunkiya da ta ɓace!' 7 Ina dai gaya muku, haka za
a yi murna sosai a sama a kan mai zunubi guda ɗaya da ya tuba,
fiye da masu adalci casa'in da tara, waɗanda ba sa bukatar tuba.

Misali a kan Kuɗin da ya Bace

8 "A ce, mace tana da kuɗin azurfa guda goma, ɗaya ya ɓata,
ai, za ta kunna fitila ta share gidan, ta yi ta nemansa sai ta same
shi. 9 Idan ta same shi, sai ta tara abokanta da waɗanda suke zama
tare da ita, ta ce musu, 'Ku taya ni murna, don na sami kuɗin
nan da ya ɓace.' 10 Ina gaya muku, haka zai zama abin murna ga
mala'ikun Allah in mai zunubi guda ya tuba."

Misali a kan Uba Mai Kauna

11 Sai Yesu ya ce, "An taɓa yin wani mutum wanda yake da
yara maza biyu. 12 Karamin a cikinsu ya ce wa babansu, 'Baba,
ni a ba ni yanzu abin da aka shirya za a ba ni bayan ka mutu.'
Sai baban ya raba musu dukiyarsa. 13 Bayan 'yan kwanaki, sai
yaron ya tattara kayansa duk, ya tashi ya bar gida. Ya je wani
gari mai nisa. A can ne ya je ya yi banza da kuɗin, cikin iskanci.

15.1-2: Luk 5.29-30

14 Bayan ya cinye duk abin da yake da shi, sai muguwar yunwa
ta shiga wannan garin; shi kuwa ya shiga cikin rashi. 15 Sai ya je
ya nemi aiki a wurin wani mutumin ƙasar, sai mutumin ya tura
shi wajen da aladunsa suke, yă je yă yi kiwo. 16 Ya nemi dusan
da aladun suke ci don yă ci, amma ba wanda ya ba shi. 17 A
ƙarshe sai ya dawo ciki hankalinsa, sai ya ce, 'Kai! Ga ma'aikatan
babana duk suna banza da abinci, a ce ga ni zan mutu da yunwa!
18 Zan tashi in koma wurin babana in ce, "Baba, na yi wa Allah
laifi, na kuma yi maka. 19 Ban ma isa a ƙara kirana yaronka ba.
Ka sa ni in zama kamar ɗaya daga cikin ma'aikatanka." ' 20 Sai
ya tashi ya kama hanya zai koma wurin babansa.

"Tun yana daga nesa, sai babansa ya gane shi. Tausayi ya
kama baban, ya tashi da gudu, ya je ya kama yaronsa, ya yi ta
rungumarsa. 21 Yaron ya ce, 'Baba, na yi wa Allah laifi na kuma
yi maka. Ban isa a ƙara kirana yaronkaf ba.' 22 Amma baban ya
kira bayinsa, ya ce, 'Maza! Ku kawo riga mafi kyau, ku sa masa.
Ku sa masa zobe da takalma, 23 a kuma kawo saniya mai ƙiban
nan a yanka, mu ci, mu yi murna. 24 Domin yaron nan nawa, dā
ya mutu amma yanzu ya dawo. Dā ya ɓace, amma yanzu an same
shi.' Sai suka yi murna sosai.

25 "To, a wannan lokacin dai babban yaronsa da ya je gona
yana dawowa. Da ya yi kusa da gida, sai ya ji ana buga ganga,
ana rawa. 26 Sai ya kira wani bawan gidan, ya tambaye shi abin
da yake faruwa.

27 "Bawan ya ce, 'Ai, ƙanenka ne ya dawo, shi ne babanka
ya sa aka yanka saniya mai ƙiban nan saboda ɗan'uwanka ya
dawo gida lafiya ƙalau.'

28 "Amma wan ya ji haushi sosai, ya ƙi yă shiga gida. Babansu
ya fito ya ba shi haƙuri, ya roƙe shi yă shiga ciki. 29 Amma ya
amsa wa babansa ya ce, 'Duba, duk waɗannan shekaru, ina maka
aiki kamar bawa, ban taɓa ƙin yi abin da ka ce in yi ba. Duk da
haka, ba ka taɓa ba ni ko ɗan akuya in kira abokaina mu ci da
su ba! 30 Amma da yaron nan naka ya dawo, wanda ya je ya cinye
dukiyarka a kan karuwai, ka yanka masa saniyan nan mai ƙiba.'
31 Sai baban ya ce masa, 'Yarona, kullum kana nan tare da ni,
duk abin da nake da shi, ai, naka ne. 32 Ya kamata mu yi murna
da farin ciki, domin ɗan'uwanka nan dā ya mutu, yanzu kuwa ya
dawo, dā ya ɓace, amma yanzu an same shi.' "

f15.21 **Yaronka**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da, "Ka ɗauke ni kamar ɗaya daga cikin ma'aikatanka."

Misali a kan Wakili Marar Gaskiya

16 [1] Yesu ya ce wa almajiransa, "An taɓa yin wani mai arziki
wanda ya ba wa wakilinsa kaya yă lura masa da su. Daga
baya an kawo masa labarin yadda wakilin nan yana banza da
kayan maigidansa. [2] Sai maigidan ya kira wakilin ya ce masa, 'Me
nake ji haka a kanka? Ka kawo mini lissafin aikin da kake yi,
domin ba za ka ƙara zama wakilina ba.' [3] Sai wakilin ya ce a
ransa, 'Maigidana zai kore ni daga aiki, me zan yi? Ga shi ba ni
da ƙarfin noma, kuma ina jin kunya in fara bara. [4] Yawwa! Na
san abin da zan yi, don idan an kore ni daga aikina, mutane su
karɓe ni a gidajensu.'

5 "Sai ya kira dukan mutanen da maigidansa yake binsu bashi.
Ya tambayi na farkon ya ce, 'Nawa ne maigidana yake binka?'
[6] Ya ce, 'Garwar mai guda ɗari.'

"Wakilin ya ce, 'Ga takardarka, maza, ka rubuta hamsin.' [7] Ya
kuma ce wa wani, 'Kai fa, nawa ne ake binka?' Sai shi kuma ya
ce, 'Buhun alkama guda ɗari ne.' Wakilin ya ce, 'Ga takardarka,
ka mai da shi tamanin.'

8 "Sai maigidan ya yabi wakilin nan marar gaskiya saboda ya
yi wayo. Gama 'yan zamani sun iya bi da mutanen zamaninsu
fiye da mutanen haske."

9 Yesu ya ci gaba da cewa, "Ina dai gaya muku, ku yi amfani
da dukiyarku don ku sami wa kanku abokai. Ta haka in dukiyar
ta ƙare, za a karɓe ku a gidajensu na har abada. [10] Wanda ya isa
a yarda da shi a ƙaramin abu, za a iya yarda da shi a babban abu
ma. Wanda yake marar gaskiya a ƙaramin abu, zai iya zama marar
gaskiya ma a babban abu. [11] Idan fa ba ku yi aminci da dukiya
ta wannan duniya ba, wa zai ba ku amanar dukiya ta gaskiya?
[12] Idan kuma ba ku yi aminci da kayan wani ba, wa ma zai ba
ku wanda yake naku?

13 "Ba bawan da zai iya bauta wa shugabanni biyu, ko dai yă
ƙi ɗaya, yă so ɗaya, ko kuwa yă yi wa ɗayan aminci, yă rena
ɗayan. Ba dama ku sa ranku ga bin Allah ku kuma sa ga kuɗi
kuma duk gaba ɗaya."

Ba Za a Iya Canza Dokar Allah Ba
(Mat 11.12-13, 5.31-32)

14 Da yake Farisiyawa masu son kuɗi ne, da jin abin nan da
Yesu ya faɗa, sai suka yi tsaki. [15] Amma Yesu ya ce musu, "Ku

---

16.13: Mat 6.24

ne masu son nuna a gaban mutane cewa ku masu adalci ne. Amma Allah ya san zuciyarku. Abubuwan da mutane suke ba su girma, su ne Allah ba ya ma son gani.

16 "Dokar Musa da littattafan annabawa ne abin da mutane suka yi ta bi har zuwa lokacin Yohanna Maibaftisma. Amma tun da aka yi wa'azin Labari Mai Dadi na mulkin Allah, kowa yana ƙoƙari sosai yă sami shiga. 17 Duk da haka zai fi sauƙi sararin sama da ƙasa su shuɗe, da a ce an yar da digo guda ɗaya daga Dokan nan.

Koyarwa a kan Kashen Aure
(Mat 19.1-12; Mar 10.1-12)

18 "Duk wanda ya saki matarsa ya auri wata, ya yi zina ke nan, kuma duk wanda ya auri matar da ta bar mijinta, zina ne yake yi da ita kawai.

Wani Mai Arziki da Li'azaru

19 "An yi wani mai arziki wanda yakan sa riguna masu tsada, yakan kuma ci abinci mai kyau kowace rana. 20 A ƙofar gidansa kuwa da wani gajiyayye mai suna Li'azaru, wanda miki sun cika jikinsa. Akan kawo shi a kwantar da shi a nan kullum. 21 Shi kuwa yakan so yă ci ko da sauran abincin da ya fādi daga kan tebur na mai arzikin nan. Har karnuka ma suna zuwa su lashe mikinsa.

22 "Ana nan sai talakan nan ya mutu, mala'iku suka ɗauke shi, suka ba shi wurin zama mai daraja tare da Ibrahim. Mai arzikin nan ma ya mutu aka kuma binne shi. 23 Ya je can wurin zaman matattu yana shan wuya, sai ya ɗaga kai ya ga Ibrahim daga nesa, tare da Li'azaru. 24 Sai ya yi kira ya ce, 'Baba Ibrahim, ka ji tausayina, ka aiki Li'azaru ya sa ɗan yatsarsa a ruwa yă ɗan sa a harshena don in ji ɗan sanyi, domin ina jin jiki a cikin wannan wuta!'

25 "Amma Ibrahim ya ce, 'Ka tuna fa yarona, a lokacin da kake duniya, kana da abubuwa masu kyau, Li'azaru kuwa ya sha wuya. Amma yanzu yana jin dadi, kai kuwa kana shan wahala. 26 Ban da haka ma, tsakaninmu da ku akwai wani ƙaton rami mai zurfi sosai da aka shirya don kada waɗanda suke son ƙetarewa daga can zuwa wurinmu su iya, kada kuma kowa yă ƙetare daga wurinmu zuwa can.' 27 Sai mai arzikin nan ya ce, 'To, baba, ina roƙonka, ka aike shi zuwa gidan babana, 28 don ina da 'yan'uwa

16.16: Mat 11.12-13 **16.17:** Mat 5.18 **16.18:** Mat 5.32; 1 Kor 7.10-11

guda biyar maza, yă je yă yi musu magana, kada su ma su zo nan wurin wahala.'

29 "Ibrahim ya ce, 'Ai, 'yan'uwanka suna da Dokar Musa da littattafan annabawa, su ji abin da suke faɗa musu.' 30 Mai arzikin ya amsa masa ya ce, 'A'a, baba Ibrahim, in dai wani ya tashi daga kabari ya je wurinsu za su tuba.' 31 Amma Ibrahim ya ce, 'Idan ba su ji abin da Dokar Musa da littattafan annabawa suke cewa ba, kai, ko da wani ya tashi daga kabari, ba za su ji shi ba!' "

Magana a kan Zunubi da Yafewar Zunubi

(Mat 18.6-7, 21-22; Mar 9.42)

17 1 Yesu ya ce wa almajiransa, "Dole ne a sami abubuwan da za su sa mutane su yi zunubi. Amma zai zama abin tausayi ga duk wanda ya zama dalilin kawo su! 2 Da wani yă sa ɗaya daga cikin 'yan yaran nan yă yi zunubi, gara a ɗaura babban dutsen niƙa a wuyansa a jefa shi cikin teku. 3 Ku lura da kanku fa.

"Idan ɗan'uwanka ya yi maka laifi, ka yi masa magana. In ya nemi gafara, ka yafe masa. 4 Ko da ya yi maka laifi sau bakwai wato, ba iyaka a rana ɗaya, in har ya riƙa cewa, 'Na yi laifi, ka yafe mini,' sai ka yafe masa."

Kara Mana Bangaskiya

5 Sai manzanni suka ce wa Ubangiji, "Ka ƙara mana bangaskiya."

6 Ubangiji ya amsa musu ya ce, "Idan kuna da bangaskiya dą ta kai ko da misalin ƙwayar mastad, wadda ta fi ƙankanta ciki iri duka za ku ce wa wannan babban itace, 'Ka bar nan, ka je ka tsaya a can cikin teku!' Zai kuma bi abin da kuka ce yă yi.

Zama Bawan Kirki

7 "Misali, wane ne a cikinku in yana da bawa wanda yake yi masa noma ko kuwa kiwon tumaki da in ya dawo daga gona, zai ce masa, 'Yi maza, ka zo ka zauna, ka ci abinci?' 8 A maimakon haka ba za ka ce masa, 'Ka shirya mini abincin yamma tukuna, ka kawo mini in ci in sha, kafin ka ci naka, ba?' 9 Za a gode wa bawa don ya yi aikin da ya kamata yă yi ne? 10 Haka ku ma, idan kuka bi duk abin da aka ce muku ku yi, sai ku ce, 'Mu bayi ne kawai. Mu dai muna yin abin da ya kamata mu yi ne kawai.' "

17.3: Mat 18.15

Yesu Ya Warkar da Kutare Guda Goma

11 Da Yesu ya kama hanya zai je Urushalima, sai ya bi kan
iyaka da take tsakanin Samariya da Galili. 12 Zai shiga wani ƙauye
ke nan sai ga kutare wato, masu ciwon fatar jiki guda goma, suka
tsaya da nisa 13 suka ɗaga murya suka ce, "Ya Yesu Mai girma!
Ka ji tausayinmu!"

14 Da Yesu ya gan su, sai ya ce musu, "Ku je wurin firistoci
su gan ku."

Suna kan hanyar tafiya ke nan sai suka tsarkake. 15 Da ɗayansu
ya ga an warkar da shi, sai ya koma, yana yabon Allah da murya
mai ƙarfi. 16 Ya zo ya durƙusa a gaban Yesu, ya gode masa. Shi
mutumin nan Basamariye ne. 17 Yesu ya ce, "Ba mutane goma
ne aka warkar da su ba? Ina sauran taran? 18 Me ya sa sai baƙon
nan ne kaɗai ya dawo don yă yi wa Allah godiya?" 19 Yesu ya
ce masa, "Tashi ka tafi abinka, bangaskiyarka ce ta sa ka warke."

Zuwan Mulkin Allah
(Mat 24.23-28, 37-41)

20 Da waɗansu Farisiyawa suka tambayi Yesu lokacin da
mulkin Allah zai zo, sai ya ce musu, "Ai, zuwan mulkin Allah
ba da ido ake ganinsa ba. 21 Ba wanda zai ce, 'Ai, ga shi nan,'
ko kuma 'ga shi can.' Domin mulkin Allah yana nan a cikinku."

22 Yesu ya kuma ce wa almajiransa, "Lokaci yana zuwa
wanda za ku yi marmarin ganin rana ɗaya daga cikin ranakun
Ɗan Mutum, amma ba za ku gani ba. 23 Mutane za su ce muku,
'Duba can,' ko kuma, 'Duba nan.' Amma kada ku je ku duba.
24 Lokacin da Ɗan Mutum zai sāke zuwa, zai zo kamar walƙiyar
da take haskakawa daga wannan bangon duniya zuwa wancan.
25 Amma sai ya fara shan wahala iri-iri tukuna, har mutanen
zamanin nan su ƙi shi. 26 Kamar yadda dai ya faru a zamanin
Nuhu, haka ne zai faru a lokacin da Ɗan Mutum zai dawo.
27 Mutane suka riƙa ci da sha, maza suna aure, ana ba da mata
ga aure har zuwa ranar da Nuhu ya shiga jirgi, ruwan tsufana
kuma ya zo ya halaka su duka. 28 Haka ma aka yi a lokacin Lutu.
Kowa yana ci, yana sha, ana saya, ana sayarwa, ana shuki, ana
kuma gine-gine. 29 Amma a ranar da Lutu ya bar Sodom, aka
zuba wuta da duwatsu masu zafi daga sama, aka kakkashe su
duka. 30 Haka zai zama a ranar da Ɗan Mutum zai bayyana.

17.14: L. Fir 14.1-32 **17.26**: Far 6.5-8 **17.27**: Far 7.6-24
17.28-29: Far 18.20—19.25

31 "A ranan nan fa, wanda yake kan rufin ɗaki kada yă sauko
wai zai kwashe kayansa a cikin gida. Haka ma duk wanda ya je
gona, kada yă koma gida. 32 Ku tuna fa da matar Lutu! 33 Duk
wanda yake son ajiyar ransa, zai rasa shi; amma wanda ya ba da
ransa, ajiyarsa yake yi. 34 Ina gaya muku, a daren da wannan zai
faru za a ga mutane biyu suna kwance a gado ɗaya za a ɗauki
ɗaya a bar ɗaya. 35 Mata biyu za su kasance suna niƙan dawa tare,
za a ɗauki ɗaya, a bar ɗaya."[g]

37 Sai almajiran suka tambaye shi, suka ce, "Ina ne,
Ubangiji?"

Ya ce musu, "Ai, inda gawa take, nan ne ungulaye suke
taruwa."

Misali a Kan Yin Addu'a ba Fasawa

18 1 Sai Yesu ya ba wa almajiransa wani misali don yă koya
musu cewa ya kamata su riƙa yin addu'a kullum, kada su
gaji. 2 Ya ce, "An taɓa yin wani alƙali a wani gari wanda ba ya
tsoron Allah, ba ya kuma kula da mutane. 3 A nan garin kuma
akwai wata macen da mijinta ya mutu wadda ta riƙa zuwa wurin
alƙalin tana roƙonsa cewa, 'Ka ba ni hakkina cikin ƙarar da aka
kawo a kaina.' 4 Da farko, ya ƙi, amma daga baya ya ce a ransa,
'Ko da yake ba na tsoron Allah, ba na kuma kula da mutane,
5 amma don macen nan ta dame ni, zan yi ƙoƙari in ga cewa ta
sami abin da ta roƙa, don kada yawan zuwanta yă kawo mini
gajiya!' "

6 Sai Ubangiji ya ce, "Ku ji fa abin da alƙalin nan marar
gaskiya ya ce! 7 Ashe, Allah ba zai biya wa mutanen da ya zaɓa
waɗanda suke masa kuka dare da rana hakkinsu ba? Zai yi
sanyin jiki wajen taimakonsu ne? 8 Ina dai gaya muku, zai biya
musu hakkinsu, da wuri-wuri kuwa. Amma sa'ad da Ɗan
Mutum ya dawo, zai sami wani da bangaskiya a duniyan nan
kuwa?"

Misali na Bafarisiye da Mai Karɓar Haraji

9 Yesu ya kuma faɗa wannan misali ga mutanen da sun ɗauke
kansu masu adalci ne har suna rena sauran mutane. 10 Ya ce, "An
taɓa yin mutane biyu waɗanda suka shiga haikali don su yi

17.31: Mat 24.17-18; Mar 13.15-16 **17.32:** Far 19.26
17.33: Mat 10.39; 16.25; Mar 8.35; Luk 9.24; Yoh 12.25
[g] **17.35** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya ta 36 haka "Mutum biyu za su kasance a gona, za a ɗauki ɗaya, a bar ɗaya."

addu'a. Daya a cikinsu Bafarisiye ne, ɗayan kuma mai karɓar haraji.

11 "Sai Bafarisiyen ya tashi ya tsaya,[k] ya fara addu'a yana cewa, 'Allah, na gode maka saboda ni ba kamar sauran mutane ba ne, masu sata, masu cuta, masu zina. Ni ba kamar mai karɓar harajin nan ba ne. 12 Ina azumi sau biyu a mako, ina kuma ba da kashi ɗaya bisa goma na kowane abin da na samu.'

13 "Amma mai karɓar harajin nan ya tsaya da nisa, bai ko ɗaga idonsa sama ba. Saboda baƙin cikinsa ya yi ta bugun ƙirjinsa, yana cewa, 'Allah, ka ji tausayina, ni mai zunubi ne!' " 14 Yesu ya ce, "Ina gaya muku, mai karɓar harajin nan ya koma gidansa da samun zaman marar laifi a gaban Allah, ba kamar Bafarisiyen ba. Gama duk wanda ya ɗaga kansa, za a mai da shi ba kome ba. Amma duk wanda ya mai da kansa ba kome ba, za a ba shi girma."

Yesu Ya Sa wa 'Yan Yara Albarka

(Mat 19.13-15; Mar 10.13-16)

15 Waɗansu suka kawo 'yan yaransu domin Yesu ya sa musu albarka. Da almajiransa suka ga haka, sai suka fara tsawata musu. 16 Amma Yesu ya kirawo 'yan yaran, ya ce, "Ku bar yara ƙanana su zo wurina. Kada ku hana su. Gama, mulkin Allah na irinsu ne. 17 Gaskiya ina gaya muku duk wanda bai karɓi mulkin Allah kamar yadda ƙaramin yaro yake yi ba, ba zai taɓa shiga cikinsa ba."

Shugaba Mai Arziki

(Mat 19.16-30; Mar 10.17-31)

18 Wani shugaban Yahudawa ya tambayi Yesu ya ce, "Malam, mai kirki, me zan yi in sami rai na har abada?"

19 Yesu ya tambaye shi, ya ce, "Don me kake ce da ni mai kirki? Ai, ba wani mai kirki sai Allah kaɗai. 20 Ka dai san abin da dokoki suka ce, 'Kada ka yi zina. Kada ka yi kisankai. Kada ka yi sata. Kada ka yi shaidar ƙarya. Ka ba da girma ga babanka da mamarka.' "

21 Mutumin ya ce, "Ai, duk na kiyaye waɗannan tun ina yaro."

18.14: Mat 23.12; Luk 14.11 **18.20**: Fit 20.12-16; M. Sh 5.16-20

[k] **18.11 Ya tsaya**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da, "Ya tashi yana yi wa kansa addu'a" ne a nan.

22 Da jin haka, sai Yesu ya ce masa, "Akwai abu ɗaya tak da
ya rage maka ka yi. Ka sayar da duk abin da kake da shi, ka raba
wa talakawa, za ka sami dukiya a sama. Sa'an nan ka zo ka bi
ni." 23 Da jin wannan magana, sai mutumin ya ɓata rai, don shi
mai arziki ne sosai.

24 Da Yesu ya ga ya ɓata rai, sai ya ce, "Zai zama da wuya
sosai masu arziki su shiga mulkin Allah! 25 Gama zai fi wa raƙumi
sauƙi yă bi ta ramin allura, da mai arziki yă shiga mulkin Allah."

26 Mutanen da suka ji wannan magana suka tambaye shi, suka
ce, "To, in haka ne, wa zai iya samun ceto?"

27 Yesu ya ce, "Abin da ya fi ƙarfin mutum, bai fi ƙarfin
Allah ba."

28 Sai Bitrus ya ce, "To, ga shi mun bar gidajenmu mun bi
ka."

29 Yesu ya amsa ya ce, "Na san da haka, kuma ina gaya muku,
ba wanda zai bar gida, ko mata, ko 'yan'uwa, ko iyaye, ko 'ya'ya
saboda mulkin Allah 30 da zai kāsa samun abubuwa da yawa a
yanzu, a can wurin zaman matattu kuma yă sami rai marar
ƙarewa."

Yesu Ya Sāke Yin Magana a kan Irin Mutuwar da Zai Yi

(Mat 20.17-19; Mar 10.32-34)

31 Sai Yesu ya kai sha biyun nan gefe ɗaya, ya ce musu, "Ga
shi, za mu je Urushalima, inda dukan abin da annabawa suka
rubuta a kan Ɗan Mutum zai cika. 32 Za a ba da shi ga waɗanda
ba Yahudawa ba, a yi masa ba'a, a wulaƙanta shi, a kuma tofa
masa miyau. 33 Za su yi masa bulala, su kuma kashe shi, amma
a rana ta uku zai tashi."

34 Amma almajiran ba su gane da maganan nan da Yesu ya
yi ba. An ɓoye musu ma'anar maganan nan, shi ya sa ba su gane
abin da yake faɗa ba.

Yesu Ya Warkar da Makaho Mai Bara

(Mat 20.29-34; Mar 10.46-52)

35 Da Yesu ya yi kusa da Jeriko, sai ga wani makaho yana
zaune a gefen hanya, yana bara. 36 Da ya ji mutane da yawa suna
wucewa, sai ya yi tambaya komene ne yake faruwa.

37 Suka ce masa, "Ai, Yesu Banazare ne yake wucewa."

38 Sai ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, "Yesu! Ɗan Dawuda!
Ka ji tausayina!"

39 Mutanen da suke gaba suka tsawata masa yă yi shiru.
Amma sai ya ƙara ɗaga murya da ƙarfi sosai, yana cewa, " Ya
Ɗan Dawuda, ka ji tausayina!"
40 Sai Yesu ya tsaya, ya ce a kawo shi wurinsa. Da ya zo
kusa, Yesu ya tambaye shi, 41 "Me kake so in yi maka?" Sai
makahon ya amsa ya ce, "Mai girma, ina so in sami ganin gari."
42 Yesu ya ce masa, "To, ka sami ganin gari! Bangaskiyarka
ce ta warkar da kai."
43 Nan da nan sai ya sami ganin gari, ya bi Yesu, yana
ɗaukaka Allah. Da mutane suka ga wannan, sai duka suka yabi
Allah.

Yesu Ya Ceci Zakka

19 1 Yesu ya shiga Jeriko, yana wucewa cikin garin ke nan,
2 sai ga wani shugaban masu karɓar haraji, mai suna
Zakka. Shi kuwa mai arziki ne, 3 ya yi ta ƙoƙari yă ga kowane
ne Yesun nan, amma bai iya ba domin shi wani ɗan gajere ne,
kuma mutane sun yi yawa. 4 Saboda haka sai ya yi gaba da gudu,
ya sami wani babban itace ya hau, don yă gan shi, gama Yesu
zai bi ta nan ne. 5 Da Yesu ya kai wurin, sai ya ɗaga kansa sama
ya ce, "Zakka, yi maza ka sauko! Yau zan sauka a gidanka."
6 Zakka ya yi sauri ya sauka, ya karɓe shi da murna. 7 Da jama'a
suka ga haka, sai duk suka fara gunaguni, suka ce, "Ai! Gidan
mai zunubin nan ne ya sauka!"
8 Sai Zakka ya tashi a tsaye, ya ce wa Ubangiji, "Ka ji nan,
mai girma, zan ba da rabin arzikin da nake da shi wa talakawa.
Duk wanda kuma na taɓa cutarsa, zan biya shi sau huɗu abin da
dā na karɓa."
9 Sai Yesu ya ce masa, "Yau dai, ceto ya zo gidan nan, tun
da shi ma ɗan Ibrahim ne. 10 Gama Ɗan Mutum ya zo ne yă nemi
yă kuma cece waɗanda suka ɓace."

Misali na Fam Goma
(Mat 25.14-30)

11 Tun suna jin waɗannan abubuwa, Yesu ya ci gaba da gaya
musu wani misali, domin ya yi kusa da Urushalima, mutane kuma
suna tsammani mulkin Allah zai bayyana nan da nan. 12 Sai ya
ce musu, "An taɓa yin wani babban mutum wanda za shi wani
gari da nisa don a naɗa shi sarki, yă dawo. 13 Kafin yă tafi, ya
kira bayinsa guda goma, ya ba kowannensu yawan kuɗin da

19.8: Fit 22.1; 2 Sam 12.6 **19.10**: Mat 18.11 **19.11**: Mat 25.14-30

lebura zai samu cikin wata uku, ya kuma ce musu, 'Ku yi kasuwanci da su sai na dawo.' 14 Mutanen garinsa kuwa ba sa sonsa. Saboda haka, sai suka aika da 'yan aika bayan ya tafi su ce, 'Ba ma son wannan mutum yă zama sarkinmu.'

15 "Aka nadà mutumin nan sarki, ya dawo gida. Da shigarsa sai ya aika a kira masa duk bayinsa, don yă san riba nawa suka samu a kan kudîn da ya bar musu. 16 Na fari ya zo ya ce, 'Mai girma, na ci riba fam goma daga fam ɗaya da ka ba ni.' 17 Sai maigidan kuma ya ce masa, 'Madalla, bawan kirki! Tun da ka yi gaskiya a kan ƙarami abu, zan sa ka ka yi mulkin garuruwa goma.' 18 Bawa na biyu ya zo, ya ce, 'Mai girma, na ci riba fam biyar daga fam ɗaya da ka ba ni.' 19 Maigidan ya ce wa wannan, 'Za ka yi mulkin garuruwa biyar.'

20 "Wani kuma ya zo, ya ce, 'Mai girma, ga fam ɗayanka. Na ɗaure shi a ɗan tsumma, na ɓoye. 21 Gama ina jin tsoronka, don kai wani irin mutum ne mai wuyar sha'ani. Ga so na banza a wurinka ba dama; kakan yi girbin abin da ba ka shuka ba.' 22 Sai ya ce masa, 'Kai wani mugun bawa ne! Zan yi maka shari'a a kan abin da ka faɗa da bakinka. Ashe, ka san cewa ni mutum ne mai wuyar sha'ani, mai so na banza, ina kuma girbin abin da ban shuka ba? 23 To, in ka san haka, me ya sa ba ka sa kudîna a banki ba, don in na dawo in sami riba a kai?'

24 "Sai ya ce wa waɗanda suke tsaye a wajen, 'Karɓi fam ɗayan daga wurinsa a ba wa bawan nan mai fam goma.' 25 Amma suka amsa masa suka ce, 'Mai girma, ai, yana da fam goma ko.' 26 Ya amsa ya ce, 'Ina gaya muku, gama duk wanda yake da abu za a ƙara masa. Wanda ba shi da abu kuwa, ko ɗan kaɗan dîn da yake da shi ma, sai an karɓe masa. 27 Waɗannan masu ƙina kuma, waɗanda ba sa so in yi mulki a kansu, ku kawo su nan a kashe su a gabana.' "

Yesu Ya Shiga Urushalima

(Mat 21.1-11; Mar 11.1-11; Yoh 12.12-19)

28 Da Yesu ya faɗa haka, sai ya yi gaba zuwa Urushalima. 29 Da ya kai kusa da waɗansu ƙauyukan da ake ce da su Betafaji da Betani da suke gefen Dutsen Itatuwan Zaitun, ya aika almajiransa guda biyu, 30 ya ce musu, "Ku shiga ƙauyen nan na gabanku. Da kun kai, za ku ga wani ɗan jaki da ba a taɓa hawa ba a ɗaure. Ku kunce shi ku kawo nan. 31 Idan wani ya ce, 'Don me kuke kunce jakin?' Ku ce masa, Mai girma yana bukatarsa."

19.26: Mat 13.12; Mar 4.25; Luk 8.18

32 Waɗanda aka aika, suka tafi, suka kuma sami kome kamar
dai yadda Yesu ya gaya musu. 33 Suna cikin kuncewa ke nan, sai
masu jakin suka ce musu, "Don me kuke kunce shi?"
34 Suka ce, "Ai, Mai girma ne yake bukatarsa." 35 Suka kai
shi wurin Yesu. Da suka shimfiɗa rigunansu a kan jakin, sai suka
ɗauki Yesu suka sa shi a kai. 36 Yana cikin tafiya, sai mutane
suka rika shimfiɗa rigunansu a kan hanya.
37 Da ya yi kusa da Urushalima, daidai wurin da hanyar ta
gangara a kan Dutsen Itatuwan Zaitun, sai taron almajiransa da
yawa suka fara gode wa Allah, suna yabonsa da murya mai ƙarfi
a kan abubuwa masu ban mamaki da suka gani. 38 Suna cewa,

"Mai albarka ne Sarkin da yake zuwa a cikin sunan
Ubangiji!
Salama ta kasance a sama,
ɗaukaka kuma ga Allah!"

39 Sai waɗansu Farisiyawa da suke cikin jama'ar suka ce
masa, "Malam, ka tsawata wa almajiranka su yi shiru!"
40 Ya amsa ya ce, "Ina gaya muku, ko waɗannan sun yi shiru,
duwatsu ma da kansu za su fara ihu."

Yesu Ya Yi Kuka saboda Urushalima

41 Da ya zo kurkusa, ya ga birnin Urushalima, sai ya yi
masa kuka. 42 Ya ce, "Da ma a ce yau kun san abin da ake
bukata don zaman lafiya! Amma ga shi ba za ku iya gani ba.
43 Lokaci yana zuwa da masu gāba da ku za su gina bango
kewaye da ku su yi yaƙi da ku. Sojoji za su kewaye ku ta
kowane gefe. 44 Za su yi kaca-kaca da ku, su kuma kashe
mutanenku duka. Ba ko dutse ɗaya na gine-ginenku da za a bari
a kan ɗan'uwansa. Wannan zai faru ne saboda ba ku yarda cewa
Allah ya zo domin yă cece ku ba."

Yesu Ya Tsabtace Haikali

(Mat 21.12-17; Mar 11.15-19; Yoh 2.13-22)

45 Sai Yesu ya shiga haikali ya fara korar masu sayar da kaya,
46 yana ce musu, "Ai, a rubuce yake cewa, 'Gidana zai zama gidan
addu'a.' Amma kun mai da shi wurin ɓuyan 'yan fashi!"
47 Kowace rana ya yi ta koyarwa a haikali. Amma manyan
firistoci, da malaman dokoki, da shugabannin jama'a sun nemi
hanyar da za su kashe shi. 48 Amma ba su sami hanyar da za su

19.38: Zab 118.26 **19.46:** Ish 56.7; Irm 7.11 **19.47:** Luk 21.37

kashe shi ba domin maganarsa ta ɗauki hankalin kowa da yake a wurin, kuma ba sa so ko kalma ɗaya ta wuce musu.

Ana Shakkar Iznin Yesu
(Mat 21.23-27; Mar 11.27-33)

20 1 Wata rana Yesu ya shiga haikali yana koyarwa, yana kuma wa'azin Labari Mai Daɗi ga mutane, sai manyan firistoci da malaman dokoki tare da shugabannin jama'a suka zo 2 suka ce masa, "Gaya mana iznin da kake da shi da kake yin waɗannan abubuwa. Wa ya ba ka iznin?"

3 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ni ma zan yi muku wata tambaya. Ku gaya mini, 4 iznin da Yohanna ya yi baftisma da shi, Allah ne ya ba shi, ko kuwa mutum?"

5 Sai suka tattauna a junansu, suna cewa, "Idan mun ce, 'Daga wurin Allah ya zo,' zai ce, 'Don me ba ku gaskata shi ba?' 6 In kuma muka ce, 'Daga mutum ne,' yawan mutanen nan za su jejjefe mu da duwatsu, domin kowa ya yarda cewa Yohanna annabi ne." 7 Don haka suka ce masa, "Ba mu san inda ya fito ba."

8 Sai Yesu ya ce musu, "Ni ma ba zan faɗa muku, ko da wane izni nake yin waɗannan abubuwa ba."

Misali na Masu Noma da Suka Karɓi Hayar Gonar Inabi
(Mat 21.33-46; Mar 12.1-12)

9 Sai Yesu ya gaya wa mutane wannan misali, ya ce, "An taɓa yin wani mutumin da ya yi gonar inabi, sa'an nan ya ba da hayarta ga waɗansu manoma, sa'an nan ya tafi wata ƙasa, ya daɗe a can. 10 Da lokacin girbin inabin ya yi, sai ya aiki wani bawansa yă je wurin waɗannan da suka karɓi hayar gonar, yă karɓo masa waɗansu 'ya'yan inabi daga gonar. Amma 'yan hayar suka yi masa dūka, suka sallame shi hannu wofi. 11 Sai mutumin nan ya sāke aiki wani bawa; amma waɗannan 'yan hayar suka yi masa dūka shi ma, suka kuma wulaƙanta shi suka sallame shi hannu wofi. 12 Har wa yau mutumin ya aika da wani bawa na uku, shi kuma suka ji masa ciwo, suka jefa shi waje. 13 Sa'an nan, mutumin nan mai gonar inabin ya ce, 'Yanzu me zan yi? Zan aika da ɗana wanda nake ƙauna; na san lallai za su ba shi girma!' 14 Amma da 'yan hayar suka gan shi, suka ce wa juna, 'Aha! Ga wanda zai ci gādon gonar, bari mu kashe shi, don gādonsa yă zama namu!' 15 Sai suka wurga shi a bayan katanga, suka kashe shi.

20.9: Ish 5.1

"To, me kuke tsammani mai gonan nan zai yi da 'yan hayan nan? 16 Zai zo ya halaka 'yan hayan nan, ya ba wa waɗansu hayar gonar."

Da mutane suka ji haka suka ce, "Allah yă sawwaƙe!"

17 Amma Yesu ya dube su ya ce, "Me Maganan nan ta Allah take nufi? 'Dutsen da masu gini suka ƙi shi ne ya zama dutsen da ya fi amfani duka a ginin!' 18 Duk wanda ya fāɗi a kan wannan dutsen, zai yi kucu-kucu; kuma idan dutsen nan ya fāɗi a kan wani, zai niƙa shi yă zama kamar gari."

Tambaya game da Biyan Haraji ga Kaisar

(Mat 22.15-22; Mar 12.13-17)

19 A nan ne malaman dokoki da manyan firistoci suka so su kama Yesu, domin sun gane cewa ya yi wannan misali a kansu ne; amma sun ji tsoron mutane. 20 Sai suka nemi hanya, suka biya waɗansu mutane su yi kamar su masu kirki ne. Suka aike su su sa wa Yesu tarko da irin tambayoyin da za su yi masa, don su samu su ba da shi ga iko da kuma hukuncin mai mulki. 21 Waɗanda aka aika kuwa suka tambayi Yesu, suka ce, "Malam, mun sani cewa maganarka da koyarwarka gaskiya ne, mun kuma sani ba ka nuna bambanci, kuma kana koyar da hanyar Allah cikin gaskiya. 22 To, kana gani daidai ne mu biya wa Kaisar haraji, ko a'a?"

23 Amma Yesu ya gane wayonsu, sai ya ce musu, 24 "Nuna mini dinari. Hoton wa da sunan wane ne a kansa?"

Suka amsa, "Na Kaisar ne."

25 Sai ya ce, "To, sai ku ba Kaisar abin da yake na Kaisar, ku kuma ba Allah abin da yake na Allah."

26 A nan kuma suka kāsa kama shi da magana a gaban mutane. Sai suka yi shiru suna mamakin wannan amsar da ya ba su.

Tambaya a kan Tashin Matattu

(Mat 22.23-33; Mar 12.18-27)

27 Sai ga waɗansu Sadukiyawa,[i] waɗanda suke cewa wai babu tashin matattu, sun zo wurin Yesu, suka ce, 28 "Malam, Musa ya rubuta mana wannan umarni cewa, 'Idan mutum ya mutu ya bar matarsa ba 'ya'ya, ya kamata ɗan'uwansa yă aure ta don yă samo masa 'ya'ya.' 29 To, an taba yin waɗansu mutane su bakwai, duk 'yan'uwan juna. Babban ya yi aure ya mutu ba

20.17: Zab 118.22 **20.27:** A. M. 23.8 **20.28:** M. Sh 25.5

[i] **20.27 Sadukiyawa:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

yaro. 30 Na biyun ya auri matar, ya mutu ba yaro. 31 Na ukun
ma haka. Sai ya zama dukansu bakwai dîn sun auri macen nan,
amma sai suka mutu babu 'ya'ya. 32 A ƙarshe kuma, ita macen
ta mutu. 33 To, a tashin matattu, matar wa za ta zama? Gama
duk bakwai dîn sun aure ta."

34 Yesu ya ce musu, "A zamanin nan maza suna aure, ana
kuma ba da mata ga aure, 35 amma waɗanda za su cancanci tashi
daga matattu su kuma zauna a zamani mai zuwa maza ba za su
yi aure ba, ba za a kuma ba da mata ga aure ba. 36 Gama ba ya
yiwuwa su sāke mutuwa domin za su zama kamar mala'iku. Za
su kuwa zama 'ya'yan Allah ke nan domin sun tashi daga matattu.
37 Kuma Musa ya nuna a fili cewa waɗanda suka mutu za su tashi.
A labarin ƙaramin itacen da ya ci wuta, ya yi magana a kan
Ubangiji cewa, 'Shi ne Allah na Ibrahim, Allah na Ishaku, da
kuma Allah na Yakubu'. 38 Shi ba Allah na matattu ba ne, amma
na masu rai. Wannan ya nuna cewa a gare shi kowa mai rai ne."

39 Sai waɗansu malaman dokoki suka yi magana suka ce,
"Malam ka faɗa daidai!" 40 Daga nan kuma ba su yi ƙarfin hali
su ƙara tambayarsa wani abu ba.

Tambaya a kan Almasihu

(Mat 22.41-46; Mar 12.35-37)

41 Yesu ya tambaye su ya ce, "Yaya za a ce Almasihu ɗan
Dawuda ne? 42 Dawuda da kansa ya ce a Zabura,

'Ubangiji ya ce wa Ubangijina,
"Zauna a damana,
43 Sai na sa ka taka masu ƙinka." '

44 Dawuda ya ce da Almasihu 'Ubangiji.' To, yaya kuma za a ce
da shi ɗan Dawuda?"

Yesu Ya Tona Asirin Malaman Dokoki

(Mat 23.1-36; Mar 12.38-40; Luk 11.37-54)

45 Ya gaya wa almajiransa a gaban mutane cewa, 46 "Ku yi
hankali da malaman dokoki, su masu son sa manyan riguna suna
yawo, masu so a gaishe su a kasuwa, masu so a ba su wuraren
zama masu daraja a majami'u, da wuraren zama masu kyau a
wurin biki. 47 Su ne masu cin kayan matan da mazansu suka mutu,
sa'an nan su yi doguwar addu'a don a gan su. Ai, su za su sha
hukunci mafi tsanani."

20.37: Fit 3.6 **20.42-43:** Zab 110.1

Baikon Macen da Mijinta Ya Mutu
(Mar 12.41-44)

21 [1] Yesu ya ɗaga kai ya ga waɗansu masu kuɗi suna sa
baikonsu a wurin zuba baiko. [2] Sai ya ga wata matalauciya
da mijinta ya mutu ta zo ta sa baiko na 'yan tagulla biyu da ba
su kai kobo ba. [3] Sai Yesu ya ce, "Gaskiya, ina gaya muku, baikon
da matalauciyan nan ta sa, ya fi na sauran duka. [4] Gama dukansu
sun bayar daga yawan abin da suke da shi ne, amma ita kuwa
cikin rashinta ta sa duk ɗan kuɗin da take da shi a rayuwarta."

Yesu Ya Faɗa Irin Rushewar da Za Ta Sami Haikali
(Mat 24.1-2; Mar 13.1-2)

5 Waɗansu suka fara magana a kan haikali, da irin duwatsu
masu kyau da aka gina shi da su, da kuma irin kyautai da aka yi
masa ado da su. Sai Yesu ya ce, [6] "Idan don waɗannan abubuwan
da kuke kallo ne, to, lokaci yana zuwa da ba wani dutsen da za
a bari nan a kan ɗan'uwansa, kowannensu za a rushe shi."

Farkon Wahala
(Mat 24.3-14; Mar 13.3-13)

7 Sai suka tambaye shi suka ce, "Malam, yaushe wannan zai
faru? Kuma me za mu gani don mu san lokaci ya zo da za su
faru?" [8] Sai ya ce musu, "Ku lura fa, kada wani yă ruɗe ku.
Domin mutane da yawa za su zo a cikin sunana, suna cewa, ai,
su ne ni, suna kuma cewa, 'Lokaci ya yi.' Kada fa ku bi su. [9] Kada
ma ku ji tsoro in kun ji labarin yaƙe-yaƙe da tashin hankali. Lallai
ne wannan yă fara zuwa, amma ƙarshen bai zo ba tukuna."

10 Ya ci gaba da cewa, "Al'umma za ta tasar wa al'umma,
mulki yă tasar wa mulki. [11] Za a yi mummunar rawar ƙasa, da
yunwa da annoba a wurare dabam-dabam. Za a ga abubuwa masu
ban tsoro da alamu masu ban mamaki suna fitowa daga sama.
[12] Kafin duk abubuwan nan su faru, za su kama ku, su ba da ku
don a tsananta muku. Za a kai ku gaban majami'u a kuma sa ku
a kurkuku. Za a kuma kai ku gaban sarakuna da shugabanni
saboda sunana. [13] Wannan ne zai ba ku damar ba da Labari Mai
Daɗi a kaina. [14] Saboda haka sai ku shirya a ranku tun da wuri a
kan ba za ku damu da yadda za ku kare kanku ba. [15] Gama zan
ba ku kalmomi da hikima yadda ko ɗaya daga cikin masu gāba
da ku ba zai iya juye maganar ko yă yi mūsun abin da kuka ce
ba. [16] Har iyayenku ma, da 'yan'uwanku, da danginku, da

21.14-15: Luk 12.11-12

abokanku sai sun ba da ku, su kuma sa a kashe wadansunku.
17 Kowa zai ki ku saboda sunana. 18 Amma ba ko daya daga cikin
gashin kanku da zai bata. 19 Idan kuka jimre, za ku tsira.

Yesu Ya Fada yadda Urushalima Za Ta Fādi
(Mat 24.15-28; Mar 13.14-23)

20 "Idan kuka ga sojoji sun kewaye Urushalima, ku san an yi
kusa a rushe ta. 21 To, sai wadanda suke cikin Yahudiya, su gudu
zuwa cikin duwatsu. Wadanda suke birni kuma su fita, wadanda
suke a kauye kuma kada su shiga birnin. 22 Gama kwanakin nan
kwanakin hukunci ne, don dole ne a cika duk abin da Maganar
Allah ta ce. 23 Kaiton mata masu ciki da masu goyo a wannan
lokaci! Gama mummunar wahala za ta shiga kasar, kuma fushin
Allah zai sauko a kan mutanen nan. 24 Za a kashe wadansu a yaki,
a kuma kama wadansu a kai su bauta a wadansu kasashe.
Wadanda ba Yahudawa ba za su tsananta wa Urushalima, har sai
lokacinsu ya cika.

Dawowar Dan Mutum
(Mat 24.29-31; Mar 13.24-27)

25 "Za a kuma ga abubuwa masu ban tsoro a jikin rana, da
wata, da taurari. A duniya kuma al'ummai za su rikice don tsoro
saboda tafasa da haukan teku. 26 Mutane za su yi suma don tsoro,
za su kuma yi fargaba da ganin abubuwan da suke faruwa ga
duniya. Gama za a girgiza manyan abubuwan da suke sararin
sama. 27 Sa'an nan za a ga Dan Mutum yana zuwa a cikin girgije
da iko da daukaka mai yawa. 28 Idan wadannan abubuwa suka
fara faruwa, ku shirya kanku sosai domin cetonku ya yi kusa."

Koyarwa a kan Itacen Baure
(Mat 24.32-35; Mar 13.28-31)

29 Sai Yesu ya ba su wani misali ya ce, "Ku duba itacen baure
da sauran itatuwa mana. 30 Da zarar sun fara fitar da sababbin
ganye, ku da kanku kun san cewa damina ta yi kusa ke nan.
31 Haka ma, idan kuka ga wadannan abubuwa suna faruwa, ku
sani mulkin Allah ya yi kusa.

32 "Gaskiya ina gaya muku mutanen zamanin nan ba za su
mutu ba sai duka abubuwan nan sun faru. 33 Sama da kasa za su
shude, amma maganata ba za ta shude ba ko kadan.

21.22: Hos 9.7 **21.25:** Ish 13.10; Ez 32.7; Jow 3.4; R. Yoh 6.12-13
21.27: Dan 7.13; R. Yoh 1.7

Gargaɗi a kan Zama da Shiri

34 "Ku zauna a shirye fa. Kada ku bar ciye-ciye da
shaye-shaye, da damuwar rayuwar duniya su ɗauki hankalinku.
Idan ba haka ba, Ranan nan za ta zo ba labari ta cafke ku 35 kamar
tarko. Gama za ta zo a kan kowa da yake zama a duniya duka.
36 Ku zauna a shirye fa, kuna addu'a kullum don ku sami ƙarfin
kuɓuce wa dukan waɗannan abubuwan da za su faru, ku kuma
tsaya a gaban Ɗan Mutum."

37 Kowace rana, Yesu yakan yi koyarwa a haikali, amma idan
yamma ta yi sai yă fita yă je Dutsen Itatuwan Zaitun yă kwana
a can. 38 Da sassafe kuma dukan mutane sukan zo wurinsa a
haikali su ji shi.

Shugabanni Sun Yi Shawara Su Kashe Yesu
(Mat 26.1-5; Mar 14.1-2; Yoh 11.45-53)

22 1 To, da lokacin Bikin Burodi Marar Yistin da ake ce da
shi "Bikin Ketarewa" ya yi kusa, 2 sai manyan firistoci da
malaman dokoki suka yi ta neman yadda za su kashe Yesu. Sun
nemi su yi haka a ɓoye don suna tsoron mutane.

Yahuda Ya Yarda Ya Ba da Yesu
(Mat 26.14-16; Mar 14.10-11)

3 Sai Shaiɗan ya shiga cikin zuciyar Yahuda wanda ake ce da
shi Iskariyoti, ɗaya daga cikin almajirai sha biyun nan. 4 Sai ya
je ya yi magana da manyan firistoci da shugabannin dogarawan
haikali a kan yadda zai ba da Yesu gare su. 5 Suka yi murna sosai,
suka shirya a kan za su biya shi kuɗi. 6 Yahuda kuwa ya yarda
da haka, ya fara neman hanyar da zai ba da Yesu gare su ba da
sanin mutane ba.

Yesu Ya Shirya Cin Bikin Ketarewa
(Mat 26.17-25; Mar 14.12-21; Yoh 13.21-30)

7 Da ranar Bikin Burodi Marar Yisti ta kewayo, wato ranar
yankan ragunan Bikin Ketarewa, 8 Yesu ya aiki Bitrus da Yohanna
ya ce musu, "Ku je ku shirya mana abincin Ketarewa mu ci."

9 Suka tambaye shi suka ce, "Ina kake so mu je mu shirya
shi?"

10 Ya ce musu, "Da kun shiga cikin gari, za ku sadu da wani
mutum rike da tulun ruwa. Ku bi shi zuwa gidan da zai shiga.
11 Ku ce wa maigidan, 'Malam ne ya aike mu mu ce maka, "Ina
ɗakin da ni da almajiraina za mu ci abincin Ketarewa?" ' 12 Zai

nuna muku wani babban ɗakin sama a shirye. A nan za ku shirya mana kome."

13 Sai suka tafi, suka kuma sami kome daidai kamar yadda Yesu ya faɗa musu, suka kuma shirya abincin Bikin Ketarewa.

Jibin Ubangiji

(Mat 26.26-30; Mar 14.22-26; 1 Kor 11.23-25)

14 Da lokaci ya yi sai Yesu ya zauna tare da manzanninsa don cin abinci. 15 Sai ya ce musu, "Na yi marmari in ci wannan Bikin Ketarewa tare da ku kafin in sha wahala! 16 Ina dai gaya muku, ba zan ɓara cin bikin nan ba, sai ma'anarsa ta cika a mulkin Allah."

17 Sai ya ɗauki kwaf, ya yi godiya ga Allah, ya ce, "Ku karɓa ku rarraba tsakaninku. 18 Ina gaya muku cewa, daga yanzu ba zan ɓara shan wannan ruwan inabi ba sai mulkin Allah ya zo."

19 Sai ya ɗauki burodi, ya yi godiya ga Allah, ya kakkarya shi, ya kuma ba su, yana cewa, "Wannan jikina ne wanda za a bayar dominku. Ku riƙa yin haka don tunawa da ni." 20 Haka kuma, bayan jibin, ya ɗauki kwaf ɗin, ya ce, "Wannan kwaf na sabon alkawari ne, wanda aka tabbatar da jinina, wanda za a zubar dominku.[j] 21 Amma ga wanda zai bashe ni yana ci tare da ni! 22 Dan Mutum zai mutu kamar yadda aka shirya, amma kaiton mutumin da ya ba da shi!"

23 Sai almajiran suka fara tambayar juna ko wane ne a cikinsu zai yi haka.

Gardama a kan ko Wane Ne Babba

24 Sai gardama ta tashi a cikin almajiran a kan wane ne a cikinsu zai zama babba. 25 Yesu ya ce musu, "Sarakunan mutanen da ba su san Allah ba sukan nuna wa mutanensu iko, kuma shugabanninsu sukan ce da kansu 'masu taimakon mutane.' 26 Amma kada yă zama haka a tsakaninku. A maimakon haka, bari babba a cikinku yă zama kamar ɓarami; shugaba kuma yă zama kamar bawa. 27 Wane ne ya fi girma, shi wanda ya zauna yana ci ne, ko kuma shi da yake kai masu abinci? Ai, wanda ya zauna yana ci ne. Amma ga shi ina a cikinku kamar mai kai abinci ne.

22.24: Mat 18.1; Mar 9.34; Luk 9.46 **22.25-26:** Mat 20.25-27; 10.42-44
22.26: Mat 23.11; Mar 9.35 **22.27:** Yoh 13.12-15

[j] **22.20** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da sashi na aya ta goma sha tara da kuma aya ta ashirin gaba ɗaya.

28 "Ku ne kuka tsaya da aminci tare da ni a duk gwaje-gwajen
da na sha. 29 Kamar dai yadda Ubana ya ba ni iko in yi mulki,
haka nake ba ku. 30 Za ku ci, ku sha, a teburina, a can cikin
mulkina. Kuma za ku zauna a kujerun mulki, ku yi sarautar kabilu
goma sha biyu na Isra'ila.

Bitrus Zai Yi Mūsun Sanin Yesu
(Mat 26.31-35; Mar 14.27-31; Yoh 13.36-38)

31 "Bitrus, Bitrus! Ka ji nan! Shaiɗan ya nemi izni yă gwada
ku duka, yă tankaɗe ku kamar yadda ake tankaɗe alkama daga
dusa. 32 Amma na yi maka addu'a, Bitrus, kada bangaskiyarka ta
kāsa. Bayan ka juyo wurina, ka ƙarfafa 'yan'uwanka."

33 Bitrus ya amsa, ya ce, "Ubangiji, ina a shirye in je har ma
kurkuku tare da kai. In ma mutuwa ce, mu mutu tare!"

34 Yesu ya ce, "Ina gaya maka, Bitrus, kafin zakara yă yi cara
a daren yau, za ka ce ba ka san ni ba sau uku!"

Ku Shirya Kanku don Lokacin Wahala

35 Sai Yesu ya tambayi almajiransa ya ce, "A lokacin da na
aike ku ba kudî, ba abinci, ba takalma, kun rasa wani abu ne?"

Suka ce, "A'a!"

36 Ya ce musu, "Amma yanzu, duk wanda yake da kudî, ko
abinci, yă ɗauka yă riƙe, kuma duk wanda ba shi da takobi, yă
sayar da rigarsa yă saya ɗaya. 37 Gama ina gaya muku, cewa
wannan Maganar Allah da ta ce, 'An haɗa shi cikin masu zunubi,'
dole ne ta cika a kaina. Gama abin da aka rubuta a kaina yana
kan cikawa."

38 Almajiran suka ce masa, "Mai girma, ga takobi guda biyu
a nan." Yesu ya ce, "Ya isa."

Yesu Ya Yi Addu'a a Dutsen Itatuwan Zaitun
(Mat 26.36-46; Mar 14.32-42)

39 Yesu ya bar birnin, ya hau Dutsen Itatuwan Zaitun kamar
yadda ya saba, sai almajiransa suka bi shi. 40 Da ya kai wurin, sai
ya ce musu, "Ku yi addu'a fa, don kada ku fāɗi cikin jaraba."

41 Sai ya ci gaba ya yi ɗan nisa da su, misalin nisan jifa, sai
ya durƙusa ya yi addu'a. 42 Ya ce, "Uba, in ka yarda ka ɗauke
mini wannan kwaf na wahala. Amma ba nufina ba, sai dai nufinka
za a bi."

22.30: Mat 19.28 **22.35:** Mat 10.9-10; Mar 6.8-9; Luk 9.3; 10.4 **22.37:** Ish 53.12

43 Sai ga mala'ika daga sama ya bayyana gare shi yana ƙarfafa
shi. 44 Domin yana cikin wahala sosai, sai ya ƙara nacewa cikin
addu'ar, har zufa tana sauka masa kamar jini.[k]
45 Da Yesu ya tashi daga addu'a, sai ya koma wurin da
almajiran suke, ya same su suna barci saboda baƙin ciki. 46 Ya
ce musu, "Don me kuke barci? Ku tashi, ku yi addu'a don kada
ku fāɗi cikin jaraba."

An Kama Yesu
(Mat 26.47-56; Mar 14.43-50; Yoh 18.2-11)

47 Bai ma rufe baki ba, sai ga taron mutane suka zo. Yahuda,
ɗaya daga cikin sha biyun ne, ya kawo su. Sai ya gusa kusa da
Yesu don yă rungume shi. 48 Amma Yesu ya ce, "Yahuda, ashe,
da runguma ne za ka ba da Ɗan Mutum?"
49 Da almajiran da suke tare da Yesu suka ga haka, suka
tambaye shi, suka ce, "Mai girma, mu yi amfani da takobin ne?"
50 Sai ɗayansu ya sari bawan babban firist, ya yanke kunnensa na
dama.
51 Amma Yesu ya ce musu, "Ku bari." Sai ya taɓa kunnen
mutumin da aka sara, ya warkar da shi.
52 Sai Yesu ya ce wa manyan firistoci da shugabannin
dogarawan haikali da shugabannin jama'a, waɗanda suka zo don
su kama shi, "Kun fito da takuba, da sanduna ku kama ni sai ka
ce ɗan fashi? 53 Kullum ina tare da ku a haikali, ba ku kama ni
ba. Amma wannan ne lokacinku da na ikon duhu."

Bitrus Ya Yi Mūsun Sanin Yesu
(Mat 26.57-58, 69-75; Mar 14.53-54, 66-72; Yoh 18.12-18, 25-27)

54 Suka kama Yesu suka tafi da shi, suka kai shi gidan babban
firist. Bitrus ya riƙa binsu daga nesa-nesa. 55 Da suka hura wuta
a filin gidan suka zazzauna, Bitrus ma ya zauna a cikinsu. 56 Da
ɗaya daga cikin 'yan matan da suke aiki a gidan ta gan shi zaune
kusa da wutar, ta kafa masa ido ta ce, "Ai, wannan mutumin ma
yana tare da Yesu!"
57 Amma Bitrus ya yi mūsu ya ce, "Ke! Ni ban san shi ba!"
58 Bayan ɗan lokaci kaɗan, wani mutum ya gane Bitrus, ya
ce, "Lallai, kai ma ɗayansu ne!"
Amma Bitrus ya amsa ya ce, "Kai! Ba ni ba ne!"

22.53: Luk 19.47; 21.37
[k] 22.44 Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da ayoyi 43-44.

59 Bayan kamar awa ɗaya sai wani mutum ya ce, "Ba shakka
mutumin nan ma yana tare da shi, don shi mutumin Galili ne."
60 Amma Bitrus ya ce, "Kash! Ban ma san abin da kake faɗa
ba!" Tun bai rufe baki ba, sai zakara ya yi cara. 61 Ubangiji kuma
ya juye ya dubi Bitrus. Sa'an nan Bitrus ya tuna yadda Ubangiji ya
ce masa, "Kafin zakara yă yi cara a daren yau, za ka ce ba ka san
ni ba sau uku." 62 Sai ya fita waje, ya yi kuka mai zafi.

An Yi wa Yesu Ba'a, An kuma Dūke Shi
(Mat 26.67-68; Mar 14.65)

63 Sai waɗanda suke gadin Yesu suka yi masa ba'a suka kuma
yi masa dūka. 64 Suka ɗaure masa idanu suna tambayarsa, "Ka yi
annabci, wa ya mare ka!" 65 Suka kuma yi ta yi masa waɗansu
maganganu, suna zaginsa.

An Kawo Yesu a Gaban 'Yan Majalisa
(Mat 26.59-66; Mar 14.55-64; Yoh 18.19-24)

66 Da gari ya waye, sai shugabannin jama'a da manyan
firistoci da malaman dokoki suka taru, suka kai Yesu gaban
majalisa. 67 Suka ce, "Ka faɗa mana, kai ne Almasihu?"
Sai ya amsa ya ce, "Ko na gaya muku ba za ku gaskata ba,
68 idan kuma na yi muku tambaya ba za ku ba ni amsa ba. 69 Amma
daga yanzu, Ɗan Mutum zai zauna a dama na Allah Mai Iko."
70 Sai dukansu suka ce, "Ashe, kai ɗin nan Ɗan Allah ne?"
Ya amsa ya ce, "Kun faɗa, Ni ne."
71 Sai suka ce, "Wace shaida ce kuma muke nema? Ai, mu
da kanmu mun ji abin da ya ce da bakinsa!"

An Kai Yesu Gaban Bilatus
(Mat 27.1-2, 11-14; Mar 15.1-5; Yoh 18.28-38)

23 1 Sai dukan taron majalisa suka tashi suka kai Yesu gaban
Bilatus. 2 Sai suka fara zarginsa suna cewa, "Mun sami
wannan yana rikitar da mutanenmu, yana ce musu wai kada su biya
wa Kaisar haraji. Yana kuma cewa wai shi ne Almasihu, sarki."
3 Sai Bilatus ya tambaye shi ya ce, "Kai ne sarkin
Yahudawa?"
Yesu ya ce, "Kai ne ka faɗa haka."
4 Sai Bilatus ya ce wa manyan firistoci da jama'a, "Ni kam,
ban sami mutumin nan da wani laifi ba."
5 Sai suka fara matsa masa lamba suna cewa, "Da koyarwarsa
ne yake ta da hankalin mutane a dukan Yahudiya. Ya fara tun
daga Galili, yanzu kuma har nan wurin."

An Kai Yesu Wurin Hirudus

6 Da Bilatus ya ji haka, sai ya yi tambaya, ya ce, "Shi mutumin
Galili ne?" 7 Da ya ji cewa Yesu ya fito daga sashin da Hirudus
yake mulki ne, sai ya aika da Yesu zuwa wurin Hirudus, gama a
lokacin Hirudus ma yana Urushalima. 8 Hirudus ya yi murna sosai
da ganin Yesu, gama tun dā ma yana marmari yă gan shi, don
ya riga ya ji labarinsa yana kuma fata yă ga wani abin mamakin
da Yesu zai yi. 9 Sai Hirudus ya yi masa tambayoyi masu yawa,
amma Yesu bai ce kome ba. 10 Sai manyan firistoci da malaman
dokoki suka zo gaba suka kawo zargi masu ƙarfi a kan Yesu.
11 Hirudus da sojojinsa suka yi masa renin wayo, suka yi masa
ba'a, sa'an nan suka sa masa babbar riga, suka mai da shi wurin
Bilatus. 12 A ranan nan ne Hirudus da Bilatus suka zama abokan
juna, don tun dā ba sa so su ga juna.

An Yanke wa Yesu Hukuncin Mutuwa

(Mat 27.15-26; Mar 15.6-15; Yoh 18.39-19.16)

13 Bilatus ya tara manyan firistoci, da shugabannin jama'a
da mutane duka, 14 ya ce musu, "Kun kawo mini wannan
mutum, wai yana rikitar da mutane. Yanzu, na bincike shi a
gabanku, ban same shi da wani laifi da kuka kawo a kansa ba.
15 Haka ma Hirudus. Shi ya sa ya dawo da shi nan wurinmu.
Ba abin da mutumin nan ya yi da ya isa a kashe shi. 16 Saboda
haka zan yi masa bulala in sake shi."[ƙ]

18 Amma duk suka yi ihu gaba ɗaya, suka ce, "A yi gaba da
shi, a saki mana Barabbas!" 19 Dā an sa shi Barabbas a kurkuku
saboda laifin tashin hankalin da ya jawo a garin, har aka kashe
mutum.

20 Sai Bilatus ya sāke yi musu magana, don yana so yă saki
Yesu. 21 Amma sai ihu suke ta yi, suna cewa, "A gicciye shi! A
gicciye shi!"

22 Bilatus ya sāke ce musu sau na uku, "Don me? Wane laifi
ne mutumin nan ya yi? Ni dai ban same shi da wani laifin da ya
isa a kashe shi ba. Zan sa a yi masa bulala, a sake shi."

23 Amma suka tsaya dam! Suna matsa masa lamba, cewa sai
an kashe shi. A ƙarshe dai suka ci nasara. 24 Bilatus kuwa ya
yanke shari'ar da suke so. 25 Ya saki mutumin da suka ce a sake
wato, wannan da aka jefa a kurkuku a kan laifin ta da hankali da

[ƙ] **23.17** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya ta 17 haka: "A kowane Bikin Ketarewa Bilatus yakan saki mutum ɗaya daga kurkuku, wanda mutane suka roƙa."

kuma kashe mutumin da ya yi. Amma Bilatus ya ba da Yesu gare su su yi masa abin da suke so.

An Gicciye Yesu
(Mat 27.32-44; Mar 15.21-32; Yoh 19.17-27)

26 Da sojoji suna tafiya da Yesu, sai suka sadu da wani da ake ce da shi Siman, mutumin Sayirin, yana zuwa daga ƙauye. Suka cafke shi, suka sa masa gicciye yă ɗauka yă bi Yesu a baya.

27 Mutane da yawa sosai suka yi ta binsa, a cikinsu kuwa har da waɗansu matan da suke kuka, suna ihu dominsa. 28 Amma Yesu ya juya wurinsu, ya ce, "Matan Urushalima! Kada ku yi kuka saboda ni, ku yi kuka wa kanku da 'ya'yanku. 29 Gama lokaci yana zuwa da mutane za su ce, 'Abin farin ciki ne ga matan da ba su taɓa haihuwa ba, waɗanda ba sa haihuwa, waɗanda kuma ba su goyi yara ba.' 30 A wannan lokaci ne, mutane za su ce wa duwatsu, 'Ku fāɗo a kanmu!' Za su kuma ce wa tuddai, 'Ku rufe mu.' 31 Idan fa suna yin irin waɗannan ga ɗanyen itace, yaya ke nan zai zama in ya bushe?"

32 Aka kuma kai waɗansu mutum biyu masu laifi don a kashe su tare da Yesu. 33 Da suka kai wurin da ake ce da shi "Kokon Kai", suka gicciye shi a nan, tare da masu laifin nan, ɗaya a damarsa, ɗaya kuma a hagunsa.

Hoton gicciye (23.33)

23.30: Hos 10.8; R. Yoh 6.16 **23.30**: Hos 10.8

34 Sai Yesu ya ce, "Uba, ka yafe musu, gama ba su san abin
da suke yi ba."[l]
Suka rarraba wa juna rigunansa, ta wurin jefa kuri'a. 35 Mutane
suka tsaya suna kallo. Shugabannin kuma suka yi masa ba'a, suna
cewa, "Ya ceci wadansu, to, yă ceci kansa mana, in shi ne
Almasihun da Allah ya zaba!"
36 Sojojin ma suka yi masa ba'a ta wurin zuwa wurinsa suna
mika masa ruwan tsami. 37 Suna cewa, "In kai ne Sarkin
Yahudawa, to, ceci kanka mana!"
38 Sama da shi kuma aka yi wani rubutu cewa, "Wannan shi
ne Sarkin Yahudawa."
39 Daya daga cikin masu laifin da aka gicciye ya yi masa
bakar magana, ya ce, "Shin, in ce kai dîn nan ne Almasihu? To,
ka ceci kanka, ka kuma cece mu mana!"
40 Amma dayan ya tsawata wa wancan ya ce, "Ba ka ma
tsoron Allah? Kai da ka sami hukunci daidai da shi? 41 Mu kam,
daidai aka yi mana, domin muna samun ladan abin da muka yi
ne. Amma shi fa, wane laifi ya yi?" 42 Ya kuma ce, "Ya Yesu,
ka tuna da ni cikin mulkinka!"
43 Yesu ya ce masa, "Ina gaya maka, yau dîn nan za ka zauna
tare da ni a sama."

Mutuwar Yesu
(Mat 27.45-56; Mar 15.33-41; Yoh 19.28-30)

44 Wajen tsakar rana, duhu ya rufe dukan kasar, har zuwa
karfe uku na yamma. 45 Rana ta daina haske; labulen[m] da yake
cikin haikali kuma ya yage kashi biyu. 46 Sai Yesu ya daga murya
da karfi ya ce, "Uba! A cikin hannayenka nake ba da raina." Da
ya faɗa haka, sai ya mutu. 47 Da sojan da yake wurin a lokacin
ya ga abin da ya faru, sai ya yabi Allah yana cewa, "Lallai,
wannan mutum marar laifi ne!"
48 Da mutanen da suka taru a nan don shan kallo suka ga abin
da ya faru, sai dukansu suka koma gida suna bugun kirjinsu cikin
bakin ciki. 49 Duk mutanen da suka san Yesu, da kuma matan da
suka biyo shi tun daga kasar Galili, suka tsaya da nisa suna kallo.

23.34: Zab 22.19 **23.35**: Zab 22.8 **23.36**: Zab 69.22 **23.45**: Fit 26.31-33
23.46: Zab 31.6 **23.49**: Luk 8.2-3

[l] **23.34** Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da "Yesu ya ce, 'Uba, ka yafe musu, gama ba su san abin da suke yi ba.' " (Dubi Zab 22.18).

[m] **23.45 labulen**: Wato yadin da aka rufe kofar Wuri Mafi Tsarki a cikin haikali.

Hoton babban sojan Roma (23.47)

Jana'izar Yesu
(Mat 27.57-61; Mar 15.42-47; Yoh 19.38-42)

50-51 Akwai wani mutum mai suna Yusufu, wanda shi daga wani gari ne da ake ce da shi Arimatiya, a cikin Yahudiya. Shi wani mutumin kirki ne, mai adalci kuma. Yana marmarin mulkin Allah yă zo. Shi kuma ɗaya ne daga cikin 'yan majalisa na Yahudawa, amma bai yarda da su a kan abin da suka shirya suka kuma yi ba.

52 Sai ya je wurin Bilatus don yă roƙa a ba shi jikin Yesu.
53 Sai ya sauko da jikin, ya nannaɗe shi a cikin yadin lilin, ya sa shi a wani kabarin da aka haƙa a jikin dutse, wanda ba a taɓa sa kowa a ciki ba. 54 Ranar Shiri[n] ce kuwa, ya rage kaɗan a shiga Ranar Hutun Yahudawa.

55 Matan da suka bi Yesu daga Galili suka tafi tare da Yusufu don su ga inda kabarin yake da kuma yadda aka sa jikin Yesu.
56 Sa'an nan suka koma gida, suka shirya turare da man shafawa. Ranar Hutu kuwa, suka huta kamar yadda Doka ta umarta.

23.56: Fit 20.10; M. Sh 5.14
[n]**23.54 Ranar Shiri:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

Tashin Yesu daga Matattu
(Mat 28.1-10; Mar 16.1-8; Yoh 20.1-10)

24 [1] Da sassafe Ranar Farko ta mako, matan suka je kabarin
da kayan ƙamshin da suka shirya. [2] Sai suka sami an riga
an ture dutsen daga bakin kabarin. [3] Suka shiga ciki, amma ba su
ga jikin Ubangiji Yesu ba. [4] Tun suna cikin damuwa a kan wannan
abin, sai ga waɗansu mutum biyu tsaye kusa da su, sun sa fararen
riguna masu haske sosai. [5] Cike da tsoro, matan suka sunkuyar
da kansu ƙasa. Mutanen suka ce musu, "Don me kuke neman mai
rai cikin waɗanda suka mutu? [6] Ba ya nan, ya tashi." Ku tuna da
abin da ya gaya muku tun yana Galili. [7] Ya ce, "Lallai ne a ba
da Dan Mutum a hannun mutane masu zunubi, a gicciye shi, a
rana ta uku kuma yă tashi."

8 Sai matan suka tuna da maganarsa. [9] Da suka dawo daga
kabarin, sai suka faɗa wa sha ɗayan nan da sauran mutane
dukan waɗannan abubuwa. [10] Matan da suka gaya wa
manzannin waɗannan abubuwa kuwa su ne, Maryamu daga
Magadala, da Yowana, da Maryamu mamar Yakubu, da
waɗansu matan da suke tare da su. [11] Amma manzannin suka
ɗauki maganar matan nan wani zancen banza ne kawai, don
haka ba su gaskata ba.

12 Amma Bitrus ya tashi wuf! Ya je wurin kabarin da gudu.
Ya sunkuya, ya leƙa ciki, ya ga yadin lilin a ajiye a gefe ɗaya.
Sai ya koma gida yana mamakin abin da ya faru.[o]

A Hanyar Imawus
(Mar 16.12-13)

13 A wannan ranar kuma biyu daga cikin masu bin Yesu suna
tafiya za su je wani ƙauyen da ake ce da shi Imawus, wanda
nisansa daga Urushalima ya kai misali kilomita goma sha ɗaya.

14 Suna tafi da juna a kan dukan abubuwan da suka faru.
[15] Suna cikin tafi suna tattauna ke nan, sai Yesu da kansa ya ja
kusa yana tafiya da su. [16] Amma an rufe musu idanunsu, har ba
su gane shi ba. [17] Sai ya ce musu, "Wane tafi kuke yi haka da
juna, kuna tafiya?"

Sai suka tsaya cik, suna baƙin ciki. [18] Daya daga cikinsu, mai
suna Kiliyobas, ya amsa masa ya ce, "Ashe, kai ne kawai baƙo

24.6-7: Mat 16.21; 17.22-23; 20.18-19;
Mar 8.31; 9.31; 10.33-34; Luk 9.22; 18.31-33
[o] 24.12 Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da aya ta 12.

a Urushalima da ba ka san abubuwan da suka faru a can kwana-kwanan nan ba?"

19 Sai ya ce musu, "Waɗanne abubuwa?"

Suka ce masa, "Abubuwan da suka faru da Yesu Banazare. Shi kuwa annabi ne mai iko cikin ayyuka da magana a gaban Allah da dukan mutane, 20 wanda kuma manyan firistoci da shugabanninmu suka ba da shi a yi masa hukuncin mutuwa, suka kuwa gicciye shi. 21 Dā muna tsammani shi ne zai fanshi Isra'ila! Ga shi, yau kwana uku ke nan tun da wannan abin ya faru. 22 Ban da haka ma waɗansu mata a cikinmu sun ba mu mamaki. Gama sun je kabarin da sassafe, 23 da ba su sami jikinsa ba, sai suka dawo, suka ce, an yi musu ru'uya, sun ga mala'iku waɗanda suka ce yana da rai. 24 Waɗansu a cikinmu ma suka je kabarin suka kuma sami abin nan kamar dai yadda matan suka faɗa, amma shi ɗin ba su gan shi ba."

25 Sai Yesu ya ce musu, "Haba, ku marasa tunani, ba ku da saurin gaskatawa game da abin da annabawa suka faɗa! 26 Ashe, ba dole ne Almasihu yă sha waɗannan wahaloli ba, yă kuma shiga ɗaukakarsa?" 27 Sai ya bayyana musu duk abin da Rubutattun Maganar Allah sun faɗa a kansa, daga Dokar Musa har zuwa littattafan annabawa duka.

28 Da suka yi kusa da ƙauyen da za su, sai Yesu ya yi kamar zai wuce, 29 amma suka matsa masa suka ce, "Zauna da mu, ai, yamma ta yi, ga rana duk ta fāɗi." Sai ya bi su ya sauka a wurinsu. 30 Da suka zauna za su ci abinci, sai ya ɗauki burodi ya yi godiya, ya kakkarya ya ba su. 31 Nan da nan sai idanunsu suka buɗe, suka kuma gane shi. Amma sai ya ɓace musu. 32 Suka ce wa juna, "Ashe, zuciyarmu ba ta ƙuna ba lokacin da yake magana da mu a hanya, yana bayyana mana Maganar Allah?"

33 Suka tashi nan da nan suka koma Urushalima. Suka sami sha ɗayan nan, suna nan tare da waɗansu mutane, 34 suna cewa, "Ai, Ubangiji ya tashi da gaske! Har ma ya bayyana ga Bitrus!" 35 Sa'an nan su kuma biyun suka ba da labarin abin da ya faru a hanya, da kuma yadda suka gane shi sa'ad da yake kakkarya burodi.

Aikin da Yesu Ya Ba wa Almajiransa

(Mat 28.16-20; Mar 16.14-18; Yoh 20.19-23; A. M. 1.6-8)

36 Tun suna magana game da wannan, sai kawai ga Yesu da kansa tsaye a tsakiyarsu, ya ce musu, "Salama a gare ku!" [r]

[r] **24.36 ya ce musu, "Salama a gare ku.":** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da waɗannan kalmomin.

37 Tsoro ya kama su suna rawar jiki, suna tsammani fatalwa
ce suke gani. 38 Sai ya ce musu, "Don me kuka ji tsoro haka,
kuke kuma shakka a zuciyarku? 39 Ku duba hannayena da
ƙafafuna ku gani, ai, ni ne da kaina. Ku taɓa ni, ku ji, don fatalwa
ba ta da nama da ƙashi, yadda kuke gani nake da su."
40 Da ya faɗa haka, sai ya nuna musu hannayensa da
ƙafafunsa.[s] 41 Tun suna da sauran shakka saboda yawan farin ciki
da mamaki, sai ya ce musu, "Kuna da abinci a nan kuwa?" 42 Suka
ba shi tsokar gasasshen kifi. 43 Ya karɓa ya ci, su kuma suna
kallonsa.
44 Sai ya ce musu, "Waɗannan su ne abubuwan da na yi
magana a kai tun ina tare da ku, cewa dole ne a cika duk abin
da aka rubuta a kaina a cikin Dokar Musa, da littattafan annabawa,
da kuma Zabura."
45 Sai ya wayar da hankalinsu suka gane da Rubutattun
Maganar Allah, 46 ya kuma ce musu, "Haka aka rubuta, cewa dole
ne Almasihu yă sha wuya, a rana ta uku kuma yă tashi daga
matattu. 47 Kuma a sunansa za a yi wa dukan al'umman duniya
wa'azin tuba da yafewar zunubai. Za a kuwa fara daga
Urushalima. 48 Ku ne shaidun waɗannan abubuwa. 49 Ga shi, ni
zan aiko muku da abin da Ubana ya yi alkawari. Amma ku jira
a birni tukuna, sai an ba ku iko daga sama."

An Ɗauke Yesu zuwa Sama
(Mar 16.19-20; A. M. 1.9-11)

50 Sai ya fitar da su zuwa bayan birni, suka kai har Betani. A
wurin ya ɗaga hannayensa ya sa musu albarka. 51 Yana cikin sa
musu albarka ke nan, sai ya rabu da su, aka kuma ɗauke shi zuwa
sama.[t] 52 Su kuwa suka yi masa sujada, suka koma Urushalima,
cike da farin ciki sosai. 53 Ko yaushe kuma suna cikin haikali suna
yabon Allah.

24.49: A. M. 1.4 **24.50-51:** A. M. 1.9-11

[s] **24.40** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da aya ta 40.

[t] **24.51 aka ɗauke shi zuwa sama:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da waɗannan kalmomin.

BISHARA TA HANNUN

YOHANNA

Gabatarwa

Marubucin wannan Bisharar bai ambaci sunansa a cikin littafin ba. Amma ana da tabbaci sosai cewa manzo Yohanna, "Wanda Yesu yake ƙauna" ne ya yi wannan rubutun (Dubi 13.23, 19.26, 20.2, 21.7,20). Ana zato an rubuta Bisharan nan bayan shekara ta A.D. 85.

Dalilin da aka rubuta wannan bisharar shi ne don a nuna yadda Kalman Allah ya zama mutum. Ya zama haka ne, domin ku ba da gaskiya cewa Yesu wato Kalman Allah, shi ne Almasihu, Ɗan Allah. Sa'an nan kuma, ta wurin ba da gaskiya za ku sami rai a cikin sunansa (20.31).

Bishara ta Hannun Yohanna ce ta nanata cewa Yesu shi ne Almasihun. A cikin dukan al'ajabai da abubuwan ban mamaki iri-iri da Yesu ya yi, wannan bisharar ta maimaita kaɗan ne kawai. Waɗannan kuwa su ne akan ce da su "alamu", domin manufarsu ita ce su bayyana Yesu. Waɗansu kalmomin da *Bishara ta Hannun Yohanna* ta mora sosai domin a bayyana Yesu su ne, "ba da gaskiya", "haske", "rai", "ƙofa", "hanya", "itacen inabi", "makiyayi", "abinci".

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-18
Yesu ya fara ayyukansa 1.19-51
Koyarwa da ayyukan da Yesu ya yi a fili 2.1—12.50
Shirin Yesu saboda mutuwarsa 13.1—17.26
Mutuwar Yesu 18.1—19.42
Tashin Yesu daga matattu 20.1—21.25

Kalman Ya Zama Mutum

1 [1] Tun farko akwai Kalma, Kalman kuwa tare da Allah yake, Kalman kuwa Allah ne. [2] Shi ne tun farko yake tare da Allah. [3] Ta wurinsa ne aka yi dukan abubuwa, kuma babu wani abu a cikin dukan halittar da aka yi da ba tare da shi ba. [4] Kalman ne tushen rai, wannan rai kuwa shi ne haske ga mutane. [5] Hasken yana haskakawa cikin duhu, amma duhu bai iya yă sha kansa ba.

6 Akwai wani mutum mai suna Yohanna wanda Allah ne ya aiko shi. [7] Ya zo yă shaida wa mutane gaskiya game da hasken,

---

1.6: Mat 3.1; Mar 1.4; Luk 3.1-2

don ta wurinsa dukan mutane su ji labarin hasken su kuma ba da gaskiya. 8 Ba Yohanna ne hasken ba, amma ya zo ne don yă yi shaida game da hasken. 9 Haske na gaskiya wanda yake ba da haske ga dukan mutane yana zuwa cikin duniya.

10 A dā Kalman yana cikin duniya, kuma ko da yake ta wurinsa ne aka yi duniya, duk da haka duniya ba ta san shi ba. 11 Ya zo ƙasarsa, amma mutanensa ba su karɓe shi ba. 12 Amma dukan waɗanda suka karɓe shi, suka kuma ba da gaskiya gare shi, ya ba su iko su zama 'ya'yan Allah. 13 Ba su zama 'ya'yansa ta hanyar irin ta 'yan Adam ba, ba ta wurin kwaɗayin jiki ko kuma nufin mutum ba, amma Allah ne da kansa Ubansu.

14 Kalman nan ya zama mutum, ya kuwa zauna a cikinmu. Mun ga ɗaukakarsa, ɗaukakar da take ta Makaɗaicin Ɗa daga wurin Uba, yana kuma cike da alheri da gaskiya.

15 Yohanna ya yi shaida a kansa, ya kuma ɗaga murya ya ce, "Wannan shi ne mutumin da nake magana a kansa a lokacin da na ce, 'Wanda zai zo bayana ya fi ni, don yana rayuwa kafin a haife ni.' " 16 Saboda yawan alherinsa ne ya albarkacemu duka, yana kuma ba mu albarku babu fasawa. 17 Allah ya ba da Doka ta hannun Musa, amma ya ba da alheri da gaskiya ta hannun Yesu Almasihu. 18 Ba mutumin da ya taɓa ganin Allah. Makaɗaicin Ɗansa wanda yake daidai da Allah, yake kuma tare da Uba, shi ya bayyana mana yadda Allah yake.

Yohanna Ya Yi Shaida a kan Yesu

(Mat 3.1-12; Mar 1.1-8; Luk 3.1-18)

19 Ga shaidar da Yohanna ya bayar a lokacin da Yahudawa na Urushalima suka aiki firistoci da Lawiyawa su tambaye shi, "Wane ne kai?"

20 Yohanna bai yi mūsu ba, amma ya faɗa a fili cewa, "Ba ni ne Almasihu ba".

21 Sai suka tambaye shi suka ce, "To, wane ne kai? Kai ne Iliya?"

Sai ya amsa musu ya ce, "A'a, ba ni ne shi ba"

"Kai ne Annabin[a] nan?" Ya sāke amsa ya ce, "A'a."

22 Sai suka ce masa, "To, wane ne kai? Ka ba mu amsar da za mu mayar wa waɗanda suka aiko mu. Me kake ce da kanka?"

1.21: M. Sh 18.15,18; Mal 3.23

[a] **1.21 Annabin:** Wato, wanda Yahudawa suna sa zuciya zai bayyana yă sanar musu da mai ceto.

23 Yohanna ya amsa musu da annabcin Ishaya ya ce, "Ni ne
murya ta wanda yake kira a daji cewa, 'Ku gyara hanya domin
Ubangiji.' "

24 Sai wadansu Farisiyawa[b] wadanda aka aiko[6] 25 suka
tambayi Yohanna suka ce, "Idan ba kai ne Almasihu ba, ba kai
ne Iliya ba, ba kai ne kuma Annabin nan ba, to, don me kake yin
baftisma?"

26 Sai Yohanna ya amsa musu ya ce, "Ni kam, da ruwa nake
baftisma, amma akwai wani a cikinku, wanda ba ku san shi ba.
27 Shi ne mai zuwa a bayana, wanda ni ban isa in kunce igiyar
takalminsa ba."

28 Dukan wannan ya faru ne a Betani, a hayin Kogin Urdun,
inda Yohanna yake yi wa mutane baftisma.

Yesu Shi Ne Dan Rago na Allah

29 Washegari Yohanna ya ga Yesu yana zuwa wurinsa. Sai
Yohanna ya ce, "Ku ga Dan Rago na Allah wanda yake dauke
da zunubin duniya! 30 Wannan shi ne wanda na ce, 'Wani mutum
yana zuwa bayana wanda ya fi ni, domin yana rayuwa kafin a
haife ni.' 31 A dā ni ma ban san shi ba, amma na zo ina baftisma
da ruwa ne don a bayyana shi ga mutanen Isra'ila."

32 Sai Yohanna ya ba da wannan shaida cewa, "Na ga Ruhu
yana saukowa da kamannin kurciya daga sama, ya kuma zauna
a kansa. 33 A dā ni ma ban san shi ba, sai dai Allah wanda ya
aiko ni in yi baftisma da ruwa, shi ne ya ce mini, 'Mutumin da
ka ga Ruhu yana sauko masa ya kuma zauna a kansa, to, shi ne
mai yin baftisma da Ruhu Mai Tsarki.' 34 Na kuwa ga haka ya
faru, na kuma shaida cewa, wannan mutum Dan Allah ne."

Almajiran Yesu na Farko

(Mat 4.18-22; Mar 1.16-20; Luk 5.2-11)

35 Washegari kuma Yohanna yana tsaye a wurin tare da
mutum biyu daga cikin almajiransa. 36 Sai Yohanna ya ga Yesu
yana wucewa, sai ya ce, "Ku ga Dan Rago na Allah!"

37 Da almajiran nan biyu suka ji maganar Yohanna, sai suka
bi Yesu. 38 Da Yesu ya juya ya dubi bayansa, sai ya ga suna binsa,
sai ya tambaye su ya ce, "Me kuke nema?"

1.23: Ish 40.3

[b] **1.24 Farisiyawa:** Dubi ma'anar wadansu kalmomi.

[6] **1.24 Sai wadansu Farisiyawa wadanda aka aiko:** Wani juyi na wadannan kalmomi shi ne "'Yan aika wadanda Farisiyawa suka aika".

Suka ce masa, "Rabbi" wato, Malam ke nan, "Ina kake da zama?"

39 Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Ku zo ku gani."

Wajen ƙarfe huɗu ke nan na yamma, sai almajiran nan suka je suka ga inda yake da zama, suka kuwa zauna a wurin tare da shi a ranar.

40 Andarawus, ɗan'uwan Siman Bitrus, yana ɗaya daga cikin mutane biyun nan da suka bi Yesu bayan da suka ji maganar Yohanna a kan Yesu. 41 Sai Andarawus ya fara nemi ɗan'uwansa Siman, ya ce masa, "Ai, mun sami Almasihun"[c] wato, Kiristi. 42 Sai ya kai Siman a wurin Yesu.

Yesu ya dube shi, ya ce, "Kai ne Siman ɗan Yohanna? Za a ce da kai Kefas." Ko kuma Bitrus mai ma'ana "dutse".

Yesu Ya Kira Filibus da Nataniyel

43 Washegari kuma Yesu ya yi niyyar zuwa Galili. Sai ya sami Filibus, ya ce masa, "Ka bi ni."

44 Filibus mutumin Betsaida ne, garin su Andarawus da Bitrus. 45 Filibus ya sami Nataniyel, ya ce masa, "Mun sami mutumin da aka rubuta labarinsa a Dokar Musa da littattafan annabawa wato, Yesu Banazare, ɗan Yusufu."

46 Sai Nataniyel ya yi tambaya ya ce, "Wani abin kirki zai iya fito daga Nazarat kuwa?"

Filibus ya ce masa, "Ka zo ka gani."

47 Yesu ya ga Nataniyel yana zuwa wurinsa, sai ya ce, "Ku ga mutumin Isra'ila na gaske, wanda ba shi da ƙarya a cikinsa."

48 Sai Nataniyel ya tambayi Yesu ya ce, "Ta yaya ka san ni?"

Yesu ya amsa masa ya ce, "Na gan ka tun kana gindin itacen ɓaure, kafin ma Filibus yă kira ka."

49 Sai Nataniyel ya ce wa Yesu, "Malam, kai ne Ɗan Allah; kai ne sarkin Isra'ila."

50 Yesu ya ce wa Nataniyel, "Ka ba da gaskiya ne domin na gaya maka cewa na gan ka a gindin itacen ɓaure? Ai, za ka ga abubuwan da sun fi wannan." 51 Sai Yesu ya ƙara faɗa musu cewa, "Gaskiya ina gaya muku, za ku ga sama ya buɗe, mala'ikun Allah kuma suna hawa suna sauka a kan Ɗan Mutum."

1.51: Far 28.12

[c] **1.41 Almasihun:** Da Ibraniyanci "Masiha" da Helenanci "Kiristi". Ma'anar Almasihu ita ce wanda aka shafe, aka kuma keɓe.

Bikin Aure a Kana ta Galili

2 [1] A rana ta uku sai aka yi bikin aure a Kana ta Galili. Mamar
Yesu kuwa tana wurin auren. [2] An gayyaci Yesu da
almajiransa ma a auren. [3] Da ruwan inabi ya ƙare, sai mamar Yesu
ta ce masa, "Ruwan inabinsu ya ƙare."

4 Yesu ya amsa mata ya ce, "Mama, me ya sa kika zo wurina?
Ai, lokacina bai yi ba tukuna."

5 Sai mamar Yesu ta ce wa masu hidimar, "Duk abin da Yesu
ya ce ku yi, sai ku yi."

6 Yahudawa suna da al'adar tsarkakewa, saboda haka akwai
randuna shida waɗanda da dutse ne aka gina su a ajiye a wurin,
kowacce tana cin kimanin galan ashirin zuwa talatin. [7] Sai Yesu
ya ce wa masu hidimar, "Ku cika randunan nan da ruwa." Sai
suka ciccika su fal. [8] Sa'an nan ya ce musu, "To, yanzu ku ɗiba,
ku kai wa uban bikin." Sai suka ɗiba ruwan suka kai masa.
[9] Ruwan kuwa ya canza ya zama ruwan inabi, sai uban bikin ya
sha kaɗan. Shi kuwa bai san inda aka samo ruwan inabin ba
(amma masu hidimar da suka ɗebo ruwan sun sani). Sai ya kira
angon suka tsaya a gefe, [10] sa'an nan ya ce masa, "Ai, kowa yakan
fara ba da kyakkyawan ruwan inabi tukuna, bayan mutane sun
sha da yawa, sa'an nan kuma ya kawo wanda bai kai na farin
kyau ba. Amma kai ka ɓoye kyakkyawan ruwan inabin sai
yanzu!"

11 Wannan shi ne abin ban mamaki na farko wanda Yesu ya
yi, ya kuwa yi wannan ne a Kana ta Galili inda ya bayyana
ɗaukakarsa, almajiransa kuma suka ba da gaskiya gare shi.

12 Bayan haka sai Yesu ya gangara zuwa Kafarnahum, da shi
da mamarsa da 'yan'uwansa da kuma almajiransa. Suka yi zama
na 'yan kwanaki a can.

Yesu Ya Tsabtace Haikali
(Mat 21.12-13; Mar 11.15-17; Luk 19.45-46)

13 Da lokacin Bikin Ketarewa[d] na Yahudawa ya yi kusa, sai
Yesu ya tafi Urushalima. [14] A cikin filin haikalin, ya sami mutane
suna sayar da shanu, da tumaki, da tattabaru, da kuma masu canjin
kuɗi suna zaune a teburorinsu. [15] Sai Yesu ya tuƙa bulala da igiya,
ya kore su duka daga haikalin, har da tumakin da shanun. Ya
kuma tutture teburorin masu canjin, ya warwatsar da dukan

2.3: Ezra 3.12 **2.5:** Fit 29.45-46 **2.6:** Ibr 12.26 **2.12:** Mat 4.13
2.13: Fit 12.1-27; L. Kid 19.11-22

[d] **2.13 Bikin Ketarewa:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

kuɗaɗensu. 16 Sai Yesu ya ce wa mutanen da suke sayar da
tattabarun, "Ku ɓitar da waɗannan daga nan! Kada ku mai da
haikalin Ubana kasuwa." 17 Da wannan ya faru, sai almajiransa
suka tuna da abin da aka rubuta a Maganar Allah cewa, "Kaunar
da nake yi wa haikalinka yana ƙunana kamar wuta."

18 Sai shugabannin Yahudawa suka tambayi Yesu suka ce,
"To, wane abin ban mamaki ne za ka nuna mana wanda ya sa
ka yi dukan waɗannan abubuwan da ka yi?"

19 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ku rushe wannan haikali, ni
kuwa zan ta da shi a cikin kwana uku."

20 Sai suka tambaye shi suka ce, "Ya ɗauki shekara arba'in
da shida ana kan ginin wannan haikali! Kai kuma ka ce za ka ta
da shi a cikin kwana uku?"

21 Amma haikalin da Yesu ya yi magana a kai, jikinsa ne.
22 Bayan da aka ta da Yesu daga matattu, sai almajiransa suka tuna
da wannan abin da Yesu ya faɗa, suka kuma ba da gaskiya ga
Rubutaccen Maganar Allah, da kuma maganar da Yesu ya faɗa.

Yesu Ya San Zuciyar Kowa

23 A lokacin da Yesu yana Urushalima domin Bikin Ketarewa,
mutane da yawa sun ba da gaskiya gare shi domin abubuwan ban
mamaki waɗanda suka gani ya yi. 24 Amma Yesu bai yarda da su
ba, domin ya san su duka sosai. 25 Gama ba ya bukatar wani yă
gaya masa wani abu game da mutum, domin ya san abin da yake
a zuciyar ɗan Adam.

Nikodimus Ya Zo wurin Yesu

3 1 Akwai wani mutum mai suna Nikodimus, wanda yake a
ƙungiyar Farisiyawa, shi shugaba ne cikin Yahudawa.
2 Wannan mutum ya zo wurin Yesu da dare, ya ce masa, "Malam,
mun san cewa kai malami ne wanda Allah ya aiko, domin babu
wanda zai iya yin waɗannan abubuwan ban mamaki sai dai wanda
Allah yana tare da shi."

3 Sai Yesu ya amsa masa ya ce, "Hakika, ina gaya maka, babu
wanda zai iya shiga mulkin Allah, sai dai an sāke haife shi."[d]

4 Nikodimus ya yi tambaya ya ce, "Ta yaya za a haifi mutum
bayan ya tsufa? Zai sāke koma cikin mamarsa ne a sāke
haihuwarsa sau na biyu?"

2.17: Zab 69.9 **2.19**: Mat 26.61; 27.40; Mar 14.58; 15.29

[d] **3.3 sai dai an sāke haife shi**: Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "Sai an haife shi daga sama."

5 Yesu ya amsa masa ya ce, "Hakika, ina gaya maka, in ba
an haifi mutum ta ruwa da Ruhu ba, ba zai iya shiga mulkin Allah
ba. 6 Abin da mutum ya haifa mutum ne, amma abin da Ruhu ya
haifa Ruhu ne. 7 Kada fa ka yi mamaki don na ce maka, 'Dole a
sāke haife ku'. 8 Iska tana busawa inda ta ga dama. Kakan ji
motsinta, amma ba ka san wurin da take fitowa ba, ba ka kuma
san inda za ta ba. Haka yake daidai da dukan mutumin da Ruhu
ya haifa."

9 Nikodimus ya tambayi Yesu ya ce, "Ta yaya wannan zai
yiwu?"

10 Sai Yesu ya amsa masa ya ce, "Kai babban malami ne a
Isra'ila, amma duk da haka ba ka gane waɗannan abubuwa ba?
11 Hakika, ina gaya maka, muna maganar abin da muka sani ne,
muna kuma shaida muku abin da muka gani, amma duk da haka
kun ƙi karɓar abin da muka gaya muku. 12 Ina yin muku magana
game da abubuwan da suke a nan duniya, amma ba ku ba da
gaskiya ba, yaya za ku ba da gaskiya idan na gaya muku
abubuwan da suke na sama? 13 Ba wanda ya taɓa hawa zuwa cikin
sama sai dai shi Ɗan Mutum kaɗai da ya sauko daga can.

14 "Kamar dai yadda Musa ya ɗaga maciji a daji, haka kuma
dole ne a ɗaga Ɗan mutum, 15 domin duk wanda ya ba da gaskiya
gare shi, zai sami rai na har abada.

16 "Gama Allah ya ƙaunaci duniya sosai har ya ba da
Makaɗaicin Ɗansa, domin dukan wanda ya ba da gaskiya gare
shi kada yă halaka, amma yă sami rai na har abada. 17 Gama Allah
bai aiko Ɗansa duniya don yă hukunta duniya ba, amma domin
duniya ta sami ceto ta wurinsa.

18 "Duk wanda ya ba da gaskiya ga Ɗan Allah, ba za a
hukunta shi ba. Amma duk wanda bai ba da gaskiya gare shi ba,
an riga an hukunta shi ke nan domin bai ba da gaskiya ga sunan
Makaɗaicin Ɗan Allah ba. 19 Ga yadda shari'ar take, haske ya
shigo duniya, amma mutane suka fi ƙaunar duhu da hasken, don
ayyukansu mugaye ne. 20 Duk wanda yake aikata rashin gaskiya
yakan ƙi hasken, ba zai ma zo wurin hasken ba, don kada
ayyukansa su tonu. 21 Amma mai aikata gaskiya kuwa yakan zo
wajen hasken, domin a gani a fili cewa abin da yake yi yana yi
ne da taimakon Allah."

3.14: L. Kid'21.9 3.14: L. Kid'21.5-9

Shaidar Yohanna Maibaftisma a kan Yesu

22 Bayan haka Yesu da almajiransa suka tafi yankin
Yahudiya. A nan ya jima da su, yana yi wa mutane baftisma.
23 Yohanna kuma yana yin baftisma a Ainon kusa da Salim,
domin akwai ruwa mai yawa a can. Mutane suka yi ta zuwa
ana yin musu baftisma. 24 (Wannan ya faru ne kafin a kulle
Yohanna cikin kurkuku.)

25 Sai almajiran Yohanna suka shiga gardama da wani
Bayahude[e] a kan al'adar wanke-wanke don tsarkakewa. 26 Sai
almajiran suka je wurin Yohanna suka ce masa, "Malam,
mutumin da kuke tare da shi a dā a hayin Kogin Urdun, wanda
kai da kanka ma ka ba da shaida a kansa, ga shi can yana yin
baftisma, har kowa da kowa yana zuwa wurinsa."

27 Sai Yohanna ya amsa ya ce, "Ba mai iya samun kome
sai ko an ba shi daga sama. 28 Ku da kanku ma shaiduna ne
domin na ce, 'Ba ni ne Almasihu ba, amma an aike ni ne in
riga shi zuwa.' 29 A bikin aure, ango ne mai amarya. Abokin
ango wanda ya je auren kuwa yakan jira ne kurum yă ji muryar
ango. Yakan kuma cika da farin ciki idan yă ji ango ya yi
magana. A ta haka ne farin ciki nawa ya cika. 30 Dole ne
wannan yă yi ta ƙaruwa, ni kuma in yi ta raguwa.

Wanda Ya Zo daga Sama

31 "Shi wanda ya zo daga sama ya fi kowa. Dukan wanda ya
fito duniya kuwa na duniya ne, kuma yakan yi maganar abubuwan
duniya ne. Wanda kuma ya zo daga sama ya fi kowa duka.
32 Gama yana shaidar abin da ya ji ya kuma gani ne, duk da haka
ba wanda ya yarda da shaidarsa. 33 Amma duk wanda ya karɓi
shaidarsa, ya tabbatar ke nan cewa, lallai Allah mai gaskiya ne.
34 Gama shi wanda Allah ya aiko, yana maganar Allah ne, domin
Allah ya ba shi Ruhunsa babu iyaka. 35 Uban yana ƙaunar Ɗan,
ya kuma sa kome a hannunsa. 36 Dukan wanda yake ba da gaskiya
ga Ɗan, yana da rai na har abada. Amma duk wanda ya ƙi Ɗan,
ba zai sami rai ba, sai dai fushin Allah yă kasance a kansa."

3.24: Mat 14.3; Mar 6.17; Luk 3.19-20 3.28: Yoh 1.20
3.35: Mat 11.27; Luk 10.22
[e] 3.25 **Wani Bayahude:** Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Wadansu Yahudawa" ne a nan.

Yesu da Wata Mace daga Samariya

4 [1] Farisiyawa suka ji labari cewa Yesu yana samun almajirai,
yana kuma yi musu baftisma fiye da Yohanna. [2] (Amma dai ba
Yesu ne da kansa yake yin baftismar ba, almajiransa ne.) [3] Da Yesu
ya sami labari game da wannan sai ya bar Yahudiya, ya koma Galili.

4 Ya zama dole ne Yesu ya bi ta cikin Samariya. [5] Sai ya zo
wani gari a cikin Samariya mai suna Saikar. Garin yana kusa da
yankin ƙasar da Yakubu ya ba ɗansa Yusufu tun dā. [6] A wannan
wuri ne rijiyar Yakubu take. Da Yesu ya gaji da tafiya, sai ya
zauna a bakin rijiyar. Wannan ya faru wajen tsakar rana ne.

7 Sai ga wata mace 'yar Samariya ta zo dĩban ruwa. Yesu ya
ce mata, "Ba ni ruwa in sha." [8] (Almajiransa kuwa sun shiga cikin
gari don sayen abinci.)

9 Sai macen nan Basamariya ta ce wa Yesu, "Yaya kai
Bayahude za ka roƙe ni ruwan sha, ni da nake mutuniyar
Samariya?" (Don Yahudawa ba sa haɗa ido da Samariyawa.)*f*

10 Yesu ya amsa mata ya ce, "Da kin san kyautar Allah, da
kuma wanda yake ce miki, 'Ba ni ruwa in sha,' ai, da kin roƙe
shi, shi kuwa zai ba ki ruwa mai ba da rai."

11 Sai macen ta ce wa Yesu, "Mai girma, ai, ba ka da guga,
rijiyar kuwa da zurfi. To, a ina ne za ka sami wannan ruwa mai
ba da rai? [12] Ko ka fi ubanmu Yakubu ne, wanda ya bar mana
rijiyar, har shi da kansa, da 'ya'yansa, da dabbobinsa, suka sha
ruwa daga ciki?"

13 Yesu ya amsa ya ce, "Duk wanda ya sha wannan ruwa zai
sāke jin ƙishi. [14] Amma duk wanda ya sha ruwan da zan ba shi,
ba zai ƙara jin ƙishi ba har abada. Ruwan da zan ba shi zai zama
masa maɓuɓɓugan ruwa wanda yake ɓuɓɓugowa zuwa rai
madawwami."

15 Sai macen ta ce masa, "Mai girma, ka ba ni ruwan nan,
don kada in ƙara jin ƙishi, don kada kuma in riƙa zuwa nan domin
dĩban ruwa."

16 Sai Yesu ya ce mata, "Ki je ki kira mijinki ku zo nan."

17 Sai ta amsa ta ce, "Ai, ba ni da miji."

Yesu ya ce mata, "Kin faɗa gaskiya da kika ce ba ki da miji.
[18] Don ainihin gaskiyar kuwa shi ne, kin auri maza biyar, wanda
kuke tare yanzu kuwa ba mijinki ba ne."

4.5: Far 33.19; Josh 24.32 **4.9**: Ezra 4.1-5; Neh 3.33-34

f **4.9 Don Yahudawa ba sa haɗa ido da Samariyawa:** Wani juyi na waɗannan kalmomin shi ne "Yahudawa ba sa amfani da kwaf da kwanonin da Samariyawa suka yi amfani da su."

19 Sai macen ta ce wa Yesu, "Mai girma, ina gani kai annabi
ne. 20 Kakanninmu sun yi wa Allah sujada a dutsen nan. Amma
ku Yahudawa kun ce a Urushalima ne ya kamata a yi wa Allah
sujada."
21 Sai Yesu ya amsa mata ya ce, "Uwargida, ki ba da gaskiya
ga abin da nake faɗi, gama lokaci yana zuwa da mutane ba za
su yi wa Uba sujada a dutsen nan, ko a Urushalima ba. 22 Ku
mutanen Samariya ba ku san abin da kuke yi wa sujada ba.
Amma mu Yahudawa mun san abin da muke yi wa sujada,
domin ceto ya fito daga Yahudawa ne. 23 Amma lokaci yana
zuwa, har ma ya riga ya zo, da masu sujada na gaskiya za su
yi wa Uba sujada cikin ruhu, da kuma gaskiya, domin Uba yana
neman irin waɗannan ne su yi masa sujada. 24 Allah ruhu ne,
masu yi masa sujada kuma sai su yi masa sujada cikin ruhu, da
cikin gaskiya kuma."
25 Sai macen ta ce wa Yesu, "Na sani Almasihu yana zuwa
wanda ake ce da shi Kiristi. Idan ya zo zai bayyana mana dukan
kome."
26 Yesu ya ce mata, "Ni mai magana da ke, ni ne shi."
27 Suna gama magana ke nan sai ga almajiransa suka dawo,
suka kuwa yi mamakin ganin yana magana da mace. Amma babu
wanda ya ce mata, "Me kike bukata," ko kuma yă tambaye shi,
"Me ya sa kake magana da ita?"
28 Sai macen nan ta bar tulunta a wurin ta je cikin gari ta ce
wa mutane, 29 "Ku zo, ku ga mutumin da ya gaya mini duk abin
da na taɓa yi! Ko ya yiwu wannan mutumin ne Almasihun?"
30 Sai mutane suka fiffito daga cikin gari suka zo wurin Yesu.
31 Ana cikin wannan ke nan, sai almajiran Yesu suka roƙe shi
suka ce, "Malam, ka ci abinci."
32 Amma Yesu ya ce musu, "Ina da wani abincin da zan ci
da ba ku san kome a kai ba." 33 Sai almajiransa suka tambayi
juna suka ce, "Ko wani ya kawo masa abinci ne?"
34 Amma Yesu ya ce, "Abincina shi ne in yi nufin wanda ya
aiko ni, in kuma gama aikinsa. 35 Ba kuna cewa sauran watanni
huɗu a yi girbi ba? Amma ina gaya muku fa, ku dubi gonaki da
kyau, sun nuna, sun kuma isa girbi. 36 Mai girbi yana samun lada,
yana kuma tara amfani zuwa rai na har abada, domin mai shuka
da mai girbi su yi farin ciki tare. 37 A nan kam, karin maganan
nan gaskiya ne, cewa, 'Wani ya yi shuki, wani ya yi girbi.' 38 Na
aike ku girbin abin da ba ku yi wahalarsa ba. Waɗansu sun yi
wahala, ku kuwa kun mori ribar wahalarsu."

39 Mutanen Samariya da yawa daga wannan gari suka ba da
gaskiya ga Yesu saboda maganar matan nan da ta ce, "Ya gaya
mini duk abin da na taɓa yi." 40 Da mutanen Samariya suka zo
wurin Yesu, sai suka roƙe shi yă zauna tare da su, sai ya kuwa
zauna kwana biyu.

41 Mutane da yawa kuma suka ba da gaskiya ga Yesu saboda
maganarsa. 42 Sa'an nan mutanen Samariya suka ce wa macen,
"Yanzu kam, mun ba da gaskiya, ba don ma abin da kika faɗa
kawai ba, amma don mu ma mun ji da kanmu, mun kuma tabbata
lallai wannan mutum ne Mai Ceton duniya."

Yesu Ya Warkar da Yaron Ma'aikacin Hukuma

43 Bayan kwana biyun nan sai Yesu ya tashi daga ƙasar
Samariya zuwa Galili. 44 (Gama Yesu da kansa ya taɓa faɗa cewa,
"Annabi ba shi da daraja a ƙasarsa".) 45 Da ya kai Galili, sai
mutanen Galili suka karɓe shi hannu biyu-biyu domin su ma sun
je Bikin Ketarewa a Urushalima, suka kuma ga duk abin da Yesu
ya yi.

46 Sai Yesu ya sāke koma garin Kana ta Galili, wato inda ya
mai da ruwa ya zama ruwan inabi. A wurim kuwa akwai wani
ma'aikacin hukuma wanda yaronsa a Kafarnahum ba shi da
lafiya. 47 Da wannan mutumin ya ji cewa Yesu ya dawo Galili
daga Yahudiya, sai ya tafi wurinsa ya roƙe shi yă je yă warkar
da ɗansa wanda yake bakin mutuwa. 48 Yesu ya amsa masa ya
ce, "Idan ba ku ga alamu da abubuwan ban mamaki ba, ba za ku
ba da gaskiya ba ko kaɗan."

49 Sai ma'aikacin hukuman nan ya ce wa Yesu, "Mai girma,
ka zo mu tafi kafin yarona ya mutu."

50 Yesu ya ce masa, "Ka tafi, gama yaronka zai rayu."
Mutumin kuwa ya gaskata da abin da Yesu ya faɗa masa, sai
ya yi tafiyarsa. 51 Yana kan hanyarsa zuwa gida ke nan, sai ga
bayinsa suka gamu da shi, suka ce masa, "Yaronka yana samun
sauƙi."

52 Sai ya tambaye su ainihin lokacin da ya fara samun sauƙin.
Sai suka ce masa, "Jiya da ƙarfe ɗaya na rana ne zazzaɓin ya
sake shi." 53 Sai baban yaron ya gane cewa a daidai wannan lokaci
ne Yesu ya ce masa, "Ka tafi, gama yaronka zai rayu." Sai
mutumin da dukan iyalinsa suka ba da gaskiya ga Yesu.

4.44: Mat 13.57; Mar 6.4; Luk 4.24 **4.45:** Yoh 2.23 **4.46:** Yoh 2.1-11

54 Wannan ne abin ban mamaki na biyu da Yesu ya yi bayan da ya bar Yahudiya ya tafi Galili.

Yesu Ya Warkar da Gurgu a Tafkin Betasda

5 1 Bayan wannan, Yesu ya tafi Urushalima domin wani bikin
Yahudawa. 2 A Urushalima kuwa akwai wani tafkin ruwa
wanda aka kewaye shi da rumfuna guda biyar. Da Yahudanci ana
ce da shi Betasda. Wannan tafki yana kusa da Kofar Tumaki ne.
3 A rumfuna nan ne marasa lafiya, da makafi, da guragu, da
shanyayyu da yawa sun saba kwanciya.[g] 5 A nan kuwa akwai
wani mutumin da ya yi shekara talatin da takwas a cikin rashin
lafiya. 6 Da Yesu ya gan shi kwance, ya kuma sani mutumin ya
daɗe da wannan ciwo, sai Yesu ya ce wa mutumin, "Kana so ka
warke?"

7 Mai ciwon ya amsa masa ya ce, "Mai girma, ai, ba ni da
wanda zai taimake ni in shiga cikin tafkin lokacin da aka motsa
ruwan. Idan na yi ɓoƙari in shiga, sai wani yă riga ni."

8 Sai Yesu ya ce masa, "Tashi, ka ɗauki tabarmarka, ka yi
tafiya!" 9 Nan take, mutumin ya warke, ya kuma ɗauki tabarmarsa
ya yi tafiya.

Wannan abin ya faru a Ranar Hutun Yahudawa ne, wato,
Asabar. 10 Saboda haka Yahudawa suka ce wa mutumin da aka
warkar, "Yau Ranar Hutu ne, kuma bisa ga Dokarmu ba daidai
ba ne ka ɗauki tabarmarka."

11 Sai mutumin ya amsa musu ya ce, "Ai, wanda ya warkar
da ni, shi ne ya ce mini, in ɗauki tabarmata in yi tafiya."

12 Suka tambaye shi suka ce, "Wane ne wannan mutumin da
ya ce maka ka ɗauki tabarmarka ka yi tafiya?"

13 Mutumin da aka warkar dîn kuwa bai san ko wane ne ma
ya warkar da shi ba, domin akwai mutane da yawa a wurin, kuma
Yesu ya ɓace cikin jama'a.

14 Bayan ɗan lokaci, Yesu ya same shi a cikin haikali, ya ce
masa, "Ka ga fa, ka warke! To, ka daina yin zunubi, don kada
wani abu da ya fi wannan muni yă same ka." 15 Sai mutumin ya
tafi ya gaya wa shugabannin Yahudawa cewa, Yesu ne ya warkar
da shi. 16 Saboda haka suka fara tsananta wa Yesu, don dai yana

---

5.2: Neh 3.1, 12.39 **5.10**: Neh 13.19; Irm 17.21

[g] **5.3** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya ta 3b-4 haka "Suna jira a motsa ruwan. Don a lokaci-lokaci mala'ikan Ubangiji yakan sauko ya motsa ruwan. Duk kuwa wanda ya fara shiga bayan an motsa ruwan, sai yă warke daga duk irin ciwon da yake da shi."

yin irin wadannan abubuwa a Ranar Hutu. 17 Sai Yesu kuwa ya ce musu, "Ubana yana aiki har yanzu, ni ma ina yi."

18 Wannan magana kuwa ya sa Yahudawa suka ƙara nema su kashe Yesu. Suka ce, "Ba don ma ya karya dokar Ranar Hutu kawai ba, amma ya ce Allah Ubansa ne, wato, ya mai da kansa daidai da Allah ke nan."

Ikon Yesu Dan Allah

19 Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Hakika, ina gaya muku, Dan ba ya yin kome shi kadai, sai dai abin da ya ga Uban yake yi. Domin duk abin da Uban yake yi, shi ne ma Dan yake yi. 20 Gama Uban yana ƙaunar Dan, yana kuma nuna masa duk abin da shi kansa yake yi, har ma zai nuna masa ayyukan da suka fi wadannan, domin ku yi mamaki. 21 Kamar dai yadda Uba yake ta da matattu ya kuma raya su, haka ma Dan yana ba da rai ga dai duk wanda ya ga dama. 22 Uba kuma ba ya yin wa kowa shari'a, amma ya ba Dan ikon yin dukan shari'a, 23 domin dukan mutane su girmama Dan, kamar yadda suke girmama Uban. Duk wanda ba ya girmama Dan, ba ya girmama Uban da ya aiko shi ke nan.

24 "Hakika, ina gaya muku, duk mutumin da yake jin maganata, yana kuma ba da gaskiya ga wanda ya aiko ni, yana da rai na har abada. Ba za a yi masa hukunci ba, ya riga ya ƙetare mutuwa zuwa rai. 25 Hakika, ina gaya muku, lokaci yana zuwa, ya riga ya zo ma, da matattu za su ji muryar Dan Allah, wadanda suka ji kuwa za su rayu. 26 Gama kamar yadda Uba da kansa tushen rai ne, haka ma ya sa Dansa yă zama tushen rai. 27 Ya kuma ba shi ikon yin shari'a domin shi Dan Mutum ne. 28 Kada ku yi mamakin wannan magana, domin lokaci yana zuwa da duk wadanda suke cikin kaburbura za su ji muryarsa, 29 su fito. Wadanda suka yi abu mai kyau za su tashi, su rayu, amma wadanda suka yi rashin gaskiya kuwa, za su tashi a kuwa yi musu hukunci. 30 Ba na iya yin kome ni kadai. Ina shari'ata ne yadda Allah ya fada mini in yi. Saboda haka shari'ata ta gaskiya ce, domin ba nufin kaina nake bi ba, amma nufin wanda ya aiko ni ne.

Shaidun Yesu

31 "Idan na yi wa kaina shaida, to, shaidata ba gaskiya ba ce. 32 Amma akwai wani wanda yake yin shaida a kaina, na kuma

5.29: Dan 12.2

san shaidar da yake yi a kaina gaskiya ce. 33 Kun aiki mutane
wurin Yohanna, shi kuwa ya shaida muku gaskiya. 34 Duk da haka
ban dogara da shaidar mutum ba. Na dai faɗa haka ne domin ku
sami ceto. 35 Yohanna fitila ne mai ci, mai haske kuma, kun kuwa
yarda ku yi farin ciki sosai da haskensa a ɗan lokaci kaɗan.
36 Amma ina da tawa shaida a kaina wadda ta fi shaidar da
Yohanna ya bayar game da ni. Abubuwan da nake yi, waɗanda
Ubana ya ba ni in yi, su ne abubuwan da suka zama shaidata,
cewa Uba ne ya aiko ni. 37 Uban kuma wanda ya aiko ni shi da
kansa ya zama shaidata. Ba ku taɓa jin muryarsa ba, ba ku kuma
taɓa ganin yadda yake ba. 38 Maganarsa ba ta zama a zuciyarku,
domin ba ku ba da gaskiya ga shi wanda Uba ya aiko ba. 39 Kuna
ta binciken Rubutattun Maganar Allah, don a tsammaninku za ku
sami rai na har abada a cikinsu. Waɗannan Rubutattun Maganar
Allah kuwa su ne suke ba da shaida a kaina. 40 Amma duk da
haka kun ƙi zuwa wurina ku sami rai.

41 "Ba na karɓar yabo daga wurin mutane. 42 Amma fa na
san ku, na kuma san cewa ba ku da ƙaunar Allah a cikin
zukatanku. 43 Na zo a cikin sunan Ubana, ba ku karɓe ni ba,
amma idan wani ya zo a cikin sunan kansa, za ku karɓe shi.
44 To, yaya za ku ba da gaskiya bayan kuna ƙoƙarin samun yabo
daga junanku, amma ba kwa ƙoƙarin samun yabon da yake
fitowa daga wurin Allah wanda yake ɗaya kaɗai? 45 Kada ku
yi tsammani zan yi ƙararku wurin Uba. Akwai mai ƙararku, shi
ne Musa, wanda kuke tsammani zai taimake ku. 46 Da a ce kun
ba da gaskiya ga Musa, da kun ba da gaskiya gare ni, domin
Musa ya rubuta game da ni. 47 Amma in kuwa ba ku gaskata
da abin da ya rubuta ba, ta yaya za ku gaskata da maganata?"

Yesu Ya Ciyar da Mutum Dubu Biyar

(Mat 14.13-21; Mar 6.30-44; Luk 9.10-17)

6 1 Bayan ɗan lokaci Yesu ya haye Tekun Galili, wato, Tekun
Tibariya. 2 Sai mutane da yawa suka bi shi, domin sun ga
abubuwan ban mamaki da yake yi wa masu ciwo. 3 Sai Yesu ya
hau dutse ya zauna a can tare da almajiransa. 4 To, lokacin Bikin
Ketarewa, wato, bikin Yahudawa ya yi kusa. 5 Da Yesu ya ɗaga
ido ya ga mutane da yawa suna ta zuwa wurinsa, sai ya ce wa
Filibus, "Ina za mu sayo isasshen abincin da mutanen nan za su
ci?" 6 Yesu ya yi wa Filibus wannan tambaya ne don dai ya gwada
shi, domin Yesu ya riga ya san abin da zai yi.

5.33: Yoh 1.19-27; 3.27-30 **5.37**: Mat 3.17; Mar 1.11; Luk 3.22

7 Filibus ya amsa ya ce, "Ai, ko abinci na yawan kudin da
lebura zai samu a ranaku ɗari biyu ma ba zai isa kowannensu yă
sami kaɗan ba."
8 Sai ɗaya daga cikin almajiran mai suna Andarawus,
ɗan'uwan Siman Bitrus, ya ce wa Yesu, 9 "Ga wani ɗan yaro nan
da dunƙulen burodi biyar da aka yi da garin bale da kuma kifi
biyu. Amma me waɗannan za su yi wa mutane masu yawa haka?"
10 Yesu ya ce wa almajiransa, "Ku faɗa wa mutane su zauna."
A wannan wurin kuwa akwai ciyawa da yawa. Sai mazaje suka
zazzauna, sun kai wajen dubu biyar. 11 Yesu ya ɗauki dunƙulen
burodin, bayan ya yi godiya ga Allah kuma, sai ya rarraba wa
mutanen da suke zaune, ya ba su duk abin da zai ishe su. Haka
kuma ya yi da kifin. 12 Da suka ci suka ƙoshi, sai ya ce wa
almajiransa, "Ku tattara gutsattsarin da suka rage domin kada
kome yă lalace." 13 Sai almajiran suka tattara gutsattsarin burodin
suka cika kwanduna goma sha biyu, wato, gutsattsarin nan daga
dunƙulen burodi biyar na bale nan ne waɗanda mutane suka ci
suka rage.
14 Da jama'a suka ga wannan abin mamakin da Yesu ya yi,
sai suka ce, "Ba shakka, wannan shi ne Annabin nan mai zuwa
duniya." 15 Da Yesu ya gane mutanen suna shirin zuwa su ɗauke
shi ƙarfi da yaji su naɗa shi sarki, sai ya sāke komawa kan dutse
shi kaɗai.

Yesu Ya Yi Tafiya a kan Ruwa
(Mat 14.22-33; Mar 6.45-52)

16 Da yamma ta yi, sai almajiran Yesu suka gangara zuwa
teku. 17 A lokacin wuri ya fara duhu, kuma Yesu bai riga ya zo
wurinsu ba tukuna. Sai almajiransa suka shiga jirgin ruwa suka
soma ƙetare tekun zuwa Kafarnahum. 18 Sai tekun ya fara hauka
saboda wata mummunar iska da take busawa. 19 Bayan sun yi tuƙi
wajen kilomita biyar ko shida, sai suka ga Yesu yana tafiya a kan
ruwa, yana ta zuwa kusa da jirgin. Sai almajiran suka firgita.
20 Amma Yesu ya ce musu, "Ni ne, kada ku ji tsoro." 21 Sa'an
nan suka yarda su karɓe shi cikin jirgin. Nan da nan jirgin ya kai
wurin da za su.

Mutane Sun Nemi Yesu

22 Da gari ya waye sauran mutanen da suke zaune a hayin
tekun suka lura cewa dā ma jirgi ɗaya kurum ya zo wurin, suka
kuma lura Yesu bai shiga cikin jirgin tare da almajiransa ba,

almajiransa ne kaɗai suka tafi. 23 Amma akwai waɗansu jiragen da suka zo daga Tibariya suka tsaya kusa da wurin da mutanen suka ci burodi bayan Yesu ya yi godiya ga Allah. 24 Da mutanen suka ga cewa Yesu da almajiransa ba sa nan a wurin, sai suka shiga jiragen ruwan, suka tafi Kafarnahum suna neman Yesu.

Yesu Ne Burodi Mai Ba da Rai

25 Da suka same shi a hayin tekun, suka ce masa, "Malam, yaushe ka zo nan?"

26 Yesu ya amsa musu ya ce, "Hakika, ina gaya muku, kuna nemana ne don kun ci burodi nan kun ƙoshi, amma ba don kun ga abin ban mamaki da na yi ba ne. 27 Kada ku yi wahalar aiki a kan neman abinci mai lalacewa, amma ku yi aiki a kan abincin da ba zai lalace ba, sai dai yă ba da rai na har abada. Wannan shi ne abincin da Ɗan mutum zai ba ku. Domin a kan Ɗan Mutum ne Allah Uba ya riga ya buga hatiminsa na nuna yarda."

28 Sai mutanen suka tambayi Yesu suka ce, "Me za mu yi don mu cika abin da Allah yake so?"

29 Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Wannan shi ne abin da Allah yake so ku yi, wato, ku ba da gaskiya ga wanda ya aiko."

30 Sai mutanen suka tambayi Yesu kuma suka ce, "To, wane irin abin ban mamaki ne za ka yi don mu gani mu ba da gaskiya gare ka? Me za ka yi? 31 Kakannin kakanninmu sun ci manna a daji, yadda yake a rubuce cewa, 'Ya ba su abinci daga sama don su ci.' "

32 Sa'an nan Yesu ya amsa musu ya ce, "Hakika, ina gaya muku, ba Musa ne ya ba ku abincin nan daga sama ba, Ubana ne yake ba ku abinci na gaskiya daga sama. 33 Ai, abincin Allah shi ne wanda yake saukowa daga sama yana ba duniya rai."

34 Sai suka ce masa, "Mai girma, ka rika ba mu irin wannan abinci kullum!"

35 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ni ne abinci mai ba da rai, wanda ya zo wurina ba zai ƙara jin yunwa ba, wanda ya gaskata da ni kuma ba zai taɓa jin ƙishin ruwa ba. 36 Amma kamar yadda dai na faɗa muku, kun gan ni, duk da haka ba ku ba da gaskiya ba. 37 Duk waɗanda Uba ya ba ni, za su zo wurina, wanda kuma ya zo wurina kuwa ba zan ƙi shi ba. 38 Gama na sauko daga sama, ba domin in yi nufina ba, sai dai in yi nufin wanda ya aiko ni. 39 Kuma nufin wanda ya aiko ni shi ne, kada in ɓatar da ko da

6.31: Fit 16.4,15; L. Kid 11.8; Neh 9.15; Zab 78.24

ɗaya daga cikin dukan waɗanda ya ba ni, amma dai in tashe su a ranar ƙarshe. 40 Domin wannan shi ne nufin Ubana cewa, duk wanda yake duban Ɗan, yake kuma gaskatawa da shi yana da rai na har abada, ni kuma zan tashe shi a ranar ƙarshe."

41 Sai Yahudawa suka yi gunaguni game da Yesu domin ya ce, "Ni ne abincin da ya sauko daga sama." 42 Yahudawan suka ce, "Ashe, wannan ba Yesu ne ba, yaron Yusufu, wanda mun san duk babansa da mamarsa? To, yaya yanzu zai ce, 'Na sauko ne daga sama'?"

43 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ku bar yin gunaguni a tsakaninku. 44 Ba mai iya zuwa wurina, sai dai in Uba wanda ya aiko ni ne ya jawo shi, ni kuwa zan ta da wannan mutum a ranar ƙarshe. 45 An rubuta a cikin littattafan annabawa cewa, 'Dukansu Allah ne zai koya musu.' To, duk wanda ya ji, ya kuma koya a wurin Uban, yakan zo wurina. 46 Ba wanda ya taɓa ganin Uban sai dai wanda ya fito daga wurin Allah, shi ne kaɗai ya taɓa ganin Uban. 47 Hakika, ina gaya muku, duk wanda ya ba da gaskiya yana da rai na har abada. 48 Ni ne abinci mai ba da rai. 49 Kakannin kakanninku sun ci manna a daji, amma duk da haka suka mutu. 50 Amma ga abinci mai saukowa daga sama. Duk wanda ya ci wannan abinci, ba zai mutu ba. 51 Ni ne abincin rai da ya sauko daga sama. Duk wanda ya ci wannan abinci, zai rayu har abada. Wannan abincin naman jikina ne, wanda zan bayar domin duniya ta sami rai."

52 Sai Yahudawa suka shiga gardama mai zafi a tsakaninsu, suna cewa, "Yaya mutumin nan zai ba mu naman jikinsa mu ci?"

53 Sai Yesu ya ce musu, "Hakika, ina gaya muku, in ba kun ci naman jikin Ɗan Mutum kun kuma sha jininsa ba, ba ku da rai a cikinku ke nan. 54 Duk wanda yake cin naman jikina, yake shan jinina kuma, yana da rai na har abada, zan kuwa tashe shi a ranar ƙarshe. 55 Domin naman jikina abinci ne na ƙwarai, jinina kuma, abin sha ne na ƙwarai. 56 Duk wanda yake cin naman jikina, yake kuma shan jinina, yana rayuwa a cikina, ni kuwa a cikinsa. 57 Kamar yadda Uba mai rai ya aiko ni, saboda shi ne kuma nake rayuwa, haka ne kuma wanda ya mai da ni abincinsa zai rayu saboda ni. 58 Ni ne abincin da ya sauko daga sama. Kakannin kakanninku sun ci manna, amma duk da haka suka mutu, amma duk mutumin da ya ci wannan abinci zai rayu har abada."

6.45: Ish 54.13

59 Yesu ya faɗa dukan waɗannan abubuwa ne a lokacin da
yake koyarwa a cikin majami'a[h] a Kafarnahum.

Kalmomin Rai na har Abada

60 Da jin haka, sai da yawa daga cikin almajiransa suka ce,
"Wannan maganar mai wuya ce, wa zai iya yă karɓe ta?"
61 Yesu kuwa da yake ya sani cewa almajiransa suna gunaguni
a kan wannan koyarwa, sai ya ce musu, "Wannan koyarwa ta
ɓata muku rai ne? 62 To, yaya ranku zai zama ke nan in kuka ga
Ɗan Mutum yana hawa zuwa inda ya fito? 63 Ruhu ne yake ba
da rai. Jiki ba shi da ikon kome. Kalmomin da na faɗa muku
Ruhu ne, da kuma rai. 64 Amma akwai waɗansunku da ba su ba
da gaskiya ba." Gama tun farko Yesu ya san waɗanda ba su ba
da gaskiya ba, da kuma wanda zai bashe shi. 65 Sai Yesu ya ƙara
da cewa, "Shi ya sa na gaya muku cewa, 'Babu wanda zai iya
zuwa wurina, sai dai Uban ya yarda masa.' "
66 Bayan wannan maganar da Yesu ya yi, sai da yawa daga
cikin mutanen da suke binsa suka bar shi, suka kuma daina binsa.
67 Sai Yesu ya tambayi sha biyun nan ya ce, "Ku ma kuna
so ku tafi ne?"
68 Siman Bitrus ya amsa masa ya ce, "Ubangiji, wurin wane
ne za mu je? Ai, kai ne kake da magana mai ba da rai na har
abada. 69 Mu kuwa mun ba da gaskiya, mun kuma sani cewa kai
ne Mai Tsarkin nan na Allah."
70 Sai Yesu ya amsa ya ce, "Na zaɓi dukanku goma sha biyu,
amma ɗayanku shaiɗan ne." 71 Wato, yana nufin Yahuda, ɗan
Siman Iskariyoti, don shi ne zai bashe shi, ko da yake shi ɗaya
daga cikin sha biyun nan ne.

'Yan'uwan Yesu ba Su Gaskata da Shi Ba

7 1 Bayan wannan Yesu ya zazzaga cikin Galili, amma bai so
yă tafi cikin Yahudiya ba, don Yahudawan da suke can suna
nema su kashe shi. 2 Bikin Bukkoki[i] na Yahudawa ya yi kusa ke
nan, 3 sai 'yan'uwan Yesu suka ce masa, "Ya kamata ka tashi
daga nan ka tafi Yahudiya don almajiranka su ma su ga abubuwan
ban mamakin da kake yi. 4 Ai, duk wanda yake so a san shi sosai
ba ya ɓoye abin da yake yi. Tun da yake kana yin waɗannan

6.68-69: Mat 16.16; Mar 8.29; Luk 9.20 **7.2:** L. Fir 23.34; M. Sh 16.13
[h] **6.59 majami'a:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.
[i] **7.2 Bikin Bukkoki:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

abubuwa, ai, sai ka nuna kanka domin duniya ta san ka." 5 Gama su 'yan'uwan Yesu ma ba su ba da gaskiya gare shi ba.

6 Sai Yesu ya ce musu, "Lokacina bai zo ba tukuna, amma a wajenku kowane lokaci daidai ne. 7 Ku kam duniya ba za ta iya ƙinku ba, amma ni take ƙi, domin ina faɗa mata mugayen abubuwan da take yi. 8 Ku dai ku tafi bikin. Ni ba za ni wannan biki ba, don lokacina bai yi ba tukuna." 9 Bayan da Yesu ya faɗa musu wannan magana, sai ya ɗan dakata a Galili.

10 Amma bayan da 'yan'uwansa suka tafi bikin kuwa, Yesu ma ya tafi, amma a ɓoye, ba a fili ba. 11 Yahudawa suna ta nemansa a wurin bikin, suna tambaya cewa, "Ina mutumin yake?"

12 A cikin taron nan mutane suna ta maganganu da junansu a ɓoye a kan Yesu. Waɗansu suna cewa, "Shi mutumin kirki ne."

Waɗansu kuma suna cewa, "A'a, ai, yana ruɗin mutane ne." 13 Amma ba wanda ya yi ƙarfin hali yă yi magana a kan Yesu a fili, don suna tsoron shugabannin Yahudawa.

Yesu Ya Yi Koyarwa a Bikin Bukkoki

14 Da aka ci rabin lokacin biki, sai Yesu ya shiga haikali ya fara koyarwa. 15 Sai shugabannin Yahudawa suka yi mamaki suka ce, "Wannan mutum bai taɓa zuwa makaranta don koyon karatu ba, ta yaya ya zama gwani haka?"

16 Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Abubuwan da nake koyarwa ba nawa ba ne, amma na wanda ya aiko ni ne. 17 Duk wanda ya zaɓi yin abin da Allah yake so, zai sani cewa koyarwata ta fito daga wurin Allah ne, ba wurina ba. 18 Wanda yake koyar da abubuwa na kansa, yana ƙoƙarin samo wa kansa suna ne. Amma wanda yake ƙoƙarin samo wa wanda ya aiko shi suna, shi ne mai gaskiya, kuma ba shi da rashin gaskiya a cikinsa. 19 Ashe, ba Musa ne ya ba ku Doka ba? Amma duk da haka ba wanda yake kiyaye Dokar a cikinku. Me ya sa kuke so ku kashe ni?"

20 Mutanen suka amsa suka ce, "Kana da aljani a cikinka. Su wane ne suke so su kashe ka?"

21 Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Na yi abin ban mamaki guda ɗaya tak, amma kun yi mamaki dukanku. 22 Musa ya ba ku umarnin kaciya (ko da yake ba shi ne ya fara ba, amma kakannin kakanninku ne). Duk da haka kukan yi wa yaro kaciya a Ranar Hutu. 23 To, idan an iya yi wa yaro kaciya a Ranar Hutu don dai a yi biyayya da Dokar Musa, to, me ya sa za ku yi fushi da ni

7.22: Far 17.10; L. Fir 12.3

don na warkar da jikin mutum sarai a Ranar Hutu? 24 Kada ku yi
shari'a bisa ga yadda abubuwa suke a ganin ido, amma ku yi
shari'a bisa ga abin da yake daidai."

Yesu Ne Almasihu?

25 Sai waɗansu mutanen Urushalima suka ce, "Ashe, ba
wannan ne mutumin da suke nema su kashe ba? 26 Ga shi nan
kuwa, yana magana a fili, ba su ce masa kome ba. Ko
shugabannin sun riga sun yarda cewa shi ne Almasihu ke nan?
27 Ga shi mun san inda mutumin nan ya fito, amma idan Almasihu
na gaske ya zo, ba wanda zai san inda ya fito."

28 Yesu yana koyarwa a haikalin ke nan, sai ya ɗaga murya
ya ce, "Kun dai san ni, kun kuma san inda na fito. Amma ban
zo da ikon kaina ba. Wanda ya aiko ni mai gaskiya ne, shi kuwa
ba ku san shi ba. 29 Amma ni na san shi, domin daga wurinsa na
fito, shi ne kuwa ya aiko ni."

30 Da Yesu ya faɗa wannan magana, sai mutanen suka nema
su kama shi. Amma ba wanda ya taɓa shi, don lokacinsa bai yi
ba. 31 Duk da haka mutane da yawa a cikin jama'ar suka gaskata
da Yesu, suna cewa, "Shin, lokacin da Almasihu zai zo, zai yi
abubuwan ban mamaki fiye da abubuwan da mutumin nan ya
yi ne?"

Shugabannin Yahudawa Sun Yi Kokarin Kamun Yesu

32 Farisiyawa suka ji mutane suna magana a hankali da juna
a kan Yesu, sai manyan firistoci da Farisiyawa suka aiki
dogarawan haikali su kamo shi.

33 Sai Yesu ya amsa ya ce, "Lokacin da zan zauna tare da ku
ya rage ɗan kaɗan, sa'an nan zan koma wurin wanda ya aiko ni.
34 Za ku neme ni, amma ba za ku same ni ba. Inda nake kuwa ba
za ku iya zuwa ba."

35 Sai Yahudawa suka yi magana da juna suka ce, "Ina za
shi da har ba za mu same shi ba? Ko za shi wajen Yahudawa
da suke a warwatse suna zama da Helenawa ne, yă koya wa
Helenawa a can? 36 Me yake nufi da ya ce, 'Za ku neme ni, amma
ba za ku same ni ba'? Me yake nufi kuma da 'Inda nake ba za
ku iya zuwa ba'?"

7.23: Yoh 5.9

Alkawarin Ruwan Rai

37 A ranar ƙarshe ta bikin, wadda kuma ta zama babbar rana
ta bikin, Yesu ya tsaya ya ɗaga murya ya ce, "Duk mai jin ƙishin
ruwa yă zo wurina yă sha. 38 Duk mai ba da gaskiya gare ni,
'Rafuffuka masu ba da ruwan rai za su fiffito daga kowanne
mutumin da ya ba da gaskiya gare ni' kamar yadda Rubutaccen
Maganar Allah ya faɗa.[j] 39 Yesu yana magana ne a kan Ruhu Mai
Tsarki, wanda masu ba da gaskiya gare shi za su karɓa, domin a
wannan lokacin ba a ba da Ruhu Mai Tsarki ba tukuna, saboda
ba a riga an ɗaukaka Yesu ba."

Mutane Sun Yi Gardama a kan Yesu

40 Da mutanen suka ji wannan maganar da Yesu ya yi, sai
suka ce, "Ba shakka, wannan shi ne Annabin nan."
41 Waɗansu kuwa suka ce, "Wannan shi ne Almasihun."
Amma har yanzu waɗansu suka ce, "Ashe, Almasihun daga Galili
zai fito? 42 Ba Rubutaccen Maganar Allah ya faɗa cewa Almasihu
zai fito daga zuriyar Dawuda ne ba? Ba kuma zai fito daga
Baitalami, ƙauyen da Dawuda ya zauna ne ba?" 43 Sai bakin
mutanen ya rabu a kan Yesu. 44 Waɗansunsu suka so su kama
shi, amma ba wanda ya taɓa shi.

Rashin Bangaskiyar Shugabannin Yahudawa

45 Da dogarawan haikali suka koma, sai manyan firistoci da
shugabannin Farisiyawa suka tambaye su suka ce, "Me ya sa ba
ku kawo shi ba?"
46 Sai dogarawan suka amsa suka ce, "Ai, babu mutumin da
ya taɓa magana kamar wannan mutum."
47 Farisiyawan suka ce wa dogarawan, "Af! Har ku ma ya
ruɗe ku ke nan? 48 Ko akwai wani daga cikin shugabanni ko
Farisiyawan da ya ba da gaskiya gare shi? 49 Amma wannan taron
da ba su san kome a kan Dokar Musa ba, ai, la'anannu ne."
50 Nikodimus kuwa wanda ya je wurin Yesu a dā, wanda
kuwa yana ɗaya daga cikin Farisiyawan, ya ce musu, 51 "Bisa ga
Dokarmu ba za mu iya hukunta mutum ba, sai an ji daga bakinsa,
don a san abin da yake yi."

7.37: L. Fir 23.36 **7.38:** Ez 47.1; Zak 14.8 **7.42:** 2 Sam 7.12; Mika 5.1
7.50: Yoh 3.1-2

[j] **7.37-38** Wani juyi na waɗannan ayoyin shi ne "Duk mai jin ƙishin ruwa yă zo wurina, kuma ɗuk wanda ya ba da gaskiya gare ni kuma yă sha. 38 Kamar yadda Maganar Allah ta ce 'rafuffukan ruwa mai ba da rai za su fiffito daga zuciyarsa.' "

52 Sai suka amsa masa suka ce, "Kai ma mutumin Galili ne? Ka bincika Maganar Allah ka gani mana, ai, ba wani annabin da zai zo daga Galili."

Macen da Aka Kama a Zina

53 Sai kowa ya tafi gida.

8 1 Amma Yesu ya tafi Dutsen Itatuwan Zaitun. 2 Da sassafe kuma Yesu ya sāke shiga haikali. Dukan mutane suka zo wurinsa, ya kuwa zauna yana koya musu. 3 Sai malaman dokoki da Farisiyawa suka kawo wata macen da aka kama ta tana yin zina. Suka sa ta tsaya a tsakiyarsu. 4 Sai suka ce wa Yesu, "Malam, macen nan an kama ta ne, tana cikin zina. 5 To, Dokar Musa ta umarce mu mu jejjefe irin waɗannan da duwatsu har su mutu. Kai kuwa me ka ce?" 6 Sun yi wannan tambaya ne don su gwada shi, domin dai su sami wani laifin da za su yi ƙararsa a kai.

Amma Yesu ya sunkuya, ya yi rubutu a ƙasa da yatsarsa. 7 Da suka dinga yi wa Yesu tambayoyi, sai ya ɗaga ya ce musu, "To, duk wanda bai taɓa yin zunubi a cikinku ba yă fara jifanta da dutse." 8 Sai Yesu ya sāke sunkuyawa, ya yi rubutu a ƙasa. 9 Da suka ji haka kuwa, suka fara tashi daga wurin ɗaya-ɗaya, tun daga babbansu zuwa ƙaraminsu, aka bar Yesu shi kaɗai, da macen a tsaye a gabansa. 10 Sai Yesu ya ɗaga, ya tambaye ta ya ce, "Uwargida ina suke? Ba wanda ya hukunta ki?"

11 Sai ta amsa ta ce, "Mai girma, babu kowa."

Sai Yesu ya ce, "Ni ma ban hukunta ki ba. Ki tafi, amma kada ki ƙara yin zunubi."[k]

Yesu Ne Hasken Duniya

12 Sai Yesu ya ƙara yi wa mutane magana ya ce, "Ni ne hasken duniya. Duk wanda yake bina ba zai yi tafiya a duhu ba, amma zai sami haske na rai."

13 Sai Farisiyawa suka ce wa Yesu, "Kana yi wa kanka shaida, shaidarka kuwa ba gaskiya ba ce."

14 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ko da ma na shaida kaina, ai, shaidata gaskiya ce, domin na san inda na fito, da kuma inda za ni. Amma ku ba ku san inda na fito ba, ko kuma inda za ni. 15 Ku kuna hukunci ne bisa ga ganin mutum. Ni kuwa ba na hukunta kowa. 16 Amma ko da ma zan yi hukunci, hukuncina na gaskiya ne, don ba ni ne kaɗai ba, amma Ubana da ya aiko ni yana tare

8.5: L. Fir 20.10; M. Sh 22.22-24 **8.12:** Mat 5.14; Yoh 9.5 **8.13:** Yoh 5.31

[k] **8.11** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da ayoyi 7.53-8.11.

da ni. 17 A cikin Dokarku an rubuta cewa, idan shaidu biyu sun faɗa abu iri ɗaya, to, dole ne a karɓi shaidarsu. 18 To, ni ina ba da shaida wa kaina, Uba kuma wanda ya aiko ni shi ne na biyun."

19 Sai suka tambaye shi suka ce, "Ina Uban nan naka yake?"

Yesu ya amsa musu ya ce, "Ba ku san ni ba, ba ku kuma san Ubana ba. Da kun san ni, da kun san Ubana ma."

20 Yesu ya faɗa wannan magana ne a lokacin da yake koyarwa kusa da inda ake ajiye kuɗin baiko a haikali. Amma duk da haka ba wanda ya kama shi, don lokacinsa bai yi ba tukuna.

Inda Za Ni ba Za Ku Iya Zuwa Ba

21 Sai Yesu ya ƙara gaya wa mutanen cewa, "Zan tafi, za ku kuwa neme ni, za ku kuma mutu cikin zunubinku. Inda za ni kuwa, ba za ku iya zuwa ba."

22 Wannan ya sa shugabannin Yahudawa suka ce, "Wato, zai kashe kansa ne da ya ce, 'Inda za ni kuwa, ba za ku iya zuwa ba'?"

23 Amma Yesu ya ci gaba da cewa, "Ku daga nan ƙasa kuke, ni kuwa na fito daga sama ne. Ku na duniyan nan ne, ni kuwa ba na duniyan nan ba ne. 24 Shi ya sa na ce muku za ku mutu cikin zunubanku. Domin in ba ku ba da gaskiya cewa Ni Ne shi wanda na gaya muku nake ba, za ku mutu cikin zunubanku."

25 Sai suka tambayi Yesu suka ce, "Kai wane ne?"

Yesu ya amsa musu ya ce, "Ni ne wannan da na faɗa muku tun daga farko.[ƙ] 26 Akwai abubuwa da yawa da zan iya faɗa gome da ku, in kuwa hukunta ku. Amma ina gaya wa mutane abubuwan da na ji daga shi wanda ya aiko ni ne kaɗai, kuma yana faɗin gaskiya ne."

27 Mutanen ba su gane cewa yana magana da su ne game da Uban ba. 28 Shi ya sa Yesu ya ce musu, "A lokacin da za ku ɗaga Dan Mutum, a lokacin nan ne za ku gane ni ne shi. Za ku gane cewa ba na yin kome da ikon kaina, amma ina faɗin abin da Uba ya koya mini ne kawai. 29 Wanda ya aiko ni kuwa yana tare da ni, bai bar ni ni kaɗai ba, gama kullum ina yin abin da yake so." 30 A lokacin da Yesu yake faɗin waɗannan abubuwa mutane da yawa suka gaskata da shi.

[ƙ] **8.25 Abin da na faɗa muku tun daga farko:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "Don me ma zan yi magana da ku."

'Yanci na Gaske

31 Sai Yesu ya ce wa Yahudawan nan da suka gaskata da shi,
"In dai kun ci gaba da riƙe koyarwata, ku almajiraina ne na gaske.
32 Sa'an nan za ku san gaskiya, gaskiyar kuwa za ta ba ku 'yanci."

33 Suka amsa masa suka ce, "Ai, mu zuriyar Ibrahim ne, ba
mu taɓa zama bawan kowa ba. To, me ya sa ka ce za mu sami
'yanci?"

34 Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Gaskiya, ina gaya muku,
duk mai yin zunubi bawan zunubi ne. 35 Ai, bawa ba ya zama a
gida har abada, amma ɗa na gida ne har abada. 36 Saboda haka
idan Ɗan ya 'yantar da ku za ku sami 'yanci na gaske. 37 Na san
dai ku zuriyar Ibrahim ne, amma kuna so ku kashe ni, domin ba
ku karɓi koyarwata ba. 38 Ina faɗa muku abin da na gani a gun
Ubana, amma ku kuna yin abin da kuka ji daga ubanku."

Shaiɗan Ne Ubanku

39 Suka amsa masa suka ce, "To, ai, Ibrahim ne babanmu."

Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "In da ku 'ya'yan Ibrahim ne,
da kun yi abubuwan da shi Ibrahim ya yi. 40 Ni mutum ne mai
faɗin gaskiya wadda na ji daga wurin Allah, amma kuna ƙoƙari
ku kashe ni. To, ai, Ibrahim bai yi irin wannan abu ba. 41 Saboda
haka kuna yin abin da ubanku yake yi ne."

Amma Yahudawan suka ce, "Mu ba shegu ba ne. Allah ne
Ubanmu, kuma shi ne kaɗai Uban da muke da shi."

42 Yesu ya ce musu, "Da a ce Allah ne Ubanku da kun
ƙaunace ni, domin daga wurin Allah na fito, yanzu ga ni a nan.
Ban zo da ikon kaina ba, Allah ne ya aiko ni. 43 Me ya sa ba ku
gane maganata ba? Don ba ku iya saurari koyarwata ba. 44 Ku na
ubanku Shaiɗan ne, kuma kuna so ku yi abin da yake so. Shi mai
kisa ne tun farko kuma ba ruwansa da gaskiya, domin babu
gaskiya a cikinsa. Duk lokacin da yake ƙarya yana nuna halinsa
ne, gama shi mai ƙarya ne, uban ƙarya kuma. 45 Amma domin
ina faɗin gaskiya, ba ku gaskata da ni ba. 46 Wane ne a cikinku
yana da shaida wadda ta nuna na taɓa yin zunubi? In kuwa
gaskiya nake faɗa, to, me ya sa ba ku gaskata ba? 47 Wanda yake
na Allah yakan saurari abin da Allah yake faɗa. Amma ku ba ku
saurari abin da Allah ya faɗa ba don ku ba na Allah ba ne."

8.33: Mat 3.9; Luk 3.8

Yesu Ya Fi Ibrahim

48 Yahudawa suka amsa masa suka ce, "Ashe, ba gaskiyarmu
ba kuwa, da muka ce kai mutumin Samariya ne wanda yake da
aljani?"
49 Yesu ya amsa ya ce, "Ni ba mai aljani ba ne. Ina girmama
Ubana ne, amma ku kuwa kuna yi mini wulaƙanci. 50 Ba ni nake
nema wa kaina ɗaukaka ba. Akwai wani wanda yake nema mini,
shi ne kuma mai yin hukunci. 51 Hakika, ina gaya muku, duk
wanda yake biyayya da koyarwata ba zai taɓa mutuwa ba sam."
52 Sai Yahudawan suka ce masa, "To, yanzu kam, mun
tabbata kana da aljani. Ai, Ibrahim da annabawa sun mutu, amma
kai ka ce, 'Duk wanda yake biyayya da koyarwata ba zai taɓa
mutuwa ba sam.' 53 Kana tsammani ka fi babanmu Ibrahim ne?
Shi kuwa ya mutu, haka nan ma annabawa sun mutu. Kana
tsammani kai wane ne?"
54 Yesu ya amsa musu ya ce, "Idan na ɗaukaka kaina, wannan
ɗaukaka ba a bakin kome take ba. Wanda yake ɗaukaka ni shi
ne Ubana, wanda kuke cewa wai shi ne Allahnku. 55 Ku ba ku
san shi ba, amma ni na san shi. Da a ce na ce muku ban san shi
ba, da na zama mai ƙarya kamarku. Amma na san shi, ina kuma
biyayya da abin da yake faɗa. 56 Babanku Ibrahim ya yi farin ciki
sosai don dai yă sami ganin zamanina, ya kuwa gan shi, ya kuma
yi murna."
57 Sai Yahudawa suka ce wa Yesu, "Ga shi, har yanzu ba ka
ma kai shekara hamsin ba tukuna, kuma kana cewa ka ga
Ibrahim?"[1]
58 Yesu ya ce musu, "Gaskiya, ina gaya muku, tun ba a haifi
Ibrahim ba, ina nan." 59 Da Yesu ya faɗa wannan magana sai suka
ɗebo duwatsu don su jejjefe shi. Amma Yesu ya ɓoye, ya fita ya
bar haikalin.

Yesu Ya Warkar da wanda Aka Haifa Makaho

9 1 Yesu yana wucewa ke nan, sai ya ga wani mutum wanda
tun haihuwarsa makaho ne. 2 Sai almajiransa suka tambaye
shi suka ce, "Malam, zunubin wane ne ya sa an haifi wannan
mutum makaho? Zunubinsa ne, ko zunubin iyayensa?"
3 Yesu ya amsa ya ce, "Ba wai domin mutumin nan ko
iyayensa sun yi zunubi ba ne, amma an haife shi makaho ne,
domin a nuna ikon Allah a kansa. 4 Dole ne mu ci gaba da aikin

[1] **8.57 kana cewa ka ga Ibrahim:** Wani juyi na waɗannan kalmomin
shi ne "Kana cewa Ibrahim ya gan ka?"

wanda ya aiko ni tun rana tana nan. Ai, dare yana nan zuwa, a
lokacin da ba wanda zai iya aiki. 5 Muddin ina nan a duniya, ni
ne hasken duniya."

6 Da ya faɗa haka sai ya tofa miyau a ƙasa, ya kwaɓa ƙasa
da shi, sai ya ɗebi ƙasan nan da ya kwaɓa, ya shafa a idanun
mutumin. 7 Ya ce wa mutumin, "Je ka, ka wanke ido a ruwan
tafkin Siluwam." (Wannan kalma kuwa tana nufin "Aika".) Sai
mutumin ya je ya wanke ido, ya dawo idanunsa suna gani.

8 Abokan zamansa da waɗanda suka saba ganinsa yana bara
a dā, suka ce, "Ashe, ba wannan ne yakan zauna yana bara ba?"
9 Waɗansu suka ce, "Shi ne mana."

Waɗansu kuwa suka ce, "A'a, sun dai yi kama ne kawai."

Amma mutumin da kansa ya ce, "Ai, ni ne mutumin."

10 Sai suka tambaye shi suka ce, "To, yaya aka yi idanunka
suka buɗe?"

11 Ya amsa ya ce, "Mutumin nan da ake ce da shi Yesu ne
ya kwaɓa ƙasa ya shafa mini a idanu, ya ce mini, 'Je ka ka wanke
ido a ruwan Siluwam.' Na kuwa je na wanke, sai na sami gani."

12 Suka tambaye shi suka ce, "Ina wannan mutumin yake?"

Sai ya ce, "Ban sani ba."

Farisiyawa Sun Yi Bincike a kan Warkawar Makahon

13 Sai mutanen suka kai wa Farisiyawa mutumin da yake
makaho a dā. 14 To, a Ranar Hutun Yahudawa ne Yesu ya kwaɓa
ƙasa ya buɗe wa mutumin ido. 15 Saboda haka Farisiyawa suka
tambaye shi yadda aka yi ya sami gani. Sai mutumin ya ce, "Ya
kwaɓa ƙasa ne ya shafa mini a idona, na wanke, yanzu ina gani."

16 Waɗansu Farisiyawa suka ce, "Mutumin nan ba daga wurin
Allah ya fito ba, don ba ya kiyaye Ranar Hutu."

Amma waɗansu suka yi tambaya suka ce, "Yaya mutum mai
zunubi zai iya yin abubuwan ban mamaki haka?" Sai ra'ayinsu
ya rabu.

17 Sai suka sāke tambayi mutumin suka ce, "Mene ne
ra'ayinka game da wannan mutum, tun da yake kai ne ya buɗe
maka ido?"

Mutumin ya amsa musu ya ce, "Ai, annabi ne shi."

18 Shugabannin Yahudawan kam, ba su ba da gaskiya ba cewa
mutumin nan makaho ne a dā, kuma yanzu yana gani. Saboda
haka suka aika aka kira iyayensa. 19 Suka tambaye su suka ce,

9.5: Mat 5.14; Yoh 8.12

"Wannan ɗanku ne? Kun ce an haife shi makaho? To, ta yaya ya iya gani yanzu?"

20 Sai iyayen suka amsa suka ce, "Mun dai san wannan ɗanmu ne, kuma an haife shi makaho ne. 21 Amma mu kam, ba mu san yadda aka yi yana gani yanzu ba, ba mu ma san wanda ya buɗe masa ido ba. Ku tambaye shi, ai, shi ba yaro ba ne, zai faɗa da bakinsa." 22 Iyayensa sun faɗa haka ne don tsoron shugabannin Yahudawa, don dā ma sun shirya cewa duk wanda ya ce Yesu ne Almasihu, za a kore shi daga majami'a. 23 Shi ya sa iyayensa suka ce, "Ai, shi ba yaro ba ne, ku tambaye shi."

24 Sai Farisiyawan suka sāke kira mutumin nan da yake makaho a dā, suka ce masa, "Ka faɗa gaskiya don ka ɗaukaka Allah. Mu kam, mun san mutumin nan da ya warkar da kai mai zunubi ne." 25 Sai ya amsa ya ce, "Ko mai zunubi ne, ni ban sani ba. Abu ɗaya kam na sani, dā ni makaho ne, yanzu kuwa ina gani."

26 Suka tambaye shi kuma suka ce, "Me ya yi maka? Ta yaya ya buɗe maka ido?"

27 Ya amsa musu ya ce, "Na riga na faɗa muku, ba ku ji ni ba ne. Don me kuke so ku sāke ji? Ko ku ma kuna so ku zama almajiransa ne?"

28 Sai suka zagi mutumin suka ce, "Kai ne dai almajirinsa, amma mu kam, almajiran Musa ne. 29 Mun dai san Allah ya yi magana da Musa, amma wannan mutum kam ba mu san inda ya fito ba."

30 Sai mutumin ya amsa musu ya ce, "Yau ga abin mamaki! Ba ku san inda ya fito ba, ga shi kuwa ya buɗe mini ido! 31 Mun sani Allah ba ya sauraron masu zunubi, amma yana sauraron duk wanda yake yi masa sujada, yana kuma yi masa biyayya. 32 Tun farkon duniya ba a taɓa jin wani ya buɗe idon wanda aka haifa makaho ba. 33 Ai, da mutumin nan ba daga wurin Allah ya fito ba, da ba zai iya yin kome ba."

34 Suka amsa masa suka ce, "Kai da aka haife ka cikin zunubi, kana koƙari ka koya mana ne?" Sai suka kore shi.

Makanta ta Ruhu

35 Yesu ya ji labari cewa sun kori mutumin. Da ya same shi, sai ya tambaye shi ya ce, "Ka ba da gaskiya ga Ɗan Allah?"

36 Mutumin ya amsa ya ce, "Mai girma, wane ne shi? Ka faɗa mini don in ba da gaskiya gare shi."

37 Yesu ya ce masa, "Ai, ka gan shi, shi ne ma mai magana da kai."

38 Sai mutumin ya ce, "Ubangiji, na ba da gaskiya." Ya kuma yi masa sujada.

39 Yesu ya ce, "Na shigo duniyan nan ne don in yi shari'a, domin waɗanda ba sa gani su sami gani, waɗanda suke gani kuma su zama makafi."

40 Da Farisiyawan da suke kusa da shi suka ji haka, sai suka ce masa, "Wato, kana ce mu ma makafi ke nan?"

41 Yesu ya ce musu, "Ai, da makafi ne ku, da ba ku da zunubi. Amma da yake kun ce kuna gani, to, zunubanku suna nan daram.

Misalin Mai Kiwo da Garken Tumakinsa

10 [1] "Hakika, ina gaya muku, duk wanda bai shiga garken tumaki ta ƙofa ba, amma ya haura ya shiga ciki ta wani gefe, to, shi ɓarawo ne, ɗan fashi ne kuma. [2] Wanda ya shiga ta ƙofar kuwa, shi ne makiyayin tumakin. [3] Mai gadin ƙofar yakan buɗe masa. Tumakin kuma sukan saurari muryar makiyayin. Yakan kira tumakinsa da sunayensu yă kai su waje. [4] Bayan ya fitar da dukan nasa waje, sai yă yi tafiya a gaba, tumakin kuma suna binsa a baya domin sun san muryarsa. [5] Ba za su bi baƙo ba, sai dai su guje shi, don ba su san muryar baƙo ba." [6] Yesu ya faɗa wa mutanen wannan misali, amma ba su gane abin da yake faɗa musu ba.

Yesu Ne Makiyayi Mai Kyau

7 Don haka Yesu ya sāke ce musu, "Hakika, ina gaya muku, ni ne ƙofar tumakin. [8] Duk waɗanda suka zo kafin ni ɓarayi ne da 'yan fashi, kuma tumakin ma ba su ji su ba. [9] Ni ne ƙofar, wanda ya shiga ta wurina zai sami ceto, zai shiga yă kuma fita yana kiwo. [10] Ɓarawo yakan zo ne kawai don sata, da kisa, da kuma halakarwa. Amma na zo ne domin su sami rai, su kuma same shi cikakke.

11 "Ni ne makiyayi mai kyau. Makiyayi mai kyau kuwa shi ne yakan ba da ransa domin tumakin. [12] Dan hayar da aka yi hayarsa don kiwo, shi ba makiyayi ba ne, tumakin kuma ba nasa ba ne. Saboda haka da ganin karen daji yana zuwa da gudu sai yă bar tumakin, yă gudu. Karen dajin kuwa yă kama tumakin yă kuma warwatsar da su.

13 Mutumin ya gudu ne domin aikin kuɗi ne kawai yake yi, kuma ba abin da ya dame shi da tumakin.

Hoton makiyayi mai kyau (10.11)

14 "Ni ne makiyayi mai kyau. Na san nawa, nawa kuma sun
san ni, 15 kamar yadda dai na san Uba, Uban kuma ya san ni.
Ina kuma ba da raina domin tumakin. 16 Ina da wadansu tumaki
kuma da ba na wannan garke ba ne. Su ma dole ne in kawo su.
Za su kuwa saurari muryata, za su zama garke daya, makiyayi
daya kuma. 17 Abin da ya sa Uba yana kaunata ke nan, domin
ina ba da raina saboda in sake dauko shi kuma. 18 Ba mai kwace
mini rai, domin ni da kaina nake ba da shi. Ina da iko in ba da
shi, ina da iko in dauko shi kuma. Abin da Ubana ya umarce
ni in yi ke nan."

19 Saboda wannan maganar da Yesu ya yi, sai Yahudawa
suka shiga mahawara da juna kuma. 20 Da yawa daga cikinsu,
suka ce, "Ai, yana da aljani ne shi ya sa yake hauka. Don me
za ku saurare shi?"

21 Amma wadansu kuwa suka ce "A'a, ai, wannan magana
ba ta mai aljani ba ce. Ashe, aljani zai iya bude wa makaho ido?"

10.15: Mat 11.27; Luk 10.22



Hoton Barandan Solomon (10.23)

Yahudawa Sun Ki Yesu

22 Lokacin sanyi ne ana kuma Bikin Mikawar Haikali[m] a
Urushalima. 23 Yesu kuwa yana zagawa a barandan Solomon a
cikin haikali, 24 sai Yahudawa suka kewaye shi, suka ce masa,
"Har yaushe za ka bar mu cikin shakka? In dai kai ne Almasihun
ka gaya mana a fili."

25 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ai, na riga na gaya muku ba
ku ba da gaskiya ba. Abubuwan da nake yi a cikin sunan Ubana
su ne suke nuna kowane ne ni. 26 Amma ba ku ba da gaskiya ba,
domin ku ba tumakina ba ne. 27 Gama tumakina sukan yi biyayya
da abin da nake faɗa, na san su, suna bina kuma. 28 Ina ba su rai
na har abada, kuma ba za su taɓa mutuwa ba, kuma ba wanda
zai ƙwace su daga hannuna. 29 Ubana wanda ya ba ni tumakin ya
fi duka girma,[n] ba kuwa mai iya ƙwace tumakina daga hannunsa.
30 Da ni da Uban, ɗaya ne."

31 Sai Yahudawa suka sāke ɗebo duwatsu don su jejjefe shi.
32 Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Na yi muku abubuwa masu
kyau masu yawa kuma daga wurin Uba, a kan wanne a cikinsu
za ku jejjefe ni?"

---

[m] **10.22 Bikin Mikawar Haikali:** Dubi ma'anar wadansu kalmomi.

[n] **10.29 Ubana . . . ya fi duka girma:** Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "abin da Ubana ya ba ni ya fi duka girma" ne a nan.

33 Yahudawa suka amsa masa suka ce, "Ai, ba don wani aiki mai kyau da ka yi ne za mu jejjefe ka ba, amma don maganar reni ga Allah ne, kai da kake mutum kawai kana mai da kanka daidai da Allah."

34 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ai, a rubuce yake a Dokarku cewa Allah ya ce, 'Na ce ku alloli ne.' 35 Mun dai san cewa Rubutaccen Maganar Allah ba ya ƙarya, idan Ubangiji ya ce da waɗanda suka ji saƙonsa 'alloli', 36 to, ni da Uba ya tsarkake ya kuma aiko ni duniya, maganar reni ga Allah nake yi ke nan da na ce, 'Ni Ɗan Allah ne'? 37 In ba ayyukan da Ubana yake yi su nake yi ba, to, kada ku gaskata da ni. 38 Amma in su nake yi, ko ba ku gaskata da ni ba, ku gaskata da ayyukan, don ku sani, ku kuma gane cewa, Uban yana cikina, ni kuma ina cikin Uban."

39 Sai suka sāke yin ƙoƙarin kama Yesu, amma ya fita daga hannunsu.

40 Sa'an nan Yesu ya sāke komawa hayin Kogin Urdun wurin da Yohanna ya yi baftisma da farko, ya zauna a can. 41 Sai mutane da yawa suka zo wurinsa. Mutanen suka ƙira cewa, "Ai, Yohanna bai taɓa yin wani abin ban mamaki ba, amma duk abin da ya faɗa game da wannan mutum gaskiya ne." 42 A wannan wurin kuwa mutane da yawa suka ba da gaskiya ga Yesu.

Mutuwar Li'azaru

11 1 Akwai wani mutum mai suna Li'azaru wanda ya yi rashin lafiya a ƙauyen Betani. Betani kuwa ƙauyen su Maryamu ne da 'yar'uwarta Marta. 2 Li'azaru wanda ba shi da lafiya ɗan'uwan Maryamu ne. Ita ce ta shafa wa Ubangiji man ƙamshi ta kuma share ƙafafunsa da gashinta. 3 To, 'yan'uwan nan mata suka aika wa Yesu, suka ce, "Ubangiji, ga shi, wanda kake ƙaunan nan ba shi da lafiya."

4 Da Yesu ya ji haka sai ya ce, "Wannan rashin lafiya ba zai kai shi mutuwa ba, amma zai kawo ɗaukaka ne ga Allah da kuma Dansa." 5 Gama Yesu ya ƙaunaci Marta da 'yar'uwarta, da kuma Li'azaru. 6 Amma duk da haka da ya sami labari cewa Li'azaru ba shi da lafiya, ya ƙara zama kwana biyu a wurin da yake.

7 Bayan haka ya ce wa almajiran, "Mu koma Yahudiya."

8 Almajiran suka ce masa, "Malam, kwana-kwanan nan fa Yahudawa suka nema su jejjefe ka, kuma za ka sāke komawa can?"

10.33: L. Fir 24.16 **10.34**: Zab 82.6 **10.40**: Yoh 1.28 **11.1**: Luk 10.38-39 **11.2**: Yoh 12.3

9 Yesu ya amsa ya ce, "Ba awa goma sha biyu ne yini guda
ba? To, duk wanda yake tafiya da rana ba ya tuntuɓe, don yana
ganin hasken duniyan nan. 10 Amma duk wanda yake tafiya da
dare yakan yi tuntuɓe don babu haske a wurinsa!"
11 Bayan da Yesu ya faɗa waɗannan abubuwa, ya ƙara ce
musu, "Abokinmu Li'azaru ya yi barci, amma za ni in tashe shi
daga barcin."
12 Sai almajiran suka ce masa, "Ubangiji, in dai barci ya
ɗauke shi, ai, zai warke." 13 Yesu yana nufin Li'azaru ya mutu
ne, amma su almajiransa suna tsammani yana barcin hutawa ne.
14 Sai Yesu ya gaya musu a fili ya ce, "Li'azaru ya mutu.
15 Ina kuma farin ciki saboda ku da ba na wurin domin ku ba da
gaskiya. Amma mu dai tafi wurinsa."
16 Sai Toma, wanda ake ce da shi 'Yan Biyu, ya ce wa
'yan'uwansa almajirai, "Mu ma mu tafi, mu mutu tare da shi."

Yesu Ne Tashin Matattu da kuma Rai

17 Da Yesu ya kai wurin, ya ji cewa, Li'azaru ya mutu har
an yi kwana huɗu da binne shi a kabari. 18 Betani kuwa kusa da
Urushalima yake, bai kai kilomita uku ba. 19 Yahudawa da yawa
suka zo su yi wa Marta da Maryamu ta'aziyyar ɗan'uwansu.
20 Da Marta ta ji cewa Yesu yana zuwa, sai ta je yin masa
maraba. Maryamu kuwa ta zauna a gida.
21 Sai Marta ta ce wa Yesu, "Ubangiji, ai, da kana nan da
ɗan'uwana bai mutu ba. 22 Ko yanzu ma na sani Allah zai ba ka
duk abin da ka roƙe shi."
23 Yesu ya ce mata, "Dan'uwanki zai tashi."
24 Marta ta ce masa, "Na sani zai rayu kuma a tashin matattu
a ranar ƙarshe."
25 Sai Yesu ya ce mata, "Ai, ni ne tashin matattu, ni ne kuma
rai. Wanda yake ba da gaskiya gare ni, ko ya mutu zai rayu.
26 Wanda yake a raye, yake kuwa gaskata da ni, ba zai mutu ba
har abada. Kin gaskata da wannan?"
27 Sai Marta ta amsa ta ce, "I, ya Ubangiji, na ba da gaskiya
cewa kai ne Almasihun nan, Ɗan Allah wanda yake zuwa
duniya."

Yesu Ya Yi Kuka

28 Da ta faɗa haka, sai ta je ta kirawo 'yar'uwarta Maryamu,
ta ce, "Malam ya zo, kuma yana kiranki." 29 Da jin haka,
Maryamu ta yi maza-maza ta tashi ta tafi wurin Yesu. 30 To, Yesu

dai bai riga ya shiga cikin ƙauyen ba tukuna. Har yanzu yana wurin da Marta ta yi masa maraba. 31 Da Yahudawan da suke tare da Maryamu a cikin gida suna mata ta'aziyya suka ga ta tashi da sauri ta fita, sai suka bi ta suna tsammani za ta kabarin ne, ta yi kuka a can.

32 Da Maryamu ta kai inda Yesu yake, ta gan shi, sai ta fāɗi a gabansa, ta ce masa, "Ubangiji, ai, da kana nan da ɗan'uwana bai mutu ba."

33 Da Yesu ya ga tana kuka, Yahudawan da suka zo tare da ita su ma suna kuka, sai abin ya dami Yesu a zuciya sosai. 34 Sai ya ce, "Ina ne kuka binne shi?"

Suka ce masa, "Ubangiji, zo ka gani."

35 Sai Yesu ya yi hawaye. 36 Don haka Yahudawa suka ce, "Dubi yadda yake ƙaunarsa!"

37 Amma waɗansu daga cikinsu suka ce wa junansu, "Ya buɗe idanun makahon can. To, me ya sa bai yi wani abu wanda zai hana wannan mutum mutuwa ba?"

Yesu Ya Ta da Li'azaru daga Matattu

38 Da Yesu ya sāke damuwa a ransa sosai, ya tafi kabarin. Kabarin kuwa kogon dutse ne, da wani dutse aka rufe bakin. 39 Sai Yesu ya ce, "Ku ture dutsen."

Amma Marta 'yar'uwar mutumin da ya mutu ta ce wa Yesu, "Ubangiji, ai, yanzu zai yi wari, don yau kwanansa huɗu ke nan da mutuwa."

40 Sai Yesu ya ce mata, "Ba na riga na gaya miki cewa idan kin ba da gaskiya za ki ga ɗaukakar Allah ba?"

41 Sai suka ture dutsen. Yesu kuwa ya ɗaga kai sama ya ce, "Ya Uba, na gode maka da ka saurare ni. 42 Ko dā ma na sani kullum kana saurare ni, amma na faɗa haka ne don mutanen da suke tsaye a nan su ba da gaskiya kai ne ka aiko ni."

43 Da ya faɗa haka sai ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, "Li'azaru, fito!" 44 Sai mutumin da ya mutu ɗin ya fito, ƙafa da hannu a ɗaure da guntayen yadi, fuskarsa kuma a naɗe da ƙyallen zanen da aka binne shi da shi.

Sai Yesu ya ce musu, "Ku kunce shi, yă tafi."

An Yi wa Yesu Mugun Shiri

(Mat 26.1-5; Mar 14.1-2; Luk 22.1-2)

45 Saboda haka Yahudawa da yawa da suka zo ziyarar Maryamu suka ga abin da Yesu ya yi, suka ba da gaskiya gare

shi. 46 Amma waɗansunsu suka tafi wurin Farisiyawa, suka gaya musu abin da Yesu ya yi. 47 Don haka manyan firistoci da Farisiyawa suka tara 'yan Majalisa. Suka tambayi juna suka ce, "Me muke yi ne? Ga wannan mutumin yana yin abubuwan ban mamaki da yawa! 48 In fa muka ƙyale shi yana yin abubuwan nan, dukan mutane za su ba da gaskiya gare shi. Sa'an nan Romawa kuma za su zo su ƙwace ƙasarmu da kuma haikalinmu!"

49 Amma ɗayansu mai suna Kayafa wanda ya kasance babban firist a wannan shekara, ya ce musu, "Ku dai ba ku san kome ba sam! 50 Ba ku lura ba, ai, ya fi sauƙi mutum ɗaya yă mutu saboda mutane, da a ce dukan ƙasar ta halaka." 51 Wannan maganar da Kayafa ya yi ba tunanin kansa ba ne, amma da yake shi ne babban firist a wannan shekarar, ya yi annabci cewa Yesu zai mutu saboda mutanen Yahudawa, 52 ba ma saboda Yahudawa kaɗai ba, amma don ya tattaro 'ya'yan Allah waɗanda suka bazu ko'ina su zama ɗaya.

53 Tun daga wannan rana suka yi shawara yadda za su kashe Yesu. 54 Saboda haka Yesu bai ƙara tafiya cikin Yahudawa a fili ba, amma ya bar wurin, ya tafi ƙasar da take kusa da daji, ya shiga wani gari mai suna Ifraimu. A nan ne ya zauna da almajiransa.

55 Da Bikin Ketarewa na Yahudawa ya yi kusa, mutane da yawa daga ƙauye suka tafi Urushalima don su tsarkake kansu kafin bikin. 56 Suka yi ta neman Yesu, suna tsaitsaye a haikali suna tambayar juna, suna cewa, "Me kuka gani? Zai zo bikin kuwa?" 57 Domin dā ma manyan firistoci da Farisiyawa sun riga sun ba da doka cewa, duk wanda ya san inda Yesu yake, yă zo yă faɗa don su kama shi.

An Shafa wa Yesu Man Kamshi a Betani

(Mat 26.6-13; Mar 14.3-9)

12 1 Bikin Ketarewa ya rage sauran kwana shida ke nan, sai Yesu ya je Betani, wato, inda Li'azaru, mutumin da Yesu ya ta da shi daga matattu yake da zama. 2 Nan aka yi masa abincin dare, Marta ce kuwa ta raba abincin, Li'azaru kuwa yana ɗaya daga cikin mutanen da suka ci abincin tare da Yesu. 3 Sai Maryamu ta ɗauki kwalabar man ƙamshi mai tsada wanda aka yi shi da nardi, ta shafa a ƙafafun Yesu, sa'an nan ta shafe ƙafafun da gashin kanta. Kamshi mai daɗi na wannan man ya cika dukan gidan. 4 Amma Yahuda Iskariyoti, ɗaya daga cikin almajiransa,

12.3: Luk 7.37-38

wato, wanda zai bashe shi, ya ce, 5"Me ya sa ba a sayar da man
nan a kan yawan kudîn da lebura zai samu a ranaku ɗari uku,
sa'an nan a ba talakawa kudîn ba?" 6Yahuda ya faɗa wannan
magana ne ba domin yana kula da talakawa ba, amma domin shi
ɓarawo ne. Gama shi ne mai riƙe jakar kudînsu, kuma yakan sata
daga ciki.

7 Sai Yesu ya ce, "Kyale ta, ta ajiye shi domin shirin ranar
da za a binne ni. 8Ai, kullum kuna tare da talakawa, amma ba
kullum kuke tare da ni ba."

An Yi wa Li'azaru Mugun Shiri

9 Da taron Yahudawa mai yawa suka ji labari cewa Yesu yana
a nan, sai suka zo, ba don Yesu shi kaɗai ba, amma don su ga
Li'azaru ma wanda Yesu ya tashe shi daga matattu. 10Sai manyan
firistoci suka yi shawara su kashe Li'azaru shi ma, 11domin ta
dalilin Li'azaru ne Yahudawa da yawa suna rabuwa da firistocin
suna ba da gaskiya ga Yesu.

Yesu Ya Shiga Urushalima

(Mat 21.1-11; Mar 11.1-11; Luk 19.28-40)

12 Washegari mutane da yawa waɗanda suka zo Bikin
Ketarewa, suka ji cewa Yesu yana kan hanya zuwa Urushalima.
13Sai suka ɗaɗɗauki rassan itatuwan dabino suka fiffita, suka
karɓe shi, suna ta da murya suna cewa,

"Yabo ya tabbata ga Allah!
Albarka ta tabbata ga mai zuwa a cikin sunan Ubangiji,
Albarka ta tabbata ga Sarkin Isra'ila!"

14Da Yesu ya sami wani ɗan jaki sai ya hau,
kamar yadda aka rubuta cewa,

15"Kada ku ji tsoro, ya ku mutanen Urushalima,
Ga Sarkinku yana zuwa a kan ɗan jaki!"

16 Da farko almajiransa ba su gane abin nan ba, amma bayan
da aka ɗaukaka Yesu, suka tuna cewa an yi wannan rubutun a
kansa, kuma abubuwan sun faru daidai kamar yadda aka rubuta.

17 Mutanen da suke tare da shi a lokacin da ya kira Li'azaru
yă fito daga kabari, ya kuma tashe shi daga matattu, suka yi ta
faɗa wa mutane abin da Yesu ya yi. 18Mutane da yawa sun je
karɓen Yesu ne domin sun ji wannan abin ban mamakin da ya
yi. 19Sai Farisiyawa suka yi magana da juna suka ce, "Ku duba
fa, ba ma cin nasara ko kaɗan, ga shi dukan duniya tana binsa!"

12.8: M. Sh 15.11 **12.13:** Zab 118.25-26 **12.15:** Zak 9.9

Wadansu Helenawa Sun Nemi Yesu

20 To, a cikin wadanda suka zo bikin domin yin sujada akwai wadansu Helenawa. 21 Sai suka zo wurin Filibus, mutumin Betsaida ta Galili, suka ce masa, "Mai girma, muna bukata mu tattauna da Yesu." 22 Filibus ya je ya gaya wa Andarawus, sai su biyu suka tafi suka fada wa Yesu.

23 Sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Lokaci ya yi da za a daukaka Dan Mutum. 24 Hakika, ina gaya muku, in ba dai an binne kwayar alkama ta mutu ba, za ta zauna ita kadai. Amma in ta mutu sai ta ba da 'ya'ya da yawa. 25 Wanda yake kaunar ransa zai rasa shi. Wanda kuwa ya ki ransa a duniyan nan yana ajiyarsa ke nan zuwa ga rai na har abada. 26 Duk wanda yake bauta mini, dole yă bi ni. A duk inda nake bawana zai kasance tare da ni. Ubana kuwa zai girmama duk wanda yake bauta mini."

Yesu Ya Yi Magana game da Mutuwarsa

27 "Yanzu ina jin nauyi a raina. Me zan ce ke nan? In ce, 'Ya Uba, ka dauke mini wannan lokaci?' A'a, ai, dā ma na zo musamman domin wannan lokaci ne. 28 Ya Uba, ka daukaka sunanka."

Sai murya ta fito daga sama ta ce, "Ai, na riga na daukaka shi, zan kara daukaka shi kuma." 29 Da mutanen da suke tsaye a wurin suka ji muryar, suka ce, "An yi tsawa." Wadansu kuwa suka ce, "Mala'ika ne ya yi masa magana."

30 Yesu ya ce musu, "Wannan murya ta zo dominku ne, amma ba saboda ni ba. 31 Yanzu ne za a yi wa duniyan nan shari'a, yanzu ne kuma za a tumbuke mai mulkin duniyan nan. 32 Bayan an daga ni daga kasa kuwa, zan jawo dukan mutane zuwa wurina." 33 Yesu ya fada wannan ne domin yă nuna irin mutuwar da zai yi.

34 Sai mutanen suka ce wa Yesu, "Ai, Dokarmu ta gaya mana cewa, Almasihun zai rayu har abada. To, yaya za ka ce lallai ne a daga Dan Mutum? Wane ne Dan Mutum din?"

35 Yesu ya ce musu, "Hasken yana tare da ku na dan karamin lokaci. Ku yi tafiya tun hasken yana tare da ku, kada duhu ya same ku. Mai tafiya cikin duhu bai san inda za shi ba. 36 Ku gaskata da hasken, tun kuna tare da shi, domin ku zama 'ya'yan haske."

12.25: Mat 10.39; 16.25; Mar 8.35; Luk 9.24; 17.33
12.34: Zab 110.4; Ish 9.6; Ez 37.25; Dan 7.14

Yahudawa Sun Ci gaba da Kin Ba da Gaskiya ga Yesu

Bayan da Yesu ya yi wannan magana, sai ya tafi ya ɓoye kansa daga gare su.

37 Ko da yake Yesu ya sha yin abubuwan ban mamaki da
yawa a gabansu, duk da haka ba su ba da gaskiya gare shi ba.
38 Wannan ya faru ne domin a cika abin da annabi Ishaya ya faɗa
cewa,

"Ya Ubangiji, wa ya gaskata jawabinmu,
Ga wa kuma aka bayyana ikon Ubangiji?"

39 Shi ya sa ba su iya ba da gaskiya ba,
Kamar yadda Ishaya ya kuma faɗa a wani wuri cewa,

40 "Ya mai da su makafi,
Ya kuma taurara zuciyarsu,
Don kada su gani da idanunsu,
su kuma gane a zuciya.
Har su juyo wurina in warkar da su."

41 Ishaya ya faɗa haka ne domin ya ga ɗaukakar Yesu, ya
kuma ba da labarinsa.

42 Duk da haka mutane da yawa sun ba da gaskiya ga Yesu,
har ma da yawa daga cikin shugabanninsu suka ba da gaskiya
gare shi. Amma don tsoron Farisiyawa ba su ce sun gaskata ba
don kada a kore su daga majami'a. 43 Gama sun fi son yabo daga
bakin mutane fiye da yabo daga wurin Allah.

Maganar Yesu Za Ta Yi Hukunci

44 Sai Yesu ya ɗaga murya ya ce, "Duk wanda yake ba da
gaskiya gare ni, ba gare ni yake ba da gaskiya ba, amma ga wanda
ya aiko ni ne . 45 Duk wanda yake dubana, yana ganin wanda ya
aiko ni ne. 46 Na zo kamar haske ne a cikin duniya domin kada
duk wanda yake ba da gaskiya gare ni yă zauna a cikin duhu.

47 "Duk wanda ya ji koyarwata, bai kuwa kiyaye ta ba, ba ni
ne mai yin masa hukunci ba. Gama ba don in yi wa duniya
hukunci na zo ba, amma domin in ceci duniya ne. 48 Wanda ya
ƙi ni, bai kuma karɓi maganata ba, yana da mai yin masa hukunci,
maganar da na faɗa, ita za ta hukunta shi a ranar ƙarshe.
49 Abubuwan da nake koyarwa ba daga wurina ba ne, Ubana da
ya aiko ni ne ya gaya mini abin da zan faɗa da maganar da zan
yi. 50 Na kuma san rai na har abada yana samuwa ne daga umarnin

12.38: Ish 53.1 12.40: Ish 6.10

da Uba ya bayar. Saboda haka duk abin da na faɗa, na faɗa daidai abin da Uba ya gaya mini in faɗa ne."

Yesu Ya Wanke Kafafun Almajiransa

13 [1] Ana nan tun kafin Bikin Ketarewa yă yi, Yesu kuwa ya riga ya sani cewa lokacinsa ya yi da zai bar wannan duniya yă koma wurin Uba. Gama Yesu ya ƙaunaci mutanensa da suke a duniya, ya kuma nuna musu ƙaunarsa har zuwa ƙarshe.

2 A lokacin da Yesu da almajiransa suke cin abincin dare, Shaiɗan kuwa ya riga ya sa a zuciyar Yahuda Iskariyoti ɗan Siman yă ci amanar Yesu. [3] Yesu kuma ya san cewa Uban ya sa dukan kome a hannunsa, ya kuma sani daga wurin Allah ya fito, wurin Allah kuma zai koma. [4] Lokacin da suke cin abincin, Yesu ya tashi ya tuɓe rigarsa ta waje, ya ɗauko tawul ya ɗaura kewaye da jikinsa. [5] Sa'an nan ya zuba ruwa a kwano, ya fara wanke ƙafafun almajiran, yana share ƙafafunsu da tawul da ya ɗaura kewaye da jikinsa. [6] Sai Yesu ya zo wurin Bitrus. Bitrus kuwa ya ce masa, "Ya Ubangiji, kai ne za ka wanke mini ƙafa?"

7 Yesu ya amsa masa ya ce, "Yanzu kam, ba ka san abin da nake yi ba, amma daga baya za ka gane."

8 Sai Bitrus ya ce masa, "Sam! Ba za ka taɓa wanke mini ƙafa ba."

Yesu ya amsa masa ya ce, "To, in ban wanke maka ba, ba ka da rabo a wurina."

9 Bitrus ya ce masa, "Ya Ubangiji, ba ma ƙafafuna kaɗai za ka wanke ba, amma ka wanke har da hannuwana da kaina ma."

10 Sai Yesu ya ce, "Bayan da mutum ya yi wanka, jikinsa ya tsarkake ke nan. Ba ya bukata wanka kuma sai dai yă wanke ƙafafunsa kawai. Gama ku tsarkaka ne, amma ba dukanku ba." [11] Don Yesu ya san wanda zai bashe shi, shi ya sa ya ce, "Ba dukanku ne tsarkaka ba."

12 Bayan da ya wanke ƙafafunsu, ya sa rigarsa, sai ya koma wajen zamansa ya zauna. Sai ya tambaye su ya ce, "Kun gane abin da na yi muku? [13] Kuna ce da ni Malam, da kuma Ubangiji. Daidai ne kuwa, don haka nake. [14] Tun da yake ni da nake Ubangijinku da Malaminku na wanke muku ƙafa, ashe, ku ma ya kamata ku wanke wa juna. [15] Gama na nuna muku misali ne domin ku ma ku yi yadda na yi muku. [16] Hakika, ina gaya muku, bawa ba ya fin maigidansa, ɗan aika kuma ba ya fin wanda ya

---

13.12-15: Luk 22.27

aike shi. 17 Yanzu da kun san waɗannan abubuwa za ku zama masu albarka idan kun yi su.

18 "Ba a kanku duka nake magana ba. Na san waɗanda na zaɓa. Amma dole a cika abin da aka rubuta a Maganar Allah cewa, 'Wanda yake cin abincina ya tayar mini.' 19 Ina gaya muku wannan ne yanzu kafin yă faru, domin lokacin da ya faru ku ba da gaskiya cewa ni ne shi. 20 Hakika, ina gaya muku, wanda ya karɓi duk wanda na aika da zuciya ɗaya, ya karɓe ni ne. Wanda kuma ya karɓe ni da zuciya ɗaya, ya karɓi wanda ya aiko ni ne."

Yesu Ya Ce Za a Ci Amanarsa

(Mat 26.20-25; Mar 14.17-21; Luk 22.21-23)

21 Bayan Yesu ya yi wannan magana, abin ya dame shi sosai a zuciya. Sai ya faɗa a fili cewa, "Gaskiya, ina gaya muku, ɗayanku zai bashe ni."

22 Sai almajiransa suka duddubi juna, don ba su san almajirin da Yesu yake magana a kansa ba. 23 Wani daga cikin almajiransa kuwa, wanda Yesu yake ƙauna, yana zaune kurkusa da Yesu. 24 Sai Bitrus ya yi masa magana da alamar hannu cewa yă tambayi Yesu yă gaya musu wanda yake magana a kansa.

25 Sai almajirin nan ya matso kusa da Yesu ya tambaye shi ya ce, "Wane ne shi Ubangiji?"

26 Sai Yesu ya amsa ya ce, "Zan tsoma gutsurin burodin nan a kwano. Wanda na ba shi, shi ne mutumin." Da Yesu ya ɗauki gutsurin burodin ya tsoma, sai ya ba Yahuda ɗan Siman Iskariyoti. 27 Da ya karɓi gutsurin burodin sai Shaiɗan ya shiga cikinsa nan da nan. Sai Yesu ya ce wa Yahuda, "Abin nan da za ka yi, ka yi shi da sauri." 28 Amma cikin waɗanda suke cin abincin, ba wanda ya san dalilin da ya sa Yesu ya faɗa masa haka. 29 Tun da Yahuda ne yake riƙe da jakar kuɗinsu, sai waɗansu daga cikin almajiran suka yi tsammani Yesu yana faɗa masa yă sayo abin da ake bukata a bikin ne, ko kuma ya ba talakawa wani abu. 30 Shi kuwa da ya karɓi gutsurin burodin, sai ya fita. A lokacin kuwa dare ya yi.

Sabon Umarni

31 Bayan da Yahuda ya fita, Yesu ya ce, "Yanzu ne aka ɗaukaka Ɗan Mutum, aka kuma ɗaukaka Allah ta wurinsa. 32 Idan Allah ya karɓi ɗaukaka ta wurinsa, to, Allah zai ba Ɗan ɗaukaka ta wurin kansa, nan da nan kuwa zai sami ɗaukaka.

13.16: Mat 10.24; Luk 6.40; Yoh 15.20 **13.28:** Zab 41.9

33 "Ya ku 'ya'yana ƙanana, saura ɗan lokaci kaɗan ina tare da ku. Za ku neme ni, amma kamar yadda na faɗa wa Yahudawa cewa, 'Inda za ni ba za ku iya zuwa ba,' haka nake faɗa muku yanzu.

34 "Sabon umarni nake ba ku, ku ƙaunaci juna. Kamar yadda na ƙaunace ku, haka ku ma ku ƙaunaci juna. 35 Ta haka kowa zai sani ku almajiraina ne, in dai kuna ƙaunar juna."

Bitrus Zai Yi Mūsun Sanin Yesu
(Mat 26.31-35; Mar 14.27-31; Luk 22.31-34)

36 Siman Bitrus ya tambayi Yesu ya ce, "Ya Ubangiji ina za ka?"

Yesu ya amsa ya ce, "Inda za ni ba za ka iya bina yanzu ba, amma daga baya za ka bi ni."

37 Sai Bitrus ya ce masa, "Ya Ubangiji, me ya sa ba zan iya binka a yanzu ba? Ai, zan ba da raina saboda kai."

38 Yesu ya amsa ya ce, "Ashe, za ka ba da ranka saboda ni? Hakika, ina gaya maka, kafin zakara yă yi cara, za ka yi mūsun sanina sau uku."

Yesu Ne Hanya zuwa wurin Uba

14 1 "Kada ku damu. Ku ba da gaskiya ga Allah, ku kuma ba da gaskiya gare ni. 2 A cikin gidan Ubana akwai wurin zama da yawa. Idan ba haka ba ne da ba zan faɗa muku wannan ba. Za ni can domin in shirya muku wuri. 3 In kuwa na je na shirya muku wuri, zan dawo in kai ku wurina, domin ku ma ku zauna inda nake. 4 Ai, inda za ni kun san hanya."

5 Sai Toma ya ce wa Yesu, "Ya Ubangiji, ai, ba mu san inda za ka ba, yaya za mu san hanyar?"

6 Yesu ya ce masa, "Ni ne hanya, ni ne gaskiya, ni ne kuma rai. Ba mai zuwa wurin Uba sai ta wurina. 7 Da kun san ni, da kun san Ubana ma. Amma daga yanzu kun san shi, kun kuma gan shi."

8 Sai Filibus ya ce masa, "Ya Ubangiji, in ka nuna mana Uban, to, ai, bukatarmu ta biya ke nan."

9 Yesu ya ce masa, "Na daɗe tare da ku haka, amma har yanzu ba ka san ni ba, Filibus? Duk wanda ya gan ni, ai, ya ga Uban. Yaya za ka ce, 'Nuna mana Uban'? 10 Ba ka ba da gaskiya ba cewa ina cikin Uban, Uban kuma yana cikina? Ai, maganar da nake yi muku ba da ikon kaina ba ne, Uban ne da yake zaune a cikina yake yin ayyukansa. 11 Ku gaskata da ni da na ce ina cikin

Uban, Uban kuma yana cikina, ko kuwa ku gaskata da ni saboda
abubuwan ban mamakin da na yi. 12 Hakika, ina gaya muku, duk
wanda yake ba da gaskiya gare ni, zai yi ayyukan da nake yi.
Har ma zai yi ayyukan da suka fi waɗannan, domin zan tafi wurin
Uba. 13 Duk dai abin da kuka roƙa cikin sunana zan yi, domin
Uban yă sami ɗaukaka ta wurin Ɗan. 14 Komene ne kuka roƙa a
cikin sunana, zan yi shi."

Alkawarin Zuwan Ruhu Mai Tsarki

15 "In dai kuna mini ƙauna, za ku bi umarnina. 16 Zan kuma
roƙi Uba, shi kuwa zai ba ku wani Mai Taimako yă kasance tare
da ku har abada. 17 Shi ne Ruhu na gaskiya, wanda duniya ba ta
iya karɓe shi ba don ba ta iya ta gan shi ko ta san shi ba. Amma
ku kam kun san shi, don yana zama tare da ku, zai kuma kasance
a zuciyarku.

18 "Ba zan bar ku kamar marayu ba, zan zo wurinku. 19 Saura
ɗan lokaci kaɗan duniya ba za ta ƙara ganina ba, amma ku za
ku gan ni. Domin ni ina da rai, ku ma za ku rayu. 20 A ranan
nan ne fa za ku san cewa ni ina cikin Ubana, ku kuma a cikina,
ni kuma a cikinku. 21 Duk wanda ya san umarnaina, yana binsu
kuma, shi ne yake mini ƙauna. Wanda yake mini ƙauna kuwa,
Ubana zai ƙaunace shi, ni kuma zan ƙaunace shi in bayyana
kaina a gare shi."

22 Sai Yahuda (ba Iskariyoti ba) ya ce masa, "Ya Ubangiji,
me ya sa za ka bayyana kanka gare mu, amma ba ga sauran
duniya ba?" 23 Yesu ya amsa masa ya ce, "Duk wanda yake mini
ƙauna, zai kiyaye maganata, Ubana kuwa zai ƙaunace shi, za mu
zo wurinsa mu zauna tare da shi. 24 Wanda ba ya mini ƙauna
kuwa, ba ya kiyaye maganata. Maganar da kuke ji kuwa ba tawa
ba ce, ta Uba ce wanda ya aiko ni.

25 "Duk wannan na faɗa muku ne tun ina tare da ku. 26 Amma
Mai Taimako, wato, Ruhu Mai Tsarki, wanda Uba zai aiko cikin
sunana, shi ne zai koya muku kome, yă kuma tuna muku duk
abin da na faɗa muku.

27 "Na bar ku da salama. Salamata nake ba ku. Ba kamar
yadda duniya take bayarwa nake ba ku ba. Kada ku damu, kada
kuma ku ji tsoro.

28 "Kun dai ji na ce muku zan tafi, in sāke dawo wurinku
kuma. Da kuna mini ƙauna da kun yi murna saboda za ni wurin
Uba, gama Uban ya fi ni. 29 To, yanzu na faɗa muku tun bai faru
ba, domin a lokacin da ya faru ku ba da gaskiya. 30 Ba zan ƙara

Hoton itacen inabi (15.1)

yi muku magana mai yawa ba, domin mai mulkin duniyan nan
yana zuwa, amma ba shi da iko a kaina. 31 Ina yin daidai abin da
Uba ya faɗa mini in yi ne domin duniya ta sani ina ƙaunar Uban.
Ku tashi mu bar nan.

Yesu Ne Itacen Inabi na Kwarai

15 1 "Ni ne itacen inabi na ƙwarai, Ubana kuwa shi ne
manomin.
2 Kowane reshe a cikina da ba ya ba da 'ya'ya, sai yă yanke
shi. Kowane reshe mai yin 'ya'ya kuwa yakan ƙara gyara shi don
yă ƙara haihuwa. 3 Ko yanzu ma ku tsarkaka ne saboda maganar
da na faɗa muku. 4 Ku zauna a cikina, ni kuma a cikinku. Kamar
yadda reshen itacen inabi ba ya iya ba da 'ya'ya da kansa, sai ko
yă zauna a itacen inabin, haka ku ma ba za ku iya ba, sai kun
zauna a cikina.
5 "Ni ne itacen inabi, ku kuwa rassan. Wanda ya zauna a
cikina, ni kuma a cikinsa, shi ne mai yin 'ya'ya da yawa. Domin
in ba tare da ni ba, ba za ku iya yin kome ba. 6 Duk wanda bai
zauna a cikina ba, yana kama da reshen da aka jefar da shi yă
bushe. Mutane sukan tattara irinsu ne su jefa a wuta, a ƙone su.
7 In kun zauna a cikina, maganata kuma ta zauna a cikinku, za
ku roƙi duk abin da kuke so, za a kuwa yi muku. 8 Ku yi ayyukan
da Allah yake so don ku nuna cewa ku almajiraina ne, gama
wannan ne yake kawo ɗaukaka ga Ubana. 9 Kamar yadda Uba ya
ƙaunace ni, haka ni ma ina ƙaunarku. To, ku zauna a cikin ƙaunar

da nake nuna muku. 10 Ni na bi umarnin Ubana, na kuma zauna
a cikin ƙaunarsa. Haka ku kuma, in kun bi umarnina za ku zauna
a cikin ƙaunata.
11 "Na gaya muku haka domin farin cikina yă kasance a
cikinku, farin cikinku kuma yă zama cikakke. 12 Umarnina, shi
ne, ku ƙaunaci juna kamar yadda na ƙaunace ku. 13 Ba ƙaunar da
ta fi wannan, wato, mutum yă ba da ransa saboda abokansa. 14 Ku
abokaina ne in kun yi abin da na ce ku yi. 15 Ba zan ƙara ce da
ku bayi kuma ba, don bawa bai san abin da maigidansa yake yi
ba. Amma ina ce da ku abokai, domin na gaya muku dukan abin
da na ji daga wurin Ubana. 16 Ba ku kuka zaɓe ni ba, ni ne na
zaɓe ku, na sa ku ku je ku ba da 'ya'ya, 'ya'yan da za su
dawwama. Sa'an nan Uba zai ba ku dukan abin da kuka roƙa a
cikin sunana. 17 Umarnin da na ba ku shi ne ku ƙaunaci juna.

Kiyayyar Duniya

18 "Idan dai duniya ta ƙi ku, ku sani cewa ta ƙi ni kafin ta ƙi
ku. 19 Da ku na duniya ne da duniya ta so abinta, amma saboda
ku ba na duniya ba ne, na kuma zaɓe ku daga duniya, shi ya sa
duniya take ƙinku. 20 Ku tuna da abin da na faɗa muku cewa,
'Bawa ba ya fin maigidansa.' In sun tsananta mini, ku ma za su
tsananta muku. Da sun yi biyayya da maganata, da za su yi
biyayya da taku ku ma. 21 Za su yi muku dukan waɗannan ne
saboda sunana, don ba su san wanda ya aiko ni ba. 22 Da ba domin
na zo na yi musu magana ba, da ba su da zunubi. Amma yanzu
kam, ba su da wata hujja a kan zunubinsu. 23 Wanda ya ƙi ni ya
ƙi Ubana ma. 24 Na yi ayyuka da yawa a cikinsu waɗanda ba wani
da ya taɓa yi. Da a ce ban yi ayyukan nan ba, da ba su da zunubi.
Amma yanzu sun ga abin da na yi, amma duk da haka sun ƙi ni,
sun kuma ƙi Ubana. 25 Wannan ya faru ne kuwa domin a cika
maganar da take a rubuce a Dokarsu cewa, 'Sun ƙi ni ba dalili.'
26 "Zan sa Mai Taimako yă zo wurinku daga wurin Uba. Shi
ne Ruhu na gaskiya, mai fitowa daga wurin Uba, shi ne zai yi
shaida a kaina. 27 Ku ma shaidu ne, domin tun farko kuna tare
da ni.

16 1 "Na faɗa muku waɗannan abubuwa ne don kada ku ja
baya cikin bangaskiyarku. 2 Za a kore ku daga cikin
majami'u. Babu shakka lokaci yana zuwa da duk wanda ya kashe
ku zai yi tsammani yana yin aikin Allah ne. 3 Za su yi haka ne
kuwa don ba su riga sun san Uba ko ni ba. 4 Na faɗa muku

15.25: Zab 35.19, 69.4, 109.3.

wadannan abubuwa ne, domin in lokacinsu ya yi, ku tuna na fada muku.

Aikin Ruhu Mai Tsarki

"Ban fada muku abubuwan nan tun da farko ba domin ina tare da ku. 5 Amma yanzu kuwa zan tafi wurin wanda ya aiko ni, duk da haka a cikinku ba wanda ya tambaye ni, 'Ina za ka?' 6 Zukatanku sun cika da bakin ciki domin na fada muku wadannan abubuwa. 7 Amma, ina fada muku gaskiya, tafiyata ta fi muku amfani, domin Mai Taimakon nan ba zai zo ba sai bayan na tafi. Amma idan na tafi zan aiko muku da shi. 8 Lokacin da Mai Taimakon zai zo, zai nuna wa mutanen duniya cewa tunaninsu ba daidai ba ne a kan zunubi, da a kan adalci, da kuma a kan hukunci. 9 Ra'ayinsu a kan zunubi ba daidai ba ne domin sun ki su kafa bangaskiyarsu gare ni. 10 Tunaninsu ba daidai ba ne a kan adalci, domin za ni wurin Ubana, kuma ba za ku kara ganina ba. 11 Kuma tunaninsu ba daidai ba ne a kan hukunci, domin an riga an yanke wa mai mulkin wannan duniya hukunci.

12 "Ina da sauran abubuwa da yawa da zan gaya muku tukuna, amma ba za ku iya dauke su a yanzu ba. 13 Amma sa'ad da Ruhu na gaskiya ya zo, zai bishe ku cikin dukan gaskiya, domin ba maganar kansa zai yi ba, amma zai fada abin da yake ji ne kawai, zai kuma fada muku abubuwan da za su faru. 14 Zai daukaka ni, domin zai dauki abin da na fada ne yă gaya muku. 15 Duk abin da Uba yake da shi, nawa ne. Shi ya sa na ce Ruhun zai dauko abin da na fada ne yă gaya muku.

Bakin Ciki Zai Koma Farin Ciki

16 "Bayan dan lokaci kadan ba za ku gan ni ba, bayan dan lokaci kadan kuma za ku gan ni."

17 Sai wadansu almajiransa suka ce wa juna, "Me yake nufi da ya ce mana, 'Bayan dan lokaci kadan ba za ku gan ni ba, bayan dan lokaci kadan kuma za ku gan ni'? Kuma me yake nufi da ya ce, 'Domin za ni wurin Uba'?" 18 Suka ci gaba da cewa, "Me yake nufi da cewa, 'Bayan dan lokaci kadan'? To, ba mu san abin da yake nufi ba."

19 Yesu ya sani almajiransa suna so su tambaye shi a kan wannan magana, sai ya ce musu, "Wato, kuna tambayar juna ne abin da nake nufi da na ce, 'Bayan dan lokaci kadan ba za ku gan ni ba, bayan dan lokaci kadan kuma za ku gan ni'? 20 Hakika, ina gaya muku, za ku yi kuka da bakin ciki, amma duniya za ta

yi farin ciki. Za ku yi baƙin ciki, amma baƙin cikinku zai koma
farin ciki. 21 Idan mace za ta haihu takan ji zafi sosai, domin
lokacin haihuwarta ya yi. Amma idan ta gama haihuwar jariri,
takan mance da zafin da ta ji don tana cike da murna don an haifi
jariri a duniya. 22 Haka yake a gare ku. Yanzu kuna baƙin ciki,
amma zan sāke ganinku, sa'an nan za ku yi farin ciki, kuma ba
wanda zai ƙwace muku farin cikinku. 23 A ranan nan ba za ku
roƙe ni wani abu ba. Hakika, ina gaya muku, Uba zai ba ku duk
abin da kuka roƙa a cikin sunana. 24 Har yanzu dai ba ku roƙi ko
wani abu a cikin sunana ba. Ku roƙa, za ku samu, domin farin
cikinku yă zama cikakke."

Na Yi Nasara a kan Duniya

25 "Na yi amfani da misalai ne don in bayyana muku wannan.
Amma lokaci yana zuwa da zan yi magana da ku a fili game da
Uba, kuma ba zan ƙara moran misalai ba. 26 A ran nan za ku yi
roƙo cikin sunana. Za ku roƙi Uba da kanku ba ni ne zan roƙa a
madadinku ba, 27 domin shi Uban yana ƙaunarku da kansa, domin
kun ƙaunace ni, kun kuma ba da gaskiya cewa daga wurin Allah
na fito. 28 Daga wurin Uban ne na fito, na shigo duniya, yanzu
kuma zan bar duniya in koma wurin Uban."

29 Sai almajiransa suka ce, "Yawwa! Yanzu ne fa kake
magana a fili, ba da misalai ba! 30 Yanzu kam mun gane cewa ka
san dukan kome. Ka iya ba da amsa kafin wani yă yi maka
tambaya. Wannan ya sa mun ba da gaskiya cewa daga wurin
Allah ne ka fito."

31 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ashe! Yanzu kun ba da
gaskiya? 32 To, lokaci yana zuwa, har ma ya yi, da kowanne
ɗayanku zai gudu zuwa gidansa ku bar ni ni kaɗai. Amma duk
da haka ba ni kaɗai nake ba, domin Uba yana tare da ni.

33 "Ina faɗa muku waɗannan abubuwa ne domin a cikina ku
sami salama. A cikin duniya kuna shan wuya, amma ku kasance
da ƙarfin zuciya gama na yi nasara a kan duniya."

Yesu Ya Yi Addu'a

17 1 Bayan da Yesu ya faɗa waɗannan abubuwa sai ya ɗaga
kansa ya dubi sama ya yi addu'a ya ce, "Ya Uba, lokaci
ya yi. Ka ɗaukaka Ɗanka don shi ma yă ɗaukaka ka. 2 Gama ka
ba Ɗan iko a kan dukkan mutane, don yă ba da rai na har abada
ga waɗanda ka ba shi. 3 Rai na har abada kuwa shi ne, mutane
su san ka, kai kaɗai da kake Allah na gaskiya, su kuma san Yesu

Almasihu wanda ka aiko. 4 Na ɗaukaka ka a duniya ta wurin yin
dukan aikin da ka ba ni in yi. 5 Yanzu kuma, ya Uba, ka ɗaukaka
ni da ɗaukakan nan da nake da ita a gabanka tun kafin halittar
duniya.

6 "Na riga na bayyana yadda kake ga mutanen da ka ba ni a
nan duniya. Tun dā ma su naka ne, amma ka ba ni su, sun kuma
yi biyayya da maganarka. 7 Yanzu kuwa sun san duk abin da ka
ba ni daga gare ka yake. 8 Gama magana da ka faɗa mini na faɗa
musu, sun kuwa karɓa. Sun san hakika daga wurinka ne na fito,
sun kuma ba da gaskiya kai ne ka aiko ni. 9 Ina roƙo ne dominsu.
Ba domin mutanen duniya nake yin roƙon ba, amma domin
mutanen da ka ba ni, domin su naka ne. 10 Duk abin da nake da
shi naka ne, kuma duk abin da kake da shi nawa ne. Kuma sun
nuna yadda ɗaukakarka take. 11 Ina zuwa wurinka. Ba zan zauna
a duniya kuma ba, amma su suna duniya tukuna. Ya Uba Mai
Tsarki, ka lura da su da ikon sunanka, wato, sunan da ka ba ni,
domin su zama ɗaya, kamar dai yadda nake da kai. 12 Lokacin da
nake tare da su, na lura da su da ikon sunanka, sunan da kai ka
ba ni. Na kiyaye su, kuma ba wanda ya ɓace sai dai ɗayansu nan
kawai wanda yake ɗan halaka. Ya ɓace ne domin annabcin
Rubutaccen Maganar Allah yă cika. 13 Yanzu ina zuwa wurinka.
Amma ina roƙon waɗannan abubuwa ne tun ina duniya domin
waɗannan masu bina su sami farin cikina cikakke a zukatansu.
14 Na faɗa musu maganarka. Duniya kuma ta ƙi su, domin su ba
na duniya ba ne, kamar yadda ni ma ba na duniya ba ne. 15 Ba
ina roƙonka cewa ka ɗauke su daga duniya ba, amma ina roƙo
ne ka tsare su daga Mugun nan. 16 Su ba na duniya ba ne, kamar
yadda ni ma ba na duniya ba ne. 17 Ka tsarkake su ta wurin
gaskiya, domin maganarka ita ce gaskiya. 18 Na aike su duniya,
kamar yadda kai ma ka aiko ni. 19 Saboda su ne nake miƙa kaina
domin su ma a tsarkake su da gaske.

20 "Ba kuwa waɗannan kaɗai nake roƙa wa ba, amma ina roƙo
kuma domin dukan waɗanda za su ba da gaskiya bisa ga
maganarsu. 21 Ya Uba, ina roƙo domin dukansu su zama ɗaya.
Kamar yadda kake cikina, ni kuma ina cikinka, ina roƙo bari su
ma su kasance a cikinmu. Sa'an nan mutanen duniya za su ba da
gaskiya cewa kai ne ka aiko ni. 22 Ni na ba mutanen nan ɗaukakar
da kai ka ba ni, domin su zama ɗaya kamar yadda muke ɗaya.
23 Zan zauna a cikinsu, kai kuma a cikina, domin su zama ɗaya
sosai. Sa'an nan mutanen za su sani kai ne ka aiko ni, su kuma
sani ka ƙaunace su kamar yadda ka ƙaunace ni.

24 "Ya Uba, ina so waɗannan mutanen da ka ba ni su zauna
tare da ni a inda nake. Ina so su ga ɗaukakarka, wadda ka ba ni
domin kana ƙaunata kafin a halicci duniya. 25 Ya Uba, Mai Adalci,
mutanen duniya ba su san ka ba, amma ni kam na san ka,
waɗannan mutane kuma sun san kai ne ka aiko ni. 26 Na nuna
musu yadda kake, zan kuma ci gaba da nuna musu, domin su ma
su sami irin ƙaunar da ka nuna mini, ni ma in zauna a cikinsu."

An Kama Yesu
(Mat 26.47-56; Mar 14.43-50; Luk 22.47-53)

18 1 Bayan da Yesu ya gama wannan addu'a, sai ya ƙetare
rafin Kidron zuwa wancan hayi tare da almajiransa. A
hayin rafin kuwa akwai wani lambu, sai Yesu da almajiransa suka
shiga ciki. 2 Yahuda, almajirin da ya ci amanar Yesu ya san wurin
domin Yesu ya saba haɗuwa da almajiransa a can. 3 Sai Yahuda
ya ɗauko ƙungiyar soja da waɗansu dogarawan manyan firistoci
da na Farisiyawa, suka tafi lambun, suna riƙe da fitilu, da tocilan,
da kuma makamai. 4 Yesu kuwa da ya san duk abin da zai same
shi, sai ya fito, ya ce musu, "Wa kuke nema?"

5 Suka amsa suka ce, "Yesu Banazare." Yesu ya ce musu, "Ni
ne." Yahuda wanda ya ci amanar Yesu kuwa yana tsaye tare da
su. 6 Da Yesu ya ce musu, "Ni ne", sai mutanen suka ja da baya
har suka fāɗi a ƙasa. 7 Yesu ya sāke tambayarsu ya ce, "Wa kuke
nema?" Sai suka ce, "Yesu Banazare."

8 Yesu ya amsa ya ce, "Ai, na gaya muku cewa ni ne shi. In
kuwa ni kuke nema, to, ku bar waɗannan mutane su tafi."
9 Wannan ya faru ne domin maganar da Yesu ya riga ya yi ta
cika. Gama dā ya ce, "A cikin mutanen da ka ba ni ba wanda ya
ɓace."

10 Siman Bitrus kuwa wanda yake da takobi, ya zaro shi ya
sari bawan babban firist, har ya yanke masa kunne na dama.
Sunan wannan bawan kuwa Malkus ne. 11 Sai Yesu ya ce wa
Bitrus, "Ka mai da takobinka cikin gidansa. Ba zan sha daga cikin
kwaf da Uba ya ba ni in sha ba?"

Yesu a gaban Babban Firist
(Mat 26.57-58; Mar 14.53-54; Luk 22.54)

12 Sai ƙungiyar soja da shugabansu, da dogarawan nan na
Yahudawa suka kama Yesu, suka ɗaure shi. 13 Da farko suka kai
shi wurin Hanana, don shi surukin Kayafa ne. Kayafa kuwa shi
ne babban firist a wannan shekarar. 14 Shi ne ya ba Yahudawa

shawara cewa ya fi kyau mutum ɗaya ya mutu saboda sauran mutane.

Bitrus Ya Yi Mūsun Sanin Yesu
(Mat 26.69-70; Mar 14.66-68; Luk 22.55-57)

15 Sai Siman Bitrus da wani daga cikin almajiran Yesu suka bi Yesu a baya. Wannan almajirin kuwa babban firist ya san shi, shi kuma ya shiga zauren babban firist ɗin tare da Yesu. 16 Amma Bitrus ya tsaya a bakin ƙofa daga waje. Sai almajirin nan da babban firist ya waye shi ya fita ya yi magana da yarinya mai gadin ƙofa, sa'an nan ya shigo da Bitrus.

17 Yarinyar da take gadin ƙofar ta ce wa Bitrus, "Anya! Ba kana cikin almajiran mutumin ba?" Bitrus ya amsa ya ce, "A'a, ba na ciki." 18 Ana sanyi, saboda haka bayi da dogarawan haikali suka hura wuta da gawayi, suna tsaitsaye, suna jin ɗumin wutar. Bitrus ma yana tsaye tare da su yana jin ɗumin wutar.

Babban Firist Ya Yi wa Yesu Tambayoyi
(Mat 26.59-66; Mar 14.55-64; Luk 22.66-71)

19 Sai babban firist ya yi wa Yesu tambayoyi a kan almajiransa da kuma koyarwarsa. 20 Yesu ya amsa masa ya ce, "Ai, na yi magana a fili a gaban kowa, na kuma yi ta koyarwa a majami'u da haikali, inda Yahudawa sukan taru duka. Ban taɓa faɗa kome a ɓoye ba. 21 To, me ya sa kake yi mini tambayoyi? Ai, sai ka yi wa mutanen da suka saurare ni tambayoyi a kan abin da na faɗa musu, gama sun san abin da na faɗa."

22 Da ya faɗa haka, sai wani daga cikin dogarawan da yake tsaye ya mari Yesu, ya ce, "Haka za ka amsa wa babban firist?" 23 Yesu ya amsa ya ce, "In dai na faɗa wani abu ne wanda ba daidai ba, to, sai ka nuna yadda yake. Amma in abin da na faɗa gaskiya ne, to, me ya sa ka mare ni?" 24 Sai Hanana ya sa aka kai Yesu a ɗaure wurin Kayafa, babban firist.

Bitrus Ya Sāke Mūsun Sanin Yesu
(Mat 26.71-75; Mar 14.69-72; Luk 22.58-62)

25 Har yanzu Bitrus kuwa yana tsaye yana jin ɗumin wuta, sai waɗansu da suke tsaye a wurin suka tambaye shi suka ce, "Anya! Kai ma ba cikin almajiransa kake ba?" Sai Bitrus ya yi mūsu ya ce, "Ba na ciki."

26 Wani daga cikin bayin babban firist yana nan. Wannan bawan kuwa dangin wanda Bitrus ya yanke masa kunne ne, sai ya ce wa Bitrus, "Ashe, ban gan ka tare da shi a lambun ba?"

27 Sai Bitrus ya sāke yin mūsu. Nan da nan kuwa zakara ya yi cara.

Yesu a Gaban Gwamna Bilatus
(Mat 27.1-2, 11-14; Mar 15.1-5; Luk 23.1-5)

28 Tun da sassafe suka fitar da Yesu daga gidan Kayafa zuwa fadar gwamnan Roma. Amma suka ki shiga cikin fadar, wai don kada su zama da rashin tsarki a gaban Allah har su kāsa cin abincin Bikin Ketarewa. 29 Saboda haka Bilatus ya fito waje ya same su, ya ce, "Wacce kara ce kuka kawo game da wannan mutumin?"

30 Sai suka amsa masa suka ce, "Da wannan ba mai laifi ba ne, ai, da ba mu kawo shi wurinka ba." 31 Bilatus ya ce musu, "Ku tafi da shi da kanku mana, ku hukunta shi bisa ga dokarku." Sai Yahudawa suka ce masa, "Ai, ba a ba mu ikon yanke wa wani hukuncin kisa ba." 32 Wannan ya faru ne kuwa don a cika maganar da Yesu ya yi wadda ta kwatanta irin mutuwar da zai yi.

33 Sai Bilatus ya koma cikin fadar, sa'an nan ya kira Yesu ya tambaye shi ya ce, "Kai ne sarkin Yahudawa?" 34 Yesu ya amsa ya ce, "Wannan tambayar na kanka ne, ko kuwa wadansu ne suka yi maka magana a kaina?"

35 Bilatus ya amsa ya ce, "Ai, ni ba Bayahude ba ne, mutanenka ne da manyan firistoci suka kawo ka a wurina. Me ka yi?" 36 Yesu ya amsa ya ce, "Mulkina ba iri na duniya ba ne. Da mulkina iri na wannan duniya ne, da masu yin mini hidima za su yi yaki don kada a mika ni ga Yahudawa." 37 Sai Bilatus ya ce, "Ashe, kai sarki ne?" Yesu ya amsa masa ya ce, "Kai ne da kanka ka ce ni sarki ne. Wannan shi ne dalilin da aka haife ni, shi ne kuma dalilin da na shigo duniya, don in shaida gaskiya. Kuma duk wanda yake na gaskiya, yakan saurari muryata." 38 Bilatus ya tambaye shi ya ce, "Mece ce gaskiya?"

An Yanke wa Yesu Hukuncin Mutuwa
(Mat 27.15-31; Mar 15.6-20; Luk 23.13-25)

Bayan da ya yi wannan tambaya, sai ya sāke fitowa wurin Yahudawa ya ce musu, "Ni kam, ban same shi da wani laifi ba. 39 Amma dai kuna da wata al'ada, in dai Bikin Ketarewa ya yi, nakan sakar muku da dan kurkuku guda. To, kuna so in sakar muku da sarkin Yahudawa?"

40 Suka sāke amsa, suka yi ihu suna cewa, "A'a, ba wannan
za ka sake ba, sai dai ka saki Barabbas!" (Barabbas kuwa wani
dan fashi ne.)
19 1 Sa'an nan Bilatus ya sa a yi wa Yesu bulala. 2 Sai sojoji
suka yi wani rawanin ƙaya da reshen itacen ƙaya suka sa
shi a kan Yesu, sa'an nan suka sa masa wata jar riga irin ta
sarakuna. 3 Suka yi ta zuwa wurinsa, suna ta marinsa suna cewa,
"Ranka yă dade, sarkin Yahudawa!"
4 Sai Bilatus ya sāke fitowa, ya ce wa Yahudawa, "Ga shi fa
zan fito muku da Yesu, don ina so ku sani cewa ban same shi da
wani laifi ba." 5 Sa'an nan Yesu ya fito da rawanin ƙaya a kansa
da kuma riga mai launin shuni. Sai Bilatus ya ce musu, "To, ga
mutumin."
6 Da manyan firistoci da dogarawan haikali suka ga Yesu, sai
suka yi ihu suna cewa, "A gicciye shi! A gicciye shi!" Amma
Bilatus ya ce musu, "Ku je ku gicciye shi da kanku, domin ni
ban same shi da wani laifi ba." 7 Yahudawan suka amsa masa
suka ce, "Ai, muna da doka, kuma bisa ga dokar ya kamata a
kashe shi, domin ya mai da kansa Dan Allah."
8 Da Bilatus ya ji wannan magana sai ya ƙara jin tsoro. 9 Sai
ya sāke shiga cikin fadar, ya tambayi Yesu cewa, "Daga ina ne
ka fito?" Amma Yesu bai ba shi wata amsa ba. 10 Saboda haka
Bilatus ya ce masa, "Ka ƙi ka yi magana da ni ko? Ba ka sani
cewa ina da iko in sake ka, ko in gicciye ka ba?" 11 Yesu ya amsa
masa ya ce, "Ai, ikon da kake da shi a kaina iko wanda Allah
ya ba ka ne kawai. Mutumin da ya sa ni a hannunka ya fi ka
zunubi."
12 A kan wannan magana Bilatus ya nema yă saki Yesu, amma
Yahudawa suka daga muryarsu suka yi ihu suna cewa, "In dai
ka saki wannan, to, kai ba abokin Kaisar ba ne. Ai, duk wanda
ya mai da kansa sarki, yana yi wa Kaisar tawaye ke nan."
13 Da Bilatus ya ji wannan abin da suka fada, ya fito da Yesu.
Sai shi Bilatus ya zauna a kujerar shari'a a wani wurin da aka
gina da duwatsu. Da Yahudanci kuwa ana ce da shi Gabbata.
14 Ranan nan kuwa Ranar Shirin Bikin Ketarewa ce, wajen tsakar
rana. Sai shi Bilatus ya ce wa Yahudawa, "Ga sarkinku!"
15 Amma Yahudawa suka yi ihu suna cewa, "A kashe shi! A
kashe shi! A gicciye shi!" Sai Bilatus ya tambaye su ya ce, "Kuna
so in gicciye sarkinku ne?" Sai manyan firistoci suka amsa suka
ce, "Ai, mu ba mu da wani sarki sai Kaisar." 16 Sa'an nan Bilatus
ya dauki Yesu ya ba Yahudawa don su gicciye shi.

An Gicciye Yesu
(Mat 27.32-44; Mar 15.21-32; Luk 23.26-43)

17 Sai sojoji suka tafi da Yesu. Yesu ya kuwa fita daga cikin
garin yana ɗauke da gicciyensa da kansa zuwa wani wuri wanda
ake ce da shi Wurin Kokon Kai. Da Yahudanci kuwa ana ce da
wannan wurin, Golgota. 18 A wurin ne fa aka gicciye Yesu, tare
da waɗansu mutane biyu, ɗaya a damarsa, ɗaya kuma a hagunsa.
19 Bilatus kuma ya rubuta wata sanarwa, wadda aka manne a kan
gicciyen. Abin da aka rubuta kuwa shi ne, "Yesu Banazare, Sarkin
Yahudawa." 20 Yahudawa da yawa sun karanta wannan sanarwa
domin wurin da aka gicciye Yesu kusa da birni ne. Wannan
rubutun kuwa an yi shi da Yahudanci, da Romanci da kuma
Helenanci. 21 Sai manyan firistocin Yahudawa suka ce wa Bilatus,
"Kada ka rubuta, 'Sarkin Yahudawa', amma ka rubuta, 'Wannan
mutum ya ce wai shi ne Sarkin Yahudawa'." 22 Bilatus ya amsa
ya ce, "Abin da na riga na rubuta, na rubuta ke nan."

23 Bayan da sojojin suka gicciye Yesu, suka ɗibi tufafinsa,
suka raba kashi huɗu, kowanne soja ya ɗauki kashi ɗaya. Sun
kuma ɗauki doguwar rigarsa wadda ba a ɗinka ta ba, amma an
saka ta ne tun daga sama har zuwa ƙasa. 24 Sai suka ce wa juna,
"Kada mu yage wannan rigar, amma mu yi kuri'a a kanta, mu
ga wanda zai ci." Wannan ya faru ne don a cika abin da aka
rubuta cikin Maganar Allah cewa,

"Sun raba tufafina a junansu,
Rigata kuwa, suka yi kuri'a a kanta."

Abin da sojojin suka yi ke nan. 25 To, waɗanda suka tsaya kusa
da gicciyen Yesu kuwa su ne mamarsa tare da 'yar'uwarta, da
Maryamu matar Kilobas, da kuma Maryamu daga Magadala.
26 Da Yesu ya ga mamarsa da almajirin nan da yake ƙauna tsaye
kusa, sai ya ce wa mamarsa, "Mama, wannan yă zama ɗanki!"
27 Sa'an nan ya ce wa almajirin, "Wannan ta zama mamarka."
Tun daga lokacin nan fa almajirin ya kai mamar Yesu gidansa ta
zauna tare da shi.

Mutuwar Yesu
(Mat 27.45-56; Mar 15.33-41; Luk 23.44-49)

28 Yesu ya san cewa a wannan lokaci ya gama dukan kome,
kuma domin a cika abin da aka rubuta a Maganar Allah sai ya
ce, "Ina jin ƙishin ruwa." 29 To, akwai wani gora cike da ruwan

19.24: Zab 22.18 **19.28:** Zab 69.22

tsami a ajiye a wurin. Sai suka jiƙa soso da ruwan tsamin, suka soka soson a sandan izob suka ɗaga suka kai bakin Yesu. 30 Da Yesu ya tsotsi ruwan tsamin nan sai ya ce, "An gama!" Sa'an nan ya sunkuyar da kansa ya saki ransa.

An Soki Yesu da Māshi

31 Sa'an nan shugabannin Yahudawa suka roƙi Bilatus yă ba da izni a kakkarya ƙafafun mutanen da aka gicciye, a kuma sauko da jikunansu daga gicciye. Sun yi wannan roƙo ne domin Ranar Shiri[o] ce, kuma ba sa so jikunan su kasance a kan gicciye a Ranar Hutu. Ranar Hutun nan mai zuwa kuwa Hutu ne na musamman. 32 Sai sojojin suka zo wurin mutanen da aka gicciye tare da Yesu suka kakkarya ƙafafun mutum na farko, sa'an nan suka je suka kakkarya ƙafafun mutum na biyun. 33 Amma da suka zo wurin Yesu, ba su kakkarya ƙafafunsa ba domin sun ga ya riga ya mutu. 34 Sai dai ɗaya daga cikin sojojin ya soki Yesu da māshi a gefe, wajen haƙarƙarinsa, sai nan da nan jini da ruwa suka fito. 35 Shi wanda ya ga abin da ya faru ne ya fada wannan, kuma duk abin da ya faɗa gaskiya ne. Kuma shi ma da kansa ya san gaskiya yake faɗi, kuma yana faɗinsa ne domin ku ma ku ba da gaskiya. 36 Wannan ya faru ne domin abin da aka rubuta a Maganar Allah yă cika, wato, "Ba ko ƙashinsa ɗaya da za a karya." 37 Wani Rubutaccen Maganar Allah kuma ya ce, "Za su dubi wanda suka soka."

Jana'izar Yesu

(Mat 27.57-61; Mar 15.42-47; Luk 23.50-56)

38 Bayan haka Yusufu mutumin Arimatiya, wanda yake almajirin Yesu ne, amma a ɓoye domin tsoron Yahudawa, ya roƙi Bilatus izni don yă ɗauki jikin Yesu. Bilatus kuwa ya yarda masa, ya kuwa je ya ɗauki jikin Yesu. 39 Nikodimus mutumin da ya taɓa zuwa wurin Yesu da dare, ya tafi tare da Yusufu, yana kuma riƙe da mur da alos a gauraye wajen awo ɗari. 40 Sai mutanen nan biyu suka ɗauki jikin Yesu suka nannaɗe da yadin lilin tare da kayan ƙamshin nan bisa ga al'adar Yahudawa ta jana'iza. 41 A wurin da aka gicciye shi kuwa akwai wani lambu, a cikin lambun kuma akwai wani sabon kabari wanda ba a taɓa sa kowa a ciki ba. 42 Da yake ranar shiri ce ta Yahudawa, kuma kabarin yana nan kusa sai mutanen nan suka sa jikin Yesu a nan wurin.

19.36: Fit 12.46; L. Kid 9.12; Zab 34.20 **19.37:** Zak 12.10

[o] **19.31 Ranar Shiri:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

Tashin Yesu daga Matattu
(Mat 28.1-10; Mar 16.1-8; Luk 24.1-12)

20 [1] Tun da sassafe a rana ta farko, a lokacin da gari bai gama wayewa ba, Maryamu 'yar garin Magadala ta je kabarin Yesu, ta ga an ture dutsen da ya rufe bakin kabarin. [2] Sai ta ruga da gudu zuwa wurin Bitrus da kuma almajirin nan da Yesu yake ƙauna, ta ce musu, "Ai, an ɗauki Ubangiji daga kabarin, ba mu kuwa san inda aka sa shi ba." [3] Sai Bitrus da almajirin nan suka fita suka kama hanyar kabarin. [4] Duka biyun kuwa suka ruga da gudu, amma almajirin nan ya wuce Bitrus, ya riga Bitrus kai wurin kabarin. [5] Da ya sunkuya ya leƙa ya ga yadin lilin a ajiye, amma bai shiga cikin kabarin ba. [6] Sa'an nan Bitrus ya zo a bayansa, ya kuwa shiga cikin kabarin, ya ga yadin lilin a ajiye. [7] Ya kuma ga yadin da aka naɗe kewaye da kan Yesu ajiye a wani wuri dabam da yadin lilin. [8] Sai almajirin nan da ya riga Bitrus kai wurin kabarin shi ma ya shiga. Da ya gani sai ya ba da gaskiya. [9] Amma har yanzu dai ba su gane abin da Rubutaccen Maganar Allah ta faɗa ba cewa dole ne Yesu yă sāke tashi daga matattu. [10] Sai almajiran suka koma gida.

Yesu Ya Bayyana ga Maryamu
(Mat 28.9-10; Mar 16.9-11)

11 Amma Maryamu ta tsaya a bakin kabarin daga waje, tana ta kuka. Tana cikin kuka ke nan, sai ta sunkuya ta leƙa cikin kabarin, [12] sai ta ga mala'iku biyu da fararen tufafi suna zaune a inda gawar Yesu take a dā. Mala'ika ɗaya yana zaune ta wajen kai, ɗayan kuma ta wajen ƙafafu.

13 Sai mala'ikun suka tambaye ta suka ce, "Uwargida, me ya sa kike kuka?" Ta ce musu, "Ai, an ɗauki Ubangijina, ban kuwa san inda aka sa shi ba." [14] Da ta gama faɗin wannan magana sai ta juya ta ga Yesu tsaye, amma ba ta gane cewa shi ne ba. [15] Sai Yesu ya tambaye ta ya ce, "Uwargida, me ya sa kike kuka? Wa kike nema?" Tana tsammani ko shi ne mai aiki a lambun, shi ya sa ta ce masa, "Mai gida, in kai ne ka ɗauke shi, gaya mini inda ka sa shi mana don in ɗauke shi." [16] Yesu ya kira ta ya ce, "Maryamu!" Sai ta juya zuwa wajen Yesu ta ce masa da yaren Yahudawa, "Rabboni!" (Wannan yana nufin "Malam".)

17 Yesu ya ce mata, "Kada ki riƙe ni, domin har yanzu ban hau wurin Uba ba tukuna. Amma ki tafi wurin 'yan'uwana ki ce musu, zan koma wurin Ubana kuma Ubanku, Allahna kuma Allahnku." [18] Sai Maryamu 'yar garin Magadala ta je ta ce wa

almajiran, "Ai, na ga Ubangiji." Ta kuma gaya musu abin da Yesu ya faɗa mata.

Yesu Ya Bayyana ga Almajiransa
(Mat 28.16-20; Mar 16.14-18; Luk 24.36-49)

19 Da yamma ta yi a ranar farko ta mako, almajiran Yesu suna wuri ɗaya. Sun kuma kukkule ƙofofi domin suna tsoron shugabannin Yahudawa. Sai ga Yesu ya zo ya tsaya a tsakiyarsu, ya ce musu, "Salama ta kasance tare da ku." 20 Bayan da ya faɗa wannan magana, ya nuna musu hannayensa da wajen haƙarƙarinsa. Sai almajiransa suka yi farin ciki da ganin Ubangiji.

21 Sa'an nan Yesu ya sāke ce musu, "Salama ta kasance tare da ku! Kamar yadda Uba ya aiko ni haka ni ma na aike ku." 22 Da ya faɗa haka sai ya hura musu numfashinsa, ya ce musu, "Ku karɓi Ruhu Mai Tsarki. 23 Duk wanda kuka gafarta masa zunubai, to, an gafarta ke nan, kuma duk wanda ba ku gafarta ba, to, ba a gafarta masa ba ke nan."

Shaidar Bangaskiyar Toma

24 Toma kuwa, ɗaya daga cikin sha biyun nan, wanda ake ce da shi 'Yan Biyu, ba ya nan tare da su a lokacin da Yesu ya zo. 25 Sai sauran almajiran suka ce masa, "Ai, mun ga Ubangiji." Amma Toma ya ce musu, "In ban ga ramin ƙusoshin a hannayensa ba, in sa yatsata a ramin ƙusoshin ba, in kuma sa hannuna a gefen haƙarƙarinsa ba, ba zan ba da gaskiya ba."

26 Bayan kwana takwas almajiran suna tare a gidan, kuma Toma yana tare da su. Kofofi suna kulle, amma Yesu ya zo ya tsaya a tsakiyarsu ya ce, "Salama ta kasance tare da ku." 27 Sa'an nan ya ce wa Toma, "Sa yatsarka nan, ka dubi hannayena. Miƙo hannayenka ka sa a gefen haƙarƙarina. Ka daina shakka, ka ba da gaskiya."

28 Sai Toma ya ce masa, "Ya Ubangijina, da Allahna kuma!" 29 Yesu ya ce masa, "Ai, don ka gan ni ne shi ya sa ka ba da gaskiya. Masu albarka ne waɗanda suka ba da gaskiya ba tare da sun gan ni ba."

Manufar Littafin Nan

30 Yesu ya yi abubuwan ban mamaki da yawa a idanun almajiransa waɗanda ba a rubuta a wannan littafi ba. 31 Amma an rubuta waɗannan ne, don ku ba da gaskiya Yesu shi ne Almasihu,

Dan Allah. Sa'an nan kuma, ta wurin ba da gaskiya ku sami rai a cikin sunansa.

Yesu Ya Bayyana ga Almajiransa Bakwai

21 [1] Bayan haka Yesu ya sāke bayyana kansa ga almajiransa a bakin Tekun Tibariya. Kuma ga yadda ya bayyana kansa. [2] Siman Bitrus, da Toma wanda ake ce da shi 'Yan Biyu da Nataniyel daga Kana ta Galili, da 'ya'yan Zabadi, da kuma waɗansu almajiran biyu duk suna nan tare. [3] Sai Bitrus ya ce, "Za ni kamun kifi." Sauran almajiran suka ce, "Mu ma za mu tafi tare da kai." Sai suka fita suka shiga jirgin ruwa suka tafi. Amma a wannan daren ba su kama kome ba.

4 Gari yana wayewa ke nan, sai ga Yesu a tsaye a bakin tekun, amma almajiran ba su gane Yesu ne ba. [5] Sai Yesu ya ce musu, "Samari, kuna da kifi?" Suka amsa masa suka ce, "A'a." [6] Yesu ya ce musu, "Ku jefa abin kamun kifinku a hannun dama na jirgin, za ku samu." Suka jefa shi kamar yadda Yesu ya faɗa, suka kama kifi da yawa har suka kāsa jawo abin kamun kifin zuwa cikin jirgin.

7 Sai almajirin nan da Yesu yake ƙauna ya ce wa Bitrus, "Ai, Ubangiji ne!" Da Siman Bitrus ya ji cewa Ubangiji ne, sai ya ɗauki rigarsa ya sa don tun dā ma a tuɓe yake. Sa'an nan ya yi tsalle ya shiga cikin ruwan. [8] Sauran almajiran kuwa suka je gefen tekun a cikin jirgin, suna jan abin kamun kifin cike da kifi. Don dā ma ba su da nisa da gefen tekun, misali mita ɗari ne.

9 Da fitowarsu bakin ruwa, sai suka ga garwashin wuta a wurin, da kifi a kai, da burodi kuma. [10] Yesu ya ce musu, "Ku kawo waɗansu kifi a cikin waɗanda kuka kama yanzu." [11] Sai Siman Bitrus ya hau jirgin ruwan, ya jawo abin kamun kifin zuwa gefen ruwa. Abin kamun kifin yana kuwa cike da manyan kifaye ɗari da hamsin da uku. Amma duk da yawansu haka, abin kamun kifi bai yage ba. [12] Sai Yesu ya ce musu, "Ku zo ku ci abincin safe." A cikin almajiran kuwa ba wanda ya yi ƙarfin hali yă tambaye shi kowane ne shi, domin sun san cewa Ubangiji ne. [13] Sai Yesu ya je ya ɗauki burodin ya ba su, ya kuma ɗauki kifin ya ba su. [14] Wannan shi ne sau na uku da Yesu ya bayyana kansa ga almajiran bayan da aka tashe shi daga matattu.

Yesu da Bitrus

15 Da suka gama cin abincin safen, sai Yesu ya tambayi Siman Bitrus ya ce, "Siman ɗan Yohanna, kana ƙaunata fiye da

waɗannan?" Sai Bitrus ya amsa masa ya ce, "I, Ubangiji, ai, ka san yadda nake sonka." Yesu ya ce masa, "Ka ciyar da tumakina." 16 Sai Yesu ya sāke tambayarsa sau na biyu ya ce, "Siman ɗan Yohanna, kana ƙaunata?" Ya amsa ya ce, "I, Ubangiji, ai, ka san ina sonka." Yesu ya ce masa, "Ka yi kiwon tumakina." 17 Yesu ya tambaye shi sau na uku ya ce, "Siman ɗan Yohanna, kana sona?" Sai Bitrus ya yi baƙin ciki, don a tambaya ta uku Yesu ya ce "Kana sona?" Sai shi kuwa ya amsa ya ce, "Ya Ubangiji, ai, ka san dukan kome, ka san ina sonka." Yesu ya ce masa, "To, ka ciyar da tumakina. 18 Hakika, ina gaya maka, lokacin da kake saurayi kakan sa wa kanka sutura ka je duk inda ka ga dama, amma in ka tsufa za ka miƙe hannayenka, wani yă sa maka sutura, yă kai ka inda ba ka so ka tafi." 19 (Yesu ya faɗa wannan ne domin yă nuna irin mutuwar da Bitrus zai yi don yă ɗaukaka Allah.) Bayan wannan magana, Yesu ya ce wa Bitrus, "Ka bi ni."

Yesu da Almajirin da Yake Kauna

20 Bitrus ya juya ya dubi baya, sai ya ga almajirin nan da Yesu yake ƙauna yana binsu. Wannan shi ne almajirin da ya jingina a ƙirjin Yesu a lokacin cin abincin Bikin Ketarewa. Shi ne wanda ya tambayi Yesu ya ce, "Ya Ubangiji, wane ne zai ci amanarka?" 21 Da Bitrus ya gan shi, sai ya tambayi Yesu ya ce, "Ubangiji, wannan mutum fa?" 22 Sai Yesu ya ce masa, "In na nufe shi da rayuwa har kafin in dawo, ina ruwanka? Kai dai, ka bi ni!" 23 Saboda haka wannan labari ya yi ta bazuwa cikin masu bin Yesu, cewa almajirin nan ba zai mutu ba. Amma Yesu bai ce ba zai mutu ba. Ya dai ce, "In na nufe shi da rayuwa har kafin in dawo, ina ruwanka?"

24 Wannan shi ne almajirin da yake ba da shaida a kan waɗannan abubuwa, ya kuma sa su a rubuce. Mun kuma san cewa shaidarsa gaskiya ce.

25 Amma akwai waɗansu abubuwa da yawa da Yesu ya yi, in da za a rubuta duka, ina tsammani ko duniya kanta ba za ta iya ɗaukan littattafan da za a rubuta ba.

AYYUKAN MANZANNI

Gabatarwa

Masu ilimi sun yarda cewa Luka abokin tafiyar manzo Bulus ne ya rubuta littafin *Ayyukan Manzanni* da kuma *Bishara ta Hannun Luka* (Dubi A.M. 16.10-17, 20.5-15, 21.1-18, 27.1—28.16). Ra'ayoyi dai sun rabu game da lokacin da aka rubuta wannan littafin. Waɗansu sun yarda cewa a lokaci guda ne aka rubuta shi da Bishara ta Luka.

Dalilan da suka sa aka rubuta wannan littafin su ne, domin a ba Tiyofilus ainihin tabbataccen rahoto game da yadda addinin Kirista ya samo tushe. Littafin ya kuma nuna yadda addinin Kirista ya soma a cikin Yahudawa a Urushalima har ya bazu cikin waɗanda ba Yahudawa ba ko'ina a duniya. A lokacin nan an ɗauki masu bi kamar masu tawaye ne ga masu mulki. Saboda haka aka rubuta wannan littafin domin a kāre waɗannan masu bi.

Littafin *Ayyukan Manzanni* ya zama kamar gada tsakanin ayyukan da Yesu ya yi yayin da yake a duniya da kuma ayyukan da manzanni suka ci gaba da yi. Ruhu Mai Tsarki ya yi muhimmin aiki ta wurin ba wa manzannin ikon shaida bishara. Littafin ya ba da haske sosai game da rayuwa da ayyuka na Bitrus da Bulus da sauran manzannin. Ko'ina aka yi bisharar, mutane sukan ba da gaskiya, amma wannan nasara takan zo haɗe da tsanani.

Abubuwan da Suke Ciki

Shirin wa'azin bishara 1.1-26
Wa'azin bishara a Urushalima 2.1—8.3
Bishara a Yahudiya da Samariya 8.4—12.25
Tafiyar Bulus ta farko don wa'azin bishara 13.1—14.28
Taron shugabannin jama'a masu bi a Urushalima 15.1-35
Tafiyar Bulus ta biyu don wa'azin bishara 15.36—18.22
Tafiyar Bulus ta uku don wa'azin bishara 18.23—21.16
An kama Bulus a Urushalima 21.17—23.22
An kulle Bulus a Kaisariya 23.23—26.32
An kai Bulus Roma 27.1—28.31

Alkawarin Zuwan Ruhu Mai Tsarki

1 [1] Ya Tiyofilus, a littafina na farko na rubuta maka game da
dukan abubuwan da Yesu ya fara yi, da kuma waɗanda ya
fara koyarwa, [2] har zuwa ranar da aka ɗauke shi zuwa sama. Kafin

---

1.1: Luk 1.1-4

a ɗauke shi zuwa sama, ya yi wa manzannin da ya zaɓa umarni ta wurin Ruhu Mai Tsarki.

3 Bayan mutuwarsa, ya bayyana gare su da rai, har ya tabbatar musu maganar tashinsa ta wajen ayyuka iri-iri. Ya yi kwana arba'in, yana magana a kan al'amuran mulkin Allah. 4 A lokacin da yake tare da su,[a] ya umarce su cewa, "Kada ku bar Urushalima. Ku jira sai alkawarin da Ubana ya yi ya cika tukuna, wanda na faɗa muku da bakina, cewa, 5 Yohanna ya yi wa mutane baftisma da ruwa, amma nan da 'yan kwanaki, za a yi muku baftisma da Ruhu Mai Tsarki."

An Ɗauki Yesu zuwa Sama

6 Da manzannin suka taru, sai suka tambayi Yesu suka ce, "Ubangiji, yanzu ne za ka mayar wa Isra'ila mulki?"

7 Yesu ya ce musu, "Uba kaɗai yake da ikon shirya lokatai da zamanai, amma ku ba a ba ku damar sanin waɗannan ba. 8 Amma za ku sami iko sa'ad da Ruhu Mai Tsarki ya sauko muku, za ku zama shaiduna a Urushalima, da cikin dukan Yahudiya, da Samariya, har zuwa iyakar duniya." 9 Da ya faɗa haka, suna cikin dubawa, sai aka ɗauke shi zuwa sama. Wani girgije ya rufe shi, ba su ƙara ganinsa ba.

10 Sa'ad da suke zuba ido sama, shi kuma yana tafiya, sai ga mutum biyu a tsaye kusa da su, sun sa fararen riguna. 11 Sai suka ce, "Ku mutanen Galili, don me kuke tsaye kuna kallon sama? Yesun nan da aka ɗauke daga wurinku zuwa sama, zai sāke dawowa kamar yadda kuka ga ya tafi."

An Zaɓi Matiyas Yă Ɗauki Matsayin Yahuda

12 Sai manzannin suka koma Urushalima daga Dutsen Itatuwan Zaitun, wanda yake kusa da Urushalima, misalin tafiyar Ranar Hutu guda, wato, kilomita ɗaya. 13 Da suka shiga birnin, suka hau gidan sama inda suke zama, wato, su Bitrus, da Yohanna, da Yakubu, da Andarawus, da Filibus, da Toma, da Batilomi, da Matiyu, da Yakubu ɗan Alfiyus, da Siman wanda ake ce da shi mai kishin ƙasarsu, da kuma Yahuda ɗan Yakubu. 14 Duk waɗannan sun miƙa kai ga yin addu'a da nufi ɗaya tare da waɗansu mata, da Maryamu uwar Yesu, da kuma 'yan'uwansa.

1.4: Luk 24.49 **1.5:** Mat 3.11; Mar 1.8; Luk 3.16; Yoh 1.33
1.8: Mat 28.19; Mar 16.15; Luk 24.47-48 **1.9:** Mar 16.19; Luk 24.50-51
1.13: Mat 10.2-4; Mar 3.16-19; Luk 6.14-16

[a] **1.4 lokacin da yake tare da su:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "lokacin da yake cin abinci," ko kuwa "da suka zo wuri ɗaya."

15 A kwanakin nan, akwai taron 'yan'uwa wato, masu ba da
gaskiya (wajen mutum ɗari da ashirin). Bitrus ya tashi a tsaye ya
ce, 16"'Yan'uwa, lallai ne a cika Maganar Allah da Ruhu Mai
Tsarki ya faɗa a dā ta bakin Dawuda game da Yahuda, wanda ya
yi wa masu kama Yesu jagora. 17Gama dā shi ɗaya daga cikinmu
ne, an kuma ba shi rabonsa cikin aikin nan." 18(Da ladan mugun
aikinsa, Yahuda ya sayi wani fili, sai ya fāɗi da kai, cikinsa ya
fashe, kayan cikinsa duk suka zuba a waje. 19Duk masu zama a
Urushalima kuwa sun san abin nan da ya faru, har da ake ce da
filin "Akaldama" da yarensu, wato, Filin Jini.)

20 "Gama a rubuce yake a Zabura cewa,
'Gidansa yă zama an yashe shi,
kada kowa yă zauna a ciki.'
An kuma ce,
'Matsayinsa wani yă ɗauka.'

21 "Don haka lallai ne a zaɓi wani daga cikin mutanen nan,
wanda yake tare da mu duk kwanakin da Ubangiji Yesu yake
shiga da fita a wurinmu. 22Ya kamata wannan mutum yă zama
wanda ya kasance tare da mu tun daga lokacin da Yohanna yake
yin baftisma har zuwa ranar da aka ɗauki Yesu daga wurinmu
zuwa sama. Dole ne ɗaya daga cikin mutanen nan yă shaida
tashinsa daga matattu tare da mu."

23 Sai suka gabatar da mutum biyu, Yusufu mai suna
Barsaba, wanda kuma ake ce da shi Justus, da kuma Matiyas.
24 Almajiran suka yi addu'a suka ce, "Ubangiji, ka san zuciyar
kowa. Ka nuna mana wanda ka zaɓa a cikin waɗannan mutum
biyu, 25 yă zama manzo, yă ɗauki matsayin aikin manzon da
Yahuda ya bari don yă tafi wurin da ya dace da shi." 26 Sai
suka yi kuri'a a kansu, Matiyas ya ci, aka kuma sa shi yă zama
manzo tare da goma sha ɗayan nan.

Zuwan Ruhu Mai Tsarki

2 1 Da ranar bikin Fentikos[b] ta yi, duk masu bi suna tare a wuri
ɗaya. 2Ba labari sai aka ji wata ƙara daga sama kamar ta
babbar iska, ta cika dukan gidan da suke zaune a ciki. 3Sai ga
waɗansu abubuwa kamar harsunan wuta, suka bayyana a gare su,
suna rarrabuwa, suna sassauka a kan kowane ɗayansu.

1.18-19: Mat 27.3-8 **1.20:** Zab 69.25; 109.8
1.22: Mat 3.16; Mar 1.9; 16.19; Luk 3.21; 24.51 **1.25:** Irm 17.10
1.26: K. Mag 16.33 **2.1:** L. Fir 23.15-21; M. Sh 16.9-11
[b] **2.1 Fentikos:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

Hoton Zuwan Ruhu Mai Tsarki (2.2-4)

4 Sai duk aka cika su da Ruhu Mai Tsarki, suka kuma fara
magana da wadansu harsuna dabam-dabam, yadda Ruhun ya yi
musu baiwar yin magana.

5 To, akwai wadansu 'yan addinin Yahudanci da suke zama
a Urushalima sun kuwa zo ne daga ko'ina cikin ƙasashen
duniya. 6 Da suka ji ƙarar iskar dîn nan, sai taron mutane ya
hadu. Dukansu suka yi mamaki, don kowannensu ya ji taron
masu bi suna magana da yaren garinsu. 7 Suka yi mamaki sosai,
suna cewa, "Ashe, duk masu maganan nan ba Galilawa ba ne?
8 Yaya kuma kowannenmu yana ji suna magana da yarensa?"
9 Ga mu kuwa, Fartiyawa, da Madiyawa, da Elamawa, da
mutanen Mesofotamiya, da na Yahudiya, da na Kafadokiya, da
na Fantus, da na Asiya, 10 da na Firijiya, da na Bamfiliya, da
na Masar, da kuma na kewayen Sayirin ta ƙasar Libiya, har ma
da baki daga Roma. Ga mu wadanda aka haife mu a cikin
addinin Yahudanci da wadanda suka tuba suka shiga addininmu.
11 Ga mu kuma Kiritawa, da Larabawa, duk muna ji suna
magana da yarenmu a kan manyan abubuwan da Allah ya yi.
12 Duka kuwa suka yi mamaki, suka rude, suna ce wa juna,
"Mene ne wannan yake nufi?"

13 Amma wadansu suka yi musu ba'a suka ce, "Ruwan inabi
suka sha suka bugu."

Jawabin da Bitrus Ya Yi a Ranar Fentikos

14 Sai Bitrus ya tashi tsaye tare da sha ɗayan nan, ya ɗaga
murya ya yi musu jawabi, ya ce, "Ku 'yan'uwana Yahudawa da
dukan masu zama a Urushalima, ku ji, ku kuma kula da abin da
zan faɗa muku. 15 Mutanen nan ba su bugu ba kamar yadda kuke
tsammani, tun da yake yanzu ƙarfe tara ne kawai na safe.
16 Wannan, ai, shi ne abin da annabi Jowel ya faɗa cewa,
17 'Allah ya ce:
A kwanakin ƙarshe zan zubo wa dukan 'yan Adam
Ruhuna.
'Ya'yanku maza da mata za su yi annabci.
Ru'uya za ta zo wa samarinku,
Tsofaffinku kuma za su yi mafarkai.
18 Hakika, har ma a kwanakin nan zan
zubo Ruhuna a kan bayina maza da mata,
Za su kuma yi annabci.
19 Zan nuna abubuwan al'ajabi a sararin sama,
Da abubuwan ban mamaki a nan ƙasa,
Wato jini, da wuta, da kuma bakin hayaki.
20 Za a mai da rana duhu,
Wata kuma zai zama ja kamar jini,
Kafin ranar Ubangiji ta zo,
Babbar Ranan nan mai ɗaukaka.
21 A lokacin nan ne kowa da ya yi addu'a
da sunan Ubangiji zai sami ceto.'

22 "Ya ku 'yan'uwana Isra'ilawa, ku ji wannan magana. Yesu
Banazare mutum ne da Allah ya tabbatar muku cewa ya yarda da
shi. Allah ya nuna wannan ta wurin abubuwan ban mamaki, da
abubuwan al'ajabi, da alamu waɗanda ya yi ta wurin Yesu a
cikinku, kamar yadda ku ma kuka sani da kanku don duk sun
faru a idonku. 23 Shi mutumin nan, an ba da shi gare ku bisa ga
yadda Allah ya shirya, kuma da saninsa, kuka kuwa gicciye shi,
kuka kashe shi ta hannun masu zunubi. 24 Amma Allah ya fanshe
shi daga ikon mutuwa, ya tashe shi daga matattu don ba ya
yiwuwa mutuwa ta riƙe shi. 25 Gama Dawuda ya yi magana game
da shi ya ce,
'Kullum ina ganin Ubangiji, yana nan tare da ni.
Domin yana hannun damana, ba abin da zai ba ni tsoro.
26 Saboda haka zuciyata tana murna,

2.17-21: Jow 2.28-32 **2.23:** Mat 27.35; Mar 15.24; Luk 23.33; Yoh 19.18
2.24: Mat 28.5-6; Mar 16.6; Luk 24.5

ina farin ciki sosai,
ko da yake ni mutum ne mai mutuwa, zan zauna cikin
bege.
27 Don ba zai bar raina a kabari ba,
ba kuwa zai bar Mai Tsarkinsa yă ruɓa ba.
28 Ka koya mini hanyar rayuwa.
Za ka cika ni da murna ta wurin kasancewarka tare da ni.'

29 "'Yan'uwana Isra'ilawa, zan iya yi muku magana babu shakka game da kakanmu Dawuda. Dawuda ya mutu, an binne shi, kabarinsa kuma yana nan tare da mu har wa yau. 30 Shi annabi ne, kuma ya san Allah ya yi masa alkawari tare da rantsuwa, cewa zai naɗa wani daga cikin zuriyarsa sarki, kamar yadda ya naɗa shi Dawuda. 31 Dawuda ya hango haka, ya kuma yi magana a kan tashin Almasihu daga matattu, cewa ba za a bar shi a kabari ba, jikinsa kuma ba zai ruɓa ba. 32 Allah ya ta da Yesun nan daga matattu, mu kuwa duk shaidu ne ga wannan.

33 "An ɗaukaka shi ga hannun dama na Allah, kuma ya karɓi Ruhu Mai Tsarki daga wurin Uba, yadda aka yi alkawari. Yanzu kuma ya zubo Ruhun a kanmu. Shi ne ya kawo abin da kuke gani, kuke kuma ji. 34 Ai, ba Dawuda ne ya hau sama ba, amma shi da kansa ya ce,

'Ubangiji ya ce wa Ubangijina,
Zauna a hannun damana,
35 Har in sa ka take abokan gābanka.'

36 "Saboda haka, sai duk jama'ar Isra'ila su tabbata cewa Yesun nan da kuka gicciye, Allah ya mai da shi Ubangiji, da kuma Almasihu."

37 To, da suka ji haka, maganar ta soki zuciyarsu, suka ce wa Bitrus da sauran manzannin, "'Yan'uwa, mene ne za mu yi?"

38 Sai Bitrus ya ce musu, "Sai ku tuba, a yi wa kowannenku baftisma cikin sunan Yesu Almasihu don a gafarta muku zunubanku. Za ku kuwa sami kyautar Ruhu Mai Tsarki. 39 Gama wannan alkawarin Allah dominku ne tare da 'ya'yanku, da kuma dukan waɗanda suke nesa, wato, dukan waɗanda Ubangiji Allahnmu ya kira zuwa wurinsa."

40 Sai ya yi ta tabbatar musu da maganganu masu yawa, yana ta yi musu gargaɗi yana cewa, "Ku cece kanku daga hukuncin da yake a kan masu mugun aikin nan." 41 Waɗanda suka yarda da maganar Bitrus kuwa aka yi musu baftisma. A ranan nan kuma suka ƙaru da wajen mutum dubu uku. 42 Sai suka sa hankalinsu

2.25-28: Zab 16.8-11 **2.30:** Zab 132.11; 2 Sam 7.12-13 **2.34-35:** Zab 110.1

duka a kan koyarwar da manzanni suke yi, suna cin abinci tare da juna, suna zumunci yayin da suke addu'a.

Yadda Zaman Masu Bi Ya Kasance

43 Sai tsoro ya kama kowa, don Allah yana yin abubuwan ban mamaki da alamu da yawa ta wurin manzannin. 44 Dukan waɗanda suka ba da gaskiya sun kasance tare cikin zumunci, suna amfani da kome nasu tare gaba ɗaya. 45 Suka sayar da abin da suke da shi, suka rarraba wa kowa kuɗin bisa ga bukatarsa. 46 Kowace rana kuma suna zuwa haikali da nufi ɗaya. Suna cin abinci tare a gidajensu, suna ci suna sha da farin ciki, da yarda rai, 47 tare da yabon Allah. Suna kuma da farin jini a wurin mutane duka. Kowace rana kuma Ubangiji yana ƙara musu waɗanda suke samun ceto.

An Warkar da Gurgu a Kofar Haikali

3 1 Wata rana Bitrus da Yohanna suna tafiya haikali a lokacin addu'a, da ƙarfe uku na yamma. 2 A ƙofar da ake ce da ita Kyakkyawar Kofa, akwai wani mutum wanda tun haihuwarsa shi gurgu ne. Kowace rana a kan ɗauke shi zuwa ƙofar haikali, don yă roƙi kudi daga wurin masu shiga.

3 Da ya ga Bitrus da Yohanna za su shiga haikalin ke nan, sai ya roƙe su kudi. 4 Bitrus da Yohanna suka zuba masa ido, Bitrus ya ce, "Dube mu." 5 Sai kuwa duk hankalin gurgun ya koma kansu, yana tsammani za su ba shi wani abu. 6 Amma Bitrus ya ce, "Kudi kam, ba ni da su, amma abin da nake da shi, shi zan ba ka. A cikin sunan Yesu Almasihu Banazare, tashi ka yi tafiya." 7 Sai Bitrus ya kama hannunsa na dama, ya ɗaga shi. Nan take ƙafafunsa da idanun ƙafafunsa suka yi ƙarfi. 8 Ya yi wuf! Ya miƙe tsaye, ya fara tafiya, ya shiga haikalin tare da su, yana tafiya yana tsalle yana kuma yabon Allah. 9 Dukan mutane suka gan shi yana tafiya yana yabon Allah. 10 Suka kuwa gane shi ne mai zama a bakin Kyakkyawar Kofa ta haikalin yana roƙo. Sai suka yi mamaki ƙwarai da gaske game da abin da ya faru da shi.

Jawabin Bitrus a Barandar Solomon

11 Tun gurgun nan da aka warkar a Kyakkyawar Kofa yana riƙe da Bitrus da Yohanna, sai duk jama'a suka zo wurinsu a guje a cikin barandar da ake ce da shi Barandar Solomon, suna

2.44: A.M. 4.32-35

mamaki. 12 Da Bitrus ya ga haka, sai ya yi wa jama'a jawabi ya
ce, "Ku Isra'ilawa, don me kuke mamakin wannan? Don me
kuma kuke ta kallonmu, sai ka ce da ikon kanmu ne, ko kuwa
don aniyarmu cikin bin Allah ne muka sa mutumin nan ya yi
tafiya? 13 Allahn Ibrahim, da Ishaku, da Yakubu, Allahn
kakanninmu, shi ya ɗaukaka Bawansa Yesu. Shi ne wanda kuka
bashe shi, kuka kuma ƙi shi a gaban gwamna Bilatus, ko da yake
Bilatus ya yi ƙoƙari yă sake shi. 14 Amma kuka ƙi Mai Tsarkin
nan, Mai Adalci, kuka roƙa a sakar muku mai kisankai, 15 kuka
kuwa kashe wanda shi ne Tushen rai. Amma Allah ya tashe shi
daga matattu; mu kuwa shaidu ne ga wannan. 16 To, ta ikon sunan
Yesu ne, wato, ta wurin ba da gaskiya gare shi, shi ne ya ba
mutumin nan ƙarfi. Ga mutumin. Kun san shi. Ta wurin
bangaskiya cikin Yesu, mutumin nan ya sami cikakkiyar lafiya.
Dukanku kuwa shaidun wannan ne.

17 "Yanzu, 'yan'uwa, na sani cikin rashin sani ne kuka yi
haka, kamar yadda shugabanninku ma suka yi. 18 Amma ta haka
Allah ya cika abin da ya faɗa ta bakin annabawa duka cewa,
Almasihunsa zai sha wuya. 19 Saboda haka sai ku tuba, ku juyo
ga Allah domin a wanke zunubanku, Ubangiji zai sabunta
zuciyarku, 20 zai aiko da Almasihu da ya zaɓa muku tun dā,
wato, Yesu. 21 Lallai ne Yesu yă zauna a sama, har lokacin da
za a mai da dukan abubuwa sabo, kamar yadda Allah ya faɗa
tun zamanin dā ta bakin annabawansa masu tsarki. 22 Gama
Musa ya ce, 'Ubangiji Allahnku zai aika muku da wani annabi
daga cikin 'yan'uwanku, kamar yadda ya aike ni. Lallai ne ku
saurari dukan abin da zai faɗa muku. 23 Zai zama kuma duk
wanda ya ƙi sauraron annabin nan, za a fid da shi daga cikin
jama'a.' 24 Hakika, dukan annabawan da suka yi annabci, wato,
tun daga kan Sama'ila, da waɗanda suka zo daga baya, duk sun
yi magana a kan waɗannan kwanakin. 25 Annabcin da aka yi ta
wurin annabawa, dominku ne, ku ne kuma za ku ci gādon
alkawarin da Allah ya yi wa kakanninku, da ya ce wa Ibrahim,
'Ta zuriyarka ne za a yi wa dukkan kabilun duniya albarka.'
26 Da Allah ya zaɓi Bawansa, ya fara aiko shi wurinku ne don
yă yi muku albarka yă juyo da kowane ɗayanku daga hanyar
muguntarsa."

3.13: Fit 3.15
3.14: Mat 27.15-23; Mar 15.6-14; Luk 23.13-23; Yoh 19.12-15; Ish 5.3-11
3.22: M. Sh 18.15,18 **3.23:** M. Sh 18.19 **3.25:** Far 22.18

Bitrus da Yohanna a Gaban 'Yan Majalisa

4 [1] Lokacin da Bitrus da Yohanna suke cikin yin magana da
jama'a, sai firistoci da shugaban dogarawan haikalin da
Sadukiyawa[6] suka zo wurinsu. [2] Sun yi fushi domin almajiran
suna koya wa jama'a cewa matattu za su tashi da rai kamar yadda
Yesu ya tashi. [3] Sai suka kama su, suka kulle su sai washegari,
don yamma ta yi. [4] Amma da yawa cikin mutanen da suka ji
wa'azin suka ba da gaskiya. Sai duk yawan masu bi ya kai wajen
mutum dubu biyar.

5 Washegari shugabanninsu da dattibansu, da malaman
dokokinsu suka taru a Urushalima. [6] Hanana, babban firist, yana
nan tare da Kayafa, da Yohanna, da Alekzanda, da kuma duk
waɗanda suke dangin babban firist. [7] Suka sa Bitrus da Yohanna
suka tsaya a tsakiyarsu, sai suka tambaye su suka ce, "Da wane
iko ne, ko kuwa da wane suna ne kuka yi wannan?"

8 To, Bitrus, cike da Ruhu Mai Tsarki, ya tambaye su ya ce,
"Ku shugabanni da dattiban jama'a, [9] a yau, kuna tambayarmu a
kan alherin da aka yi wa wannan gurgun ne? Kuna kuma so ku
sani wanda ya warkar da shi ne? [10] To, muna so ku sani ku tare
da dukan mutanen Isra'ila cewa, a cikin sunan Yesu Almasihu
Banazaren nan da kuka gicciye, wanda Allah ya ta da shi daga
matattu, da sunansa ne wannan mutumin yake tsaye lafiyayye a
gabanku. [11] Wannan Yesun, shi ne 'Dutsen nan da ku masu gini
kuka rena, shi ne kuwa ya zama mafi kyau cikin duwatsun gini.'
[12] Ba kuma samun ceto ga wani domin cikin dukan sunayen da
aka ba wa mutane a duniya ba wani sunan da aka bayar wanda
lallai ta wurinsa ne za mu sami ceto."

13 To, da shugabannin suka ga ƙarfin halin Bitrus da Yohanna,
suka kuma gane su marasa ilimi ne, talakawa kuma, sai suka yi
mamaki, suka kuwa gane su abokan Yesu ne. [14] Amma da
shugabannin suka ga mutumin nan da aka warkar dîn yana tsaye
tare da manzannin, sai suka rasa abin da za su ce. [15] Suka umarci
manzannin su fita daga majalisa, suka yi shawara da juna [16] suka
ce, "Me za mu yi da mutanen nan? Don lallai dukan masu zama
a Urushalima sun san cewa an yi wani babban abin ban mamaki
ta wurin mutanen nan, ba kuwa yadda za mu ce, 'Ba haka ba ne.'
[17] Amma don kada abin yă bazu a cikin mutane, sai mu ja musu

---

4.11: Zab 118.22

[6] 4.1 **Sadukiyawa:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

kunne, kada su kuskura su ƙara yi wa kowa magana cikin wannan sunan."

18 Sai suka kirawo manzannin, suka ja musu kunne, kada su kuskura su yi wa kowa magana, ko su ƙara koyarwa cikin sunan Yesu. 19 Amma Bitrus da Yohanna suka amsa musu suka ce, "To, ko daidai ne a wurin Allah mu fi jin maganarku fiye da maganar Allah? Sai ku duba ku gani. 20 Don mu kam, ba za mu iya yin shiru a kan abin da muka ji, muka kuma gani ba." 21 Da suka ƙara jan musu kunne, suka sake su. Sun kuwa rasa yadda za su yi su hore su, domin mutane duka suna ɗaukaka Allah saboda abin da ya faru. 22 Mutumin nan kuwa da ya sami warkarwa na ban mamaki, ya fi shekara arba'in da haihuwa.

Masu Bi Sun Yi Addu'a don Su Yi Magana ba Tsoro

23 Da aka sake Bitrus da Yohanna, sai suka tafi wurin mutanensu, suka ba su labarin dukan abin da manyan firistoci da shugabanni suka faɗa musu. 24 Su kuwa, da jin haka, sai suka ɗaga muryarsu ga Allah da nufi ɗaya, suka ce, "Ubangiji mai iko duka, kai ne ka halicci sama da ƙasa, da teku, da kuma dukan abubuwan da suke cikinsu. 25 Ta wurin Ruhu Mai Tsarki ka yi magana ta wurin bawanka wato, kakanmu Dawuda, ka ce,

'Don me waɗanda ba Yahudawa ba suka yi fushi?
Kabilu kuma suka yi tunanin al'amuran wofi?
26 Sarakunan duniya sun yi shirin faɗa,
shugabanninsu kuma sun haɗa kai,
suna gāba da Ubangiji, da kuma Almasihunsa.'

27 "Gama hakika a birnin nan sarki Hirudus da Buntus Bilatus sun haɗa kai tare da waɗanda ba Yahudawa ba, da jama'ar Isra'ila, suna gāba da Bawanka Yesu mai tsarki, wanda ka mai da shi Almasihu. 28 Sun taru domin su aikata duk abin da ka shirya zai faru, bisa ga ikonka da nufinka.

29 "Yanzu kuma, ya Ubangiji, ka dubi yadda suke ƙoƙarin hana mu aiki. Ka ba bayinka ƙarfin halin faɗin maganarka babu tsoro. 30 Ka riƙa miƙa hannunka na warkarwa, ka kuma yi abubuwan ban mamaki, da abubuwan al'ajabi albarkacin sunan Bawanka, Yesu mai tsarki."

31 Da suka yi addu'a, sai wurin da suka taru ya girgiza. Sai duk aka cika su da Ruhu Mai Tsarki, suka yi ta faɗin maganar Allah babu tsoro.

4.24: Fit 20.11; Neh 9.6; Zab 146.6 **4.25-26:** Zab 2.1-2
4.27: Mat 27.1-2; Mar 15.1; Luk 23.1,7-11; Yoh 18.28-29

Kome na Masu Bi Daya Ne

32 To, duk taron masu bi kuwa nufinsu ɗaya ne, ra'ayinsu ma ɗaya, ba kuma waninsu da ya ce abin da yake da shi nasa ne, sai dai nasu ne tare. 33 Da iko mai girma manzannin kuma suka ba da shaida a kan tashin Ubangiji Yesu daga matattu. Alheri mai yawa ya kasance a kan kowane ɗayansu, 34 har ba wanda ya rasa wani abu a cikinsu. Domin duk masu gonaki ko gidaje suka riƙa sayar da su, suna kawo kuɗin, 35 suna ajiye a gaban manzannin, ana kuwa rarraba wa kowa bisa ga bukatarsa.

36 Haka wani mai suna Yusufu ya yi. Shi Balawe ne, asalinsa mutumin Sayifurus ne, wanda manzannin suke ce da shi Barnaba, (wato, mai ƙarfafa zuciya). 37 Barnaba kuwa ya sayar da wata gonarsa, ya kawo kuɗin ya ajiye a gaban manzannin.

Hananiya da Safiratu

5 1 Amma wani mutum mai suna Hananiya, tare da matarsa Safiratu, ya sayar da wani abin da yake da shi. 2 Sai ya ɓoye wani abu daga cikin kuɗin, da sanin matarsa, ya kawo sashi kawai ya ajiye a gaban manzanni. 3 Sai Bitrus ya ce, "Kai Hananiya, ta yaya ka bar Shaiɗan ya shiga zuciyarka, har ka yi wa Ruhu Mai Tsarki ƙarya, ka kuma ɓoye wani abu daga cikin kuɗin gonar? 4 Kafin ka sayar ba taka ba ce? Bayan da ka sayar ma, ba a sa ka dole ka ba da kuɗin ba. Ta yaya ka yi wannan tunani a zuciyarka? Ai, ba mutum ka yi wa ƙarya ba, Allah ka yi wa." 5 Da jin wannan maganar kuwa, Hananiya ya fāɗi ya mutu. Mutanen da suka ji kuwa, tsoro ya kama su sosai. 6 Samari suka tashi suka naɗe jikinsa da yadi, suka ɗauke shi zuwa waje suka binne.

7 Bayan kamar awa uku, matar Hananiya ta shigo, ba ta san abin da ya faru ba. 8 Sai Bitrus ya ce mata, "Gaya mini, wannan shi ne iyakacin kuɗin da aka biya ku a kan gonan nan?"

Sai ta ce, "I, iyakacin kuɗin ke nan."

9 Amma Bitrus ya ce mata, "Yaya kuka haɗa baki ku gwada Ruhun Ubangiji? Ki ji tafiyar waɗanda suka binne mijinki, suna bakin ƙofa, za su kuwa ɗauke ki su fitar da ke." 10 Nan take ta fāɗi a gabansa, ta mutu. Da samarin suka shigo suka same ta ta mutu, sai suka ɗauke ta, suka fitar da ita, suka binne ta ta gefen mijinta. 11 Sai babban tsoro ya kama dukan jama'ar masu bi, da duk waɗanda suka ji labarin waɗannan abubuwa.

4.32: A.M. 2.44-45

Manzannin Sun Yi Abubuwan Ban Mamaki da Yawa

12 To, an yi alamu da abubuwan mamaki masu yawa cikin
mutane ta wurin manzanni. Dukan masu bi kuwa sukan taru a
Barandar Solomon a filin haikali. 13 Amma a cikin sauran mutane,
ba wanda ya yi ƙarfin halin shiga cikinsu, duk da haka kuwa
jama'a suna ba su girma.

14 Duk da haka masu ba da gaskiya ga Ubangiji suka yi ta
ƙaruwa da jama'a masu yawan gaske, maza da mata. 15 Har ma
ya kai ga mutane suna fito da marasa lafiya titi-titi, suna shimfiɗa
su a kan gadaje da tabarmi. Suna fata cewa idan Bitrus ya zo
wucewa, ko inuwarsa ma ta bi ta kan waɗansunsu. 16 Mutane da
yawa kuwa suka yi ta taruwa daga garuruwan da suke kewayen
Urushalima, suna ta kawo marasa lafiya da waɗanda aljanu suke
ba su wahala, dukansu kuwa aka warkar da su.

Manzanni Sun Sha Wahala saboda Bangaskiyarsu

17 Sai babban firist tare da dukan waɗanda suke tare da shi,
wato, 'yan ƙungiyar Sadukiyawa, sun ji kishin manzannin sosai.
18 Saboda haka suka taso suka kama manzannin, suka sa su a
kurkuku. 19 Amma da dare sai wani mala'ikan Ubangiji ya buɗe
ƙofofin kurkukun, ya fito da su, ya ce, 20 "Ku je ku tsaya cikin
haikali ku faɗa wa mutane dukan maganar wannan sabon rai."
21 Da suka ji haka, suka shiga haikalin da sassafe, suna koyarwa.

Sa'ad da babban firist da waɗanda suke tare da shi suka taru,
suka kira Majalisa, da dukan shugabannin Isra'ila, suka aika
kurkuku a kawo manzannin. 22 Amma da dogarawan haikalin suka
je, ba su same su a kurkukun ba, suka dawo suka ba da labari,
suka ce, 23 "Mun sami kurkukun a kulle sosai, masu gadi kuma
suna gadin bakin ƙofofin, amma da muka buɗe, sai muka samu
ba kowa a ciki." 24 Da shugaban dogarawan haikali da manyan
firistoci suka ji haka, suka rikice sosai, suna tunanin abin da
wannan zai kawo.

25 Sai wani ya zo ya ce musu, "Ai, ga shi, mutanen nan da
kuka sa a kurkuku suna tsaye a haikali, suna koyar da jama'a."
26 Sai dogarawan haikalin tare da shugabansu suka je suka kawo
manzannin, amma fa ba da ƙarfi ba, don shugabannin suna tsoro
kada jama'a su jejjefe su da duwatsu.

27 Da suka kawo manzannin, suka sa suka tsaya a gaban
Majalisa. Sai babban firist ya tuhume su, 28 ya ce, "Mun ja muku
kunne sosai kada ku ƙara yin koyarwa cikin sunan nan, amma ga

shi kun cika Urushalima duk da koyarwarku, har ma kuna nema ku tura mana alhakin jinin mutumin nan."

29 Amma Bitrus da manzannin suka amsa suka ce, "Dole ne mu yi wa Allah biyayya fiye da mu yi wa mutum. 30 Allahn kakanninmu ya ta da Yesu, wanda kuka kashe ta wurin gicciye shi a kan gungumen itace. 31 Shi ne Allah ya ɗaukaka ga damarsa yă zama Shugaba da kuma Mai Ceto, domin yă buɗe wa Isra'ila hanyar tuba, su kuma sami gafarar zunubansu. 32 Mu kuwa shaidu ne ga waɗannan abubuwa, haka kuma Ruhu Mai Tsarki, wanda Allah ya ba wa masu yi masa biyayya."

33 Da shugabannin suka ji haka, sai suka ji ƒushi sosai, har suka so su kashe manzannin. 34 Amma wani Bafarisiye mai suna Gamaliyel, malamin Doka, wanda dukan jama'a suna ba shi girma, ya tashi tsaye cikin Majalisa, ya ba da umarni a fitar da mutanen nan waje tukuna. 35 Sa'an nan ya ce wa 'yan Majalisa, "Ku 'yan'uwa Isra'ilawa, ku kula fa da abin da kuke so ku yi wa mutanen nan. 36 Shekarun baya wani mutum ya ɓullo, mai suna Tudas, ya ɗauki kansa kamar wani abu. Wajen mutum ɗari huɗu suka bi shi, amma aka kashe shi, aka kuwa watsar da masu binsa, wannan kuwa ya zama ƙarshensu. 37 Bayan wannan kuma, wani mai suna Yahuda, mutumin Galili ya ɓullo, lokacin da ake ƙirgan mutane, ya sa mutane suka bi shi. Shi ma ya halaka, masu binsa ma duka aka watsar da su. 38 To, yanzu ma, ina gaya muku, ku ƒita hanyar mutanen nan, ku bar su. Idan dai niyyarsu, ko aikinsu na mutum ne, ai, zai rushe. 39 Amma idan aikin nan na Allah ne, ba za ku iya hana mutanen nan ba. Kada fa a same ku kuna gāba da Allah."

Sai suka yarda da shawararsa, 40 suka kuma kirawo manzannin, suka yi musu bulala, suka ja musu kunne kada su ƙara yin magana cikin sunan Yesu. Sa'an nan suka sake su. 41 Manzannin suka tashi daga gaban Majalisar suna farin ciki a kan an ga sun isa su sha wulaƙanci saboda sunan Yesu. 42 Kowace rana kuwa, ko a haikali, ko a gida, ba su daina koyarwa da ba da Labari Mai Daɗi na cewa Yesu shi ne Almasihu ba.

An Zaɓi Masu Hidima Bakwai

6 1 To, a kwanakin nan da almajirai suna ƙaruwa, sai Yahudawa masu jin Helenanci suka yi gunaguni a kan Yahudawa masu jin yaren Aramaya. Yahudawa masu jin Helenanci sun yi gunaguni ne don a wajen rabon taimako na kowace rana ba a

5.28: Mat 27.25

kula da matansu waɗanda mazansu suka mutu. 2 Sai sha biyun
nan suka kirawo duk jama'ar masu bi, suka ce, "Ai, bai yi kyau
mu bar wa'azin maganar Allah, mu shiga sha'anin abinci ba.
3 Saboda haka, 'yan'uwa, sai ku zaɓi mutum bakwai daga cikinku,
waɗanda suke da halin kirki, cike da Ruhu da kuma hikima,
waɗanda za mu ba su wannan aiki. 4 Mu kuma sai mu sami damar
nacewa da yin addu'a da kuma koyar da maganar Allah."

5 Jama'a duka kuwa suka ji daɗin abin da suka faɗa. Sai suka
zaɓi Istifanus, wani mutumin da yake cike da bangaskiya da Ruhu
Mai Tsarki, da Filibus, da Burokoras, da Nikano, da Timon, da
Barminas, da Nikolas mutumin Antakiya, wanda ba Bayahude ba
ne amma ya shiga addinin Yahudanci. 6 Waɗannan ne aka gabatar
a gaban manzanni. Bayan sun yi addu'a kuma, suka sa musu
hannun albarka.

7 Maganar Allah kuwa sai ƙara yaɗuwa take. Yawan masu bi
kuma a cikin birnin Urushalima sai ƙaruwa yake ta yi sosai,
firistoci masu yawa sosai kuma suka karɓi bangaskiyan nan.

An Kama Istifanus

8 To, Istifanus, cike da alheri da iko, ya yi ta yin manyan
abubuwan ban mamaki da alamu a cikin jama'a. 9 Sai waɗansu
na majami'ar da ake ce da ita majami'ar 'Yantattu,[c] suka tayar
wa Istifanus da gardama. Waɗannan kuwa Yahudawa ne daga
Sayirin da Alekzandiriya, da kuma daga ƙasar Kilikiya, da ta
Asiya. 10 Amma a ina! Sun kāsa gardama da shi, domin yana
magana da hikima, Ruhun Allah kuwa ya sauko a kansa. 11 Sai
suka zuga waɗansu mutane a ɓoye don su ce, "Mun ji shi yana
zagin annabi Musa, yana yi wa Allah maganar reni." 12 Ta haka,
suka ta da hankalin jama'a, da shugabanni, da malaman dokoki,
su kuma suka hau masa, suka kama shi, suka kai shi gaban
Majalisa. 13 Sai shugabannin jama'a suka kawo masu shaidar
ƙarya, waɗanda suka ce, "Mutumin nan ko yaushe yana maganar
banza a kan wurin nan mai tsarki da kuma Dokar Musa. 14 Mun
ji shi yana cewa wai Yesu Banazaren nan zai rushe wurin nan,
yă kuma canza duk al'adun da annabi Musa ya bar mana." 15 Duk
waɗanda suke zaune a Majalisar kuwa suka zura masa ido, suka
ga fuskarsa ta zama kamar ta mala'ika.

[c] **6.9 'Yantattu:** Wannan yana nufin Yahudawa waɗanda suka samu 'yancin kansu daga bauta.

Jawabin Istifanus

7 1 Sai babban firist ya tambayi Istifanus ya ce, "Abubuwan nan, gaskiya ne?"

2 Sai Istifanus ya ce, "Ku 'yan'uwa da ubanni, ku saurare ni. Allah Maɗaukaki ya bayyana ga kakanmu Ibrahim sa'ad da yake a ƙasar Mesofotamiya, tun bai zauna a Haran ba. 3 Allah ya ce masa, 'Ka tashi daga ƙasarku, ka bar 'yan'uwanka, ka je ƙasar da zan nuna maka.' 4 Sai kakanmu ya tashi daga ƙasar Kaldiyawa, ya je ya zauna a Haran. Daga can kuma, bayan babansa ya mutu, Allah ya kawo shi ƙasan nan da kuke zama a ciki yanzu. 5 Amma kuwa Allah bai ba shi Ibrahim gādon ƙasar ba, ko da taki ɗaya. Sai dai ya yi masa alkawari zai sa ƙasar ta zama tasa, shi da zuriyar da za su bi bayansa, ko da yake ba shi da yaro a lokacin. 6 Allah kuwa ya faɗa cewa, zuriyar Ibrahim za su yi baƙunci a wata ƙasa, mutanen ƙasar kuwa za su mai da su bayi, za su ba su wahala har shekara ɗari huɗu. 7 Allah ya ce zai hukunta ƙasar da za su bauta wa, bayan haka kuma zuriyar Ibrahim za su fito su bauta wa Allah a wannan wuri. 8 Allah kuma ya yi wa Ibrahim alkawari game da kaciya.[d] Shi ya sa da Ibrahim ya haifi Ishaku, ya yi masa kaciya a rana ta takwas. Ishaku ya haifi Yakubu, Yakubu kuma ya haifi kakanninmu goma sha biyun nan.

9 "Kakannin nan kuwa, da yake suna kishin ɗan'uwansu Yusufu, suka sayar da shi, aka kai shi Masar. Amma Allah yana tare da shi, 10 ya kuma fitar da shi daga dukan wahalarsa. Allah kuma ya sa ya zama mai hikima, mai farin jini a wurin Fir'auna, sarkin Masar. Fir'auna kuwa ya ba shi mulkin Masar, ya kuma sa jama'ar gidansa duka a hannun Yusufu. 11 Ana nan, sai yunwa ta shigo a duk ƙasar Masar da Kan'ana, tare da wahala mai tsanani, har kakanninmu suka rasa abinci. 12 Amma da Yakubu ya ji akwai hatsi a Masar, ya aiki yaransa wato, kakanninmu zuwa Masar. Wannan ya zama tafiyarsu ta farko. 13 A tafiyarsu ta biyu Yusufu ya sanar da kansa ga 'yan'uwansa, Fir'auna kuma ya gane asalinsa. 14 Sai Yusufu ya aika babansa Yakubu yă zo, da kuma dukan 'yan'uwan shi Yusufu. Dukansu kuwa mutum saba'in da biyar ne. 15 Sai Yakubu ya tafi Masar. A can ne ma ya mutu, shi da kakanninmu. 16 Sai aka kwaso su aka mai da su Shekem, aka

---

7.2-3: Far 12.1 **7.4:** Far 11.31; 12.4 **7.5:** Far 12.7; 13.15; 15.18; 17.8
7.6-7: Far 15.13-14 **7.7:** Fit 3.12
7.8: Far 17.10-14; 21.2-4; 25.26; 29.31—35.18 **7.9:** Far 37.11,28; 39.2,21
7.10: Far 41.39-41 **7.11:** Far 42.1-2 **7.13:** Far 45.1,16
7.14: Far 45.9-10; 17.18; Far 46.27 **7.15:** Far 46.1-7; 49.33

[d] **7.8 kaciya:** Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

sa su a kabarin da Ibrahim ya saya da kuɗin azurfa a wurin
'ya'yan Hamor a nan Shekem.

17 "Amma da lokacin cikar alkawarin da Allah ya yi wa
Ibrahim ya yi kusa, jama'armu ta ƙaru, ta yi yawa sosai a ƙasar
Masar. 18 Sa'an nan aka yi wani sarki a Masar, wanda bai ma
san kowane ne Yusufu ba. 19 Wannan sarki kuwa ya cuci
kabilarmu, ya yi wa kakanninmu tsanani yana sa a yar da
jariransu, don kada su rayu. 20 A lokacin nan ne aka haifi Musa,
yaro mai kyan gaske. An yi renonsa wata uku a gidan babansa.
21 Da aka yar da shi, 'yar Fir'auna ta ɗauke shi, ta lura da shi
kamar ɗanta. 22 Sai aka koya wa Musa dukan hikimar Masarawa,
shi kuwa mutum ne mai iko cikin magana, da ayyukansa. 23 Da
ya kai shekara arba'in ke nan, sai ya yi tunani yă je yă ziyarci
'yan'uwansa Isra'ilawa. 24 Da ya ga wani mutumin Masar yana
cutar ɗayansu, ya je ya taimaki mutumin Isra'ilar, ya rama masa,
ya bugi mutumin Masar, ya kashe shi. 25 Ya yi tsammani
'yan'uwansa za su gane Allah zai yi amfani da shi domin yă
cece su. Amma mutanen ba su gane ba. 26 Washegari kuma ya
gan waɗansu Isra'ilawa suna faɗa, sai ya so yă shirya su, ya ce,
'Ku jama'a, ku 'yan'uwa ne fa, don me kuke cutar juna?'
27 Amma mai cutar ɗan'uwansa ya ture Musa gefe, ya ce, 'Wa
ya sa ka ka zama shugabanmu da alƙalinmu? 28 Ashe, kana so
ka kashe ni kamar yadda ka kashe mutumin Masar nan na jiya?'
29 Da Musa ya ji haka, sai ya gudu ya yi zaman baƙunci a ƙasar
Midiyan, a can ya haifi 'ya'ya biyu maza.

30 "To, bayan shekara arba'in, wani mala'ika ya bayyana ga
Musa a harshen wuta, a ɗan itace a wani daji kusa da Dutsen
Sinai. 31 Da Musa ya ga haka, ya yi mamakin abin da ya gani.
Da ya zo kusa don yă duba, sai ya ji muryar Ubangiji ta ce, 32 'Ni
ne Allahn kakanninka, Allahn Ibrahim, da Ishaku, da Yakubu.'
Sai jikin Musa ya fara rawa, bai ma iya dubawa ba.

33 "Sai Ubangiji ya ce masa, 'Ka cire takalmanka, domin
wurin nan da kake tsaye wuri mai tsarki ne. 34 Lallai, na ga
wahalar da ake ba mutanena da suke Masar, na ji kukansu, na
kuma sauko in cece su. To, yanzu sai ka yi shiri in aike ka
zuwa Masar.'

35 "To, shi Musan nan ne suka ƙi, suna cewa, 'Wa ya sa ka
ka zama shugabanmu da alƙalinmu?' Shi ne Allah ya aiko yă

7.16: Far 23.3-16; 33.19; 50.7-13; Josh 24.32 **7.17-18**: Fit 1.7-8
7.19: Fit 1.10-11,22 **7.20**: Fit 2.2 **7.21**: Fit 2.3-10 **7.28**: Fit 2.14
7.23-29: Fit 2.11-15 **7.29**: Fit 18.3-4 **7.32**: Fit 3.6 **7.30-34**: Fit 3.1-10

zama shugaba, da mai ceto, ta wurin mala'ikan nan da ya bayyana
a gare shi a ɗan itacen nan. 36 Shi ne kuwa ya fito da su, bayan
ya yi abubuwan ban mamaki, da kuma alamu a ƙasar Masar, da
Jan Teku, da kuma a cikin daji har shekara arba'in. 37 Musan nan
shi ne wanda ya ce wa Isra'ilawa, 'Allah zai aiko muku da wani
annabi daga cikin mutanenku, kamar yadda ya aike ni.' 38 Musa
shi ne mutumin da ya tattara jama'ar Isra'ila a cikin daji. Ya
kasance a can tare da kakanninmu da kuma mala'ikan nan da ya
yi magana da shi a kan Dutsen Sinai. Shi ne kuma ya karɓo
magana mai ba da rai daga wurin Allah ya kawo mana. 39 Amma
kakanninmu suka ƙi yin masa biyayya, suka ƙi jin maganarsa,
suka yi marmarin komawa ƙasar Masar.

40 "Suka ce wa Haruna, 'Ka yi mana allolin da za su yi mana
jagora, don Musan nan kam, da ya fito da mu daga ƙasar Masar,
ba mu san abin da ya faru da shi ba.' 41 A lokacin nan, suka yi
siffar ɗan saniya, suka miƙa wa gunkin nan hadaya, suka riƙa
murna da aikin da suka yi da hannunsu.

42 "Saboda haka Allah ya juya musu baya, ya miƙa su ga
bautar taurari. Wannan ya yi daidai da abin da yake a rubuce a
littafin annabawa cewa, 'Ku jama'ar Isra'ila, ni ne kuka yanka
wa dabbobi, kuka miƙa wa hadaya, har shekara arba'in a cikin
daji? 43 Ai, da tentin gunki Molek kuka riƙa yawo, da tauraron
gunkinku Rifan, wato, gumakan nan da kuka yi don ku yi musu
sujada. Ni kuwa zan kawar da ku can gaba da Babila.'

44 "A dā kakanninmu suna da tentin da yake shaida kasancewar
Allah a daji. Wannan ne tentin da Allah ya umarci Musa yă yi,
kuma an yi shi daidai kamar yadda Allah ya nuna wa Musa.
45 Tentin nan ne kakanninmu suka gāda, suka kuma kawo a ƙasan
nan a zamanin Joshuwa, bayan sun karɓa ƙasar a hannun al'umman
da Allah ya kora a idonsu. Tentin nan kuwa yana nan har zuwa
zamanin Dawuda. 46 Dawuda kuwa ya sami yarda a wurin Allah,
har ya yi roƙo don yă gina wurin sujada domin Allahn kakanmu
Yakubu.[d] 47 Amma Solomon ne ya yi wa Allah ginin.

48 "Duk da haka, Maɗaukaki ba ya zama a gidajen da mutum
ya gina. Yadda annabi ya ce,

49 'Sama shi ne gadon sarautata,

7.35: Fit 2.14 **7.36**: Fit 7.5; 14.21; L. Kid 14.33 **7.37**: M. Sh 8.15,18
7.38: Fit 19.1—20.17; M. Sh 5.1-33 **7.40**: Fit 32.1 **7.41**: Fit 32.2-6
7.42-43: Amos 5.25-27 **7.44**: Fit 25.9,40 **7.45**: Josh 3.14-17
7.46: 2 Sam 7.1-16; 1 Tar 17.1-14 **7.47**: 1 Sar 6.1-38; 2 Tar 3.1-17

[d] **7.46 Allahn kakanmu Yakubu**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Na mutanen Isra'ila" ne a nan.

ƙasa kuwa matashin ƙafata,
in ji Ubangiji.
Wane irin gida ne za ku gina mini?
Ko kuwa wane wuri ne wurin hutuna?
50 Ba ni ne na halicci duk waɗannan abubuwan ba?'

51 "Ku masu taurinkai, masu taurin zuciya, masu kunnen ƙashi, kullum kuna ƙin biyayya da Ruhu Mai Tsarki. Yadda kakanninku suka yi, haka ku ma kuke yi. 52 Cikin annabawa, akwai wanda kakanninku ba su tsananta masa ba? Sun kashe waɗanda suka yi magana a kan zuwan Mai Adalcin nan. Ku kuwa, kuka ci amanarsa, kuka kashe shi. 53 Ku ne kuwa kuka karɓi doka ta wurin mala'iku, amma ba ku kiyaye ta ba!"

An Jejjefi Istifanus har Ya Mutu

54 Da suka ji haka, suka yi fushi sosai, har suka ciji baki don haushi. 55 Amma Istifanus cike da Ruhu Mai Tsarki, ya zuba ido yana kallon sama, ya ga ɗaukakar Allah, da kuma Yesu a tsaye a hannun dama na Allah. 56 Sai Istifanus ya ce, "Duba, ina ganin sama a buɗe, da kuma Ɗan Mutum a tsaye a hannun dama na Allah."

57 Amma suka fara ihu sosai, suka tottoshe kunnuwansu, suka hau masa gaba ɗaya. 58 Suka fitar da shi bayan gari, suka yi ta jifansa da duwatsu. Shaidu kuwa suka ajiye tufafinsu wurin wani saurayi, mai suna Shawulu. 59 Suna ta jifan Istifanus, shi kuwa ya yi addu'a ya ce, "Ubangiji Yesu, ka karɓi raina." 60 Sai ya durƙusa, ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, "Ubangiji, kada ka riƙe wannan zunubin a kansu." Da faɗar haka, sai ya mutu.

8 1 Shawulu kuwa ya goyi bayan kisan Istifanus.

Shawulu Ya Tsananta wa Jama'ar Masu Bi

A ranan nan kuwa, wani babban tsanani ya fāɗo wa jama'ar masu bin da take a Urushalima. Duk aka warwatsa ta a yankin Yahudiya da na Samariya, sai dai manzannin ne kawai suka rage. 2 Sai waɗansu masu bauta wa Allah suka binne Istifanus, suka yi kuka ƙwarai saboda shi. 3 Amma Shawulu ya yi ta tsananta wa jama'ar masu bi ƙwarai da gaske, yana shiga gida-gida, yana jan maza da mata, yana sa su cikin kurkuku.

An Yi Wa'azin Bishara a Samariya

4 To, waɗanda aka warwatsar dīn nan kuwa, suka yi ta zazzagawa suna yin wa'azin bishara. 5 Filibus ya tafi wani birnin

---

7.49-50: Ish 66.1-2 **7.51:** Ish 63.10 **8.3:** A.M. 22.4-5; 26.9-11

Samariya, yana ta yi musu wa'azin Almasihu. 6 Da mutane suka
ji, suka kuma ga abubuwan ban mamakin da yake yi, da nufi ɗaya
suka mai da hankali ga abin da ya faɗa. 7 Aljanu kuwa da ihu suka
yita fito daga jikin mutane da yawa. Aka warkar da shanyayyu da
guragu da yawa. 8 Saboda haka aka yi farin ciki sosai a birnin.

9 Akwai wani mutum kuwa mai suna Siman, wanda dā yake
yin sihiri a birnin, har yana ba Samariyawa mamaki, yana cewa
shi wani babban mutum ne. 10 Jama'a duka kuwa suka mai da
hankali a kansa, babba da yaro, suna cewa, "Mutumin nan, ai,
ikon nan na Allah ne, da ake ce da shi Mai Girma." 11 Sai suka
mai da hankali sosai a kansa, don ya daɗe yana ta ba su mamaki
da sihirinsa. 12 Amma da suka gaskata Labari Mai Daɗin da
Filibus ya yi a kan mulkin Allah, da kuma sunan Yesu Almasihu,
dukansu aka yi musu baftisma, maza da mata. 13 Har Siman da
kansa ma ya ba da gaskiya. Bayan an yi masa baftisma kuma ya
manne wa Filibus. Da ya ga yadda Filibus yake yin alamu da
manyan abubuwan ban mamaki, sai ya yi mamaki ƙwarai.

14 To, da manzannin da suke Urushalima suka ji Samariyawa
sun karɓi maganar Allah, sai suka aika musu Bitrus da Yohanna.
15 Su kuwa da suka je, suka yi musu addu'a su karɓi Ruhu Mai
Tsarki. 16 Domin Ruhu Mai Tsarki bai sauko wa waninsu ba
tukuna, sai dai kawai an yi musu baftisma ne da sunan Ubangiji
Yesu. 17 Sai Bitrus da Yohanna suka sa musu hannun albarka,
suka kuwa karɓi Ruhu Mai Tsarki.

18 To, da Siman ya ga, ashe ta sa hannun manzanni ne ake
samun Ruhun, sai ya miƙa musu kuɗi, 19 ya ce, "Ni ma ku ba ni
wannan iko, don kowa na sa masa hannu, yă sami Ruhu Mai
Tsarki."

20 Amma Bitrus ya ce masa, "Kai da kuɗinka, ku halaka!
Kana tsammani da kuɗi ne za ka sami kyautar Allah? 21 Ba
ruwanka da wannan sha'anin ko kaɗan, don zuciyarka ba daidai
take ba a gaban Allah. 22 Sai ka tuba daga wannan mugun aiki
naka, ka roƙi Ubangiji ko zai gafarta maka abin nan da ka shirya
a zuciyarka. 23 Gama na ga kana cike da mugun kishi, kana ɗaure
cikin zunubi."

24 Sai Siman ya amsa ya ce, "Ku roƙe mini Ubangiji, kada
ko ɗaya daga cikin abubuwan da kuka faɗa yă faru da ni."

25 To, bayan Bitrus da Yohanna suka yi shaida suka kuma yi
wa'azin Labari Mai Daɗi na maganar Ubangiji, sai suka koma
Urushalima. Yayin da suke komawa Urushalima sai suka yi ta
yin wa'azin Labari Mai Daɗi a ƙauyukan Samariya da yawa.

Filibus da Mutumin Itiyofiya

26 Ana nan sai wani mala'ikan Ubangiji ya ce wa Filibus,
"Tashi ka bi ta kudu, ka bi hanyar da ta fito daga Urushalima
zuwa Gaza," wato hanyar hamada. 27 Sai ya tashi ya tafi. Sai ga
wani mutumin Itiyofiya wanda shi bābā ne, wato, an daƙe shi,
mai babban matsayi a mulkin Kandis, sarauniyar Itiyofiya. Shi
ne kuma ma'ajin sarauniyar. Ya zo Urushalima ne don yă yi
sujada. 28 Da yana komawa gida a zaune cikin keken dokinsa, ya
buɗe littafin annabi Ishaya yana karatu. 29 Sai Ruhu ya ce wa
Filibus, "Matsa ka yi kusa da keken dokin nan." 30 Sai Filibus ya
gudu zuwa wurinsa, ya ji shi yana karatun littafin annabi Ishaya.
Sai Filibus ya tambaye shi, "Ka gane abin da kake karantawa
kuwa?"

31 Sai ya amsa, "Ina fa? Sai ko wani ya yi mini fassara." Sai
ya ce wa Filibus yă hau keken dokin su zauna tare.

32 Ga sashin Rubutaccen Maganar Allah da yake karantawa:

"An ja shi kamar tunkiya zuwa wurin yanka.
Kamar yadda ɗan rago yake shiru a hannun mai aski
masa gashin jikinsa,
haka bai ko buɗe bakinsa ba.
33 An yi masa wulaƙanci
har an hana masa gaskiyarsa.
Wa zai iya bayyana labarin zamaninsa?
Don an ɗauki ransa daga duniya."

34 Sai bābān nan ya ce wa Filibus, "A kan wane ne annabin
nan yake magana ne? A kansa ne ko a kan wani?" 35 Sai Filibus
ya buɗe bakinsa ya fara tun daga wannan sashin Rubutaccen
Maganar Allah, yana ba shi Labari Mai Dadi na Yesu. 36 Suna
cikin tafiya ke nan, suka kai wurin ruwa, sai bābān nan ya ce,
"Duba, ga ruwa! Mene ne zai hana a yi mini baftisma?"[e]

38 Sai ya ba da umarni a tsai da keken dokin. Dukansu biyu
suka sauka suka shiga cikin ruwan, sai Filibus ya yi wa mutumin
nan baftisma. 39 Da suka fito daga cikin ruwan, Ruhun Ubangiji
ya ɗauki Filibus, bābān bai sāke ganinsa ba. Sai mutumin ya yi
tafiyarsa yana farin ciki. 40 Amma Filibus ya ga kansa a Azotus.
Sai ya zazzaga dukan garuruwan, yana ba da Labari Mai Dadi,
har ya kai Kaisariya.

8.32-33: Ish 53.7-8

[e] **8.36** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya ta 37 haka: Filibus ya ce, "Idan dai ka gaskata da zuciya ɗaya, ai, sai ayi maka." Bābā nan ya ce, "Na gaskata, Yesu Almasihu Dan Allah ne."

Tubar Shawulu
(A.M. 22.6-16, 26.12-18)

9 [1] Shawulu kuwa yana ci gaba da yin wa masu bin Ubangiji
tsanani sosai, har da cewa zai kashe su. Sai ya je wurin
babban firist, [2] ya roƙe shi yă ba shi wasiƙu zuwa majami'un
Dimashƙu, don idan ya sami masu bin Hanyar Ubangiji, maza ko
mata, yă kawo su ɗaure a birnin Urushalima. [3] Yana cikin tafiya
ke nan, ya yi kusa da Dimashƙu, ba labari, sai ga wani haske
daga sama ya haskaka kewaye da shi. [4] Sai ya fāɗi a ƙasa, ya
kuma ji wata murya tana ce masa, "Shawulu, Shawulu, don me
kake tsananta mini?"

5 Shi kuwa ya ce, "Wane ne kai, Mai girma?"

Sai muryar ta amsa cewa, "Ni ne Yesu wanda kake tsananta
masa. [6] Ka tashi ka shiga cikin gari, a can za a faɗa maka abin
da za ka yi."

7 Abokan tafiyarsa kuwa suka kāsa magana, suna jin murya,
amma ba su ga kowa ba. [8] Sai Shawulu ya tashi, amma da ya
buɗe ido bai iya gani ba. Sai suka riƙe masa hannu suka kawo
shi Dimashƙu. [9] Ya yi kwana uku, ba ya gani, ba ya ci, kuma ba
ya sha.

10 To, akwai wani mai bi a Dimashƙu, mai suna Hananiya.
Ubangiji ya yi masa magana cikin ru'uya ya ce, "Hananiya!" Shi
kuwa ya amsa, "Ga ni, ya Ubangiji."

11 Sai Ubangiji ya ce masa, "Tashi ka tafi titin nan da ake ce
da shi Miƙaƙƙe, ka je gidan Yahuda, ka tambaya ko akwai wani
mutumin Tarsus, mai suna Shawulu. Ga shi nan yana addu'a a
wurin. [12] Har ma a cikin ru'uya ya ga wani mutum mai suna
Hananiya ya shigo, ya sa masa hannun albarka don ya sāke samun
ganin gari."

13 Amma Hananiya ya amsa ya ce, "Ubangiji, na sha jin
labarin mutumin nan wurin mutane da yawa, kan yawan
muguntar da ya yi wa masu binka a Urushalima. [14] Ga shi kuma
manyan firistoci sun ba shi izni yă kama duk mai yin addu'a da
sunanka ma."

15 Amma Ubangiji ya ce masa, "Kai dai, ka je, domin shi
mutum ne da na zaɓa yă yi aikina domin yă sanar da sunana ga
waɗanda ba Yahudawa ba, da sarakuna, da kuma Isra'ilawa. [16] Ni
da kaina zan nuna masa wuyar da lallai zai sha saboda sunana."

17 Sai Hananiya ya je, ya shiga gidan. Ya miƙa hannu ya taɓa
Shawulu, ya ce, "Dan'uwana Shawulu, Ubangiji ne ya aiko ni,
wato, Yesu wanda ya bayyana a gare ka a kan hanyar da ka biyo.

Yana so ka sāke iya gani, a kuma cika ka da Ruhu Mai Tsarki."
18 Nan take, sai wani abu kamar ɓawo ya fāɗi daga idanun
Shawulu, sai ya sāke gani. Sa'an nan ya tashi, aka yi masa
baftisma. 19 Sai ya ci abinci, ya sāke samun ƙarfi.

Shawulu Ya Yi Wa'azi a Dimashƙu

Shawulu kuwa ya yi 'yan kwanaki tare da sauran masu bin da
suke a Dimashƙu. 20 Ba da daɗewa ba, Shawulu ya fara wa'azin
Yesu a majami'un Yahudawa cewa Yesu shi ne Ɗan Allah. 21 Duk
waɗanda suka ji shi kuwa suka yi mamaki, suka ce, "Ashe, ba
wannan ne ya kakkashe ya kuma watsar da masu yin addu'a da
sunan nan a Urushalima ba? Ba ya zo nan da niyyar yă kai su
gaban manyan firistoci a ɗaure ba ne?"

22 Amma Shawulu ya ƙara samun ƙarfi, yana ta rikitar da
hankalin Yahudawan da suke zama a Dimashƙu, yana tabbatar
musu cewa Yesu shi ne Almasihu.

Shawulu Ya Kuɓuce wa Yahudawa

23 Bayan 'yan kwanaki, Yahudawa suka yi shawara su kashe
Shawulu. 24 Amma shi kuwa ya ji labarin shirinsu. Dare da rana
suna zuba ido a ƙofofin gari don su kashe shi, 25 amma da dare
almajiransa suka ɗauke shi, suka saukar da shi ta wata ƙofa a
jikin bangon birnin cikin babban kwando.

Shawulu Ya Koma Urushalima

26 Da Shawulu ya zo Urushalima, ya yi ƙoƙari yă shiga cikin
almajiran, amma duk suka ji tsoronsa, don ba su yarda shi almajiri
ba ne. 27 Amma Barnaba ya ɗauke shi ya kai shi wurin manzanni.
Ya faɗa musu yadda Shawulu ya ga Ubangiji a hanya, da yadda
Ubangiji ya yi masa magana, da kuma yadda Shawulu ya yi
wa'azi da sunan Yesu a Dimashƙu, ba tsoro. 28 Daga nan Shawulu
ya rika shiga da fita da su a Urushalima, 29 yana wa'azi da sunan
Ubangiji ba tsoro. Ya kuma rika yin magana da Yahudawa masu
jin Helenanci, yana kuma gardama da su, amma suka yi ta neman
hanya su kashe shi. 30 Da 'yan'uwa suka gane haka, sai suka kai
shi Kaisariya, suka aika da shi zuwa Tarsus.

31 Sa'an nan ne jama'ar masu bi na dukan Yahudiya, da Galili,
da Samariya, ta sami zaman lafiya. Jama'ar masu bi ta sami ƙarfi
ta kuma ƙaru sosai ta wurin taimakon Ruhu Mai Tsarki, yayin da
take rayuwa a cikin tsoron Ubangiji.

9.23-25: 2 Kor 11.32-33

Bitrus Ya Warkar da Iniyas

32 To, da Bitrus ya zazzaga yankin duka, sai ya kuma je wurin
tsarkakan nan da suke zama a Lidda. 33 A wurin ya sadu da wani
mutum mai suna Iniyas, wanda yake a kwance shekara takwas
don shi shanyayye ne. 34 Sai Bitrus ya ce masa, "Iniyas, Yesu
Almasihu ya warkar da kai. Tashi ka nade abin kwanciyarka."
Nan da nan Iniyas ya tashi. 35 Duk mutanen Lidda da na ƙasar
Sharon kuwa suka gan shi wanda ya warke, sa'an nan suka juyo
ga Ubangiji.

Bitrus Ya Ta da Tabita daga Matattu

36 A Joffa kuwa akwai wata mai bi, mai suna Tabita, wato,
Dokas*f* ke nan. Macen kuwa ta ba da kanta ɗungum cikin yin
aikin kirki, da kuma yin taimako. 37 A lokacin nan ta yi rashin
lafiya, ta mutu. Da suka yi mata wanka, suka kwantar da jikinta
a ɗakin sama. 38 Da yake Lidda tana kusa da Joffa, sa'ad da
masu bi suka ji Bitrus yana Lidda, sai suka aika mutum biyu
zuwa wurinsa, su roƙe shi yă zo wurinsu da sauri. 39 Sai Bitrus
ya tashi ya tafi tare da su. Da ya iso, suka kai shi ɗakin saman.
Duk mata waɗanda mazansu suka mutu, suka tsaya kusa da shi,
suna kuka, suna nuna riguna da sauran kayan da Dokas ta yi
musu tun tana tare da su. 40 Bitrus ya fitar da su waje duka, ya
durƙusa ya yi addu'a. Ya juya wajen gawar, ya ce, "Tabita,
tashi." Sai ta buɗe ido. Da ta ga Bitrus, sai ta tashi ta zauna.
41 Bitrus kuwa ya miƙa mata hannu ya taimake ta ta tashi. Sai
ya kira masu bi, da matan nan waɗanda mazansu suka mutu, ya
miƙa musu ita da rai. 42 Labarin nan ya bazu a dukan Joffa,
mutane da yawa kuwa suka gaskata da Ubangiji. 43 Bitrus ya
zauna kwanaki da yawa a Joffa, a gidan wani mai aikin fatun
dabbobi, sunansa Siman.

Bitrus Ya Ziyarci Babban Sojan Roma

10 1 Akwai wani mutum a Kaisariya mai suna Koneliyus. Shi
wani babban sojan Roma ne na ƙungiyar sojan da ake ce
da ita Kungiyar Italiya. 2 Shi kuwa mutum ne mai bi, yana tsoron
Allah, shi da iyalinsa duka. Yana ƙoƙari sosai wajen taimakon
talakawan Yahudawa, yana kuma yin addu'a ga Allah kullum.
3 Wata rana, wajen ƙarfe uku na yamma, ya ga wani mala'ikan
Allah a fili a cikin ru'uya, ya zo wurinsa, ya ce, "Koneliyus!"

*f***9.36 Dokas:** "Tabita" a yaren Aramaya da "Dokas" a Helenanci duk suna nufin wani irin naman daji ne kamar barewa.

4 Shi kuwa ya zuba masa ido cikin tsoro ya ce, "Ubangiji,
mene ne?"
Mala'ikan kuma ya ce masa, "Addu'arka da taimakon talakawan
da kake yi sun kai har gaban Allah, abubuwan tunawa ne kuma a
gare shi. 5 Ka aika mutane yanzu zuwa Joffa su kirawo Siman,
wanda ake ce da shi Bitrus. 6 Ya sauka a gun Siman mai aikin fata,
wanda gidansa yake a bakin teku." 7 Da mala'ikan da ya yi masa
magana ya tafi, sai Koneliyus ya kira bayinsa biyu, da kuma wani
soja mai bin Allah daga cikin waɗanda suke yi masa aiki kullum.
8 Bayan ya faɗa musu kome duka, sai ya aike su zuwa Joffa.
9 Washegari, kusan tsakar rana, bayin Koneliyus suna cikin
tafiya, sun zo kusa da garin ke nan, sai Bitrus ya hau kan ɗakin
sama don yă yi addu'a. 10 Yunwa ta kama shi, har ya so yă ci wani
abu. Amma da ana cikin shirya abincin, sai ya ga ru'uya. 11 Ya ga
sama ya buɗe, wani abu kuma yana saukowa kamar babban mayafi,
ana sauko da shi ƙasa ta kwanansa huɗu. 12 A cikinsa akwai kowace
irin dabba. Akwai masu ƙafa huɗu, da masu rarrafe, da tsuntsaye.
13 Sai ya ji wata murya ta ce masa, "Bitrus, tashi ka yanka
ka ci."



Hoton ru'uyar da Bitrus ya gani, (10.11-12)

14 Amma Bitrus ya ce, "Sam! Ubangiji, ban taɓa cin wani abu
marar tsarki ko marar tsabta ba."
15 Sai ya sāke jin murya, sau na biyu, ta ce, "Abin da Allah
ya tsarkake, kada ka ce da shi marar tsarki." 16 Wannan ya faru
sau uku, sai nan da nan aka ɗauki abin zuwa sama.
17 Bitrus yana cikin damuwa ƙwarai a kan ko mece ce ma'anar
ru'uyar da aka nuna masa, sai ga mutanen da Koneliyus ya aiko,
suna tsaye a ƙofa, sun riga sun tambayi gidan Siman. 18 Suna
sallama, suna tambaya ko Siman da ake ce da shi Bitrus ya sauka
a wurin.
19 Tun Bitrus yana tunani a kan ru'uyan nan, Ruhu ya ce
masa, "Ga mutum uku[g] nan suna nemanka. 20 Tashi, ka sauka,
ka bi su. Kada ka yi shakka, don ni ne na aiko su." 21 Sai Bitrus
ya sauka zuwa wurin mutanen, ya ce musu, "Ni ne kuke nema?
Wane dalili ne ya kawo ku?"
22 Sai suka ce, "Wani babban sojan Roma ne, mai suna
Koneliyus, ya aike mu. Shi mutumin kirki ne, mai tsoron Allah,
wanda duk jama'ar Yahudawa suke faɗin abin kirki a kansa. Shi
ne wani mala'ika mai tsarki ya umarce shi yă aiko ka je gidansa,
yă ji abin da za ka ce." 23 Sai Bitrus ya shigo da su, ya ba su
wurin kwana.
Washegari ya tashi, suka tafi tare, waɗansu masu bi daga
garin Joffa kuma suka raka shi. 24 Washegari kuma suka shiga
Kaisariya. Dā ma Koneliyus yana sa rai za su zo, har ya kirawo
'yan'uwansa duka da abokansa. 25 Bitrus yana shiga gidan ke
nan, sai Koneliyus ya tarye shi, ya fāɗi a gabansa, ya yi masa
sujada. 26 Amma Bitrus ya sa yă tashi, ya ce, "Tashi, ai, ni ma
mutum ne." 27 Bitrus yana magana da shi, sai ya shiga ya sami
mutane da yawa sun taru. 28 Sai ya ce musu, "Ku da kanku kun
sani cewa bai kamata Bayahude yă haɗa kai ko yă ziyarci wani
na wata kabila dabam ba. Amma Allah ya nuna mini kada in ce
da kowa marar tsarki, ko mai ƙazanta. 29 Saboda haka, da aka
aika in zo, ban ce a'a ba. To, yanzu ina so in san abin da ya sa
kuka kira ni."
30 Sai Koneliyus ya ce, "Kwana uku da suka wuce, kamar
wannan lokacin, wajen ƙarfe uku na yamma, ina addu'a a gidana,
sai ga wani mutum ya tsaya a gabana. Kayan da ya sa kuwa masu
haske ne sosai. 31 Mutumin ya ce, 'Koneliyus, an amsa addu'arka,
taimakon talakawan da kake yi kuma ya zama abin tunawa ga

[g] **10.19 Ga mutum uku:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "waɗansu" ne a nan. Daya kuma yana da "biyu" ne a nan.

Allah. 32 Saboda haka sai ka aika zuwa Joffa a kirawo Siman,
wanda ake ce da shi Bitrus, ya sauka a gidan Siman mai aikin
fata, wanda gidansa yana a bakin teku.' 33 Shi ya sa na aika a kira
ka, ka kuma kyauta da ka zo. To, ga mu duk mun taru a gaban
Allah, don mu saurari duk abin da Ubangiji ya umarce ka."

Bitrus Ya Yi Jawabi a Gidan Koneliyus

34 Sai Bitrus ya soma yin musu magana ya ce, "Lallai, na
gane Allah ba ya nuna bambanci, 35 amma yana karɓar duk mai
tsoronsa, da kuma mai aikata adalci wato, yin rayuwar da Allah
yake so, a kowace al'umma. 36 Kun san saƙon da ya aiko wa
jama'ar Isra'ila, ana ba su Labari Mai Daɗi na salama ta wurin
Yesu Almasihu, shi ne kuwa Ubangijin kowa. 37 Kun san yadda
labarin nan ya bazu a dukan Yahudiya, ya fara tun daga cikin
Galili, bayan baftismar da Yohanna ya yi wa'azi. 38 Kun san
labarin Yesu Banazare, yadda Allah ya shafe shi da Ruhu Mai
Tsarki, da kuma iko. Domin Allah yana tare da shi, ya riƙa
zagawa yana yin aikin alheri, yana warkar da duk waɗanda
Shaiɗan ya matsa musu. 39 Mu kuwa shaidu ne ga duk abin da
Yesu ya yi a ƙasar Yahudawa, da kuma cikin Urushalima. Shi ne
kuma suka kashe shi ta wurin gicciye shi a kan gungumen itace.
40 Amma Allah ya ta da shi a rana ta uku, ya kuma yarda yă
bayyana ga mutane. 41 Bai bayyana ga dukan jama'a ba, sai dai
ga mu, wato, mu da Allah ya zaɓa tun dā don mu zama shaidu.
Mu ne muka ci, muka sha tare da shi, bayan ya tashi daga matattu.
42 Ya kuma umarce mu mu yi wa mutane wa'azi, mu kuma yi
shaida cewa shi ne wanda Allah ya sa yă zama mai yi wa masu
rai da matattu shari'a. 43 Duk annabawa sun yi shaida a kansa
cewa ta wurin sunansa duk wanda ya ba da gaskiya gare shi zai
sami gafarar zunubai."

An Ba Wa Waɗanda ba Yahudawa ba Ruhu Mai Tsarki

44 Bitrus yana cikin magana, sai Ruhu Mai Tsarki ya sauko a
kan dukan waɗanda suke jin maganarsa. 45 Yahudawa masu bi,
waɗanda suka zo tare da Bitrus, suka yi mamakin ganin waɗanda
ba Yahudawa ba su ma sun sami baiwar Ruhu Mai Tsarki.
46 Gama sun ji suna magana da harsuna,[h] suna ɗaukaka Allah.
Sa'an nan Bitrus ya ce, 47 "Akwai wani da zai hana a yi wa

10.34: M. Sh 10.17

[h] **10.46 harsuna:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Waɗansu yare dabam-dabam" ne a nan.

waɗannan mutane baftisma da ruwa? Ai, su ma sun sami Ruhu Mai Tsarki kamar yadda mu ma muka samu." 48 Sai Bitrus ya ba da umarni a yi musu baftisma cikin sunan Yesu Almasihu. Sa'an nan suka roƙe shi yă zauna da su na 'yan kwanaki.

Bitrus Ya Yi wa Jama'ar Masu Bi a Urushalima Bayani

11 1 Manzanni da sauran masu bi da suke a ko'ina a Yahudiya
suka ji cewa waɗanda ba Yahudawa ba ma sun karɓi
maganar Allah. 2 Da Bitrus ya je Urushalima, waɗansu manyan
Yahudawa masu bi, waɗanda suka tsaya a kan al'adarsu ta kaciya,
suka yi masa faɗa. 3 Suka ce, "Don me ka je wurin marasa kaciya,
har ka ci abinci tare da su?"

4 Sai Bitrus ya fara yi musu bayani dalla-dalla cewa:

5 "Ina birnin Joffa ina addu'a, sai na ga ru'uya, na ga wani
abu yana saukowa kamar babban mayafi, an sauko da shi daga
sama ta kwanansa huɗu, har ya iso kusa da ni. 6 Da na dube
shi sosai, na ga dabbobi masu ƙafa huɗu, da namomin daji, da
masu rarrafe, da kuma tsuntsaye a ciki. 7 Na kuma ji wata murya
ta ce mini, 'Bitrus, ka tashi, ka yanka ka ci.' 8 Amma na ce,
'Sam! Ubangiji, ba wani abu marar tsarki, ko marar tsabta, da
ya taɓa shiga bakina.' 9 Sai murya ta amsa daga sama ta yi
magana sau na biyu, ta ce, 'Abin da Allah ya tsarkake, kada ka
ce da shi marar tsarki.' 10 An yi wannan sau uku, sa'an nan aka
ɗauki abin zuwa sama. 11 A daidai wannan lokacin, sai ga
mutum uku sun tsaya a bakin ƙofar gidan da nake,[i] an aiko su
wurina ne daga Kaisariya. 12 Sai Ruhu ya ce mini in bi su, kada
in nuna bambanci tsakanin su da mu. 'Yan'uwan nan shida
kuma suka rako ni, har muka shiga gidan mutumin nan. 13 Sai
ya faɗa mana yadda ya ga mala'ika ya tsaya a gidansa, yana
cewa, 'Ka aika zuwa Joffa a kirawo Siman, wanda ake ce da
shi Bitrus. 14 Shi zai kawo maka saƙon da za ka sami ceto ta
wurinsa, kai da mutanen gidanka duka.' 15 Na fara yin musu
magana ke nan, sai Ruhu Mai Tsarki ya sauko musu, daidai
yadda ya sauko mana da farko. 16 Sai na tuna da maganar
Ubangiji, yadda ya ce, 'Yohanna dai ya yi baftisma da ruwa,
amma ku da Ruhu Mai Tsarki za a yi muku baftisma.' 17 To,
da yake Allah ya yi musu baiwa daidai da wadda ya yi mana,
sa'ad da muka ba da gaskiya ga Ubangiji Yesu Almasihu, wane
ni in hana Allah!"

11.16: A.M. 1.5

[i] **11.11 nake:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "muke" ne a nan.

18 Da Yahudawa masu bi suka ji haka, suka rasa abin da za
su ce, sai suka yabi Allah suna cewa, "Ashe, har waɗanda ba
Yahudawa ba ma Allah ya yi musu hanyar tuba da samun rai."

Jama'ar Masu Bi a Antakiya ta Suriya

19 To, masu bi suka warwatse saboda tsananin nan da ya tashi
saboda kashewar Istifanus. Waɗansu suka tafi har zuwa ƙasar
Finikiya da Sayifurus, da birnin Antakiya. Suna wa'azin maganar
Allah, amma ga Yahudawa kaɗai. 20 Amma akwai waɗansu masu
bi daga Sayifurus da Sayirin, waɗanda suka tafi Antakiya suka yi
wa Helenawa magana, suna ba su Labari Mai Daɗi na Ubangiji
Yesu. 21 Ikon Ubangiji kuwa yana tare da su, har mutane da yawa
suka tuba, suka juyo wurin Ubangiji. 22 Labarin abin da ya faru a
Antakiya kuwa ya kai kunnen jama'ar masu bin da take a
Urushalima. Jama'ar masu bi kuma ta aika Barnaba zuwa can
Antakiya.

23 Da ya zo, ya kuma ga alherin da Allah ya yi musu, ya yi
farin ciki, ya gargaɗe su duka su tsaya da bangaskiya cikin
Ubangiji da dukan zuciyarsu. 24 Barnaba kuwa mutumin kirki ne,
cike da Ruhu Mai Tsarki da bangaskiya. Sai mutane masu yawan
gaske suka juyo zuwa wurin Ubangiji. 25 Daga nan sai Barnaba
ya tafi Tarsus don yă nemi Shawulu. 26 Da ya same shi kuwa, sai
ya kawo shi Antakiya. Shekara ɗaya cif, suna taruwa da jama'ar
masu bi, suna koya wa mutane masu yawan gaske. A Antakiya
ne aka fara kiran masu bin Almasihu da suna Kirista.

27 To, a wannan lokacin ne waɗansu annabawa suka zo
Antakiya daga Urushalima. 28 Ɗaya daga cikinsu, mai suna Agabus,
ya tashi tsaye, ya yi magana da ikon Ruhu cewa za a yi wata babbar
yunwa a duniya duka. (Wannan kuwa ya faru a zamanin
Kalaudiyus.) 29 Sai almajiran suka yanke shawara cewa su aika wa
'yan'uwan da suke cikin Yahudiya taimako, kowa daidai ƙarfinsa.
30 Haka kuwa suka yi, suka aika wa dattiban jama'ar masu bi a
Yahudiya taimakon ta hannun Barnaba da Shawulu.

An Kara Tsananta wa Jama'ar Masu Bi

12 1 A lokacin nan kuwa sarki Hirudus ya fara tsananta wa
waɗansu a cikin jama'ar masu bi. 2 Hirudus ya sa aka
kashe Yakubu, ɗan'uwan Yohanna, da takobi. 3 Da ya ga
Yahudawa sun ji daɗin abin da ya yi, sai ya kama Bitrus shi ma.
Wannan ya faru a kwanakin Bikin Burodi Marar Yisti ne. 4 Da

11.19: A.M. 8.1-4 **11.28:** A.M. 21.10

Hirudus ya kama Bitrus, ya sa shi a kurkuku a hannun sojoji goma sha shida su yi gadinsa. Yana da niyya yă kawo shi gaban jama'a yă hukunta shi bayan bikin.

5 Sa'ad da Bitrus yake a kurkuku, jama'ar masu bi kuwa ta nace da yin addu'a ga Allah saboda shi.

An Ceci Bitrus daga Kurkuku

6 A daren nan da Hirudus yana tunani zai fitar da Bitrus idan gari ya waye, Bitrus kuwa yana ɗaure da sarƙa biyu, yana barci tsakanin sojoji biyu. Masu gadin kurkuku kuma suna bakin ƙofa suna gadi. 7 Ba labari, sai ga wani mala'ikan Ubangiji ya bayyana, wani haske kuma ya haskaka ɗakin. Sa'an nan mala'ikan ya taɓa Bitrus a gefe ya tashe shi, ya ce, "Maza ka tashi." Sai kuma sarƙoƙin suka fita daga hannun Bitrus. 8 Mala'ikan ya ce masa, "Ka sa rigarka, ka kuma sa takalmanka." Sai ya yi haka. Mala'ikan ya ce masa, "Yafa mayafinka ka biyo ni." 9 Sai ya fito ya bi shi, bai san cewa abin da mala'ikan nan yake yi gaskiya ba ne, ya ɗauka ru'uya ce yake gani. 10 Da suka wuce masu gadi na farko da na biyu, suka kai ƙofar ƙarfe ta shiga gari, ƙofar kuwa ta buɗe musu da kanta. Sai suka fita. Sun zo ƙarshen wani titi ke nan sai nan take mala'ikan ya rabu da shi.

11 Sa'an nan Bitrus ya komo cikin hankalinsa ya ce, "Yanzu kam na tabbata Ubangiji ne ya aiko mala'ikansa yă cece ni daga hannun Hirudus, da kuma dukan muguntar da Yahudawa suka shirya a kaina." 12 Da Bitrus ya gane haka, sai ya je gidan Maryamu, mamar Yohanna wanda ake ce da shi Markus, inda mutane suka taru da yawa suna addu'a.

13 Da ya ƙwanƙwasa ƙofar zauren, wata yarinya mai aiki a gidan mai suna Roda ta zo ta ga ko wane ne. 14 Da ta gane muryar Bitrus, ba ta buɗe ƙofar ba don murna, sai ta koma ciki da gudu, ta gaya musu cewa Bitrus yana tsaye a ƙofar zaure. 15 Sai suka ce mata, "Kina hauka!" Ita kuwa ta nace cewa shi ne. Su kuwa suka ce, "To, mala'ikansa ne!"

16 Bitrus dai ya yi ta ƙwanƙwasawa. Da suka buɗe suka gan shi, suka yi ta mamaki. 17 Shi kuwa ya yi musu alama da hannu su yi shiru, sa'an nan ya bayyana musu yadda Ubangiji ya fito da shi daga kurkuku. Ya kuma ce, "Ku faɗa wa Yakubu da sauran 'yan'uwa wannan abu." Sa'an nan ya tashi ya tafi wani wuri.

12.4: Fit 12.1-27

18 Da gari ya waye, ba ƙaramar ruɗewa ce ta tashi tsakanin
sojojin nan ba, a kan abin da ya sami Bitrus. 19 Da Hirudus ya
neme shi bai same shi ba, sai ya tuhume masu gadin, ya kuma
ba da umarni a kashe su.

Bayan wannan Hirudus ya tashi daga Yahudiya, ya tafi
Kaisariya ya yi 'yan kwanaki a can.

Mutuwar Hirudus

20 A lokacin nan, Hirudus yana fushi sosai da mutanen Taya
da na Sidon. Suka zo wurin Hirudus da nufi ɗaya, suka kuma
nemi goyon bayan Bilastus sarkin fada, shi kuwa ya yarda yă
taimake su. Sa'an nan suka je wurin Hirudus suka nemi zaman
lafiya, domin suna dogara ne ga ƙasar sarkin nan saboda
abincinsu. 21 A ranar da aka shirya, Hirudus ya sa kayansa na
sarauta, ya zauna a kujerar sarauta, ya yi musu jawabi. 22 Da taron
suka ji shi sai suka ta da murya "Ku ji wannan fa!" suna cewa,
"Muryar wani allah ne, ba ta mutum ba!" 23 Nan take, sai wani
mala'ikan Ubangiji ya buge shi, don bai ɗaukaka Allah ba. Sai
tsutsotsi suka yi ta cinsa har ya mutu.

24 Maganar Allah kuwa ta yi ta ci gaba, tana ta yaɗuwa. 25 Sai
Barnaba da Shawulu suka dawo daga[j] Urushalima, bayan sun cika
aikin da aka ba su su yi, suka kuma zo da Yohanna wanda ake
ce da shi Markus.

An Zaɓi An kuma Aiki Barnaba da Shawulu

13 1 To, a jama'ar masu bin da take a Antakiya, akwai
waɗansu annabawa da malamai, wato, Barnaba, da
Simiyon wanda ake ce da shi Baƙi, da Lushiyos daga Sayirin, da
Manayen (wanda ya yi girma tare da sarki Hirudus), da kuma
Shawulu. 2 Sa'ad da suke yi wa Ubangiji sujada, suna kuma yin
azumi, sai Ruhu Mai Tsarki ya ce, "Ku keɓe mini Barnaba da
Shawulu domin aikin da na kira su su yi." 3 Bayan da suka yi
azumi da addu'a, sai suka sa wa Barnaba da Shawulu hannun
albarka, suka sallame su.

Barnaba da Shawulu a Sayifurus

4 Barnaba da Shawulu kuwa, bayan da Ruhu Mai Tsarki ya
aike su, suka tafi Salukiya, daga can kuma suka shiga jirgin ruwa
zuwa Sayifurus. 5 Da suka kai Salamis, suka yi wa'azin maganar

[j] **12.25 daga:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "zuwa" ne a nan.

Allah a majami'un Yahudawa. Yohanna kuma yana tare da su yana taimakonsu.

6 Bayan sun zazzaga tsibirin duka har Bafos, suka sadu da wani Bayahude mai sihiri, shi annabin ƙarya ne, mai suna Bar-Joshu'a, 7 wanda yake tare da gwamna Sarjiyus Bulus. Gwamna Sarjiyus Bulus kuwa mutum mai hikima ne. Sai gwamnan ya kira Barnaba da Shawulu don yana so yă ji maganar Allah. 8 Amma mai sihirin nan Alimas, (don sunansa ke nan da Helenanci), bai ba su goyon baya ba, yana nema yă juye hankalin gwamnan nan don kada yă ba da gaskiya. 9 Amma Shawulu kuwa, wanda ake ce da shi Bulus, cike da Ruhu Mai Tsarki, ya zuba wa Alimas ido, 10 ya ce, "Kai ɗan Shaiɗan! Mai gāba da duk abin da yake na adalci! Kana cike da rudi, dà mugunta kawai. Ba za ka daina ɓata miƙaƙƙun hanyoyin Ubangiji ba? 11 Yanzu fa, fushin Ubangiji yana kanka, za ka zama makaho. Za a ɗauki ɗan lokaci ba ka ga hasken rana ba."

Nan take kuwa sai wani hazo da duhu suka rufe idanunsa, ya yi ta lalubawa yana neman wanda zai yi masa jagora. 12 Da gwamna ya ga abin da ya faru, sai ya ba da gaskiya, yana mamakin koyarwar maganar Ubangiji.

Bulus da Barnaba a Antakiya ta Bisidiya

13 Sai Bulus da abokan tafiyarsa suka tashi daga Bafos a cikin jirgin ruwa, suka je Ferga ta ƙasar Bamfiliya. Yohanna wanda ake ce da shi Markus kuwa ya bar su ya koma Urushalima. 14 Su kuwa suka ci gaba daga Ferga, suka tafi Antakiya ta ƙasar Bisidiya. Ranar Hutu kuwa suka shiga majami'a suka zauna. 15 Bayan an yi karatu daga Dokar Musa da littattafan annabawa, sai shugabannin majami'a suka aika musu cewa, "'Yan'uwa, idan kuna da wata maganar gargaɗin da za ku yi wa jama'a, sai ku yi."

16 Sai Bulus ya miƙe tsaye, ya ɗaga hannu a yi shiru, ya ce: "Ku 'yan'uwana Isra'ilawa, da sauran masu tsoron Allah, ku saurara! 17 Allahn jama'ar Isra'ila ya zaɓi kakanninmu, ya mai da jama'an nan al'umma mai girma a lokacin da suke a ƙasar Masar, ya kuma fito da su daga ƙasar da maɗaukakin iko. 18 Ya yi haƙuri da su wajen shekara arba'in a cikin daji. 19 Bayan ya halaka al'umma bakwai a ƙasar Kan'ana, ya ba jama'ar Isra'ila gādon ƙasar. 20 Wannan ya ɗauki wajen shekara ɗari huɗu da hamsin.

13.17: Fit 1.7; 12.51 **13.18:** L. Kid 14.34; M. Sh 1.31 **13.19:** M. Sh 7.1; Josh 14.1

"Bayan haka kuma Allah ya naɗa musu alƙalai har zuwa
zamanin annabi Sama'ila. 21 Sa'an nan suka roƙa a naɗa musu
sarki, sai Allah ya ba su Shawulu ɗan Kish, mutumin kabilar
Benjamin, wanda ya yi mulki har shekara arba'in. 22 Bayan Allah
ya cire Shawulu, ya sa Dawuda yă zama sarkinsu. Cikin shaidar
da Allah ya bayar game da Dawuda, ya ce, 'Na sami Dawuda
ɗan Jesse, mutum ne da nake ƙauna sosai, wanda kuma zai aikata
dukan nufina.' 23 Daga zuriyar mutumin nan ne Allah ya kawo
wa Isra'ila Mai Ceto, Yesu, kamar yadda ya yi alkawari. 24 Kafin
zuwan Yesu, Yohanna ya yi wa mutanen Isra'ila duka wa'azi su
tuba a kuma yi musu baftisma. 25 Yayin da Yohanna ya kusa gama
aikinsa, sai ya ce, 'Wa kuke tsammani nake? Ba fa ni ne shi ɗin
nan ba. Amma akwai wani da zai zo a bayana, wanda ko igiyar
takalmansa ma ban isa in kunce ba.'

26 "Ku 'yan'uwana, zuriyar Ibrahim, da kuma waɗanda ba
Yahudawa ba masu tsoron Allah a cikinku, mu ne fa aka aiko
mana labarin ceton nan. 27 Gama masu zama a Urushalima da
shugabanninsu ba su gane shi ne Mai Ceton ba, ba su kuma
gane maganar annabawan da ake karantawa a kowace Ranar
Hutu ba. Amma sun cika wannan maganar annabawa ta wurin
hukunta Yesu. 28 Ko da yake ba su same shi da laifin da za a
kashe shi ba, duk da haka suka roƙi Bilatus a kashe shi. 29 Da
suka cika duk abin da aka rubuta game da shi, sai suka sauko
da shi daga kan gungumen itace, suka sa shi a kabari. 30 Amma
Allah ya tashe shi daga matattu. 31 Kwanaki da yawa kuwa yana
ta bayyana ga waɗanda suka bi shi zuwa Urushalima daga Galili,
waɗanda yanzu su ne shaidunsa ga jama'a. 32 Mu ma mun kawo
muku bishara, cewa alkawarin nan da Allah ya yi wa
kakanninmu, 33 ya cika mana shi, mu da muke 'ya'yansu, sa'ad
da ya ta da Yesu daga matattu. Kamar yadda yake a rubuce cikin
Zabura ta biyu cewa,

'Kai Ɗana ne,
Na zama ubanka yau.'

34 "Allah ya ta da Yesu daga matattu a kan cewa Yesu ba zai
sāke mutuwa ba balle yă ruɓa. Hakika, Allah ya cika wannan
magana game da tashinsa cewa:

13.20: L. Mah 2.16; 1 Sam 3.20 **13.21:** 1 Sam 8.5; 10.21
13.22: 1 Sam 13.14; 16.12; Zab 89.20 **13.23:** Ish 11.1-16 **13.24** Mar 1.4; Luk 3.3
13.25: Mat 3.11; Mar 1.7; Luk 3.16; Yoh 1.20,27
13.28: Mat 27.22; Mar 15.13-14; Luk 23.21-23; Yoh 19.15
13.29: Mat 27.57-61; Mar 15.42-47; Luk 23.50-56; Yoh 19.38-42 **13.31:** A.M. 1.3
13.33: Zab 2.7

'Zan ba ka albarkun nan masu tsarki kuma tabbatattu
waɗanda na yi wa Dawuda alkawari.'
35 Domin a wata Zabura ma ya ce, 'Ba za ka bar Mai Tsarkinka
yă ruɓa ba.'
36 "Bayan da Dawuda ya cika aikin da Allah ya ba shi a
zamaninsa, sai ya mutu, aka kuwa binne shi tare da kakanninsa,
jikinsa kuma ya ruɓe. 37 Amma Yesu wanda Allah ya ta da shi
daga matattu bai ruɓa a kabari ba.
38 "Saboda haka 'yan'uwana, ku san wannan cewa ta wurin
Yesun nan ne ake sanar da gafarar zunubanku. 39 Ta wurinsa
kuma duk wanda ya ba da gaskiya ya sami 'yanci ke nan daga
dukan zunuban da Dokar Musa ta kāsa ba da 'yanci a kai.
40 Saboda haka sai ku mai da hankali, kada abin nan da Allah ya
faɗa cikin littattafan annabawa yă faru da ku, wato:
41 'Ku saurara, ku masu yin ba'a!
Ku ruɗe da mamaki, ku mutu!
Domin zan yi wani aiki a kwanakinku,
aikin da ba za ku gaskata ba,
ko da wani ya gaya muku.' "
42 Bulus da Barnaba suna fita daga majami'ar ke nan, sai
mutane suka roƙe su su ƙara yi musu magana a kan abubuwan
nan kuma a Ranar Hutu mai zuwa. 43 Da jama'a suka watse,
Yahudawa da yawa, da kuma waɗansu waɗanda ba Yahudawa ba
da suka shiga addinin Yahudanci, suka bi Bulus da Barnaba. Su
kuma suka yi musu magana, suka ƙarfafa su su ci gaba da rayuwa
cikin alherin Allah.
44 Da Ranar Hutu ta kewayo, kusan duk birnin suka taru don
su ji maganar Allah. 45 Amma da Yahudawa suka ga taron mutane
masu yawa, suka yi kishi sosai, suna mūsun abubuwan da Bulus
ya faɗa suna zaginsa. 46 Amma Bulus da Barnaba suka yi magana
ba tsoro, suka ce: "Ku Yahudawa ku ne ya kamata a fara yi muku
maganar Allah. Amma tun da kuka ƙi ta, kun nuna ba ku cancanci
ku sami rai na har abada ba. To, za mu je wurin waɗanda ba
Yahudawa ba. 47 Domin Ubangiji ya riga ya umarce mu da ya ce:
'Na sa ka ka zama haske ga waɗanda ba Yahudawa ba,
Don ka kawo ceto har zuwa ƙarshen duniya.' "
48 Da waɗanda ba Yahudawa ba suka ji haka, suka ji daɗi
sosai, suka yabi maganar Ubangiji. Waɗanda aka shirya musu
samun rai na har abada kuma suka ba da gaskiya.

13.34: Ish 55.3 **13.35**: Zab 16.10 **13.41**: Hab 1.5 **13.47**: Ish 42.6; 49.6

49 Maganar Ubangiji kuwa sai ta ƙara bazu a ƙasar duka.
50 Amma Yahudawa suka zuga waɗansu mata masu tsoron
Allah, waɗanda ake ba su girma, da kuma waɗansu manyan
mutanen garin. Suka ta da tsanani ga Bulus da Barnaba, suka
kore su daga garinsu. 51 Manzannin kuwa suka kakkaɓe ƙurar
ƙafafunsu don shaida a kan mutanen garin, suka tafi Ikoniya.
52 Masu bi na Antakiya kuma suna farin ciki sosai, suna kuma
cike da Ruhu Mai Tsarki.

Bulus da Barnaba a Ikoniya

14 1 To, a Ikoniya, Bulus da Barnaba suka shiga majami'ar
Yahudawa kamar yadda sun saba. Suka yi wa'azi, har
mutane masu yawa, Yahudawa da waɗanda ba Yahudawa ba,
suka ba da gaskiya. 2 Amma Yahudawan da suka ƙi gaskata, suka
zuga waɗanda ba Yahudawa ba, suka ɓata tsakaninsu da masu bi.
3 Duk da haka Bulus da Barnaba suka daɗe a nan sosai, suna
wa'azi da zuciya ɗaya bisa ga ikon Ubangiji. Ubangiji kuwa ya
yi shaidar maganar alherinsa ta wurin ba da iko a yi alamu da
abubuwan ban mamaki ta hannunsu.
4 Amma mutanen garin suka rabu kashi biyu, waɗansu suna
goyon bayan Yahudawa, waɗansu kuma suna goyon bayan
manzannin. 5 Sai waɗanda ba Yahudawa ba da Yahudawa tare da
shugabanninsu suka yi shiri don su wulaƙanta manzannin, su
jejjefe su da duwatsu.
6 Da manzannin suka ji haka, sai suka gudu zuwa biranen
Likoniya, wato, Listira da Darbe, da kuma kewayensu. 7 A wurin
suka ci gaba da wa'azin Labari Mai Daɗi.

Bulus Ya Yi Wa'azi a Listira

8 A Listira kuwa akwai wani mutum wanda shi gurgu ne, bai
taɓa yin tafiya ba tun da aka haife shi. Yana zaune, 9 yana
sauraron wa'azin Bulus. Sai Bulus ya zuba masa ido. Da Bulus
ya ga mutumin yana da bangaskiyar da za ta isa a warkar da shi,
10 sai ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, "Tashi ka tsaya kan
ƙafafunka." Mutumin kuwa ya tashi ya fara tafiya. 11 Da taron
suka ga abin da Bulus ya yi, suka ɗaga murya gaba ɗaya suna
cewa da yaren Likoniya, "Lallai, alloli sun sauko mana da siffar
mutane!" 12 Sai suka ba Barnaba suna Zeyus, Bulus kuwa suka
ce da shi Hermes, domin shi ne shugaban magana. 13 Sai sarkin
tsafin Zeyus, wanda ɗakin gunkinsa yake a bayan gari, ya kawo

13.51: Mat 10.14; Mar 6.11; Luk 9.5; 10.11

shanu da fure a ƙofar gari. Sarkin tsafin da jama'a suna so su yi wa manzannin hadaya.

14 Amma da manzannin nan Barnaba da Bulus, suka ji haka, sai suka yayyage rigunansu don ɓacin rai, suka shiga cikin taron da gudu, suna ɗaga murya suna cewa, 15 "Don me kuke yin haka? Ai, mu ma mutane ne kamarku, mun dai kawo muku Labari Mai Daɗi ne, domin ku juya wa abubuwan banzan nan baya, ku kuma juyo ga Allah mai rai, wanda ya halicci sama da ƙasa, da teku, da kuma dukkan abin da yake cikinsu. 16 A zamanin dā, ya bar dukan mutane su yi yadda suka ga dama. 17 Duk da haka kuwa bai taɓa barin kansa babu shaida ba. Shi yake ba ku ruwan sama, da damina mai albarka. Yana ƙosar da ku da abinci, yana kuma sa ku yi farin ciki." 18 Duk da waɗannan maganganun ma da kyar suka hana jama'an nan yin hadaya dominsu.

19 Amma waɗansu Yahudawa suka zo daga Antakiya da Ikoniya suka rinjayi taron, suka jejjefi Bulus, suka ja shi zuwa bayan gari, suna tsammani ya mutu. 20 Amma da masu bi suka kewaye shi, sai ya tashi ya koma cikin gari. Washegari kuma ya tafi Darbe tare da Barnaba.

Komawa Antakiya ta Suriya

21 Bayan Bulus da Barnaba suka yi wa'azin Labari Mai Daɗi a Darbe, sun kuma sami almajirai da yawa, suka koma Listira, da Ikoniya, da kuma Antakiya ta Bisidiya. 22 Suna ƙarfafa masu bi, suna yi musu gargaɗi su tsaya da ƙarfi cikin bangaskiya. Suna cewa, "Sai tare da shan wuya mai yawa za mu shiga mulkin Allah." 23 Bayan kuma sun zaɓa musu dattibai a kowace jama'ar masu bi, tare da addu'a da azumi, suka miƙa su ga Ubangiji wanda suka gaskata da shi.

24 Sun bi ta ƙasar Bisidiya zuwa Bamfiliya. 25 Da kuma suka faɗa maganar Allah a Ferga, sai suka tafi Ataliya. 26 Daga nan kuma suka shiga jirgin ruwa suka koma Antakiya, inda tun dā aka yi musu fatar alherin Allah ya kiyaye su cikin aikin nan da suka gama.

27 Da suka iso, suka tara jama'ar masu bi suka ba da labarin dukan abin da Allah ya yi ta wurinsu, da kuma yadda ya buɗe wa waɗanda ba Yahudawa ba ƙofar bangaskiya. 28 Sun ɗan daɗe a can tare da masu bi.

14.15: Fit 20.11; Zab 146.6

Majalisar Shugabannin Jama'ar Masu Bi a Urushalima

15 [1] Sai kuma waɗansu mutane suka zo Antakiya daga
Yahudiya suna koya wa masu bi, suna cewa, "Idan ba
an yi muku kaciya kamar yadda al'adar Musa take ba, ba za ku
iya samun ceto ba." [2] Ba ƙaramar gardama Bulus da Barnaba
suka yi da mutanen nan a kan wannan maganar ba. Sai aka sa
Bulus da Barnaba da kuma waɗansu su je Urushalima wurin
manzanni da dattiban jama'ar masu bi don su tattauna a kan
wannan magana.

3 Jama'ar masu bi ta raka su, suka tafi, suka bi ta ƙasar
Finikiya da Samariya, suna ba da labarin yadda waɗanda ba
Yahudawa ba suka ba da gaskiya. Wannan ya sa duk masu bi
suka yi farin ciki sosai. [4] Da suka isa Urushalima, dukan jama'ar
masu bi, da manzanni, da dattiban jama'ar masu bi suka yi musu
maraba. Sai Bulus da Barnaba kuma suka faɗa musu duk abin
da Allah ya yi ta wurinsu. [5] Amma waɗansu masu bi, 'yan
ɗarikar Farisiyawa, suka tashi tsaye suka ce, "Dole ne a yi wa
masu bi waɗanda ba Yahudawa ba kaciya, a kuma sa su dole
su bi Dokar Musa."

6 Manzannin da dattiban jama'ar masu bi suka taru don su
tattauna a kan wannan maganar. [7] Bayan an yi ta gardama sosai,
sai Bitrus ya tashi tsaye ya ce musu, "'Yan'uwa, kun sani tun
tuni Allah ya zaɓe ni a cikinku, cewa ta wurina ne waɗanda ba
Yahudawa ba za su ji Labari Mai Daɗi, su kuma ba da gaskiya.
[8] Allah kuwa wanda ya san zuciyar kowa, ya nuna cewa ya karɓe
su da ya ba su Ruhu Mai Tsarki, kamar yadda ya ba mu. [9] Kuma
bai nuna bambanci tsakaninmu da su ba, don ya tsarkake
zukatansu ta wurin bangaskiyarsu. [10] Saboda haka don me kuke
gwada Allah ta wurin sa wa almajiran nan waɗansu kaya wato,
dokokin da mu da kakanninmu duka ba mu iya ɗauka ba?
[11] Amma mun gaskata cewa ta wurin alherin Ubangiji Yesu ne
mun sami ceto, kamar yadda su ma suka samu."

12 Sai duk taron mutanen suka yi shiru, suka saurari Barnaba
da Bulus sa'ad da suka ba da labarin alamu da abubuwan ban
mamakin da Allah ya yi ta wurinsu a cikin waɗanda ba
Yahudawa ba.

13 Bayan sun gama magana, sai Yakubu ya amsa ya ce,
"'Yan'uwa, ku saurare ni. [14] Siman ya ba da labari yadda Allah
ya fara nuna ƙauna ga waɗanda ba Yahudawa ba, ta wurin ɗaukar

---

15.1: L. Fir 12.3 **15.7:** A.M. 10.1-43 **15.8:** A.M. 2.4; 10.44

wata jama'a daga cikinsu ta zama tasa. 15 Wannan kuwa ya yi
daidai da maganar annabawa yadda yake a rubuce cewa,

16 'Bayan haka zan dawo in sāke gina gidan Dawuda da ya
rushe.
Ko da yake ya rushe, zan sāke gina shi,
in kuma ta da shi.
17 Ta haka sauran mutane za su neme ni ni Ubangiji,
wato, waɗanda ba Yahudawa ba da na zaɓa su zama
nawa.
18 Haka Ubangiji ya faɗa,
shi da ya bayyana waɗannan abubuwa tun zamanin dā.'

19 "Saboda haka na ga bai kamata mu matsa wa waɗanda ba
Yahudawa ba waɗanda suke juyowa ga Allah. 20 Sai dai mu rubuta
musu wasiƙa mu gaya musu kada su ci abincin da aka miƙa wa
gumaka, kada su yi lalata ko su ci naman dabbar da aka murɗe,
da kuma jini. 21 Gama tun zamanin dā, a kowane gari akwai masu
yin wa'azi da Dokar Musa, ana kuma karanta su a majami'u
kowace Ranar Hutu."

Amsar Shugabannin Jama'ar Masu Bi

22 Sai manzannin da dattiban jama'ar masu bi, tare da dukan
'yan jama'ar masu bi, suka ga ya yi kyau su zaɓi waɗansu daga
cikinsu, su aike su zuwa Antakiya tare da Bulus da Barnaba. Sai
suka zaɓi Yahuda, wanda ake ce da shi Barsaba, da kuma Sila,
waɗanda su shugabanni ne cikin masu bi. 23 Suka ba su wasiƙar
da take cewa:

"Daga 'yan'uwanku, manzanni da dattiban jama'ar masu bi,
zuwa ga masu bi waɗanda asalinku ba Yahudawa ba ne, a
Antakiya da ƙasar Suriya da ta Kilikiya. Muna gaisuwa.

24 "Mun sami labari cewa waɗansu daga cikinmu sun tayar
muku da hankali da maganganunsu, suna rikitar da ku, ko da
yake ba mu ba su umarni su yi haka ba. 25 Don haka, bayan
muka tattauna sai muka ga ya yi kyau mu zaɓi waɗansu mu
aika muku su, tare da abokanmu, wato, Barnaba da Bulus,
26 waɗanda suka ba da ransu saboda sunan Ubangijinmu Yesu
Almasihu. 27 Don haka mun aiko muku Yahuda da Sila. Su da
kansu za su tabbatar muku waɗannan abubuwa da bakinsu.

28 "Ruhu Mai Tsarki ya ga ya yi kyau, haka kuma muka ga
ya yi kyau, kada a sa muku wani nauyi fiye da na waɗannan
abubuwan da suka zama dole, 29 wato, abin da aka miƙa wa

15.16-18: Amos 9.11-12 **15.20:** Fit 34.15-17; L. Fir 17.10-16; 18.6-23

gunki, da cin nama tare da jini, da cin namar dabbar da aka murɗe, da kuma lalata. Idan kun kiyaye kanku daga waɗannan abubuwa, kun yi abin da yake da kyau ke nan. Ku huta lafiya."

30 Sai aka aike su, suka tafi Antakiya. Da suka tara jama'ar masu bi, sai suka ba da wasiƙar. 31 Da jama'ar suka karanta wasiƙar kuwa, suka yi farin ciki saboda ƙarfafawar da suka samu. 32 Yahuda da Sila kuma, don su annabawa ne, suka yi wa 'yan'uwa gargaɗi da maganganu masu yawa, suka kuma ƙarfafa su.

33 Bayan sun yi 'yan kwanaki a wurin, sai aka sallame su lafiya, suka komo wurin waɗanda suka aiko su.[k] 35 Bulus da Barnaba suka yi 'yan kwanaki a Antakiya. Su da waɗansu mutane da yawa suna koyarwa suna kuma yin bisharar maganar Ubangiji.

Bulus da Barnaba Sun Rabu

36 Bayan 'yan kwanaki, Bulus ya ce wa Barnaba, "Zo mu je duk garuruwan da muka yi bisharar maganar Ubangiji a dā, mu ziyarci 'yan'uwa, mu ga yadda suke." 37 Barnaba ya so su ɗauki Yohanna wanda ake ce da shi Markus yă tafi tare da su. 38 Amma Bulus ya ga bai yi kyau su tafi da Markus ba saboda a dā ya bar su a ƙasar Bamfiliya, ya kuma ƙi ya ci gaba da yin aiki tare da su. 39 Rashin yardar ya yi zafi har ya kai su ga rabuwa. Barnaba ya ɗauki Markus, suka shiga jirgin ruwa zuwa Sayifurus. 40 Amma Bulus ya zaɓi Sila. Bayan masu bi sun miƙa su ga alherin Ubangiji yă kiyaye su. Sai suka tashi. 41 Suka bi ta ƙasashen Suriya da Kilikiya, suna ƙarfafa jama'un masu bi.

Timoti Ya Bi Bulus da Sila

16 1 Sai Bulus ya je Darbe da Listira. Akwai wani almajiri a Listira mai suna Timoti, ɗan wata Bayahudiya mai bi. Babansa kuwa Bahelene ne. 2 Masu bi da suke a Listira da Ikoniya kuwa suna yabon Timoti. 3 Bulus ya so Timoti ya raka shi. Don haka ya ɗauke shi ya yi masa kaciya saboda Yahudawan da suke waɗannan wuraren duk sun san babansa Bahelene ne.

4 Lokacin da Bulus da Sila suke tafiya suna bin gari-gari, suka riƙa bayyana wa jama'a ƙa'idodin da manzanni da dattiban jama'ar masu bi suka yarda a kai a Urushalima, suka gaya wa masu bi su kiyaye su. 5 Ta haka jama'un masu bi suka ƙara ƙarfi cikin bangaskiya, suna ƙara yawa kowace rana.

15.38: A.M. 13.13

[k] **15.33** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya ta 34 haka: Amma Sila ya ga ya yi kyau yă zauna a nan tukuna.

Bulus Ya Ga Ru'uya a kan Makidoniya

6 Sai suka zazzaga ƙasashen Firijiya da Galatiya, don Ruhu
Mai Tsarki ya hana su yin maganar Ubangiji a Asiya. 7 Da suka
zo kan iyakar ƙasar Misiya, suka yi ƙoƙari su je ƙasar Bitiniya,
amma Ruhun Yesu bai yarda musu ba. 8 Suka kuwa bi ta gefen
ƙasar Misiya, suka gangara zuwa Toruwas. 9 Da dare Bulus ya
ga ru'uya. A ru'uyar kuwa ya ga wani mutumin ƙasar Makidoniya
yana tsaye, yana roƙonsa yana cewa, "Ka zo Makidoniya ka
taimake mu." 10 Da Bulus ya ga ru'uyan nan kuwa, nan take muka
yi ƙoƙari mu ƙetare zuwa Makidoniya, don mun tabbata cewa
Allah ne ya kira mu mu yi musu wa'azin Labari Mai Daɗi.

Lidiya Ta Ba da Gaskiya

11 Sai muka tashi a cikin jirgin ruwa daga Toruwas muka miƙe
har Samutarkiya. Washegari kuma sai Niyafolis. 12 Daga nan
kuma sai muka wuce zuwa Filibi wadda take ƙarƙashin mulkin
Roma, kuma ita ce babban birni ta yankin Makidoniya. Muka yi
'yan kwanaki a nan. 13 Ranar Hutu muka fita ƙofar gari, muka je
bakin kogi inda muke tsammani akwai wurin yin addu'a na
Yahudawa, muka zauna muka yi magana wa matan da suka taru
a wurin. 14 Akwai wata mace mai suna Lidiya, mai bautar Allah,
tana sauraronmu. Ita 'yar garin Tayatira ce, tana sayar da yadunan
jan garura mai tsada. Ubangiji ya buɗe zuciyarta, har ta sa hankali
ta saurari abin da Bulus ya faɗa. 15 Da aka yi mata baftisma tare
da mutanen gidanta, sai ta roƙe mu ta ce, "Idan kun yarda ni mai
ba da gaskiya ga Ubangiji ce, to, sai ku zo gidana ku sauka." Ta
lallashe mu, sai muka yarda.

An Kulle Bulus da Sila a cikin Kurkuku

16 Wata rana za mu je wurin yin addu'a sai muka gamu da
wata yarinya mai aljani mai duba. Masu yarinyar kuwa suna
samun kuɗi sosai ta wurin duban da take yi. 17 Sai ta riƙa binmu,
mu da Bulus, tana ihu tana cewa, "Mutanen nan bayin Allah
Maɗaukaki ne, suna sanar da ku hanyar ceto!"

18 Ta yi ta yin haka kwanaki da yawa. Sai Bulus ya ji fushi
sosai, ya juya ya ce wa aljanin, "Na umarce ka cikin sunan Yesu
Almasihu, ka rabu da ita." Nan take kuwa ya rabu da ita.

19 Da masu yarinyar suka ga hanyar da suke samun kuɗi ta
toshe, sai suka kama Bulus da Sila, suka ja su har cikin kasuwa
gaban masu shari'a. 20 Da suka kai su gaban alƙalai, suka ce,
"Waɗannan Yahudawa suna damun garinmu fa. 21 Suna koyar da

al'adun da bai kamata mu karɓa ko mu bi ba, don mu Romawa ne." 22 Sai jama'a suka taru a kansu gaba ɗaya, alƙalan kuma suka yayyage musu tufafinsu, suka tuttuɓe su, suka ba da umarni a dūke su. 23 Da aka dūke su sosai, aka sa su cikin kurkuku, aka umarci mai gadin kurkukun yă yi gadinsu da kyau. 24 Shi kuwa da ya karɓi wannan umarni, sai ya sa su can ciki-cikin kurkuku, ya sa ƙafafunsu a turu.

Hoton Bulus da Sila a cikin Kurkuku (16.23-25)

25 Wajen tsakar dare, Bulus da Sila suna addu'a suna waƙoƙin yabon Allah, sauran 'yan kurkukun kuwa suna sauraronsu. 26 Ba labari sai aka yi wata babbar rawar ƙasa, har tushen ginin kurkukun ya girgiza. Nan da nan ƙofofin duka suka buɗe, sarƙoƙin dukan 'yan kurkukun suka kunce. 27 Da mai gadin 'yan kurkukun ya tashi daga barci ya ga ƙofofin kurkukun a buɗe, ya zaro takobinsa, yana shiri yă kashe kansa, domin yana tsammani 'yan kurkukun sun gudu. 28 Amma Bulus ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, "Kada ka ji wa kanka ciwo, ai, dukanmu muna nan!"

29 Sai mai gadin 'yan kurkuku ya ce a kawo fitilu. Sai ya yi wuf ya shiga ciki, ya fāɗi a gaban Bulus da Sila, yana rawar jiki don tsoro. 30 Sa'an nan ya ƒito da su waje ya ce, "Shugabanni, me zan yi in sami ceto?" 31 Su kuwa suka ce, "Ka gaskata da

Ubangiji Yesu, kai da iyalinka za ku sami ceto." 32 Sa'an nan
suka gaya masa maganar Ubangiji, shi da mutanen da suke
gidansa duka. 33 A cikin daren nan ya ɗauke su, ya wanke musu
mikinsu. Nan da nan kuwa aka yi masa baftisma da dukan
iyalinsa. 34 Sa'an nan ya shigo da su cikin gidansa, ya kawo musu
abinci. Shi da iyalinsa duka suka cika da farin ciki don dukansu
sun ba da gaskiya ga Allah.

35 Da gari ya waye, alƙalan suka aiko 'yan sanda da umarni
cewa, "A saki mutanen nan." 36 Sai mai gadin 'yan kurkukun ya
kawo wa Bulus saƙon ya ce, "Alƙalai sun aiko a sake ku. Don
haka yanzu sai ku fito ku tafi lafiya."

37 Amma Bulus ya ce musu, "Ai, a gaban mutane suka yi mana
bulala, ba tare da an yi mana shari'a ba, ko da yake mu Romawa
ne. Suka kuma jefa mu cikin kurkuku, yanzu kuma za su fitar da
mu a ɓoye? Ina! Sai dai su zo da kansu su fitar da mu."

38 Sai 'yan sandan suka je suka faɗa wa alƙalan wannan
magana. Alƙalan kuwa suka ji tsoro da suka ji wai Bulus da Sila
Romawa ne. 39 Sa'an nan suka zo suka roƙi gafara a wurin Bulus
da Sila. Bayan haka sai suka fitar da su suka roƙe su su bar garin.
40 Bayan Bulus da Sila suka fito daga kurkukun, sai suka tafi
wurin Lidiya. Bayan sun ga masu bi, suka kuma ƙarfafa musu
zuciya, sai suka tafi.

An Yi Tashin Hankali a Tasalonika

17 1 To, da Bulus da Sila suka bi ta Amfibolis da Afoloniya,
suka kai Tasalonika, inda akwai majami'ar Yahudawa.
2 Sai Bulus ya shiga wurinsu kamar yadda ya saba, Ranar Hutu
guda uku a jere yana mahawara da su daga cikin Rubutattun
Maganar Allah. 3 Yana yi musu bayani, yana kuma tabbatar musu
cewa lallai ne Almasihu yă sha wahala, yă kuma tashi daga
matattu. Bulus ya kuma ce, "Yesun nan da nake sanar muku, shi
ne Almasihu." 4 Sai waɗansu mutanen Yahudawa da kuma
Helenawa masu bautar Allah haɗe da manyan mata masu yawa
sosai, duk suka yarda da maganar Bulus da Sila, suka kuma haɗa
kai da su.

5 Amma Yahudawa suka yi kishi, sai suka tara waɗansu 'yan
iska a kasuwa. Da dukansu suka taru sai suka ta da hankalin
mutanen garin. Suka ruga cikin gidan Jason suna neman Bulus
da Sila don su kawo su gaban jama'a. 6 Da ba su same su ba, sai
suka jawo Jason da waɗansu masu bi, suka kai su har gaban masu
shari'a, suna ihu suna cewa, "Mutanen nan da suke ta da hankali

a ko'ina a duniya, ga su sun zo har nan ma. 7 Har ma Jason ya
ba su masauki. Dukansu kuwa suna karya dokokin Kaisar, suna
cewa akwai wani sarki, wai sunansa Yesu." 8 Da mutanen garin
da masu shari'a suka ji wannan, hankalinsu ya tashi. 9 Ba su saki
Jason da sauransu ba, sai da suka karɓi kuɗin beli a hannunsu.

Bulus da Sila a Biriya

10 Da dare ya yi, masu bi suka sallami Bulus da Sila su tafi
Biriya. Da suka kai can, suka shiga majami'ar Yahudawa. 11 To,
waɗannan Yahudawan sun fi na Tasalonika hankali, domin sun
karɓi maganar hannu biyu-biyu. Suna ta binciken Rubutattun
Maganar Allah kullum, su gani ko abin da Bulus ya faɗa gaskiya
ne. 12 Saboda haka da yawa daga cikin Yahudawa suka ba da
gaskiya, har da waɗansu matan Helenawa masu matsayi da kuma
mazan Helenawa da yawa. 13 Amma da Yahudawan da suke a
Tasalonika suka ji cewa Bulus yana yi bishara a Biriya ma, suka je
suka zuga jama'a a can ma, suna ta da hankalinsu. 14 Nan da nan
kuwa masu bi suka sa Bulus yă tafi bakin teku, amma Sila da Timoti
suka tsaya tukuna a nan. 15 Waɗanda suka yi wa Bulus rakiya kuwa
suka kai shi har Atina. Da za su dawo sai Bulus ya ba su saƙo zuwa
wurin Sila da Timoti cewa su zo su same shi da sauri, sai suka tafi.

Bulus a Atina

16 To, sa'ad da Bulus yake jiran Sila da Timoti a Atina, ya yi
baƙin ciki ƙwarai da ya ga garin ya cika da gumaka. 17 Don haka
yakan yi mahawara a cikin majami'a da Yahudawa, da waɗansu
Helenawa masu yi wa Allah sujada. Kowace rana kuwa yakan yi
mahawara da waɗanda yake samu a kasuwa. 18 Haka kuma
waɗansu Abikuriyawa da Sitokiyawa masu ilimi suka yi
mahawara da shi. Waɗansunsu suka ce, "Mene ne wannan mai
surutun yake so ya ce?"

Waɗansu suka ce, "Kamar mai yin wa'azin waɗansu alloli ne
da ba na nan ba." Sun faɗa haka domin Bulus yana yin bisharar
Yesu, da kuma tashi daga matattu. 19 Saboda haka suka kai shi
Tudun Arasa wato, Majalisarsu, suka ce masa, "Ko za ka bayyana
mana wannan sabuwar koyarwar da kake yi? 20 Don ba mu taɓa
jin irin waɗannan maganganu ba. Muna so mu san abin da suke
nufi." 21 Duk Atinawa da baƙin da suke zama a Atina, sun fi so
su ji sabon abu su kuma yi magana a kai,. fiye da kome.

22 Sai Bulus ya tashi tsaye a gaban majalisar, ya ce, "Ku
mutanen Atina, na lura cewa ku masu son bin addini ne sosai ta

kowane gefe. 23 Don lokacin da nake zagawa cikin garin, na duba
abubuwan da kuke yi wa sujada, har ma na ga wani bagaden hadaya
da rubutu a samansa mai cewa, 'Domin Allahn da ba a sani ba.'
To, shi wannan da kuke yi wa sujada da ba ku san shi ba, shi ne
nake sanar muku. 24 Allahn da ya halicci duniya da dukkan abin da
yake cikinta, shi da yake Ubangijin sama da ƙasa ba ya zama a
haikalin da mutum ya gina. 25 Haka kuma ba ya neman taimako
daga wurin mutum, ba ya bukatar wani abu, tun da yake shi ne
yake ba dukkan mutane rai, da numfashi da dukkan abubuwan da
suke bukata. 26 Shi ne kuma ya halicce dukkan al'umma daga
mutum guda, domin su zauna a duk sararin duniya. Ya shirya iyakar
lokaci, da kuma wuraren da kowace al'umma za ta kasance. 27 Allah
ya yi haka don su neme shi, ko watakila za su laluba su same shi,
ko da yake bai yi nesa da kowannenmu ba. 28 Ai,

'Ta gare shi ne muke rayuwa,
muke motsi, muka kuma kasance,'
yadda waɗansu mawaƙanku ma suka faɗa cewa,
'Hakika, mu ma zuriyarsa ce.'

29 To, da yake mu zuriyar Allah ne, ai, bai kamata mu yi tsammani
Allah yana kama da wata siffar zinariya, ko ta azurfa, ko ta dutse
ba, wadda mutum ya ƙera da dabararsa. 30 A dā Allah bai hukunta
mutane gwargwadon laifofinsu ba, saboda rashin saninsu. Amma
yanzu ya umarci dukkan mutane a ko'ina su tuba. 31 Domin ya
tsai da ranar da zai zo yă yi wa duniya shari'a ta gaskiya ta wurin
wani da ya zaɓa. Allah ya ba da tabbacin yin haka ta wurin ta da
mutumin nan daga matattu."

32 Da suka ji maganar tashi daga matattu, sai waɗansu suka yi
masa ba'a, amma waɗansu suka ce, "Muna so mu sāke jin abin da
za ka faɗa game da wannan magana." 33 A nan ne Bulus ya rabu
da su. 34 Amma waɗansunsu suka koma wajen Bulus, suka ba da
gaskiya, cikinsu har da Diyonisiyus, ɗan majalisa, da wata mace
mai suna Damaris, da waɗansu kuma.

Bulus a Korinti

18 1 Bayan haka Bulus ya bar Atina ya tafi Korinti. 2 A can
ya tarar da wani Bayahude mai suna Akila, ɗan garin
Fontus. Akila da matarsa Biriskila ba su daɗe da zuwa daga ƙasar
Italiya ba, don Kalaudiyus ya yi doka cewa dukan Yahudawa su
bar Roma. Sai Bulus ya je wurinsu. 3 Da yake sana'arsu iri ɗaya
ce da tasa wato, ta ɗinkin tenti, sai ya yi zama tare da su. Suka

17.24-25: 1 Sar 8.27; Ish 42.5; A.M. 8.47

yi ta aiki tare. 4 Kowace Ranar Hutu kuma Bulus ya rika
mahawara a majami'a, yana kokari yă rinjaye Yahudawa da
wadanda ba Yahudawa ba.

5 Sa'ad da Sila da Timoti suka zo daga Makidoniya, Bulus ya
ba da dukan lokacinsa a kan yin wa'azi, yana tabbatar wa Yahudawa
cewa, Yesu shi ne Almasihu. 6 Amma suka yi masa mūsu, suna
zaginsa. Don haka sai ya kakkabe tufafinsa ya ce musu, "Alhakinku
a wuyanku! Ni dai ba ni da laifi. Daga yau wurin wadanda ba
Yahudawa ba za ni." 7 Sai ya tashi a wurin ya tafi gidan wani mutum
mai suna Titiyus Justus, mai bautar Allah, gidansa kuwa yana kusa
da majami'a sosai. 8 Sai Kiribus, shugaban majami'a ya ba da
gaskiya ga Ubangiji, shi da mutanen gidansa duka. Wadansu
Korintiyawa kuma da yawa da suka ji maganar Bulus, suka ba da
gaskiya, aka kuwa yi musu baftisma.

9 Wata rana da dare, Ubangiji ya nuna wa Bulus ru'uya, ya ce
masa, "Kada ka ji tsoro. Ka yi ta yin wa'azi, kada ka yi shiru,
10 domin ina tare da kai. Ba wanda zai sa hannu yă yi maka wani
abu, don ina da mutane da yawa a wannan birnin." 11 Bulus ya
zauna a wurin har shekara daya da wata shida, yana ta koyar musu
maganar Allah.

12 Amma lokacin da Galiyo yake mulkin kasar Akaya,
Yahudawa suka hada kai suka tasar wa Bulus, suka kai shi gaban
masu shari'a. 13 Suka ce, "Wannan mutumin yana kokari yă sa
mutane su bauta wa Allah ta hanyar da doka ta hana."

14 Bulus yana shirin yă yi magana ke nan, sai Galiyo ya ce
wa Yahudawa, "Da ma wani laifi ya yi, ko babban laifi, da sai
in ji ku. 15 Amma tun da yake gardama ce kawai a kan kalmomi,
da sunaye, da kuma dokarku, ai, sai ku ji da shi da kanku. Ni
kam, ban yi niyyar yin shari'a kan irin wadannan abubuwa ba."
16 Sai ya kore su daga dakin shari'ar. 17 Sai dukansu suka kama
Sostanus shugaban majami'ar, suka yi masa dūka a gaban dakin
shari'a. Amma Galiyo bai ko kula ba.

Bulus Ya Koma Antakiya ta Suriya

18 Bayan wannan sai Bulus ya kara 'yan kwanaki a Korinti.
Sa'an nan ya yi wa masu bi bankwana. Ya shiga jirgin ruwa tare
da Biriskila da Akila suka kama hanya zuwa Suriya. Amma kafin
su tashi Bulus ya aske kansa[k] a Kankiriya domin ya dauki alkawari.
19 Da suka kai Afisa, a can ne Bulus ya bar Biriskila da Akila, shi

[k] **18.18 aske kai:** Wannan al'adar Yahudawa ce ta nunan cewa mutum ya cika alkawarin da ya dauka.

kuwa ya shiga majami'a ya yi mahawara da Yahudawa. 20 Sai suka roƙe shi yă ɗan ƙara zama a wurinsu, amma bai yarda ba. 21 Amma da zai bar su, ya ce, "Zan dawo wurinku idan Allah ya yarda." Sa'an nan ya tashi daga Afisa a jirgin ruwa.

22 Da ya sauka a Kaisariya, sai ya haura ya gai da jama'ar masu bi, sa'an nan ya tafi Antakiya. 23 Bayan ya ɗan daɗe kaɗan a wurin, sai ya tashi ya zazzaga ƙasar Galatiya da ƙasar Firijiya, yana bin gari-gari, yana ƙarfafa dukan masu bi.

Afolos Ya Yi Wa'azi a Afisa

24 Ana nan sai wani Bayahude mai suna Afolos ya zo Afisa. Shi kuwa ɗan garin Alekzandiriya ne, mai iya magana, ya san Rubutattun Maganar Allah sosai-sosai. 25 An koyar da shi cikin hanyar Ubangiji. Yakan nuna ƙwazo sosai cikin magana, yana kuma koyar da ainihin gaskiya game da Yesu. Amma fa baftismar Yohanna kaɗai ne ya sani. 26 Sai ya fara wa'azi da dukan ƙarfinsa a majami'a. Da Biriskila da Akila suka ji maganarsa, sai suka ja shi gefe suka ƙara bayyana masa hanyar Allah sosai-sosai. 27 Da Afolos ya so yă ƙetare zuwa ƙasar Akaya, masu bi suka taimake shi. Suka rubuta wa masu bi na Akaya wasiƙa don su karɓe shi hannu biyu-biyu. Da ya kai can kuwa ya zama da taimako sosai ga waɗanda suka ba da gaskiya ta wurin alherin Allah, 28 don ya ƙa da Yahudawa ƙwarai a gaban jama'a, yana tabbatar musu daga cikin Rubutattun Maganar Allah cewa Yesu shi ne Almasihu.

Bulus a Afisa

19 1 A lokacin da Afolos yake a Korinti, Bulus ya zazzaga cikin ƙasar har ya kai Afisa, inda ya tarar da waɗansu almajirai. 2 Sai ya ce musu, "Kun sami Ruhu Mai Tsarki lokacin da kuka ba da gaskiya?"

Suka ce masa, "Ba mu ma san akwai Ruhu Mai Tsarki ba." 3 Sai ya ce, "Wace irin baftisma aka yi muku ke nan?" Suka ce, "Irin ta Yohanna ce."

4 Bulus ya ce, "Ai, Yohanna ya yi baftisma don a tuba ne, yana faɗa wa mutane su gaskata da wani da zai zo bayansa, wato Yesu." 5 Da suka ji haka, sai aka yi musu baftisma cikin sunan Ubangiji Yesu. 6 Da Bulus ya sa musu hannun albarka, Ruhu Mai Tsarki kuwa ya sauko musu, suka kuwa yi magana da waɗansu harsuna, suna annabci. 7 Su wajen mutum goma sha biyu ne duka.

18.18: L. Kid'6.18 19.4: Mat 3.11; Mar 1.4; 7-8; Luk 3.4,16; Yoh 1.26-27

8 Sai Bulus ya shiga majami'a yana wa'azi da zuciya ɗaya,
ya kuma yi wata uku yana kawo musu dalilai, yana rinjayarsu a
kan sha'anin mulkin Allah. 9 Amma waɗansunsu suka nuna
taurinkai suka ƙi su gaskata, har suka yi wa masu bin wannan
Hanyar Ubangiji baƙar magana a gaban jama'a. Don haka Bulus
ya rabu da su, ya tafi da masu bi, yana ta koyarwa kowace rana
a makarantar Tiranus. 10 Haka ya yi ta yi har shekara biyu, har
dukan masu zama a ƙasar Asiya suka ji maganar Ubangiji,
Yahudawa da waɗanda ba Yahudawa ba duka.

'Ya'yan Siba

11 Ta hannun Bulus kuma Allah ya yi waɗansu manyan
abubuwan ban mamaki da ba a saba gani ba, 12 yadda har ma
idan aka ɗauki hankicif nasa ko rigar da ta taɓa jikinsa, aka kai
wa waɗanda ba su da lafiya, sai su warke, aljanu kuma su rabu
da su. 13 Sai waɗansu Yahudawa masu yawo gari-gari suna fitar
da aljanu suka yi ƙoƙari su yi amfani da sunan Ubangiji Yesu
a kan masu aljanu. Suna cewa, "Na umarce ku da sunan Yesun
nan da Bulus yake wa'azinsa." 14 To akwai waɗansu 'ya'ya
bakwai maza, na wani babban firist na Yahudawa, mai suna
Siba, dukansu suna yin haka.

15 Amma aljanin ya amsa musu ya ce, "Yesu dai na san shi,
na kuma san Bulus, to, ku kuma ku wane ne?"

16 Sai mutumin nan mai aljani ya yi tsalle, ya hau musu, ya
sha ƙarfinsu dukkansu, har suka fita daga gidan a guje tsirara, da
jikinsu duk ciwo. 17 Da dukan masu zama a Afisa, Yahudawa da
waɗanda ba Yahudawa ba, suka ji labarin wannan abin da ya faru,
sai tsoro ya kama su, suka kuwa ɗaukaka sunan Ubangiji Yesu.
18 Da yawa kuma da suka ba da gaskiya suka zo suna faɗin
mugayen ayyukansu a fili. 19 Mutane da yawa kuwa masu yin
sihiri, suka tattaro littattafansu suka ƙone su a gaban jama'a duka.
Da suka yi lissafin kuɗin littattafan, sun kai kuɗin da lebura zai
samu na aikin kwana dubu hamsin. 20 Ta haka maganar Ubangiji
ta ƙara bazuwa, ta kuma yi ƙarfi sosai.

Tashin Hankali a Afisa

21 Bayan waɗannan abubuwa, Bulus ya shirya a ransa cewa
idan ya zazzaga ƙasar Makidoniya da ta Akaya, zai je Urushalima.
Ya kuma ce, "Bayan na je can kuwa dole ne in je in ga birnin
Roma." 22 Sai ya aika da masu taimakonsa su biyu, wato, Timoti

da Erastus, zuwa Makidoniya, shi kuwa ya ɗan tsaya a ƙasar Asiya.

23 A lokacin nan aka yi wani babban tashin hankali game da wannan Hanya. 24 Wannan tashin hankalin ya fara da wani maƙeri mai suna Dimitiriyus wanda yake amfani da azurfa yana ƙera siffar haikalin Artemis. Shi da ma'aikatansa suna samun kuɗi ta wannan sana'arsu ba kaɗan ba.

Hoton Dimitiriyus da Ma'aikatansa (19.24)

25 Sai ya tara su da duk masu yin irin wannan aikin, ya ce, "Ku jama'a, kun sani fa da sana'an nan muke yin arziki. 26 Kuma kuna ji kuna gani, ba a nan Afisa kaɗai ba, kusan duk ƙasar Asiya ma, Bulus ɗin nan ya rinjayi mutane da yawa sosai. Ya juyar da su, yana cewa allolin da aka yi da hannu ba alloli ba ne. 27 To, akwai hatsari. Za a ɓata sunan aikinmu. Ban da haka ma, har da haikalin babban alliya Artemis za a mai da shi banza, har kuma a raba alliyar da darajarta, ita wadda duk ƙasar Asiya, kai har ma dukan duniya take bauta mata."

28 Da suka ji haka, sai suka cika da fushi sosai, suka ɗaga
murya gaba ɗaya suna cewa, "Girma yă tabbata ga Artemis ta
Afisawa!" 29 Sai garin duk ya rude, jama'a suka ruga zuwa filin
taro, suna jan Gayus da Aristarkus, mutanen Makidoniya,
waɗanda suke abokan tafiyar Bulus. 30 Bulus ya so yă shiga taron
nan, amma masu bi suka hana shi. 31 Waɗansu manyan hakimai
na ƙasar Asiya, waɗanda suke abokansa, su ma suka aika masa,
suka roƙe shi kada ya kuskura ya shiga wajen taron nan.
32 Mutanen da suka taru kuwa duk ma a rikice suke, don ba su
ma san abin da ya sa suka taru ba. Waɗansu suna ta da murya
suna faɗin wani abu, waɗansu kuma suna faɗin wani abu dabam.
33 Waɗansu Yahudawa suka tura wani mai suna Alekzanda gaba,
shi kuwa ya ɗaga hannu a yi shiru don yă yi musu bayani.
34 Amma da suka gane cewa shi Bayahude ne, suka ɗaga murya
gaba ɗaya suna cewa, "Girma yă tabbata ga Artemis ta Afisawa!"
Sun yi haka har wajen awa biyu.

35 Amma da sakataren garin ya sa suka yi shiru, sai ya ce,
"Ku mutanen Afisa! Ai, kowa ya san cewa birnin Afisa ne yake
kula da haikalin mai girma Artemis, da kuma dutse mai tsarkin
nan da ya fāɗo daga sama. 36 To, tun da yake ba dama a yi mūsun
waɗannan abubuwa, ai, ya kamata ku natsu, kada ku yi kome da
garaje. 37 Ga shi kuwa mutanen nan da kuka kawo a nan, ba su
yi sata a ɗakin alliyarmu ba, ba su kuma zage ta ba. 38 Amma
idan Dimitiriyus da abokan sana'arsa suna da wata damuwa game
da wani, ai, ga ɗakin shari'a a bude, ga kuma masu shari'a, sai
su kai ƙara. 39 Amma idan akwai wani abu dabam da kuke so ku
sani, ai, sai a daidaita a majalisa. 40 Hakika muna cikin hatsarin
amsar ƙara a kan tawayen yau, tun da yake ba za mu iya ba da
dalilin da ya sa wani tashin hankali ya faru ba."

41 Da ya faɗa haka sai ya sallami taron.

Bulus Ya Koma Makidoniya da Hellas

20 1 Bayan rikicin ya kwanta, Bulus ya kira masu bi. Da ya
ƙarfafa musu zuciya, sai ya yi bankwana da su, ya tafi
ƙasar Makidoniya. 2 Da ya zazzaga waɗannan yankuna, ya kuma
ƙarfafa musu zuciya sosai, sai ya isa ƙasar Hellas. 3 Ya yi wata
uku a nan. Yana shirin yă shiga jirgin ruwa yă tafi ƙasar Suriya
ke nan, Yahudawa kuwa suka yi masa mugun shiri. Saboda haka
sai ya zaɓi yă koma ta Makidoniya. 4 Sufata ɗan Farus daga
Biriya, tare da Aristarkus da Sakundus, mutanen Tasalonika, da
Gayus daga Darbe, da Timoti, har ma da Tikikus da Tarofimus,

mutanen Asiya, suka raka shi. 5 Sun riga mu tafiya suka jira mu
a Toruwas. 6 Mu kuwa muka tashi daga Filibi a jirgin ruwa, bayan
Bikin Burodi Marar Yisti, muka same su a Toruwas bayan kwana
biyar. A Torawus muka yi kwana bakwai.

Ziyarar Karshe ta Bulus a Toruwas

7 A ranar farko ta mako kuma muka taru don mu rarraba
burodi. Sai Bulus ya yi musu jawabi. Don yana shiri yă tafi
washegari, ya yi ta jawabi har tsakar dare. 8 Akwai kuwa fitilu
da yawa a gidan saman da muka taru. 9 Wani saurayi mai suna
Yutikus yana zaune a kan taga, sai barci ya dame shi sosai lokacin
da Bulus yake ta yin dogon jawabinsa. Har barcin ya kwashe
Yutikus, sai ya fāɗo daga can sama, daga hawa ta uku, kuma aka
ɗauke shi matacce. 10 Amma Bulus ya sauka ƙasa ya sunkuya ya
rungume shi, ya ce, "Kada ku damu, ai, yana da rai." 11 Sai Bulus
ya koma sama ya rarraba burodi muka ci. Ya ci gaba da yin musu
magana har gari ya waye, sa'an nan ya tafi. 12 Sai suka tafi da
saurayin da rai, suka kuwa yi murna sosai.

Tafiya daga Toruwas zuwa Militus

13 Mu kuwa muka yi gaba zuwa jirgin ruwan, muka miƙe
zuwa Asus da nufin mu ɗauki Bulus daga can. Don dā ma haka
ya shirya, shi kuwa ya yi niyya yă tafi da ƙafa. 14 Da ya same
mu a Asus, muka ɗauke shi a jirgin muka zo Mitilin. 15 Daga
nan kuma muka ci gaba da tafiya a cikin jirgin ruwan.
Washegari kuma sai ga mu a gefen Kiyos. Washegari kuma sai
ga mu a Samos, washegari kuma sai Militus. 16 Dā ma kuwa
Bulus ya sa rai ba zai sauka a Afisa ba, don kada yă ɓata lokaci
a Asiya. Yana sauri, idan zai yiwu ma yă kai Urushalima kafin
ranar Bikin Fentikos.

Bulus Ya Yi wa Dattiban Jama'ar Masu Bi na Afisa Bankwana

17 Daga Militus ne Bulus ya aika zuwa Afisa a kira masa
dattiban jama'ar masu bi. 18 Da suka zo wurinsa sai ya ce musu,
"Ku da kanku kun san irin zaman da na yi a cikinku tun ranar
da na sa ƙafata a ƙasar Asiya. 19 Ina bauta wa Ubangiji da tawali'u
sosai har da hawaye. Na jimre gwaje-gwajen da suka zo mini ta
wurin mugayen shirye-shiryen da Yahudawa suka sha yi mini.
20 Ban daina gaya muku kowane abu mai amfani ba, ina yi muku
wa'azi da koyarwa a fili, da kuma gida-gida. 21 Na gargaɗe

Yahudawa da waɗanda ba Yahudawa ba duka game da tuba zuwa
wurin Allah, su kuma ba da gaskiya ga Ubangijinmu Yesu.
22 "Ga shi kuma yanzu Ruhu yana sauko a kaina, zan tafi
Urushalima, ban kuwa san abin da zai same ni a can ba, 23 ko da
yake Ruhu Mai Tsarki yana tabbatar mini a kowane gari cewa
kullewa a kurkuku, da shan tsanani suna jirana. 24 Amma ni ban
mai da raina kamar wani abu ba, idan dai zan iya gama aikin nan
da Ubangiji Yesu ya ba ni, wato, in shaida Labari Mai Daɗi na
alherin Allah.
25 "To, yanzu na sani dukanku ba za ku sāke ganina ba, ku da
na zazzaga cikinku ina yi muku bisharar mulkin Allah. 26 Saboda
haka ina dai tabbatar muku a yau, cewa ba alhakin ko ɗayanku a
kaina, 27 domin na sanar muku da nufin Allah duka. 28 Ku lura da
kanku, da kuma dukan garken da Ruhu Mai Tsarki ya sa kuka zama
masu lura da shi, ku kuma ci gaba da kiwon jama'ar masu bi
waɗanda Allah[l] ya samo wa kansa da jinin Ɗansa.
29 "Na sani bayan na tafi waɗansu mugayen kuraye za su
shigo cikinku, ba kuwa za su bar garken ba. 30 Har ma a cikinku
waɗansu za su taso su yi maganganun ƙarya, don su jawo masu
bi zuwa gefensu. 31 Saboda haka sai ku zauna da shiri, ku tuna
fa, shekara uku ke nan, dare da rana, ban fasa yi wa kowane
ɗayanku gargaɗi ba, har da hawaye.
32 "Yanzu kuma na miƙa ku ga Ubangiji. Bari maganar
alherinsa ta kiyaye ku, ita ce za ta iya gina ku, ta kuma ba ku
gādo tare da dukan masu tsarki. 33 Ban yi kwaɗayin kudi ko
tufafin kowa ba. 34 Ku da kanku kun sani na yi aiki da hannayena
domin in biya bukatuna da na waɗanda suke tare da ni. 35 Cikin
wannan duka na ba ku misali cewa dole ne ku yi aiki haka don
mu taimaki marasa ƙarfi. Kuna tuna kuma da maganar Ubangiji
Yesu da ya ce, 'Ya fi albarka a bayar da a karɓa.' "
36 Da Bulus ya gama faɗin haka, sai ya durƙusa ya yi addu'a
tare da su duka. 37 Sai duk suka fashe da kuka, suka fāɗi a wuyar
Bulus suna rungumarsa, 38 suna baƙin ciki musamman don
maganar da ya yi ta cewa ba za su ƙara ganinsa ba. Daga nan
suka raka shi har bakin jirgi.

20.24: 2 Tim 4.7

[l] **20.28 jama'ar masu bi waɗanda Allah:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Jama'ar masu bi waɗanda Ubangiji" ne a nan.

Tafiyar Bulus zuwa Urushalima

21 1 Sa'ad da muka bar su, muka shiga jirgin ruwa muka
miƙe sai Kos, washegari kuma sai Rods, daga nan kuma
sai Fatara. 2 Da muka sami jirgin da zai je ƙasar Finikiya, sai
muka shiga muka tafi. 3 Da muka fara hangan Sayifurus, muka
mai da shi hagunmu, muka ci gaba da tafiya har ƙasar Suriya.
Sai muka sauka a Taya, don a nan ne jirgin zai sauke kayansa.
4 Da muka sami inda masu bi suke, muka zauna a nan kwana
bakwai. Sai Ruhu ya sauko a kansu suka gaya wa Bulus kada
yă je Urushalima. 5 Amma da lokacin tashinmu ya yi, muka
tashi muka ci gaba da tafiyarmu. Dukan masu bi kuma har da
matansu da 'ya'yansu suka raka mu har bayan gari. Sa'an nan
muka durƙusa a gefen ruwa muka yi addu'a, 6 muka yi wa juna
bankwana. Sa'an nan muka shiga jirgi, su kuma suka koma
gida.

7 Da muka gama tafiyarmu daga Taya, muka kai Tolemayis,
muka gaisa da 'yan'uwa, muka kuma yi kwana ɗaya a wurinsu.
8 Washegari muka tashi muka je Kaisariya, muka shiga gidan
Filibus mai wa'azi, wanda yake ɗaya daga cikin bakwai ɗin nan
waɗanda aka zaɓa domin hidimar jama'a masu bi a Urushalima,
muka sauka a wurinsa. 9 Yana da 'ya'ya huɗu 'yan mata
waɗanda ba su yi aure ba. Su masu yin annabci ne. 10 To, bayan
mun yi 'yan kwanaki a wurin, sai wani annabi mai suna Agabus
ya zo daga Yahudiya. 11 Da Agabus ya zo wurinmu, sai ya ɗauki
bel na Bulus. Sai shi Agabus ya ɗaure hannayensa da ƙafafunsa
ya ce, "Ga abin da Ruhu Mai Tsarki ya ce, 'Haka Yahudawan
Urushalima za su ɗaure mai wannan bel, su kuma ba da shi ga
waɗanda ba Yahudawa ba.' " 12 Da muka ji haka, mu da
mutanen da suke wurin muka roƙi Bulus kada yă je Urushalima.
13 Sai Bulus ya amsa ya ce, "Don me kuke yin haka? Me ya sa
kuna kuka kuna ɓata mini zuciya? Ai, a shirye nake ba ma a
ɗaure ni kawai ba, har ma a kashe ni a Urushalima saboda sunan
Ubangiji Yesu."

14 Da dai muka kāsa shan kansa, sai muka yi shiru, muka ce,
"Bari Ubangiji yă yi nufinsa."

15 Bayan kwanakin nan muka shirya muka tafi Urushalima.
16 Waɗansu almajirai daga Kaisariya suka raka mu, suka kai mu
wurin Manason wanda za mu sauka a wurinsa, shi mutumin
Sayifurus ne, ɗaya daga cikin masu bi na farko.

21.8: A.M. 6.5; 8.5 **21.10:** A.M. 11.28

Bulus Ya Kiyaye Ka'idar Yahudawa domin Bishara

17 Da muka zo Urushalima, 'yan'uwa suka karɓe mu da murna.
18 Washegari Bulus ya tafi tare da mu zuwa wurin Yakubu, dattiban
jama'ar masu bi kuwa duka suna nan. 19 Bayan ya gaisa da su, sai
ya bayyana musu dalla-dalla abubuwan da Allah ya yi a cikin
waɗanda ba Yahudawa ba ta wurin aikin da shi Bulus ya yi. 20 Da
suka ji haka, suka yi wa Allah yabo. Suka ce wa Bulus, "To, ka
gani ɗan'uwa, dubban mutane a cikin Yahudawa sun ba da gaskiya,
dukansu kuwa masu ƙoƙari ne wurin bin Doka. 21 An gaya musu
labarinka, wai kana koya wa dukan Yahudawan da suke cikin
waɗanda ba Yahudawa ba su yar da Dokar Musa. Wato, kana ce
musu kada su yi wa 'ya'yansu kaciya, ko kuwa su bi sauran
al'adunmu. 22 To, yaya za mu yi, da yake lallai za su ji labarin
zuwanka. 23 Saboda haka sai ka yi abin da za mu faɗa maka. Muna
da mutum huɗu a nan da suka yi alkawari. 24 Sai ka tafi da su ku
tsarkake gaba ɗaya, ka kuma biya kuɗin tsarkakewar don a yi musu
aski. Ta haka kowa zai sani cewa duk abin da aka gaya musu game
da kai ba gaskiya ba ne, za a ga cewa kai kana kiyaye dokoki.
25 Amma game da waɗanda ba Yahudawa ba da suka ba da gaskiya,
mun riga mun aika wasiƙa a kan mun yanka hukunci cewa, kada
su ci abin da aka yanka wa gunki, kada su yi lalata, kada su ci
naman dabbar da aka murɗe ko nama tare da jini."

26 Washegari Bulus ya ɗauki mutanen nan suka tsarkake tare.
Sa'an nan ya shiga haikali domin yă sanar da ranar cikar
tsarkakewarsu, wato, ranar da za a ba da baiko domin kowane
ɗayansu.

An Kama Bulus a cikin Haikali

27 Da kwana bakwai ɗin suka kusan cika, waɗansu Yahudawa
daga Asiya suka ga Bulus a haikali. Sai suka zuga taron mutane,
suka kama shi, 28 suna ihu suna cewa, "Ku 'yan'uwa Isra'ilawa,
ku taimaka! Ga mutumin nan da yake bi ko'ina yana zagin
mutanenmu, da dokokinmu, da kuma wannan haikalinmu. Har ma
ya kawo waɗansu Helenawa a cikin haikali ya ƙazantar da wurin
nan mai tsarki." 29 Sun ce haka ne saboda dā sun ga Bulus tare
da Turofimus, mutumin Afisa, a cikin gari. Wannan ne ya sa suka
yi tsammani Bulus ya shigo tare da shi a cikin haikalin.

30 Sai duk garin ya ruɗe, jama'a suka taso gaba ɗaya a guje
suka kama Bulus, suka fitar da shi daga haikali, aka kuma rufe

21.23-24: L. Kid'6.13-21 **21.25:** A.M. 15.29 **21.29:** A.M. 20.4

ƙofofin nan da nan. 31 Suna ƙoƙari su kashe shi ke nan, sai labari
ya kai wurin shugaban ƙungiyar sojoji cewa Urushalima tana
cikin rikici ainu. 32 Nan take ya ɗibi sojoji da manyan sojojin
Roma, suka tafi wurin da gudu. Da jama'ar suka ga shugaban da
sojoji, sai suka daina dūkan Bulus. 33 Sai shugaban ya zo ya kama
Bulus, ya sa a ɗaure shi da sarƙa biyu. Sa'an nan ya yi tambaya
ko shi wane ne, da kuma abin da ya yi. 34 Taron kuwa suna ta
hayaniya, waɗansu su ce wannan, waɗansu su ce wancan. Saboda
yawan hayaniyar shugaban bai iya samun ainihin tushen maganar
ba, sai ya ba da umarni a kai Bulus barikin soja. 35 Da Bulus ya
zo bakin matakala, sai da sojoji suka ɗauke shi saboda rikicin
taron ya yi yawa. 36 Taron mutanen da suka biyo suka yi ta ihu
suna cewa, "A yi gaba da shi!"

Bulus Ya Yi wa Taron Magana

37 An kusa shigar da Bulus barikin soja ke nan, sai ya ce wa
shugaban, "Ko ka yarda in yi magana da kai?"

Sai shugaban ya ce, "Ashe ka iya Helenanci? 38 Ba kai ne
mutumin Masar nan da shekarun baya ya jawo tawaye ba, har ya
ja mutanen nan dubu huɗu masu kisankai a daji?"

39 Sai Bulus ya amsa ya ce, "Ai, ni Bayahude ne na Tarsus
a ƙasar Kilikiya. Ni ɗan birnin nan mai muhimminci ne. Ina
roƙonka, ka bar ni in yi wa mutanen nan magana."

40 Sai ya ba shi izni, Bulus kuwa ya tsaya a kan matakala, ya
ɗaga wa jama'a hannu su yi shiru. Da suka yi tsit, sai ya yi musu
magana da yaren Aramaya.[m]

22 1 "Ku 'yan'uwa da iyaye, ku saurara in bayyana muku
abin da ya faru, don in nuna cewa ba ni da laifi." 2 Da
suka ji ya yi musu magana da yaren Aramaya, sai suka ƙara yin
shiru. Sa'an nan ya ce:

3 "Ni Bayahude ne, an haife ni a Tarsus, ƙasar Kilikiya, amma
a nan garin na yi girma. Na yi makaranta a ƙarƙashin Gamaliyel,
wanda ya koya mini kome game da dokokin kakanninmu. Ina da
ƙoƙari cikin bauta wa Allah, kamar yadda dukanku kuke yi a yau,
4 har na tsananta wa masu bin wannan Hanyar. Ina kakkashe su,
ina ɗaure mutane maza da mata, ina sa su cikin kurkuku. 5 Babban
firist ma da dukan Majalisar shugabannin jama'a za su iya
shaidata. Daga wurinsu ne na karɓi wasiƙu zuwa ga 'yan'uwanmu

---

22.3: A.M. 5.34-39

[m] **21.40 yaren Aramaya:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Ibraniyanci" ne a nan.

Yahudawa a cikin Dimashƙu. Na tafi wurin domin in kama masu bin Hanyan nan waɗanda suke a can ma, in kawo su Urushalima domin a hukunta su.

Bulus Ya Faɗa yadda Ya Juyo ga Bin Ubangiji
(A.M. 9.1-19, 26.12-18)

6 "Ina cikin tafiya, na kusa in kai Dimashƙu, da tsakar rana,
sai babban haske daga sama ya haskaka kewaye da ni. 7 Sai na
faɗi a ƙasa na kuma ji wata murya tana ce mini, 'Shawulu,
Shawulu, don me kake tsananta mini?' 8 Na amsa, 'Wane ne kai,
Mai girma?' Sai ya ce mini, 'Ni ne Yesu Banazare wanda kake
tsananta wa.' 9 To, waɗanda suke tare da ni sun ga hasken, amma
ba su ji muryar wanda yake magana da ni ba. 10 Sai na tambaya
na ce, 'To, me zan yi, Ubangiji?' Sai Ubangiji ya ce mini, 'Tashi,
ka shiga Dimashƙu, a can ne za a gaya maka abin da aka shirya
maka ka yi.' 11 Tun da ba na iya gani saboda tsananin hasken nan,
waɗanda suke tare da ni suka kama hannuna, suka yi mini jagora
zuwa cikin Dimashƙu.

12 "Sai kuma wani mai suna Hananiya ya zo wurina. Shi mai
bautar Allah ne bisa ga Dokarmu, wanda dukan Yahudawan can
suke yabonsa. 13 Ya zo ya ce mini, 'Ɗan'uwana Shawulu, ka iya
sāke ganin gari.' Nan take idanuna suka buɗe, na kuwa gan shi.
14 Sai ya ce, 'Allahn kakanninmu ya zaɓe ka ka san nufinsa, ka
ga Mai Adalcin nan, ka kuma ji maganarsa. 15 Don za ka zama
mai shaidarsa ga dukan mutane game da abin da ka gani, ka kuma
ji. 16 To, yanzu me kake jira? Tashi a yi maka baftisma a wanke
zunubanka ta wurin kira bisa ga sunan Ubangiji.'

Kiran Bulus zuwa ga Waɗanda ba Yahudawa ba

17 "Bayan na dawo Urushalima, ina addu'a a haikali, sai na
ga ru'uya. 18 A cikin ru'uyar kuwa na ga Yesu yana ce mini, 'Yi
maza, ka tashi ka bar Urushalima da sauri, don ba za su yarda
da shaidarka game da ni ba.' 19 Ni kuma na ce, 'Ubangiji, ai, su
ma kansu sun sani cewa a kowace majami'a na ɗaɗɗaure waɗanda
suka gaskata da kai, na kuma dūke su. 20 Sa'ad da kuma aka zub
da jinin Istifanus mai shaidarka, ni da kaina ina tsaye a wurin,
ina goyon bayan abin da aka yi, har ma ina gadin tufafin waɗanda
suka kashe shi.' 21 Sai Ubangiji ya ce mini, 'Tashi ka tafi, zan
aike ka can nesa wurin waɗanda ba Yahudawa ba.' "

22.4-5: A.M. 8.3; 26.9-11 **22.20:** A.M. 7.58

22 Taron sun yi ta sauraron Bulus har ya iso wannan kalma,
sai suka yi ihu suka ce, "A kashe shi! A raba irin mutumin nan
da duniya, bai kamata yă rayu ba!" 23 Sai suka dinga ihu suna
jefa mayafansu, suna ta da ƙura. 24 Saboda haka sai shugaban ya
ba da umarni a kai Bulus barikin soja a bincike shi da bulala, don
a nemi dalilin da ya sa taron suke yi masa ihu haka. 25 Amma
bayan sun ɗaure shi domin su yi masa bulala, sai Bulus ya ce wa
babban sojan Roma da yake tsaye kusa, "Ashe, daidai ne bisa ga
doka ka yi wa mutumin da yake da 'yancin Roma bulala, ba tare
da an yi masa shari'a ba?"

26 Da babban sojan Roma ya ji haka, sai ya je wurin shugaban
ya ce masa, "Me kake shirin yi ne? Mutumin nan fa yana da
'yancin Roma."

27 Sai shugaban ya zo ya ce wa Bulus, "Gaya mini gaskiya,
kai kana da 'yancin Roma?"

Sai Bulus ya ce, "I."

28 Sai shugaban ya ce, "Ni fa da kuɗi mai yawa na sami
'yancin nan."

Bulus ya ce, "Ni kuwa da shi aka haife ni."

29 Saboda haka waɗanda suke shirin bincikensa suka ja baya
nan da nan. Shi ma shugaban da ya gane Bulus mai 'yancin Roma
ne sai ya ji tsoro, ga shi kuwa ya riga ya ɗaure shi.

Bulus a gaban 'Yan Majalisa

30 Washegari kuma shugaban yana so yă san ainihin ƙarar da
Yahudawa suke yi game da Bulus, sai ya kunce shi, ya ba da
umarni manyan firistoci da dukan Majalisa su taru. Sa'an nan ya
kawo Bulus ya sa shi yă tsaya a gabansu.

23 1 Sai Bulus ya zuba wa 'yan Majalisar ido ya ce, "Ku
'yan'uwana, har wa yau, a cikin zuciyata ba ni da shakka
ko wani abin damuwa a kan rayuwar da na yi a gaban Allah."
2 Da jin wannan sai Hananiya babban firist ya sa waɗanda suke
tsaye kusa da Bulus su buge shi a baki. 3 Sai Bulus ya ce masa,
"Kai bango ne da aka shafe yă zama fari, wato, munafuki, kai
ma Allah zai buge ka! Ka zauna kana yi mini hukunci bisa ga
Doka, amma ga shi kuwa kana sa a buge ni, wanda bai yi daidai
ba bisa ga Doka."

4 Waɗanda suke tsaye a wurin suka ce wa Bulus, "Babban
firist na Allah za ka yi masa zagi?"

23.3: Mat 23.27-28

5 Bulus kuwa ya ce, "'Yan'uwana, ban san shi ne babban firist
ba. Gama an rubuta cewa, 'Kada ka zagi shugaban jama'a.' "
6 Da Bulus ya kula cewa waɗansu Sadukiyawa ne, waɗansu
kuma Farisiyawa ne, sai ya ta da murya a Majalisar ya ce,
"'Yan'uwa, ni ma Bafarisiye ne, ɗan Farisiyawa. Ga shi kuwa
don na sa zuciya ga tashin matattu shi ya sa ake yi mini shari'a."
7 Da ya faɗa haka sai gardama ta tashi tsakanin Farisiyawa da
Sadukiyawa, har taron ya rabu kashi biyu. 8 Gama Sadukiyawa
suna riƙe da ra'ayi cewa babu tashin matattu, babu mala'iku, ko
ruhohi. Farisiyawa kuwa sun yarda akwai duka uku. 9 Sai babban
rikici ya tashi, waɗansu malaman dokoki na ƙungiyar Farisiyawa
suka tashi tsaye, suka yi ta gardama suka ce, "Mu ba mu sami
mutumin nan da laifin kome ba. Mai yiwuwa wani ruhu, ko
mala'ika ne ya yi masa magana."
10 Da gardamar ta yi tsanani sai shugaban ya ji tsoro kada su
yi kaca-kaca da Bulus. Sai ya ba da umarni sojojin su sauko su
ƙwace Bulus da ƙarfi daga wurinsu, su kai shi barikin soja.
11 Da dare ya yi sai Ubangiji ya tsaya kusa da Bulus ya ce,
"Ka ci gaba da ƙarfin zuciyarka, domin kamar yadda ka shaide
ni a Urushalima, haka kuma lallai ne za ka shaide ni a Roma."

An Yi Shawara a Kashe Bulus

12 Da gari ya waye, Yahudawa suka yi shiri su kashe Bulus.
Suka yi rantsuwa cewa ba za su ci ba, ba za su sha ba, sai sun
kashe Bulus. 13 Waɗanda suka yi wannan mugun shirin kuwa sun
fi mutum arba'in. 14 Sai suka je wurin manyan firistoci da
shugabanni, suka ce, "Mun yi babbar rantsuwa cewa ba za mu
ci ba, ba za mu sha ba sai mun kashe mutumin nan. 15 Saboda
haka yanzu ku da Majalisa ku ce wa shugaban sojoji yă kawo
muku shi, kamar kuna so ne ku ƙara bincike maganarsa sosai, mu
kuwa a shirye muke mu kashe shi kafin yă iso."
16 To, da ɗan 'yar'uwar Bulus ya ji labarin shirin da suke yi,
sai ya je ya shiga barikin ya faɗa wa Bulus. 17 Bulus kuwa ya
kira wani babban sojan Roma ya ce, "Ka kai saurayin nan wurin
shugaba, yana da wata maganar da zai gaya masa." 18 Sai babban
sojan Roma ya ɗauki saurayin ya kai shi wurin shugaban. Babban
sojan Roma ya ce, "Ɗan kurkukun nan Bulus, ya kira ni, ya roƙe
ni in kawo saurayin nan a wurinka, don saurayin yana da abin da
zai gaya maka."

23.5: Fit 22.28 **23.6**: A.M. 26.5; Filib 3.5 **23.8**: Mat 22.23; Mar 12.18; Luk 20.27

19 Sai shugaban ya kama hannun saurayin, ya ja shi gefe ɗaya,
ya tambaye shi, shi kaɗai, "Me za ka gaya mini?"

20 Yaron ya ce, "Shugabannin Yahudawa sun shirya za su
roƙe ka ka kai Bulus Majalisa gobe, kamar suna so su ƙara bincike
maganarsa sosai. 21 Amma kada ka yarda musu, don fiye da
mutum arba'in daga cikinsu suna nema su kashe shi, sun kuma
yi rantsuwa cewa ba za su ci ba, ba za su sha ba sai sun kashe
shi. Yanzu kuwa a shirye suke, suna jira ne kawai ka yarda."

22 Sai shugaban ya ja masa kunne ya ce, "Kada ka gaya wa
kowa cewa ka gaya mini wannan magana." Sa'an nan ya
sallame shi.

An Aika da Bulus zuwa Wurin Gwamna Felis

23 Sa'an nan shugaban ya kira manyan sojojin Roma biyu ya
ce musu, "Ku shirya don za ku tashi zuwa Kaisariya da ƙarfe
tara na dare, tare da sojoji ɗari biyu, da sojoji saba'in masu hawan
dawakai, da sojoji ɗari biyu masu faɗa da māshi. 24 Ku kuma
samo dawakin da Bulus zai hau. Sai ku kai shi wurin gwamna
Felis lafiya lau." 25 Shugaban sojan kuma ya rubuta wasiƙa haka:

26 "Daga Kalaudiyus Lisiyas, zuwa ga mai girma gwamna
Felis. Gaisuwa mai yawa.

27 "Mutumin nan, Yahudawa sun kama shi, sun kusa su kashe
shi, sai na yi sauri da sojojina na ƙwato shi, domin na ji shi mai
'yancin Roma ne.

28 "Tun da ina so in ji laifin da suke zarginsa da shi, sai na
kai shi Majalisarsu. 29 Na kuwa samu suna zarginsa a kan
maganar shari'arsu, amma laifin da suka ɗora masa bai isa a
ɗaure shi ko a kashe shi ba.

30 "Da aka sanar mini cewa akwai wani mugun shirin da aka
ƙulla masa, nan da nan na aika da shi wurinka. Na kuma umarci
masu ƙararsa su faɗa a gabanka laifin da suka ga ya yi."

31 Saboda haka sojojin suka ɗauki Bulus, kamar yadda aka
umarce su, suka kai shi Antifatiris da daddare. 32 Washegari suka
bar sojoji masu hawan dawaki su ci gaba da shi, su kuwa suka
koma barikinsu. 33 Da sojoji masu hawan dawakin suka isa
Kaisariya, sai suka ba gwamna wasiƙar, suka kuma bar Bulus a
hannunsa.

34 Da gwamna ya karanta wasiƙar, ya tambayi Bulus ko shi
daga wane yanki ne. Da ya ji daga Kilikiya yake, 35 sai ya ce,
"Zan saurari maganarka, lokacin da masu ƙararka sun zo." Sai

gwamnan kuma ya ba da umarni a tsare shi a fadar da sarki Hirudus ya gina.

Yahudawa Sun Kai Karar Bulus

24 [1] Bayan kwana biyar sai babban firist, Hananiya, ya zo tare da waɗansu shugabanni, da kuma wani lauya mai suna Tartulus, don su yi ƙarar Bulus a gaban gwamna. [2] Aka shigo da Bulus, sai Tartulus ya fara kai ƙarar Bulus a gaban gwamna ya ce:

"Mai girma, ta wurin hikimarka ne aka kyautata zaman jama'armu, kuma don kana da hangen nesa, shi ya sa zaman jama'armu yana da kyau; [3] mutanenmu ko'ina, suna gode maka ba iyaka. [4] Amma don kada in ɓata maka lokaci, ina roƙonka, cikin kirkinka ka saurari gajeren abin da za mu faɗa maka. [5] Mun sami wannan mutum mai yawan rikici ne, yana ta kawo tashin hankali a cikin Yahudawa ko'ina a cikin duniya, kuma shi ne shugaban ɗarikar Nazarawa wato, masu bin Yesu ke nan. [6] Har ma yana nema yă wulaƙanta haikali, amma muka kama shi.[n] [8] Idan kuwa ka bincike shi kai da kanka, za ka iya sani daga wurinsa dukan abubuwan da muke tuhumarsa da su." [9] Yahudawa ma suka goyi bayan haka, suka yarda cewa haka abin yake.

Bulus Ya Kāre Kansa a gaban Felis

10 Da gwamna ya ba Bulus zarafi yă yi magana, sai Bulus ya amsa ya ce: "Zan kāre kaina da farin ciki, tun da na sani ka yi shekaru da yawa kana shari'ar jama'an nan. [11] Ai, idan ka bincika za ka gane cewa bai fi kwana goma sha biyu ba tun da na tafi Urushalima in yi sujada. [12] Waɗannan masu ƙarata kuwa ba su taɓa samuna ina mahawara da kowa ba, ko kuwa ina ta da hankalin mutane a haikali, ko a majami'u, ko kuwa a cikin birnin ba. [13] Abubuwan da suke faɗa a kaina yanzu ma ba za su iya tabbatar maka ba. [14] Abu ɗaya ne na yarda da shi, shi ne ina bin Allah na kakanninmu ta Hanyan nan da waɗannan suke ce ba gaskiya ba, ina kuma gaskata dukan abin da yake a rubuce bisa ga Doka, da kuma littattafan annabawa. [15] Ina sa zuciya ga Allah, yadda su waɗannan ma suke yi, cewa, za a ta da matattu, masu adalci da marasa adalci duka. [16] Shi ya sa kullum nake ƙoƙari a

[n] **24.6** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da ayoyi 6b-8 haka: Mun yi niyya mu hukunta shi bisa ga shari'armu. 7 Amma shugaba Lisiya ya zo ya ƙwace shi daga hannunmu da ƙarfi da yaji, 8 ya sa masu ƙarar mutumin nan su zo gabanka.

zuciyata in kasance ba ni da shakka ko wani abin damuwa a gaban Allah da mutane.

17 "To, bayan 'yan shekaru sai na dawo Urushalima domin in kawo taimako wurin jama'armu masu bukata, in kuma ba da baiko. 18 Ina cikin yin haka sai suka same ni a haikali. Na gama tsarkake kaina, ba na kuwa tare da wani taro, ban kuwa ta da hankalin jama'a ba. 19 Amma akwai waɗansu Yahudawa daga ƙasar Asiya da suke a wurin, su ne kuwa ya kamata su zo nan gabanka su yi ƙarata idan suna da wata magana game da ni. 20 Ko kuwa bari waɗannan mutanen su faɗa laifin da suka same ni da shi lokacin da na tsaya a gaban Majalisa, 21 sai dai ko idan maganan nan ɗaya kawai da na faɗa a lokacin da nake tsaye a gabansu, da na ɗaga murya cewa, 'Game da maganar tashin matattu ake yi mini shari'a a gabanku yau.' "

An Tsare Bulus a Kaisariya

22 Felis kuwa ya san abubuwa da ɗan dama game da Hanyar Yesu, sai ya tsayar da su ya ce, "Sai shugaba Lisiya ya zo tukuna zan yanka muku shari'a." 23 Felis ya ba babban sojan Roma umarni yă yi gadin Bulus, amma kada yă matsa masa da yawa, kada kuma yă hana abokansa zuwa wurinsa su biya masa bukatunsa.

24 Bayan 'yan kwanaki, Felis tare da matarsa Durusila, wata Bayahudiya, suka zo. Sai ya aika a kawo Bulus, ya kuma saurare shi a kan maganar gaskatawa da Almasihu Yesu. 25 Sa'an nan Bulus ya soma ba da bayani a kan adalci, da shan ƙarfin sha'awar jiki, da kuma ranar hukuncin nan mai zuwa. Da jin haka sai tsoro ya kama Felis, sai ya ce wa Bulus, "Yanzu dai ka koma. Idan na sami zarafi zan kira ka." 26 Don yana sa rai Bulus zai ba shi kuɗi, shi ya sa Felis ya yi ta kiransa a kai a kai, yana hira da shi.

27 Amma bayan shekara biyu sai Fokiyus Festus ya zama gwamna a maimakon Felis. Felis kuwa don yana neman farin jini a wurin Yahudawa ya bar Bulus a kurkuku.

Bulus Ya Ɗaukaka Kara zuwa Gaban Kaisar

25 1 To, bayan kwana uku da Festus ya iso domin yă kama aikin gwamna, sai ya tashi daga Kaisariya ya tafi Urushalima. 2 Sai manyan firistoci da shugabannin Yahudawa suka kai ƙarar Bulus a wurinsa. Suka roƙe shi, 3 yă sa a mai da Bulus Urushalima domin sun shirya waɗansu su jira su kashe shi

24.17-18: A.M. 21.17-28 **24.21**: A.M. 23.6

a hanya. 4 Festus ya amsa ya ce, "Za a yi gadin Bulus a Kaisariya,
ni da kaina zan je can ba da jimawa ba. 5 Saboda haka sai
manyanku su zo tare da ni, idan kuwa mutumin nan yana da wani
laifi sai su tuhume shi."

6 Bai fi kwana takwas ko goma a wurinsu ba, sai ya koma
Kaisariya. Washegari kuma ya zauna a kujerar shari'a, ya sa a
kawo Bulus a gabansa. 7 Da Bulus ya zo, Yahudawan da suka zo
daga Urushalima suka tashi suka kewaye shi, suna ta kawo
ƙararraki masu yawa, masu tsanani a kansa, waɗanda ma ba su
iya tabbatarwa ba. 8 Amma Bulus ya kāre kansa ya ce, "Ni ban
yi wa Dokar Yahudawa laifi ba, ban kuma yi wa haikali, ko Kaisar
laifi ba ko kaɗan."

9 Amma Festus yana so ya faranta wa Yahudawa rai, ya
tambayi Bulus, "Ko ka yarda ka je Urushalima a yi maka shari'a
a gabana a can game da waɗannan abubuwa?"

10 Amma Bulus ya ce, "Ina gaban kotun Kaisar, a nan ne ya
kamata a yi mini shari'a. Ban yi wa Yahudawa wani laifi ba, kai
ma ka san da haka sosai. 11 Idan ni mai laifi ne, har na yi laifin
da ya isa a kashe ni, ai, ba zan ƙi a kashe ni ba. Amma idan ba
wata gaskiya a cikin ƙarar da suke yi, to, ba mai iya ba da ni
gare su. Na roƙa a ɗaukaka ƙarata zuwa gaban Kaisar."

12 Bayan Festus ya yi shawara da majalisarsa, sai ya amsa ya
ce, "To, ka roƙa a ɗaukaka ƙararka zuwa gaban Kaisar, wurin
Kaisar kuwa za ka tafi."

Bulus a gaban Agiriffa da Banis

13 Bayan 'yan kwanaki, sarki Agiriffa da Banis suka zo
Kaisariya domin su marabci Festus. 14 Tun da za su yi kwanaki
da dama a can, sai Festus ya kawo maganar Bulus ga sarki. Festus
ya ce: "Akwai wani mutumin da Felis ya bar mini a kurkuku.
15 Lokacin da nake Urushalima manyan firistoci da shugabannin
Yahudawa suka kawo mini ƙarar mutumin nan, suka roƙe ni in
yanke masa hukunci. 16 Amma na gaya musu cewa mu Romawa
ba mu saba yi wa mai laifi shari'a ba sai an kawo shi a gaban
masu ƙararsa, sai an kuma ba shi zarafi domin yă kāre kansa
game da ƙarar da aka yi. 17 Saboda haka da suka zo nan tare da
ni, ban ɓata lokaci ba, washegari kawai na hau kujerar shari'a,
na kuma sa a kawo mutumin. 18 Da masu ƙarar suka tashi, ba su
kawo ƙararsa a kan wani mummunan laifin da nake tsammani ya
yi ba. 19 Sai dai suna da waɗansu maganganun da ba su yarda da
Bulus a kai ba, game da addininsu, da wani Yesu wanda ya mutu,

wanda Bulus ya nace cewa yana da rai. 20 Ni kuwa da na rasa
yadda zan bincike wadannan abubuwa, sai na tambayi Bulus ko
ya yarda yă je Urushalima a yi masa shari'a a can game da
abubuwan nan. 21 Amma da ya nemi a tsayar da maganarsa domin
babban sarki Kaisar yă yanke masa shari'a, sai na ba da umarni
a yi gadinsa har zuwa lokacin da zan aika da shi wurin Kaisar."

22 Sai sarki Agiriffa ya ce wa Festus, "Ni ma dai zan so in
saurari mutumin nan da kaina."

Festus ya ce, "Za ka kuwa ji shi gobe."

23 To, washegari sai Agiriffa da Banis suka shigo shiga irin
ta sarauta, sun zo tare da shugabannin yaki da kuma manyan
garin. Sai Festus ya ba da umarni a shigo da Bulus. 24 Sai Festus
ya ce, "Sarki Agiriffa, da dukan mutanen da suke nan tare da mu,
ga mutumin da duk jama'ar Yahudawa suka kawo mini kararsa
a Urushalima, da kuma a nan, har suna ihu wai bai kamata a bar
shi da rai ba. 25 Amma ni ban ga ya yi wani abin da ya isa a
kashe shi ba. Tun da kuma shi da kansa ya nema a kai shari'arsa
gaban mai girma Kaisar, na ce to zan aika da shi wurinsa.
26 Amma ba ni da wata tabbatacciyar maganar da zan rubuta wa
mai girma sarkin Roma a kansa. Saboda haka na kawo shi
gabanku, musamman gabanka, sarki Agiriffa, don bayan mun
bincike shi, ko zan sami abin da zan rubuta. 27 Don ni a ganina,
wauta ce a aika da dan kurkuku, ba tare da an nuna laifofin da
ya yi ba."

Bulus Ya Kāre Kansa a gaban Agiriffa

26 1 Daga nan sai Agiriffa ya ce wa Bulus, "An ba ka izni
ka kāre kanka." Sa'an nan Bulus ya daga hannu, ya fara
magana ya ce:

2 "Lallai na yi sa'a, sarki Agiriffa, tun da a gabanka ne zan
kāre kaina yau game da duk maganganun da Yahudawa suka fada
a kaina, 3 musamman da yake kai gwani ne cikin sanin al'adun
Yahudawa da abubuwan da suke gardama a kai. Saboda haka ina
rokonka ka saurare ni da hakuri.

4 "Dukan Yahudawa sun san irin zaman da na yi tun ina
saurayi, wato, tun da farko a garinmu da kuma a Urushalima har
zuwa yau. 5 Sun san ni tun tuni, har ma idan sun so za su iya ba
da shaida cewa lallai ni Bafarisiye ne bisa ga darikan nan da ta
fi tsanani cikin addinin nan namu. 6 Yanzu ina tsaye a gabanku a
yi mini shari'a saboda na sa zuciya a kan cikar alkawarin da Allah

26.5: A.M. 23.6; Filib 3.5

ya yi wa kakanninmu. 7 Alkawarin nan ne kabilunmu goma sha biyu suka sa rai za su ga cikarsa, har suna ƙokari suna bauta wa Allah dare da rana. Ya sarki, saboda na sa zuciya ga cikar alkawarin nan ne Yahudawa suke ganin laifina fa! 8 Me ya sa a ganinku ba ya yiwuwa Allah yă ta da matattu?

9 "To, ni da kaina ma a dā na ga kamar daidai ne in yi abubuwa da yawa in hana cin gaban maganar Yesu Banazare. 10 Abin da na yi ke nan a Urushalima, har na sami izni daga wurin manyan firistoci domin in kulle masu tsarki da yawa a kurkuku. Har ma lokacin da ake kashe su ina goyon bayan haka. 11 Na kuma bi dukan majami'u ina hukunta su ina ƙokarin sa su su zargi sunan Yesu. Don kuma ina fushi da su sosai, sai ina ta binsu har zuwa garuruwa na waɗansu ƙasashe in tsananta musu.

Labarin Juyowar Bulus
(A. M. 9.1-19, 22.6-16)

12 "Ana cikin haka ne, wata rana ina tafiya zuwa Dimashƙu, da iznin manyan firistoci da kuma takardar ikon da suka ba ni. 13 Da tsakar rana a hanya, ranka yă daɗe, na ga wani haske fiye da hasken rana ya haskaka daga sama, ya kewaye ni da abokan tafiyata. 14 Da dukanmu muka fādī a ƙasa, sai na ji wata murya tana ce mini da Ibraniyanci, 'Shawulu, Shawulu, don me kake tsananta mini? Kana ba kanka wahala ne da kake gāba da ni.' 15 Sai na ce, 'Wane ne kai Mai girma?'

"Sai Ubangiji ya ce mini, 'Ni ne Yesu wanda kake tsananta wa. 16 Amma tashi tsaye. Na bayyana a gare ka ne in sa ka yi mini aiki, ka kuma yi shaidar abubuwan da ka gani game da ni, da kuma abubuwan da zan bayyana maka nan gaba. 17 Zan cece ka daga mutanenka, da kuma waɗanda ba Yahudawa ba, waɗanda zan aike ka zuwa wurinsu. 18 Za ka buɗe musu idanunsu, su juyo daga duhu zuwa haske, daga kuma mulkin Shaiɗan zuwa wurin Allah. Ta haka za su sami gafarar zunubai, da kuma gādo tare da dukan waɗanda suka zama masu tsarki saboda sun ba da gaskiya gare ni.'

Bulus Ya Shaida Ayyukansa

19 "Saboda haka, ya sarki Agiriffa, ban ƙi yin biyayya da ru'uyan nan da ta zo mini daga sama ba. 20 Na fara yin wa'azi wa mutanen Dimashƙu, sa'an nan na yi ga mutanen Urushalima da dukan kewayen Yahudiya, sa'an nan kuma na yi wa waɗanda

26.9-11: A.M. 8.3; 22.4-5 **26.12-18** A.M. 9.1-19; 22.6-16

ba Yahudawa ba cewa su tuba su juyo ga Allah, su kuma yi abubuwan da za su nuna sun tuba. 21 Shi ne ya sa Yahudawa suka kama ni a cikin haikali suna ƙoƙari su kashe ni. 22 Amma Allah ya taimake ni har zuwa yanzu, shi ya sa ina nan ina yin shaida ga manya da ƙanana. Ba wani abu dabam nake faɗa ba sai dai abin da annabawa da Musa suka ce zai faru, 23 wato, lallai ne Almasihu yă sha wahala, yă zama na farkon da zai tashi daga matattu. Ta haka zai kawo haske ga dukan mutane, Yahudawa da waɗanda ba Yahudawa ba duka."

24 Bulus yana cikin kāre kansa ke nan, sai Festus ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, "Bulus, kana hauka! Yawan karatunka ya juya maka kai!"

25 Amma Bulus ya ce, "Mai girma Festus, ba na hauka. Gaskiya nake faɗa cikin natsuwa. 26 Ai, sarki ya san wannan abin, ina kuma yi masa magana ba tsoro. Na tabbata ya san waɗannan al'amura duka, don wannan abu ba a ɓoye aka yi shi ba. 27 Sarki Agiriffa, ka gaskata da annabawa? Na sani ka gaskata."

28 Sai Agiriffa ya ce wa Bulus, "Wato, a ɗan gajeren lokacin nan kake so ka rinjaye ni in zama Kirista?"

29 Bulus kuwa ya ce, "Ko a ɗan gajeren lokaci, ko a dogo, ina fata Allah zai sa ba kai kaɗai ba, har ma dukan waɗanda suke saurarona a yau, su zama kamar yadda nake, sai dai ban da sarƙan nan."

30 Sai sarki ya tashi, haka ma gwamna da Banis, da waɗanda suke zaune tare da su. 31 Da sun fita daga wurin shari'a suka ce wa juna, "Ai, mutumin nan bai yi wani abin da ya isa a kulle shi, ko a kashe shi ba."

32 Sai Agiriffa ya ce wa Festus, "Da ba don dai mutumin nan ya ɗaukaka ƙararsa zuwa gaban Kaisar ba, da sai a sake shi."

Bulus Ya Shiga Jirgin Ruwa zuwa Roma

27 1 Da aka shirya mu tashi a cikin jirgin ruwa zuwa ƙasar Italiya, sai suka ba da Bulus da waɗansu 'yan sarƙa a hannun wani babban sojan Roma, mai suna Juliyos, ɗaya daga cikin sojojin ƙungiyar Kaisar. 2 Da muka shiga wani jirgi na Adiramitiyum, mai shirin tashi zuwa waɗansu garuruwan da suke gefen Asiya, muka fara tafiya. Aristarkus, wani mutumin Tasalonika ta ƙasar Makidoniya, yana tare da mu. 3 Washegari sai ga mu a Sidon. Juliyos kuwa ya yi wa Bulus alheri, ya bar shi yă je yă ga abokansa su biya masa bukatarsa. 4 Da muka tashi

26.20: A.M. 9.20; 28-29 **26.23:** Ish 42.6; 49.6; 1 Kor 15.20

daga nan a jirgin ruwa, iska tana gāba da mu. Saboda haka muka
zaga ta bayan Sayifurus inda iska ba ta da ƙarfi. 5 Bayan mun
ƙetare tekun da yake kusa da ƙasar Kilikiya da Bamfiliya, muka
isa Mira ta ƙasar Likiya. 6 A nan babban sojan Roma ya sami
wani jirgin Alekzandiriya mai zuwa ƙasar Italiya, ya sa mu a ciki.
7 Muka yi kwana da kwanaki muna tafiya a hankali, har da
kyar muka kai kusa da Kinidus. Da iska ta hana mu ci gaba, sai
muka zagaya gefen da ba iska, wato, ta bayan tsibirin Kirit kusa
da Salmoni. 8 Muka wuce shi da kyar, har muka isa wani wurin
da ake ce da shi Amintacciyar Mafaka, kusa da birnin Likiya.
9 Da yake mun ɓata lokaci da yawa a wurin, tafiyar ma ta
zama da hatsari, domin a lokacin shekara ya yi nisa har Ranar
Bikin Fansar Zunubai[o] ta wuce. Sai Bulus ya ba su shawara, 10 ya
ce musu, "Jama'a, na ga fa tafiyan nan za ta zama da hatsari da
kuma hasara mai yawa, ba hasarar kaya da jirgin kawai ba, har
ma da rayukanmu." 11 Amma Juliyos bai yarda da abin da Bulus
ya faɗa ba, a maimakon haka ya saurari maganar mai tuƙin jirgin
da kuma ta mai jirgin. 12 Da yake mafakar Likiya bai yi kyau
jirage su ci damina a nan ba, sai yawancinsu suka yarda a ci gaba
da tafiya, a kuma yi ƙoƙari a kai Finikiya, in ya yiwu, domin su
ci damina a can. Finikiya kuwa wata tashar jirgi ce a Kirit wadda
take fuskantar arewa ta wajen yamma, da kuma kudu ta wajen
yamma.

Hadari a Teku

13 Da iska ta soma hurawa daga kudu kaɗan-kaɗan, sai
mutanen suka yi tsammani bukatarsu ta biya, sai suka jawo
ƙarfen da yake riƙe jirgin, suka bi gefen tsibirin Kirit, kusa da
bakin teku. 14 Ba da jimawa ba sai ga wata babbar iska daga
arewa ta gabas ta bugo daga tsibirin. 15 Da iskar ta bugo jirgin,
har ya kāsa fuskantar iskar, sai muka bari kawai iskar ta yi ta
tura mu. 16 Da muka bi ta bayan wani ɗan tsibiri mai suna
Kauda, inda iska ta ragu, da kyar muka jawo ƙaramin jirgin kusa
da jirgin. 17 Bayan sun jawo ƙaramin jirgin zuwa cikin babban
jirgin, suka yi dabara suka ɗaɗɗaura igiyoyi kewaye da babban
jirgin, domin kada ya farfashe. Suka kuma sauke filafilai su bar
iska ta tura jirgin domin ba su iya tuƙa shi ba. Sun yi haka
domin suna tsoro kada a jefa su a yashin Sirtis mai haɗiye kome.

[o] **27.9 Ranar Bikin Fansar Zunubai**: Ana wannan bikin kusa da ƙarshen watan
Satumba ko farkon watan Oktoba, a wannan lokacin kuwa akan yi mummunar
iska a teku.

18 Saboda ruwan yana hauka, yana jijjigamu sosai, sai washegari
suka fara kwashe kayan da yake a cikin jirgin, suka jefa a cikin
ruwa. 19 A rana ta uku kuma, su da hannayensu suka jefar da
wadansu kayan aikin jirgin. 20 Da dai muka yi kwana da kwanaki
ba mu ga rana ko taurari ba, kuma babbar iskar hadari tana ta
dūkanmu, sai muka fid da zuciya za mu tsira.

21 Da yake sun dade ba su ci abinci ba, sai Bulus ya tashi
tsaye a tsakiyarsu, ya ce, "Jama'a, da kun ji maganata cewa
kada ku tashi daga tsibirin Kirit, da ba ku fāda wa wannan
hatsari da masifa ba. 22 Amma yanzu ina yin muku gargadī ku
yi ƙarfin hali, don ba wanda zai yi hasarar ransa a cikinku, sai
dai a yi hasarar jirgin. 23 Gama a daren jiya wani mala'ikan
Allah wanda nake nasa, wanda nake kuma bauta masa, ya tsaya
kusa da ni, 24 ya ce, 'Kada ka ji tsoro, Bulus. Lallai za ka tsaya
a gaban Kaisar. Ga shi kuma ta dalilinka Allah cikin alherinsa
zai ceci abokan tafiyarka.' 25 Saboda haka sai ku yi ƙarfin hali,
ku jama'a, domin na gaskata Allah a kan cewa yadda aka fada
mini din nan, haka zai zama. 26 Amma fa dole ne iska ta jefar
da mu a yashin wani tsibiri."

27 A dare na goma sha hudu, ana ta kore mu dai a tekun
Adiriya. Wajen tsakiyar dare sai masu tuƙin jirgin suka yi
tsammani mun yi kusa da ƙasa. 28 Sai suka gwada zurfin ruwan
suka ga ya kai ƙafa dari da ashirin. Da muka ci gaba kadan, sai
suka sāke gwadawa, suka sami ƙafa casa'in. 29 Don tsoro kada
jirginmu yă yi karo da duwatsu, sai suka saki ƙarafa masu nauyi
guda hudu ta bayan jirgin domin a hana jirgin tafiya. Sai suka
zuba ido suka roƙi Allah gari yă waye da sauri. 30 Amma masu
tuƙin jirgin sun yi ƙoƙari su gudu. Sai suka saukar da ƙaramin
jirgin suna wayo kamar za su saukar da ƙarfe mai nauyi daga
gaban babban jirgin. 31 Sai Bulus ya ce wa babban sojan Roma
da kuma sojojin, "Idan mutanen nan ba su tsaya a cikin jirgin
nan ba, ba yadda za ku tsira." 32 Da jin haka sai sojojin suka
yayyanke igiyoyin ƙaramin jirgin, suka bar shi ya bi ruwa.

33 Da gari ya kusan wayewa, sai Bulus ya roƙe su su dan ci
abinci, ya ce, "Yau fa, kwana goma sha hudu ke nan kuke zaman
tsammani, ba ku ci wani abu ba. 34 Saboda haka ina roƙonku ku
ci abinci don lafiyarku, tun da yake ba wani a cikinku wanda zai
rasa ko gashin kansa guda daya." 35 Da ya fada haka, sai ya dauki
burodi, ya yi godiya ga Allah a gabansu duka, ya karraba ya fara
ci. 36 Sai duka suka sami ƙarfafawa, su ma suka ci abinci. 37 Mu
duka a cikin jirgin kuwa mutum dari biyu da saba'in da shida ne.

38 Da suka ci suka ƙoshi, sai suka rage wa jirgin nauyi ta zubar da alkama cikin ruwa.

Rafkuman Ruwa Sun Farfashe Jirgin

39 Da gari ya waye masu tuƙin jirgin ba su iya gane da ƙasar da suke ba, amma dai sun lura da wani lungu mai yashi. Sai suka yi shiri su kai jirgin kan yashi idan zai yiwu. 40 Sai suka yanke igiyoyi na dukan ƙarafa masu nauyin, suka bar su a ruwa. A daidai lokacin kuma suka ɓalle maɗaurin abin juya jirgin. Sa'an nan kuma suka ta da filafilan da suke gaban jirgin daidai yadda iska za ta tura shi gaba. Sai suka sa kai zuwa gefen teku. 41 Amma da muka isa wani wurin da ruwan yake haɗuwa, sai jirgin ya buga yashi, har kan jirgin ya shiga cikin yashin ya kāsa motsi. Sai jirgin kuma ya fara faffashewa ta baya saboda haukan rafkuman ruwa.

Hoton faffashewar jirgi (27.41)

42 Sai sojojin suka yi shiri su kakkashe 'yan kurkukun, don kada waninsu yă yi iyo yă gudu. 43 Amma da yake babban sojan Roma ya so ya ceci Bulus, sai ya hana su. Ya kuma ba da umarni dukan waɗanda suka iya ruwa su fara tsalle su shiga cikin ruwa su yi iyo zuwa gefen teku, 44 sauran kuwa su hau katakai, ko su hau tarkacen jirgin. Da haka duka suka kai gefen teku lafiya lau.

Bulus a Tsibirin Malta

28 [1] Bayan mun tsira sai muka ji, ashe, sunan tsibirin nan Malta
ne. [2] Mutanen garin kuwa sun yi mana alheri ƙwarai da
gaske. Sai suka karɓe mu duka, suka hura mana wuta domin ana
ruwa, ana kuma sanyi. [3] Bulus ya tattaro itace yana sawa a wutar,
sai wani maciji mai dafi ya fito don zafin wutar, ya cafke hannun
Bulus. [4] Da mutanen garin suka ga macijin yana lilo a hannun Bulus,
sai suka ce wa junansu, "Lallai mutumin nan mai kisankai ne, kun
ga ko da yake ya tsira daga teku, duk da haka alhaki yana binsa sai
ya mutu." [5] Bulus kuwa ya jijjiga hannunsa ya jefa macijin cikin
wuta, bai kuwa ji ciwo ba. [6] Suna tsammani zai kumbura ko yă fādi
nan take yă mutu, amma da suka daɗe ba su ga wani abu ya faru
da shi ba, sai suka sāke tunani suka ce shi wani allah ne.

7 Nan kusa kuwa akwai filaye, na shugaban tsibirin nan, mai
suna Fubiliyus. Shi ne ya karɓe mu, ya ba mu masauki mai kyau,
har kwana uku. [8] Baban Fubiliyus kuwa yana kwance yana fama da
zazzaɓi da atuni. Sai Bulus ya shiga wurinsa ya yi masa addu'a, ya
sa hannu a kansa, mutumin ya warke. [9] Da haka ya faru, sai dukan
sauran marasa lafiya a tsibirin suka riƙa zuwa ana warkar da su.
[10] Suka yi mana kyauta mai yawa. Da za mu tashi a jirgin ruwa
kuma, suka tattara mana duk abubuwan da muke bukata.

Bulus Ya Kai Birnin Roma

11 Bayan wata uku, muka tashi cikin jirgin Alekzandiriya
wanda ya ci damina a wannan tsibirin. An kuwa yi masa alamar
siffar tagwayen alloli.

12 Da muka zo Sirakus muka yi kwana uku a wurin. [13] Daga
nan kuma muka tafi, sai ga mu a Rigiyum. Bayan kwana ɗaya,
iska ta taso daga kudu, washegarin kuma muka kai Futiyoli. [14] A
nan muka sadu da waɗansu masu bi, suka roƙe mu mu yi kwana
bakwai tare da su. Da haka dai muka kai Roma. [15] Da masu bi
na Roma suka ji labarinmu, sai suka zo su marabce mu har a
kasuwar Affiyus, da kuma wurin nan da ake ce da shi Masauki
Uku. Da Bulus ya gan su kuwa ya yi godiya ga Allah, ya kuma
ƙara samun ƙarfin gwiwa.

16 Da muka shiga Roma aka yarda wa Bulus yă je yă zauna
a gidan haya tare da sojan da yake gadinsa.

Wa'azin Bulus a Roma

17 Bayan kwana uku, Bulus ya kira manyan Yahudawa. Da
suka taru sai ya ce musu, "Ku 'yan'uwa, ko da yake ban yi wa



Hoton jirgin ruwa tare da abin juya shi (28.11)

jama'armu wani laifi ba, ko laifi game da al'adun kakanninmu, duk da haka an kama ni a Urushalima aka ba da ni ga Romawa a ɗaure. **18** Su kuwa da suka bincike ni, suna so su sake ni, domin ba su same ni da wani laifin da ya isa a kashe ni ba. **19** Amma da Yahudawa suka ƙi yarda, sai ya zama mini dole in ɗaukaka ƙarata zuwa gaban Kaisar, ko da yake ba wai ina ƙarar jama'armu ba ne. **20** Shi ya sa na nemi in gan ku, in kuma tattauna da ku tun da yake dai saboda da shi wannan da Isra'ilawa suke begen zuwansa ne aka ɗaure ni da sarƙan nan."

21 Sai suka ce masa, "Mu dai ba mu sami wata wasiƙa daga Yahudiya game da kai ba, ba kuwa wani ɗan'uwanmu da ya zo nan ya kawo labarinka, ko yă faɗa wata magana marar kyau game da kai. **22** Amma muna so mu ji ra'ayinka daga bakinka, don abin da muka sani dai shi ne, sabuwar ɗarikan nan kowa yana muguwar magana a kanta."

23 Da suka sa ranar da za su haɗu, sai suka zo masaukinsa; sun kuwa zo da yawa sosai. Daga safe har zuwa yamma ya yi ta

28.19: A.M. 25.11

yi musu bayyani yana shaida musu a kan mulkin Allah, yana ƙoƙarin yă jawo su zuwa wurin Yesu ta hanyar Dokar Musa da littattafan annabawa. 24 Waɗansu suka yarda da abin da ya faɗa,
amma waɗansu ba su gaskata ba. 25 Saboda haka ba su yarda da
juna ba. Kafin su bar wurin sai Bulus ya yi musu magana ɗaya
ya ce, "Ashe kuwa, Ruhu Mai Tsarki ya faɗa gaskiya, da ya yi
wa kakanninku magana ta bakin annabi Ishaya cewa,

26 'Ka je wurin jama'an nan, ka ce,
ji kam, za ku riƙa ji,
amma ba za ku fahimta ba sam,
gani kam, za ku riƙa gani,
amma ba za ku gane ba sam.
27 Don zuciyar jama'an nan ta yi tauri,
sun toshe kunnuwansu,
sun rufe idanunsu,
don kada su gani da idanunsu,
su kuma ji da kunnuwansu,
su kuma gane da zuciyarsu,
har su juyo wurina in warkar da su.'

28 "To, sai ku sani fa, Allah ya aika da labarin ceto har zuwa
ga waɗanda ba Yahudawa ba. Su kuwa za su saurara."[r]

30 Bulus ya zauna a wannan gidan da yake haya har shekara
biyu, yana karɓar duk waɗanda suka zo wurinsa. 31 Da yake ba
a hana shi wa'azi ba, ya yi ta yin wa'azin mulkin Allah, yana
koyarwa game da Ubangiji Yesu Almasihu babu tsoro.

28.26-27: Ish 6.9-10

[r] **28.28** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya ta 29 haka: Da Bulus ya faɗa haka, sai Yahudawan suka tashi daga wurin suna gardama mai zafi a tsakaninsu.

WASIKAR BULUS ZUWA GA
ROMAWA

Gabatarwa

Manzo Bulus ne ya rubuta wannan wasika zuwa ga masu bi a birnin Roma a shekara ta AD 57, ko kuwa kusa da haka. Mai yiwuwa ya yi rubutun a birnin Korinti a lokacin tafiyarsa ta uku ta wa'azin bishara.

Bulus ya rubuta wasikan nan don yă gabatar da kansa ga jama'ar masu bi a Roma kafin yă zo, tun da yake bai taba ziyarci jama'ar masu bin da suke a can ba. Kwayar magana ta wasikan nan tana a 1.16-17. Wasikar ta ce, "Bishara ba abin kunya ba ce gare ni, domin ita ce ikon Allah da take kai kowane mutum wanda ya gaskata ga samun ceto . . . Gama ta wurinta ne ana bayyana adalcin nan wanda daga wurin Allah yake, kuma ana samun adalcin nan ta wurin bangaskiya daga farko har zuwa karshe." A cikin wannan wasika ne an bayyana dalla-dalla duk abin da an sani game da koyarwar Bishara.

Wasikar ta nuna cewa dukan mutanen duniya suna karkashin ikon zunubi, kuma duka suna bukatar samun zaman marasa laifi a gaban Allah (1.8—3.20). Sa'an nan kuma ta tabbatar cewa ta wurin bangaskiya ga Yesu Almasihu ne, mutum zai iya samun zaman marar laifi a gaban Allah ba ta wurin ayyukan da mutum ya yi da kansa ba (3.21—4.25). Wasikar kuma ta bayyana abubuwan da suka zama dole ne kowane mai bi yă kasance da su, da kuma yadda rayuwa bisa ga ikon Ruhu Mai Tsarki takan sa a yi nasara a kan halin mutuntaka (5.1—8.39). Wasikar kuma ta ci gaba da nuna yadda shirin da Allah ya yi saboda ceton mutane ya shafi kowa da kowa, wato, Yahudawa da wadanda ba Yahudawa ba (9.1—11.36). Daga baya an yi gargadi a kan yadda rayuwar mai bi ta shafi dangantaka a tsakanin 'yan'uwa, da kuma a tsakanin masu bi da shugabannin gwamnati (12.1—15.13).

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-17
Duk 'yan Adam masu zunubi ne 1.18—3.20
Hanyar samun ceto 3.21—4.25
Sabon rai cikin Almasihu 5.1—8.39
Shirin Allah saboda Isra'ila 9.1—11.36
Yadda mai bi ya kamata ya yi rayuwarsa 12.1—15.13
Maganar karshe da gaisuwa 15.14—16.27

Gaisuwa

1 [1] Daga Bulus, bawan Almasihu Yesu, wanda aka kira shi yă
zama manzo, aka kuma keɓe shi don shelar Labari Mai Daɗi
na Allah.

2 Labari Mai Daɗin nan ne Allah ya yi alkawarinsa tun dā ta
wurin annabawansa, kamar yadda yake a rubuce cikin Rubutattun
Maganar Allah masu tsarki. [3] Wannan bisharar kuwa game da
Ɗansa Yesu Almasihu Ubangijinmu take. Bisa ga mutuntaka shi
daga zuriyar Dawuda ne, [4] amma bisa ga tsarkinsa na Allahntaka[a]
an tabbatar da shi Ɗan Allah. An kuwa tabbatar da shi da iko
sosai ta wurin tashinsa daga matattu. [5] Ta wurin Almasihu Yesu
da kuma don sunansa ne na sami alheri da kiran zaman manzo
domin in kira mutane daga cikin al'ummai duka don su gaskata
su kuma yi biyayya. [6] Wannan kuwa ya shafe ku, ku waɗanda
Allah ya kira ku ku zama na Yesu Almasihu.

7 Ga dukanku da kuke a Roma, waɗanda Allah yake ƙauna,
ya kuma kira ku ku zama tsarkaka:

Alheri da salama daga Allah Ubanmu da kuma Ubangiji Yesu
Almasihu su kasance tare da ku.

Addu'ar Godiya

8 Da farko dai ina yi wa Allahna godiya ta wurin Yesu
Almasihu saboda ku duka, domin ana ba da labarin bangaskiyarku
ko'ina a cikin duniya. [9] Don Allah wanda nake yi masa hidima
da dukan zuciyata ta wurin shelar Labari Mai Daɗi na Ɗansa, shi
ne shaidata cewa ina tunawa da ku ba fasawa, [10] a duk lokacin
da nake addu'a. Ina roƙon Allah cewa, idan nufinsa ne, ko ta yaya
in sami dama yanzu in zo wurinku. [11] Gama ina marmari in gan
ku don in ba ku wata kyauta ruhu wadda za ta ƙarfafa ku.
[12] Nufina shi ne, ni da ku mu ƙarfafa juna, wato, in ƙarfafa ku da
bangaskiyata, ku kuma ku ƙarfafa ni da taku.

13 'Yan'uwa, ina so ku sani cewa sau da yawa na yi shiri in
zo wurinku, amma har yanzu an hana ni yin haka. Dalilin zuwana
kuwa shi ne don in yi girbi a cikinku kamar yadda na yi a cikin
sauran waɗanda ba Yahudawa ba. [14] Akwai hakkin kowa a kaina,
na mutanen birni da na mutanen ƙauye, na masu ilimi da na
marasa ilimi. [15] Shi ya sa na yi niyya sosai in shaida muku Labari
Mai Daɗi, ku ma da kuke a Roma.

1.13: A.M. 19.21

[a] **1.4 tsarkinsa na Allahntaka:** Wani juyi na waɗannan kalmomin shi ne "ruhu na tsarki".

Ikon Bishara

16 Bishara ba abin kunya ba ce a gare ni, domin ita ce ikon
Allah da take kai kowane mutum wanda ya gaskata ga samun
ceto, da farko ga Yahudawa, sa'an nan ga waɗanda ba Yahudawa
ba. 17 Gama ta wurinta ne ana bayyana adalcin [b] nan wanda daga
wurin Allah yake, kuma ana samun adalcin nan ta wurin
bangaskiya daga farko har zuwa ƙarshe. Kamar yadda yake a
rubuce cewa, "Mai adalci zai rayu bisa ga bangaskiya ne."

Laifin 'Yan Adam Duka

18 Gama ana bayyana fushin Allah daga sama a kan dukan
marasa hali irin na Allah da aikin mugunta na mutane waɗanda
suke danne gaskiya ta aikin muguntarsu. 19 Gama abin da ana iya
sani game da Allah yana nan a fili a gare su, domin Allah ne ya
bayyana musu shi. 20 Halin Allahntaka na Allah da kuma ikonsa
na har abada ba abubuwan da ake iya gani da ido ba ne. Amma
tun halittar duniya an bayyana waɗannan abubuwa a fili, ana
kuma iya gane su bisa ga abubuwan da aka halitta. Saboda haka
mutane ba su da wata hujja! 21 Ko da yake sun san Allah, duk da
haka ba su ɗaukaka shi a matsayinsa na Allah ba, ba su kuma
nuna masa godiya ba. A maimakon haka sai tunaninsu ya zama
banza, zukatansu marar ganewa kuwa suka duhunta. 22 Ko da yake
sun ce wai suna da wayo, amma su wawaye ne. 23 A maimakon
su yi wa Allah marar mutuwa sujada, sai suna yi sujada ga gunkin
da aka yi da kamannin mutum mai mutuwa, da kuma gumaka
masu kamannin tsuntsaye, da dabbobi, da halittu masu rarrafe.

24 Saboda haka Allah ya bashe su ga aikata mugayen
sha'awace-sha'awacen zukatansu, da jikinsu kuma suna yin abin
kunya da juna. 25 Sun mai da gaskiyar Allah ta zama ƙarya. Suna
bauta wa abubuwan da aka halitta, har suna yi musu hidima a
maimakon su yi wa Mahalicci da kansa, shi wanda ya isa a yabe
shi har abada. Amin.

26 Saboda haka Allah ya bashe su ga sha'awace-sha'awacen
masu ban kunya. Matansu kuwa suka canza daga haɗuwar mace
da miji wadda ita ce daidai bisa ga halitta zuwa irin haɗuwar da
ba daidai ba. 27 Haka kuma da sha'awar junansu ta sha kansu, sai
maza suka bar haɗuwa da mata wadda ita ce daidai bisa ga halitta.

1.16: Mar 8.38 **1.17:** Hab 2.4 **1.21:** Afi 4.17-18 **1.23:** M. Sh 4.16-18

[b] **1.17 adalcin:** Wannan kalmar a nan tana nufin yadda matsayinmu yake a gaban Allah, wato, irin rayuwar da ya zama abin yarda da abin karɓa ga Allah.

Maza da maza suna aikata abin kunya, ta haka suka kuma jawo
wa kansu hukuncin da ya yi daidai da mugayen ayyukansu.
28 Da yake sun ƙi su kasance da sanin Allah sai Allah ya
bashe su ga tunanin banza da wofi don su aikata abin da bai
kamata a yi ba. 29 Suna cike da kowane rashin adalci, da mugunta,
da kwaɗayi, da mugun hali. Suna cike da kishi, da kisankai, da
faɗa, da ruɗu, da baƙar zuciya. Su masu gulma ne, 30 masu cin
mutunci, masu gāba da Allah, masu zagi, masu ɗaga kai, masu
girmama kansu, masu ƙulla mugunta, masu rashin biyayya ga
iyaye. 31 Su marasa hankali ne, marasa cika alkawari, marasa
ƙauna, da marasa tausayi. 32 Sun san dokar Allah cewa duk masu
aikata halayen nan sun cancanci mutuwa, amma ba wai suna
aikata abubuwan nan kaɗai ba, har suna goyon bayan waɗanda
su ma suna aikata haka.

Hukuncin Allah Daidai Ne

2 1 Saboda haka kai mai ganin laifin wani, ba ka da wata hujja,
ko kai wane ne. Gama a sa'ad da kake ganin laifin wani
kana hukunta kanka ne, domin laifin da kake ganin wani da shi,
shi ne kai ma kake aikatawa. 2 Mun san cewa hukuncin Allah
daidai ne a kan waɗanda suke yin abubuwan nan. 3 Kai mutum!
Ga shi kuwa kai da kanka kana aikata laifin nan da kake ganin
wani da shi! Kana tsammani za ka kuɓuce wa hukuncin Allah?
4 Ko kuwa kana rena yawan alherin Allah, da haƙurinsa, da rashin
saurin fushin da yake yi gare ka? Ashe, ba ka sani cewa alherin
Allah yana jawo ka ga tuba ba? 5 Amma ta dalilin taurin kan da
kake yi da taurin zuciyar da kake da shi, kana tara wa kanka
hukunci wanda yake jiranka a Ranar fushin Allah, a lokacin da
za a bayyana hukuncin nan da yake bisa ga adalcin Allah. 6 Allah
zai saka wa kowa bisa ga ayyukansa. 7 Akwai waɗanda suke
neman ɗaukaka da daraja da rai marar ƙarewa. Waɗannan ne sun
aikata alheri cikin haƙuri, su ne kuma Allah zai ba su ladan rai
na har abada. 8 Amma masu sonkai, waɗanda ba sa yin biyayya
da gaskiya sai dai mugunta, za a saka musu da fushi da kuma
haushi. 9 Tsanani da wahala su ne suke jiran kowane mutum mai
aikata mugunta; da farko ga Yahudawa, sa'an nan ga waɗanda
ba Yahudawa ba. 10 Amma duk mai aikata nagarta zai sami
ɗaukaka da girma da salama; da farko ga Yahudawa, sa'an nan
ga waɗanda ba Yahudawa ba. 11 Gama Allah ba mai nuna
bambanci ba ne.

2.1: Mat 7.1; Luk 6.37 **2.6**: Zab 62.13; K. Mag 24.12 **2.11**: M. Sh 10.17

12 Duk masu yin zunubi ba tare da sanin Dokar Musa ba, za
su halaka ba tare da Dokar ba, amma duk waɗanda suka yi zunubi
cikin sanin Dokar, za a hukunta su bisa ga Dokar. 13 Gama ba jin
Dokar kawai shi ne yakan sa mutane su zama da adalci a gaban
Allah ba, amma yin biyayya da Dokar shi ne yakan sa a iya ce
da su masu adalci. 14 Waɗanda ba Yahudawa ba ba su da Doka.
Duk da haka wani lokaci suna yin abin da Dokar ta umarta, yadda
zukatansu sun ba su. Wannan ya nuna cewa su da suke marasa
Dokar sun zama dokar ga kansu ke nan. 15 Ayyukansu sun nuna
cewa abin da Dokar ta ce a yi yana nan a rubuce cikin zukatansu.
A cikin tunanin zukatansu kuwa akwai shaida game da wannan,
don tunaninsu yakan same su da laifi a wani lokaci, a wani lokaci
kuma ba ya samunsu da laifi. 16 Saboda haka, kamar yadda Labari
Mai Daɗin nan da nake wa'azinsa yake faɗa, haka zai zama a
Ranan da Allah ta wurin Almasihu Yesu zai shari'anta dukan
abubuwan da suke a ɓoye a tunanin mutane.

Yahudawa da Dokar Musa

17 To, kai mai ce da kanka Bayahude fa? Kana dogara ga
Dokar Musa, kana kuma taƙama da dangantakarka da Allah,
18 kana cewa wai ka san nufin Allah, kuma kana da ganewa bisa
ga Dokar yadda za ka zaɓi abin da yake daidai. 19 Kana da tabbaci
cewa kai jagora ne ga makafi, haske ga waɗanda suke cikin duhu,
20 mai koyar da wawaye, da kuma malami ga masu tunanin yara.
Ka kuma tabbata cewa a cikin Dokar ne kana da cikakken sani
da ainihin gaskiya. 21 To, kai mai koya wa waɗansu, ka koya wa
kanka mana! Kai mai yin wa'azi cewa kada a yi sata, kai ba ka
sata? 22 Kai mai cewa kada a yi zina, ba ka yin zina? Kai mai
ƙyamar gumaka, ba ka sata daga ɗakin gumaka? 23 Kai mai
taƙama da Dokar Musa, ba ka ɓata sunan Allah ta wajen karya
dokarsa? 24 Kamar yadda yake a rubuce, "Saboda ku Yahudawa
ake mugun magana game da sunan Allah a cikin waɗanda ba
Yahudawa ba."

25 Idan kana biyayya da Dokar, kaciyarka[6] tana da amfani ke
nan. Amma idan rashin biyayya kake yi, zai zama kamar ba ka
ma yi kaciya ba. 26 Ashe idan waɗanda ba masu kaciya ba suna
aikata abin da Dokar ta ce a yi, Allah ba zai ɗauke su kamar
masu kaciya ke nan ba? 27 Waɗanda su ba masu kaciya ba ne a
jiki amma suna aikata abin da Dokar ta ce a yi, za su yi maka

2.24: Ish 52.5
[6] 2.25 Dubi ma'anar waɗansu kalmomi.

hukunci, kai da kake da Dokar a rubuce, mai kaciya kuma, amma
kana karya Dokar Allah. 28 Gama Bayahude na gaske ba mutum
ne wanda yake Bayahude bisa ga jiki kurum ba, kuma kaciya ta
ainihi ba bisa ga alamar jiki take ko ta yankan fata ba. 29 A
maimakon haka, Bayahude na gaske shi ne wanda yake Bayahude
a zuciya, kuma kaciya ta gaske ita ce kaciya ta zuciya, wato, abin
da Ruhu ne ya yi, ba ta wurin Dokar da aka rubuta ba. Irin wannan
mutum kuwa Allah ne yakan yi masa yabo, ba ɗan Adam ba.

3 1 To, ina amfani na cewa kai Bayahude ne? Ina ribar kaciya?
2 Akwai kam, ta kowace hanya! Da farko, su Yahudawa ne
Allah da kansa ya ba su amanar maganan nan da suke na Allah.
3 Amma idan waɗansunsu sun nuna rashin bangaskiya fa? Rashin
amincinsu zai sa amincin Allah yă zama banza ke nan? 4 Ina! Ko
kaɗan! Dole ne Allah yă zama mai aminci, ko da yake kowane
mutum maƙaryaci ne. Kamar yadda yake a rubuce cewa:

"Dole ne ka kasance mai gaskiya
ka kuma sha kan kowa idan ana yin bincike a kanka."

5 To, idan rashin adalcinmu ya zama hanyar tabbatar da
adalcin Allah fa, me za mu ce ke nan? Za mu ce Allah marar
adalci ne in ya hukunta mu? (Ina dai yin magana yadda ɗan Adam
zai yi ne.) 6 Ina! Ko kaɗan! In haka ne, ta yaya Allah zai yi
shari'ar duniya?

7 Idan rashin gaskiyata ya sa gaskiyar Allah ta fita a fili sosai,
ya kuma zama abin ɗaukaka Allah, to, don me har yanzu za a
hukunta ni a kan cewa ni mai zunubi ne? 8 In haka ne, ba sai mu
ci gaba da yin mugunta don yă zama hanyar samun nagarta ba?
Waɗansu mutane kuwa masu baƙar magana game da mu suna
cewa wai haka muke faɗa. Za a hukunta waɗannan kamar yadda
ya yi daidai a yi musu.

Babu Mai Adalci Ko Daya

9 To, yaya ke nan? Ko mu Yahudawa mun fi sauran mutane
ne? Ina! Ko kaɗan! Mun riga mun nuna cewa da Yahudawa da
waɗanda ba Yahudawa ba duka suna da laifi, kuma duka suna
ƙarƙashin ikon zunubi. 10 Kamar yadda yake a rubuce cewa:

"Babu wani da yake mai adalci,
babu, ko ɗaya;
11 Babu wani da yake mai ganewa,
ko wani mai neman Allah.
12 Duk sun juya wa Allah baya;

2.29: M. Sh 30.6 **3.4**: Zab 51.6

sun zama marasa amfani gaba ɗaya;
Babu wani da yake aikata nagarta,
babu, ko ɗaya.
13 Bakinsu kamar kabarin da yake a buɗe ne;
Suna amfani da harshensu don ruɗu,
Maganganunsu kamar dafin mugun maciji ne.
14 Bakinsu yana cike da baƙar magana da zage-zage.
15 Sukan yi garajen zub da jini,
16 Ko'ina suka bi sai halaka da baƙin ciki.
17 Ba su kuwa san hanyar salama ba.
18 Babu tsoron Allah a gare su ko kaɗan."

19 Mun dai san cewa duk abin da Dokar take faɗa, tana faɗa wa waɗanda suke ƙarƙashinta ne. Wannan ya kasance haka don a hana duk masu neman hujja, a kuma sa dukan duniya a ƙarƙashin hukuncin Allah. 20 Gama ba wanda zai sami zaman marar laifi a gaban Allah ta hanyar kiyaye abin da Dokar ta ce a yi. Abin da Dokar take yi shi ne ta nuna wa mutum zunubinsa.

Adalci ta Wurin Bangaskiya

21 Amma yanzu kam an bayyana wata hanyar samun adalcin Allah. Wannan adalci kuwa ba ta doka yake samuwa ba, ko da yake Dokar Musa da littattafan annabawa sun ba da shaida game da shi. 22 Adalcin nan wanda daga wurin Allah yake, yana samuwa ne ta wurin bangaskiya cikin Yesu Almasihu ga dukan masu ba da gaskiya. Ba kuwa wani bambanci, 23 domin kowa ya yi zunubi, kuma kowa ya kāsa kai ga darajar Allah. 24 Amma bisa ga alherin da Allah ya yi wa kowa a kyauta, kowa ya sami zaman marar laifi a gaban Allah ta wurin fansar da Almasihu Yesu ya yi. 25 Allah ya aiki Yesu yă zama hadaya a madadinmu don ta wurin jininsa a gafarta wa mutane zunubansu ta wurin bangaskiyarsu. Allah ya yi wannan domin yă nuna adalcinsa, don a cikin haƙurinsa ya ƙyale zunuban da aka yi a dā. 26 Ta haka Allah ya nuna a wannan lokaci cewa shi da kansa mai adalci ne, kuma yana sa duk mai ba da gaskiya ga Yesu yă sami zaman marar laifi a gaban Allah.

27 To, a kan mene ne za mu yi taƙama? Ai, ba wani abu! Ta wane dalili aka kawar da taƙama? Ta hanyar kiyaye Dokar? A'a, sai dai ta bangaskiya. 28 Gama mun ga cewa ta wurin bangaskiya ne akan sami zaman marar laifi a gaban Allah, ba ta wurin bin

3.10-12: Zab 14.1-3; 53.1-3 **3.13:** Zab 5.9; 140.3 **3.14:** Zab 10.7
3.15-17: Ish 59.7-8 **3.18:** Zab 36.1 **3.20:** Zab 143.2; Gal 2.16 **3.22:** Gal 2.16

umarnin Doka ba. 29 Ko kuwa Allah na Yahudawa ne, su kaɗai?
Ashe, ba na mutanen da ba Yahudawa ba ne kuma? Kwarai kuwa,
shi ma na waɗanda ba Yahudawa ba ne kuma, 30 don Allah ɗaya
ne, zai sa masu kaciya su sami zaman marasa laifi a gare shi ta
wurin bangaskiya, haka ma marasa kaciya za su sami zaman
marasa laifi ta wurin wannan bangaskiya. 31 Shin, mun kawar da
Dokar ke nan bisa ga wannan bangaskiyar? Ko kaɗan! A
maimakon haka, tabbatar da ita ne muke yi.

Misalin Ibrahim

4 1 To, me za mu ce game da Ibrahim, kakan kakanninmu bisa
ga jiki? Mene ne ya fahimci game da zancen bangaskiya?
2 Idan Ibrahim ya sami zaman marar laifi a gaban Allah ta
ayyukansa ne yana da abin da zai yi taƙama da shi ke nan, amma
fa ba a gaban Allah ba. 3 Rubutaccen Maganar Allah ya ce,
"Ibrahim ya ba da gaskiya ga Allah, saboda haka aka ce da shi
mai adalci." 4 Mutumin da yake yin aikin lada, albashinsa ba
kyauta ba ne, ladan aikinsa ne. 5 To, mutumin da bai dogara ga
ayyukansa ba amma ya dogara ga Allah wanda shi ne yake sa
masu laifi su sami zaman marasa laifi a gare shi, za a ɗauki
bangaskiyar mutumin nan kamar adalcinsa ke nan. 6 Wannan shi
ne abin da Dawuda yake nufi da ya yi magana game da albarkar
da aka yi wa mutumin da Allah ya ce da shi mai adalci, ba ta
dalilin ayyukan da mutumin ya yi ba, 7 cewa:

"Masu albarka ne waɗanda aka gafarta musu laifofinsu,
waɗanda kuma aka wanke zunubansu.
8 Mai albarka ne wanda ko kaɗan Ubangiji ba zai lissafta
zunubinsa a kansa ba."

9 Wannan albarkar ta shafi masu kaciya ne kawai, ko kuwa
har da marasa kaciya? Ai, abin da muke faɗa shi ne, "Ibrahim
ya ba da gaskiya ga Allah, saboda haka aka ce da shi mai
adalci." 10 To, a wane lokaci ne aka ce da shi mai adalci? Bayan
an yi masa kaciya ko tun ba a yi masa ba? Ai, tun ba a yi masa
kaciya ba ne. 11 Amma da ya karɓi alamar kaciya, wannan ta
zama alamar shaida mai ƙarfi game da adalcin da yake da shi
bisa ga bangaskiyarsa tun lokacin da yake marar kaciya. Saboda
haka Ibrahim ya zama uban masu ba da gaskiya ga Allah,
waɗanda aka ɗauke su masu adalci ne, ko da yake ba su da
kaciya. 12 Haka ma Ibrahim ya zama uba ga masu kaciya

3.30: M. Sh 6.4; Gal 3.20 **4.3:** Far 15.6; Gal 3.6 **4.7-8:** Zab 32.1-2
4.11: Far 17.10

waɗanda ba kaciya kaɗai suke da ita ba, amma har ma suna bin misalin irin bangaskiyar da Ibrahim yake da ita tun ba a yi masa kaciya ba.

Alkawarin Allah da Bangaskiyar Mutum

13 Alkawarin nan da aka yi wa Ibrahim da zuriyarsa cewa zai ci gādon duniya, ai, ba ta wurin Doka aka yi masa ba, sai dai ta adalcin nan da ake samu ta wurin bangaskiya. 14 Gama idan masu bin Dokar su ne waɗanda za su ci gādon duniya, ai, bangaskiyar mutum ta zama banza, kuma alkawarin Allah ya zama wofi ke nan. 15 Dokar takan jawo fushin Allah ne, don inda babu doka, ba yadda za a yi rashin biyayya.

16 Saboda haka, a kan bangaskiya ne alkawarin nan ya dogara. Wannan kuwa don yă zama bisa ga alherin Allah, a kuma tabbatar da shi ga dukan zuriyar Ibrahim, wato, ba ga waɗanda suke ƙarƙashin Dokar kaɗai ba, amma har ga waɗanda suke ba da gaskiya yadda Ibrahim ya yi. Ibrahim kuwa shi ne ubanmu duka. 17 Kamar yadda yake a rubuce cewa: "Na sa ka ka zama uban al'ummai masu yawa." Wato, an tabbatar da alkawarin nan a gaban Allah wanda shi ne Ibrahim ya ba da gaskiya gare shi, wanda kuma shi ne mai ba da rai ga matattu. Shi ne kuma mai ikon kiran abubuwan da ba su kasance ba su kasance. 18 Ko da yake sa zuciyar Ibrahim ta zama kamar a banza ne, duk da haka ya ci gaba da sa zuciya, yana ba da gaskiya har ya zama "Uban al'ummai masu yawa." Wannan kuwa bisa ga yadda aka faɗa masa ne, cewa, "Zuriyarka za su zama da yawa." 19 A lokacin kuwa Ibrahim yana da shekara wajen ɗari ne, amma bai yi sanyi cikin bangaskiyarsa ba, ko da yake yana ganin yadda ƙarfin jikinsa ya ƙare don tsufa, da kuma yadda Saratu ta wuce lokacin da za ta iya haihuwa. 20 Bai yi shakkar alkawarin Allah ta nuna rashin bangaskiya ba, amma ya ƙara ƙarfi cikin bangaskiyarsa, yana ɗaukaka Allah. 21 Ya kuma kasance da cikakken tabbaci cewa Allah yana iya cika alkawarinsa. 22 Shi ya sa Ibrahim, ta wurin bangaskiyarsa "aka ce da shi mai adalci." 23 Wannan magana mai cewa, "aka ce da shi mai adalci," ba saboda shi kaɗai ne aka rubuta ba. 24 Amma an rubuta wannan magana saboda mu mu ma, mu da Allah zai mai da mu masu adalci, wato, mu da muka ba da gaskiya ga wanda ya ta da Yesu Ubangijinmu daga matattu. 25 Saboda zunubanmu ne aka bashe Yesu ga mutuwa,

4.13: Far 17.4-6; 22.17-18; Gal 3.29 **4.14:** Gal 3.18 **4.16:** Gal 3.7 **4.17:** Far 17.5 **4.18:** Far 15.5 **4.19:** Far 17.17

kuma an ta da shi da rai domin mu sami zaman marasa laifi a gaban Allah.

Amfanin Zaman Marar Laifi a gaban Allah

5 [1] Saboda haka tun da yake mun sami zaman marasa laifi a gaban Allah ta wurin bangaskiya, muna da[c] salama da Allah ke nan ta wurin Ubangijinmu Yesu Almasihu. [2] Ta wurinsa ne muka sami shiga alherin nan da muke zama a ciki ta wurin bangaskiyarmu. Muna kuma yin farin ciki[d] saboda mun sa zuciya cewa za mu zama masu tarayya cikin ɗaukakar Allah. [3] Ba haka kaɗai ba, har muna farin ciki[d] cikin wahalolinmu, don mun san cewa wahala takan jawo jimrewa, [4] jimrewa takan jawo halin kirki, halin kirki kuma yakan jawo sa zuciya. [5] Sa zuciyan nan ba za ta zama abin banza ba ko kaɗan, don Allah ya zuba ƙaunarsa cikin zukatanmu ta wurin Ruhu Mai Tsarkin da Allah ya ba mu.

6 Gama a daidai lokaci, a sa'ad da ba mu iya taimakon kanmu ba, Almasihu ya mutu saboda mu, mu marasa bin Allah. [7] Da kyar ne wani yă mutu saboda mutum mai adalci. Amma watakila wani yana iya yin ƙarfin hali yă mutu saboda mutum mai halin kirki. [8] Amma Allah ya nuna mana yawan ƙaunarsa, don tun muna masu zunubi, Almasihu ya mutu saboda mu. [9] To, tun da yake mun sami zaman marasa laifi a gaban Allah ta wurin jinin Almasihu, balle fa yanzu, ai, za a cece mu daga fushin Allah ta wurin Almasihu. [10] To, da yake lokacin da muke masu gāba da Allah ne aka shirya tsakaninmu da Allah ta mutuwar Ɗansa, balle fa yanzu da aka mayar da mu abokan Allah, za a cece mu ta rayuwar Ɗan ke nan. [11] Fiye da haka, har muna farin ciki saboda abin da Allah ya yi ta wurin Ubangijinmu Yesu Almasihu, wanda ta wurinsa ne muka sami gyarar tsakaninmu da Allah.

Adamu da Almasihu

12 Zunubi ya shigo cikin duniya ta wurin mutum guda, zunubin nan kuwa shi ya jawo mutuwa. Haka kuma mutuwa ta bi ta shafi kowa, don kowa ya yi zunubi. [13] Kafin a ba da Dokar,

---

4.25: Ish 53.4-5 **5.12**: Far 3.6

[c] **5.1 muna da**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Bari mu sami" ne a nan.

[d] **5.2 Muna kuma yin farin ciki**: Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne, "Bari mu yi farin ciki."

[d] **5.3 Muna farin ciki**: Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne, "Bari mu yi farin ciki."

zunubi yana a duniya. Amma ba a yin lissafin zunubi inda babu doka. 14 Duk da haka mutuwa ta yi mulki a kan mutane duka daga zamanin Adamu zuwa zamanin Musa, har ma ta yi iko a kan waɗanda zunubansu ba na karya doka ba ne kamar yadda na Adamu ya kasance.

Adamu kuwa kwatancin wani ne wanda zai zo da kyautar Allah. 15 Amma kyautar da Allah ya bayar ta wurin mai zuwan nan dabam take ƙwarai da laifin Adamu. Ga shi zunubin mutum gudan nan ya jawo wa mutane da yawa mutuwa. Amma alherin Allah ya yi yawa, har kyautarsa da ya yi ta wurin alherin mutum gudan nan, wato, Yesu Almasihu, ta jawo babbar albarka ga mutane da yawa. 16 Kwarai kuwa, kyautar Allah dabam take da zunubin mutum gudan nan. Gama hukuncin da ya bi bayan laifi gudan nan shi ne hukuncin mutuwa, amma kyautar da Allah ya bayar ita ce ta jawo mana hukuncin marar laifi a gabansa ko da yake mun yi zunubi da yawa. 17 Ta wurin laifin mutum guda, wato, Adamu, mutuwa ta yi mulki a kan kowa, amma wannan yin mulki ba kome ba ne idan an gwada shi da wanda mutum guda, wato, Yesu Almasihu ya kawo. Ta wurinsa ne mun karɓi alherin Allah mai yawa da kyautarsa ta zaman adalci a gabansa. Ta wurinsa za mu yi mulki cikin rayuwa.

18 Saboda haka, yadda laifin mutum guda ya jawo hukuncin mutuwa a kan kowa, haka kuma aikatawar adalci da mutum guda ya yi ya kawo albarka ga kowa, wato, samun zaman marar laifi a gaban Allah da kuma sabon rai. 19 Kamar yadda mutane da yawa suka zama masu zunubi ta wurin rashin biyayyar mutum guda, haka kuma da yawa za su zama masu adalci ta wurin biyayyar mutum guda.

20 Dalilin da aka shigo da Dokar shi ne don laifi yă fito a fili. Amma sa'ad da zunubi ya ƙaru, sai alherin Allah yă fi ƙaruwa. 21 Wato, kamar yadda zunubi ya yi mulkinsa ta wurin mutuwa, haka kuma alherin Allah yake mulkinsa yanzu ta wurin adalci, yana kai mu ga rai na har abada ta wurin Yesu Almasihu Ubangijinmu.

Mutuwa ga Zunubi, Rayuwa ga Almasihu

6 1 Me za mu ce ke nan? Za mu ci gaba da rayuwa cikin zunubi don alherin Allah ya ƙaru? 2 Ina! Ko kaɗan! Ai, mun riga mun mutu ga zunubi. Yaya kuma za mu ci gaba da rayuwa a cikinsa? 3 Ashe, ba ku sani ba dukanmu da aka yi mana baftisma zuwa cikin Almasihu Yesu, zuwa cikin mutuwarsa ne aka yi mana

baftismar? 4 Wato, ta wurin baftismarmu an binne mu tare da shi,
mun kuma zama ɗaya da shi cikin mutuwarsa, domin yadda aka
ta da Almasihu ta wurin ikon nan mai ɗaukaka na Uba, haka mu
ma mu yi zaman sabuwar rayuwa.

5 Gama da yake mun zama ɗaya da shi cikin irin mutuwarsa,
ba shakka za mu zama ɗaya da shi cikin tashinsa daga matattu.
6 Mun kuwa san cewa an riga an gicciye halayenmu na dā tare
da shi, domin a kawar da ikon zunubin nan da yake cikin jikinmu.
An yi haka don kada mu ƙara zama bayin zunubi. 7 Gama idan
mutum ya mutu, ya sami 'yanci daga ikon zunubi ke nan. 8 Da
yake mun riga mun mutu tare da Almasihu, mun ba da gaskiya
za mu rayu tare da shi kuma. 9 Gama mun san cewa an ta da
Almasihu daga matattu, kuma ba zai sāke mutuwa ba, wato,
mutuwa ba ta da sauran iko a kansa. 10 Mutuwan nan da ya yi,
ya mutu ne sau ɗaya tak ba ƙari don yă karye ikon zunubi, amma
rayuwar da yake yi, yana yi ne cikin zumunci da Allah. 11 Haka
kuma ku ɗauki kanku kamar matattu ne ga ikon zunubi, amma
rayayyu ne a cikin zumunci da Allah ta wurin Almasihu Yesu.

12 Saboda haka kada ku yarda zunubi ya yi mulki a cikin jikin
nan naku mai mutuwa, har yă sa ku ku bi mugun sha'awarsa ta
halin mutuntaka. 13 Kada kuma ku miƙa gaɓoɓinku ga zunubi har
su zama kayan yin aikin mugunta. Sai dai ku miƙa kanku ga Allah
yadda ya dace da waɗanda aka cire su daga hannun mutuwa zuwa
samun rai, ku kuma miƙa kanku ga Allah don su zama kayan yin
aikin adalci. 14 Kada zunubi yă yi mulki a kanku, tun da yake ba
doka ce take iko a kanku ba, sai dai alherin Allah.

Bayin Adalci

15 Yaya ke nan? Wato, sai mu yi zunubi domin doka ba ta
iko a kanmu, sai dai alherin Allah? Ina! Ko kaɗan! 16 Ba ku sani
ba idan kun miƙa kanku don ku zama masu biyayya ga wani,
wato, kun zama bayi ke nan a hannun shi wanda kuke yi masa
biyayya? Kuna iya zama bayin zunubi, wanda yake kai ga
mutuwa, ko kuma masu biyayya ga Allah, wanda yake kai ga
adalci. 17 Amma godiya ta tabbata ga Allah, don ko da yake a dā
ku bayin zunubi ne, amma yanzu kam kuna biyayya da dukan
zuciyarku ga irin koyarwan nan da aka yi muku. 18 An 'yantar da
ku daga zunubi, kun kuma zama bayi ga adalci. 19 Ina kuwa yi
muku magana kamar yadda ɗan Adam yake magana ne, wannan

6.4: Kol 2.12

kuma saboda kāsawarku ta mutuntaka ne. A dā kun saba da miƙa gaɓoɓin jikinku ga bautar abubuwan ƙazanta, da kuma ga mugunta wadda take ta ƙaruwa kawai. Amma yanzu sai ku miƙa kanku ga bautar adalci, wato, don aikata tsarkakan ayyuka.

20 A lokacin da kuke bayin zunubi, ba ruwanku da aikin adalci. 21 Wane amfani kuka samu daga abubuwan nan da yanzu suka zama muku abin kunya? Ai, sakamakon waɗannan abubuwa mutuwa ne! 22 Amma yanzu an 'yantar da ku daga zunubi, kun kuma zama bayin Allah. Amfanin da kuke samu daga wannan shi ne tsarkakewar rayuwarku, wadda kuma za ta haifa muku rai na har abada. 23 Gama ladan zunubi shi ne mutuwa, amma baiwar Allah ita ce rai na har abada ta wurin Almasihu Yesu Ubangijinmu.

Aure Misali Ne na Dangantakarmu da Almasihu

7 1 To, 'yan'uwana, tun da yake dukanku masu sanin doka ne, za ku gane abin da zan faɗa. Doka takan yi iko a kan mutum sa'ad da mutumin yana da rai ne kawai. 2 Misali, mace mai aure, doka ta ɗaure ta ga mijinta sa'ad da mijinta yana da rai. Amma idan mijinta ya mutu ta sami 'yanci ke nan daga dokan nan da ta ɗaure ta da mijin. 3 Saboda haka idan ta auri wani dabam sa'ad da mijinta yana da rai, za a ce da ita mai zina. Amma idan mijinta ya mutu tana da 'yanci ke nan bisa ga dokar ɗaurin aure. Idan kuwa ta sāke auri wani, ita ba mai zina ba ce.

4 'Yan'uwana, wannan misali ne game da ku. Mutuwar Almasihu a kan gicciye ta sa kuka zama matattu game da Dokar. Ta haka yanzu kun zama na wani, wato, shi da aka ta da shi daga matattu, don ku ba da amfani ga Allah a rayuwarku. 5 Gama yayin da muke zama bisa ga halin mutuntaka, Dokar ta yi ta zuga muguwar sha'awarmu. Sha'awan nan tamu kuma ta yi ta aiki a cikin jikinmu, kuma dukan ayyukanmu suna haifar mana mutuwa. 6 Amma yanzu kam mun sami 'yanci daga Dokar don mun mutu ga abin da ya ɗaure mu. Saboda haka yanzu muna bauta wa Allah cikin sabuwar rayuwa ta Ruhunsa. Tsohuwar bautar da muka yi wa rubutattun dokoki ta wuce.

Dokar Musa da Ikon Zunubi

7 To, me za mu ce ke nan? Dokar da kanta zunubi ce? A'a, ko kaɗan! Ai, ba yadda zan iya san abin da yake zunubi idan ba ta wurin Dokar ba. Da Dokar ba ta ce, "Kada ka yi kwaɗayi abin wani ba," ai, da ban san abin da ake ce da shi kwaɗayi ba. 8 Amma

saboda umarnin nan sai zunubi ya sami dama yă zuga kowane
irin kwaɗayi a cikina. Don idan ba tare da doka ba, zunubi kamar
gawa ne. 9 A dā kam a raye nake, ba da sanin doka ba, amma da
na san umarnin, sai zunubi ya tashi da rai, ni kuwa na mutu.
10 Umarnin nan da aka nufe shi yă kawo rai, ya kuwa jawo mini
mutuwa. 11 Zunubi ya sami zarafinsa, kuma ta wurin umarnin ya
ruɗe ni, ya kuma kashe ni.

12 Saboda haka Dokar da kanta mai tsarki ce, umarnin kuwa
mai tsarki ne, daidai ne, nagari ne kuma. 13 Wato, ko za a ce
Dokan nan da take mai nagarta ta jawo mini mutuwa ke nan?
Ina! Ko kaɗan! Zunubi ne ya jawo mini wannan. Ta wurin Dokan
nan da take mai nagarta zunubi ya jawo mini mutuwa, don a san
ainihin yadda zunubi yake. Wato, ta wurin umarnin nan zunubi
ya fita a fili da iyakar muninsa.

Yaƙin da Yake a cikin Mutum saboda Zunubinsa

14 Mun dai san cewa Dokar abu ce ta ruhu. Ni kuwa mai halin
mutuntaka ne, bawa kawai a hannun zunubi. 15 Ban gane da abin
da nake yi ba. Don abin da nake so in yi, ba shi nake yi ba; kuma
abin da nake ƙi, shi nake yi. 16 Idan kuwa abin da nake yi shi ne
abin da ba na so in yi, na yarda ke nan cewa Dokar nagari ne.
17 Wato, ba ni ne da kaina nake aikata wannan abu ba, sai dai
zunubin nan da yake zama a cikina. 18 Na san cewa ba wani abu
mai kyau da yake zama a cikina, wato, a halina na mutuntaka.
Gama ina da niyyar yin abin da yake mai kyau, amma yin haka
ya gagare ni. 19 Ba na yin abu mai kyau da nake so in yi, sai dai
ina yin muguntar da ba na so in yi. 20 To, idan ina yin abin da
ba na so in yi, wannan ya nuna cewa ba ni ne nake yin wannan
abu ba, sai dai zunubin nan da yake zama a cikina.

21 Sai na ga, ashe, ya zama mini ƙa'ida cewa idan ina so in
yi abu mai kyau, sai in ga mugunta tare da ni. 22 Gama a ciki-cikin
zuciyata dokar Allah tana faranta mini rai, 23 amma a cikin
gaɓoɓina ina ganin wata ƙa'ida dabam wadda take yaƙi da ƙa'idar
da hankalina ya ɗauka. Wannan kuwa ta ɗaure ni ga ƙa'idan nan
ta zunubi wadda take zama a cikin gaɓoɓina. 24 Kaitona! Abin
tausayi ne ni! Wane ne zai cece ni daga jikin nan mai kai ga
mutuwa? 25 Godiya ta tabbata ga Allah don ya cece ni ta wurin
Yesu Almasihu Ubangijinmu!

7.7: Fit 20.17; M. Sh 5.21 7.11: Far 3.13 7.15: Gal 5.17

Saboda haka ni da kaina dokar Allah nake bauta wa da hankalina, amma da halina na mutuntaka kuwa, dokar zunubi nake bauta wa.

Rayuwa cikin Ruhu

8 [1] Saboda haka babu wani hukuncin mutuwa yanzu a kan waɗanda suke a cikin zumunci da Almasihu Yesu. [2] Don ta wurin Almasihu Yesu ƙa'idar Ruhun nan mai ba da rai ta 'yantar da ni[e] daga ƙa'idar zunubi da mutuwa. [3] Gama abin da Dokar ba ta iya aikatawa ba saboda kāsawar halin mutuntaka, shi ne abin da Allah ya aikata. Allah kuwa ya aiko da Ɗansa ɗaya tak da kamannin jikin nan namu mai zunubi don yă zama hadaya saboda zunubi, a kuma rushe ikon zunubi cikin jiki. [4] Allah ya yi wannan ne domin duk ayyukan adalcin da Dokar ta ce a yi su sami cikawa a gare mu, mu da ba rayuwar halin mutuntaka muke yi ba, sai dai ta Ruhu. [5] Masu rayuwar halin mutuntaka sukan mai da hankalinsu ga sha'anin jiki ne, amma masu rayuwar Ruhu sukan mai da hankalinsu ga abin da Ruhu yake so ne. [6] Mai da hankali ga sha'anin jiki yakan kawo mutuwa, amma mai da hankali ga Ruhu yakan kawo rai da salama. [7] Duk wanda ya mai da hankalinsa ga sha'anin jiki ya zama abokin gāban Allah ke nan, don ba ya biyayya da dokar Allah, ba kuwa zai iya ba. [8] Masu rayuwar halin mutuntaka ba dama su faranta wa Allah rai.

9 Ku kam ba rayuwar halin mutuntaka kuke yi ba, sai dai ta Ruhu, idan Ruhun Allah yana zaune a zukatanku. Duk wanda ba shi da Ruhun Almasihu kuwa, shi ba na Almasihu ba ne. [10] Idan Almasihu yana zama cikinku ko da yake jikinku yana hanyar mutuwa saboda zunubi, Ruhun Allah yana rayar da ku saboda Allah ya karɓe ku kamar masu adalci. [11] Idan kuma Ruhun Allah, wanda ya ta da Yesu daga matattu yana zama a zukatanku, to, shi wanda ya ta da Almasihu daga matattu zai ba da rai ga jikinku mai mutuwa ta wurin Ruhunsa wanda yake zama a zukatanku.

12 Saboda haka, 'yan'uwa, muna da hakki, amma ba na wanda za mu yi rayuwar da halin mutuntakarmu yake so ba. [13] Don idan rayuwar halin mutuntaka kuke yi, za ku mutu; amma idan kuwa rayuwa ta Ruhu kuke yi, kuka kuma daina yin

---

8.11: 1 Kor 3.16

[e] **8.2 ni:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Kai" ne a nan, waɗansu kuma suna da "mu".

ayyukan zunubi, za ku rayu. 14 Gama waɗanda Ruhun Allah
yake bishe su, su 'ya'yan Allah ne. 15 Gama Ruhun da aka ba
ku ba na bauta ba ne da za ku sāke zama cikin tsoro; a'a, Ruhun
nan na zaman 'ya'yan Allah ne, kuma ta wurin Ruhun ne muke
kira ga Allah, mu ce da shi "Abba!*f* Baba!" 16 Ruhun Allah da
kansa tare da ruhunmu yana tabbatar cewa mu 'ya'yan Allah
ne. 17 Tun da yake mu 'ya'ya ne, mun zama masu cin gādo ke
nan. Wato, mu masu cin gādon albarkun Allah da kuma abokan
gādo tare da Almasihu ne. Idan kuwa mun sha wahala tare da
Almasihu, za a ɗaukaka mu tare da shi.

Ɗaukaka Mu da Za a Yi nan Gaba

18 Ai, na tabbata cewa ba yadda za a kwatanta wahalolin da
muke sha a wannan zamani da ɗaukakar da za a bayyana mana
nan gaba. 19 Dukan halitta tana marmari sosai, tana jiran Allah yă
bayyana 'ya'yansa. 20 Gama an sa halitta ta kāsa kai ga manufarta,
wannan kuwa ba bisa ga nufin halitta da kanta ba ne, sai dai don
haka ne Allah ya so. An yi wannan da sa zuciya 21 cewa halitta da
kanta za ta sami tsira daga bautar da take wa ruɓewa, za ta kuma
sami 'yancin nan na ɗaukakar da za a yi wa 'ya'yan Allah. 22 Mun
dai san cewa har wa yau dukan halitta tana nishi kamar yadda mace
mai jin zafi lokacin haihuwa takan yi. 23 Ba halitta kaɗai take nishi
ba, har da mu ma. Mu da mun riga mun sami Ruhu Mai Tsarki
wanda shi ne baiwa ta farko na abubuwan da aka ba mu, muna
nishi a ranmu, muna jira da marmari sosai don Allah yă mayar da
mu cikakkun 'ya'yansa, yă kuma 'yantar da jikin nan namu.
24 Gama ta sa zuciyan nan ne aka cece mu. Amma idan mun riga
mun ga abin da muke sa zuciya a kai, ai, wannan ba sa zuciya
kuma ba ke nan. Wane mutum yake sa zuciya ga abin da ya riga
ya samu? 25 Amma idan muna sa zuciya ga abin da ba mu riga
mun samu ba, ai, mukan jira, muna haƙuri.

26 Haka kuwa Ruhu yake yi mana taimako cikin kāsawarmu.
Ba mu san yadda ya kamata mu yi addu'a ba, amma Ruhu da
kansa yana roƙon Allah saboda mu tare da nishe-nishe waɗanda
kalmomi ba za su iya bayyana ba. 27 Allah kuma, wanda shi ne
mai ganin zuciyar mutum, ya san duk nufin Ruhu, domin Ruhu
yana yin roƙo saboda tsarkaka bisa ga nufin Allah ne.

8.15: Mar 14.36; Gal 4.6 **8.15-17**: Gal 4.5-7 **8.20**: Far 3.17-19 **8.23**: 2 Kor 5.2-4

f **8.15 Abba**: Da yaren Aramaya "baba" ke nan.

28 Mun dai san cewa a cikin dukan kome Allah yana aikata
abu mai kyau saboda waɗanda suke yin masa ƙauna ne,[g] wato,
waɗanda aka kira su bisa ga nufinsa. 29 Gama waɗanda Allah ya
riga ya zaɓa tun tuni, su ne ya kuma keɓe su ɗauki kamannin
Ɗansa, don yă zama na fari a cikin 'yan'uwa masu yawa.
30 Saboda waɗanda Allah ya zaɓa, su ne ya kira. Waɗanda ya
kira, su ne ya mai da su masu samun zaman marasa laifi a
gabansa. Waɗanda suka sami zaman marasa laifi a gabansa kuwa,
su ne ya kuma ɗaukaka.

Ƙaunar Allah cikin Almasihu Tabbatacciya Ce

31 To, me za mu ce game da wannan batu? Idan Allah yana
goyon bayanmu, wa ya isa yă yi gāba da mu? 32 Allah kuwa bai
hana mana Ɗansa ba, amma ya miƙa shi saboda mu duka. Ashe,
shi Allahn da ya riga ya ba mu Ɗansa ba zai ba mu duk sauran
abubuwa hannu sake ba? 33 Wane ne zai kawo ƙara a kan waɗanda
Allah ya zaɓa? Ai, Allah da kansa ne yake mai da su su zama
marasa laifi a gabansa. 34 Wane ne ya isa yă yi wa mutum hukunci,
Almasihu Yesu wanda ya mutu, ko kuwa a ce, wanda aka ta da
shi daga matattu, wanda yana kuma zama a hannun dama na Allah,
shi ne kuwa yana roƙon Allah saboda mu.

35 Wane ne zai iya raba mu da ƙaunar da Almasihu yake yi
mana? Wahala ce, ko wuya, ko tsanani, ko yunwa, ko rashi, ko
hatsari, ko mutuwa? 36 Kamar yadda Rubutaccen Maganar Allah
ya ce:

"Saboda kai muke fuskantar mutuwa kullum;
an ɗauke mu kamar tumakin da za a yanka."

37 Ai! A cikin dukan waɗannan al'amura mun wuce a ce da mu
masu nasara kawai; wannan kuwa ta wurin shi wanda ya ƙaunace
mu ne. 38 Gama na tabbata cewa ko mutuwa ko rai, ko mala'iku
ko aljanu, ko halin yanzu ko na nan gaba, ko ikoki iri-iri, 39 ko
tsawo ko zurfi, ko wani abu dabam a dukan halitta, duk ba su
isa ba sam su raba mu da ƙaunar da Allah yake yi mana ta wurin
Almasihu Yesu Ubangijinmu.

8.36: Zab 44.22

[g] **8.28** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da, "A cikin dukan al'amura Allah yana aikata alheri ga waɗanda suke ƙaunarsa;" waɗansu rubuce-rubucen hannu kuma suna da, "Dukan al'amura suna aikata tare zuwa ga alheri ga masu ƙaunar Allah" ne a nan.

Allah Ya Zaɓi Isra'ila

9 1 Ina faɗin gaskiya cikin Almasihu, ba ƙarya nake yi ba. A
ciki tunanin zuciyata ina da tabbaci bisa ga shaidar Ruhu Mai
Tsarki game da wannan. 2 Ina da baƙin ciki ƙwarai, da kuma
damuwa a kullum cikin zuciyata. 3 Da ma a ce ni kaina an la'anta
ni, an kuma raba ni da Almasihu saboda ceton 'yan'uwana, wato,
mutanen kabilata! 4 Waɗannan kuwa su ne Isra'ilawa. Su ne Allah
ya mai da su 'ya'yansa, ya bayyana musu ɗaukakarsa, ya ba su
alkawarinsa da Dokarsa, ya nuna musu hanyar sujada ta gaske,
ya kuma ba su sauran alkawuran. 5 Asalinsu kuwa daga kakannin
kakannin nan ne waɗanda aka sansu sosai. Almasihu kuwa, bisa
ga mutuntakarsa, shi daga kabilarsu ne. Bari Allah mai mulki a
kan kome, yă karɓi yabo har abada.[h] Amin.

6 Ba wai manufar Allah game da mutanensa ta zama banza ba
ne. Don ba duk waɗanda asalinsu Isra'ila ne mutanen Allah ba.
7 Kuma ba duk waɗanda suke daga zuriyar Ibrahim ne 'ya'yan
Allah ba. A maimakon haka Allah ya ce wa Ibrahim, "Ta wurin
Ishaku ne za ka sami 'ya'yan nan da na yi maka alkawari."
8 Wato, 'ya'yan da ake samu ta haihuwar jiki ba su ne 'ya'yan
Allah ba, sai dai 'ya'yan da ake samu ta cikawar alkawari, su ne
akan ce da su 'ya'ya na gaske. 9 Gama ga abin da Allah ya ce a
lokacin da ya yi wa Ibrahim alkawari, "A sa'ad da lokaci ya cika
zan komo, Saratu kuwa za ta haifi ɗa."

10 Akwai wani misali kuma. 'Ya'yan Rifkatu suna da baba
ɗaya ne, wato, ubanmu Ishaku. 11-12 Amma kafin a haifi yaran
nan biyu, Allah ya faɗa wa Rifkatu cewa, "Babban zai bauta wa
ƙaramin." Wannan ya faru kafin ma su aikata wani abu mai kyau,
ko marar kyau. Allah ya faɗa haka don yă zama cewa, wanda za
a zaɓa za a zaɓe shi ne bisa ga shirin Allah ba wai saboda
ayyukansa ba. 13 Kamar yadda yake a rubuce cewa, "Na ƙaunaci
Yakubu, na kuwa ƙi Isuwa."

14 To, me za mu ce? Allah bai yi daidai ba ke nan? Ina! Ko
kaɗan! 15 Gama Allah ya ce wa Musa, "Ga wanda zan nuna wa
jinƙai zan nuna masa jinƙai, Ga wanda zan nuna wa tausayi zan
nuna masa tausayi." 16 Wato, wannan bai dogara ga son mutum
ko ƙoƙarinsa ba, sai dai ga jinƙan Allah kawai. 17 Gama

9.4: Fit 9.4 **9.7:** Far 21.12 **9.9:** Far 18.10 **9.12:** Far 25.23 **9.13:** Mal 1.2-3
9.15: Fit 33.19

[h] **9.5 Bari Allah . . . karɓi yabo har abada:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "Bari Allah, wanda yake mulki a kan kome, yă karɓi yabo har abada", ko kuwa "Bari shi kuma, wanda yake Allah mai mulki a kan kome, yă karɓi yabo har abada!"

Rubutaccen Maganar Allah, ya ce wa Fir'auna: "Na sa ka ka
zama sarki saboda in nuna ikona ta wurinka, a kuma sanar da
sunana cikin duniya duka." 18 Ta haka Allah yakan nuna jinkai
ga wanda yake so yă nuna masa jinkai, yakan kuma taurara
zuciyar wanda yake so yă taurara masa zuciya.

Fushin Allah da Jinkansa

19 Waninku zai iya ce mini, "To, idan haka ne, me ya sa Allah
yana ganinmu da laifi har yanzu? Wane ne zai iya kin yarda da
nufin Allah?" 20 Amma wane ne kai, ya mutum, da har za ka yi
mūsu da Allah? Abin da aka gina zai iya ce wa wanda ya gina
shi, "Me ya sa ka gina ni haka?" 21 Ai, mai yin tukwanen laka
yana da iko yă yi amfani da laka yadda yake so. Yana iya yin
amfani da dunkule guda na laka yă yi wadansu tukwane saboda
aiki mai daraja, wadansu kuma saboda aiki marar daraja.

22 Haka ma aikin Allah yake. Ya so yă nuna fushinsa, yă kuma
bayyana ikonsa a fili. Amma fa cikin hakuri sosai ya jimre da
wadanda suka cancanci fushinsa, wadanda Allah yake a shirye yă
halaka. 23 Haka kuma ya so yă bayyana yalwar daukakarsa ga
wadanda ya nuna musu jinkansa, wadanda ya shirya tun da farko
don su sami daukakarsa. 24 Wato, mu ke nan, mu wadanda Allah
ya kira, ba daga cikin Yahudawa kawai ba, amma har daga cikin
wadanda ba Yahudawa ba ma. 25 Kamar yadda aka fada a littafin
Hosiya cewa,

"Su wadanda ba mutanena ba ne
zan ce da su 'Mutanena.'
Kuma al'ummar da ban kaunace ta ba
zan ce da ita 'Wadda nake kauna.'
26 Kuma a daidai inda aka ce musu, 'Ku ba mutanena ba',
a wurin ne za a ce da su ''ya'yan Allah mai rai.' "
27 Game da Isra'ila kuwa annabi Ishaya ya daga murya ya
ce,
"Ko da yake yawan Isra'ilawa yana kama da yashin
bakin teku,
wadanda suka zama ragowa daga cikinsu ne kawai za a
cece su.
28 Gama Ubangiji zai hukunta duniya gaba daya,
ba da 6ata lokaci ba."
29 Kamar yadda Ishaya ya yi annabci cewa,

9.17: Fit 9.16 **9.20**: Ish 29.16; 45.9 **9.25**: Hos 2.23 **9.26**: Hos 1.10
9.27-28: Ish 10.22-23

"Da ba don Ubangiji Mai Iko duka ya bar mana zuriya
ba,
da mun zama kamar Sodom, da an mai da mu kamar
Gomora."

Rashin Bangaskiyar Isra'ila

30 To, yaya ke nan? Ai, waɗanda ba Yahudawa ba da ba su
yi ƙoƙari su sami adalcin Allah ba, sun samu. Adalcin nan da
suka samu kuwa irin da ake samu ta bangaskiya ne. 31 Amma
Isra'ilawa da suka yi ƙoƙarin neman hanyar adalcin Allah ta wurin
bin doka, ba su samu ba. 32 Me ya sa haka? Don ba ta hanyar
bangaskiya ne suka neme shi ba, sai dai ta ƙoƙarin kansu. Sai
suka yi tuntuɓe da "dutsen nan mai sa tuntuɓe." 33 Kamar yadda
yake a rubuce cewa:

"Ga shi na sa dutse a Sihiyona,
dutse mai sa tuntuɓe.
Zai sa mutane da yawa su fāɗi.
Amma duk wanda ya ba da gaskiya gare shi
ba zai sha kunya ba."

10 1 To, 'yan'uwana, abin da na fi so fiye da kome shi ne
Isra'ilawa su sami ceto. Addu'ar da nake yi wa Allah
saboda su ke nan. 2 Na dai shaida cewa sun ba da kansu sosai ga
bautar Allah, amma wannan kuwa ba tare da ganewa ta gaskiya
ba. 3 Tun da yake ba su san hanyar da Allah yake sa mutane su
zama marasa laifi ba, kuma suna ƙoƙari su kafa tasu hanyar zaman
marasa laifi a gaban Allah, sai wannan ya sa ba su ba da kansu
ga hanyar da Allah yake sa mutane su zama marasa laifi ba.
4 Gama Almasihu shi ne wanda ya kawo ƙarshen Dokar, don duk
mai ba da gaskiya yă sami zaman marar laifi a gaban Allah.

Ceto na Kowa Ne

5 Musa ya yi rubutu game da samun zaman marar laifi ta wurin
bin Dokar. Ya ce, "Duk wanda ya bi Dokan nan zai rayu ta
wurinta." 6 Amma ga abin da Rubutaccen Maganar Allah ya ce
game da samun zaman marar laifi ta wurin bangaskiya: "Kada ka
ce a cikin zuciyarka, 'Wane ne zai hau sama?' " (Wato, don yă
sauko da Almasihu.) 7 "Ko kuwa ka ce, 'Wane ne zai sauko har
ƙarƙashin duniya.' " (Wato, don yă ta da Almasihu daga matattu.)
8 Abin da Rubutaccen Maganar Allah yake faɗi shi ne: "Maganar
Allah tana kusa da kai, tana a bakinka, da kuma a cikin zuciyarka."

9.29: Ish 1.9 **9.33**: Ish 28.16 **10.5**: L. Fir 18.5 **10.6-7**: M Sha 30.12-13

Maganan nan kuwa ita ce sakon bangaskiyar da muke wa'azinta.
9 Idan ka shaida da bakinka cewa Yesu shi ne Ubangiji, ka kuma
ba da gaskiya cikin zuciyarka cewa Allah ya ta da shi daga matattu,
za a cece ka. 10 Gama da zuciya ne akan ba da gaskiya a sami
zaman marar laifi a gaban Allah, kuma da baki ne akan ba da
shaida a sami ceto. 11 Kamar yadda Rubutaccen Maganar Allah ya
ce, "Duk wanda ya ba da gaskiya gare shi ba zai sha kunya ba."
12 Gama ba bambanci tsakanin Yahudawa da wadanda ba
Yahudawa ba. Ubangijin nan daya shi ne Ubangijin kowa, shi ne
kuma yakan ba da albarku masu yawa ga duk masu kai kukansu
a gare shi. 13 Kamar yadda Rubutaccen Maganar Allah ya ce, "Duk
wanda ya kira bisa sunan Ubangiji zai sami ceto."

14 Amma ta yaya za su kira ga wanda ba su gaskata da shi
ba? Ta yaya za su gaskata da wanda ba su taba ji ba? Ta yaya
kuma za su ji in babu wanda zai yi musu wa'azi? 15 Ta yaya kuma
masu wa'azi za su yi wa'azi in ba a aike su ba? Kamar yadda
yake a rubuce cewa, "Isowar masu kawo bishara abu mai kyau
ne kwarai!" 16 Amma ba dukan Isra'ilawa ne suka yarda da Labari
Mai Dadin ba. Kamar yadda Ishaya ya ce, "Ya Ubangiji, wa ya
gaskata da sakonmu?" 17 Saboda haka akan ba da gaskiya ta wurin
jin sakon ne, kuma akan ji sakon ta wa'azi a kan Almasihu ne.

18 Amma ina tambaya, "Wai gaskiya ne ba su ji ba?" Ai, sun
ji. Gama Rubutaccen Maganar Allah ya ce,

"Muryarsu kuwa ta bi ta duniya duka,
maganganunsu kuma sun kai iyakar duniya."

19 Ina sake tambaya. "Wai Isra'ilawa ba su gane ba ne?" Da farko,
Musa ya amsa cewa Allah ya ce:

"Zan sa ku ku yi kishin jama'ar da ba al'umma ba ce;
kuma ta wurin al'umma marar wayo zan sa ku ku yi
fushi."

20 Sa'an nan kuma Ishaya ya yi karfin hali har da cewa Allah ya
ce:

"Wadanda ba su neme ni ba,
su ne suka same ni;
Na bayyana kaina ga wadanda ba su ma yi tambaya
yadda za su same ni ba."

21 Amma game da Isra'ila, Allah kuma ya ce,

"Duk yini na mika hannayena ga jama'a masu rashin
biyayya da masu kin ji."

10.6-8: M. Sh 30.12-14 **10.11**: Ish 28.16 **10.13**: Jow 2.32 **10.15**: Ish 52.7
10.16: Ish 53.1 **10.18**: Zab 19.4 **10.19**: M. Sh 32.21 **10.20**: Ish 65.1

Allah bai Ki Isra'ila Gaba Daya Ba

11 [1] To, ina tambaya: Allah ya ki mutanensa ke nan? Ina! Ko kaɗan! Ni da kaina mutumin Isra'ila ne, daga zuriyar Ibrahim, kuma mutumin kabilar Benjamin. [2] Allah bai ki mutanensa waɗanda ya zaɓa tun daga farko ba. Kun dai san abin da Rubutaccen Maganar Allah ya faɗa game da Iliya, wato, yadda shi Iliya ya kai kuka ga Allah a kan Isra'ila cewa, [3] "Ubangiji, sun kakkashe annabawanka, sun kuma rurrushe bagadanka; ni ne kaɗai na rage, kuma suna nema su kashe ni." [4] Wace amsa ce Allah ya ba shi? Ya amsa da cewa, "Na yi wa kaina ajiyar mutane dubu bakwai waɗanda ba su durƙusa su yi wa allahn nan mai suna Ba'al bauta ba." [5] Haka wannan ya kasance a yanzu ma. Akwai ragowar mutane waɗanda Allah ya zaɓa bisa ga alherinsa. [6] Zaɓen nan da Allah ya yi kuwa ya dogara ga alherinsa ne, ba ga ayyukan da mutanen suka yi ba. Gama in ba haka ba, alheri bai zama alheri na gaske ba.

7 To, yaya ke nan? Ai, Isra'ilawa sun kāsa samun abin da suke nema. Waɗansu kaɗan da aka zaɓa a cikinsu sun samu, amma sauran sun zama masu taurin kai. [8] Kamar yadda yake a rubuce cewa: "Allah ya mai da su marasa hankali da marasa ganewa; ya ba su idanu da ba sa gani, da kunnuwa da ba sa ji. Wannan kuwa ya ci gaba har wa yau."

[9] Kuma Dawuda ya ce,
"Bari bikinsu yă zama musu tarko,
abin jawo musu hatsari.
Bari yă sa su yi tuntuɓe
yă jawo musu hukunci.
[10] Bari idanunsu su duhunta don kada su iya gani,
yawan wahala kuma yă zuba musu nauyi har abada."

Ceton Waɗanda ba Yahudawa Ba

11 Har yanzu ina tambaya. Da Isra'ilawa suka yi tuntuɓe, sun fāɗi ba za su tashi ba ke nan? Ina! Ko kaɗan! Saboda zunubinsu ceto ya kai ga waɗanda ba Yahudawa ba, don a sa Isra'ilawa su ji kishinsu. [12] In kuwa zunubin da suka yi ya kawo wa duniya albarka, in kuma kāsawarsu ta kawo albarku ga waɗanda ba Yahudawa ba, to, yaya fa albarkan nan zai zama a lokacin da yawan Isra'ilawa masu ɗungumawa ga Allah sun cika?

10.21: Ish 65.2 **11.1:** Filib 3.5 **11.3:** 1 Sar 19.10,14 **11.4:** 1 Sar 19.18
11.8: M. Sh 29.4; Ish 29.10 **11.9-10:** Zab 69.22-23

13 Yanzu, da ku waɗanda ba Yahudawa ba nake magana. Tun
da yake ni manzo ne ga waɗanda ba Yahudawa ba, zan yi ɗan
taƙama da aikin nan nawa. 14 Ta yin haka ina fata cewa zan iya
sa mutanena Isra'ilawa su ji kishi, har ma wannan ya sa a ceci
waɗansunsu. 15 A sa'ad da aka yar da su, sai ya buɗe hanya, aka
shirya tsakanin Allah da mutanen duniya. A sa'ad da za a karɓe
su fa, ba samun rai daga matattu ne wannan zai kawo ba?

16 Idan an keɓe gutsurin burodin hatsin nunan fari, ta hanyar
miƙa shi ga Allah, an keɓe dukan burodin ke nan. Idan kuma aka
keɓe wa Allah saiwar itace, dukan rassan itacen ma an keɓe su
ke nan. 17 To, an sassare waɗansu rassan itacen zaitun irin da aka
nome, sai aka ɗauki wani reshen itacen zaitun irin na daji, aka
kuma yi musu aure. Ku waɗanda ba Yahudawa ba kuwa, kamar
reshen itacen zaitun na daji kuke, ku ne aka haɗa ku da tushen
nan, wato Yahudawa, waɗanda daga gare su ne kuke samun
albarkun Allah. 18 Saboda haka kada ku yi taƙama a kan cewa
kun fi waɗancan rassan da aka sassare. Idan kuwa kuna taƙama,
sai ku tuna cewa ba tushen ne yake dogara a gare ku ba, sai dai
ku ne kuke dogara ga tushen.

19 Amma kana iya cewa, "Ai, an sassare rassan ne domin a
sami dama a haɗa ni da tushen." 20 Kwarai kuwa! Amma saboda
rashin bangaskiya ne aka sassare su daga tushen, kai kuma bisa
ga bangaskiya ne kake da dama ka ci gaba da zama a kan tushen.
Saboda haka kada ka yi taƙama; a maimakon haka, ka ji tsoro.
21 Gama idan Allah bai bar rassan nan waɗanda su ne ainihin na
tushen ba, kai ma ba zai bar ka ba. 22 A nan muna iya ganin yadda
Allah yake da alheri, da kuma tsanani. Ya nuna tsananinsa ga
waɗanda suka fāɗi, amma ya nuna alherinsa a gare ka, wato, idan
ka ci gaba da zama cikin alherinsa. Idan kuwa ba ka ci gaba da
haka ba, kai ma za a sare ka daga tushen ke nan. 23 Idan kuwa
su Isra'ilawa ba su ci gaba da rashin bangaskiya ba, za a haɗa su
da tushen, don Allah yana iya yă sāke mai da su a tushen. 24 Ku
waɗanda ba Yahudawa ba dai, kuna kamar itacen zaitun nan irin
na daji wanda bayan aka saro shi, sai aka haɗa masa aure da
itacen zaitun irin da aka nome. Wannan kuwa da aka yi ba bisa
ga ƙa'idar auren itatuwa ne ba. To, tun da yake su Isra'ilawa su
ne kamar irin itacen zaitun wanda aka nome, zai zama abu mai
sauƙi sosai ga Allah yă sāke mai da rassan nan da aka sare a
itacen nan wanda shi ne asalinsu.

11.16: L Kid 15.17-21

Allah Yana Nuna Jinkai ga Kowa

25 Ba na so ku kasance da rashin sanin wannan asirin
'yan'uwa, don kada ku zama masu ɗaga kai. Taurin zuciya ya
faru ga sashi na Isra'ila har dukan yawan waɗanda ba Yahudawa
ba da za su shiga wurin Allah yă cika. 26 Ta haka za a ceci dukkan
Isra'ila. Kamar yadda yake a rubuce cewa,

"Mai Ceto zai zo daga Sihiyona;
Zai kawar da duk ƙin bin Allah daga zuriyar Yakubu.
27 Wannan shi ne alkawarina da su,
a sa'ad da zan ɗauki zunubansu."

28 Yahudawa sun zama masu gāba da Allah saboda ƙin
Labari Mai Daɗin da suka yi; wannan kuma saboda amfaninku
ne. Amma saboda zaɓensu da aka yi, su mutane ne da Allah
yake ƙauna; wannan kuwa albarkacin kakannin kakanninsu ne.
29 Gama baiwar Allah da kirarsa ba abubuwa ne da Allah zai
canza ba. 30 A dā ku waɗanda ba Yahudawa ba, ku masu rashin
biyayya ga Allah ne, amma yanzu kam kun sami jinkai ta wurin
rashin biyayyar Yahudawa. 31 Haka kuma su Yahudawa sun
zama masu rashin biyayya ga Allah a yanzu;[i] wannan kuwa
don su sami jinkai ne ta wurin jinkan nan da Allah ya nuna
muku. 32 Gama Allah ya mai da dukan mutane kamar 'yan
kurkuku saboda rashin biyayya. Ya yi haka don yă nuna jinkai
ga kowa.

Yabo ga Allah

33 Hakika, zurfin hikimar Allah da kuma na saninsa marar
iyaka ne! Hukunce-hukuncensa sun fi gaban bincike. Abubuwan
da yake aikatawa sun wuce gaban ganewa!

34 "Wa ya taɓa sanin zuciyar Ubangiji?
Wa ya taɓa zama abokin shawararsa?
35 Wa ya taɓa ba wa Allah wani abu
har da zai zama dole Allah yă mayar masa?"

36 Gama shi ne ya halicci dukan abubuwa, kuma abubuwan nan
duka suna kasancewa ta wurinsa ne, kuma saboda shi. Bari
ɗaukaka ta tabbata ga Allah har abada. Amin.

11.26: Ish 59.20-21 **11.27**: Irm 31.33-34 **11.33**: Ish 55.8 **11.34**: Ish 40.13
11.35: Ayu 41.11 **11.36**: 1 Kor 8.6

[i] **11.31 Yanzu**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da wannan kalmar.

Hadaya Mai Rai

12 [1] Saboda haka, 'yan'uwa, bisa ga jinkan nan na Allah, ina
rokonku ku mika kanku hadaya wadda take mai rai, mai
tsarki, da kuma abin so ga Allah. Wannan kuwa ita ce hanyar
da za ku yi wa Allah hidima ta ainihi. [2] Kada ku yarda tunani
irin na zamanin nan yă bi da hankalinku, amma ku yarda Allah
yă canza ku yă sabunta zuciyarku da hankalinku. Ta haka za ku
iya tabbatar da abin da yake nufin Allah, wato, abin da yake mai
kyau, abin so ga Allah, da kuma abin da yake cikakke.

3 Bisa ga alherin nan da aka yi mini, ina yin wa kowane
dayanku gargadi cewa kada kowa yă dauki kansa da girma fiye
da yadda ya kamata yă yi. A maimakon haka kowa yă mai da
hankali game da yadda yake ganin kansa, wato, yă rika ganin
kansa daidai gwargwadon bangaskiyar da Allah ya ba shi.
[4] Muna da gaɓoɓi da yawa cikin jiki guda, kuma duk gaɓoɓin
nan suna da aikinsu dabam-dabam. [5] Haka kuma, mu da muke
mutane masu yawa, mun zama jiki daya cikin Almasihu,
kowane dayanmu kuwa gaɓar dan'uwansa ne. [6] Saboda haka ya
kamata mu yi amfani da baye-bayen nan iri-iri daidai
gwargwadon alherin da Allah ya yi mana. Idan baiwarmu ta
yin annabci ce, sai mu yi annabci daidai gwargwadon
bangaskiyarmu. [7] Idan baiwarmu kuwa ta yin hidima ce, sai mu
yi hidima; idan ta yin koyarwa ce, mu yi koyarwa; [8] idan ta
karfafawar juna ce, bari mu kasance masu karfafawa. In kuma
baiwarmu ta biyan bukatar 'yan'uwa ce, sai mu yi haka din
hannu sake; idan ta shugabanci ce, sai mu ba da hankalinmu
sosai ga shugabanci; idan ta nuna tausayi ce, sai mu yi haka
din da farin ciki.

Yadda Za a Gane da Mai Bi na Gaske

9 Bari kaunarku ta zama ta gaskiya. Ku ki duk abin da yake
mugu, amma ku rike abin da yake mai kyau da karfi sosai. [10] Ku
ba da kanku ga juna da kauna irin ta 'yan'uwa. Ku kuma yi kokari
sosai wajen girmama wani fiye da kanku. [11] Kada ku taɓa zama
da rashin kwazo, amma ku dauki niyya sosai a zukatanku kuna
yi wa Allah hidima. [12] Ku yi farin ciki a cikin sa zuciyarku, ku
yi hakuri a cikin wahalarku, ku yi aminci kuma a cikin addu'arku.
[13] Ku rika raba abin da kuke da shi da mutanen Allah wadanda
suke da bukata. Ku rika karɓar baki hannu biyu-biyu.

12.4-5: 1 Kor 12.12 **12.6-8**: 1 Kor 12.4-11

14 Ku sa wa waɗanda suke tsananta muku albarka. Ku sa musu
albarka, kada ku la'anta su. 15 Ku yi farin ciki tare da waɗanda
suke farin ciki, ku yi kuka tare da waɗanda suke kuka. 16 Ku yi
zaman lafiya da juna. Kada ku nuna halin ɗaga kai, amma ku mai
da kanku abokai ga waɗanda ba a ɗauke su a bakin kome ba.[j]
Kada ku ɗauki kanku kamar kun fi sauran mutane wayo.

17 Idan kowa ya yi muku mugunta, kada ku saka masa da
mugunta. Ku lura don ku aikata abin da kowa zai iya gani cewa
daidai ne. 18 Ku yi iyakar ƙoƙarinku, in zai yiwu, ku yi zaman
lafiya da kowa. 19 Kada ku zama masu ramuwa, 'yan'uwana, sai
dai ku bar wa Allah yă rama muku da fushinsa. Don kuwa a
rubuce yake cewa, "Ramuwa tawa ce; ni kuwa zan rama, in ji
Ubangiji." 20 Rubutaccen Maganar Allah ya sāke cewa: "Idan
abokin gābanka yana jin yunwa, ka ba shi abinci; idan yana jin
ƙishin ruwa; ka ba shi ruwan sha. Ta yin haka zai zama kamar
kana tara garwashin wuta a kansa ne." 21 Kada ku bar mugunta
ta yi nasara a kanku, a maimakon haka ku yi nasara a kan mugunta
ta wurin aikatawar abin da yake mai kyau.

Yin Biyayya ga Shugabannin Gwamnati

13 1 Dole ne kowa yă yi biyayya ga shugabannin gwamnati,
gama babu wani ikon shugabanci sai dai da yardar Allah.
Kuma duk masu ikon shugabancin da muke da su, Allah ne ya
kafa su. 2 Saboda haka duk wanda ya ƙi yin biyayya ga
shugabannin gwamnati, ya ƙi yin biyayya da abin da Allah ya
kafa ne. Masu aikata haka kuwa za su jawo wa kansu hukunci
ne. 3 Gama shugabanni ba abin tsoro ba ne ga waɗanda suke yin
abin da yake daidai, sai dai ga waɗanda suke yin abin da yake
mugu. Kana so ka rabu da tsoron mutumin da yake da ikon
shugabanci? To, sai ka aikata abin da yake daidai, shi kuwa zai
yabe ka, 4 don shi bawan Allah ne saboda amfaninka. Amma idan
kai mai yin mugunta ne, sai ka ji tsoro, don ba a banza ne
shugaban nan yake riƙe da takobinsa ba. Shi bawan Allah ne,
kuma ta wurinsa fushin Allah yakan tabbata don a hukunta mai
mugunta. 5 Saboda haka dole ne ku yi biyayya ga shugabannin
gwamnati. Ba don ku guje wa fushin Allah kaɗai ba, amma don
tunaninku yă kasance babu laifi.

12.14: Mat 5.44; Luk 6.28 **12.16:** K. Mag 3.7 **12.19:** M. Sh 32.35
12.20: K. Mag 25.21-22

[j] **12.16 Ku mai da kanku abokai ga waɗanda ba a ɗauke su a bakin kome ba:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne, "Ku yarda da yin irin aikin da ba a gani da daraja."

6 Wannan ne kuma ya sa kuke biyan haraji, don shugabannin
gwamnati ma'aikatan Allah ne waɗanda suke ba da duk lokacinsu
saboda aikin shugabanci. 7 Ku biya wa kowa duk abin da yake
binku. Idan harajin kanku ne ya kamata ku biya, sai ku biya; idan
ma harajin kayanku ne, sai ku biya. Ku ji tsoron wanda ya isa a
ji tsoronsa, ku kuma girmama wanda ya isa a girmama shi.

Kaunar Juna

8 Kada ku ɓiɓe hakkin kowa. Sai dai hakkin nan wanda ya
zama muku dole ku yi, wato, nuna ƙaunar juna. Don wanda yake
ƙaunar wani ya cika Dokar ke nan. 9 Waɗannan umarnai, wato,
"Kada ka yi zina; kada ka yi kisankai; kada ka yi sata; kada ka
yi kwaɗayi," da duk sauran umarnan da ake da su, duk sun sami
cikawa cikin maganan nan da ta ce, "Ka ƙaunaci kowa kamar
kanka." 10 Idan kana ƙaunar wani, ba za ka taɓa yin masa mugunta
ba. Saboda haka ƙauna ita ce cikawar Dokar.

11 To, ku aikata wannan domin kun gane irin zamanin da
muke ciki. Lokaci ya yi da za ku tashi daga barcinku, don lokacin
da za a cece mu ya yi kusa yanzu fiye da a lokacin da muka tuba.
12 Dare ya kusan ƙarewa, kuma sauran lokaci kaɗan gari yă waye.
Saboda haka bari mu watsar da ayyukan da suke na duhu, mu sa
kayan yaƙinmu na haske. 13 Bari mu yi rayuwa ta kirki yadda ya
dace da waɗanda suke zama a cikin haske; ba tare da shaye-shaye
iri-iri da buguwa ba, ko da halin lalata da neman jin daɗi na rashin
kunya, ko da faɗa da kishi. 14 A maimakon haka sai ku ɗauki
halin Ubangiji Yesu Almasihu, kada kuma ku yarda da halin
mutuntaka da zai bi da ku bisa ga sha'awace-sha'awacensa.

Kada Ka Ɗora wa Ɗan'uwanka Laifi

14 1 Ku karɓi mutumin da bangaskiyarsa ba ta yi ƙarfi ba,
amma kada ku neme shi da laifi idan ra'ayinsa dabam
yake da naku. 2 Bangaskiyar wani mutum za ta yarda masa yă ci
duk abin da ya ga dama, amma mutumin da ba shi da ƙarfi cikin
bangaskiyarsa, sai kayan lambu kawai yake ci. 3 Mutumin da yake
cin duk irin abincin da ya ga dama kada yă rena shi wanda ba
ya cin kowane irin abinci. Kuma wanda ba ya cin kowane irin
abinci, kada yă ɗora laifi a kan wanda yake cin kowane irin abinci,
don Allah ya riga ya karɓe shi. 4 Kai wane ne da za ka ɗora laifi
a kan bawan wani? Ko bawan ya yi aiki mai kyau, ko ya kāsa,

13.6-7: Mat 22.21; Mar 12.17; Luk 20.25
13.9: Fit 20.13-15,17; M. Sh 5.17-19,21; L. Fir 19.18

ai, wannan ruwan maigidansa ne. Ga shi kuwa nasara zai yi, don Ubangiji ya iya sa shi yă yi nasara.

5 Wani yakan ga wata rana da muhimminci fiye da sauran ranaku. A ganin wani kuwa dukan ranaku daidai ne. Kowa dai yă sami nasa cikakken tabbaci a cikin zuciyarsa. 6 Duk mai ganin wata rana da muhimminci yana yin haka ne cikin girmamawar Ubangiji. Duk mai cin kowane irin abinci yana yin haka ne cikin girmamawar Ubangiji, don yakan ba da godiya ga Allah saboda abincin. Duk wanda ba ya cin kowane irin abinci shi ma yana haka ne cikin girmamawar Ubangiji, don shi ma yakan yi wa Allah godiya. 7 A cikinmu, ba don amfanin kansa mutum yake rayuwa ba. Ba don amfanin kansa yake mutuwa ba kuma. 8 Idan muna rayuwa, saboda Ubangiji muke rayuwa, in kuma mutuwa za mu yi, saboda Ubangiji muke mutuwa. Saboda haka ko rayuwa ne muke yi ko mutuwa, mu na Ubangiji ne. 9 Gama Almasihu ya mutu ya kuma tashi da rai don yă zama Ubangiji na waɗanda suke matattu da kuma waɗanda suke masu rai. 10 Kai fa, me ya sa kake ganin ɗan'uwanka da laifi? Kai kuma me ya sa kake rena ɗan'uwanka? Dukanmu dai za mu tsaya a gaban Allah wanda shi ne mai yi mana shari'a. 11 Gama a rubuce yake cewa,

"Na rantse da kaina, in ji Ubangiji,
Kowace gwiwa za ta durƙusa a gabana;
kowane harshe zai shaida cewa ni ne Allah."

12 To, kowane ɗayanmu zai ba da lissafin rayuwarsa ga Allah.

Kada Ka Sa wa Ɗan'uwanka Abin Tuntuɓe

13 Saboda haka sai mu daina halin nan na ganin laifin juna. A maimakon haka sai kowa yă ɗauki niyya cewa ba zai zama dalilin tuntuɓe ko abin sa zunubi ga ɗan'uwansa ba. 14 Na sani, ina kuma da cikakken tabbaci cikin Ubangiji Yesu cewa babu wani abu wanda yake da rashin tsabta bisa ga asalinsa. Amma idan wani ya ɗauka cewa wani abu mai rashin tsabta ne, to, a gare shi ne abin yake da rashin tsabta. 15 Idan kana ɓata wa ɗan'uwanka zuciya saboda abincin da kake ci, ba halin ƙauna kake nunawa ba ke nan. Kada abincin da kake ci yă zama hanyar lalatar da ɗan'uwanka wanda Almasihu ya mutu dominsa. 16 Kada abin da yake daidai a ganinka yă zama abin zargi ga waɗansu. 17 Gama mulkin Allah ba zancen ci da sha ba ne, zancen adalci ne, da salama, da farin ciki a cikin Ruhu Mai Tsarki. 18 Kuma

14.1-6: Kol 2.16 **14.10:** 2 Kor 5.10 **14.11:** Ish 45.23

duk wanda yake yi wa Almasihu bauta ta wannan hanya, shi mai faranta wa Allah rai ne, mai samun yarda a wajen mutane kuma.

19 Saboda haka bari mu yi iyakacin ƙoƙarinmu don mu aikata
abin da zai kawo zaman lafiya da ƙarfafawar juna. 20 Kada ku
rushe aikin Allah saboda sha'anin cin abinci. Lallai ana iya cin
kowane irin abinci, amma ba abu mai kyau ba ne idan abincin
da ake ci ya zama abin sa wa wani tuntuɓe. 21 Ya fi kyau kada
ka ci nama, ko ka sha ruwan inabi, ko ka aikata kowane irin abu
idan zai sa ɗan'uwanka yă fāɗî. 22 Bari duk ra'ayin da kake da
shi game da wannan sha'ani yă kasance tsakaninka da Allah. Mai
albarka ne wanda zuciyarsa ba ta ba shi laifi ba, game da abin
da shi da kansa ya ɗauka cewa daidai ne. 23 Amma mutumin da
yake da shakka a kan abin da yake ci, yana jawo wa kansa
hukuncin Allah ne idan ya ci, don halin nan da yake yi bai dogara
ga bangaskiya ba. Kuma duk abin da bai dogara ga bangaskiya
ba, zunubi ne.

Faranta wa Dan'uwanka Rai, ba Kanka Ba

15 1 Mu da muke masu ƙarfi cikin bangaskiyarmu ya kamata
mu ɗauki nauyin waɗanda ba su da ƙarfi, don mu taimake
su cikin kāsawarsu. Kada kuma mu nuna halin sonkai. 2 Bari kowa
a cikinmu yă faranta wa ɗan'uwansa rai saboda amfaninsa da
kuma ginawar bangaskiyarsa. 3 Gama ko Almasihu ma ba kansa
ya faranta wa rai ba. Kamar yadda yake a rubuce cewa,
"Zage-zagen masu yin maka zagi sun fāɗo a kaina." 4 Gama duk
abin da aka rubuta tun dā a cikin Rubutattun Maganar Allah an
rubuta ne don a koyar da mu, don mu zama da sa zuciya ta wurin
jimrewa da ƙarfafawa waɗanda maganar Allah takan ba mu. 5 Bari
Allah mai ba da jimrewa da ƙarfafawa yă kai ku ga yadda za ku
yarda da juna a sa'ad da kuna bin misalin Almasihu Yesu. 6 Ta
haka dukanku za ku kasance da baki ɗaya, da nufi ɗaya kuma,
kuna ɗaukaka Allah wanda shi ne Uban Ubangijinmu Yesu
Almasihu.

7 Ku karɓi juna hannu biyu-biyu kamar yadda Almasihu ya
karɓe ku hannu biyu-biyu don ku sa a ɗaukaka Allah. 8 Gama ina
dai gaya muku cewa dalilin da Almasihu ya zama mai yin hidima
ga Yahudawa shi ne domin a nuna gaskiyar maganar Allah, a
kuma tabbatar da alkawuran da aka yi wa kakannin kakanninsu,
9 don kuma waɗanda ba Yahudawa ba su ɗaukaka Allah saboda
jinƙansa. Kamar yadda yake a rubuce cewa:

15.3: Zab 69.9

"Saboda haka zan yabe ka a cikin waɗanda ba
Yahudawa ba,
zan rera waƙoki don yabon sunanka."
10 Rubutaccen Maganar Allah ya sāke cewa,
"Ya ku waɗanda ba Yahudawa ba, ku yi farin ciki
tare da mutanen Allah."
11 An ƙara da cewa,
"Ku yabi Ubangiji, ku waɗanda ba Yahudawa ba duka,
ku yi masa yabo, ku kabilu duka."
12 Kuma Ishaya ya ce,
"Wani daga zuriyar Jesse zai bayyana,
Zai tashi yă yi mulkin waɗanda ba Yahudawa ba,
a gare shi ne waɗanda ba Yahudawa ba za su sa zuciya."
13 Bari Allah mai kawo sa zuciya yă ba ku cikakken farin ciki da salama a sa'ad da kuke ba da gaskiya gare shi. Ta haka za ku zama da cikakkiyar sa zuciya ta wurin ikon Ruhu Mai Tsarki.

Hidimar Bulus ga Waɗanda ba Yahudawa ba

14 'Yan'uwana, ni da kaina na amince cewa ku da kanku kuna cike da kirki kuna kuma cike da cikakken sani, har kun isa ku koya wa junanku. 15 A rubutun nan nawa na fita a fili sosai ina magana a kan waɗansu abubuwa don in tuna muku da su. Na yi wannan kuwa bisa ga alherin nan wanda Allah ya yi mini, 16 wanda ya sa ni in zama mai hidimar Almasihu Yesu ga waɗanda ba Yahudawa ba. Ina aikin firist ta wurin hidimar shelar Labari Mai Daɗi na Allah don waɗanda ba Yahudawa ba su zama hadaya mai karɓuwa ga Allah, waɗanda aka tsarkake su ta wurin Ruhu Mai Tsarki. 17 Saboda haka ina iya yin taƙama cikin Almasihu Yesu game da hidimar da nake yi wa Allah. 18 Ba zan yi ƙarfin hali in yi magana game da wani abu ba, sai dai abin da Almasihu ya aikata ta wurina. Wannan abin kuwa shi ne yadda aka kawo waɗanda ba Yahudawa ba ga yin biyayya ga Allah ta wajen maganganuna da ayyukana, 19 ta wajen ikon alamu da abubuwan ban mamaki, duka kuwa ta wurin ikon Ruhun Allah ne. Wato, daga Urushalima na kewaye har zuwa Ilirikum na yi shelar Labari Mai Daɗi na Almasihu, har na cika aikin nan duka. 20 A koyaushe niyyata ita ce in yi wa'azin Labari Mai Daɗi a duk inda ba a san Almasihu ba, don kada yă zama cewa ina yin gini

15.9: 2 Sam 22.50; Zab 18.49 **15.10:** M. Sh 32.43 **15.11:** Zab 117.1
15.12: Ish 11.10

a kan tushen da wani ne dabam ya kafa. 21 A maimakon haka, sai
dai kamar yadda yake a rubuce cewa,
"Waɗanda ba a yi musu magana game da shi ba za
su gani,
kuma waɗanda ba su ji ba, za su gane."
22 Wannan ne ya sa sau da yawa aka hana ni zuwa wurinku.

Shirin Bulus Yă Ziyarci Roma

23 Yanzu kam na riga na gama aikina a wannan wurin da
nake. Tun da yake tun shekaru masu yawa ina marmarin zuwa
wurinku don in gan ku, 24 na shirya in ziyarce ku yanzu. Ina
fata cewa a lokacin da zan wuce zuwa ƙasar Asbaniya, zan bi
ta wurinku in kawo ziyara. Ina fata kuma bayan na ji daɗin
zama tare da ku na ɗan lokaci, zan ci gaba da tafiyata zuwa
can tare da taimakonku. 25 Yanzu kam za ni Urushalima don in
kai taimako wa tsarkaka da suke wurin. 26 Jama'ar masu bi da
take a Makidoniya da waɗanda suke a Akaya sun ji daɗin ba
da kyautai don taimakon waɗanda suke da rashi cikin tsarkakan
Urushalima. 27 Sun ji daɗin yin haka, ko da yake lallai wannan
kamar hakki ne a kansu. Da yake waɗanda ba Yahudawa ba
sun sami nasu rabon albarkun ruhaniya daga Yahudawa, ya
zama musu kamar bashi ke nan su yi amfani da albarkunsu na
duniya don su biya bukatar Yahudawa. 28 In kuwa na gama
wannan aiki, na kuma tabbata cewa na danƙa musu wannan
taimakon da aka bayar saboda su, zan kama hanyar Asbaniya,
in kuma kawo ziyara sa'ad da zan wuce zuwa can. 29 Na tabbata
cewa in na zo wurinku, zan zo ne da cikakkiyar albarkar
Almasihu.

30 'Yan'uwa, saboda Ubangijinmu Yesu Almasihu da kuma
bisa ga ƙaunar da Ruhu yake bayarwa, ina roƙonku cewa ku
taimake ni cikin famata ta wurin yin addu'a ga Allah saboda
ni. 31 Ku yi addu'a don in sami tsira daga hannun marasa bi
waɗanda suke a Yahudiya, don kuma taimakon da zan bayar a
Urushalima yă zama abin karɓa ga tsarkakan da suke a wurin.
32 Ta haka kuwa, idan nufin Allah ne, zan iso wurinku da farin
ciki, in kuma sami hutawa tare da ku. 33 Allah mai ba da salama
yă kasance tare da ku duka. Amin.

15.21: Ish 52.15 **15.22**: Rom 1.13 **15.25-26**: 1 Kor 16.1-4 **15.27**: 1 Kor 9.11

Gaisuwa

16 [1] Ina gabatar muku 'yar'uwarmu Fibi wadda na shaida cewa ita mai kirki ce. Ita kuwa mai hidimar jama'ar masu bi ce a Kankiriya. [2] Ku karɓe ta cikin sunan Ubangiji yadda ya dace a karɓi tsarkaka. Ku kuma ba ta kowane irin tamaikon da take bukata daga gare ku, don ita kanta ta taimaki mutane da yawa, ɗuk da ni ma.

3 Ku gai da Biriskila da Akila, abokan aikina cikin Almasihu Yesu. [4] Su kuwa sun ba da ransu har kusan mutuwa saboda ni. Ba ni kaɗai ne mai godiya a gare su ba, har ma da duk jama'un masu bi na waɗanda ba Yahudawa ba. [5] Ku gai da jama'ar masu bi da take taruwa a gidansu.

Ku gai da Afanitus, abokina na ƙwarai, wanda shi ne na farko wanda ya zama mai bin Almasihu a duk ƙasar Asiya. [6] Ku gai da Maryamu wadda ta sha famar aiki sosai saboda ku. [7] Ku gai da Andaronikus da Yuniya, waɗanda Yahudawa ne kamar ni, waɗanda kuma aka ɗaure su a kurkuku tare da ni. Su kuwa mutane ne da an san su sosai a cikin manzanni, kuma sun riga ni ba da gaskiya cikin Almasihu.

8 Ku gai da Amfiliyatus, abokina na ƙwarai cikin zumuncin Ubangiji. [9] Ku gai da Urbanus abokin aikinmu cikin Almasihu, da kuma abokina Sitakis. [10] Ku gai da Afalis wanda amincinsa cikin Almasihu tabbatacce ne. Ku gai da iyalin Aristobulus. [11] Ku gai da Hirudiyan wanda shi ma Bayahude ne. Ku gai da waɗanda suke cikin Ubangiji a iyalin Narkisus.

12 Ku gai da Tirayifina da Tirayifusa, matan nan masu fama cikin aikin Ubangiji. Ku kuma gai da Farsis, abokiyata da nake ƙauna, wadda kuma ta sha famar aiki sosai saboda Ubangiji. [13] Ku gai da Rufus wanda lallai shi sananne ne a cikin Ubangiji. Ku kuma gai da mamarsa wadda ta ɗauke ni kamar ɗanta. [14] Ku gai da Asinkiritus, da Filigona, da Harmis, da Faturobas, da Harmas da kuma dukan 'yan'uwan da suke tare da su. [15] Ku gai da Filologus, da Juliya, da Niriyus da 'yar'uwarsa, da Olimfas, da duk tsarkakan da suke tare da su.

16 Ku gai da juna da gaisuwar ƙauna. Duk jama'un masu bin Almasihu suna gai da ku.

17 'Yan'uwana, ina dai roƙonku ku mai da hankali da masu kawo rabe-rabe tsakaninku, waɗanda suna sa ku tuntuɓe, suna kuma gāba da koyarwar da kuka karɓa. Ku yi nisa da su! [18] Don

---

16.3: A.M. 18.2 **16.13:** Mar 15.21

kuwa irin waɗannan mutane ba Almasihu Ubangijinmu suke bauta wa ba, sai dai cikinsu. Ta wajen dadîn bakinsu da yabon ƙarya sukan rudî masu jinsu. Masu jinsu kuwa masu tunanin yara ne. 19 Kowa ya ji labarin yadda kuke biyayya da bishara, wannan kuwa ya sa ina farin ciki saboda ku. Amma ina so ku zama masu hikima ga abin da yake mai kyau, ku kuma zama marasa laifi ga duk abin da ya shafi mugunta. 20 Allah mai ba da salama kuwa zai tattaka Shaiɗan, yă kuma ba ku iko a kansa, ba da daɗewa ba,

Alherin Ubangijinmu Yesu yă kasance tare da ku.

21 Timoti, abokin aikina, yana gai da ku; haka ma Lushiyos, da Jason, da Sosifata, waɗanda su ma Yahudawa ne.

22 Ni Tartiyus, mai rubuta wannan wasiƙa, ina gai da ku cikin Ubangiji.

23 Gayus, wanda ya karɓe ni a gidansa, kuma mai karɓar dukan jama'ar masu bi a gidansa, yana gai da ku. Erastus, ma'ajin gari, da kuma ɗan'uwanmu Kwartus suna gaishe ku. 24 Bari alherin Ubangijinmu Yesu Almasihu yă kasance tare da ku duka. Amin. [k]

Addu'ar Karshe

25 Bari ɗaukaka ta tabbata ga Allah wanda yake da iko yă kafa ku cikin bangaskiya bisa ga Labari Mai Dadîn nan da nake wa'azinsa a kan Yesu Almasihu. Labari Mai Dadîn kuwa asiri ne wanda aka ɓoye tun zamanin dā, 26 amma a yanzu an fitar da shi a fili ta wajen rubuce-rubucen annabawa. Bisa ga umarnin Allah madawwami kuma an bayyana shi ga dukkan al'ummai, don su ba da gaskiya su kuma yi biyayya.

27 Bari ɗaukaka ta tabbata ga Allah, wanda shi ne kaɗai mai hikima, ta wurin Yesu Almasihu har abada! Amin.

16.21: A.M. 16.1 **16.23**: A.M. 19.29; 1 Kor 1.14; 2 Tim 4.20

[k] **16.23** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da aya 24.

WASIKAR BULUS TA FARKO ZUWA GA
KORINTIYAWA

Gabatarwa

Marubucin *Wasika ta Farko zuwa ga Korintiyawa*, wato manzo Bulus, ya rubuta wasikar ne a shekara ta A.D. 55 a lokacin da yake da zama a birnin Afisa (Dubi 16.8).

Bulus ya rubuta wasikar don yă ba da shawara a kan damuwa iri-iri da halayen kāsawa dabam-dabam da ake da su a jama'ar masu bi wadda shi da kansa ya kafa.

A zamanin Bulus, Korinti wani babban birni ne wanda aka san shi da halaye dabam-dabam. Halayen nan kuwa su ne: kasuwanci da ciniki; fokarin neman ilimi da hikima; fokarin bin addini; da kuma halin lalata, musamman wani irin karuwancin da ake yi a kan cewa ana yi wa Allah bauta ne.

Ko da yake jama'ar masu bi a Korinti ta kasance da baye-bayen Ruhu Mai Tsarki, wadansu cikin 'yan jama'ar masu bi ba su nuna halin da ya dace da rayuwar mai bi ba. Saboda haka wasikar ta nace sosai tana ba da shawara, tana kuma yin gargadi a kan halaye dabam-dabam wadanda ya kamata jama'ar masu bi su yi gyara a kai. Wasikar ta yi magana a kan rabe-raben da yake tsakanin jama'ar masu bi (1.10—4.31), da halin lalatar da wadansu suke ciki (5.1-13, 6.12-20), da karar 'yan'uwan da wadansu sukan yi a gaban masu shari'a wadanda ba masu bi ba (6.1-8), da kuma cin jibin Ubangijin da wadansu cikin jama'ar masu bi suke yi ta hanyar da ba ta dace ba (11.17-34). Ban da haka ma, akwai gyaran da wasikar ta yi a kan wata koyarwar karyar da ake da ita a kan tashin matattu (15.1-58).

A karshe Bulus ya nuna cewa amsa ta wadannan damuwoyi a Korinti ita ce, su nuna wa juna irin kaunar da suka karba daga wurin Allah (sura 13).

Abubuwan da Suke Ciki

Gaisuwa da addu'a 1.1-9
Rabe-rabe a cikin jama'ar masu bi 1.10—4.21
Damuwa game da dangantaka 5.1—7.40
Daukaka Allah a maimakon gumaka 8.1—11.1
Yadda za a yi wa Allah sujada 11.2—14.40
Tashin Yesu daga matattu, da na masu bi 15.1-58
Bayarwa domin masu bi na Yahudiya 16.1-4
Maganar karshe da gaisuwa 16.5-24

Gaisuwa

1 1 Daga Bulus, wanda aka kira yă zama manzo na Yesu
Almasihu da yardar Allah, da kuma ɗan'uwanmu Sastanis,
2 zuwa ga jama'ar masu bin Allah wadda take a Korinti, zuwa
kuma ga waɗanda aka kira su zama tsarkaka cikin Yesu
Almasihu, tare da dukan waɗanda a ko'ina suke addu'a da sunan
Yesu Almasihu Ubangijinmu, Ubangijinsu da namu duka.
3 Alheri da salama daga Allah Ubanmu da Ubangiji Yesu
Almasihu su kasance tare da ku.

Bulus Ya Gode wa Allah

4 Ina gode wa Allah koyaushe dominku, saboda alherin da ya
ba ku ta wurin Almasihu Yesu. 5 Gama ta kowace hanya aka yi
muku arziki a cikinsa, wajen yin magana da ilimi duka, 6 domin
an tabbatar da shaidarmu game da Almasihu a cikinku. 7 Saboda
haka ba ku kāsa samun kowace irin baiwar ruhaniya ba, yayin da
kuke zuba ido kuna jiran sāke dawowar Ubangijinmu Yesu
Almasihu. 8 Zai kuma ƙarfafa ku har zuwa ƙarshe, domin ku zama
marasa laifi a ranar da Ubangijinmu Yesu Almasihu zai dawo.
9 Allah mai cika alkawari ne, shi ne kuma ya kira ku ku yi
zumunci tare da Dansa Yesu Almasihu Ubangijinmu.

Rabe-rabe a cikin Jama'ar Masu Bi

10 Ina roƙonku, 'yan'uwa, saboda sunan Ubangijinmu Yesu
Almasihu cewa, bari bakinku yă zama ɗaya. Kada ku zauna a
rabe, sai dai ku haɗa kai, ku zauna da nufi ɗaya, ra'ayinku
kuma ɗaya. 11 Don kuwa, 'yan'uwana, mutanen gidan Kuluwi
sun gaya mini cewa kuna faɗa da junanku. 12 Abin da nake nufi
shi ne, kowannenku yana faɗin abu dabam, wani yana cewa,
"Ni na Bulus ne," wani yana cewa, "Ni na Afolos ne," wani
yana cewa, "Ni na Kefas[a] ne," wani kuma yana cewa, "Ni na
Almasihu ne." 13 Ashe, an raba Almasihu kashi-kashi ne? Bulus
ya mutu a gicciye dominku? Ko kuwa an yi muku baftisma da
sunan Bulus ne?
14 Na gode wa Allah ban yi wa waninku baftisma ba sai
Kiribus da Gayus. 15 Ta haka ba wanda zai iya cewa da sunana
aka yi muku baftisma. 16 Na kuma tuna na yi wa mutanen gidan
Istifanus baftisma, amma ban da waɗannan ban san ko na yi wa

1.2: A.M. 18.1 1.12: A.M. 18.24 1.14: A.M. 18.8; 19.29; Rom 16.23
[a] 1.12 **Kefas**: Wato, Siman Bitrus ke nan.

wani baftisma ba. 17 Ai, Yesu bai aiko ni domin in yi baftisma
ba, sai dai in yi aikin ba da Labari Mai Dadi ba tare da amfani
da hikimar mutum ba, don kada a kāsa ganin darajar mutuwar
Yesu a kan gicciye.

Almasihu Ikon Allah Ne da Hikimarsa

18 Gama saƙon ceto kamar maganar banza ce ga waɗanda
suke hanyar halaka, amma a gare mu, mu da aka cece mu,
maganar ceto ikon Allah ne. 19 Domin an rubuta cewa:

"Zan ɓata hikimar waɗanda
suke tsammani suna da hikima;
Zan kuma rikitar da wayon waɗanda
suke tsammani suna da wayo."

20 To, ina masu hikima? Ina malaman dokoki? Ina waɗanda
suke tsammani sun san kome da kome? Ashe, Allah bai nuna
cewa wayon masu hikimar wannan duniya wawanci ne ba?

21 Gama bisa ga hikimar Allah mutanen duniya ba su san
Allah ta wurin tasu hikimar ba. A maimakon haka, Allah ya zaɓi
yă cece waɗanda suka ba da gaskiya gare shi ta wurin shelar
bisharar da ake gani kamar shirme ne. 22 Yahudawa suna so su
ga alama, Helenawa kuma suna neman hikima. 23 Mu kuwa muna
wa'azin Almasihu wanda ya mutu a kan gicciye ne, abin da ya
zama dalilin tuntuɓe ga Yahudawa, abin da kuma waɗanda ba
Yahudawa ba suke gani kamar wawanci ne. 24 Amma saƙonmu
shi ne, Almasihu ikon Allah da hikimar Allah ne ga waɗanda aka
kira, ko su Yahudawa ne, ko waɗanda ba Yahudawa ba. 25 Domin
abin da ake gani kamar Allah ya yi wawanci ne, ya fi wayon
mutum, abin da kuma ake tsammani kāsawa ce ta Allah, ya fi
duk ƙarfin mutum.

26 'Yan'uwa, ku tuna yadda kuke lokacin da Allah ya kira ku.
Kaɗan daga cikinku ne suke da wayo bisa ga ganin mutum, kaɗan
kuma daga cikinku ne suke rińe da babban matsayi, kuma kaɗan
ne suke 'ya'yan manya. 27 Allah yana zaɓar abin da mutane suke
tsammani wawanci ne, domin yă ba masu hikima irin ta duniya
kunya. Allah yana zaɓar abin da mutane suke gani kamar ya kāsa
ne, domin yă ba mai ƙarfi kunya. 28 Abin da mutane suka ɗauka
ba shi da daraja, ko ba shi da amfani, ko kuma ba kome ba ne,
shi ne abin da Allah yake amfani da shi yă rushe abin da mutane
suke gani kamar yana da muhimminci. 29 Allah ya yi duk wannan

1.16: 1 Kor 16.15 **1.19**: Ish 29.14 **1.20**: Ayu 12.17; Ish 19.12; 33.18; 44.25

domin kada wani ɗan Adam yă ɗaga kansa a gaban Allah. 30 Allah
ne ya sa kuka kasance cikin Almasihu Yesu, Allah ne kuma ya
sa Almasihu ya zama mana hikima. Ta wurinsa ne kuma muka
sami yardar Allah da tsarkakewa, da ceto. 31 Saboda haka, kamar
yadda yake a rubuce, "Duk mai yin ƙama yă yi ƙama cikin
Ubangiji."

Saƙo a kan Almasihu da Aka Gicciye

2 1 'Yan'uwa, sa'ad da na zo in gaya muku asirin[b] da Allah ya
gaya mana, ban gaya muku wannan saƙon ta wurin iya
magana, ko nuna hikima ba. 2 Don na yi niyya a zuciyata cewa,
a lokacin da zan zauna tare da ku ba zan koyar da kome ba sai
zancen Yesu Almasihu, shi wanda aka gicciye. 3 Farkon zuwana
wurinku ba ni da ƙarfi, ina rawar jiki saboda tsoro, 4 jawabina da
wa'azina ba su dogara ga maganar lallashi ko wayo ba, sai dai
sun dogara ne ga shaida ta ikon Ruhu. 5 Kada bangaskiyarku ta
dogara ga hikimar mutane, sai dai ga ikon Allah.

Hikimar Allah

6 Duk da haka muna maganar hikima ga waɗanda suka yi
girma cikin bangaskiyarsu, sai dai ba hikima irin ta wannan
zamanin ba, ba kuwa irin ta masu mulkin zamanin nan waɗanda
suke shuɗewa ba. 7 Amma muna maganar hikimar Allah wacce
take a asirce, da dā a ɓoye take, wato, hikimar Allah da ya shirya
tun kafin farkon zamanai, domin ɗaukakarmu. 8 A cikin masu
mulki na yanzu ba wanda ya gane hikiman nan, domin da a ce
sun gane ta, da ba su gicciye Ubangiji Maɗaukaki ba. 9 Amma
kuwa yadda yake a rubuce ke nan cewa:

"Abin da Allah ya shirya wa masu ƙaunarsa ba wanda ya
taɓa gani,
ba wanda ya taɓa ji,
ba kuma wanda ya taɓa tunani."

10 Amma Allah ya nuna mana waɗannan abubuwa ta wurin Ruhu,
gama Ruhu shi yake bincike kome, har ma abubuwan Allah masu
wuyar ganewa. 11 Wane ne zai iya sanin tunanin da yake zuciyar
wani mutum idan dai ba ruhun mutumin ba? Haka kuwa yake,
ba wanda zai gane tunanin Allah, sai dai Ruhun Allah. 12 Mu
kuwa ba ruhun duniya muka karɓa ba, sai dai Ruhu wanda yake

1.31: Irm 9.24. 2.3: A.M. 18.9 2.9: Ish 64.4

[b] **2.1 asirin**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "shaida" ne a nan.

daga wurin Allah, domin mu gane abubuwan da Allah ya ba mu hannu sake.

13 Muna gaya muku wadannan abubuwa ba da kalmomin da ake koyarwa ta hikimar mutum ba, sai dai ta Ruhu, ta wurin bayyana abubuwan Ruhu ga wadanda suke na Ruhu.[6] 14 Mutumin da ba Ruhu ne yake bi da shi ba, ba ya karba abubuwan Ruhun Allah, don a gare shi wawanci ne, ba kuwa zai iya gane su ba, don ta wurin Ruhu ake ganewa. 15 Mutumin da Ruhu yake bi da shi kuwa, yana iya gwada kome amma ba wanda zai iya gwada shi.

16 "Wa ya san tunanin Ubangiji
har da zai koya masa?"

Amma mu dai tunaninmu na Almasihu ne.

Abokan Aiki na Allah

3 1 'Yan'uwa, ni ban iya yi muku magana kamar wadanda Ruhu yake bi da su ba, sai dai kamar mutanen duniya, kamar jarirai cikin bin Almasihu. 2 Na ciyar da ku da madara, ba da abinci mai tauri ba, don ba ku isa cin abinci mai tauri ba. Har yanzu ma ba ku isa ba, 3 don har yanzu kuna da halin mutuntaka. Idan dai kuna kishi, kuna fada da junanku, ai, har yanzu kuna da halin mutuntaka ke nan, kuna kuma yin ayyuka irin na halin mutum. 4 Don idan wani ya ce, "Ni na Bulus ne," wani kuma ya ce, "Ni na Afolos ne," ashe, ba halin mutum kuke nunawa ba ke nan?

5 Wane ne ma Afolos? Wane ne Bulus? Ashe, ba masu aiki ba ne kawai, wadanda kuka ba da gaskiya ta wurinsu, kowannensu kuwa bisa ga abin da Ubangiji ya ba shi? 6 Ni na shuka, Afolos ya yi ban ruwa, amma Allah ne ya sa shukar ta yi girma. 7 Saboda haka da wanda ya shuka, da wanda ya yi ban ruwan ba a bakin kome suke ba, sai dai Allah kadai shi da ya sa shukar ta yi girma. 8 Da mai shukar, da shi mai ban ruwan nufinsu daya ne, sai dai kowanne zai sami ladansa bisa ga aikinsa. 9 Gama mu abokan aiki na Allah ne, ku kuwa gona ce ta Allah, ginin Allah kuma.

10 Ta wurin alherin da Allah ya ba ni, na kafa tushen gini kamar gwanin gini, wani kuma yana gini a kai. Dole kowane mai gini yă yi lura da irin ginin da zai yi a kai. 11 Gama ba wanda zai iya kafa wani tushe dabam da ya fi wannan da an riga an kafa

---

2.16: Ish 40.13 3.2: Ibr 5.12-13 3.4: 1 Kor 1.12 3.6: A.M. 18.4-11,24-28

[6] **2.13 ga wadanda suke na Ruhu:** Da Helenanci an rubuta "a cikin kalmomin ruhaniya" ne a nan.

wato, Yesu Almasihu. 12 To, idan wani ya yi gini a kan tushen
nan da zinariya, ko da azurfa, ko da duwatsu masu daraja, ko da
itace, ko da ciyawa, ko da kara 13 za a ga aikin kowanne mai gini,
za a tona shi a Ranan nan. Domin da wuta za a nuna aikin kowa,
kuma wutar za ta gwada irin aikin da kowa ya yi. 14 Idan ginin
da aka yi a kan tushen bai ƙone ba, to, wanda ya yi ginin zai
sami lada. 15 Idan kuwa ginin ya ƙone, mai ginin zai yi hasara,
amma zai sami ceto, amma dai kamar ya bi ta cikin wuta ne.

16 Ashe, ba ku san ku haikalin Allah ne ba, kuma Ruhun Allah
yana zaune a cikinku? 17 Duk wanda ya ɓata haikalin Allah, Allah
zai ɓata shi, don haikalin Allah yana da tsarki, kuma ku ne
haikalinsa.

18 Kada kowa yă rudi kansa. Idan wani yana tsammani yana
da wayo a yanzu, sai yă mai da kansa kamar wawa don yă zama
mai wayo. 19 Gama wayon wannan duniya wawanci ne a wurin
Allah, domin a rubuce yake cewa,

"Yakan kama masu wayo a dabararsu."

20 Kuma a rubuce yake cewa, "Ubangiji ya san cewa tunanin masu
hikima banza ne." 21 Don haka kada wani yă yi taƙama da mutum!
Gama kome duka naku ne: 22 ko Bulus, ko Afolos, ko Kefas, ko
duniya, ko rai, ko mutuwa, ko abubuwan yanzu, ko na nan gaba,
ai, duk naku ne, 23 ku kuwa na Almasihu ne, Almasihu kuma na
Allah ne.

Manzannin Almasihu

4 1 Ku ɗauke mu mu masu aikin Almasihu ne, waɗanda Allah
ya ba su amanar gaskiyar asirinsa. 2 A kan haka kuma dole
ne masu rikon amana su zama masu aminci. 3 Amma ƙaramin abu
ne gare ni ku gwada ni, ko kuma a gwada ni bisa ga ganin mutum.
Ba na gwada kaina. 4 Ban sani ko ina da wani laifi ba, amma
hakan bai zama cewa ba ni da laifi ba sam. Ubangiji ne zai gwada
ni. 5 Don haka kada ku yanke wa wani hukunci tun lokaci bai yi
ba, ku jira sai Ubangiji ya dawo. Shi ne zai nuna abubuwan da
suke ɓoye a duhu, yă kuma bayyana nufin zukatan mutane. A
sa'an nan ne kowa zai karɓi yabo daga wurin Allah daidai
gwargwado.

6 To, 'yan'uwa, ga zancen waɗannan abubuwa na mai da su
misali ga kaina da kuma Afolos saboda ku, don ku yi koyi a kan
maganan nan mai cewa, "Kada ku zarce abin da aka rubuta."
Don kada waninku yă yi taƙama da nasa mai koyarwa a kan na

3.16: 1 Kor 6.19; 2 Kor 6.16 **3.19**: Ayu 5.13 **3.20**: Zab 94.11

wani. 7 Wane ne ya ce ka fi sauran? Mene ne kake da shi wanda
ba Allah ne ya ba ka ba? To, in haka ne mene ne ya sa kana ɗaga
kai kamar ba a kyauta ka samu ba?

8 Kun riga kun sami duk abin da kuke so! Kun riga kun zama
masu arziki! Kun zama kamar sarakuna, mu kuwa ba kome ba
ne! Da ma a ce ku sarakuna ne, sai mu yi mulki tare da ku!
9 Gama a ganina, Allah ya nuna a fili cewa mu manzanni mu ne
ƙarshe a kome, kamar waɗanda aka yanke wa hukuncin mutuwa,
don mu mun zama abin da duniya duka, da mala'iku, da mutane
za su sa wa ido. 10 Mun zama wawaye don Almasihu, amma ku
kuna da wayo cikin Almasihu! Ba mu da ƙarfi, amma ku kuna
da ƙarfi! Ana ganinku da mutunci, amma mu ana wulaƙanta mu!
11 A yanzu haka muna jin yunwa da ƙishin ruwa, ba ma sa kayan
kirki, ana dūkanmu, ba mu da gida. 12 Muna famar aiki da kanmu.
Idan aka zage mu, sai mu sa albarka a maimako, idan aka ba mu
wahala sai mu jimre. 13 Idan mutane suka ci mutuncinmu, sai mu
yi musu magana cikin salama. Mun zama kamar mu ne bolar
duniya, abin da kowa yake ƙyama, har wa yau ma, haka yake.

14 Na rubuta muku wannan ba don in sa ku ji kunya ba ne,
sai dai don in yi muku gargaɗi don ku 'ya'yana ne waɗanda nake
ƙauna kuma. 15 Ko da kuna da malamai cikin Almasihu guda dubu
goma, ba ku da ubanni da yawa. Lallai cikin Almasihu Yesu na
zama babanku ta wurin kawo muku Labari Mai Daɗi. 16 Don haka
ina roƙonku ku yi koyi daga wurina. 17 Saboda haka na aika muku
Timoti wanda yake ɗana wanda nake ƙauna, mai aminci kuma
cikin Ubangiji. Zai kuma sa ku tuna da yadda nake bin Almasihu
Yesu, yadda nake koyarwa ko'ina a kowace jama'ar masu bi.

18 Amma waɗansunku sun ɗauka ba zan zo wurinku ba, har
suna ɗaga kai. 19 Amma idan Ubangiji ya yarda zan zo wurinku
ba da daɗewa ba, zan kuma duba in ga wanne iko masu ɗaga
kan nan suke da shi, ba maganganunsu ba. 20 Don mulkin Allah
ba ga maganar baki yake ba, sai dai ga iko. 21 To, me kuka
zaɓa, in zo muku da bulala, ko kuwa in nuna muku ƙauna cikin
saukinkai?

Hukunci don Masu Halin Lalata

5 1 Na ji labari cewa akwai halin lalata a tsakaninku, irin ma
wanda ba a yi ko a cikin waɗanda ba su san Allah ba, har
ma wani yă mai da matar babansa kamar matarsa. 2 Har ma kuna
takama! Ashe, bai kamata ku yi baƙin ciki, ku fitar da wanda ya

4.12: A.M. 18.3 **4.16**: 1 Kor 11.1; Filib 3.17 **5.1**: M. Sh 22.30

yi wannan abin daga cikinku ba? 3 Ko da yake dai ba na tare da ku a jiki, ina tare da ku a ruhu. A cikin sunan Ubangijinmu Yesu na riga na yanke hukunci wa mutumin da ya yi wannan abin kamar ina nan. 4 A sa'ad da kuka taru ruhuna kuma yana nan, da kuma ikon Ubangijinmu Yesu, 5 sai ku ba da mutumin nan ga Shaiɗan, don ko da yake Shaiɗan ya ɓata jikinsa, za a ceci ransa a Ranar Ubangiji.

6 Taƙamar da kuke yi ba abu mai kyau ba ne. Ashe, ba ku sani ba, ɗan yisti kaɗan yake kumburar da duk curin burodi? 7 Ku fitar da tsohon yistin nan, don ku zama sabon curi, don lallai an raba ku da yistin. Haka yake a gare ku an riga an yanka ɗan ragonmu na Bikin Ketarewa, wato, Almasihu. 8 Saboda haka sai mu yi Bikin Ketarewa, ba da burodi mai tsohon yisti ba, ba kuwa tare da yisti na ƙeta da mugunta ba, sai dai da burodi marar yisti, burodi na aminci da gaskiya.

9 Na rubuta muku a cikin wasiƙata cewa kada ku haɗa kai da masu halin lalata. 10 Ba ina nufin masu halin lalata na wannan duniya ba, ko masu kwaɗayi, ko masu sata, ko masu bautar gumaka. Domin idan haka ne dole ku fita daga cikin duniya. 11 Amma ina rubuta muku cewa kada ku haɗa kai da duk wanda ake ce da shi ɗan'uwa mai bi idan yana da halin lalata, ko mai kwaɗayi ne, ko mai bautar gumaka, ko mai zage-zage, ko mashayi, ko mai sata, kada ku ko ci abinci tare da irin waɗannan. 12 Ina ruwana da hukunta waɗanda ba namu ba? Ba waɗanda suke cikin jama'ar masu bi za ku hukunta ba? 13 Allah ne yake hukunta waɗanda ba namu ba. Ku kori mugun nan daga cikinku.

Kada Masu Bi Su Kai Karar Juna

6 1 Idan waninku yana so yă kai ƙarar ɗan'uwansa, ashe, ba rashin kunya ne ba yă kai shi kotu wurin waɗanda ba masu bi ba, a maimakon yă kai shi wurin masu bi? 2 Ashe, ba ku sani ba cewa tsarkaka ne za su yi wa duniya shari'a? Idan kuwa ku ne za ku yi wa duniya shari'a, shi ne ba za ku iya yin shari'a a kan ƙananan abubuwa ba? 3 Ba ku san cewa za mu yi wa mala'iku shari'a ba? Balle abubuwan da suka shafi zaman wannan duniya? 4 Idan kuna da irin waɗannan ƙararrakin, don me kuke kai su wurin waɗanda ba kome ba ne ga jama'ar masu bi? 5 Na faɗa wannan don ku ji kunya. Wato, babu ko mutum ɗaya ke nan mai hikima a cikinku da zai iya shirya tsakanin 'yan'uwa? 6 Amma a

---

5.6: Gal 5.9 **5.7:** Fit 12.5 **5.8:** Fit 13.7; M. Sh 16.3 **5.13:** M. Sh 13.5; 17.7

maimakon haka, ɗan'uwa yakan kai ƙarar ɗan'uwansa a kotu, har ma a gaban waɗanda ba masu bi ba!

7 Karar junanku ma da kuke yi, ai, kāsawa ce a gare ku. Ba gara ku haƙura a cuce ku ba? Ku kuma haƙura ko an hana muku hakkinku? 8 Amma ga shi, ku da kanku kuna cuta, kuna riƙe hakkin juna, har ma 'yan'uwanku ne kuke yi wa!

9 Ashe, ba ku sani ba cewa marasa adalci ba za su shiga mulkin Allah ba? Kada fa a ruɗe ku: ba masu halin lalata, ko masu bautar gumaka, ko masu zina, ko 'yan daudu, ko maza masu kwana da maza, 10 ko ɓarayi, ko masu kwaɗayi, ko mashaya, ko masu zage-zage, ko masu zamba, ba waninsu da zai shiga mulkin Allah. 11 Haka waɗansunku ma suke dā, amma an tsarkake ku, an miƙa ku ga Allah, an kuma mai da ku marasa laifi a gaban Allah cikin sunan Ubangiji Yesu Almasihu, da kuma Ruhun Allahnmu.

Ku Ɗaukaka Allah da Jikinku

12 "An yarda mini in yi kome", amma ba kome ne yake da amfani ba. "An yarda mini in yi kome", amma ba zan zama bawan kome ba. 13 "An yi abinci don ciki ne, ciki kuma don abinci," kuma Allah zai halaka duka biyu. Ba don lalata aka yi jiki ba, sai dai don Ubangiji, Ubangiji kuma don jiki. 14 Allah ya ta da Ubangiji daga matattu, haka mu ma zai ta da mu ta wurin ikonsa.

15 Ashe, ba ku sani ba cewa jikinku gaɓoɓin Almasihu ne? Sam! Ba zan ɗauki gaɓoɓin Almasihu in mai da su gaɓoɓin karuwa ba. 16 Ba ku sani cewa duk wanda ya haɗa jiki da karuwa sun zama jiki ɗaya ke nan ba? Gama an ce, "Su biyun za su zama jiki ɗaya." 17 Amma duk wanda ya haɗa kansa da Ubangiji sun zama ɗaya a ruhu ke nan. 18 Ku guje wa halin lalata! Duk wani zunubin da mutum yake yi bai shafi jikinsa ba, amma mai lalata yana ɓata jikinsa. 19 Ko ba ku sani ba cewa jikinku haikalin Ruhu Mai Tsarki ne wanda yake cikinku, yake kuma daga wurin Allah? Kuma ba ku ne kuke da ikon kanku ba; 20 sayenku aka yi, aka kuwa biya. Saboda haka ku ɗaukaka Allah da jikinku.

6.12: 1 Kor 10.23 **6.16**: Far 2.24 **6.19**: 1 Kor 3.16; 2 Kor 6.16

Damuwa game da Aure

7 [1] To, game da abin da kuka rubuto, yana da kyau mutum yă
zauna ba mata. [2] Amma don a guje wa halin lalata, kowane
mutum yă kasance da matarsa, kuma kowace mace da mijinta.
[3] Miji yă ba matarsa hakkinta na aure, haka kuma matar ga
mijinta. [4] Don matar ba ta da iko da jikinta, sai dai mijin, haka
ma mijin ba shi da iko da jikinsa, sai dai matar. [5] Kada ɗayanku
yă hana wa ɗayan, sai ko kun yarda da haka na ɗan lokaci domin
ku natsu cikin addu'a. Sa'an nan ku sāke haɗuwa, kada Shaiɗan
yă ruɗe ku wajen rashin kamewa.

6 Wannan shawara ce nake ba ku, ba umarni ba. [7] Da ma a ce
kowa kamar ni yake, amma dai kowa yana da baiwar da Allah
ya ba shi, wani yana da irin wannan, wani yana da irin wancan.

8 Game da waɗanda ba su yi aure ba, da waɗanda mazansu
suka mutu, ina gani zai fi kyau su zauna ba aure kamar yadda
nake.

9 Amma idan ba su da kamewa, ya kamata su yi aure. Gama
gara a yi aure da sha'awa ta sha kan mutum.

10 Waɗanda suka yi aure kuma, ina ba ku umarni, ba ni ba
ne, amma Ubangiji, cewa, kada mata ta rabu da mijinta. [11] Idan
kuwa ta rabu da shi, kada ta yi aure, sai dai ta sāke shirya da
mijinta, miji kuma kada yă saki matarsa.

12 Game da sauran kuma, in ji ni, ba in ji Ubangiji ba, idan
wani ɗan'uwa yana da mace marar bi, ta kuma yarda su zauna
tare, to, kada yă rabu da ita. [13] Kuma idan wata mace tana da miji
marar bi, ya kuwa yarda su zauna tare, to, kada ta rabu da shi.
[14] Na ce haka ne, don miji marar ba da gaskiya a tsarkake yake
ta wurin zama ɗaya da matarsa, haka kuwa mace marar ba da
gaskiya a tsarkake take, ta wurin zama ɗaya da mijinta. In ba
haka ba 'ya'yanku ba za su zama da tsarki ba, amma yanzu su
masu tsarki ne. [15] Idan kuwa marar bin yana so yă rabu da mai
bin, to, sai su rabu. A wannan hali, ɗan'uwa ko 'yar'uwa mai bi
babu dole a kansu, don Allah ya kira mu ga zaman lafiya ne.
[16] Ke mata, kin sani ko za ki ceci mijinki? Kai miji, ka sani ko
za ka ceci matarka?

Irin Zaman da Ubangiji Yake So a Yi

17 Sai dai a cikin kowane hali, kowa yă yi zama irin wanda
Ubangiji yake so yă yi. Umarnin da nake ba dukan jama'un masu

---

7.10-11: Mat 5.32; 19.9; Mar 10.11-12; Luk 16.18

bi ke nan. 18 Duk wanda Allah ya kira, wanda dā ma yana da
kaciya, to, kada yă nemi yă zama marar kaciya. Wanda kuma
Allah ya kira, wanda dā ma ba shi da kaciya, to, kada yă ce sai
an yi masa kaciya. 19 Kaciya, ko rashin kaciya, ba kome ba ne,
amma yin biyayya da dokokin Allah shi ne da muhimminci.
20 Kowa yă kasance yadda yake sa'ad da aka kira shi. 21 Idan kai
bawa ne lokacin da aka kira ka, kada ka damu. Idan kuwa za ka
iya samun 'yanci, sai ka yi amfani da wannan damar. 22 Duk
wanda yake shi bawa ne, kuma aka kira shi zuwa wurin Ubangiji,
shi ba bawa ba ne kuma, shi na Ubangiji ne. Haka kuma bawan
da Ubangiji ya ba shi 'yanci ya zama bawan Almasihu. 23 Sayenku
aka yi, aka kuwa biya, kada ku zama bayin mutane. 24 To,
'yan'uwa, duk halin da mutum yake ciki lokacin da aka kira shi,
sai yă zauna haka tare da Allah.

Marasa Aure da Waɗanda Mazansu Suka Mutu

25 Game da matan da ba su yi aure ba kuwa, Ubangiji bai ba
ni umarni ba, amma ina ba da ra'ayina ne a kan cewa ni wanda
aka amince da shi ne, bisa ga jinkan Ubangiji. 26 Ina gani zai fi
kyau mutum yă zauna yadda yake saboda an fara shiga lokacin
wahala. 27 Idan ka yi aure, kada ka kashe auren. Idan ba ka riga
ka yi aure ba, kada ka yi aure. 28 Amma idan ka riga ka yi aure,
ba laifi, ba zunubi ba ne, kuma idan yarinya[c] ta yi aure, ba zunubi
ba ne. Duk da haka waɗanda suka yi aure za su sha wahala saboda
zaman iyali, kuma ina so in tsare ku daga haka.

29 Abin da nake nufi 'yan'uwa, shi ne lokacin da aka shirya
ya kusa ƙarewa. Daga yanzu, masu aure su zama kamar ba su da
aure. 30 Waɗanda suke bakin ciki su zama kamar ba sa bakin ciki,
waɗanda suke murna su zama kamar ba sa murna, kuma masu
sayan kaya su zama kamar ba su da kome, 31 masu more kayan
duniya kuma kada su dogara gare su, don yanayin wannan duniya
mai wucewa ne.

32 Ina so ku daina damuwa. Wanda bai yi aure ba yakan damu
da sha'anin Ubangiji sosai, yadda zai sa Ubangiji yă ji daɗi.
33 Amma wanda yake da aure yakan damu da abubuwan duniya,
yadda zai sa matarsa ta ji daɗi. 34 Hankalinsa ya rabu biyu ke nan.
Kuma mace marar aure, ko yarinya, takan damu da sha'anin
Ubangiji sosai don ta zama mai tsarki a cikin jiki da ruhu. Mace
mai aure kuwa takan damu da abubuwan duniya, yadda za ta sa

[c] **7.28 yarinya:** Da Helenanci an rubuta "budurwa" ne nan.

mijinta yă ji dadi. 35 Na fada haka don amfaninku ne, ba don in
matsa muku ba, sai dai don zamanku yă yi kyau, don ku bauta
wa Ubangiji ba tare da wani abu ya hana ku ba.

36 Amma a ce mutum ya yi alkawari da wata da ta isa aure,
kuma yana tsammani yana yin abin da bai dace ba gare ta, sa'an
nan yana sha'awarta sosai (haka kuwa ya kamata yă zama), idan
haka ne, to, su yi aure, ba laifi ba ne. 37 Amma mutumin da ya
tsaya sosai a kan shawarar zuciyarsa, abin kuwa ba dole ba ne
gare shi, kuma yana iya kame kansa, har kuma ya ɗauka a ransa
ba zai aure ta ba, to, wannan ma daidai ne. 38 Saboda haka wanda
ya auri yarinyar da ya yi alkawari da ita, ya yi daidai. Shi kuwa
da bai aure ta ba ma ya fi.[d]

39 Mace ba za ta rabu da mijinta ba in dai yana da rai, amma
idan ya mutu, tana iya auren wani da ranta yake so, amma fa mai
bin Ubangiji . 40 Amma a nawa ra'ayin, za ta fi jin dadi idan ta
zauna yadda take. A ganina kuwa ina da Ruhun Allah.

Abincin da Aka Miƙa wa Gumaka

8 1 To, game da abincin da aka miƙa wa gumaka, mun sani
dukanmu muna da ilimi. Ilimi yakan kawo ɗaga kai, amma
ƙauna, tana ginawa. 2 Duk wanda yake gani kamar ya san wani
abu, to, har yanzu bai san abin da ya kamata yă sani ba. 3 Amma
duk wanda yake ƙaunar Allah, Allah ya san da shi.

4 Game da cin abincin da aka miƙa wa gumaka kuwa, mun
sani cewa, a duk duniyan nan, gunki ba a bakin kome yake ba,
mun kuma san cewa Allah ɗaya ne, babu wani. 5 Ko da yake wai
akwai wadanda ake ce da su "alloli" a sama ko a ƙasa, don kuwa
akwai alloli da iyayengiji da yawa, 6 duk da haka, mu dai a gare
mu kam, Allah ɗaya ne. Wato, Uba wanda dukan abubuwa suke
daga gare shi, wanda kuma muke rayuwa dominsa, Ubangiji kuma
ɗaya ne, Yesu Almasihu, wanda ta wurinsa ne dukan abubuwa
suka fito, mu kuma ta wurinsa ne muka kasance.

7 Amma dai ba kowa ne ya san wannan ba, tun da har yanzu
wadansu da sun saba da bautar gumaka sukan yi tsammani cewa

[d] **7.36-38** Wata fassara ta wadannan ayoyi ita ce: 36 "Idan uban 'ya budurwa da
ta wuce lokacin aure ya ga ba ya bi da ita yadda ya kamata, ya kuma ga cewa
ya kamata ta yi aure, to, yă yi yadda ya dace. Wannan ba laifi ba ne. Yă bar
ta ta yi aure. 37 Amma idan mutumin nan ya ɗauki niyya a zuciyarsa, abin
kuwa ba dole ba ne a gare shi, amma yana da iko bisa nufin kansa, ya kuwa
riga ya yi niyya a zuciyarsa cewa zai tsare ta, to, haka daidai ne. 38 Saboda
haka wanda ya yi wa 'ya budurwarsa aure, ya yi daidai, amma wanda bai
aurar da ita ba ya yi abu mafi kyau."

abincin da suke ci na gumaka ne. Yana da wuya su gane abin da yake mai kyau da abin da yake mummuna. Saboda haka sai su damu. 8 Abinci ba zai kawo mu kusa da Allah ba. In ba mu ci ba, ba za mu ragu ba, kuma in mun ci, ba za mu ƙaru ba.

9 Amma ku yi hankali kada wannan 'yancin yă zama dalilin yin zunubi ga waɗanda ba su da ƙarfi. 10 Don idan waɗanda suka gan ka, kai da kake da ganewa, kana cin abinci a haikalin gumaka, ashe, wannan ba zai zuga su har su ma su ci abincin da aka miƙa wa gumaka ba, tun da yake ba su da ƙarfi? 11 Ta haka sanin nan naka zai zama dalilin fāɗuwar wani ɗan'uwa wanda Almasihu ya mutu dominsa. 12 Ta wurin yi wa 'yan'uwanku laifi ne kuke yi wa Almasihu laifi, kuna sa musu damuwa saboda ba su san abin da yake mai kyau da abin da yake mummuna ba. 13 Saboda haka idan cin abinci yana sa ɗan'uwana yă yi zunubi, ba zan taɓa cin nama ba don kada in sa ɗan'uwana yă yi zunubi.

Hakki da Aikin Manzo

9 1 Ni ba ni da 'yanci ne? Ni ba manzo ba ne? Ban ga Yesu Ubangijinmu ba? Ku ba sakamakon aikina ba ne a cikin Ubangiji? 2 Idan ni ba manzo ga kowa ba, ni manzo ne gare ku don kuwa ku ne tabbaci cewa ni manzo ne a gaban Ubangiji.

3 Da wannan nake kāre kaina a gaban waɗanda suke so su bincike ni. 4 Ashe, ba mu da iko a ba mu ci da sha? 5 Ba mu da 'yancin tafiya da matarmu ta aure mai bi, kamar yadda sauran manzanni, da 'yan'uwan Ubangiji, da kuma Kefas suke yi? 6 Ko kuwa dai ni da Barnaba ne kawai ya zama dole mu yi aikin ciyar da kanmu? 7 Wane ne yake aikin soja sa'an nan yă ciyar da kansa? Wane ne zai yi noma gonar inabi, yă kāsa cin 'ya'yan? Wane ne zai yi kiwon garke, yă kāsa shan nonon?

8 Ina faɗin haka bisa ga ra'ayin mutum ne? Ba Doka ma ta faɗa haka ba? 9 Don an rubuta a Dokar Musa cewa, "Kada ka rufe wa saniyar noma baki a lokacin da take aikin sussuka." Shanu ne kawai Allah yake kula da su? 10 Ba musamman saboda mu yake magana ba? Lallai, saboda mu ne aka rubuta, don ya kamata mai noma da mai sussuka su sa zuciyar samun rabonsu daga amfanin gona. 11 Idan mun shuka iri na ruhu a zuciyarku, to, wani babban abu ne idan mun girbe amfaninku iri na duniya? 12 Har idan waɗansu suna da damar yin haka, ashe, ba mu fi su damar yin haka ba?

9.9: M. Sh 25.4; 1 Tim 5.18 **9.11**: Rom 15.27

Duk da haka, ba mu yi amfani da wannan damar ba, amma
mun jimre da kome a maimakon kawo abin da zai hana aikin
Labari Mai Dadi na Almasihu. 13 Ashe, ba ku sani ba masu aiki
a haikali daga wurin suke samun abincinsu? Masu aiki a bagade
kuma, a nan suke samun rabo daga abin da aka miƙa hadaya?
14 Haka yake kuma, Ubangiji ya yi umarni cewa masu aikin
bishara su sami abin zaman gari ta wurin aikin bishara.

15 Amma ban yi amfani da ko ɗaya daga cikin waɗannan
'yancin ba, kuma ba ina rubuta wannan don a yi mini haka ba
ne. Ai, gara in mutu, da a hana ni taƙama da wannan. 16 Don ina
aikin bishara, wannan bai zama mini dalilin yin taƙama ba, don
dole ne in yi aikin. Kaitona kuma idan na ƙi yin aikin bishara.
17 Da don ganin damata nake yi, da sai an ba ni lada. Amma da
yake ba don ganin dama nake yi ba, an ba ni amana ke nan. 18 To,
mene ne ladana? Ladana shi ne, idan zan yi wa'azin Labari Mai
Dadi, in yi ta kyauta. Ba na amfani da cikakken 'yancina duka
cikin aikina na bishara.

19 Ko da yake ni ba bawan kowa ba ne, na mai da kaina bawan
kowa, domin in jawo mutane masu yawa. 20 Ga Yahudawa, sai
na zama kamar Bayahude don in jawo Yahudawa. Ga waɗanda
Doka take iko a kansu, sai na zama kamar wanda Doka take iko
a kansa (ko da yake ba Doka take iko a kaina ba), domin in jawo
waɗanda Doka take iko a kansu. 21 Ga waɗanda ba sa ƙarƙashin
Doka kuwa, sai na zama kamar wanda ba ya ƙarƙashin Doka (ba
wai cewa ba wata dokar Allah da take iko a kaina ba, a'a, ina
ƙarƙashin dokar Almasihu), don in jawo waɗanda ba sa ƙarƙashin
Doka. 22 Ga marasa ƙarfi cikin bangaskiya, sai na zama kamar
marar ƙarfi don in jawo su. Na zama kowane irin abu ga ko
waɗanne irin mutane domin ko ta yaya in cece waɗansu. 23 Duk
ina yin haka ne saboda bishara, don in sami rabona a cikin
albarkar bishara.

24 Ashe, ba ku sani ba, a wajen gasar gudu, dukan masu gudu
sukan yi ƙoƙari wuce juna, amma ɗaya ne kaɗai yake samun
kyautar? To, sai ku yi ta gudu yadda za ku yi nasara. 25 'Yan
wasa sukan hori kansu a cikin kome, suna yin haka ne don su
samu ladan da yake lalacewa, amma mu kuwa ladanmu marar
lalacewa ne. 26 Saboda haka guduna ba na banza ba ne, dambena
kuwa ba iska nake bugu ba. 27 Amma ina horon jikina, na mai da

9.13: M. Sh 18.1 **9.14:** Mat 10.10; Luk 10.7

shi bawana, don kada bayan da na yi wa wadansu wa'azi ni kaina a yashe ni.

Gargadi daga Tarihin Isra'ilawa

10 1 To, ina so ku sani 'yan'uwa, cewa kakanninmu duka sun
yi tafiya a karkashin girgije, dukansu kuma sun ketare ta
cikin jan teku. 2 A cikin girgijen da kuma cikin tekun aka yi wa
dukansu baftisma ga bin Musa. 3 Dukansu kuwa suka ci abincin
nan na ruhu,[d] 4 duka kuwa suka sha ruwan nan na ruhu.[e] Gama
sun sha ruwa daga Dutsen nan na ruhu, wanda ya yi tafiya da su.
Dutsen nan kuwa Almasihu ne. 5 Duk da haka Allah bai ji dadin
yawancinsu ba, har aka kakkashe su a daji.

6 To, wadannan abubuwa sun zama mana misali ne don kada
mu so mugayen abubuwa yadda suka yi. 7 Kada ku zama masu
bautar gumaka yadda wadansunsu suka zama. Kamar yadda yake
a rubuce cewa, "Mutanen sun zauna, suka ci, suka sha, kuma
suka tashi suka yi rawa." 8 Kada fa mu shiga halin lalata yadda
wadansunsu suka yi, har mutum dubu ashirin da uku suka mutu
a rana daya. 9 Kada mu gwada Ubangiji[f] yadda wadansunsu suka
yi, har macizai suka kakkashe su. 10 Kada mu yi gunaguni yadda
wadansunsu suka yi, har Mala'ika Mai Halakarwa ya halaka su.

11 Wadannan abubuwan da suka faru da su misali ne, an
kuma rubuta ne don a yi mana gargadi, mu da karshen zamani
ya same mu.

12 Saboda haka idan kana tsammani kana tsaye daram, to, sai
ka yi hankali kada ka fadi. 13 Ba wani gwajin da ya taba samunku,
wanda ba a saba yi wa mutum ba. Allah mai aminci ne, ba zai
bari a gwada ku fiye da karfinku ba, amma game da gwajin, zai
bude hanya yadda za ku iya jimrewa.

14 Saboda haka ku da nake kauna, ku guje wa bautar gumaka.
15 Ina magana da ku a kan ku masu hankali ne, ku duba da kanku
ku ga abin da nake fada. 16 Kwaf din nan na albarka[g] da muke
godiya a kai, ashe, ba shi ne yake sa mu mu zama daya cikin

10.1: Fit 13.21-22; 14.22-29 **10.3**: Fit 16.35 **10.4**: Fit 17.6; L. Kid 20.11
10.5: L. Kid 14.29-30 **10.6**: L. Kid 11.4 **10.7**: Fit 32.6 **10.8**: L. Kid 25.1-18
10.9: L. Kid 21.5-6 **10.10**: L. Kid 17.6-14

[d] **10.3 abincin nan na ruhu**: Wato, "Manna" (Dubi Fit. 16.2-36).

[e] **10.4 ruwan nan na ruhu**: Wato, Ruwa daga dutse wanda Allah ya ba wa Isra'ilawa (Dubi Fit 17.1-7).

[f] **10.9 Ubangiji**: Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Almasihu" ne a nan.

[g] **10.16 Kwaf din nan na albarka**: Da Helenanci an rubuta, "kwaf din nan na godiya" ne a nan.

jinin Almasihu ba? Burodin da muke gutsurawa kuma ba shi ne yake sa mu mu zama ɗaya cikin jikin Almasihu ba? 17 Da yake burodin nan ɗaya ne, ashe, mu da muke da yawa jiki ɗaya ne, gama dukanmu burodi ɗaya muke ci. 18 Ku dubi mutanen Isra'ila. Ashe, waɗanda suke ci daga hadayu, ba ɗaya suke da juna cikin cin hadayun da aka miƙa wa Allah a bagaden hadaya ba? 19 Mene ne nake nufi a nan? Abin da aka yanka wa gumaka ne ainihin wani abu? Ko kuwa gunkin ne wani abu? 20 A'a, ina nufin cewa, abin da masu bautar gumaka suke yankawa, suna yanka wa aljanu ne, ba Allah ba. Ba na so fa ku zama ɗaya da aljanu. 21 Ba dama ku sha a kwaf na Ubangiji, ku kuma sha a na aljanu. Ba dama ku ci abinci a teburin Ubangiji, ku kuma ci a na aljanu. 22 Ko muna tsokanar Ubangiji yă ji kishi ne? Mun fi shi ƙarfi ne?

Yi Kome don Ɗaukaka Allah

23 "Dukan abubuwa an yarda mana," amma ba dukan abubuwa ne suke da amfani ba. "Dukan abubuwa an yarda mana," amma ba dukan abubuwa ne suke ginawa ba. 24 Kada ka kula da kanka kawai, amma ka kula da ɗan'uwanka kuma. 25 Ku ci duk irin abin da ake sayarwa a wurin sayar da nama, ba sai kun tambaya ba, saboda kada zuciyarku ta damu da inda naman ya fito. 26 Gama Maganar Allah ta ce, "Duniya da abin da yake cikinta duk na Ubangiji ne." 27 Idan wani marar bi ya kira ku cin abinci, kuka yarda ku je, sai ku ci duk irin abin da aka ba ku, ba sai kun tambaya ba, saboda kada zuciyarku ta damu da inda abincin ya fito. 28 Amma idan kuwa wani ya ce muku, "An yanka wannan saboda gunki ne fa," to, kada ku ci, saboda duban mutuncin wannan mai gaya muku, don kuma tunaninku yă kasance babu laifi. 29 Ina nufin tunanin zuciyarsa, ba naku ba. To, waninku yana iya cewa "Don me fa tunanin zuciyar wani zai hana 'yancina? 30 Idan na ci abinci da godiya, don me za a zarge ni a kan abin da na ci da godiya ga Allah?"

31 To, duk abin da kuke yi, ko kuke ci, ko kuke sha, ku yi kome saboda ɗaukakar Allah. 32 Kada ku zama dalilin yin zunubi ga Yahudawa, ko waɗanda ba Yahudawa ba, ko jama'ar masu bin Allah. 33 Ku yi kamar dai yadda nake yi. Ina ƙoƙari in sa kowa yă ji daɗi cikin duk abin da nake yi, ba don kaina kaɗai nake yi ba, sai dai don amfanin mutane da yawa, don su sami ceto.

10.16: Mat 26.26-28; Mar 14.22-24; Luk 22.19-20 **10.18:** L. Fir 7.6
10.20: M. Sh 32.17 **10.22:** M. Sh 32.21 **10.23:** 1 Kor 6.12 **10.26:** Zab 24.1

11 [1] Ku bi misalina kamar yadda nake bin misalin Almasihu.

Koyarwa game da Rufin Kai

2 Ina yabe ku ne don kuna tunawa da ni cikin kome, kuna
kuma riƙe koyarwan[h] nan sosai, daidai yadda na ba ku. [3] Amma
ina so ku gane cewa, Almasihu ne shugaban kowane mutum,
miji kuma shi ne shugaban matarsa, Allah ne kuma shugaban
Almasihu. [4] Duk namijin da ya yi addu'a ko annabci da kansa
a rufe ya yi banza da shugabansa.[i] [5] Amma duk macen da ta
yi addu'a ko annabci da ba ta ɗaura ɗankwali a kanta ba, ta yi
banza da shugabanta ke nan, kuma daidai ne da a ce ta aske
kanta. [6] Idan mace ta ƙi ɗaura ɗankwali, to, sai ta aske kanta,
amma da yake abin kunya ne mace ta aske kanta, to, sai ta
ɗaura ɗankwali. [7] Namiji kam bai kamata yă rufe kansa ba, don
yana nuna kamanni da ɗaukakar Allah ne. Amma mace tana
nuna ɗaukakar namiji ne. [8] Ai, namiji ba daga jikin mace yake
ba, amma mace daga jikin namiji take. [9] Ba a kuma yi namiji
don mace ba, sai dai mace don namiji. [10] Saboda haka dole
mace ta ɗaura ɗankwali, wato, alamar iko ke nan, saboda
mala'iku. [11] Duk da haka, a cikin Ubangiji, mace ba a rabe take
da namiji ba, namiji kuma ba a rabe yake da mace ba. [12] Wato,
kamar yadda mace take daga namiji, haka ma mace ce ta haifi
namiji, amma kome daga wurin Allah yake. [13] Ku duba ku gani
da kanku, ya yi kyau mace ta yi addu'a ga Allah da kanta a
buɗe? [14] Ai, hali ma ya koya muku cewa idan namiji ya bar
gashinsa bai aske ba, abin kunya ne. [15] Idan kuwa mace tana
da dogon gashi, daraja ce a gare ta; gama an yi mata gashi don
rufe kanta ne. [16] Idan kuwa wani yana so yă yi gardama a kan
wannan, mu dai ba mu san wata al'ada ba, haka kuma sauran
jama'un masu bin Allah.

Wulaƙanci wajen Cin Jibin Ubangiji

17 Game da umarnin nan kuwa, ban yabe ku ba don
taruwarku ba ta kirki ba ce, ta rashin kunya ce. [18] To, da farko
dai sa'ad da kuka taru, taruwa irin ta jama'ar masu bi, na ji
cewa akwai rabe-rabe a cikinku, har na ɗan yarda da zancen.
[19] Lallai ne a samu rabuwa a cikinku don a iya gane waɗanda
suke masu aminci a cikinku. [20] Ashe kuwa, in kuka taru ba don

11.1: 1 Kor 4.16; Filib 3.17 11.7: Far 1.26-27 11.8-9: Far 2.18-23

[h] **11:2 koyarwa:** Da Helenanci an rubuta, "al'adu" ne a nan.

[i] **11.4 shugabansa:** Wato, Almasihu ke nan.

ku ci jibin Ubangiji ba ne. 21 Domin a wajen cin abinci, kowa
yakan mai da hankali yă yi ta cin abincinsa, har a bar wani
yana jin yunwa, wani kuwa yă sha har yă bugu. 22 Ba ku da
gidajen da za ku zauna ku ci ku sha a ciki ne? Ko kuwa kun
rena jama'ar masu bin Allah ne, kuna kuma wulaƙanta waɗanda
ba su da kome? To, me zan ce muku, in yabe ku saboda wannan
ne? Sam! Ba zan yabe ku ba.

Kafawar Cin Jibin Ubangiji
(Mat 26.26-29, Mar 14.22-25, Luk 22.14-20)

23 Abin nan kuwa da na ba ku, na karɓa ne daga wurin
Ubangiji, cewa, Ubangiji Yesu, a daren da aka bashe shi, ya
ɗauki burodi, 24 bayan ya yi godiya ga Allah, sai ya kakkarya,
ya ce, "Wannan jikina ne, wanda aka bayar saboda ku. Ku riƙa
yin haka don tunawa da ni." 25 Haka kuma bayan jibin, sai ya
ɗauki kwaf ya ce, "Kwaf ɗin nan na sabon alkawari ne, na
jinina. Ku yi haka duk lokacin da kuke sha, don tunawa da ni."
26 Wato, duk lokacin da kuke cin burodin nan, kuke kuma sha
a kwaf ɗin nan, kuna shelar mutuwar Ubangiji ke nan, har yă
dawo.

Cin Jibin Ubangiji da Rashin Cancanta

27 Saboda haka duk wanda ya ci burodin nan, ko ya sha
kwaf ɗin nan na Ubangiji da rashin cancanta, ya yi zunubi wa
jiki da jinin Ubangiji ke nan. 28 Sai dai kowa yă bincike kansa,
sa'an nan yă ci burodin yă kuma sha kwaf ɗin. 29 Duk wanda
ya ci burodin, ya sha kwaf ɗin ba tare da ya tabbatar da
matsayin jikin Ubangiji ba, ya jawo wa kansa hukunci ke nan
ta ci da sha da ya yi. 30 Shi ya sa da yawanku suke da rashin
ƙarfi, da rashin lafiya, waɗansu ma sun yi barci wato, sun mutu.
31 Amma idan muka bincika kanmu tukuna, ba za a hukunta mu
ba. 32 Idan kuwa Ubangiji ne yake hukunta mu, muna samun
horo ke nan don kada a yanke mana hukunci tare da duniya.

33 Saboda haka, 'yan'uwana, idan kuka taru don cin abinci,
sai ku jira juna. 34 Idan kuwa wani yana jin yunwa, sai yă ci abinci
a gida, kada yă zama cewa taronku ya jawo muku hukunci. Game
da sauran abubuwa kuma, idan na zo zan ba da umarni.

11.25: Fit 24.6-8; Irm 31.31-34

Baye-baye na Ruhu Mai Tsarki

12 [1] To, yanzu kuma, 'yan'uwana, game da baye-baye na Ruhu Mai Tsarki, ba na so ku kasance da rashin sani. [2] Kun san a lokacin da kuke ba masu bi ba, an ruɗe ku, kuka shiga bautar gumakan nan da ba su da rai. [3] Don haka ina so ku gane cewa, ba wanda Ruhun Allah yake bishe shi da zai taɓa cewa, "Yesu la'ananne ne!" Kuma ba wanda zai iya cewa, "Yesu Ubangiji ne," sai wanda Ruhu Mai Tsarki yake bi da shi.

4 To, akwai baiwa iri-iri, amma Ruhu ɗaya ne yake ba da su. [5] Akwai hanyoyi dabam-dabam na yin hidima, amma Ubangiji ɗaya ake yi wa. [6] Akwai ayyuka iri-iri, amma Allah ɗaya ne yake ba kowa ikon yinsu duka. [7] Allah yana ba wa kowane mutum alamar kasancewar Ruhu Mai Tsarki, don amfani kowa. [8] Wani an ba shi baiwar koyar da hikima ta wurin Ruhu Mai Tsarki, wani kuma an yi masa baiwar koyar da sani ta wurin wannan Ruhun. [9] Wani kuma an yi masa baiwar bangaskiya ta wurin Ruhun nan, wani kuma baiwar warkarwa ta wurin Ruhun nan. [10] Wani kuma baiwar yin abubuwan ban mamaki, wani kuma annabci, wani kuma iya bambanta tsakanin ruhohi, wani kuma iya magana da harsuna dabam-dabam, wani kuma iya fassara harsuna. [11] Dukan waɗannan Ruhu ɗaya ne yake yinsu, yake kuma rarraba wa kowa yadda yake so.

Dukanmu Gaɓoɓin Jiki Ɗaya Ne

12 Gama kamar yadda jiki yake guda, yake kuma da gaɓoɓi da yawa; ko da yake gaɓoɓin suna da yawa, su jiki ɗaya ne. To, haka yake ga Almasihu. [13] Don dukanmu an yi mana baftisma ta wurin Ruhu guda zuwa cikin jiki ɗaya, ko Yahudawa ne ko waɗanda ba Yahudawa ba, ko bayi ne ko 'ya'ya dukanmu kuwa an sa muka sha daga Ruhu guda.

14 Jiki ba gaɓa ɗaya ba ne, gaɓoɓi ne da yawa. [15] Da ƙafa za ta ce, "Don ni ba hannu ba ce, ai, ni ba gaɓar jiki ba ce." Wannan ba zai hana ta ta zama gaɓar jiki ba. [16] Haka kuma idan kunne ya ce, "Ni ba ido ba ne, don haka ni ba gaɓar jiki ba ne," wannan ba zai hana shi yă zama gaɓar jiki ba. [17] Da dukan jiki ido ne, da me za a ji? Da dukan jiki kunne ne, da me za a sansana? [18] Amma ga shi Allah ya shirya kowacce gaɓa a jiki yadda ya zaɓa. [19] Da dukan jikin gaɓa ɗaya ne, da ina sauran jikin? [20] Amma ga shi kuwa akwai gaɓoɓi da yawa, jiki kuwa ɗaya ne. [21] Ba dama ido yă ce wa hannu,

---

12.4-11: Rom 12.6-8 12.12: Rom 12.4-5

"Ba ruwana da kai," ko kuwa, kai yă ce wa ƙafafu, "Ba ruwana da ku." 22 Ba haka ba ma, sai ma gaɓoɓin da ake gani kamar ba su da ƙarfi, su ne masu muhimminci. 23 Gaɓoɓin jiki kuma da ake ganin kamar ba su kai sauran daraja ba, mukan fi ɗaukaka su. Ta haka gaɓoɓinmu da ba su da kyan gani, a kan ƙara kyansu. 24 Gaɓoɓinmu masu kyan gani kuwa ba sai an yi musu kome ba. Amma Allah ya shirya jiki, ya mai da gaɓa da ba ta da daraja ta zama da muhimminci, 25 don kada rashin haɗa kai yă kasance a jiki, sai dai gaɓoɓi su kula da junansu, kula ta iri ɗaya. 26 Don haka idan wata gaɓa ta ji ciwo, duk sai su ji zafi tare, idan kuwa an yabi wata gaɓa, sai duka su yi murna tare.

27 To, ku jikin Almasihu ne, kowannenku kuwa gaɓarsa ne. 28 A cikin jama'ar masu bi, Allah ya ba manzanni wuri na farko, ya ba annabawa wuri na biyu, ya ba masu koyarwa wuri na uku, sai masu yin ayyukan ban mamaki, sai masu baiwar warkarwa, da masu taimako, da masu kula da aikin jama'ar masu bi, da kuma masu magana da harsuna iri-iri. 29 Dukansu manzanni ne? Dukansu annabawa ne? Dukansu masu koyarwa ne? Ko dukansu masu yin abubuwan ban mamaki ne? 30 Duka ne suke da baiwar warkarwa? Duka ne suke magana da harsuna? Ko kuwa duka ne suke fassara? 31 Amma ku yi marmarin baye-bayen da suka fi girma. Zan kuma nuna muku hanyar da ta fi kyau.

Kauna

13 1 Ko da na iya yin magana da harsunan mutane da na mala'iku, amma in ba ni da ƙauna, na zama kamar ƙararrawa mai yawan ƙara ne kawai, ko ganga mai yawan ƙara. 2 Ko da ina yin annabci, ina kuma gane dukan asirai, ina kuma da dukan ilimi, ko da kuma ina da bangaskiya sosai, har yadda zan iya matsar da duwatsu, amma in dai ba ni da ƙauna, to, ni ba kome ba ne. 3 Ko da zan bayar da duk abin da nake da shi, in kuma ba da jikina a ƙone, to, idan ba ni da ƙauna, ai, ba ni da ribar kome.

4 Kauna takan sa haƙuri da kirki, ƙauna ba ta kishi, ba ta taƙama, ko girmankai, 5 ko ɗaga kai, ko ƙin kula da yadda waɗansu za su ji, ko sonkai; ba ta son tsokana, ba ta riƙe laifi a zuciya. 6 Kauna ba ta jin daɗin mugunta, amma takan ji daɗin gaskiya. 7 Kauna takan sa haƙuri cikin kowane hali, da bangaskiya cikin kowane hali, da sa zuciya cikin kowane hali, da kuma jimiri cikin kowane hali.

12.28: Afi 4.11 13.2: Mat 17.20; 21.21; Mar 11.23

8 Kauna ba ta ƙarewa har abada. Annabci dai zai shuɗe,
harsuna kuma za su ɓace, ilimi kuma zai ƙare. 9 Hakika, iliminmu
ba cikakke ba ne, annabcinmu ma ba cikakke ba ne. 10 Sa'ad da
kuwa cikakken ya zo, sai wanda ba cikakken ba yă shuɗe. 11 Da
nake yaro, nakan yi magana irin ta yara, nakan yi tunani irin na
yara, nakan ba da dalilai irin na yara. Da na yi girma kuwa sai
na bar halin yarantaka. 12 Don yanzu kam muna gani kamanni ne
a madubi duhu-duhu, a ranan nan za mu gani fuska da fuska.
Yanzu sanina ba cikakke ba ne, a ranan nan kuwa zan gane daidai
yadda Allah ya gane ni. 13 To, yanzu abubuwan nan uku sun
tabbata, wato, bangaskiya, da sa zuciya, da kuma ƙauna, amma
mafi girma duka a cikinsu ita ce ƙauna.

Baye-bayen Harsuna da Annabci

14 1 Ku nace ku nemi ƙauna, ku kuma yi marmarin
baye-baye na Ruhu Mai Tsarki, musamman na yin
annabci. 2 Don mai magana da harsuna ba mutane yake wa
magana ba, da Allah yake magana, don ba wanda yake gane abin
da yake faɗa, saboda yana faɗin abubuwan asiri ta wurin ikon
Ruhu ne. 3 Amma wanda yake annabci yana wa mutane magana
ne don gina su, da ƙarfafa su, da yin musu ta'aziyya. 4 Mai
magana da harsuna yana gina kansa ne, amma mai annabci yana
gina jama'ar masu bi ne. 5 To, ina so dukanku ku yi magana da
harsuna, amma na fi so ku yi annabci. Wanda yake yin annabci
ya fi wanda yake magana da harsuna, sai dai in wani ya yi fassara
don jama'ar masu bi ta ginu.

6 To, 'yan'uwa, idan na zo ina yi muku magana da harsuna,
amfanin me zan yi muku, in ba na zo muku da wani bayani, ko
ilimi, ko annabci, ko koyarwar maganar Allah ba? 7 Daidai ne
da yadda abubuwa marasa rai suke, kamar su busa da molo, idan
muryarsu ba ta fita sosai ba, yaya wani zai san abin da ake
kaɗawa ko busawa? 8 Idan ba a busa ƙaho daidai yadda za a
gane ba, wa zai yi shirin yaƙi? 9 Haka kuma yake gare ku, in
kuka yi magana da wani harshe wanda ba a gane ba, yaya za a
san abin da kuke faɗa? Kun yi magana a banza ke nan. 10 Akwai
harsuna iri-iri a duniya, kowanne kuwa yana da ma'ana. 11 Idan
kuwa ba na gane harshen, sai in zama baƙo ga mai maganar,
mai maganar kuma yă zama baƙo gare ni. 12 Haka kuma yake
gare ku. Tun da yake kuna marmarin samun baye-baye na Ruhu,
sai ku yi ƙoƙari ku ba da ƙarfinku ga yin amfani da waɗanda
za su gina jama'ar masu bi.

13 Saboda haka duk mai magana da wani harshe, sai yă yi
addu'a don a ba shi baiwar fassara. 14 Idan na yi addu'a a wani
harshe, ruhuna ne yake addu'a, amma tunanina bai amfana kome
ba. 15 To, me zan yi? Zan yi addu'a da ruhu, amma kuma zan
yi har da tunanina ma. Zan yi waƙar yabon Allah da ruhuna,
amma zan yi har da tunanina kuma. 16 Idan ba haka ba, in ka
gode wa Allah da ruhu kawai, ta yaya wanda yake sauraronka
da ba ya gane wannan harshe zai ce, "Amin" a kan godiyar da
kake yi, in bai san abin da kake faɗa ba? 17 Ko da yake ka gode
wa Allah sosai, amma wannan mutumin bai ƙaru ba. 18 Na gode
Allah ina magana da harsuna fiye da dukanku. 19 Duk da haka
dai a taron jama'ar masu bi, na fi so in faɗa kalmomi biyar da
tunanina don in koyar da waɗansu, da in faɗa kalmomi dubu
goma da wani harshe.

20 'Yan'uwa, kada ku yi tunani kamar yara, sai dai wajen
mugunta ku zama kamar jarirai, amma ku zama da tunani irin na
manya. 21 A rubuce yake cikin Rubutaccen Maganar Allah cewa,

"Zan yi magana da mutanen nan
ta wurin mutane masu harsuna dabam,
da kuma ta leɓunan baƙi, duk da haka
kuwa ba za su saurare ni ba,
in ji Ubangiji."

22 To ashe, harsuna ba alama ba ne ga masu bi, sai dai ga marasa
bi. Annabci kuwa don masu bangaskiya ne, ba don marasa ba da
gaskiya ba. 23 Saboda haka, idan dukan jama'ar masu bi ta taru,
kowa kuma yana magana da wani harshe dabam, sai waɗansu da
ba su san abin da ake yi ba, ko marasa bi suka shigo, ashe, ba
sai su ce kun haukace ba? 24 Amma idan kowa yana annabci, wani
marar bi, ko wanda bai san abin da ake yi ba ya shigo, sai maganar
kowa ta taɓa shi, har yă nemi tuba. 25 Za a tona asiran zuciyarsa,
ta haka sai yă fāɗi yă yi wa Allah sujada, yana cewa, "Lallai
Allah yana cikinku."

A Yi Sujada yadda Ya Kamata

26 To, yaya za a yi ke nan 'yan'uwa? Sa'ad da kuka taru, wani
yana waƙar yabon Allah, wani bayani, wani yin magana da wani
harshe, wani kuma fassara, sai dai a yi kome don ginawa. 27 Idan
kuwa waɗansu za su yi magana da wani harshe, kada su fi mutum
biyu ko uku, su kuma yi shi bi da bi, wani kuma yă yi fassara.

14.21: Ish 28.11-12

28 Idan kuwa ba mai fassara, sai kowannensu yă yi shiru cikin
jama'ar masu bi, yă yi wa kansa magana da kuma Allah. 29 Masu
yin annabci kuma, sai dai biyu ko uku su yi magana, sai wadansu
su auna abin da ake fada. 30 Idan kuwa Allah ya yi wa wani wanda
yake zaune kusa bayani, sai na farkon nan mai magana yă yi
shiru. 31 Dukanku kuna iya yin annabci daya-daya, har kowa yă
sami koyo, kowa yă kuma sami karfafawa. 32 Ruhohin annabci
kuwa suna karkashin annabawa ne. 33 Don Allahnmu ba Allah
mai kawo rikicewa ba ne, amma shi mai salama ne.

Haka yake kuwa a duk jama'un masu bi na tsarkaka. 34 Ya
kamata mata su yi shiru a cikin jama'un masu bi, don ba a ba su
izni su yi magana ba, sai dai su bi, kamar yadda Dokar Musa ma
ta ce. 35 Idan akwai wani abin da suke so su sani, to, sai su tambayi
mazansu a gida. Don abin kunya ne mace ta yi magana a cikin
jama'ar masu bi. 36 A kanku ne maganar Allah ta fara, ko kuwa
ku kadai ne ta kai wajenku?

37 Idan wani yana tsammani shi annabi ne, ko kuwa mai wata
baiwa ta ruhu, to, sai ya gane cewa, abin nan da nake rubuta
muku umarni ne na Ubangiji. 38 Idan kuwa wani ya ki yă kula da
wannan, shi ma sai a ki kula da shi. 39 Saboda haka 'yan'uwana,
ku rika marmarin yin annabci, kada kuma ku hana yin magana
da wadansu harsuna. 40 Sai dai a yi kome yadda ya kamata, a
shirye kuma.

Tashin Almasihu daga Matattu

15 1 Yanzu kuma, 'yan'uwa, zan tuna muku da Labari Mai
Dadin da na sanar muku, wadda kuka karba, kuke kuma
bi. 2 Ta bisharan nan ne kuke samun ceto, muddin kuna rike
maganar da na sanar da ku sosai, in ba sama-sama ne kuka
gaskata ba.

3 Abu mafi muhimmincin da na sanar da ku, shi ne wanda na
karbo, cewa: Almasihu ya mutu saboda zunubanmu, kamar yadda
Rubutattun Maganar Allah sun fada, 4 cewa an binne shi, an ta
da shi a rana ta uku, kamar yadda Rubutattun Maganar Allah sun
fada, 5 ya kuma bayyana ga Kefas, sa'an nan ga sha biyun. 6 Sa'an
nan ya bayyana ga 'yan'uwa fiye da dari biyar a lokaci guda,
yawancinsu kuwa suna nan har yanzu, amma wadansu sun yi
barci. 7 Sa'an nan ya bayyana ga Yakubu, sa'an nan kuma ga
dukan manzanni. 8 Daga karshe duka, ya bayyana gare ni, ko da

---

15.3: Ish 53.5-12 15.4: Zab 16.8-10; Mat 12.40; A.M. 2.24-32
15.5: Mat 28.16-17; Mar 16.14; Luk 24.34,36; Yoh 20.19

yake ni kamar mutum ne wanda an haifa a lokacin da bai kamata ba. 9 Don ni ne mafi ƙanƙanta a cikin manzanni, ban ma isa a ce da ni manzo ba, saboda na tsananta wa jama'ar masu bin Allah. 10 Amma saboda alherin Allah ne na zama yadda nake, kuma alherin da ya yi mini kuwa ba a banza ba ne. Har ma na fi kowane manzo aiki, ko da yake ba ni ba ne, alherin Allah ne da yake tare da ni. 11 To, ko ni ne dai, ko kuma su ne, haka muke wa'azi, ta haka kuma kuka gaskata.

Tashin Matattu

12 To, idan har ana wa'azin tashin Almasihu daga matattu, yaya waɗansunku suke cewa ba tashin matattu? 13 Idan ba tashin matattu, ashe, Almasihu bai tashi daga matattu ba ke nan. 14 Idan kuwa Almasihu bai tashi daga matattu ba, ashe, wa'azinmu banza ne, bangaskiyarku kuma ta zama banza. 15 Sai ya zama mun yi wa Allah shaidar ƙarya ke nan, don mun yi wa Allah shaida cewa ya ta da Almasihu, wanda kuwa bai tasar ba, idan da gaskiya ne ba a ta da matattu. 16 Gama idan ba a ta da matattu, ashe, Almasihu ma ba a tashe shi ba ke nan. 17 Idan kuwa ba a ta da Almasihu ba, ashe, bangaskiyarku banza ce, har yanzu kuma kuna cikin zunubanku. 18 Ashe, waɗanda suka mutu cikin Almasihu, sun halaka ke nan. 19 Da sa zuciyarmu ga Almasihu don wannan rayuwar ne kaɗai, ai, da mun fi kowa zama abin tausayi.

20 Amma, hakika an ta da Almasihu daga matattu, wannan ya nuna za a ta da waɗanda suka yi barci. 21 Tun da yake mutuwa ta zo ne ta wurin mutum, haka ma tashin matattu ya zo ne ta wurin mutum. 22 Gama kamar yadda duka ake mutuwa saboda Adamu, haka za a ta da duka saboda Almasihu. 23 Amma za a ta da kowanne bi da bi, Almasihu kuwa na fari, sa'an nan waɗanda suke nasa a ranar da zai dawo. 24 Sa'an nan sai ƙarshen yă zo, sa'ad da zai mayar wa Allah Uba mulki, bayan ya kawar da dukan sarauta, da mulki, da iko. 25 Don kuwa dole ne Almasihu yă yi mulki, har Allah yă sa yă take dukan abokan gābansa. 26 Abokiyar gāba ta ƙarshe da za a halaka ita ce mutuwa. 27 Gama "Allah ya mai da dukan abu a ƙarƙashin mulkinsa". Amma da aka ce, "Dukan abu yana ƙarƙashin mulkinsa," a fili yake ke nan cewa, shi wanda ya ba shi iko a kan dukan abu, ba ya ƙarƙashinsa. 28 Sa'ad da Allah ya mai da dukan abu a ƙarƙashinsa, sai Ɗan shi

15.8: A.M. 9.3-6 **15.9:** A.M. 8.3 **15.25:** Zab 110.1 **15.27:** Zab 8.6

ma yă zama a ƙarƙashin Allah wanda ya mai da dukan abu a ƙarƙashinsa, don Allah yă zama shi ne kome da kome.

29 Idan ba haka ba, me mutanen nan za su yi, waɗanda aka yi wa baftisma a madadin matattu? Idan ba a ta da matattu sam, don me ake yi wa mutane baftisma a madadinsu? 30 Kuma don me muke sa kanmu cikin hatsari kowane lokaci? 31 Ina mutuwa kullum. Gaskiya ne 'yan'uwa, kamar yadda yake tabbatacce cewa ina taƙama da ku cikin Almasihu Yesu Ubangijinmu. 32 Idan na yi kokawa da namun daji a Afisa, bisa ga begen mutum, mece ce ribata idan dai har ba a ta da matattu? "Ba sai mu yi ta ci da sha ba, tun da gobe za mu mutu"?

33 Kada fa a ruɗe ku! "Zama da mugaye
yakan ɓata halayen kirki".

34 Ku dawo cikin tunani mai kyau, ku daina yin zunubi. Waɗansunku ba su san Allah ba. Na faɗa wannan ne don ku ji kunya.

Tashin Jiki

35 Amma waɗansu za su yi tambaya su ce, "Yaya ake ta da matattu? Da wane irin jiki suke fitowa?" 36 Wawa! Abin da ka shuka ba zai tsira ba sai ya mutu. 37 Abin da ka shuka kuma, ba shi ne ainihin abin da zai tsira ba, ƙwaya ce kawai, ko ta alkama, ko wata irin ƙwaya dabam. 38 Amma Allah yakan ba ƙwayar wani kamanni, yadda ya nufa, kowace ƙwaya da irin kamanninta. 39 Ba dukan nama ne iri ɗaya ba: Mutane da irin nasu, dabbobi da irin nasu, tsuntsaye da irin nasu, kifaye kuma da irin nasu. 40 Akwai halitta irin ta sama, akwai kuma irin ta ƙasa. Amma ɗaukakar irin ta sama dabam, ɗaukakar irin ta ƙasa kuma dabam. 41 Daukakar rana dabam, ta wata dabam, ta taurari kuma dabam, har ma wani tauraro yakan zama dabam da wani wajen ɗaukaka.

42 Haka kuma yake game da tashin matattu. Abin da aka shuka yana ruɓewa, abin da aka ta da shi kuma ba ya ruɓewa. 43 Akan shuka shi cikin ƙaskanci, akan ta da shi cikin ɗaukaka. Akan shuka shi cikin rashin ƙarfi, akan ta da shi cikin ƙarfi. 44 Akan shuka shi cikin jiki na mutuntaka, akan ta da shi cikin jiki na ruhu. Tun da akwai jiki na mutuntaka, lallai akwai jiki na ruhu. 45 Haka yake a rubuce, "Mutum na farko, Adamu, ya zama mutum mai rai." Adamu na ƙarshe kuwa ruhu ne mai ba da rai. 46 Amma ba na ruhun ne farko ba, na mutuntaka ne kafin na ruhu.

15.32: Ish 22.13 **15.45:** Far 2.7

47 Mutumin farko daga ƙasa yake, na turɓaya ne. Na biyun kuwa
daga sama yake. 48 Kamar yadda shi na turɓayan nan yake, haka
kuma waɗanda suke na turɓaya suke. Kamar yadda shi na saman
nan yake, haka kuma waɗanda suke na sama suke. 49 Kamar yadda
muka ɗauki kamanni na turɓayan nan, haka kuma za mu ɗauki
kamanni na saman nan.

50 Abin da nake gaya muku, 'yan'uwa, shi ne ba zai yiwu
jikinmu na nama da jini yă sami gādo a mulkin Allah ba, haka
kuma mai ruɓa ba ya gādon marar ruɓa.

51 Ku saurara, zan gaya muku wani asiri! Ba dukanmu ne za
mu mutu ba, amma dukanmu za a sāke kamanninmu, 52 farat ɗaya,
da ƙyaftawar ido, da jin ƙarar ƙaho na ƙarshe. Gama za a busa
ƙaho, za a kuma ta da matattu da jiki irin wanda ba ya ruɓewa,
za a kuma sāke kamanninmu. 53 Don lallai ne, marar ruɓa yă
mamaye mai ruɓan nan, marar mutuwa kuma yă mamaye mai
mutuwan nan. 54 Sa'ad da kuma marar ruɓa ya mamaye mai ruɓan
nan, marar mutuwa kuma ya mamaye mai mutuwan nan, a lokacin
nan ne fa maganan nan da take a rubuce za ta cika, cewa,

"An haɗiye mutuwa,
an yi nasara a kanta."
55 "Ke, mutuwa, ina nasararki?
Ke, mutuwa, ina dafinki?"

56 Ai, zunubi shi ne dafi mutuwa, shari'a kuwa ita ce dalilin ƙarfin
zunubi.

Zunubi ya sami ikonsa ta dalilin shari'ar Allah wadda tana
bayyana zunubi ta kuma hukunta shi. 57 Bari godiya ta tabbata ga
Allah wanda yake ba mu nasara ta wurin Ubangijinmu Yesu
Almasihu.

58 Saboda haka 'yan'uwana waɗanda nake ƙauna, ku tsaya
daram, kada ku matsa, kullum kuna ƙoƙari cikin aikin Ubangiji,
don kuwa kun san famar da kuke yi saboda Ubangiji ba a banza
take ba.

Taimako don Masu Bi

16 1 To, game da zancen ba da taimako don masu bi, ku yi
kamar yadda na umarci jama'un masu bi na Galatiya su
yi. 2 A kowace ranar farko ta mako, kowannenku yă riƙa samun
wani abu, yana ajiyewa bisa ga abin da ya iya samu, ba sai na
zo ba tukuna kafin a tara taimakon. 3 Sa'ad da na iso, sai in aika
waɗanda kuka yarda da su, tare da wasiƙu na gabatarwa, su kai

15.51-52: 1 Tas 4.15-17 **15.54**: Ish 25.8 **15.55**: Hos 13.14 **16.1**: Rom 15.25-26

bayarwarku Urushalima. 4 Idan ya yi kyau ni ma in je, to, sai su raka ni.

Shirye-shiryen Tafiya

5 Zan zo muku ziyara, bayan na zazzaga ƙasar Makidoniya, don na yi niyyar bi ta Makidoniya. 6 Watakila zan jima a wurinku, ko ma har damina ta ƙare, don ku yi mini rakiya duk inda za ni. 7 Ba sona ne in gan ku yanzu in wuce kawai ba, don ina fata ma in yi kwanaki a wurinku, idan Ubangiji ya yarda. 8 Amma zan tsaya a Afisa har ranar Fentikos. 9 Don kuwa an buɗe mini hanya mai fāɗi ta yin aiki mai amfani, ko da yake akwai abokan gāba da yawa.

10 Idan Timoti ya zo, ku sa yă sake a cikinku, don shi ma yana aikin Ubangiji ne kamar yadda nake yi. 11 Saboda haka kada kowa yă rena shi, ku raka shi lafiya yă dawo wurina, don ina duban hanyarsa tare da 'yan'uwa.

12 Game da ɗan'uwanmu Afolos kuma, na roƙe shi sosai yă zo wurinku tare da sauran 'yan'uwa, amma bai yi niyyar zuwa yanzu ba sam. Zai zo dai a lokacin da ya ga ya dace.

Maganar Karshe

13 Ku zauna da shiri, ku tsaya sosai cikin bangaskiyarku, ku zama da ƙarfafawa, kuma da ƙarfi. 14 Bari dukan abin da za ku yi, ku yi shi da ƙauna.

15 To, 'yan'uwa, kun san dai mutanen gidan Istifanus su ne na farko da suka tuba a ƙasar Akaya, sun kuwa ba da kansu ga yin wa masu bi hidima. 16 Ina roƙonku ku yi wa irin waɗannan mutanen biyayya, har ma da dukan waɗanda muka yi aiki da fama tare.

17 Na ji daɗin zuwan Istifanus, da Fartunatus, da Akaikus, wanda ya zama mini kamar ku ne kuka zo. 18 Don sun faranta mini raina, da ku kuma. Irin waɗannan mutanen ya kamata a girmama su.

19 Jama'un masu bi a ƙasar Asiya suna gaishe ku. Akila da Biriskila, tare da jama'ar masu bi da take taru a gidansu, suna gaishe ku sosai cikin Ubangiji. 20 Dukan 'yan'uwa suna gaishe ku. Ku gai da junanku da gaisuwar ƙauna.

21 Ni Bulus ne nake rubuta gaisuwan nan da hannuna.

16.5: A.M. 19.21 **16.8:** L. Fir 23.15-21; M. Sh 16.9-11 **16.8-9:** A.M. 19.8-10 **16.10:** 1 Kor 4.17 **16.15:** 1 Kor 1.16 **16.19:** A.M. 18.2

22 Duk wanda ba ya ƙaunar Ubangiji yă zama la'ananne. Zo, ya Ubangiji.
23 Alherin Ubangijinmu Yesu yă kasance tare da ku. 24 Ina ƙaunarku duka cikin Almasihu Yesu.

WASIKAR BULUS TA BIYU ZUWA GA KORINTIYAWA

Gabatarwa

An rubuta *Wasiƙar Bulus ta biyu zuwa ga Korintiyawa* ba da daɗewa ba bayan da aka rubuta ta farkon. Ana zato manzo Bulus ya yi wannan rubutu a shekara ta A.D. 55 ne, a lokacin da yake a yankin Makidoniya inda ya yi aikin bishara (Dubi 2.12, 7.5).

An rubuta wannan wasiƙa ne domin a tabbatar wa jama'ar masu bi na Korinti cewa har yanzu Bulus yana ƙaunarsu kuma sakonsa nan na cewa su zama abokan Allah ta wurin Yesu yana nan daram. Wannan ya zama haka ko da yake ya riga ya tsawata musu a wata wasiƙar da ya rubuto musu. Bayan wannan magana sai Bulus ya roƙe su su tattara kuɗin taimakonsu da zai kai Urushalima tun da zai zo wurinsu ba da daɗewa ba.

Za a ga cewa a cikin wannan wasiƙa ne Bulus ya yi zance game da kansa fiye da a cikin duk sauran wasiƙunsa. Wannan ya zama haka don a lokacin da Bulus ya rubuta wasiƙan nan akwai damuwa sosai a tsakaninsa da waɗansu cikin jama'ar masu bi a Korinti.

A cikin wasiƙar Bulus ya kāre kansa game da zargin da malaman ƙarya suke yi masa na cewa shi ba manzo na gaskiya ba ne.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-11
Bulus da jama'ar masu bi a Korinti 1.12—7.16
Bayarwa don masu bi a Yahudiya 8.1—9.15
Bulus ya kāre kansa 10.1—13.10
Maganar ƙarshe 13.11-14

Gaisuwa

1 [1] Daga Bulus wanda Allah ya zaɓa domin yă zama manzon Almasihu Yesu, da kuma ɗan'uwanmu Timoti, zuwa ga jama'ar masu bin Allah a Korinti, tare da dukan tsarkaka a duk fāɗin ƙasar Akaya.

2 Alheri da salama daga Allah Ubanmu da Ubangiji Yesu Almasihu su kasance tare da ku.

Allah Mai Ta'aziyya Ne

3 Bari mu gode wa Allah Uba, shi da yake Uban Ubangijinmu Yesu Almasihu, Uba mai yawan tausayi, Allahn da yake yi mana kowace irin ta'aziyya. [4] Allah yana yi mana ta'aziyya a cikin dukan wahalarmu, don mu ma mu yi wa waɗansu ta'aziyya a cikin kowane irin wahalarsu, da wannan ta'aziyyar da muka samu daga wurin Allah. [5] Kamar yadda muke shan wuya yadda Almasihu da kansa ya sha, haka kuma ta wurin Almasihu za mu sami babbar ta'aziyyan nan ta Allah. [6] Ko muna shan wahala, ai, muna shanta ne domin ta zama abin ta'aziyya a gare ku ta kuma ƙarfafa rayuwarku ta ruhaniya. Idan kuma ta'aziyya ake mana ne, to, ku ma kun sami ta'aziyya ke nan yadda za ku sami ƙarfin yin haƙuri a kan wannan wahala da mu ma muke sha. [7] Ba ma shakkarku ko kaɗan, domin mun sani cewa kamar yadda kuke shan wahala irin tamu, haka ku ma za ku sami irin ta'aziyyar da ake yi mana.

8 'Yan'uwa, ba ma so ku kasance da rashin sani game da irin wahalar da muka sha a ƙasar Asiya, wannan wahalar ta yi yawa sosai har ba mu san za mu rayu ba. [9] Har ma muka ji kamar hukuncin mutuwa aka yi mana. Amma wannan ya faru ne domin kada mu dogara ga ƙoƙarin kanmu sai dai mu dogara ga Allah, wanda yake ta da waɗanda suka mutu. [10] Allah ya fitar da mu daga wannan muguwar mutuwa,[a] mun tabbata zai cece mu kuma. A gare shi ne muke dogara domin yă sāke cece mu. [11] Ku taimake mu da addu'a. Ta haka ne mutane da yawa za su gode wa Allah saboda mu,[b] saboda albarkun da za mu samu ta wurin amsa addu'o'i masu yawa.

1.1: A.M. 18.1 1.8: 1 Kor 15.32

[a] **1.10 muguwar mutuwa:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "hatsarin mutuwa" ne a nan.

[b] **1.11 mu:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "ku" ne a nan.

Bulus Ya Sãke Shirin da Ya Yi na Ziyara

12 Abin da yake sa mu taƙama shi ne tunanin zuciyarmu tana
shaida mana cewa mun yi zama mai tsarki a duniya da zuciya
ɗaya, musamman cikin zaman da muka yi da ku. Zan ce mun yi
haka cikin gaskiya ta Allah. Mun yi wannan ta alherin Allah ne,
ba ta wayon wannan duniya ba. 13-14 Muna rubuta muku abin da
za ku iya karanta ku gane ne kawai. Amma ko da yake kun sami
ganewa kaɗan yanzu, ina fata za ku sami ganewar kome da kome,
domin ranar da Ubangijinmu Yesu zai dawo, ku yi taƙama da
mu, kamar yadda mu ma za mu yi taƙama da ku.

15 Na san da haka, shi ya sa na so in zo wurinku da farì,
domin ku sami albarka sau biyu. 16 Na shirya in bi wurinku
idan zan tafi Makidoniya, in sãke bin wurinku kuma idan ina
dawowa, domin in sami taimakonku don tafiyata zuwa
Yahudiya. 17 Kuna gani cewa na yi wannan shirin ba da sanin
abin da nake yi ba ne? Ko kuwa, kuna gani na yi shirin nan da
halin mutuntaka ne, don in ce, "I" in koma in ce, "A'a"?
18 Kamar dai yadda Allah yake mai aminci, haka ma maganar
da muka yi muku, ba ta "I" da "A'a" ba ce. 19 Domin Ɗan
Allah Yesu Almasihu, wanda ni da Sila[6] da Timoti muka yi
muku wa'azinsa, ai, ba wani mai "I" da "A'a" ba ne, amma a
cikinsa "I" ne kullum. 20 Domin ta wurinsa ne Allah ya cika
dukan alkawaran da ya yi. Shi ya sa ta wurin Yesu Almasihu
muke cewa "Amin" domin ɗaukakar Allah. 21 Allah ne yake
tabbatar mana, da mu da ku gaba ɗaya, samun rai a cikin
Almasihu, shi ne kuma ya zaɓe[c] mu, 22 ya sa mana lambarsa
na nuna cewa mu nasa ne, ya kuma ba mu kyautar Ruhunsa a
zuciyarmu domin yã tabbatar mana abin da zai yi nan gaba.

23 Allah ne shaidata idan ƙarya ne nake yi cewa dalilin da ban
koma Korinti ba shi ne don kada in ƙara muku wahala. 24 Ba wai
muna so mu nuna muku iko a kan bangaskiyarku ba ne, a'a, muna
aiki ne tare, domin ku yi farin ciki, saboda kuna tsaye da ƙarfi
cikin bangaskiyarku.

2 1 Saboda haka na ɗauki niyya a kan ba zan sãke zuwa
wurinku in sa ku baƙin ciki ba. 2 To, idan na sa ku baƙin ciki,
wa zai sa raina yã ji daɗi, in ba wanda na sa shi baƙin cikin ba?
3 Dalilin da ya sa na rubuto muku waccan wasiƙar kuwa shi ne,

---

1.16: A.M. 19.21 **1.19:** A.M. 18.5

[6] **1.19 Sila:** Da Helenanci an rubuta "Silbanus" ne a nan.

[c] **1.21 Zaɓe:** Da Helenanci, ma'anar kalman nan ta ƙunshi keɓewa da shafewa domin aikin Allah.

don ba na so in zo in sami mutanen da ya kamata su sa ni farin ciki, su ɓata mini rai. Domin na tabbata cewa idan na yi murna, dukanku ma za ku yi murna. 4 Na rubuto muku ne ina cikin wahala da baƙin ciki mai yawa, har da hawaye sosai, ba wai don in sa ku baƙin ciki ba, sai dai domin ku san yadda nake ƙaunarku sosai.

Yafewa ga Wanda Ya Yi Laifi

5 Idan wani ya yi abin baƙin ciki, ba ni ne ya yi mini ba, amma a wani gefe ya yi wa dukanku ne. Ba wai ina faɗa haka in matsa muku lamba ba ne. 6 Horon da mutumin nan ya sha a ta wannan hanya daga wurin yawancinku, ya isa haka. 7 Yanzu kuma, sai ku yafe masa, ku kuma ƙarfafa shi, don kada ku bar shi har baƙin ciki yă sha ƙarfinsa. 8 Saboda haka ina roƙonku ku nuna masa cewa kuna ƙaunarsa sosai. 9 Na rubuto muku wannan wasiƙar domin in gwada ku ne, in gani ko kuna a shirye ku bi umarnaina a koyaushe. 10 Duka wanda kuka yafe masa kome, ni ma na yafe masa. Abin da na yafe kuwa, in ma akwai abin yafewa, na yafe ne saboda ku, don albarkacin Almasihu, 11 domin kada Shaiɗan yă sami dama yă rude mu, don mun san dabarunsa sarai.

Damuwar Bulus a Toruwas

12 Da na zo Toruwas don in yi wa'azin Labari Mai Daɗi na Almasihu, Ubangiji kuma ya ba ni dama in yi aiki a nan, 13 amma sai na damu sosai domin ban ga ɗan'uwana Titus a nan ba. Saboda haka sai na yi bankwana da su, na wuce zuwa Makidoniya.

Nasara cikin Almasihu

14 Amma godiya ga Allah, shi da yake bi da mu kullum mu ci nasara ta wurin Almasihu. Yana amfani da mu don mu kai saƙon Almasihu ko'ina kamar turare mai ƙamshi da aka fesa. 15 Domin mu kamar turare mai ƙamshi ne wanda Almasihu ya miƙa wa Allah, wanda ya bazu cikin waɗanda ake cetonsu da kuma waɗanda suke hanyar halaka. 16 Ga waɗanda suke hanyar halaka kuwa, ƙamshin nan warin mutuwa ne, mai kawo mutuwa; amma ga waɗanda suke samun ceto, ƙamshin nan rai ne mai kawo rai. Babu wani da zai iya ɗaukar nauyin aikin nan. 17 Mu ɗin nan ba kamar sauran mutane muke ba, waɗanda suke maganar Allah don neman riba. Amma da yake Allah ne ya aiko mu, muna magana cikin gaskiya a gabansa, a matsayin masu hidimar Almasihu.

2.12-13: A.M. 20.1

Masu Hidimar Sabon Alkawari

3 [1] Wato, yabon kanmu za mu fara yi kuma? Ko kuwa muna
neman wasiƙun shaida ne zuwa wurinku, ko daga wurinku,
kamar yadda waɗansu suke yi? [2] Ai, ku da kanku ku ne wasiƙar
da muke da ita, wadda aka rubuta a zuciyarmu[d] don kowa yă
gani yă kuma karanta. [3] Kun nuna cewa ku wasiƙa ce ta Almasihu,
wadda take sakamakon hidimarmu. Wannan wasiƙar kuwa ba a
rubuta ta da biro ba, amma an rubuta ta da Ruhu Mai Tsarki na
Allah mai rai. Ba a rubuta ta a kan allon duwatsu ba, amma a
zukatan mutane.

4 Mun faɗa haka domin muna da tabbaci a gaban Allah ta
wurin Almasihu. [5] Ba mu da wani abin da za mu nuna cewa da
iyawarmu ne muke aikin nan. Iyawarmu daga wurin Allah ne
ya fito. [6] Shi ya sa muka iya zama masu hidimar sabon alkawari,
wanda ba na dokar da aka rubuta ba, amma na Ruhu. Dokan
nan da take a rubuce ita ce take kawo mutuwa, amma Ruhu
yana ba da rai.

7 An rubuta Dokar Musa a kan allunan duwatsu, kuma
ɗaukakar Allah ta bayyana a sa'ad da ake bayar da ita. Ko da
yake hasken da yake a fuskar Musa mai shuɗewa ne, ya haskaka
sosai har ma mutanen Isra'ila suka kāsa kafa ido a fuskarsa. Idan
har Doka wadda take kawo mutuwa ta zo da ɗaukaka haka, [8] to,
yaya yawan ɗaukaka wadda take ta Ruhu za ta kasance? [9] Idan
abin da yake kawo mutuwa ya sami ɗaukaka, lallai abin da yake
jawo samun adalcin Allah ya fi shi ɗaukaka nesa. [10] Hakika,
ɗaukaka ta tsohon alkawari ba ta da wata daraja yanzu, idan an
gwada ta da daraja ta sabon alkawari. [11] Idan har abin nan mai
shuɗewa ya zo da ɗaukaka, yaya zai zama ga abin nan da zai
kasance har abada!

12 Saboda muna da irin wannan sa zuciya, shi ya sa muke da
ƙarfin hali sosai. [13] Mu ba kamar Musa ba ne, wanda ya rufe
fuskarsa da mayafi, don kada Isra'ilawa su ga ƙarewar ɗaukakan
nan mai shuɗewa. [14] Amma hankalinsu ya taurare, domin har
zuwa yau akwai wani abu da yake hana su ganin gaskiyan nan
in ana karatun Tsohon Alkawari. Mayafin nan har yanzu ba a cire
shi ba, domin ba a iya cire shi sai ta wurin Almasihu kaɗai. [15] Har
wa yau, idan ana karatun littattafan Musa, sai wannan mayafi yă

3.3: Fit 24.12; Irm 31.33; Ez 11.19; 36.26 **3.6**: Irm 31.31 **3.7**: Fit 34.29
3.13: Fit 34.33

[d] **3.2 zuciyarmu**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "zuciyarku" ne a nan.

rufe zuciyarsu. 16 Amma za a iya cire shi idan mutum ya juyo ga
Ubangiji. 17 To, Ubangiji fa, shi ne Ruhu; inda Ruhun Ubangiji
yake kuwa a nan 'yanci yake. 18 Mu da ba a rufe fuskarmu ba,
muna nuna ɗaukakar Ubangiji kamar madubi, kuma ana sāke mu
mu zama kamarsa. Wannan sākewar da ake yi mana tana daɗa
ƙaruwa cikin ɗaukaka wadda ta fito daga wurin Ubangiji, wanda
yake shi Ruhu ne.

Arziki a cikin Tulun Laka

4 1 Saboda haka, da yake muna da wannan hidima bisa ga
jinƙan Allah ba za mu fid da zuciya ba. 2 Ba ruwanmu da
ɓoye-ɓoye na munafuncin da suke abubuwan kunya. Ba
ruwanmu da rudî, ko mu yi ƙarya da maganar Allah. Amma
muna faɗin gaskiya a fili. Ta haka ne kowa zai yi shaidar
gaskiyarmu a gaban Allah cikin zuciyarsa. 3 Idan ma bisharan
nan da muke wa'azinta a ɓoye take, tana a ɓoye ne ga waɗanda
suke a hanyar halaka. 4 Ba su ba da gaskiya ba, domin mai
mulkin wannan duniya[d] ya sa zuciyarsu ta yi duhu. Ya hana su
ganin hasken da yake haskaka su, hasken nan da yake fitowa
daga Labari Mai Daɗi a kan ɗaukakar Almasihu, wanda shi ne
kamannin Allah. 5 Domin ba wa'azin kanmu muke yi ba, sai
dai na Yesu Almasihu, cewa shi ne Ubangiji, mu kuwa kamar
bayinku ne saboda Yesu. 6 Allahn da ya ce; "Bari haske yă
haskaka daga duhu," shi ne kuma ya sa haskensa yake
haskakawa a cikin zuciyarmu, don a haskaka mutane su san
ɗaukakar Allah a fuskar Almasihu.

7 Duk da haka, mu da muke da wannan arziki na ruhaniya
muna kamar tulunan laka ne kawai. Mun zama haka domin mu
nuna cewa Allah ne yake da cikakken iko, ba mu ba. 8 Ana ba
mu wahala ta kowace hanya, duk da haka ba a iya sa mu gaji
da aikin ba. Wani lokaci ma mukan yi shakka, amma ba ma fid
da zuciya. 9 Ana tsananta mana, duk da haka Allah bai bar mu
ba. Wani lokaci akan ba mu wuya, duk da haka ba a halaka mu
ba. 10 Kullum muna a hatsarin mutuwa kamar yadda aka yi wa
Yesu, domin a bayyana rayuwar Yesu a jikin nan namu mai
mutuwa. 11 Dukan kwanakinmu a duniya, muna cikin hatsarin
mutuwa saboda Yesu, don dai a ga rayuwar Yesu a jikin nan
namu mai mutuwa. 12 Shi ya sa muke fuskanta mutuwa domin
ku ku sami rai.

3.16: Fit 34.34 **4.6**: Far 1.3

[d] **4.4 mai mulkin wannan duniya**: Wato, Shaiɗan ke nan.

13 Rubutaccen Maganar Allah ta ce, "Na gaskata, saboda haka
na yi magana." Tun da yake muna da ruhun bangaskiya iri ɗaya,
haka mu ma mun gaskata, saboda haka kuma muke magana.
14 Domin mun san cewa Allah wanda ya ta da Ubangiji Yesu daga
matattu, zai ta da mu tare wanda Yesu, yă kuma kawo mu gabansa
tare da ku. 15 Duk wannan fa don amfaninku ne, yayin da alherin
Allah yana ta kaiwa ga mutane masu yawa, zai zama dalilin
yawan godiya ga Allah, domin a ɗaukaka shi.

Rayuwa ta wurin Bangaskiya

16 Saboda haka ba mu fid da zuciya ba. Ko da yake jikin nan
namu yana ta lalacewa, duk da haka ana mai da ruhunmu sabo
kullum. 17 Gama wannan 'yar wahalar da muke sha ba za ta daɗe
ba, za ta kai mu ga madawwamiyar ɗaukaka mai yawa, wadda
ta wuce gaban misali. 18 Domin ba abubuwan da idanu suke gani
ne muke dubawa ba, sai dai abubuwan da ba a gani. Domin
abubuwan da ake gani, suna saurin wucewa, amma abubuwan da
ba a gani kuwa, marar wucewa ne.

5 1 Gama mun san cewa idan an rushe rumfan nan da muke
zama a ciki, wato, jikinmu na wannan duniya, Allah da kansa
zai yi mana gida a sama. Gidan nan kuwa ba mutum ne ya gina
shi ba, kuma zai kasance har abada. 2 A yanzu kam, muna ajiyar
zuciya, muna marmari sosai mu sami wannan wurin zama wanda
za a rufe mu da shi a sama. 3 Idan kuwa aka rufe mu da shi, ba
za a same mu tsirara ba. 4 Sa'ad da muke zaune cikin jikin nan
na duniya muna nishi don an matse mu. Ba wai muna so mu rabu
da jikin nan namu na duniya ba, amma muna so a rufe mu da na
sama, domin abu mai rai na har abada yă rufe abin nan mai
mutuwa gaba ɗaya. 5 Allah da kansa ne ya shirya mana wannan
sākewa, kuma ya ba mu Ruhunsa domin yă tabbatar da abin da
zai yi mana nan gaba.

6 Shi ya sa kullum muke da ƙarfin zuciya, mun kuma san cewa
idan dai muna da wannan jiki na duniya, to, muna nesa da
gidanmu wanda yake tare da Ubangiji. 7 Gama rayuwar
bangaskiya muke yi, ba bisa ga abin da muke gani da ido ba.
8 Hakika muna da ƙarfin zuciya, kuma mun fi so mu rabu da
wannan jiki mu zauna tare da Ubangiji a sama. 9 Fiye da kome
dai, mun fi so yă ji daɗinmu, ko muna a wannan duniya ko muna
a sama. 10 Don dole ne dukanmu mu tsaya a gaban Almasihu, don

---

4.13: Zab 116.10

yă yi mana shari'a. Gama kowa zai karɓi ladan aikin da ya yi a wannan jiki na duniya, ko mai kyau ne ko kuma marar kyau.

Rayuwar Yin Sulhu

11 Tun da yake mun san abin da ake nufi in ana maganar tsoron Allah, shi ya sa muke ƙoƙari mu jawo waɗansu. Allah ya san duk yadda muke, kuma ina fata kun san da wannan a zuciyarku. 12 Ba wai muna so mu yabi kanmu a gabanku ba ne, sai dai muna ƙoƙari mu ba ku dalili mai kyau ne wanda za ku ji dadînmu, don ku iya ba da amsa ga waɗanda suke ɗaga kai saboda matsayinsu, a maimakon halinsu. 13 Muna hauka ne, kamar yadda waɗansu suka faɗa? Ko ma muna hauka ne, muna yi ne domin ɗaukakar Allah. In kuma ba hauka muke yi ba, wannan dominku ne. 14 Kome muka yi, mun yi shi ne ba don ribarmu ba, amma saboda ƙaunar Almasihu wadda take bi da mu. Da yake mun ba da gaskiya Almasihu ya mutu domin dukan mutane, saboda haka duka sun mutu tare da shi. 15 Ya kuwa mutu ne saboda dukan mutane, domin waɗanda suke da rai, kada su yi zaman ganin dama nan gaba, sai dai su yi zama saboda wanda ya mutu dominsu, aka kuma tashe shi saboda su.

16 Saboda haka nan gaba ba ma ƙara duban wani bisa ga ganin mutum, domin ko da yake mun taɓa duban Almasihu bisa ga ganin mutum, yanzu ba ma ƙara dubansa haka. 17 Saboda haka idan mutum yana cikin Almasihu, ya zama sabuwar halitta ke nan, tsofaffin abubuwa duk sun wuce, ga shi, kome ya zama sabo. 18 Duk wannan kuwa yin Allah ne, wanda ta wurin Almasihu ya canza mu daga zama abokan gābansa zuwa abokan arziki, ya kuma ba mu aikin jawo waɗansu don su ma su zama abokansa. 19 Saƙonmu shi ne Allah yana mai da mutanen duniya duka su zama abokansa ta wurin Almasihu. Allah ba ya lissafta zunubansu a kansu, shi kuma ya ba mu saƙo na sa mutane su zama abokansa.

20 Saboda haka mu wakilai ne na Almasihu, kamar dai Allah ne da kansa yake magana ta wurinmu. A cikin sunan Almasihu, muna roƙonku ku shirya da Allah ku zama abokansa, ba masu gāba da shi ba. 21 Almasihu bai taɓa yin zunubi ba, amma saboda mu Allah ya mai da shi kamar mai zunubi. Ta wannan dalilin ne, cikin Almasihu, za mu iya sami adalcin **Allah**.

4.13: Zab 116.10 **5.10**: Rom 14.10

6 [1] A cikin aikinmu tare da Allah, muna roƙonku ku da kuka
sami alherin Allah, kada ku bari yă zama a banza. [2] Ku ji
abin da Allah ya ce,

"Da lokacin da zan nuna muku alheri ya yi,
Na ji ku.
Da ranar ceto ta zo,
Na taimake ku."

Ku ji! Wannan ne lokacin da za ku karɓi alherin Allah, yau ne ranar da za ku sami ceto! [3] Ba ma so wani yă same mu da laifi a aikinmu. Saboda haka ba mu sa wa wani abin tuntuɓe a hanya ba. [4] A maimakon haka, duk abin da muke yi, muna yi shi don mu nuna cewa mu masu hidimar Allah ne. Muna yin haka cikin jimrewa, da shan wahala, da shan wuya, har da masifu. [5] An yi mana dūka, an sa mu a kurkuku, an kuma ji mana ciwo cikin tashin hankali, mun yi aiki wanda ya sha ƙarfinmu, mun kuma rasa barci da kuma abinci. [6] Ta halinmu mai tsarki, da kuma sanin da muke da shi, da haƙuri tare da kirki, mun nuna cewa mu masu hidimar Allah ne ta wurin Ruhu Mai Tsarki, da kuma ƙaunarmu ta gaske, [7] da saƙonmu mai gaskiya, da kuma ikon Allah. Muna da adalci wanda shi ne kamar makamin da muke riƙe shi a hannun dama da hagunmu. [8] Ana ɗaukaka mu, ana kuma wulaƙanta mu, ana yabonmu, ana kuma zaginmu. An mai da mu masu ƙarya, duk da haka mu dai muna faɗin gaskiya. [9] Kamar ma ba a san mu ba, an kuwa san mu sarai; kamar a bakin mutuwa muke, ga shi kuwa muna da rai; ana ta ba mu horo, amma ba a kashe mu ba, [10] a cikin damuwa, mukan sami dalilin farin ciki. Ko da yake ba mu da kome, duk da haka mun sa mutane da yawa suka yi arziki. Kamar mu ba mu da wani abu, amma kome namu ne.

[11] Ya ku Korintiyawa, ba mu ɓoye muku kome ba, kuma mun nuna muna ƙaunarku sosai. [12] Ai, ba mu ne muka ƙi ku ba, ku ne ba ku buɗe zuciyarku kun yarda da mu ba. [13] Ina maganan nan da ku kamar yadda baba yake yi wa 'ya'yansa magana ne, ku ma ku nuna mana kuna ƙaunarmu.

Kada Ku Haɗa Kai da Marasa Bi

[14] Kada ku haɗa kai da mutanen da ba sa bin Ubangiji. Mutumin kirki zai iya zauna lafiya da mai mugunta? Ko kuma mene ne ya haɗa haske da duhu? [15] Almasihu abokin Shaiɗan ne? Ko kuwa mene ne ya haɗa masu bi da marasa bi? [16] Mene ne ya

6.2: Ish 49.8 **6.5:** A.M. 16.23

haɗa haikalin Allah da gidan tsafi? Mu fa haikali ne na Allah mai rai. Kamar yadda Allah ya ce,

"Zan zauna tare da su,
in yi yawo a cikinsu.
Zan kuma zama Allahnsu,
su kuma su zama mutanena.
17 Saboda haka sai ku fito daga cikin marasa bi,
ku raba kanku da su,
in ji Ubangiji,
kada ku haɗa kanku da wani abu marar tsabta,
ta haka ne zan yarda da ku.
18 Zan zama ubanku,
Ku kuma za ku zama 'ya'yana maza da mata,
in ji Ubangiji Mai Iko duka."

7 1 An yi mana alkawarin waɗannan duka, 'yan'uwa. Saboda haka bari mu tsarkake kanmu daga dukan abin da zai sa jiki da zuciyarmu zunubi, bari kuma mu zama da cikakken tsarki ta wurin zama cikin tsoron Allah.

Bulus Ya Yi Murna don Korintiyawa Sun Tuba

2 Ku nuna kuna ɓaunarmu. Ai, ba mu yi wa kowa laifi ba, ba mu kuma ɓata kowa ba, balle mu cuci wani. 3 Ba ɗora muku laifi nake yi ba da na ce haka, kamar dai yadda na riga na faɗa muku, babu abin da zai iya raba ku da ɓaunarmu, ko a mutuwa ko a rayuwa. 4 Na yarda da ku sosai, ina kuma taɓama da ku. Zuciyata tana da ɓarfafawa sosai. Duk da wahalar da muke sha, ina nan dai, cike da farin ciki.

5 Ko lokacin da muka zo ɓasar Makidoniya ma, ba mu sami hutu ba. Ko'ina muka juya ga fitina, a waje ga tsokana, a ciki kuma tsoro ya cika zuciyarmu. 6 Amma Allahn da yake ɓarfafa wanda ya fid da zuciya, ya ɓarfafa mu da zuwan Titus. 7 Ba don zuwansa ne kawai ya sa muka yi murna ba, amma labarin da ya gaya mana na yadda kuka ɓarfafa shi. Ya gaya mana yadda kuke so ku gan ni sosai, da kuma yadda kuka yi baɓin ciki game da abin da ya faru, da niyyar da kuka yi na goyon bayana. Wannan ne ya sa na ji daɗi sosai.

8 Ko ma wasiɓata ta sa ku baɓin ciki, ban damu ba. A dā kam na yi baɓin ciki, don na ga wasiɓar ta ɓata muku rai, ko da yake dai na ɗan lokaci kaɗan ne kawai. 9 To, kamar dai yadda abubuwa

---

6.16: L. Fir 26.12; Ez 37.27; 1 Kor 3.16; 6.19 **6.17:** Ish 52.11
6.18: 2 Sam 7.14; 1 Tar 17.13; Ish 43.6; Irm 31.9 **7.5:** 2 Kor 2.13

suke, ina farin ciki. Ko da yake ban ji dadîn yadda na ɓata muku rai ba, amma baƙin cikinku ya sa kuka tuba kuka canza halayenku. Baƙin cikinku nufin Allah ne, saboda haka ba mu yi muku laifi a kan abin da muka yi ba. 10 Gama baƙin ciki wanda ikon Allah ne ya sa, zai sa mutum yă tuba, yă koma wurin Allah, ta haka kuma zai sami ceto. Kuma babu "da na sani" a ciki. Amma baƙin cikin da mutum ne ya jawo, yakan kai ga mutuwa. 11 Ku duba ku ga abin da wannan baƙin cikin da Allah ya sa a zukatanku ya jawo muku. Ya sa ku marmarin aikatawa, da nuna cewa kun yi kuskure. Ya sa kuka yi fushi, kuka kuma ji tsoro. Ya sa kuka sa zuciya, kuka kuma sa aniya. Ya sa kuna a shirye ku ga an yi horon da ya dace. Game da wannan sha'ani kam, lallai ta kowace hanya kun nuna cewa ba ku da laifi. 12 Lokacin da na rubuto wancan wasiƙar, ban damu da mutumin da ya yi laifin ba, ko kuma mutumin da aka yi masa laifin. A maimako na rubuta ne don in bayyana muku dalla-dalla cewa Allah ya san kun yarda da mu sosai. 13 Dalilin da ya sa muka sami ƙarfafawa a zukatanmu ke nan.

Ban da ƙarfafawar zukatanmu, har wa yau mun ƙara farin ciki ƙwarai saboda irin farin cikin da Titus yake ciki, domin dukanku kun taimaka a kan ƙarfafawa da ya samu. 14 Don ko da na gaya masa ina taƙama da ku, ban ji wata kunya ba. Kamar yadda duk abin da muka gaya muku gaskiya ne, haka kuma taƙamarmu game da ku ta zama gaskiya a idon Titus. 15 Kaunar da Titus yake yi muku tana ta ƙaruwa sosai yayin da ya tuna da biyayyarku duka, da kuma irin yawan ban girmar da kuka nuna masa lokacin da kuka karɓe shi. 16 Ina farin ciki yanzu don na amince da ku ƙwarai da gaske.

Bayarwar Masu Bi

8 1 Yanzu kuma, 'yan'uwana muna so ku san abin da alherin Allah ya yi a cikin jama'un masu bi a Makidoniya. 2 Gama sun sha wuya sosai saboda tsananin wahalar da suka shiga ciki, har yawan farin cikinsu ya kai su ga yin alheri ta bayarwa ga wadansu, ko da yake suna cikin tsananin talauci. 3 Na tabbata sun bayar daidai ƙarfinsu har ma fiye da haka. Sun bayar da yardar rai, ba don dole ba. 4 Sun roƙe mu mu ba su damar hidimar taimakawa, don su ma su sami damar shiga cikin wadanda suke taimakon masu bin da suke a Yahudiya. 5 Har ma suka bayar fiye da yadda muka yi tsammani. Da farko dai, sun miƙa kansu ga

8.1-4: Rom 15.26

Ubangiji, daga nan kuma sai suka ba da kansu gare mu, kamar
yadda Allah yake so. 6 Da ganin haka sai muka roƙi Titus yă ci
gaba da wannan aikin tara bayarwa na yardar rai, tun da yake shi
ne ya fara shi. 7 A cikin kome kuna a kan gaba, ko ta
bangaskiyarku cikin Almasihu, ko cikin magana, ko a sanin
gaskiya, ko a son aikin hidima, da kuma ƙaunar da kuke mana.[e]
Saboda haka muna so ku ci gaba cikin wannan alherin bayarwa
hannu sake.

8 Ba wai dole nake sa ku ba, sai dai ina nuna muku yadda
waɗansu sun nuna ƙwazo. Wannan zai gwada irin ƙaunar da kuke
da ita. 9 Gama kun san alherin Ubangijinmu Yesu Almasihu. Ko
da yake yana cike da kome, duk da haka sai ya zama matalauci
dominku. Ta talaucinsa kuma ku sami arziki a gaban Allah.
10 Shawarar da zan ba ku ita ce, zai fi kyau ku gama abin da kuka
fara a shekarar da ta wuce, ba wai kawai kun bayar ba ne, a'a,
ai, kuna da niyyar yi. 11 To, sai ku gama aikin da irin zuciyar da
kuka fara, ku yi wannan gwargwadon ƙarfinku. 12 Idan kuna da
zuciyar bayarwa, Allah zai ji daɗin bayarwar, wato, idan kun
bayar gwargwadon ƙarfinku. Allah ba ya so ku yi abin da ƙarfinku
bai kai ba. 13 Ba wai ina so in ba wa waɗansu abu mai sauƙi sa'an
nan ku kuma a ba ku mai nauyi ba ne. 14 Amma don a raba aikin
nan daidai yadda ya kamata, sai ku taimake su a yanzu da kuna
da hanyar taimako. Ku kuma lokacin da ba ku da wani abu, su
kuma suna da shi, sai su ma su taimake ku. Ta haka kome zai
zama daidai. 15 Kamar yadda Rubutaccen Maganar Allah ya ce,
"Wanda ya tara mai yawa, abin nan da ya tara bai fi ƙarfinsa ba,
wanda ya tara kaɗan kuwa, wannan ɗin ma bai kāsa masa ba."

Titus da Abokansa

16 Mun gode wa Allah wanda ya sa Titus ya ɗauki niyyar son
taimakonku, kamar yadda na so. 17 Ba wai kawai ya yarda yă je
wurinku kamar yadda muka roƙe shi yă yi ba, amma ya so yă zo
kamar yadda ya riga ya ɗauki niyya. 18 Ga shi, mun aiko ɗan'uwan
nan tare da shi, wanda ya yi suna wajen yin bishara a dukan
jama'un masu bi. 19 Ban da haka ma, jama'un masu bi sun zaɓe
shi yă rika tafiya tare da mu a kan wannan aikin alheri wanda
muke yi saboda ɗaukakar Ubangiji, kuma don mu nuna cewa
muna da niyyar taimako. 20 Muna gudun kada kowa yă zarge mu

8.15: Fit 16.18

[e] **8.7 kuke mana**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "muke muku" ne a nan.

a kan yadda muke bi da kyautan nan da aka ba mu da yardar rai.
21 Niyyarmu ita ce mu yi abin da ya fi kyau, ba wai a gaban
Ubangiji kaɗai ba, amma har ma a gaban mutane.

22 Muna kuma aiko da ɗan'uwanmu tare da su, wanda sau da
yawa muka gwada muka kuma tabbatar da niyyarsa a kan
abubuwa iri-iri. A yanzu kuma da ya amince da ku, yana so yă
taimaka sosai. 23 Ku tuna cewa Titus abokin aikina ne; da ni da
shi muna aikin nan saboda ku ne. Sauran 'yan'uwanmu waɗanda
suke tare da shi, jama'un masu bi ne suka aiko su, aikinsu yana
kawo ɗaukaka ga Almasihu. 24 Ku nuna wa waɗannan mutanen
irin ƙaunar da kuke musu. Jama'un masu bin da suka aike su za
su ji abin da kuka yi, wannan zai tabbatar musu cewa taƙamar
da muke yi a kanku gaskiya ce.

Taimako ga Masu Bi

9 1 Ba lallai sai na rubuta muku a kan taimakon nan don masu
bi ba, 2 domin na san niyyarku, har ma ina taƙama da ku
gun mutanen Makidoniya a kan haka. Ina ce musu ku mutanen
Akaya kun yi shiri tun a shekarar da ta wuce. Irin aniyan nan
da kuke da ita ta sa su ma suka tashi tsaye. 3 Yanzu kuma, ga
shi ina aika waɗannan 'yan'uwa, don kada taƙamar da muke yi
a kanku a wannan aiki ta zama maganar banza da wofi. Amma
ina so ku zauna da shiri, kamar yadda dā na shaida za ku yi.
4 Don idan na zo tare da waɗansu masu bi daga Makidoniya, ba
na so su zo su samu ba ku riga kun shirya taimakonku ba. In
haka ya faru, zan sha kunya saboda yawan taƙamar da na yi a
kanku, ba ni kaɗai zan sha kunyar ba, har ma da ku. 5 Saboda
haka na ga dai ya yi kyau in roƙi 'yan'uwan nan su zo kafin ni,
don su tattara abubuwan da kuka yi alkawari za ku bayar, domin
a same su a shirye. Wannan zai nuna cewa da yardar rai kuka
bayar, ba a kan dole ba.

6 Ku tuna, mutumin da ya shuka iri kaɗan, zai girbe amfanin
gona kaɗan, amma mutumin da ya shuka iri da yawa, zai sami
amfanin gona da yawa. 7 Kowa yă bayar kamar yadda ya yi niyya,
ba tare da ɓacin rai ko tilas ba, domin Allah yana son mai bayarwa
da daɗin rai. 8 Allah kuma yana iya ba ku albarka fiye da abin
da kuke bukata, domin a ko yaushe ku sami dukkan abin da kuke
bukata, har ma fiye da haka, domin ku yi aikin alheri. 9 Kamar
yadda Rubutaccen Maganar Allah ya ce,

"Ya ba wa mutanen da ba su da kome abubuwa da yawa.

8.21: K. Mag 3.4

Aikinsa na alheri yana nan har abada."
10 Allah ne yake ba wa mai shuka iri yă shuka, yă kuma ba
shi abinci. Saboda haka Allah zai ba ku iri don ku shuka, shi ne
kuma zai sa irin yă yi girma. Ta haka ne zai sa bayarwan nan
taku ta yardar rai ta ƙara muku albarkar ayyukanku na alheri. 11 A
koyaushe zai albarkace ku cikin dukkan kome don ku zama masu
bayarwa da dadîn rai kullum. Ta haka mutane da yawa za su gode
wa Allah saboda kyautai waɗanda za ku aika musu ta wurinmu.
12 Domin aikin nan na alherin da kuke yi ba biyan bukatar masu
bi kaɗai yake yi ba, har ma yana ƙara kawo godiya ga Allah.
13 Kuma saboda abin shaidar da wannan aikin yake kawowa game
da ku, yawanci za su ɗaukaka Allah don biyayyarku ga bisharar
Almasihu, wadda kuka gaskata da ita, kuma saboda taimakon da
kuka yi musu da sauran mutane duka hannu sake. 14 Su kuwa za
su yi muku addu'a, suna kuma tunaninku a zuciyarsu saboda
alherin nan wanda ya wuce gaban misalin da Allah ya yi muku.
15 Mu gode wa Allah saboda wannan kyautar da ya yi mana,
kyautar da ta fi ƙarfin magana.

Bulus Ya Kāre Kansa game da Aikinsa

10 1 Ni Bulus da kaina, ina roƙonku, ni da ake ce da ni "mai
sauƙin kai" idan ina tare da ku, amma "mai matsawa"
in ba na tare da ku. Bisa ga tawali'u da sauƙinkai na Almasihu,
2 ina roƙonku, kada ku tilasta ni in matsa muku sa'ad da na zo,
domin na san zan iya matsa wa waɗanda suke cewa wai abin
da muke yi, sha'anin duniya ne. 3 Ko da yake muna zama a
duniya, yaƙin da muke yi ba irin na duniya ne ba. 4 Gama
makamanmu na yaƙi ba na duniya ba ne, na ikon Allah ne,
waɗanda muke amfani da su don rushe makamai masu ƙarfin
da suke kāre abokan gābanmu. 5 Muna ka da kowane mai mūsu,
muna rushe dukkan wani abin da zai hana sanin Allah, muna
kuma sa mutane su yi tunani cikin bauta da biyayya ga
Almasihu. 6 A shirye muke mu ba wa kowa da ya ƙi yin biyayya
horo, in dai kun tabbata kuna biyayya.
7 Ku dubi abin da yake a bayyane mana!*f* Idan wani ya ce shi
na Almasihu ne, bari wannan mutum yă sāke tunani, zai gane
cewa mu ma na Almasihu ne. 8 Ko da ina taƙama a kan ikon nan
namu da Ubangiji ya ba mu saboda gina ku, ba don rushe ku ba,

---

9.9: Zab 112.9 **9.10:** Ish 55.10

f **10.7 Ku dubi abin da yake a bayyane mana:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "Kuna duba abubuwa yadda ido yake gani ne kawai."

ba ni da abin jin kunya a ciki. 9 Ba na so ku yi tsammani tsoro
nake so in ba ku a cikin wasiƙuna. 10 Ana cewa, "Wasiƙun Bulus
masu tsanani da ƙarfi ne, amma idan yana nan tare da mu da
kansa, shi ba mai magana mai ƙarfi ba ne, kuma maganarsa ba
kome ba ne." 11 Dole irin mutanen nan su gane cewa babu wani
bambanci tsakanin abin da muka rubuta a cikin wasiƙunmu in ba
ma nan, da kuma abin da za mu yi in muna tare da ku.

12 Wane mu! Ai, ba mu isa mu gwada, ko mu ɗauki kanmu
kamar mutanen da suke gani sun fi kowa ba. Su waɗannan mutane
masu auna kansu da juna, suna kuma neman bambanci tsakaninsu
da juna, wawaye ne!

13 Amma dai ba za mu yi taƙama fiye da yadda ya kamata
ba, sai dai mu tsaya a kan iyakar da Allah ya yanke mana, wadda
ta haɗa har da ku. 14 Ai, ku ma kuna cikin iyakar da Allah ya ba
ni, saboda haka ban wuce gona da iri ba da na je har wurinku
don wa'azin Labari Mai Daɗi na Almasihu. 15 Taƙamarmu ba fiye
da yadda ya kamata take ba, ba ta kuma shafi aikin waɗansu ba.
Amma muna sa zuciya bangaskiyarku za ta riƙa ƙaruwa, ta haka
kuma filin aikinmu a cikinku yă riƙa ƙaruwa sosai. 16 Ta haka za
mu yi wa'azin Labari Mai Daɗi a waɗansu ƙasashe gaba da ku,
ba tare da neman suna a aikin da wani ya riga ya yi a filin da
aka sa shi ba.

17 Amma kamar yadda Rubutaccen Maganar Allah ya ce,
"Duk wanda zai yi taƙama, yă yi taƙama da Ubangiji." 18 Gama
ba mai yabon kansa ake yarda da shi ba, sai dai mutumin da
Ubangiji ya yaba.

Bulus da Manzannin Karya

11 1 Ina fata za ku yi haƙuri da ni ko ina ɗan wawanci. Sai
ku dai yi haƙuri da ni! 2 Ina kishi saboda ku, da irin kishin
da Allah yake yi a kanku. Na shirya aurenku da Almasihu, ina
kuma so ku zauna da tsarki, don in miƙa ku gare shi kamar yadda
ake miƙa amarya mai tsarki ga wanda shi ne kaɗai mijinta.
3 Amma ina tsoro kada yă zama abin da ya faru da Hawwa'u, yă
faru da ku. Maciji ya ruɗe ta da wayonsa har ta yi zunubi. Haka
ku ma, tunaninku zai iya zama marar kirki, ta haka, ba za ku
kasance da cikakken ba da kai da kuma aminci cikin Almasihu
ba. 4 Gama kuna da saukin yarda da waɗanda suke zuwa wurinku.
Kun yarda da koyarwarsu a kan Yesu, ko da yake ta yi dabam
da wadda muka yi wa'azi. Kun yarda da ruhun da suka yi muku

10.17: Irm 9.24 **11.3:** Far 3.1-5,13

alkawari, wannan ruhu kuwa ba Ruhu Mai Tsarki da kuka karɓa ba ne. Kun kuma yarda da bishararsu, ko da yake ta yi dabam da wadda muka yi muku.

5 Ban yi tsammani waɗannan da kuke ce da su "manyan manzanni" sun fi ni da wani abu ba. 6 Mai yiwuwa ba a koyar da ni a magana ba, amma ina da sani. Mun nuna muku wannan a ta kowace hanya.

7 Na yi muku wa'azin Labari Mai Daɗin nan na Allah a kyauta. Na ɗauki matsayi marar girma, don a ɗaga ku zuwa babban matsayi. Na yi laifi ke nan? 8 Na karɓo kuɗi daga waɗansu jama'un masu bi don aikina a cikinku. Zan ma ce na yi musu ƙwace domin in yi muku aiki. 9 Lokacin da nake tare da ku, na bukaci kuɗi, duk da haka ban dame ku ba. 'Yan'uwa masu bin da suka zo daga Makidoniya ne suka kawo mini duk abin da nake bukata. Ban ɗora muku nauyi a lokacin ba, kuma zan ci gaba da yin haka. 10 Bisa ga gaskiyar Almasihu da take a cikina ta sa na ce ba wanda ya isa a duk faɗin ƙasar Akaya yă ce in bar yin taƙama. 11 Ina faɗin haka wai don ba na ƙaunarku ne? Allah ya san ina ƙaunarku.

12 Zan ci gaba da matakin nan nawa na ƙin yarda da taimakon kuɗi daga gare ku, domin in hana waɗannan "manyan manzannin" wani dalilin taƙama cewa, ai, suna aiki daidai da mu. 13 Irin mutanen nan ba manzannin gaskiya ba ne, amma masu aikin ƙarya ne. Suna mai da kansu kamar manzannin Almasihu. 14 Ba abin mamaki ba ne, domin ko Shaiɗan ma da kansa yakan mai da kansa kamar mala'ikan haske. 15 Saboda haka ba abin mamaki ba ne idan bayinsa sun mai da kansu kamar masu aikin adalci. A ƙarshe za su sami ladan da ya yi daidai da aikinsu.

Wahalar da Bulus Ya Sha cikin Aikinsa

16 Ina sāke cewa, kada wani yă yi tsammani wai ni wawa ne. Amma idan kuna tsammanin haka ne, to, ku yarda da ni kamar wawa, don ni ma in ɗan sami abin taƙama. 17 Ba wai ina bin abin da Ubangiji ya umarce ni da ina taƙama haka ba; a wannan zance na taƙama dai, ina magana kamar wawa ne. 18 Da yake akwai waɗansu masu taƙama kamar yadda mutanen duniya suke yi, bari ni ma in yi haka. 19 Ku kam kuna da wayo sosai, har kuna jimre wa wawaye da murna! 20 Gama in wani ya sa ku bauta, kukan jimre masa, ko ya yi muku ƙwace, ko ya more ku, ko ya nuna

11.9: Filib 4.15-18

muku isa, ko kuwa ya mare ku a fuska. 21 Ina jin kunya in ce
mun nuna kāsawa da ba mu yi wadannan abubuwan ba!
Amma idan wani yana daga kai a kan wani abu ne, ni ma zan
yi haka. A nan dai ina magana ne kamar wawa! 22 Idan su
Ibraniyawa ne, ni ma haka. Idan su Isra'ilawa ne, ni ma haka. In
su zuriyar Ibrahim ne, ni ma haka. 23 In su masu hidimar Almasihu
ne, ni na fi su! (Ina magana kamar ina hauka ne fa!) Ai, na fi su
ƙoƙari ƙwarai da gaske, ga shan dauri, na sha dūka da yawa, na
kuma sha shiga hatsarin mutuwa sau da yawa. 24 Sau biyar
hukumar Yahudawa suka yi mini bulala talatin da tara.[g] 25 Sau
uku hukumar Romawa suka yi mini bulala. An kuma taɓa jefe ni
da duwatsu sau daya. Sau uku jiragen ruwa sun faffashe ina ciki.
Na kuma taɓa kwana har na yini a cikin teku, kafin aka zo aka
cire ni. 26 A cikin tafiye-tafiyena na gamu da hatsari a koguna,
na kuma gamu da hatsari a hannun 'yan fashi. Na sha shiga hatsari
daga hannun 'yan kabilarmu, na kuma sha shiga hatsari a hannun
wadanda ba Yahudawa ba. Na sha shiga hatsari a birane, na sha
shiga hatsari a daji, na sha shiga hatsari a teku, na kuma sha shiga
hatsari a hannun 'yan'uwan ƙarya. 27 Na sha fama, da wuya, da
rashin barci, da yunwa, da ƙishin ruwa. Sau da yawa na rasa
abinci, na sha sanyi, na kuma rasa rigar da zan sa. 28 Ban da
wadansu abubuwa dabam-dabam kuma, kowace rana ina da
nauyin kula da dukan jama'un masu bi. 29 Idan wani ya kāsa,
nakan ji kamar ni ne na kāsa, idan kuma an sa wani ya fāɗi cikin
zunubi, abin yakan sa ni in ji fushi sosai.
30 In ma ya zama lallai ne in yi taƙama, to, sai in yi taƙama
da abubuwan da suka nuna kāsawata. 31 Allah ya san ba ƙarya
nake yi ba, shi da yake Allah, kuma Uban Ubangiji Yesu
Almasihu. Bari a yi masa yabo har abada! 32 Lokacin da nake
Dimashƙu, gwamnan da yake ƙarƙashin sarki Aretas ya tsare
ƙofofin birnin Dimashƙu don yă kama ni. 33 Amma abokaina suka
sauko da ni a cikin kwando daga katangar birnin, na kuɓuce masa.

Abubuwan da Yesu Ya Bayyana wa Bulus cikin Ru'uya

12 1 Ko da yake ba zā ta amfana kome ba, dole ne in yi
taƙama. A yanzu, zan ci gaba da zance a kan abubuwan
da Ubangiji Yesu Almasihu ya bayyana mini kamar a mafarki da

11.23: A.M. 16.23 **11.24:** M. Sh 25.3 **11.25:** A.M. 16.22; 14.19
11.26: A.M. 9.23; 14.15 **11.32-33:** A.M. 9.23-25

[g] **11.24 bulala talatin da tara:** Wannan shi ne horo mai zafi da za a iya yi wa Bayahude a jiki. (Dubi M. Sh 25.1-3).

kuma cikin ru'uya. 2 Na san wani mutum[h] wanda yau shekara
goma sha hudu ke nan, aka ɗauke shi zuwa sama na uku bisa ga
ikon Almasihu, ko yana cikin jiki ne, ko ba cikin jiki ba, ban sani
ba, Allah kaɗai ya sani. 3 Na kuma san mutumin nan, an ɗauke
shi zuwa sama na uku,[i] ko yana cikin jiki ne, ko ba cikin jiki ba,
ban sani ba, Allah kaɗai ya sani. 4 A can ya ji waɗansu
maganganun da ba za a iya faɗa ba, irin waɗanda ɗan Adam ba
zai iya yin magana a kai ba. 5 Zan yi taƙama a kan mutumin nan,
amma ba zan yi taƙama da kaina ba, sai dai a kan abubuwan da
suka nuna kāsawata. 6 Da na so yin taƙama, ba zan zama wawa
ba, don zan faɗa gaskiya ne. Amma ba zan yi taƙama ba, don ba
na so wani yă ɗauke ni fiye da yadda yake ganina, da yadda ya
taɓa ji daga gare ni.

7 Don a sa kada in yi taƙama da waɗannan mafifitan ru'uya
sai an aiko mini wata cuta ƙamar yadda ƙaya take zafi a jiki.
Wannan ya zama ƙamar wanin da Shaiɗan ya aiko ne don yă
dinga ba ni wuya, don kuma yă hana ni yawan ɗaga kai. 8 Sau
uku na roƙi Ubangiji domin in rabu da wannan abu, 9 amma ya
ce mini, "Alherina ya ishe ka, domin ta wajen kāsawarka ake
ganin cikakken ikona." Saboda haka da murna zan ƙara taƙama
da kāsawan nan tawa domin ikon Almasihu yă zauna tare da ni.
10 Saboda haka na gamsu da kāsawata, da cin mutuncin da ake yi
mini, da shan wuya, da tsanani, da masifu saboda Almasihu. Don
idan ina da kāsawa, a nan ne nake da ƙarfi.

Damuwar Bulus game da Masu Bi a Korinti

11 Na yi wawanci kam, amma ku kuka sa ni. Ku ne kuwa ya
kamata ku yabe ni. Ko da yake ni ba kome ba ne, bai zama cewa
"manyan manzannin" nan naku sun fi ni ba. 12 Allah ya yi
abubuwan ban mamaki da al'ajabi ta wurina a cikinku, da na yi
aikina cikin haƙuri. Waɗannan abubuwan ban mamaki, sun shaida
cewa ni manzo ne na gaskiya. 13 Ta wace hanya ce na nuna cewa
ba ku zama daidai da waɗansu jama'un masu bi ba? Ko kuwa
domin na hana ku ku taimake ni da kuɗi? Ku yafe mini don abin
nan da na yi muku!

14 Ina a shirye in ziyarce ku sau na uku yanzu. Ba zan sa
muku wani kaya ba, domin ku nake so, ba kuɗinku ba. Gama bai

[h] **12.2 wani mutum:** Wannan mutumin da Bulus yake magana a kai, Bulus ne da kansa.

[i] **12.3 sama na uku:** Da Helenanci an rubuta "Faradais" ne a nan. Wato, inda Allah yake.

kamata yara su ɗauki nauyin iyayensu ba, sai dai iyaye su ɗauki nauyin yaransu. 15 Zan ji dadî in kashe duk abin da nake da shi, har da kaina ma, don in taimake ku. Za ku rage ƙaunar da kuke yi mini don ina ta ƙara ƙaunar da nake yin muku?

16 Za ku yarda da ni cewa ban zama muku wani kaya ba. Amma wani zai ce na yi muku wayo ne, na rinjaye ku da ƙarya. 17 Na cuce ku ne ta wurin wani daga cikin waɗanda na aiko gare ku? 18 Na roƙi Titus yă je, na kuma aiko da wani ɗan'uwa mai bi tare da shi. Za ku ce Titus ya cuce ku ne? Ashe, ni da shi ba manufa ɗaya take bi da mu ba? Ba kuma hanya ɗaya muke bi ba?

19 Kada ku yi tsammani cewa duk wannan lokacin, muna ƙoƙarin kāre kanmu gare ku ne. Allah ne shaidarmu, muna faɗin gaskiya cikin Almasihu. Kuma ko mene ne muka yi, ya ku waɗanda nake ƙauna, mun yi ne domin ku ginu. 20 Ina tsoro kada wataƙila idan na zo in same ku ba yadda nake so ba, ku kuma ku gan ni ba yadda kuke so ba. Ina tsoro zan tarar da faɗa da kishi, da zafin rai, da sonkai, da zagi, da gulma, da ɗaga kai, da kuma tashin hankali. 21 Ina tsoro cewa in na sāke kai wurinku, Allahna zai sa in ji kunya a gabanku. Ina tsoro kada in yi ɓakin ciki saboda mutane da yawa da suke ta yin zunubi a dā, waɗanda ba su tuba daga aikin lalata ba, da iskanci, da waɗansu irin ayyukan nan dai.

Gargaɗin Bulus na Karshe

13 1 Wannan zai zama zuwana na uku a wurinku. "Lallai ne a tabbatar da kowace magana a bakin shaidu biyu ko uku" kamar yadda Rubutaccen Maganar Allah ya faɗa. 2 A zuwana na biyu wurinku na gargaɗe waɗanda suka yi zunubi da sauran mutane duka su daina yin zunubi. Yanzu da ba na nan tare da ku, ina maimaita irin gargaɗin nan domin idan na zo ba wanda zai kuɓuce wa horon nan. 3 In dai kuna so ku sami tabbaci cewa Almasihu yana magana ta wurina, to, ga tabbacin: Almasihu bai kāsa ba a cikinku, a maimakon haka ya nuna ikonsa a cikinku. 4 Ko da yake an gicciye shi ne da rashin ƙarfi, duk da haka yana da rai ta ikon Allah. Mu ma marasa ƙarfi ne a cikinsa, amma game da aikin da za mu yi a cikinku, muna da rai tare da shi, ta ikon Allah.

5 Ku gwada kanku gaba ɗaya don ku san ko kuna bin Yesu Almasihu cikin aminci. Ku riƙa auna kanku. Ashe, ba ku sani

13.1: M. Sh 17.6; 19.15

cewa Almasihu yana a cikinku ba? Lallai yana nan, wato, in ba ku fādì a wannan gwadawar ba. 6 Ina fata za ku san cewa mu ba mu kāsa ba. 7 Ba wai muna ƙoƙari mu mai da kanmu kamar mun yi nasara ko ba. Muna addu'a ga Allah cewa kada ku yi mugun abu, amma ku yi abin da yake da kyau, ko da yake mutane za su gani kamar mun kāsa ne. 8 Gama za mu bi bayan gaskiya, ba za mu iya yin abin da yake gāba da ita ba. 9 Murna muke yi in ba mu da ƙarfi, amma ku kuwa kuna da ƙarfi. Kuma muna addu'a ku zama cikakku. 10 Shi ya sa na rubuta muku wannan tun ba na nan tare da ku, don in na zo, kada yă zama mini dole in yi muku tsanani game da yin amfani da ikon nan da Ubangiji ya ba ni, ikon ginawa, ba na rushewa ba.

Maganar Ƙarshe

11 A ƙarshe dai, 'yan'uwana, sai wata rana. Ku yi ƙoƙarin zama cikakku, ku ji roƙona, ku yarda da juna ku yi zaman lafiya da juna. Ta haka Allah mai ƙauna da salama zai kasance tare da ku. 12 Ku gai da juna da gaisuwar ƙauna. 13 Dukan masu bi suna gaishe ku. 14 Alherin Ubangijinmu Yesu Almasihu, da ƙaunar Allah, da zumuntar Ruhu Mai Tsarki, su kasance tare da ku dukka.

WASIKAR BULUS ZUWA GA
GALATIYAWA

Gabatarwa

Manzo Bulus ya rubuta wannan wasiƙa saboda wani rikicewar da ya taso cikin masu bin Yesu na ƙasar Galatiya, inda a dā Bulus ya yi wa'azi.

Rikicewar ita ce, Yahudawan da suke masu bi sun nace cewa dole waɗanda suka tuba su bi dukan al'adu na Yahudawa da kuma Dokar Musa kafin su sami ceto. Amma Bulus ya nace cewa ana samun ceto ta wurin alherin Allah cikin Yesu ne ba ta wurin bin Dokar Musa ba. Bin Dokar Musa yana sa mutane su zama kamar bayi.

Wasiƙar ta ƙarfafa masu bi su miƙa kansu ga Almasihu domin su zama mutane waɗanda aka 'yantar da su. Wasiƙar ta nuna Ruhun Allah yakan zauna cikin masu bi har yă sa su yi abin da Allah yake so. Ruhu Mai Tsarki kuwa yakan fid da ayyuka masu kyau kamar ƙauna, da farin ciki, da salama, da haƙuri.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-10
Bulus ya yi bayani game da matsayinsa na manzo 1.11—2.21
Ceto ta wurin bangaskiya yake 3.1—4.31
Kira zuwa ga zama cikin Allah 5.1—6.10
Maganar ƙarshe 6.11-18

Gaisuwa

1 [1] Daga Bulus manzo. Ba daga wurin mutane ko ta wurin mutum ne kiran ya zo mini ba. Amma kiran ya zo mini ne daga Yesu Almasihu da Allah Uba wanda ya ta da shi daga matattu. [2] Dukan 'yan'uwan da suke tare da ni a nan su ma suna gai da dukan jama'un masu bi da suke a Galatiya.

3 Alheri da salama daga Allah Ubanmu da Yesu Almasihu su kasance tare da ku.

4 Shi Yesu Almasihu ya ba da kansa domin zunubanmu, don yă cece mu daga wannan mugun zamani. Wannan kuwa bisa ga nufin Allah Ubanmu ne. [5] Bari ɗaukaka ta tabbata a gare shi har abada abadin. Amin.

Ba Wata Bishara Dabam

6 Abin nan da kuke yi ya ba ni mamaki sosai. A cikin ɗan ƙanƙanin lokaci haka kuna so ku bar bin wanda ya kira ku ta
wurin alherin Almasihu, har ma kuna komawa zuwa wata
sabuwar bishara. 7 Ai, babu wata bishara dabam. Na faɗa haka ne
don akwai waɗansu da suke ta da hankalinku, suna kuma ƙoƙari
su canza gaskiyar bisharar Almasihu. 8 Amma ina gaya muku,
idan waninmu zai yi muku wata bishara dabam da wadda muka
yi, ko shi mala'ika daga sama ne, ko mu da kanmu ma, to, bari
yă zama la'ananne! 9 Kamar yadda muka riga muka faɗa muku
a dā, ina sāke faɗa muku yanzu cewa duk wanda ya yi muku
wa'azin wata bishara dabam da wadda kuka riga kuka ji, to, bari
yă zama la'annane!

10 Ko za a ce, ta wurin yin wannan magana haka ina ƙoƙari
in sa mutane su yarda da ni ne? A'a. Abin da nake so shi ne,
Allah yă yarda da abin da nake yi. Kuna tsammani ina ƙoƙari in
faranta wa mutane zuciya ne? A'a. Da mutane ne nake faranta
wa zuciya, da ban zama bawan Almasihu ba.

Yadda Bulus Ya Zama Manzo

11 'Yan'uwana, ina so in faɗa muku cewa bisharan nan da
nake muku wa'azinta, ba daga wurin mutum ta fito ba. 12 Ban
karɓe ta daga wurin mutum ba. Kuma ba wanda ya koya mini
ita; Yesu Almasihu da kansa ne ya bayyana mini ita.

13 Kun ji irin zaman da dā na yi a cikin addinin Yahudanci,
yadda na ba wa 'yan jama'ar masu bin Allah wahala mai zafi
ƙwarai da gaske, har na yi ta ƙoƙari in kashe su. 14 Kun kuma
san yadda a cikin addinin Yahudanci na fi yawancin Yahudawa
waɗanda muka yi girma tare. Na yi ƙoƙarin bin al'adun
kakanninmu da gaske sosai.

15 Amma Allah cikin alherinsa ya zaɓe ni tun kafin a haife
ni, ya kuma kira ni, har ya yarda 16 ya buɗe mini ido don in san
Dansa Yesu, domin in yi wa'azin Labari Mai Daɗi ga waɗanda
ba Yahudawa ba. Da ya yi haka ban nemi shawara daga wajen
wani mutum ba, 17 ban kuma je Urushalima wurin waɗanda suka
riga ni zama manzanni ba. Abin da na yi shi ne, nan da nan na
je ƙasar Larabawa, sa'an nan na komo Dimashƙu. 18 Sai bayan
shekara uku ne na tafi Urushalima domin in ga Kefas wato, Siman
Bitrus. Na kuwa yi kwana goma sha biyar tare da shi. 19 Bayan

1.13: A.M. 8.3; 22.4-5; 26.9-11 1.14: A.M. 22.3
1.15-16: A.M. 9.3-6; 22.6-10; 26.13-18 1.18: A.M. 9.26-30

wannan kuma, ban ga ko ɗaya daga cikin sauran manzannin ba, sai dai Yakubu ɗan'uwan Ubangiji. 20 Abin nan da nake rubuta muku, ba ƙarya ba ne, gaskiya ne; a gaban Allah nake faɗa.

21 Daga baya kuma, na tafi ƙasar Suriya da ta Kilikiya. 22 Amma a wancan lokaci, jama'un masu bin Almasihu da suke cikin Yahudiya, ba su san ni ido da ido ba tukuna. 23 Sun dai ji kawai an ce, "Mutumin nan wanda dā yake wahalar da mu, ga shi yanzu yana sanar da maganar bangaskiyan nan da dā yake ɓatawa!" 24 Sai suka ɗaukaka Allah saboda abin da ya yi ta wurina.

Sauran Masu Bishara Sun Yarda da Bulus

2 1 Bayan shekara goma sha huɗu na sāke komawa zuwa Urushalima. A wannan lokacin na tafi tare da Barnaba da kuma Titus. 2 Allah ne ya nuna mini a cikin ru'uya cewa in tafi. Da na kai can, sai na haɗu da waɗansu shugabannin jama'ar masu bi, na bayyana musu yadda nake yin bishara ga waɗanda ba Yahudawa ba. Na yi musu wannan bayani, su kaɗai, kada ƙwazon da nake yi cikin aikin nan, ko ƙoƙarin da na riga na yi, su zama ba amfani. 3 Titus abokin tafiyata ma, ko da yake shi mutumin Hellas ne ba wanda ya sa shi dole a yi masa kaciya. 4 Maganar kaciya ta tashi ne saboda 'yan'uwan nan na ƙarya waɗanda suka shigo a ɓoye. Sun shigo ne domin su ɓata wannan 'yancin da muke da shi ta wurin Almasihu Yesu. Suna so su mai da mu bayi, 5 amma ko kaɗan ba mu yarda musu ba, saboda mu tsare muku gaskiyar bishara.

6 Amma su mutanen nan da aka ɗauka cewa su manya ne, ba su ƙara kome a kan koyarwar da nake yi ba, (a ganina ko su wane ne duk ɗaya ne a wurina, domin Allah ba ya nuna bambanci). 7 Su dai sun ga yadda Allah ya yarda ya ba ni aikin wa'azin bishara ga waɗanda ba Yahudawa ba kamar yadda aka ba wa Bitrus aikin wa'azi ga Yahudawa. 8 Ga shi Allah wanda ya yi aiki a zuciyar Bitrus don hidima ga Yahudawa, shi ne kuma ya yi aiki a zuciyata don amfanin waɗanda ba Yahudawa ba.

9 Da ganin yadda Allah ya nuna mini alherinsa haka, su Yakubu, da Bitrus da Yohanna, suka yarda. Su da aka ɗauke su shugabannin jama'ar masu bi suka karɓe ni da Barnaba da zuciya ɗaya. Mun yarda da juna cewa mu za mu je wurin waɗanda ba Yahudawa ba, su kuwa su je wurin Yahudawa. 10 Sai dai suka

---

2.1: A.M. 11.30; 15.2 **2.6:** M. Sh 10.17

tuna mana cewa kada mu manta da talakawan da suke wajensu. Ni kuwa tun dā ma nake marmarin yin haka ƙwarai.

Bulus Ya Tsawata wa Bitrus a Antakiya

11 A lokacin da Bitrus ya zo Antakiya, sai na tsawata masa
fuska da fuska domin laifinsa a fili yake. 12 Da farko, yana cin
abinci tare da masu bi na waɗanda ba Yahudawa ba. Amma bayan
da Yakubu ya aiki waɗansu zuwa Antakiya, sai Bitrus ya janye,
ya ware kansa. Ya yi haka ne domin yana tsoron waɗanda suke
so a yi wa waɗanda ba Yahudawa ba kaciya.
13 Haka ma sauran Yahudawa masu bi sun yi wannan aikin
rashin gaskiya kamar Bitrus, har ma sun ɗauki hankalin Barnaba
a cikin wannan rashin gaskiya. 14 Amma da na ga ba sa yin abinsu
bisa ga gaskiyar bishara, sai na ce wa Bitrus a gaban kowa duka,
"Kai Bayahude ne, amma kana bin al'adun waɗanda ba
Yahudawa ba. Yanzu za ka sa wa waɗanda ba Yahudawa ba dole
ne su bi al'adun Yahudawa?"

An Ceci Yahudawa da Sauran Waɗanda ba Yahudawa ba ta Hanya Daya

15 "Ko da yake mu Yahudawa ne bisa ga haihuwa, ba
waɗanda ba Yahudawa ba ko masu zunubi ba, 16 mun sani mutum
ba zai samu zaman marar laifi a gaban Allah ta wurin bin Doka
ba, sai dai idan ya ba da gaskiya ga Yesu Almasihu. Saboda haka
mu ma mun ba da kanmu ga Almasihu Yesu. Mun yi haka domin
mu samu zaman marar laifi a gaban Allah ta wurin dogara ga
Almasihu ba ta wurin bin Doka ba. Gama babu wanda yakan
samu zaman marar laifi a gaban Allah ta wurin bin Doka. 17 In
kuwa ya zama muna so mu sami zaman marasa laifi a gaban
Allah ta wurin dogara ga Almasihu, sa'an nan an same mu mu
kanmu ma masu zunubi ne, ashe, ko wannan zai nuna Almasihu
yana ƙarfafa zunubi ke nan? A'a, ko kusa!
18 "Amma idan na tashi ina sāke gina abubuwan da dā na
rushe na zama mai karyar Doka ke nan. 19 Ai, ta wurin Doka na
zama matacce ga Doka, domin in rayu ga Allah. 20 An gicciye ni
tare da Almasihu. Yanzu ina rayuwa, amma ba don kaina ba ne,
Almasihu ne yake raye a zuciyata. Wannan rayuwa ta jikin da
nake yi, rayuwa ce ta wurin dogara ga Dan Allah, wanda ya
ƙaunace ni har ya mutu domina. 21 Ba zan ƙi alherin Allah ba.
Amma idan mutum yana iya samun zaman marar laifi a gaban

2.16: Zab 143.2; Rom 3.20,22

Allah ta wurin bin Doka, wannan ya nuna cewa mutuwar Almasihu ta zama banza ke nan."

Bin Doka ko Ba da Gaskiya ga Almasihu

3 1 Ya ku Galatiyawa, kuna hauka ne? Ko wani ya yi muku magani ne? Ga shi a fili na bayyana muku Yesu Almasihu wanda ya mutu a kan gicciye. 2 Yanzu ina so in yi muku tambaya ɗaya tak. Ruhun Allah ya zo muku saboda kun bi Doka ne, ko kuwa saboda kun gaskata da maganar da kuka ji ne? 3 Yanzu wane irin rashin tunani kuke da shi haka? Ga shi kun fara da Ruhun Allah, amma yanzu kuna so ku ƙarasa da ƙoƙarin kanku na halin mutuntaka! 4 Ashe, wahaloli dabam-dabam da kuka sha sun zama banza ke nan? Haka zai yiwu kuwa? 5 Wato, Allah wanda ya ba ku Ruhunsa, yana kuma yin abubuwa masu ban mamaki a cikinku, kuna tsammani yana yin haka ne domin kuna bin Doka, ko kuwa saboda kun ji maganar Almasihu kun kuma gaskata?

6 Ku duba rayuwar Ibrahim mana. An rubuta cewa, "Ya ba da gaskiya ga Allah, saboda haka aka ce da shi mai adalci." 7 To, sai a gane cewa, masu ba da gaskiya ga Allah su ne 'ya'yan Ibrahim. 8 Rubutaccen Maganar Allah ya faɗa tun dā cewa sauran waɗanda ba Yahudawa ba za su iya samun matsayin adalci a gaban Allah ta wurin ba da gaskiya gare shi. Saboda tun dā ma an sanar wa Ibrahim Labari Mai Daɗi cewa, "Ta wurinka za a yi wa dukkan al'ummai albarka." 9 Ibrahim ya ba da gaskiya ga Allah an kuma albarkace shi, haka kuma duk wanda ya ba da gaskiya ga Allah, za a albarkace shi tare da Ibrahim.

10 Gama duk waɗanda suke tsammani Allah zai karɓe su don suna bin Dokar Musa, an la'anta su ke nan. Gama Rubutaccen Maganar Allah ya ce, "Duk wanda bai aikata dukan abin da yake a rubuce a Littafin Dokar ba, an la'anta shi ke nan." 11 To, a fili yake, babu wanda zai iya zama mai adalci a gaban Allah ta wurin bin Doka, domin an rubuta cewa, "Wanda yake da adalci ta wurin bangaskiya ga Allah zai rayu." 12 Ba abin da ya haɗa bin Doka da bangaskiya. Kamar yadda aka rubuta, "Wanda ya aikata dukan abin da aka faɗa cikin Doka, a gare ta ne zai rayu."

13 La'antawan nan ta Doka mun kuɓuce mata, saboda Almasihu ya fanshe mu daga la'antawan nan, da yake an mai da shi abin la'ana ne. Don an rubuta, "Duk wanda aka kafa shi a

---

3.6: Far 15.6; Rom 4.3 **3.7:** Rom 4.16 **3.8:** Far 12.3 **3.10:** M. Sh 27.26
3.11: Hab 2.4 **3.12:** L. Fir 18.5

kan gungumen itace, ya zama an la'anta shi ke nan." 14 Almasihu
ya yi wannan ne domin albarkan nan da aka yi wa Ibrahim, a yi
wa sauran waɗanda ba Yahudawa ba kuma ta wurin Almasihu
Yesu. Ta haka, mu ma, ta wurin bangaskiya, mun iya samun
Ruhun nan da Allah ya yi alkawari.

Bambanci tsakanin Doka da Alkawari

15 Yan'uwa, bari in ba ku misalin abin da kuka saba da shi.
Idan mutum biyu sun yi alkawari sun kuma sa hannu don tabbatar
da shi, to, ba mai soke shi, ba kuma mai ƙara wani abu a kai. 16 To,
Allah ya yi alkawari da Ibrahim da kuma zuriyarsa. Ba a rubuta
cewa "da zuriyoyi" ba, wanda zai nuna kamar da yawa. A'a, an ce
"zuriyarka," mutum ɗaya ke nan, wato Almasihu. 17 Abin da nake
nufi shi ne Allah ya yi alkawari da Ibrahim ya kuma tabbatar da
alkawarin. Dokan nan da aka kawo bayan shekara ɗari huɗu da
talatin ba za ta iya soke alkawarin nan da Allah ya yi tun dā ba.
18 Gama da cewa albarkan nan ta Allah tana samuwa ta wurin bin
Doka ne, ashe, da ba za ta samu ta wurin alkawari ba. Ibrahim
kuwa, ta wurin alkawari ne Allah ya ba shi albarkan.

19 To, in haka ne, don me aka kawo Doka? An yi ƙari da
Doka ne don a fito da abin da yake laifi a fili. An kawo ta da
nufin cewa za a yi aiki da ita har ranan nan da zuriyan nan[a] na
Ibrahim zai zo, wanda dominsa ne aka yi alkawarin. Ga shi kuwa
wannan Doka, mala'iku ne suka ba da ita, ta hannun mutum
wanda yake tsakanin Allah da mutane. 20 Kuma akan bukaci wani
a tsakani ne idan da mutum biyu ake zance, Allah kuwa ɗaya ne.

Manufar Doka

21 Ashe, wannan yana nufin Doka tana gāba da alkawarin Allah
ke nan? A'a, ko kusa! Gama da a ce an kawo wata Doka wadda
za ta sa mu rayu, wannan zai nuna za a sami adalcin Allah ta hanyar
bin Doka ke nan. 22 Maimakon haka an rubuta cikin Rubutaccen
Maganar Allah cewa, dukan duniya tana ƙarƙashin ikon zunubi.
Don me? Domin alkawarin nan da aka yi bisa ga bangaskiya ga
Yesu Almasihu, a cika ta ta wurin waɗanda suka ba da gaskiya.

23 Kafin lokacin bangaskiya yă zo, Dokan nan ta kulle mu
kamar 'yan kurkuku. Ba dama mu fita sai ta wurin bangaskiya
ga Yesu, wadda aka bayyana daga baya. 24 Wato, aka danƙa mu
a hannun Doka don ta kai mu ga Almasihu. Ta haka, ya zama ta

3.13: M. Sh 21.23 **3.16:** Far 12.7 **3.17:** Fit 12.40 **3.18:** Rom 4.14
[a] **3.19 zuriyan nan:** Wato, Yesu ke nan.

wurin bangaskiya ne muka sami zaman marasa laifi a gaban Allah. 25 Yanzu kuwa da yake lokacin bangaskiya ya zo, ba mu ƙarƙashin Doka kuma.

26 Ta wurin bangaskiya ne dukanku kuka zama 'ya'yan Allah saboda zamanku a cikin Almasihu Yesu. 27 An kuma yi muku wankan baftisma wadda ta nuna cewa ku na Almasihu ne, saboda haka kun kuma ɗauki halin Almasihu, ya zama halinku. 28 Saboda haka, ba bambanci tsakanin Yahudawa da waɗanda ba Yahudawa ba. Ba kuma bambanci tsakanin ɗa ko bawa, ko tsakanin mace da namiji. Dukanku ɗaya ne ta wurin tarayya da Almasihu Yesu. 29 In kuwa ku na Almasihu ne, kun zama zuriyar Ibrahim ke nan, kuma za ku karɓi gādon nan da Allah ya yi alkawarinsa.

4 1 Wato, yaro wanda yake magaji lokacin da yake ɗan yaro, shi da bawa duk ɗaya ne, ko da yake dukan abin da yake gidansu nasa ne. 2 Yana hannun iyayen goyonsa da wakilai har zuwa lokacin da ubansa ya sa. 3 Haka yake gare mu, sa'ad da muke yara kafin hanyar Almasihu ta bayyana. Muna kamar bayi ga ikokin da suke mulkin wannan duniya. 4 Amma sa'ad da lokacin da Allah ya shirya ya cika, sai Allah ya aiko da Ɗansa. Ya zo ta wurin haihuwar mace. An sanya shi ƙarƙashin ikon Doka tun daga haihuwa, 5 domin yă fanso waɗanda suke ƙarƙashin Doka, yă kuma mai da su a matsayin 'ya'yan Allah.

6 Domin a nuna ku 'ya'yansa ne, Allah ya aiko da Ruhun Ɗansa a cikin zuciyarku, yana kira ga Allah cewa, "Baba!" 7 Don haka kai ba bawa ba ne kuma, kai ɗa ne. Da yake kai ɗa ne, Allah zai sa ka ci albarkar gādonsa.

Bulus Ya Damu a kan Galatiyawa

8 Dā ba ku san Allah ba, kuna bauta wa waɗansu alloli waɗanda ainihi ba kome suke ba. 9 Amma yanzu kun san Allah, ko kuma a ce Allah ya san ku, yaya za ku sāke komawa ƙarƙashin mulkin ikokin duniyan nan marasa ƙarfi? Abin tausayi ne su. Me ya sa kuke so ku sāke zama bayinsu kuma? 10 Ga shi kukan ba da kanku ga kiyayen waɗansu ranaku da watanni, da lokatai, da shekaru. 11 Abin da kuke yi ya ba ni tsoro, don ya zama kamar duk wahalar da na yi a kanku banza ne!

12 Ina roƙonku 'yan'uwana, ku zama kamar yadda nake. Gama ni ma kamar ku nake. Ba ku yi mini wani laifi ba. 13 Kun san rashin lafiyar da na yi, shi ne ya yi mini hanyar da na kawo muku bishara da farko. 14 Ko da yake rashin lafiyata ta zama

3.29: Rom 4.13 **4.5-7:** Rom 8.15-17

babbar damuwa a wurinku, duk da haka ba ku yi mini reni ko ku ƙi ku kula da ni ba. Kun dai karɓe ni kamar mala'ika daga sama, ko kuwa kamar yadda kuka karɓi Almasihu Yesu da kansa. 15 Kun yi murna sosai a lokacin! To, yanzu fa, ina farin cikin da kuka ji saboda ni? Na tabbata, a lokacin, da mai yiwuwa ne da kun ciccire idanunku kun ba ni! 16 Ashe, yanzu kun mai da ni abokin gābanku ne saboda na gaya muku gaskiya?

17 Waɗannan mutane sun riƙe ku da aniya sosai, amma abin da suke nufi ba shi da kyau. Suna so su raba ku da ni, don duk niyyarku ta koma gare su. 18 Ai, yana da kyau a kasance da irin wannan niyya idan da nufi mai kyau ne. Wannan yă kuma kasance haka koyaushe, ba wai sai lokacin da nake tare da ku kawai ba. 19 Ya ku 'ya'yana, yanzu ya zama sau biyu ke nan da nake jin zafin haihuwarku. Kuma zan ci gaba da wannan wahala sai halin Almasihu ya kafu a zukatanku. 20 Ayya! Da ce ina tare da ku yanzu, da sai in canza muryata. Kai, na damu ƙwarai saboda ku!

Misali a kan Hajaratu da Saratu

21 Ku gaya mini ku da kuke so ku bi Doka, kun gane da abin da Doka take nufi ne? 22 Gama a rubuce yake cewa Ibrahim yana da 'ya'ya biyu maza, ɗaya ɗan an haife shi ne ta wurin 'yargidansa,[b] ɗayan kuma ta wurin matarsa. 23 Ɗan nan na 'yargida, Ibrahim ya samu ne ta hanyar da aka saba samun 'ya'ya. Amma ɗaya ɗan nan na matarsa an haife shi ne ta wurin alkawarin da Allah ya yi masa. 24 Wannan misali ne, matan nan biyu sun nuna alkawari biyu. Hajaratu ita ce mai haihuwar bayi, ita kwatanci ce na alkawarin da aka yi a Dutsen Sinai.[6] 25 Wato, Hajaratu ta zama misalin Dutsen Sinai wanda yake a ƙasar Larabawa. Ita ce kwatancin birnin Urushalima ta yanzu, don ita da 'ya'yanta duk bayi ne. 26 Amma Urushalima ta sama tana da 'yanci, kuma ita ce wadda ta haife mu. 27 A rubuce yake cewa,

"Ki yi farin ciki
ya ke mace wadda ba kya haihuwa,
Ki yi ihu na murna
ke da ba ki taɓa jin zafin haihuwa ba,
Don yaran mace wadda mijinta ya bar ta sun yi yawa.
Sun fi yaran mace mai miji."

4.22: Far 16.15; 21.2 **4.27**: Ish 54.1

[b] **4.22 'yargidansa**: Da Helenanci an rubuta "baiwa" ne a nan.

[6] **4.24 Dutsen Sinai**: Shi ne inda Allah ya ba da dokokinsa ga Musa.

28 To, 'yan'uwa, mu ma mun zama 'ya'yan Allah ta wurin
alkawari kamar Ishaku. 29 A wancan lokaci kuwa ɗan nan da aka
haifa ta hanyar da aka saba ya tsananta wa ɗan nan da aka haifa ta
wurin ikon Ruhun Allah. Haka kuma yake har yanzu. 30 Amma a
rubuce yake cikin Rubutaccen Maganar Allah cewa, "Ka kori
'yargidan nan da ɗanta, domin yaron 'yargidanka ba zai raba gādo
tare da ɗan nan da matarka ta haifa ba." 31 Saboda haka 'yan'uwa,
mu ba 'ya'yan 'yargida ba ne, mu dai 'ya'yan mace ne wadda take
da 'yanci.

'Yanci cikin Almasihu

5 1 Don zaman 'yanci shi ne dalilin da Almasihu ya 'yantar da
mu. Saboda haka sai ku tsaya da ƙarfi, kada ku yarda ku
zama bayi kuma.

2 To, ku ji ni. Ni Bulus ina gaya muku, in kun yarda a yi muku
kaciya, wannan ya nuna Almasihu ba shi da amfani gare ku ke nan.
3 Ina sāke tuna muku cewa duk wanda ya yarda ya bi dokar yin
kaciya, to, ya zama dole yă bi dukan Doka ke nan. 4 Ku da kuke
ƙoƙarin samun zaman marasa laifi a gaban Allah ta wurin bin Doka,
kun riga kun fid da kanku daga bin Almasihu ke nan. Kun kauce
wa alherin Allah. 5 Mu dai mun sa zuciya Allah zai sa mu sami
zaman marasa laifi a gabansa, wannan shi ne abin da muke jira
kuma daga wurin Ruhun Allah wanda yake aiki ta wurin
bangaskiyarmu ga Almasihu. 6 Gama in muna cikin Almasihu Yesu,
ko da kaciya, ko da rashin kaciya ba wani abu ba ne a gare mu.
Amma abin da muka fi kula da shi shi ne mutum yă ba da gaskiya
ga Almasihu, yă kuma yi wannan ta hanyar ƙauna.

7 Da farko kuna ci gaba sosai. Wane ne ya hana ku bin
gaskiya? 8 Lallai rudin da aka yi muku bai zo daga wurin Allah,
wanda ya kira ku ba. 9 Kamar yadda akan faɗa, "Dan ƙanƙanin
yisti ne yakan sa babban burodi yă kumbura." 10 Saboda
zumuncinmu cikin aikin Ubangiji, na tabbata ba za ku bi wani
ra'ayi dabam da nawa ba. Kuma shi wanda yake ta da hankalinku
zai sha hukunci, ko shi wane ne.

11 'Yan'uwana, idan har yanzu ina wa'azi a yi kaciya ne,
to, don me har yanzu mutane suke ba ni wuya? Idan ina goyon
bayan cewa dole ne a yi kaciya, ai, da maganata game da
mutuwar Almasihu a kan gicciye ba za ta zama abin tuntuɓe
ga kowa ba ke nan! 12 Ai, masu ta da hankalinku ɗin nan,
gwamma su ci gaba su yanke gabansu gaba ɗaya!

4.29: Far 21.9 **4.30**: Far 21.10 **5.9**: 1 Kor 5.6

13 'Yan'uwana, ku dai an kira ku zuwa 'yanci musamman.
Amma ku lura kada 'yancin nan naku yă zama dalilin bin sha'awar
jiki. Maimakon haka bari 'yancin nan yă kai ku ga yi wa juna bauta
cikin ƙauna. 14 Gama dukkan Doka an haɗa ta a kalma guda, wato,
"Ka ƙaunaci abokin zamanka kamar kanka." 15 Amma in kuna faɗa
da juna, kuna cizo, kuna cinye juna kamar namomin daji, ku mai
da hankali fa, ko kuma dukanku gaba ɗaya ku halaka!

Bambanci tsakanin Ruhun Allah da Mutuntaka

16 Nufina shi ne, ku bar Ruhun Allah yă bi da ku. Idan kun
yi haka ba za ku bi halin mutuntaka ba. 17 Don halin mutuntaka
ba ya yarda da Ruhu, Ruhu kuma ba ya yarda da halin mutuntaka.
Waɗannan halayen biyu suna gāba da juna. Shi ne ya sa ba ku
iya yin abin da kuke so ku yi. 18 In Ruhun Allah ne yake bi da
ku, to, ba kwa ƙarƙashin Dokan nan ke nan.

19 Ayyukan da halin mutuntaka yake yi, suna nan a fili. Ga
iskanci, da aikin lalata da yin abubuwa masu ban ƙyama, 20 da bautar
gumaka, da maita. Mutane sukan ƙi juna suna faɗa, suna kishin
juna. Ga kuma fushi, da sonkai, da rabuwa, da yin tawaye, 21 da
kishi, da buguwa, da haɗa kai don yin lalata ta wurin shaye-shaye,
da kuma sauran irin abubuwa kamar haka. Ina yi muku gargaɗi,
kamar yadda na riga na yi a dā, cewa masu yin irin waɗannan
abubuwa ba za su sami mulkin Allah ba.

22 Amma halayen da Ruhun Allah yake haihuwa, su ne ƙauna,
da farin ciki, da salama, da haƙuri, da kirki, da nagarta da yin
aminci, 23 da ladabi da kuma shan ƙarfin sha'awar jiki. Ai, ba ruwan
Doka da waɗannan abubuwa. 24 Kuma dukan waɗanda suke na
Almasihu Yesu sun kashe halin mutuntaka da mugayen abubuwa
iri-iri da jiki yake marmarinsu. 25 Tun da yake Ruhu ne ya ba mu
rai, bari Ruhu yă bi da mu kuma cikin dukkan zamanmu. 26 Kada
mu zama masu girmankai ko masu ta da hankalin juna, ko masu
jin kishin juna.

Ku Taimaki Juna

6 1 'Yan'uwa, in an ga wani yana cikin yin laifi, ku da Ruhu
Mai Tsarki yake tare da ku, sai ku komo da shi kan hanya.
Amma ku yi haka da halin ladabi, a hankali kuma, domin kada
maimakon dawowa da ɗan'uwanku, ku ma ku fāɗi cikin jaraba.
2 Ku taimaki juna ta wajen ɗaukan wahalar juna. Ta haka ne za ku
cika dokar Almasihu. 3 In wani yana tsammani shi wani abu ne

5.14: L. Fir 19.18 5.17: Rom 7.15-23

alhali kuwa shi ba kome ba ne, rudîn kansa yake yi. 4 Bari kowa yă gwada aikinsa yă gani. Idan ya yi kyau, sa'an nan zai iya ƙama da abin da ya yi da kansa, ba sai ya gwada kansa da wani ba. 5 Gama ya kamata kowa yă ɗauki kayan kansa.

6 Duk wanda aka koya masa maganar Almasihu sai yă ba da nasa rabo na abubuwan alheri zuwa ga wanda ya koya masa.

7 Kada ku rudî kanku, ai, ba ya yiwuwa a yi wa Allah wayo. Duk abin da mutum ya shuka, shi zai girba. 8 Idan mutum ya yi shuka ta biyan sha'awar jiki, wannan zai kai shi ga mutuwa. Idan kuwa ya yi shuka ta biyan bukatar Ruhu, zai sami rai na har abada. 9 Saboda haka kada mu gaji da yin abin da yake da kyau. Gama idan ba mu gaji muka bar ƙokari ba, lokaci zai zo da za mu yi girbi mai albarka. 10 To, saboda haka, duk sa'ad da muna da zarafi, sai mu kyautata wa dukkan mutane, tun ba waɗanda suke 'yan'uwanmu cikin Almasihu ba.

Maganar Karshe

11 Ku dubi irin manya-manyan rubutun da nake yi muku da hannuna. 12 To, mutanen nan da suke so ku yi kaciya su masu girmankai ne, suna so a ga su wani abu ne. Suna yi muku haka ne don suna tsoron shan wuyar da za su yi saboda gicciyen Almasihu. 13 Ai, ko waɗanda aka yi musu kaciya ma ba sa kiyaye Doka. Su dai suna so a yi muku kaciya don su yi ta ɗaga kai cewa su ne suka sa a yi muku kaciya. 14 Amma ni ko kusa ba zan ɗaga kai ba. Ko zan ɗaga kai ma, sai dai a kan gicciyen Ubangijinmu Yesu Almasihu. Gama ta wurin mutuwarsa a kan gicciye ne sha'anin duniya ya mutu a gare ni, ni kuma na mutu ga sha'anin duniya. 15 Kaciya da rashin kaciya ba kome suke ba, babban abu shi ne mutum yă zama sabuwar halitta. 16 Salama da jinƙai su kasance tare da dukan waɗanda suke bin wannan sabuwar doka, wato, dukan mutanen Allah na gaske.

17 A ƙarshe 'yan'uwa, kada kowa yă ƙara damuna da wani abu, domin alamun raunukan da nake da su a jikina[c] sun nuna cewa ni bawan Yesu ne.

18 Bari alherin Ubangijinmu Yesu Almasihu yă kasance tare da ku, 'yan'uwa. Amin.

[c] **6.17 alamun raunukan da nake da su a jikina:** Wato, raunuka daga bulalar da aka yi masa saboda yana wa'azin Almasihu.

WASIKAR BULUS ZUWA GA
AFISAWA

Gabatarwa

Manzo Bulus ne ya rubuta wannan wasika mai yiwuwa a shekara ta A.D. 60 a lokacin da yake a kurkuku a Roma. An aika da *Wasikar Bulus zuwa ga Afisawa* da nufin idan sun gama karantawa, su aikar da ita zuwa ga wadansu jama'ar masu bi.

Muhimmin abu cikin wannan wasika shi ne yadda Allah ya shirya zai tara mutanen duniya duka a karkashin ikon Yesu Almasihu, ba mutane kawai ba, amma har ma da dukkan halitta a sama da kasa. Wasikar kuwa ta karfafa masu bi su yi zamansu ta hanyar da za ta nuna cewa sun zama daya da gaske, ba ta baki kawai ba.

Da farko wasikar ta fara maganar hada kai, tana nuna yadda Allah Uba ya zaɓi mutanensa, ya bayyana alherinsa ta hanyar gafarta musu laifofinsu, ya 'yantar da su daga ikon zunubi ta wurin mutuwar Yesu Almasihu, har ya tabbatar da alkawarinsa ta wurin aikin Ruhu Mai Tsarki. A cikin wannan wasika za a sami misalai wadanda suka nuna zumuncin mutanen Allah da Almasihu: An kwatanta jama'ar Almasihu da jikin mutum, Almasihu kuma shi ne kai; an kwatanta su da amarya, Almasihu kuma shi ne ango. An kwatanta su da tushen gini, Almasihu kuma shi ne dutsen da ya sa ginin gaba daya ya zama da karfi. Ya yi dukan wannan saboda daukakar sunansa.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-2
Zama daya na 'yan Adam cikin Almasihu 1.3—3.21
Yadda za a nuna an zama daya 4.1—6.20
Maganar karshe 6.21-24

Gaisuwa

1 [1] Daga Bulus, manzon Almasihu Yesu ta wurin nufin Allah,
zuwa ga mutanen Allah wadanda suke Afisa,[a] wadanda suke
da aminci cikin bin Almasihu Yesu.

2 Alheri da salama daga Allah Ubanmu da Ubangiji Yesu
Almasihu su kasance tare da ku.

1.1: A.M. 18.19-21; 19.1

[a] **1.1 wadanda suke Afisa**: Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da wadannan kalmomi.

Albarkun Ruhaniya cikin Almasihu

3 Mun gode wa wanda yake Allah na Ubangijinmu Yesu
Almasihu da Ubansa kuma, da yake ta wurin Almasihu ne Allah
ya yi mana albarka cikin mulkinsa a samaniya, ya kuma ba mu
kowace albarka ta ruhaniya. 4 Ya zaɓe mu ta wurin zamanmu
ɗaya da Almasihu tun ba a halicci duniya ba, mu zama masu
tsarki, marasa laifi a gabansa.

Saboda ƙaunarsa, 5 Allah ya riga ya shirya mu mu zama
'ya'yansa ta wurin Yesu Almasihu, bisa ga nufinsa na alheri. 6 Ya
yi haka domin mu yabi darajar alherinsa da ya ba mu kyauta a
yalwace ta wurin Ɗansa da yake ƙauna. 7 Ta wurin mutuwar
Almasihu ne muka sami 'yanci, wato, yafewar zunubanmu. Ya
yi wannan kuma bisa ga yawan alherinsa 8 da ya ba mu ba iyaka.

Da hikima marar iyaka, da ganewa kuma, 9 Allah ya sa muka
san asirin nufinsa na abin da ya nufa, wanda ya kuma cika ta
wurin Almasihu. 10 Nufinsa ke nan, idan lokaci ya cika, yă
harhaɗa dukan abubuwa a ƙarƙashin ikon Almasihu, wato, dukan
abubuwan da suke sama da abubuwan da suke ƙasa gaba ɗaya.

11 Ta wurin Almasihu kuma, Allah ya zaɓe mu mu zama
mutanensa. Tun da farko ma, ya riga ya shirya wannan. Ai, shi
ne wanda yake aikata dukan abubuwa bisa ga nufinsa. 12 Nufinsa
da ya zaɓe mu shi ne domin mu da muka fara sa zuciya ga
Almasihu mu yi zaman yabon ɗaukakar Allah.

13 Ta wurin Almasihu, ku ma kun zama mutanen Allah
lokacin da kuka ji maganar gaskiya, wato, Labari Mai Daɗin da
ya kawo muku ceto. A lokacin da kun ba da gaskiya ga Almasihu,
Allah ya ba ku Ruhu Mai Tsarki kamar yadda aka yi muku
alkawari zai yi, yă zama kamar alama wanda yake nuna ku nasa
ne. 14 Ruhu Mai Tsarki shi ne ya tabbatar mana cewa Allah zai
ba mu abin da ya yi alkawari, har ya sa muka sani nan gaba Allah
zai ceci waɗanda suke nasa. Wannan kuma domin yabon
ɗaukakarsa ne.

Addu'ar Bulus don Mutanen Afisa

15 Saboda haka da yake na ji labarin yadda kuka ba da gaskiya
ga Ubangiji Yesu, da kuma yadda kuke ƙaunar dukan mutanen
Allah, 16 ban fasa gode wa Allah saboda ku ba. Duk sa'ad da nake
addu'a dominku, nakan yi haka 17 da nufin cewa Allah na
Ubangijinmu Yesu Almasihu, Uba Maɗaukaki, yă riƙa ba ku

1.7: Kol 1.14

Ruhunsa mai ba da hikima da bayani don ku ƙaru cikin sanin
Allah. 18 Ina addu'a kuma Allah yă ba ku ganewa domin ku san
komene ne sa zuciyan nan da ya kira mu a kansa, ku kuma san
darajar dukiyan nan wadda take ta mutanen Allah, wato,
albarkunsa. 19 Ina addu'a har yanzu ku san ƙarfin ikonsa wanda
ya wuce gaban misali, wanda yake aiki a cikinmu, mu da muka
ba da gaskiya. Ikon nan da yake aiki a cikinmu, ɗaya ne da ikon
nan 20 wanda ya yi aiki cikin Almasihu sa'ad da Allah ya tashe
shi daga matattu, ya kuma ba shi wurin zama mai daraja tare da
shi a sama. 21 A can Almasihu yake mulki a kan dukan masu
sarauta da iko da ƙarfi da mulki. Yana da suna wanda ya fi
kowane suna da za a bayar, ba a duniya kaɗai ba, har a wurin
zaman matattu ma. 22 Allah kuma ya sa kome a ƙarƙashin ikon
Almasihu, ya kuma sa shi, shi mai mulkin abu duka, yă zama
shugaban jama'ar masu bi. 23 Jama'ar masu bi ita ce jikin
Almasihu. A cikin jama'ar masu binsa kuma Almasihu ya zama
cikakke, kamar yadda shi kansa shi ne cikawar dukan abubuwa
ko'ina.

Daga Mutuwa zuwa Rai

2 1 A dā kuna kamar mutanen da suka mutu ne, saboda
laifofinku da zama cikin zunubin 2 da kuke lokacin da kuke
bin hanyoyin duniyan nan, kuna bin sarkin masu iko a sararin
sama,[b] wato, ruhun nan da yake zuga zuciyar mutanen da suka
ƙi biyayya ga Allah. 3 Dukanmu dai haka muke a dā, muna bin
sha'awace-sha'awacen jikinmu, muna yin abin da jiki da zuciya
suke zuga mu mu yi kawai. Ta haka, bisa ga halinmu na 'yan
Adam, mu ma dā fushin Allah ya zo kanmu kamar yadda yake
a kansu su ma.

4 Amma Allah mai yawan tausayi ne, ƙaunarsa kuma zuwa
gare mu ta yi yawa ƙwarai, 5 har tun sa'ad da muke matattu ta
wurin zunubanmu, sai ya rayar da mu tare da Almasihu. Ta
wurin alheri ne aka cece ku. 6 Ya tashe mu tare da Almasihu,
har ta wurin Almasihu Yesu, muka sami wurin zama a
samaniya. 7 Allah ya yi wannan kuwa domin a zamani mai zuwa
yă nuna yawan alherinsa wanda ba iyaka. Alherin nan nasa, ya
nuna mana shi a cikin Almasihu Yesu. 8 Ai, ta alherin Allah ne
kuka sami ceto ta wurin bangaskiya. Wannan kuwa ba ƙoƙarin
kanku ba ne, kyauta ce ta Allah. 9 Ba kuwa saboda aikin lada

1.20: Zab 110.1 **1.22**: Zab 8.7 **1.22-23**: Kol 1.18 **2.1-5**: Kol 2.13

[b] **2.2 sarkin masu iko a sararin sama**: Wato, Shaiɗan ke nan.

ba, don kada wani yă ɗaga kai. 10 Ai, mu da kanmu aikinsa ne,
an canza halittarmu albarkacin Almasihu Yesu, musamman
domin mu yi ayyuka masu kyau waɗanda Allah ya riga ya
shirya mana tun da fari mu yi.

Almasihu Ya Haɗa Dukan Mutane

11 Saboda haka, ku tuna yadda kuke a dā. Ku ba Yahudawa
ba ne bisa ga haihuwa. Su waɗanda suke kiran kansu "masu
kaciyan" nan, sukan kira ku "marasa kaciya". Ga shi kuwa,
kaciyan nan ta jiki ce, wadda ake yi da hannu. 12 Ku tuna a
lokacin ba ruwanku da Almasihu, ba ku da matsayi cikin
jama'ar Allah, ba ku cikin alkawaran nan da Allah ya yi wa
iyayenmu. Ku dai a duniyan nan ba ku da bege, ba ku da Allah.
13 Amma yanzu kuna cikin Almasihu Yesu, ku da dā kuke can
da nesa, an kawo ku kusa ta wurin jinin Almasihu. 14 Gama
Almasihu shi ne salamarmu, shi wanda ya ɗauki Yahudawa da
waɗanda ba Yahudawa ba, ya sa su su zama ɗaya. Ya rushe
katangan nan da ta raba su, wato, ƙin juna da yake tsakaninsu.
15 Ya soke Dokan nan mai umarnai da dokoki ta wurin ba da
jikinsa. Ya yi haka domin yă halicci sabuwar zuriya daga
zuriyan nan biyu. Ta haka kuma ya kawo salama tsakaninsu.
16 Ya mai da su duka biyu ga Allah, su zama jiki ɗaya. Ya yi
haka ta wurin mutuwarsa a kan gicciye, da yake ya ƙid da
ƙiyayyar da ta raba su a dā. 17 Ya kuwa zo ya yi muku wa'azin
Labari Mai Daɗi na salama, ku waɗanda ba Yahudawa ba, ku
da kuke nesa da Allah; ya yi wa Yahudawa kuma haka, su da
suke kusa. 18 Ai, ta wurinsa ne dukanmu biyu za mu sami damar
zuwa wurin Uba ta hanya ɗaya, wato, Ruhun Allah.

19 Saboda haka, yanzu ku waɗanda ba Yahudawa ba ba baƙi
ba ne kuma, ba ku rasa wurin zama ba. Ai, ku masu 'yanci ne
tare da sauran tsarkaka, 'yan gida ne kuma kamar sauran iyalin
Allah. 20 An kafa ku duka a bisa tushen da manzanni da
annabawa suka gina, Almasihu Yesu kansa kuwa shi ne
muhimmin dutsen ginin. 21 Shi ne wanda ta wurinsa dukan ginin
yake haɗe, shi ne kuma yake sa ginin yă yi ta ƙara girma har
yă żama wurin sujada mai tsarkin da aka keɓe wa Ubangiji.
22 A cikinsa ne ku kuma aka gina ku, tare da sauran domin ku
zama gida inda Allah yake zama ta wurin Ruhunsa.

2.15: Kol 2.14 **2.16:** Kol 1.20 **2.17:** Ish 57.19

Hidimar da Bulus Ya Yi wa Waɗanda ba Yahudawa ba

3 [1] Domin haka, ni Bulus, na zama ɗan kurkuku saboda
Almasihu Yesu domin amfanin ku waɗanda ba Yahudawa
ba. [2] Na tabbata kun ji labari yadda Allah, a cikin alherinsa, ya
ba ni baiwa ta yin hidiman nan don taimakonku, [3] wato, yadda ta
wurin ru'uya Allah ya sanar da ni asirin nufinsa kamar yadda na
riga na rubuta labarinsa a taƙaice. [4] Idan kuwa kun karanta, za ku
iya gane da abin da na sani a kan asirin Almasihu. [5] A zamanin
dā ba a gaya wa 'yan Adam wannan ba, kamar yadda yanzu Allah
ya bayyana wa manzanninsa masu tsarki da annabawa masu tsarki
ta wurin Ruhu. [6] Asirin shi ne, ta wurin bisharar Almasihu Yesu,
su waɗanda ba Yahudawa ba sun zama abokan gādo tare da mu
Yahudawa. Su, da mu, mun zama kamar gaɓoɓin jiki ɗaya ne.
Su ma suna da rabonsu cikin alkawarin da Allah ya yi mana ta
wurin Almasihu Yesu.

7 An kuwa mai da ni mai hidimar wannan bishara. Aikin nan
kuwa, baiwa ce aka yi mini, wato, alherin da Allah ya ba ni ta
wurin ikonsa, ikon da yake aiki a cikina. [8] Ko da yake ni ba kome
ba ne cikin mutanen Allah, ni aka ba wannan baiwa mai daraja,
in kai wa waɗanda ba Yahudawa ba arzikin Labari Mai Daɗin
nan a kan Almasihu, wanda ba a iya lissafi. [9] Domin kuma in
bayyana wa dukan mutane yadda Allah yake aikata shirin nan na
asiri wanda shekara da shekaru yake a ɓoye a gunsa, shi wanda
ya halicci dukan abubuwa. [10] Nufinsa shi ne, yanzu, ta wurin
jama'ar masu bi, a sanar da hikimar Allah iri-iri ga masu sarauta
da masu iko a samaniya. [11] Wannan kuwa an yi shi ne bisa ga
nufin nan da Allah ya nufa tun daga farko, ya kuma aikata cikin
Almasihu Yesu Ubangijinmu. [12] Cikinsa ne muke da ƙarfin hali
zuwa wurin Allah babu tsoro, da amincewa, ta wurin
bangaskiyarmu gare shi. [13] Saboda haka ina roƙonku, kada ku
koma baya da ganin dukan wahalar da nake sha dominku. Ai,
wahalar za ta zama muku da amfani.

Addu'ar Bulus don Mutanen Afisa

14 Saboda haka ina durƙusawa a gaban Ubanmu na sama,
[15] shi wanda ya sa kowace kabila ta sama da ta ƙasa su kasance.
[16] Ina roƙonsa yă ba ku baiwa daga cikin arzikin darajarsa, yă
ƙarfafa ku da ikonsa, don ku zama da ƙarfi a zuciyarku ta wurin
Ruhunsa, [17] har ma Almasihu yă zauna a zuciyarku ta wurin

3.4-6: Kol 1.26-27

bangaskiya. Ina addu'a cewa ku kafu sosai cikin ƙauna. Bari ƙauna ta zama tushenku, 18 domin ku sami damar ganewa ta wurin kafuwarku cikin ƙauna ku da dukan sauran mutanen Allah kuma, ku san girmar ƙaunar Almasihu, wato, faɗinta, da tsawonta, da girmanta, da zurfinta. 19 Ku kuma san ƙaunar Almasihu wadda ta fi gaban sani domin ku cika da dukan cikar Allah.

20 Daukaka ta tabbata ga Allahnmu wanda ta wurin ikonsa a cikinmu yana aiki har yana aikata abubuwa fiye da dukan abin da za mu roƙa, ko abin da za mu yi tunaninsa. 21 Daukaka ta tabbata a gare shi cikin jama'ar masu bi da kuma cikin Almasihu Yesu, har zuwa dukan zamanai, har abada abadin. Amin!

Zaman Dayantaka

4 1 Saboda haka, ni da nake cikin kurkuku saboda bin Ubangiji, ina roƙonku ku yi zaman da ya dace da darajar kiran da aka yi muku. 2 Kullum ku kasance da tawali'u da saukinkai da haƙuri, ku kuma yarda da juna cikin ƙauna. 3 Ku yi ƙoƙari sosai ku kiyaye zama ɗayan nan da Ruhu ya ba ku, ta wurin salaman nan da ta ɗaure ku tare. 4 Mu jiki guda ne, Ruhu Mai Tsarki kuma ɗaya ne. Haka kuma akwai sa zuciyan nan ɗaya wanda aka kira ku dominsa. 5 Akwai Ubangiji ɗaya, bangaskiya ɗaya, kuma baftisma ɗaya tak. 6 Allah ɗaya ne, shi ne Uban dukan mutane. Shi ne yana bisa dukkan mutane, yana aikinsa ta wurin dukkan mutane, yana kuma cikin dukkan mutane.

7 Amma an ba kowannenmu baiwarsa bisa ga yawan alherin Almasihu. 8 Kamar yadda Maganar Allah ta ce,

"Sa'ad da ya hau sama
ya ɗauki waɗanda ya kama[6] tare da shi,
ya kuma yi wa 'yan Adam baiwa iri-iri."

9 Me ake nufi da "ya hau"? Ana nuna cewa, da farko ya sauka har zuwa can ƙarƙashin ƙasa! 10 Shi wanda ya sauka ɗin, shi ne kuma ya hau can sama, domin yă cika sama da ƙasa duka. 11 Shi ne kuma ya yi wa 'yan Adam baiwa. Ga waɗansu ya sa su zama manzanni, waɗansu su zama annabawa, waɗansu su zama masu shelar bishara, waɗansu su zama masu lura da mutane da masu koyarwa. 12 Ya yi wannan domin yă shirya mutanen Allah su yi masa aikin hidima don gina jikin Almasihu. 13 Ta haka dukanmu za mu kai ga zaman ɗayan nan cikin bin Ubangiji, mu zama ɗaya

---

4.2: Kol 3.12-13 4.8: Zab 68.18

[6] **4.8 waɗanda ya kama:** Mai yiwuwa ba mutane kawai ne ya kama ba amma har da ruhohi.

kuma cikin sanin Ɗan Allah. Za mu zama cikakkun mutane, mu kuma kai matsayi na dukan cikar Almasihu.

14 An yi wannan kuwa don kada mu koma halin yara, ko mu zama kamar waɗanda ake yawo da hankalinsu, iskar kowace koyarwa tana tura su tana ɗauke hankalinsu, mutane masu wayo kuma suna rudĩnsu suna cutarsu. 15 Maimakon haka sai mu faɗi gaskiya cikin ƙauna, mu yi girma cikin al'amuranmu duka har mu kai ga halin Almasihu wanda shi ne kamar kan jikin mutum. 16 Domin shi ne yake mulkin dukan gaɓoɓin jiki. Sun haɗu suna riƙe da juna ta wurin aikin kowace jijiya, har ta wurin aikin kowace gaɓa daidai jikin yake ƙara girma, yana ginuwa da halin ƙauna.

Sabon Rai cikin Almasihu

17 To, ina dai faɗa muku, ai, gargaɗi ne nake yi muku cikin sunan Ubangiji cewa, kada ku zama kamar waɗanda ba Yahudawa ba, masu tunanin banza. 18 Zuciyarsu cike da duhu take. An raba su kuma da rai wanda Allah yake bayarwa, saboda rashin saninsu da taurin kansu. 19 Ga kuwa rashin kunya gare su. Sun ba da kansu ga yin lalata, suna sha'awar yin kowace irin ƙazanta.

20 Wannan ba shi ne abin da kuka koya game da Almasihu ba! 21 Na tabbata an ba ku labarinsa. Da yake ku mutanensa ne, an koya muku gaskiyar da take cikin Yesu. 22 Ai, abin da aka koya muku, shi ne ku yar da halin da ba shi da kyau wanda kuke ciki a dā, halin da yake lalacewa saboda son abubuwa masu ruɗu. 23 Ya kamata a sabunta tunaninku da hankalinku. 24 Ku ɗauki sabon halin nan da Allah ya halitta bisa ga kamannin kansa. Halin nan kuwa, ya bayyana cikin adalci, da zaman tsarki.

25 Saboda haka sai ku rabu da ƙarya! Kowa yă riƙa faɗa wa abokin zamansa gaskiya, don dukanmu gaɓoɓin juna ne. 26 In kun yi fushi, kada yă kai ku ga zunubi. Kada ma fushinku yă daɗe yă kai har rana ta fāɗi. 27 Kada kuma ku ba wa Shaiɗan wata dama. 28 Kada mai sata yă ƙara yin sata. A maimakon haka sai yă yi aikin gaskiya da hannunsa, har da zai sami wani abin da zai iya taimakon waɗanda ba su da shi. 29 Kada wani ƙazamin zance yă fita daga bakinku, sai dai irin maganar da take da amfani domin ƙarfafawar juna bisa ga bukatarku. Ta haka maganarku za ta zama da amfani ga masu jinta. 30 Ku kuma kula fa, kada ku ɓata wa Ruhu Mai Tsarki na Allah rai, domin shi alama ne na

4.16: Kol 2.19 **4.22:** Kol 3.9 **4.24:** Far 1.26; Kol 3.10 **4.26:** Zab 4.4

Allah a kanku da zai nuna a Ranar ƙarshe cewa ku nasa ne. 31 Ku
rabu da kowane irin zafin rai, da haushi, da fushi, da faɗa, da
zage-zage, da kowace irin mugunta. 32 Ku yi wa juna kirki, ku ji
tausayin juna, ku yafe wa juna kamar yadda Allah ya yafe muku
ta wurin Almasihu.

5 1 Tun da yake kun zama 'ya'ya waɗanda Allah yake ƙauna,
sai ku ɗauki misali daga wurin Allah a cikin zamanku. 2 Ku
yi zaman ƙauna kamar yadda Almasihu ya ƙaunace mu, ya
kuma ba da kansa dominmu, sadaka mai ƙamshi, hadaya kuma
ga Allah.

3 Kada ma a ko ambaci iskanci da kowane irin aikin lalata ko
kwaɗayi a tsakaninku, domin kuwa bai dace da tsarkaka ba.
4 Haka ma da ƙazamar magana da zancen banza da wauta, don
bai kamata ba. A maimakon haka ku riƙa gode wa Allah. 5 Ku
dai san cewa, mai yin iskanci, ko mai aikin lalata, ko mai kwaɗayi
(wanda shi da mai bautar gumaka ɗaya ne), ba su da rabo a mulkin
Almasihu da na Allah, ko kaɗan. 6 Kada wani kuwa yă rude ku
da maganar wofi; ai, saboda waɗannan zunubai ne fushin Allah
yake zuwa a kan waɗanda suka ƙi jinsa. 7 Saboda haka kada ku
haɗa kai da su.

8 Domin dā kuna a duhu, amma a yanzu, kun sami haske ta
wurin Ubangiji. Ku yi zaman mutanen haske, 9 domin haske shi
ne yake ba da babban amfani wajen ayyuka masu kyau, da
zaman adalci, da maganar gaskiya. 10 Ku tabbata cewa kun koyi
abin da zai gamshi Ubangiji. 11 Ku rabu da ayyukan banza na
duhu da mutane suke yi, amma ku tona su. 12 Gama abin kunya
ne a ma faɗa abubuwan da suke yi a ɓoye. 13 Sa'ad da aka kawo
dukan abu a gaban haske, za a san ainihin yadda suke. 14 Shi
ya sa aka ce,

"Tashi, kai da kake barci!
Ka tashi daga matattu!
Almasihu kuwa zai haskaka ka."

15 Saboda haka sai ku mai da hankali ƙwarai ga zamanku.
Kada ku zama kamar wawaye, sai dai kamar masu hikima. 16 Ku
yi amfani da kowane zarafi na yin kirki, don kwanakin da muke
ciki yanzu mugaye ne. 17 Saboda haka kada ku zama wawaye, sai
dai ku gane abin da yake nufin Ubangiji. 18 Kada kuma ku bugu
da ruwan inabi, wannan hanyar lalaci ne. A maimakon haka ku
cika da Ruhu, 19 ku yi magana da juna da kalmomin zabura, da

4.32: Kol 3.13 5.2: Fit 29.18; Zab 40.6 5.16: Kol 4.5

wakɔkin yabo, da wakɔki na ruhaniya. Ku yi ta rera wakɔki da
zabura ga Ubangiji da dukan zukatanku. 20 Kullum ku rika gode
wa Allah Uba da sunan Ubangijinmu Yesu Almasihu a kan kome.

Zaman Mata da Maza cikin Aure

21 Ku yi biyayya da juna cikin tsoron Almasihu.

22 Ku matan aure, ku yi biyayya ga mazanku, kamar yadda
kuke yi wa Ubangiji. 23 Don miji shi ne shugaban matarsa, kamar
yadda Almasihu yake shugaban jama'ar masu bi wato, jikinsa.
Shi kansa kuma shi ne Mai Ceton jikin. 24 Kamar yadda jama'ar
masu bi take yin biyayya ga Almasihu, haka kuma mata su yi
biyayya ga mazansu ta kowane hali.

25 Ku maza ku ƙaunaci matanku kamar yadda Almasihu ya
ƙaunaci jama'ar masu bi har ya ba da kansa dominta, 26 don yă
mika ta da tsarki ga Allah ta wurin maganarsa bayan ya wanke
ta da ruwa. 27 Ya yi wannan domin a sa'ad da zai ɗauko wa kansa
jama'ar masu bi, ta zama da daraja sosai ba tare da datti ko wata
alamar rashin kyan gani ba, ta kuma zama da tsarki, babu wani
abu marar kyau. 28 Ta haka ya kamata maza su ƙaunaci matansu
kamar yadda suke ƙaunar jikinsu. Ai, wanda ya ƙaunaci matarsa,
ya ƙaunaci kansa ke nan. 29 Domin ba wanda ya taɓa ƙin jikinsa,
sai dai yakan lura da shi yă kula da shi sosai kamar yadda
Almasihu yake kula da jama'ar masu bi. 30 Gama mu gaɓoɓin
jikinsa ne. 31 Kamar yadda yake a rubuce,

"Mutum zai bar mamarsa da babansa, yă manne wa
matarsa,
su biyu su zama jiki guda."

32 A cikin wannan ayar akwai babbar magana a ɓoye. Ni kaina
na ɗauke ta tana nufin Almasihu da jama'ar masu bi ne. 33 Duk
da haka dai, maganar ta shafe ku ku ma. Bari kowane ɗayanku
yă ƙaunaci matarsa kamar kansa, ita matar kuwa ta yi wa mijinta
biyayya.

Zaman 'Ya'ya da Iyayensu

6 1 Ku 'ya'ya, saboda Ubangiji ku yi wa iyayenku biyayya,
domin wannan shi ne daidai. 2 Doka ta fari wadda aka haɗa
da alkawari ta ce,

"Ka girmama babanka da mamarka,
3 don ka zauna lafiya,

5.19-20: Kol 3.16-17 **5.22:** Kol 3.18; 1 Bit 3.1 **5.25:** Kol 3.19; 1 Bit 3.7
5.31: Far 2.24 **6.1:** Kol 3.20

ka kuma daɗe a duniya."

4 Ku ubanni, kada ku sa 'ya'yanku su yi fushi, sai dai ku goye su da horo da gargaɗi ta hanyar Ubangiji.

Bayi da Iyayengijinsu

5 Ku bayi, ku yi biyayya ga waɗanda suke iyayengijinku na duniyan nan. Ku nuna musu halin bangirma, kuna kuma musu biyayya cikin dukan kome, da zuciya ɗaya kuma, kamar hidimar Almasihu ce kuke yi. 6 Kada ku yi aikin ganin ido, kamar waɗanda suke neman yabo wurin mutane, amma da yake ku bayin Almasihu ne, ku aikata abin da Allah yake so, da zuciya ɗaya. 7 Ku yi aikinku na hidima da kyakkyawar nufi, kamar ga Ubangiji kuke yi, ba mutane ba. 8 Kun sani, kowane alherin da mutum ya yi, ko shi bawa ne ko ɗan gida ne, Ubangiji zai ba shi ladansa.

9 Ku iyayengiji, ku ma ku yi wa bayinku haka. Ku daina ba su tsoro. Ku sani ku da su duk kuna da Ubangiji a sama, shi kuwa ba ya nuna bambanci.

Dukan Kayan Yaƙi na Allah

10 A ƙarshe kuma ku ƙarfafa kanku cikin Ubangiji da kuma cikin ƙarfin ikonsa. 11 Ku ɗaura wa jikinku dukan kayan yaƙi na Allah don ku iya tsaya ku yi gāba da dabarun Shaiɗan. 12 Ai, ba da 'yan Adam muke fama ba, amma da mugayen ruhohi ne na sararin sama, masu mulki, masu iko, da waɗanda mulkin zamanin nan mai duhu yake hannunsu. 13 Saboda haka sai ku ɗauki dukan kayan yaƙi na Allah domin ku tsaya a muguwar ranan nan, har bayan da kuka gama kome da kome, a same ku a tsaye.

14 Saboda haka fa ku tsaya da ƙarfi, gaskiya ta zama ɗamararku, adalci yă zama rigar ƙarfenku ta yaƙi. 15 Shirin kai Labari Mai Daɗi na salama, yă zama kamar takalma a ƙafafunku. 16 Ban da haka ma, bari bangaskiya ta zama garkuwarku[c] wadda za ku ɗauka ku kashe kibiyoyi na wutan Mugun nan.

17 Ku ɗauki hular yaƙi, wato, ceto, da kuma takobin Ruhu, wato, Maganar Allah. 18 Kullum ku yi addu'a ta ikon Ruhu cikin komen da kuke yi, kuna kuma roƙon Allah abin da kuke bukata. Da nufin haka, ku yi tsaro kullum yayin da kuke addu'a kuna tuna da tsarkaka. 19 Ni ma ku yi mini addu'a, in sami baiwar yin

6.2-3: Fit 20.12; M. Sh 5.16 **6.4**: Kol 3.21 **6.5-8**: Kol 3.22-25
6.9: M. Sh 10.17; Kol 3.25; 4.1 **6.14**: Ish 11.5; 59.17 **6.15**: Ish 52.7
6.17: Ish 59.17

[c] **6.16 garkuwarku**: A zamanin dā sojoji sukan ɗauke ta a hannu don su tare kibiyoyi daga abokan gāba.

Hoton soja da garkuwa a hannun hagunsa (6.16)

magana ba tsoro, in sanar da asirin bishara ga mutane. 20 Ta dalilin wannan bishara ne na zama wakili, ko da yake ina ɗaure! Ku yi mini addu'a domin duk lokacin da nake yin wa'azi in yi shi ba tsoro kamar yadda ya kamata in yi.

Maganar Karshe

21 Tikikus, ɗan'uwanmu wanda muke ƙauna, mai hidima, mai aminci kuma ga Ubangiji, zai sanar da ku kome don ku ma ku san yadda nake da lafiya da kuma halin da nake ciki. 22 Na aike shi gare ku musamman domin ku san yadda muke, yă kuma ƙarfafa muku zuciya. 23 'Yan'uwa, salama daga Allah Uba da Ubangiji Yesu Almasihu ta kasance a cikinku, tare da ƙauna da bangaskiya. 24 Alheri yă kasance tare da dukan masu ƙaunar Ubangijinmu Yesu Almasihu da ƙauna marar ƙarewa.

6.21: A.M. 20.4; 2 Tim 4.12 **6.21-22**: Kol 4.7-8

WASIKAR BULUS ZUWA GA
FILIBIYAWA

Gabatarwa

Manzo Bulus ne ya rubuta wannan *Wasikar Bulus zuwa ga Filibiyawa* a tsakanin shekara ta A.D. 59 da A.D. 61. Bulus ya rubuto wasikan nan zuwa ga jama'ar masu bi na farkon da ya kafa a kasar Turai a lokacin da yake a kurkuku a Roma.

Dalilin da ya sa an rubuta wannan wasika shi ne domin a gode wa masu bi na birnin Filibi a kan taimako na kyautai da addu'o'in da suka yi a lokacin da Bulus yake wahala.

A cikin wasikar an tsawata wa sauran masu aikin bisharar da suka ki hada kai da Bulus. (An kuma nuna damuwa saboda koyarwar karyar da take tasowa a cikin jama'ar masu bi a Filibi da kuma yadda ake matsa wa mutane cewa wai sai sun kiyaye Dokar Musa kafin su sami ceto.) Wasikar ta karfafa bangaskiyarsu ta kuma nemi su yi koyi da irin hakuri da saukinkai irin na Yesu da kuma irin jimrewar da Bulus ya yi, su kuma kasance da farin ciki kullum. A karshe wasikar ta shawarce su su yi zaman lafiya da junansu.

Abubuwan da Suke Ciki

Gaisuwa da addu'a 1.1-11
Manufar rayuwa ga Bulus 1.12-26
Rayuwa cikin Almasihu 1.27—2.18
Timoti da Abaforiditus 2.19-30
Gargadi da karfafawa 3.1—4.9
Gaisuwar karshe 4.10-23

Gaisuwa

1 [1] Daga Bulus da Timoti, bayin Almasihu Yesu zuwa ga dukan tsarkaka da suke bin Almasihu Yesu a Filibi, tare da dattiban jama'ar masu bi da masu yi muku hidima.

2 Alheri da salamar Allah Ubanmu da Ubangiji Yesu Almasihu su kasance tare da ku.

Addu'ar Bulus domin Filibiyawa Masu Bin Yesu

3 Ina gode wa Allah a duk lokacin da na tuna da ku. [4] Da farin ciki kuwa nake yin roke-rokena ga Allah saboda ku duka. [5] Ina

---

1.1: A.M. 16.12

godiya saboda kun haɗa kai da ni cikin aikin bishara tun daga ranar farko har zuwa yau. 6 Na tabbata shi wanda ya fara aiki mai kyan nan a cikinku, zai ci gaba har yă gama shi a Ranar da Yesu Almasihu zai dawo. 7 Daidai ne in riƙa tunaninku haka, ku duka, domin kuna zuciyata, saboda dukanku kun nuna mini alherin Allah a lokacin da aka kulle ni a kurkuku, da kuma ta wurin kāre bishara da tabbatar da ita. 8 Allah shi ne shaidata, ya san yadda nake ƙaunarku duka da ƙaunar Almasihu Yesu.

9 Addu'ata ita ce ku ƙaru cikin ƙauna da sanin Allah da kowace irin ganewa. 10 Wannan zai taimake ku ku iya zaɓan abin da ya fi kyau, don a Ranar da Almasihu zai dawo ku zama masu tsarki, marasa laifi. 11 A kuma cika ku da ayyuka masu kyau da suke nuna halin kirkin da ake samuwa ta wurin Yesu Almasihu domin ɗaukaka da yabon Allah.

Bulus Yana Rayuwa domin Almasihu

12 'Yan'uwa, ina so ku sani cewa, abin da ya faru da ni ya ƙara sa bishara ta yaɗu, 13 har sojojin fadar sarki, da sauran mutane suka sani cewa an kulle ni a kurkuku saboda Almasihu ne. 14 Kulle ni da aka yi a kurkuku ya sa 'yan'uwa da yawa a cikin Ubangiji suka ƙara samun ƙarfin hali su yi maganar Allah ba tare da tsoro ba.

15 Waɗansu dai suna wa'azin Almasihu saboda kishi da neman faɗa ne, amma waɗansu suna yi da nufi mai kyau. 16 Waɗannan da suke wa'azi da nufin mai kyau suna wa'azi da ƙauna ne, don sun sani an kulle ni domin ina kāre bishara. 17 Sauran suna wa'azi a kan Almasihu da halin sonkai ne ba cikin gaskiya ba. Sonsu ne in ƙara shan wahala a kurkuku.

18 To, ba kome. Ta kowane hali dai, ko da nufin ƙarya, ko da nufin gaskiya, ana wa'azi a kan Almasihu ne. Wannan yana sa in yi farin ciki. I, zan ci gaba da yin farin ciki, 19 domin na sani, ta wurin addu'o'inku, da taimako daga wurin Ruhun Almasihu Yesu, a ƙarshe za a sake ni. 20 Ina marmari, kuma ina sa zuciya cewa kada in kawo wa kaina kunya cikin aikin Ubangiji, amma in yi maganata ba tare da tsoro ba. Cikin dukan abin da zan yi, bari Almasihu yă sami ɗaukaka yanzu da kowane lokaci a wurina, ko ina da rai ko na mutu. 21 Domin ni kam, idan na rayu, don Almasihu ne; idan ma na mutu, duk riba ce. 22 Idan ya zama zan rayu cikin jiki, zan yi aiki mai amfani ke nan. Amma na rasa

1.13: A.M. 28.30

wanda zan zaɓa. 23 Duka biyu suna jan hankalina. Sona dai in
koma wurin Almasihu in zauna tare da shi. Haka ya fi kyau.
24 Amma don in taimake ku, gara in rayu cikin jiki. 25 Tun da na
tabbatar da haka, na sani zan zauna tare da ku duka domin ku ci
gaba da farin ciki cikin bangaskiyarku. 26 Ta haka idan na sāke
kawo muku ziyara, za ku sami babban dalilin yin taƙama da
Almasihu Yesu ta wurina.

27 Sai dai ku yi zaman da ya dace da bisharar Almasihu. Ta
haka, ko na zo na gan ku, ko ma ban zo ba, zan ji labarinku in
sani cewa kun tsaya sosai tare, kuna fama tare, ra'ayinku ɗaya
saboda bangaskiyar bishara, 28 ba tare da jin tsoron abokan
gābanku ba ko kaɗan. Ai, wannan tabbaci ne a gare su cewa za
su halaka, amma a wurinku tabbacin cetonku ke nan. Wannan
tabbacin kuwa daga wurin Allah yake. 29 Don alherin da ya yi
muku ba don ku gaskata da Almasihu kaɗai ba ne, amma har ma
don ku sha wahala saboda shi, 30 kuna shan fama irin yadda kuka
taɓa gani nake sha, kuka kuma ji ina sha har yanzu.

Misalin Kasƙantar Almasihu

2 1 Idan rayuwarku a cikin Almasihu tana ƙarfafa ku, ƙaunarsa
kuma tana yin muku ta'aziyya, idan kuna zumunci cikin
Ruhu, kuna kuma ƙauna da tausayin juna, 2 to, ina roƙonku ku sa
in ji daɗi sosai. Bari kuma tunaninku yă zama ɗaya, kuna ƙaunar
juna, kuna kuma haɗa kanku tare. 3 Kada ku yi kome da sonkai
ko girmankai, sai dai ku ƙasƙanta kanku. Bari kowa yă mai da
wani ya fi shi. 4 Kada ku kula da kanku kaɗai, amma ku kula da
waɗansu kuma. 5 Bari ku zama da irin halin Almasihu Yesu.

6 Ko da yake shi Allah ne,
bai mai da kasancewarsa daidai da Allah
abin da zai rike da ƙarfi ba,
7 sai dai ya mai da kansa kamar ba kome ba,
ya ɗauki matsayin bawa.
Da kamannin mutum ne ya zo.
8 Ya ƙasƙantar da kansa ta yin biyayya wadda ta kai shi
har ga mutuwa,
mutuwar ma ta kan gicciye.
9 Saboda haka ne ma Allah ya ɗaukaka shi sosai.
Ya ba shi sunan nan da ya fi kowane suna,
10 don kowace gwiwa sai ta durƙusa wa sunan nan na Yesu,
a sama da ƙasa, da kuma can ƙarƙashin ƙasa.

1.30: A.M. 16.19-40

11 Kuma kowane harshe yă shaida cewa
Yesu Almasihu Ubangiji ne,
don ɗaukakar Allah Uba.

Yin Haske a Duniya kamar Fitilu

12 Saboda haka, ya ku waɗanda nake ƙauna ina roƙonku kamar yadda kullum kuke yi mini biyayya ko ba na nan, yanzu ma da ba na nan ku ƙara yin biyayya. Ku cika aikin cetonku ta wurin ci gaba da ƙoƙarin rayuwa mai kyau tare da tsoron Allah. 13 Gama Allah shi ne yake aiki a zuciyarku, shi ne yake sa ku yarda da abin da yake so, ku kuma yi shi.

14 Duk abin da za ku yi, kada ku yi shi da gunaguni, ko gardama, 15 don ku zama marasa laifi, masu tsarki, cikakkun 'ya'yan Allah. Kuna zama ne a cikin mugayen mutane masu taurin kai, waɗanda kuke haskakawa a cikinsu kamar fitilu a duniya. 16 Idan kuka riƙe saƙo mai ba da rai sosai, zai sa in yi taƙama a Ranar da Almasihu zai dawo, don yă zama ban sha fama da wahala a banza ba.

17 Bangaskiyarku da aikinku a cikin Ubangiji kamar hadaya ne a gare shi, kuma ko da na zub da jinina a kan hadayan nan, zan ji daɗi, in yi murna tare da ku duka. 18 Haka kuma za ku yi farin ciki, ku yi murna tare da ni.

Timoti da Abaforiditus

19 Ina sa zuciya cikin Ubangiji Yesu cewa zan aika Timoti wurinku ba da daɗewa ba, don ni ma in ƙara samun ƙarfafawa ta wurin jin labarinku. 20 Ba ni da wani kamarsa wanda ya damu da ku sosai. 21 Sauran dai, abin da ya shafe su kawai suka damu da shi, ba abin da ya shafi Yesu Almasihu ba. 22 Ai, kun san yadda Timoti yake, yadda muka yi aikin bishara tare kamar ɗa da babansa. 23 Saboda haka ina fata zan aika shi da zarar na ji abin da zai faru da ni. 24 Kuma idan Ubangiji ya yarda, ni ma zan zo ba da daɗewa ba.

25 Na ga ya kamata in aika muku da ɗan'uwana, Abaforiditus. Shi abokin aikina ne, abokin famana kuma, wanda kuka aiko yă yi mini hidima. 26 Yana marmari yă gan ku duka, har ma ya damu sosai don kun ji ya yi rashin lafiya. 27 Lallai ya yi rashin lafiya har ma ya kusa mutuwa. Amma Allah ya ji tausayinsa, ba shi kaɗai ba, har ma da ni. Da ba haka ba da bakin ciki zai yi mini yawa.

2.10-11: Ish 45.23 **2.15:** M. Sh 32.5

28 Shi ya sa na yi niyya sosai in aika shi don ku ji daɗin sāke
ganinsa, ni kuma in rage damuwata. 29 Ku karɓe shi da murna
sosai saboda Ubangiji. A girmama irinsu yadda ya kamata,
30 domin ya kusa yă mutu don aikin Almasihu, yana ba da ransa
don yă yi mini taimakon da ku ba ku iya yi ba.

Adalci na Gaskiya

3 1 A ƙarshe kuma, 'yan'uwa, ku yi farin ciki cikin Ubangiji.
Bai dame ni in sāke rubuta muku waɗannan abubuwa ba. Ga
shi kuwa, domin amfaninku ne.

2 Ku yi hankali da karnukan nan,[a] masu mugayen ayyuka,
masu yankan jikin nan, wai suna kaciya. 3 Ai, mu ne masu kaciya
ta ainihi, mu da muke bauta wa Allah ta wurin Ruhu Mai Tsarki,
masu taƙama da Almasihu Yesu, mu da ba mu dogara da ayyukan
da ake gani ba, 4 ko da yake ni ina iya dogara da ayyukan da ake
gani. Idan kuma akwai wanda yake tsammani yana da dalilin
dogara da ayyukan da ake gani ne, to, ni na fi shi. 5 Ga shi an yi
mini kaciya a rana ta takwas, asalina, ni ɗan Isra'ila ne, na kabilar
Benjamin, cikakke ɗan Ibraniyawa kuwa. Game da bin Dokar
addinin Yahudanci kuwa, ni Bafarisiye ne. 6 Wajen ƙwazon bin
addini kuma ina tsananta wa jama'ar masu bi, wajen kiyaye
umarnan Doka kuma, ba ni da laifi. 7 Amma abin da dā ya zama
mini riba yanzu, na ɗauka hasara ce saboda Almasihu. 8 Ai, babu
abin da ya fi daraja kamar sanin Almasihu Yesu Ubangijina. Na
mai da dukkan abubuwa hasara ce, domin in san shi. Saboda shi
na yi hasarar dukkan abubuwa. Na mai da su abin banza, domin
in sami Almasihu, 9 in kuma zama a cikinsa. Wannan kuwa ba
don adalcina ta wajen kiyaye Dokar addini ba, sai dai ta adalcin
nan wanda yake fitowa daga bangaskiya cikin Almasihu, wato,
da adalcin nan wanda yake samuwa daga Allah ta wurin
bangaskiya. 10 Ina so in san Almasihu da ikon tashinsa daga
matattu. Ina so in yi tarayya cikin shan wuyarsa, da mutuwarsa.
11 Domin ko ta yaya in kai ga tashin nan daga matattu.

Kokarin Yin Nasara

12 Ba wai na riga na zama yadda ya kamata in zama ba, ko
kuma na riga na zama cikakke ba, a'a, sai dai ina ta fama in yi
nasara, don Almasihu Yesu ya riga ya mai da ni nasa. 13 To,

3.5: A.M. 23.6; 26.5; Rom 11.1 **3.6:** A.M. 8.3; 22.4; 26.9-11

[a] **3.2 karnukan nan:** Yahudawa suna ganin waɗanda ba Yahudawa ba kamar karnuka. Amma a nan ana nufin waɗanda suke gāba da koyarwar Bulus ne.

'yan'uwa, ban ce na riga na rike abin ba, amma abu daya nake yi, ina mantawa da abin da ya riga ya wuce, ina kokarin yin abin da yake gaba. 14 Ina kokari in yi nasara don in sami ladan kiran nan zuwa sama da Allah ya yi mini ta wurin Almasihu Yesu.

15 Saboda haka dukanmu da muka yi girma cikin ruhaniya, sai mu dauki wannan tunani. Amma idan wadansunku suna da wani ra'ayi dabam, to, Allah zai bayyana muku wannan kuma. 16 Babban abin shi ne duk inda muka kai, mu ci gaba daga nan.

17 'Yan'uwana, ina so ku bi misalina, ku kuma dubi wadanda zamansu ya yi daidai da yadda muka nuna muku. 18 Akwai wadansu mutanen da na sha yi muku gargadi a kansu. Ina kuma sake gaya muku yanzu, har da hawaye cewa rayuwarsu ta mai da su masu gaba da mutuwar Almasihu a kan gicciye. 19 A karshe za su halaka. Abin da jikinsu yake so ne kawai suka damu da shi. Suna takama da rashin kunyarsu. Sun damu da abubuwan duniya. 20 Mu dai 'yan mulkin sama ne. Daga can ne kuma muke jiran zuwan Mai Ceto, Ubangiji Yesu Almasihu. 21 Shi ne mai ikon kawo dukan abubuwa karkashin mulkinsa. Ta wurin ikon nan nasa zai sake jikin nan namu na kaskanci, yă mai da shi kamar jikin nan nasa na daukaka.

Tsayawa da Karfi cikin Ubangiji

4 1 Saboda haka, 'yan'uwana, ku da kuke a zuciyata kullum, har ina marmarin ganinku, ku da kuke sa zuciyata ta ji dadi, ku da nake takama da ku, ina rokonku ku tsaya da karfi cikin Ubangiji, ku wadanda nake kauna.

2 Ina jan kunnen Yudiya da Sintiki, su shirya da juna cikin Ubangiji. 3 Kai, abokin aikina[b] mai aminci, ina rokonka ka taimaki wadannan matan, don sun sha fama tare da ni a cikin aikin bishara. Haka ma Kilemen da sauran abokan aikina, wadanda sunayensu suke a rubuce a littafin rai.

4 Ku yi farin ciki cikin Ubangiji kullum. Ina sake gaya muku ku yi farin ciki.

5 Bari ku zama da saukinkai ga kowa. Ubangiji ya yi kusan zuwa. 6 Kada ku damu da kome, sai dai a cikin kome ku fada wa Allah bukatunku ta wurin addu'a da roko, tare da godiya. 7 Ta haka kuwa Allah zai ba ku salama irin da ta wuce ganewar dan Adam, za ta tsai da zukatanku da tunaninku cikin Almasihu Yesu.

3.17: 1 Kor 4.16; 11.1

[b] **4.3 abokin aikina:** Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Sizigus" ne a nan.

8 Daga ƙarshe kuma, 'yan'uwana, ku riƙa yin tunani a kan
duk abin da yake gaskiya, abin girmamawa, abin da yake daidai,
abin tsarki, abin so, abin da yake mai dacewa, wato, dukan abin
da yake mafi kyau, ko abin da ya isa yabo. 9 Ku yi aiki da
abubuwan da kuka koya kuka kuma karɓa, da kuma abubuwan
da kuka ji, kuka gani a wurina. Ta haka, Allah mai salama zai
kasance tare da ku.

Bulus Ya Gode wa Masu Bi na Filibi

10 Na yi farin ciki sosai ga Ubangiji don yanzu kun sāke nuna
kuna kula da ni. Ko da yake dā ma kun kula da ni amma ba ku
sami dama ku nuna mini ba. 11 Ba wai ina kukan rashin wani abu
ba ne. Ai, na koyi yadda zan zauna da kwanciyar rai a kowane
halin da nake ciki. 12 Na san yadda zan zauna ko cikin talauci ko
cikin arziki. Zan iya zama a kowane irin hali, ko cikin yunwa ko
cikin ƙoshi, ko cikin rashi ko cikin samu. 13 Zan iya yin kome ta
wurin Almasihu wanda yake ƙarfafa ni.

14 Duk da haka kun kyauta da kuka taimake ni a lokacin da
nake cikin wahala. 15 Ku Filibiyawa kun sani, a lokacin da na fara
aikin wa'azin Labari Mai Daɗi, da na bar ƙasar Makidoniya ba
wata jama'ar masu bin da ta haɗa kai da ni ta wurin bayarwa da
karɓa, sai ku kaɗai. 16 Don ko a lokacin da nake Tasalonika ma
kun aiko mini da taimakon abubuwan da nake bukata ba ma sau
ɗaya ba. 17 Kada ku yi tsammani ina neman kyauta a wurinku ne,
a'a, sai dai ina nema muku amfani ne da za a ƙara a kan ribarku.
18 An biya ni duka, biyan da ya wuce misali. Bukatata ta biya, da
yake na karɓi kyautarku da kuka aiko ta hannun Abaforiditus.
Wannan hadaya ce mai ƙamshi, baiko ne kuma mai kyau da Allah
zai karɓa yă kuma ji dadinsa. 19 Allahna kuma zai biya muku ko
wace bukatarku bisa ga albarkunsa masu yawa ta wurin Almasihu
Yesu. 20 Daukaka ta tabbata ga Allahnmu da Ubanmu, har abada.
Amin.

Gaisuwar Karshe

21 Ku gai da dukan tsarkaka cikin Almasihu Yesu.
'Yan'uwan da suke tare da ni suna gaishe ku.

22 Tsarkaka duka suna gaishe ku, musamman waɗanda suke
a fadar Kaisar.

23 Alherin Ubangiji Yesu Almasihu yă kasance tare da ku.
Amin.

4.15-16: 2 Kor 11.9 **4.16:** A.M. 17.1 **4.18:** Fit 29.18

WASIKAR BULUS ZUWA GA
KOLOSIYAWA

Gabatarwa

Manzo Bulus ne ya rubuta wannan wasika zuwa ga jama'ar masu bi da take a Kolosi wadda wani mataimakin Bulus mai suna Abafaras ne ya kafa. Wasikar Kolosiyawa da ta Afisawa da ta Filibiyawa da ta Filimon su ne akan ce da su wasiku daga kurkuku. Manzo Bulus ya rubuta wadannan wasiku ne daga birnin Roma a lokacin nan da yake tsare a wani gida har na tsawon shekara biyu (Dubi A. M. 28.16-31). An rubuta wannan wasika wajen shekara ta A.D. 60.

Bulus kuwa ya rubuta wannan wasika domin ta zama hanyar yin gyara game da koyarwar karyan da ta taso a Kolosi. Koyarwar karyan nan ta ce samun ceto ya dogara ga kiyayen al'adun mutane ne. Ta shafi bautar mala'iku da ruhohi. Ban da haka ma ta ce dole ne mai bi ya bi al'adu iri-iri na ci da sha da yin kaciya da sauransu.

Wasikar ta bayyana cewa ana samun cikakkiyar ceto daga wurin Yesu ne. Ta kuma ce Yesu shi ne kamannin Allah na ainihi. Wato, cikakkiyar Allahntaka ta kasance ga Yesu ke nan. Yesu shi ne kuma mahalicci wanda yake nan tun kafin kome yă kasance, dominsa ne kuma kome ya kasance. Wasikar ta bayyana Yesu a kan cewa shi ne kan jama'ar masu bi, shi ne na farkon da ya tashi daga matattu, shi ne kuma mai shirya tsakanin Allah da mutane.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-14
Yesu Almasihu da aikinsa 1.15-23
Hidimar Bulus ga jama'ar masu bi 1.24—2.7
Rayuwa cikin Almasihu 2.8—4.6
Gaisuwar karshe 4.7-18

Gaisuwa

1 [1] Daga Bulus, wanda Allah ya zaba don yă zama manzon
Yesu Almasihu, tare da Timoti, dan'uwanmu, [2] zuwa ga
tsarkaka masu aminci cikin Almasihu da suke zama a Kolosi.

Alherin Allah Ubanmu da salamarsa su kasance tare da ku.

Godiya da Addu'a

3 Kullum muna gode wa Allah, Uban Ubangijinmu Yesu Almasihu, a duk lokacin da muke addu'a dominku. [4] Don mun ji

yadda kuka gaskata cikin Almasihu Yesu, da kuma yadda kuke ƙaunar dukan tsarkaka. 5 Dalilin da kuke yin haka kuwa shi ne,
kuna sa zuciya a kan abubuwan nan masu kyau waɗanda aka yi
muku ajiyarsu a sama. Wannan shi ne Labari Mai Dadîn da aka
yi muku tun da farko, wato, maganar gaskiyan nan da kuka ji.
6 Bisharan nan tana ta kawo albarku, tana kuma bazuwa cikin
dukan duniya, kamar yadda ta yi a cikinku tun lokacin da kuka
fara jin labarin alherin Allah, kuka kuma gane yadda take.
7 Abafaras, abokinmu da muke ƙauna ne ya fara kawo muku
wannan labarin alherim Allah. Da mu da shi duk masu bauta ne
na Almasihu. Shi mai aminci ne kuwa, yana hidimar a cikinku a
madadinmu[a] ne. 8 Shi ne kuma ya ba mu labarin irin ƙaunar
mutanen da kuke yi cikin Ruhu.

9 Shi ya sa tun lokacin da muka ji labarin, ba mu fasa yin
addu'a dominku ba, muna roƙon Allah yă nuna muku nufinsa
dalla-dalla domin ku sami hikima ta Ruhu, ku kuma sami ganewar
kome duka. 10 Ta haka ne za ku yi rayuwa wadda ta dace da masu
bin Ubangiji, kuma za ku riƙa yin abubuwan da yake so. Yadda
kuke rayuwa kuma zai nuna halaye masu kyau, za ku kuma riƙa
ƙaruwa da sanin Allah. 11 Bari Allah yă ƙarfafa ku da ƙarfinsa
mai ɗaukaka yadda za ku tsaya da ƙarfi sosai, domin ku jimre a
kan kowane abin da ya faru, kuna haƙuri cikin farin ciki. 12 Ku
riƙa gode wa Uba a kowane lokaci, domin shi ne ya sa muka isa
samun rabo cikin abubuwan nan da ya shirya wa mutanensa, cikin
mulkin haske. 13 Gama shi ya cire mu daga mulkin duhu, ya kai
mu mulkin Ɗansa wanda yake ƙauna, 14 wanda ta wurinsa ne
muka sami fansa, wato, yafewar zunubanmu.[b]

Yesu Almasihu da Aikinsa

15 Almasihu shi ne kamannin Allah da ba a iya gani, shi ne
Ɗan fari kafin a halicci kome, 16 don ta wurinsa ne aka yi kome
da kome da yake sama da kuma ƙasa, da abubuwan da ake gani
da waɗanda ba a iya gani. Ta wurinsa ne aka yi dukan abubuwan
da suke da iko a sama, da kuma shugabanni, da masu mulki, har
ma dukan abin da aka yi, an yi ne ta wurinsa, kuma dominsa.
17 Almasihu yana nan kafin kome, ta wurinsa ne ma kome yake
a harhaɗe. 18 Shi ne kai na jiki, wato, jama'ar masu bi. Shi ne

1.7: Kol 4.12; Fil 23 1.14: Afi 1.7

[a] **1.7 madadinmu:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "maimakonku" ne a nan.

[b] **1.14 yafewar zunubanmu:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā sun ƙara "ta wurin jininsa" a nan.

tushe, shi ne kuma na farkon da ya tashi daga matattu, don cikin kome da kome, yă zama shi ne na fari. 19 A gare shi ne dukan Allahntakar Allah ta kasance. 20 Ta wurin Ɗan ne kuma Allah ya komar da dukan halittarsa, zuwa wurinsa. Wato, ta wurin zub da jini wanda Ɗansa ya yi a kan gicciye, ya komar da kome da yake sama da ƙasa zuwa wurinsa.

21 A dā dai kun yi nisa da Allah, har kun zama masu gāba da shi a zuciyarku saboda mugayen abubuwan da kuke yi. 22 Amma yanzu, ta wurin Almasihu wanda ya zama mutum ya kuma mutu, Allah ya mai da ku abokansa. Yanzu kuma Almasihu ya miƙa ku masu tsarki, marasa laifi, marasa zargi a gaban Allah. 23 Sai dai ku ci gaba cikin bangaskiyarku, kuna tsayawa sosai a kan tushen nan. Kada kuma ku yarda a jijjiga ku ku bar sa zuciyan nan da kuka samu a lokacin da kuka ji bisharan nan. Wannan bisharar da aka yi wa'azinta ga kowa a duniya ne, ni Bulus, na zama mai hidimarta.

Hidimar Bulus ga Jama'ar Masu Bi

24 Yanzu, ina farin ciki saboda wuyar da nake sha dominku, don ta wurin wuyan nan zan cika abin da ya rage na wuyar da Almasihu ya sha saboda jikinsa, wato, jama'ar masu bi. 25 Allah ne ya zaɓe ni domin in zama bawan jama'ar masu bi, ya ba ni wannan aiki domin in taimake ku, in yi wa'azin cikakkiyar maganar Allah. 26 Wannan labarin da nake gaya muku, asiri ne da yake a ɓoye tun zamanai masu yawa, amma yanzu an bayyana shi ga tsarkakansa. 27 Nufinsa ne mutanensa su san yawan dukiya da take cikin asirin nan nasa mai ɗaukaka wanda ya shirya domin dukan waɗanda ba Yahudawa ba. Wannan asirin kuwa shi ne yadda Almasihu yake zama a cikin zuciyarku, kuna kuma sa rai za ku kasance tare da shi a cikin ɗaukakarsa. 28 Shi ya sa muke gaya wa kowa a kan Yesu Almasihu, muna jan kunnen kowane mutum, muna kuma koyar da waɗannan abubuwa da dukkan hikimarmu don mu miƙa kowa cikakke cikin Almasihu. 29 Saboda wannan ne ina fama ina kuma ƙoƙari da iyakar ƙarfin nan da Almasihu yake iza a cikina ta wurin ikonsa.

2 1 Ina so ku san irin ƙoƙarin da nake yi dominku da mutanen da suke Lawudikiya, da kuma dukan waɗanda ba su taɓa ganina ba. 2 Sona shi ne, ƙauna ta haɗa su, su kuma sami ƙarfafawa a zuciyarsu. Ta haka za su sami babban arzikin nan, wato, tabbaci wanda ya zo ta wurin ganewa har su kai ga sanin

1.18: Afi 1.22-23 **1.20**: Afi 2.16

zurfin asirin Allah, wato, Almasihu da kansa[6] ke nan. 3 A cikinsa
ne aka ɓoye dukkan dukiya ta hikima da ta sani.
4 Ina gaya muku wannan ne saboda kada wani yă ruɗe ku da
zaƙin baki. 5 Ko da yake ni kaina ba na nan tare da ku, amma
zuciyata tana tare da ku. Ina farin ciki sosai da jin yadda kuke
tsaye daram, kuna kuma dagewa cikin bangaskiyarku cikin
Almasihu.

Bin Almasihu Ya Kawo Sabuwar Rayuwa

6 Tun da kun yarda cewa Yesu Almasihu shi ne Ubangijinku,
sai ku ci gaba da yin rayuwarku a cikinsa. 7 Ku yi ta neman
ƙarfinku a cikinsa, ku gina ranku a kansa, kuma kuna cin gaba
da gaskata da shi kamar dai yadda muka koya muku, kuna kuma
gode masa kowane lokaci.
8 Ku lura fa kada wani yă ɗauki ilimin duniyan nan yă ruɗe
ku har ku bar hanyan nan ta gaskiya. Wannan irin ilimi rudi ne
na banza. Daga wurin mutane ne ya fito, kuma daga wurin
ruhohin da suke da iko a duniya ne, ba daga Almasihu ba. 9 Domin
a cikin Almasihu ne, wanda ya zama mutum dukkan Allahntaka
take tabbata. 10 Haka ma a cikinsa rayuwarku ta zama cikakke.
Shi ne kuwa shugaban dukkan sarauta da iko.
11 A cikinsa ne kuma aka yi muku sabuwar kaciya, wadda ba
irin da mutum ne yake yi ba, amma wadda Almasihu ne ya yi
muku, ta wurin tuɓe muku halinku na jiki. 12 Da aka yi muku
baftisma, an binne ku ne tare da Almasihu ke nan. Ta wajen
baftisma kuma aka ta da ku tare da Almasihu, ta wurin
bangaskiyarku a cikin ikon Allah wanda ya ta da shi daga matattu.
13 A dā ku matattu ne saboda zunubi da kuma saboda rashin
kaciyarku, amma Allah ya ta da ku rayayyu cikin Almasihu. Ya
yafe mana zunubanmu. 14 A dā an sa shaida a kanmu a rubuce
cewa mu masu karyar doka ne. Shari'a kuma tana gāba da mu.
Amma Allah ya soke ta, har ana iya cewa ya kafe ta da kusa a
jikin gicciyen Almasihu. 15 Ya ƙwace makamai na ikoki da
mulkoki, ya ba su kunya a fili, yadda ya ci nasara a kansu a kan
gicciye.

2.12: Rom 6.4 **2.13**: Afi 2.1-5 **2.14**: Afi 2.15

[6] **2.2 Almasihu da kansa**: Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "asirin Allah, duk da na Uba da na Almasihu" ne a nan.

Bin Dokoki Bai Isa Ba

16 Saboda haka kada ku bar wani yă ba ku laifi a kan
abubuwan da za ku ci ko abubuwan da za ku sha, ko kuma yă
ba ku laifi a kan rashin tunawa da wani biki, ko tsayawar wata,
ko hutu a Ranar Hutu. 17 Wadannan abubuwa kamar hoto ne
kawai wadanda suka nuna wa mutane abin da zai zo, amma
Almasihu shi ne ainihin abin. 18 Saboda haka kada ku bar kowa
mai daga kai yă rena ku da cewa shi wani abu ne saboda wai
yana ganin ru'uya. Irin mutumin nan yakan nuna ƙaskancin kai
na ƙarya, wai yana yin wa mala'iku sujada, alhali kuwa kumburan
kansa yake yi ba dalili, sai son zuciya irin ta halin mutum kawai.
19 Ai, irin wannan ya riga ya rabu da Almasihu wanda shi ne kan
jama'ar masu bi, wanda ta gare shi ne dukkan jiki ya dogara. Ai,
Almasihu shi ne yake sa jikin yă hadu ta wurin gaɓoɓi da jijiyoyi,
yana kuma girma da girman da Allah yake sawa.

20 Da yake kun mutu tare da Almasihu, har kun rabu da
mugayen ruhohi na duniyan nan, don me kuke wadansu halaye
kamar har yanzu ku na duniya ne? Don me kuka yarda da dokoki
wadanda mutane suke bayarwa 21 kamar dokoki masu cewa,
"Kada ka taɓa, kada ka dandana, kada ka kama?" 22 Irin
wadannan dokoki suna magana a kan abubuwan da ba sa dadewa.
Ayyukan mutum ne su, sun kuma fito daga koyarwar mutum. 23 A
idon mutane irin dokokin nan suna da alamar hikima, sukan kawo
ƙwazo da yawa da ƙaskantar da kai cikin addini (ko da yake
wadannan ƙarya ne), har mutane suna ba wa jikinsu wahala.
Amma gaskiyar ita ce dokokin nan ba su da wani ikon da zai
taimaki mutum yă sha kan sha'awar jikinsa.

3 1 Tun da yake Allah ya ta da ku da rai tare da Almasihu, sai
ku sa ido a kan abubuwan nan da suke sama, inda Almasihu
yake, yana kuwa zama a hannun dama na Allah. 2 Ku sa zuciyarku
a kan abubuwan nan da suke sama, kada ku damu da abubuwan
duniyan nan. 3 Gama kun riga kun mutu, ranku kuwa yana a ɓoye
tare da Almasihu cikin Allah. 4 Almasihu ne ran naku nan na
gaskiya. Idan ya sāke zuwa, ku ma za ku kasance tare da shi cikin
daukakarsa.

Rayuwa cikin Tsarki

5 Saboda haka sai ku kashe halin sha'awace-sha'awacen
duniya a zuciyarku, wato, iskanci, da aikin lalata, da muguwar

---

2.16: Rom 14.1-6 **2.19:** Afi 4.16 **3.1:** Zab 110.1

sha'awa, da mugun hali, da kuma kwaɗayi, wanda shi ma bautar gumaka ne. 6 Saboda mugayen abubuwa irin waɗannan ne fushin
Allah yake sauko wa mutanen da suka ƙi binsa.[c] 7 Dā ku da kanku
kuna da irin waɗannan halayen, sa'ad da kuke cikin wannan
muguwar rayuwa. 8 Amma yanzu dole ne ku rabu da dukan irin
halayen nan. Ku bar yin fushi, da zafin rai, da mugun nufi, da
zage-zage, da maganar banza. 9 Kada ku yi wa juna ƙarya, da
yake kun riga kun bar halinku na dā da ayyukansa, 10 har kun
ɗauki sabon hali. Allah kuwa mahaliccin wannan sabon halin
naku zai yi ta sabunta shi don yă zama kamar nasa, don ku san
shi sosai. 11 Da yake kun sami sabon hali, babu sauran bambanci
tsakaninku ke nan. Da Yahudawa da waɗanda ba Yahudawa ba,
duk ɗaya ne. Ko an yi wa mutum kaciya ko ba a yi masa ba, duk
ɗaya ne. Babu bambanci tsakanin masu hali iri na dabba da
baƙauye, ko bawa ko mai 'yanci, domin Almasihu shi ne kome,
shi ne kuma yake cikinmu dukka.

12 Allah ya zaɓe ku don ku zama mutanensa masu tsarki
waɗanda yake ƙauna ƙwarai. Saboda haka ku riƙa jin tausayin
juna, kuna yin alheri, kuna nuna tawali'u da saukinkai da jimrewa.
13 Ku riƙa yin haƙuri da juna. Idan wani a cikinku ya yi wa wani
laifi, ku yafe masa. Kamar yadda Ubangiji ya yafe muku
zunubanku, haka ma ku ma ku yafe wa juna. 14 Fiye da waɗannan,
ku ƙaunaci juna, domin ƙauna ce za ta haɗa kome duka don yă
zama kamar yadda Allah yake so. 15 Bari salama ta Almasihu ta
bi da ku a kowane abin da za ku yi, don saboda salaman nan ce
Allah ya kira ku cikin jiki ɗaya, ku kuma zama masu gode wa
Allah kullum. 16 Bari maganar Almasihu ta kasance a zuciyarku
a yalwace, kuna koya wa juna, kuna yi wa juna gargaɗi da dukan
hikima, kuna waƙoƙin zabura da na yabon Allah, kuna yi wa
Allah waƙa, kuna kuma gode masa a zuciyarku. 17 A kowane abin
da kuke yi, cikin magana ko ayyuka, ku yi shi a cikin sunan
Ubangiji Yesu, kuna gode wa Allah Uba ta wurinsa.

Zaman Dacewa ga Iyali

18 Ku matan aure, ku ba mazanku girma kamar yadda ya dace
cikin Ubangiji.

3.9: Afi 4.22 **3.10:** Far 1.26; Afi 4.24 **3.12-13:** Afi 4.2 **3.13:** Afi 4.32
3.16-17: Afi 5.19-20 **3.18:** Afi 5.22; 1 Bit 3.1

[c] **3.6 mutanen da suka ƙi binsa:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da waɗannan kalmomi.

19 Ku maza kuma ku ƙaunaci matanku. Kada ku nuna musu
hali marar tausayi.
20 Ku yara, ku yi wa iyayenku biyayya cikin kowane abu,
domin haka Ubangiji yake so.
21 Ku ubanni, kada ku matsa wa yaranku lamba, don kada su
fid da zuciya.
22 Ku bayi, ku yi biyayya ga iyayengijinku na duniya a
kowane abu. Kada ku yi aikin ganin ido kamar masu neman yabon
mutane, a maimakon haka, ku yi aiki tsakaninku da Allah, kamar
masu tsoron Ubangiji. 23 Duk abin da kuke yi, ku yi shi da dukan
zuciyarku domin kuna yi wa Ubangiji ne, ba mutum ba. 24 Ku
sani fa Ubangiji zai ba ku gādo wanda yake ladanku. Gama
Ubangiji Almasihu kuke bauta wa! 25 Mai aikin mugunta kuwa,
zai sami ladan muguntarsa, don babu nunan bambanci.
4 1 Ku iyayengiji, ku riƙe bayinku da kyau. Ku ba su abubuwan
da ya kamata su samu. Ku tuna, ku ma kuna da Ubangiji a
sama.
2 Ku nace cikin addu'a, kuna tsaro, kuna kuma godiya. 3 Ku
kuma yi mana addu'a, yadda Allah zai buɗe mana hanyar yin
maganarsa, mu sanar wa mutane asirin nan na Allah, wato, labarin
Almasihu. Saboda asirin nan ne nake a kurkuku. 4 Ku yi mini
addu'a in bayyana asirin nan sosai, kamar yadda ya kamata in yi.
5 A cikin zamanku tare da marasa bi, ku yi kome da hikima,
kuna amfani da kowane zarafin da kuke da shi. 6 Bari maganarku
ta zama da ladabi da kuma daɗin ji, domin ku san irin amsar da
ya yi kyau ku ba kowa.

Gaisuwar Ƙarshe

7 Tikikus zai gaya muku kome game da yadda nake a nan.
Shi ɗan'uwanmu ne wanda muke ƙauna sosai, kuma shi mai
aminci ne cikin hidima. Mu da shi duk masu hidima ne na
Ubangiji. 8 Abin da ya sa na aike shi wurinku shi ne don yă kawo
muku labarin lafiyarmu, sa'an nan kuma yă ƙarfafa zuciyarku.
9 Ga kuma Onisimus tare da shi, wanda shi ma ɗan wajenku ne.
Shi ɗan'uwanmu ne da muke ƙauna ƙwarai, mai aminci ne kuwa.
Su biyun za su faɗa muku abin da yake faruwa a nan.
10 Aristarkus, wanda yake a kurkuku a nan tare da ni, ya ce
in gaishe ku, haka kuma Markus wanda kakansa ɗaya ne da

3.19: Afi 5.25; 1 Bit 3.7 **3.20**: Afi 6.1 **3.21**: Afi 6.4 **3.22-25**: Afi 6.5-8
3.25: M. Sh 10.17; Afi 6.9 **4.1**: Afi 6.9 **4.5**: Afi 5.16 **4.7**: A.M. 20.4; 2 Tim 4.12
4.7-8: Afi 6.21.22 **4.9**: Fil 10-12

Barnaba. (Shi ne na riga na yi magana a kansa, na ce muku in ya zo, ku karɓe shi hannu biyu-biyu.) 11 Joshuwa wanda ake ce da shi Justus, shi ma yana gaishe ku. Waɗannan mutane uku ne kawai Yahudawa a cikin waɗanda suke aikin mulkin Allah tare da ni. Sun kuwa taimake ni ƙwarai.

12 Abafaras wanda yake ɗaya daga cikinku, wanda shi ma bawan Yesu Almasihu ne, yana gaishe ku. Kullum yana kokawa cikin addu'a ga Allah don ku tsaya daram, ku kuma zama cikakku, kuna aikata dukan abin da Allah yake so, ba tare da shakka ba. 13 Ni kaina na shaida yadda shi Abafaras yake shan wuya don yă taimake ku da kuma mutanen Lawudikiya da na Hirafolis.

14 Luka, likitan nan da muke ƙauna, da kuma Dimas, suna gaishe ku.

15 Ku gai mini da dukan 'yan'uwan da suke Lawudikiya, da kuma Nimfa tare da jama'ar masu bi da take taruwa a gidanta. 16 In kun gama karanta wannan wasiƙa, sai ku aika da ita zuwa ga jama'ar masu bin da take a Lawudikiya, don su ma su karanta. Ku ma ku karanta wasiƙar da mutanen Lawudikiya za su aika muku. 17 Ku kuma gaya wa Arkibus ya mai da hankali yă gama aikin nan da Ubangiji ya ba shi.

18 Ni Bulus ne da hannuna nake rubuta muku wannan gaisuwa. Kada ku manta cewa ina nan a kurkuku. Alherin Allah yă kasance tare da ku.

4.10: A.M. 12.12,25; 13.13; 15.37-39; 19.29; 27.2; Fil 24

WASIKAR BULUS TA FARKO ZUWA GA
TASALONIKAWA

Gabatarwa

Manzo Bulus ne ya rubuta wannan wasiƙa zuwa ga jama'ar masu bi a Tasalonika wadda take a yankin ƙasar Makidoniya. Ana tsammani Bulus ya rubuta wasiƙan nan a tsakanin shekara ta A.D. 50-51 a Korinti. Wato, a sa'ad da aka kore shi daga Tasalonika (A. M. 17.10) ya bi ta Biriya da Atina (A. M. 17.14) zuwa Korinti (18.1,5).

Jama'ar masu bi a Tasalonika tana ɗaya daga cikin jama'un masu bi na farkon da manzo Bulus ya kafa. A kafawarta ba ta sami isasshen reno ba saboda fitinar Yahudawa (A. M. 17.1-9). An rubuta wasiƙar don a ƙarfafa jama'ar masu bi su tsaya da ƙarfi cikin bangaskiyarsu.

Da farko, Bulus ya gode wa Allah saboda bangaskiyarsu da ayyukansu na ƙauna da kuma sa zuciyar da suke da shi cikin Almasihu. Wasiƙar ta yi bayani game da waɗanda suka mutu cikin Almasihu, ta ƙarfafa masu bi kada su damu game da lokacin dawowar Almasihu, ta kuma gaya musu yadda za su zauna, su kuma ci gaba da yin aiki har Yesu yă dawo.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-3
Bangaskiyar Tasalonikawa 1.4—3.13
Rayuwar da Allah yake so 4.1-12
Abin lura a dawowar Ubangiji 4.13—5.11
Umarni na ƙarshe da gaisuwa 5.12-28

Gaisuwa

1 [1] Daga Bulus, da Sila, da Timoti, zuwa ga jama'ar masu bi a Tasalonika, wadda take ta Allah Uba da Ubangiji Yesu Almasihu.

Alheri da salama su kasance tare da ku.

Bangaskiyar Tasalonikawa da irin Zamansu

2 Kullum muna gode wa Allah saboda ku duka, muna kuma sa ku cikin addu'o'inmu koyaushe. [3] Muna tunawa da ayyukan bangaskiyarku a gaban Allahnmu, da Ubanmu, da faman da kuke yi don ƙauna, da kuma sa zuciyarku mai ƙarfi ga Ubangijinmu

1.1: A. M. 17.1

Yesu Almasihu. 4 'Yan'uwa waɗanda Allah yake ƙauna, mun san
cewa Allah ya zaɓe ku, 5 saboda mun kawo muku Labari Mai
Daɗi ba da magana kaɗai ya zo muku ba, amma har ma da iko,
da Ruhu Mai Tsarki da kuma cikakken tabbaci. Kun san irin
zaman da muka yi a cikinku domin amfaninku. 6 Kuka kuwa zama
masu koyi da mu, da kuma Ubangiji, kuka kuma karɓi maganar
Allah da farin cikin da Ruhu Mai Tsarki yake sawa, ko da yake
kun sha wahala sosai. 7 Ta haka ku ma kuka zama misali ga duk
masu bi na ƙasar Makidoniya da Akaya. 8 Domin daga wurinku
ne maganar Ubangiji ta bazu, ba ma a ƙasar Makidoniya da Akaya
kaɗai ba, har ma a ko'ina an san da bangaskiyarku ga Allah, ba
ma sai mun faɗa ba. 9 Don mutanen ne da kansu suke ba da labarin
yadda kuka karɓe mu, da kuma yadda kuka rabu da gumaka, kuka
juyo gun Allah, don ku bauta wa Allah na gaskiya kuma mai rai,
10 ku kuma jira dawowar Ɗansa daga sama. Allah ya ta da Ɗan
daga matattu, wato, Yesu wanda zai fitar da mu daga fushin nan
mai zuwa.

Hidimar Bulus a Tasalonika

2 1 Ai, 'yan'uwa, ku ma kun sani cewa zuwanmu wurinku bai
zama a banza ba. 2 Amma ko da yake mun riga mun sha wuya
da wulaƙanci a Filibi, kamar yadda kuka sani, Allahnmu ya
ƙarfafa mu don mu sanar muku Labarinsa Mai Daɗi, duk da
tsananin gāba da ake yi wa Labari Mai Daɗin nan. 3 Gama
gargaɗin da muke yi muku babu ƙarya a ciki, ko mugun nufi, ko
rudi. 4 Sai dai kamar yadda Allah ya yarda da mu ya ba mu aikin
wa'azin Labari Mai Daɗi, haka muke sanar da shi, ba don mu
faranta wa mutane rai ba, sai dai don mu faranta wa Allah, shi
da yake gwada zuciyarmu. 5 Kamar yadda kun sani, maganarmu
ba ta daɗin baki ba ne, kuma ba wai muna da halin kwaɗayin da
muke ɓoyewa ba. Allah kuwa shi ne shaidarmu. 6 Ba wai kuma
muna neman yabo daga wurin mutane, ko daga wurinku ko
waɗansu dabam ba, ko da yake, da muna so, da mun yi amfani
da ikon nan namu na manzannin Almasihu don mu nemi taimako.
7 Amma mun nuna halin saukinkai a cikinku, kamar yadda uwa
take lura da 'ya'yanta. 8 Domin mun damu da ku sosai, shi ne ya
sa ba mu yi muku wa'azin Labari Mai Daɗi na Allah kaɗai ba,
amma har mun ji daɗin ba da rayukanmu ma saboda ku, don kun
shiga ranmu sosai.

1.6: A. M. 17.5-9 **2.2:** A. M. 16.19-24; 17.1-9

9 'Yan'uwa, kun tuna da aiki da fama da muka sha! Mun yi
ta aiki dare da rana saboda kada mu sa wa kowane ɗayanku nauyi
sa'ad da muke yi muku wa'azin Labari Mai Daɗin da ya fito daga
wurin Allah. 10 Ku shaidu ne, Allah ma shaida ne game da irin
halin da muka nuna muku, ku masu bi, wato, halin tsarki, da
adalci, da na rashin abin zargi. 11 Kamar yadda kuka sani, mun
bi da kowane ɗayanku kamar yadda baba yake bi da 'ya'yansa.
12 Muka yi muku gargaɗi, muka ƙarfafa ku, muka roƙe ku ku yi
zaman da ya yi kyau a gaban Allah, shi wanda ya kira ku cikin
mulkinsa da ɗaukakarsa.

13 Saboda wannan ne kuma muke gode wa Allah kullum, don
sa'ad da kuka karɓi maganar Allah da kuka ji daga wurinmu, ba
ku karɓe ta kamar maganar mutum ce ba, sai dai ainihin yadda
take, wato, maganar Allah, wadda take aiki a zuciyarku, ku da
kuka gaskata. 14 Gama ku 'yan'uwa, kun yi koyi da jama'un masu
bin Allah cikin Almasihu Yesu, waɗanda suke a Yahudiya; domin
kun sha wahala daga mutanen ƙasarku, kamar yadda suka sha
daga hannun Yahudawa. 15 Yahudawa ne suka kashe Ubangiji
Yesu da annabawa, suka kuma kore mu. Suna ɓata wa Allah rai
sosai! Suna gāba da kowa! 16 Suna hana mu yin wa waɗanda ba
Yahudawa ba wa'azi don kada su sami ceto. Ta haka kullum suke
ƙara cika mudun zunubansu. Amma fa fushin Allah ya riga ya
sauka a kansu.

Niyyar Bulus Yă Sāke Ziyarci Tasalonikawa

17 To, 'yan'uwa, lokacin da aka raba mu da ku na ɗan lokaci,
wato, a rabuwa ta jiki ba ta zuciya ba, muna ta marmari, muna
ta ƙoƙari mu gan ku ido da ido. 18 Mun yi niyyar zuwa wurinku
ba shakka. Ni Bulus, na yi ƙoƙari in zo ba sau ɗaya ba, ba sau
biyu ba, amma Shaiɗan ya hana mu. 19 Gama mene ne abin sa
zuciyarmu, da abin farin cikinmu, da kuma abin taƙamarmu a
gaban Ubangiji Yesu a ranar dawowarsa, in ba ku ba? 20 Ai, ku
ne abin taƙamarmu, da abin farin cikinmu.

3 1 Saboda haka da muka kāsa daurewa, sai muka ga ya yi kyau
a bar mu a Atina mu kaɗai. 2 Mun aika Timoti ɗan'uwanmu,
wanda yake aiki tare da mu cikin hidimar Allah da kuma cikin
sha'anin Labari Mai Daɗi na Almasihu, yă kafa ku, yă kuma
ƙarfafa ku game da bangaskiyarku, 3 don kada tsananin nan yă sa
wani yă fid da zuciya. Ai, ku kanku kun sani cewa wannan shi

2.14: A. M. 17.5 **2.15**: A. M. 9.23,29; 13.45,50; 14.2,5,19; 17.5,13; 18.12
3.1: A. M. 17.15

ne abin da aka nufe mu da shi. 4 A gaskiya, sa'ad da muke tare
da ku mun gaya muku tun da wuri, cewa za mu sha wahala. Haka
kuwa ya zama, yadda kuka sani. 5 Saboda haka ne, da na kāsa
daurewa, sai na aika don in ji labarin bangaskiyarku. Ina tsoro
kada dai Mai ruɗin nan, wato, Shaiɗan ya riga ya ruɗe ku, kuma
aikinmu yă zama banza.

6 Amma ga shi yanzu da Timoti ya dawo daga wurinku ya
kawo mana labari mai daɗi game da bangaskiyarku da ƙaunarku.
Ya kuma gaya mana cewa kuna tunawa da mu da alheri kullum,
har kuna marmari ku gan mu yadda mu ma muke marmarin
ganinku. 7 Saboda haka, 'yan'uwa, cikin wahalarmu da
tsananinmu mun sami ƙarfafawa cikin zuciyarmu don
bangaskiyarku. 8 Yanzu kam, za mu ƙara rayuwa idan kuka ci
gaba da tsayawa sosai cikin Ubangiji. 9 Wace irin godiya za mu
yi wa Allah saboda ku, a kan yawan farin cikin da muke yi a
gaban Allahnmu dominku? 10 Dare da rana muna dagewa cikin
addu'a sosai domin mu samu mu gan ku ido da ido, mu kuma
cika abin da ya kāsa a cikin bangaskiyarku.

11 Bari Allah da kansa wanda yake Ubanmu, da kuma
Ubangijinmu Yesu, yă shirya mana hanyar zuwa wurinku. 12 Ku
kuma, Ubangiji yă sa ku ƙaru ku kuma yalwata da ƙaunar junanku
da dukan mutane, kamar yadda muke yi muku. 13 Bari yă ƙarfafa
zuciyarku cikin tsarki, ku zama marasa abin zargi a gaban Allah
wanda yake Ubanmu, a ranar da Ubangijinmu Yesu zai dawo tare
da dukan tsarkakansa.

Irin Rayuwar da Allah Yake So

4 1 A ƙarshe kuma, 'yan'uwa, muna roƙonku, muna kuma yi
muku gargaɗi saboda Ubangiji Yesu cewa, ku yi rayuwa
wadda Allah yake jin daɗinta, kamar yadda muka koya muku. Ko
da yake kuna yi irin rayuwan nan, sai ku ƙara ƙoƙari sosai. 2 Gama
kun san umarnin da muka ba ku ta wurin iznin Ubangiji Yesu.
3 Domin wannan shi ne nufin Allah, wato, ku yi rayuwa mai tsarki,
ku guje wa halin lalata. 4 Kowa yă san yadda zai bi da jikinsa[a]
cikin tsarki da mutunci, 5 ba ta muguwar sha'awa ba yadda
waɗanda ba Yahudawa ba suke yi, waɗanda ba su san Allah ba.
6 Kada wani yă cuci ɗan'uwansa ko yă ɓata masa rai a wannan
sha'anin, gama Ubangiji zai hukunta dukan waɗannan abubuwa,

3.6: A. M. 18.5

[a] **4.4 bi da jikinsa:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "auro wa kansa mace".

kamar yadda muka gaya muku tun da farko, muka kuma yi muku gargaɗi. 7 Allah bai kira mu domin mu yi zama marar tsarki ba, sai dai na tsarki. 8 Saboda haka duk wanda ya ƙi yarda da wannan koyarwar, ba mutum ya ƙi ba, Allah ne ya ƙi, shi da yake ba ku Ruhunsa Mai Tsarki.

9 Game da ƙaunar 'yan'uwa kuwa, ba sai wani ya rubuta muku ba, don ku da kanku Allah ya koya muku cewa ku ƙaunaci juna. 10 Hakika kuwa, kuna ƙaunar dukan 'yan'uwa a duk ƙasar Makidoniya. Sai dai muna so ku ƙara yin haka sosai, 'yan'uwa. 11 Ku yi ƙoƙari ku yi zaman natsuwa, ku kula da ayyukan da suke gabanku kawai, kuna kuma aiki da hannayenku yadda muka ce ku yi. 12 Ta haka za ku zama masu mutunci ga waɗanda ba masu bi ba, kuma ba za ku dogara a kan kowa ba.

Dawowar Ubangiji

13 Amma 'yan'uwa, ba ma so ku yi zama da rashin sani game da waɗanda suka yi barci, wato, sun mutu, don kada ku yi baƙin ciki kamar sauran mutane waɗanda ba su da abin sa zuciya. 14 Tun da muka gaskata Yesu ya mutu, ya kuwa tashi, haka kuma ta wurin Yesu, Allah zai dawo da waɗanda suka yi barci, tare da Yesu.

15 Muna kuwa shaida muku bisa ga maganar Ubangiji cewa, mu da za mu kasance da rai a lokacin da Ubangiji zai dawo, ba za mu riga waɗanda suka yi barci tashi ba, ko kaɗan. 16 Gama Ubangiji da kansa ma zai sauko daga sama, da kira mai ƙarfi, da muryar babban mala'ika, da kuma busar ƙahon Allah. Waɗanda suka mutu cikin Almasihu, su ne za su fara tashi. 17 Sa'an nan mu da za mu kasance da rai a lokacin, za a ɗauke mu tare da su a cikin girgije, domin mu sadu da Ubangiji a sararin sama. Za mu kuma kasance tare da Ubangiji har abada. 18 Saboda haka sai ku yi wa juna ta'aziyya da wannan maganar.

Ku Zauna da Shiri don Zuwan Ubangiji

5 1 To, 'yan'uwa, game da lokaci ko ranar da waɗannan abubuwan za su faru, ba sai an rubuta muku ba. 2 Gama ku ma kun sani sosai cewa Ranar Ubangiji za ta zo kamar zuwan ɓarawo da dare. 3 Lokacin da mutane suke cewa, "Muna zaman lafiya da salama" sai kawai halaka ta auko musu, kamar yadda naƙuda[b] take kama mace mai ciki, ba kuwa hanyar tsira. 4 Amma, ai, ba a cikin duhu kuke ba, 'yan'uwa, har da Ranan nan za ta

4.15-17: 1 Kor 15.51-52 **5.2**: Mat 24.43; Luk 12.39; 2 Bit 3.10

[b] **5.3 naƙuda**: Wato, zafin da mace takan ji lokacin haihuwa.

same ku kamar ɓarawo. 5 Domin ku duka mutanen haske ne, na
rana kuma. Mu ba na dare ko duhu ba ne. 6 Saboda haka kada
mu yi barci yadda waɗansu suke yi, sai dai mu zauna cikin shiri
da natsuwa. 7 Gama waɗanda suke barci da dare suke yi, waɗanda
suke buguwa kuwa da dare suke yi. 8 Amma tun da mu na rana
ne, sai mu natsu, mu sa rigar ƙarfen bangaskiya da ƙauna. Sa
zuciya ga samun ceto kuma yă zama hular kwanonmu. 9 Allah
bai nufe mu da fushinsa ba, sai dai ga samun ceto ta wurin
Ubangijinmu Yesu Almasihu, 10 wanda ya mutu saboda mu,
domin ko muna da rai, ko mun yi barci, mu zama muna tare da
shi. 11 Saboda haka sai ku ƙarfafa juna, ku rika gina juna, kamar
yadda kuke yi yanzu.

Gargaɗi da Gaisuwa

12 Amma muna roƙonku, 'yan'uwa, ku ba wa masu fama da
aiki a cikinku girma, wato, shugabanninku cikin Ubangiji, masu
yi muku gargaɗi. 13 Ku rike su da mutunci sosai da ƙauna saboda
aikinsu. Ku yi zaman lafiya da juna.

14 Muna kuma roƙonku, 'yan'uwa, ku yi wa masu ƙyuyan nan
faɗa, ku ƙarfafa waɗanda ba su da ƙarfin zuciya, ku taimaki
marasa ƙarfi, ku yi haƙuri da kowa. 15 Ku kula fa kada kowa yă
rama mugunta da mugunta, sai dai kullum ku yi ƙoƙarin yin abin
kirki wa junanku da sauran mutane kuma.

16 Ku rika farin ciki kullum. 17 Ku rika yin addu'a ba fasawa.
18 A cikin kowane hali ku gode wa Allah, domin wannan shi ne
nufin Allah zuwa gare ku a cikin Almasihu Yesu.

19 Kada ku danne Ruhu Mai Tsarki. 20 Kada ku rena annabci,
21 sai dai ku gwada kome, ku rike abin da yake da kyau. 22 Ku
guje wa kowace irin mugunta.

23 Bari Allah da kansa, mai salama, yă tsarkake ku gaba ɗaya,
yă kuma kiyaye ruhunku, da ranku, da jikinku duka, ku kasance
marasa laifi a ranar da Ubangijinmu Yesu Almasihu zai dawo.
24 Shi wanda ya kira ku mai aminci ne, zai kuwa aikata.

25 'Yan'uwa, ku yi mana addu'a.

26 Ku gai da dukan 'yan'uwa da gaisuwar ƙauna.

27 Na roƙe ku cikin sunan Ubangiji, ku karanta wa dukan
'yan'uwa wasiƙan nan.

28 Alherin Ubangijinmu Yesu Almasihu yă kasance tare da
ku.

5.8: Ish 59.17; Afi 6.13-17

WASIKAR BULUS TA BIYU ZUWA GA
TASALONIKAWA

Gabatarwa

Manzo Bulus ya rubuta wannan wasika a shekara ta A.D. 51-52 a Korinti ba da dadewa ba bayan da aka rubuta wasika ta fari zuwa ga Tasalonikawa.

An rubuta wannan *Wasika ta Biyu zuwa ga Tasalonikawa* domin har yanzu akwai damuwa a cikin jama'ar masu bi. Har yanzu kam koyarwar karyan nan game da dawowar Yesu tana rikitar da hankalin masu bi. Bulus ya yi wa mutanen da suka ce wai Yesu ya riga ya dawo gyara a kan cewa Yesu ba zai dawo ba sai wadansu abubuwa sun faru tukuna. Mugunta za ta yi yawa har ta kai yadda ba a taba yin irinta ba karkashin "sarkin tawayen nan". Wasikar ta gaya wa masu bi kada su yarda wani yă rude su da koyarwar karya game da wannan batu.

Wasikar ta kuma gargadi jama'ar Allah su ci gaba da tsayawa da karfi sosai cikin bangaskiyarsu ko da yake akwai wahala da tsanani. A karshe ta kuma ja musu kunne kada su zama masu kyuya, amma su yi aiki don ciyar da kansu.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-2
Koyarwa game da dawowar Yesu 1.3—2.12
Yin zaman aminci 2.13-17
Gargadi a kan kyuya 3.1-15
Addu'ar karshe 3.16-18

Gaisuwa

1 [1] Daga Bulus da Sila, da Timoti, zuwa ga jama'ar masu bi a Tasalonika wadda take ta Allah Ubanmu da Ubangiji Yesu Almasihu.

2 Alheri da salama daga Allah Uba da Ubangiji Yesu Almasihu su kasance tare da ku.

Almasihu Zai Dawo Yă Yi Shari'a

3 Dole ne kullum mu gode wa Allah saboda ku, 'yan'uwa, haka kuwa ya yi kyau, da yake bangaskiyarku tana kara girma sosai, har ma kaunar kowane dayanku ga juna tana ta karuwa.

1.1: A. M. 17.1

4 Don haka mu kanmu muke taƙama da ku a cikin jama'un masu
bin Allah, saboda jimrewarku, da bangaskiyarku cikin yawan
tsanani, da wahalar da kuke ciki.
5 Duka wannan ya nuna cewa shari'ar Allah mai adalci ce,
wannan kuma ya tabbatar cewa kun isa zama a mulkin Allah don
a kan mulkin ne kuke shan wahala. 6 Allah mai adalci ne, saboda
haka su waɗanda suke ba ku wahala zai saka musu da wahala,
7 amma ku da kuke shan wahala kuwa zai hutar da ku, har ma da
mu. Wannan zai faru a ranar da Ubangiji Yesu zai bayyana daga
sama tare da manyan mala'ikunsa 8 a cikin harsunan wuta, zai
hukunta waɗanda suka ƙi sanin Allah, da kuma waɗanda suka ƙi
biyayya da Labari Mai Daɗi na Ubangijinmu Yesu. 9 Za su sha
hukuncin halaka ta har abada, za a kau da su daga gaban Ubangiji
da kuma ɗaukakar ikonsa. 10 A wannan lokacin da zai dawo kuwa,
tsarkakansa za su ɗaukaka shi, dukan masu bi kuma za su yi
mamakinsa a Ranan nan tare da ku, don kun gaskata da shaidar
da muka yi.
11 Saboda wannan ne kullum muke yi muku addu'a cewa
Allahnmu yă sa ku cancanci kiransa, yă sa ku iya yin duk
abubuwa masu kyau da kuke fata za ku yi, da aikin bangaskiya
da ƙarfin ikonsa. 12 Ta haka za a ɗaukaka sunan Ubangijinmu
Yesu a cikinku, ku kuma a cikinsa, bisa ga alherin Allahnmu, da
Ubangiji Yesu Almasihu.

Sarkin Tawaye

2 1 To, 'yan'uwa, game da dawowar Ubangijinmu Yesu
Almasihu da kuma yadda za a tattara mu zuwa gare shi, muna
roƙonku 2 kada ku jijjigu da sauri a zuciyarku, ko kuwa
hankalinku yă tashi a kan cewa Ranar Ubangiji ta riga ta zo. Mai
yiwuwa wani yana iya faɗa haka a cikin magana ta ruhu, ko a
jawabi, ko a wasiƙa a kan cewa daga wurinmu yake. 3 Kada kowa
yă ruɗe ku ko ta yaya, domin wannan ranar ba za ta zo ba sai an
yi tawayen nan, sarkin tawaye[a] kuma yă bayyana, wato, wanda
aka shirya masa halaka. 4 Shi ne magabci, yana ɗaukaka kansa
gāba da duk abin da ya shafi sunan Allah, ko kuma wanda ake
yi wa sujada. Har ma yakan zauna a haikalin Allah, yana cewa
wai shi ne Allah.

1.9: Ish 2.10 **2.1**: 1 Tas 4.15-17 **2.4**: Dan 11.36; Ez 28.2

[a] **2.3 sarkin tawaye:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "mai zunubi" ne a nan. Sarkin tawaye ba Shaiɗan ne ake nufi a nan ba, amma wani ne da zai tashi yă zama shugaban ikoki na mugu a kwanakin ƙarshe.

5 Ashe, ba ku tuna ba, nakan gaya muku waɗannan
abubuwan tun ina tare da ku? 6 To, yanzu dai kun san abin da
yake hana shi zuwa; don kada yă bayyana kafin lokacinsa.
7 Gama ikon tawayen nan ya riga ya fara aiki a ɓoye, amma shi
wanda yake hanawa zai ci gaba da hanawa har sai Allah ya
kawar da shi. 8 Sa'an nan ne fa za a bayyana sarkin tawayen
nan, amma a dawowar Ubangiji Yesu kuwa, Yesu zai kashe shi
da numfashin bakinsa, yă kuma halaka shi da ɗaukakar
bayyanarsa. 9 Za a gane zuwan sarkin tawayen nan ta wurin
ayyuka da kuma ikon Shaiɗan, zai aikata abubuwan ban
mamaki, da alamu, da aikin sihiri na ƙarya iri-iri, 10 yana mugun
ruɗin waɗanda suke hanyar halaka, domin sun ƙi ƙaunar gaskiya
har yadda za su sami ceto. 11 Saboda haka Allah zai aiko musu
da babban ruɗu don su gaskata ƙarya, 12 don a hukunta duk
waɗanda suka ƙi gaskata gaskiya, suke kuma jin daɗin mugunta.

Yin Zaman Aminci

13 Amma dole ne kullum mu gode wa Allah saboda ku,
'yan'uwa waɗanda Ubangiji yake ƙauna, domin Allah ya zaɓe ku
ku fara samun ceto ta wurin tsarkakewar Ruhu, da kuma
gaskatawa da gaskiya. 14 Saboda wannan dalilin ne ya kira ku ta
wurin Labari Mai Daɗin nan da muka ba ku, domin ku sami
ɗaukakar Ubangijinmu Yesu Almasihu. 15 Saboda haka,
'yan'uwa, sai ku dage, ku kuma riƙe ƙa'idodin nan da muka koya
muku, ko ta magana, ko ta wasiƙa.

16 To, Ubangijinmu Yesu Almasihu da kansa, da kuma Allah
Ubanmu, wanda ya ƙaunace mu, ya kuma ba mu ta'aziyya marar
ƙarewa, da bege mai kyau ta wurin alherinsa, 17 yă yi muku
ta'aziyya, yă kuma ƙarfafa ku cikin kowane aiki da magana mai
kyau.

A Yi Addu'a Dominmu

3 1 A ƙarshe, 'yan'uwa, ku yi mana addu'a don maganar
Ubangiji ta yaɗu da sauri, ta sami ɗaukaka kamar yadda ta
samu a cikinku. 2 Ku kuma yi addu'a don a cece mu daga
mugayen mutane masu mugunta, don ba duka suka ba da
gaskiya ba.

3 Amma Ubangiji mai aminci ne, zai ƙarfafa ku, yă tsare ku
daga Mugun nan, wato, Shaiɗan. 4 Mun amince da Ubangiji game

2.8: Ish 11.4 **2.9:** Mat 24.24

da ku cewa, kuna bin umarnin da muka yi muku, za ku kuma ci gaba da bi.

5 Ubangiji yă mai da hankalinku kan ƙaunan nan ta Allah, da kuma tsayawa da ƙarfi na Almasihu.

Lallai Ne A Yi Aiki

6 To, 'yan'uwa, muna ba ku umarni cikin sunan Ubangijinmu Yesu Almasihu, ku ƙita hanyar duk wani ɗan'uwan da yana ƙin yin aiki, wanda ba ya bin ƙa'idodin da kuka samu a wurinmu. 7 Ai, ku ma kun san ya kamata ku yi koyi da mu, don lokacin da muke tare da ku, ba mu nuna muku rashin son yin aiki ba, 8 kuma ba mu kuwa ci abinci kyauta a hannun kowa ba. Sai dai mun sha fama da wahala, muna aiki dare da rana, don kada mu sa wa ko ɗayanku nauyi. 9 Ba wai don ba hakkinmu ba ne, a'a, sai dai don mu zama abin misali a gare ku kawai, don ku yi koyi da mu. 10 Ai, ko dā da muke tare da ku, mun ba ku umarni cewa duk wanda ya ƙi yin aiki, kada a ba shi abinci.

11 Gama mun ji labari cewa waɗansunku masu ƙyuya ne, ba sa aikin kome, sai shige-shige kawai. 12 To, irin waɗannan mutanen muna ba su umarni, muna kuma yi musu gargaɗi cikin Ubangiji Yesu Almasihu, su riƙa yin aiki da natsuwa, suna ciyar da kansu.

13 'Yan'uwa, kada ku gaji da yin abin da yake daidai. 14 Idan wani ya ƙi biyayya da abin da muka faɗa a cikin wasiƙan nan, sai ku lura da shi, ku guje masa don yă ji kunya. 15 Amma kada ku ɗauke shi kamar abokin gāba, sai dai ku gargaɗe shi kamar ɗan'uwa.

Maganar Karshe

16 To, Ubangiji mai salama, shi da kansa yă ba ku salama a kowane lokaci, a kowane hali. Ubangiji yă kasance tare da ku duka.

WASIKAR BULUS TA FARKO ZUWA GA
TIMOTI

Gabatarwa

Manzo Bulus ne ya rubuta wannan *Wasiƙa zuwa ga Timoti* wanda shi Bulus ya yi renonsa cikin hanyar Ubangiji. Ana zato an rubuta wasiƙan nan tsakanin shekara ta A.D. 65-67 a yankin Makidoniya.

Bulus ya bar Timoti a Afisa, don yă zauna a wurin yă ƙarfafa masu bi da koyarwa ta gaskiya saboda kada a rude su da muguwar koyarwa. Bulus ya rubuta wannan wasiƙa domin yă gargaɗi Timoti yadda zai bi da aiki a wurin.

Wasiƙar ta fara da gargaɗi game da koyarwar ƙarya wadda ta sha bamban da koyarwa ta gaskiyar da Bulus ya yi. Ta kuma ba da umarni game da yadda za a yi sujada da yadda za a yi shugabancin jama'ar masu bi da kuma halayen da shugabanni sun kamata su kasance da su. A ƙarshe an ba Timoti shawara game da yadda zai zama mai hidima nagari na Almasihu da kuma aikin da yake da shi ga mutane iri dabam-dabam.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-2
Gargaɗi game da jama'ar masu bi da ma'aikatanta 1.3—3.16
Gargaɗi ga Timoti a kan aikinsa 4.1—6.21

Gaisuwa

1 [1] Daga Bulus manzon Almasihu Yesu bisa ga umarnin Allah
Mai Cetonmu da Almasihu Yesu wanda shi ne abin sa
zuciyarmu, [2] zuwa ga Timoti ɗana na gaske cikin bangaskiya.
Alheri da jinƙai da salama daga Allah Uba da Almasihu Yesu
Ubangijinmu su kasance tare da kai.

Gargaɗi game da Koyarwar Karya

3 Ina so ka ɗan zauna a Afisa, kamar yadda na roƙe ka a lokacin
da nake a hanyata zuwa Makidoniya, don akwai waɗansu mutanen
da suke koyarwar ƙarya, ka gargaɗe su su daina. [4] Ka faɗa musu
cewa kada su ba da hankalinsu ga tatsuniyoyi da bin lissafin sunayen
kakanni waɗanda ma ba su da iyaka. Domin irin wannan yana kawo

---

1.2: A. M. 16.1

gardama ne kawai, a maimakon ɗaukaka shirin Allah wanda ake
sani ta wurin bangaskiya. 5 Manufar wannan umarnin ita ce ƙauna,
wadda take fitowa daga zuciya mai tsabta, da tunanin da yake
tabbatar mana ba mu da laifi, da kuma bangaskiya ta ƙwarai.
6 Waɗansu mutane sun riga sun kauce daga bin waɗannan
abubuwan, har suka ɓace, suka shiga bin maganganun banza.
7 Mutanen suna son zaman masu koyar da Dokar Allah, ga shi kuwa
ba su da ganewar abubuwan da suke faɗa, balle abubuwan da suke
ta nacewa a kansu.

8 Mun san cewa Dokar tana da kyau idan aka yi amfani da ita
a hanyar da ta dace. 9 Mun kuma san cewa, ba don marasa laifi
akan bayar da dokoki ba, sai dai don masu ƙin ji da marasa biyayya,
da marasa hali irin na Allah, da masu zunubi, da marasa tsarki, da
masu zargin Allah, da masu kashe babansu, ko mamansu, da masu
kisankai, 10 da masu zina, da maza masu kwana da maza, ko mata
masu kwana da mata, da masu satan mutane, da masu ƙarya, da
masu shaidar ƙarya, da kuma duk abin da yake dabam da koyarwa
ta gaskiya. 11 Wannan koyarwa tana bisa ga bisharan nan mai daraja
ta Allah, mai albarka wadda aka sa mini a hannu in yi shelarta.

Godiya don Jinƙan Allah

12 Ina gode wa Almasihu Yesu Ubangijinmu, wanda ya ƙarfafa
ni don aikina. Ya bincike ni ya kuma amince da ni har ya kira ni
zuwa ga aikinsa, 13 ko da yake a dā ni mai zargin Allah ne, mai
tsananta masa, kuma mai wulaƙanta shi. Amma duk da haka na
sami jinƙai don duk abin da na aikata na yi ne cikin rashin sani da
rashin bangaskiya. 14 Alherin Ubangijinmu ya cika ni sosai ya kuma
ba ni bangaskiya da ƙaunar da suke cikin Almasihu Yesu.
15 Maganan nan tabbatacciya ce, kuma ta isa a karɓe ta gaba ɗaya
cewa, "Almasihu Yesu ya zo duniya domin ceton masu zunubi," a
cikinsu duka ni ne na fi zunubi. 16 Amma Allah ya yi mini jinƙai
musamman don ta kaina, ni da na fi su zunubi, Almasihu Yesu yă
nuna cikakken haƙurinsa in zama misali ga duk waɗanda nan gaba
za su gaskata da shi su kuma sami rai na har abada. 17 Bari girma
da ɗaukaka su tabbata har abada abadin ga wanda yake sarkin
zamanai, wanda ba shi da ƙarshe, wanda ba a ganinsa, kuma shi ne
kaɗai Allah! Amin.

18 Timoti, ɗana, ina ba ka wannan umarni ne bisa ga
annabce-annabcen da aka yi tun dā a kanka. Domin ta wurin

1.13: A. M. 8.3; 9.4-5

kiyaye waɗannan umarnan za ka iya yin yaƙi, ka kuma yi shi da
kyau sosai, 19 kana riƙe da bangaskiya da tunanin da yake tabbatar
maka ba ka da laifi. Waɗansu mutane sun kashe bangaskiyarsu
ta dalilin ƙin bin abin da tunaninsu suke gaya musu. 20 A cikinsu
akwai Himeniyus da Alekzanda, waɗanda na miƙa wa Shaiɗan
don suyi koyi su daina maganar reni ga Allah.

Gargaɗi a kan Sujada

2 1 Da fari dai, ina ƙarfafa cewa a yi ta roƙo, ana addu'a, ana
roƙe-roƙe, ana godiya ga Allah saboda dukan mutane. 2 A yi
haka saboda dukan sarakuna da dukan waɗanda suke da manyan
matsayi, don mu zauna lafiya da kwanciyar rai cikin tsoron Allah
sosai da kuma yin rayuwa mai kyau ta kowace hanya. 3 Wannan
yana da kyau, kuma Allahn da yake Mai Cetonmu yana jin daɗin
haka sosai, 4 shi wanda yake so dukan mutane su sami ceto, su
kuma kai ga sanin gaskiya. 5 Gama Allah ɗaya ne, wanda yake
tsakanin Allah da mutane kuwa ɗaya ne, wato, mutumin nan
Almasihu Yesu. 6 Shi ne ya ba da kansa domin yă fanshi mutane
duka. Wannan ne shaidar da aka bayar a daidai lokaci. 7 Saboda
wannan ne aka naɗa ni manzo da kuma mai wa'azi. Na zama
malami mai koya wa dukan waɗanda ba Yahudawa ba saƙon nan
cikin bangaskiya da gaskiya. Gaskiya nake faɗa ba ƙarya ba.

8 Ina so a ko'ina, maza su ɗaga hannaye masu tsarki cikin
addu'a ba tare da fushi ko gardama ba. 9 Biye da wannan, ina
so mata su lura su yi wa kansu adon da ya cancanta, da rigunan
da suka dace, ban da yawan adon kai, ko kayan zinariya, ko
lu'ulu'ai, ko riguna masu tsada, 10 sai dai da ayyuka masu kyau
waɗanda sun dace da matan da suke bayyana cewa su masu
tsoron Allah ne. 11 Bari mace ta karɓi koyarwa cikin kwaciyar
hankali da cikakken ladabi. 12 Ban ba mace izni ta yi koyarwa
ba. Ban kuma ba ta izni ta yi mulki a kan maza ba, sai dai ta
zauna shiru. 13 Domin Adamu ne aka fara halitta kafin
Hawwa'u. 14 Ba Adamu ne kuma aka yi masa ruɗu ba, amma
dai macen ce aka ruɗe ta har ta zama mai zunubi. 15 Duk da
haka dai mace za ta sami ceto ta wurin haihuwar 'ya'ya,[a] idan
ta ci gaba[b] cikin bangaskiya da ƙauna da tsarki, tare da natsuwa.

2.7: 2 Tim 1.11 **2.9:** 1 Bit 3.3 **2.13:** Far 2.7,21-22 **2.14:** Far 3.1-6

[a] **2.15 Za ta sami ceto ta wurin haihuwa 'ya'ya:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "Za ta tsira ta wurin haihuwa".

[b] **2.15 Idan ta ci gaba:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "Idan sun ci gaba".

Irin Mutumin da Ya Cancanci Zaman Shugaban Jama'ar Masu Bi

3 [1] Maganan nan tabbatacciya ce cewa, duk wanda yake
marmarin zaman shugaban jama'ar masu bi, yana marmarin
aiki mai kyau ne. [2] Shugaba yă kasance marar laifi a gaban
mutane, yă kasance mai mata ɗaya,[6] mai kame kansa, mai halin
natsuwa, mai bi da kansa da kyau, mai karɓan baki, mai iya
koyarwa sosai, [3] wanda ba mashayi ba, ba mai rikici ba amma
mai hankali, ba mai faɗa ba, kuma ba mai yawan son kudi ba.
[4] Lallai ne yă kasance wanda ya iya bi da iyalinsa da kyau, yana
sa yaransa su zama masu biyayya da bangirma gare shi ta kowace
hanya. [5] Gama in har wani bai san yadda zai bi da iyalinsa ba,
to, yaya zai iya lura da jama'ar masu bin Allah? [6] Kada yă zama
sabon tuba, in ba haka ba girman kai zai sa har yă shiga cikin
irin hukuncin da aka yi wa Shaiɗan. [7] Shugaba yă kasance wanda
yake da shaida mai kyau a gaban mutanen da ba masu bi ba, don
kada yă zama abin kunya, yă fāɗi cikin tarkon Shaiɗan.

8 Haka ma masu hidima a cikin jama'ar masu bi, dole ne su
kasance masu hankali, ba masu baki-biyu a magana ba, ba kuma
masu yawan shan ruwan inabi ko masu kwaɗayin kudi ba. [9] Dole
ne su kuma riƙe asirin bangaskiya da tunanin da yake tabbatar
musu ba su da laifi. [10] Waɗannan masu hidimar kuma sai an fara
gwada su, sa'an nan, idan an tabbatar ba su da laifi, to, sai su
kama aiki na hidima. [11] Haka ma mata su zama masu hankali,
ba masu gulma ba, amma waɗanda suka kame kansu, suna
aminci cikin kome.

12 Mai hidima a cikin jama'ar masu bi yă kasance da mace
guda, yana kuma koyar da yaransa da sauran iyalinsa sosai.
[13] Waɗanda suke hidima mai kyau a cikin jama'ar masu bi sukan
samo wa kansu suna mai kyau suna magana gabagadi game da
bangaskiyarsu cikin Almasihu Yesu.

Asirin Addininmu

14 A sa'ad da nake rubuta wannan umarni zuwa gare ka, ina
sa zuciya zan zo wurinka ba da jimawa ba. [15] Amma idan an ci
mini lokaci, sai ka kasance da sani yadda ya kamata mu bi da
kanmu a cikin gidan Allah, wanda yake jama'ar masu bin Allah

3.2-7: Tit 1.6-9

[6] **3.2 yā kasance mai mata ɗaya:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "Wanda ya yi aure sau ɗaya kawai". Dubi Titus 6.9.

mai rai, wanda yake ginshiki da kuma tushen gaskiya. 16 Ba da
wata shakka ba, asirin addininmu da zurfi yake:
An bayyana shi[c] cikin jiki,
Ruhu ya nuna shi mai gaskiya ne[d]
Mala'iku suka gan shi, aka yi shelarsa ga al'ummai,
an ba da gaskiya gare shi cikin duniya duka,
an ɗauke shi sama cikin ɗaukaka.

Koyarwar Karya

4 1 To, Ruhu ya bayyana a sarari cewa a kwanakin ƙarshe
waɗansu za su yar da bangaskiyarsu ta masu bi su mai da
hankali ga ruhohi masu ruɗu da koyarwar ƙarya ta aljanu.
2 Koyarwan nan za ta taso ta wurin munafuncin masu ƙarya
waɗanda tunaninsu ya mutu sarai. 3 Irin mutanen nan suna hana
yin aure da kuma cin waɗansu abinci. Ga shi kuwa Allah ne ya
halicci abincin domin waɗanda sun ba da gaskiya suna kuma sane
da gaskiyar su karɓa da godiya. 4 Gama duk abin da Allah ya
halitta yana da kyau, kuma kada a ƙi kome in dai an karɓe shi
cikin godiya, 5 gama an tsarkake shi ta wurin maganar Allah da
addu'a.

Mai Hidima Mai Kyau na Almasihu Yesu

6 Idan ka koyar da 'yan'uwa waɗannan abubuwa za ka zama
mai hidima mai kyau na Almasihu Yesu, wanda ya yi girma a
cikin maganan nan ta bangaskiya da kuma koyarwan nan mai
kyau wanda kake bi har wa yau. 7 Ka yi nesa da tatsuniyoyin
banza marasa amfani. Ka hori kanka ka kasance da hali irin na
Allah. 8 Ko da yake horon jiki yana da ɗan amfani, amma dai
kasancewa da hali irin na Allah ya ƙi amfani ta kowace hanya,
don yana jawo albarka ga rayuwan nan ta yanzu da kuma
rayuwa mai zuwa. 9 Wannan magana tabbatacciya ce, kuma ta
isa a karɓe ta ɗungum. 10 Muna fama[d'] da aiki, don mun sa
zuciyarmu ga Allah mai rai wanda yake Mai Ceton kowa,
musamman ga waɗanda suka ba da gaskiya.
11 Ka umarta ka kuma koyar da waɗannan abubuwa. 12 Kada
ka bar wani yă rena ƙuruciyarka, amma ka zama abin koyi ga

[c] **3.16 An bayyana shi**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "An bayyana Allah", waɗansu kuma "Wanda aka bayyana" ne a nan.

[d] **3.16 Ruhu ya nuna shi mai gaskiya ne**: Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne, "A cikin Ruhu an nuna shi mai gaskiya ne".

[d'] **4.10 muna fama**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Muke shan wulaƙanci" ne a nan.

sauran masu bi, cikin magana, da rayuwa, da ƙauna, da bangaskiya, da kuma tsabtar rai. 13 Kafin in zo, ka ci gaba da karanta Rubutaccen Maganar Allah wa jama'a, da wa'azi, da kuma koyarwa. 14 Kada ka ƙyale wannan baiwar da take cikinka, wadda aka ba ka ta wurin annabci lokacin da majalisar dattibai suka sa maka hannun albarka. 15 Ka aikata waɗanna abubuwa cikin aiki, ka miƙa kanka ɗungum gare su, don kowa yă ga cin gabanka. 16 Ka lura sosai da kanka da kuma koyarwarka. Ka ci gaba da yin waɗannan abubuwa, don in ka yi haka za ka ceci kanka da kuma masu jinka.

Koyarwa game da Gwauraye, Dattibai da Bayi

5 1 Kada ka tsawata wa tsoho, amma ka yi masa magana kamar shi baba ne a gare ka. Samari kuma ka yi musu magana kamar 'yan'uwa, 2 tsofaffin mata kuma kamar uwaye, sa'an nan 'yan mata kamar 'yan'uwa, da matuƙar tsabtar rai.

3 Ka ba da girma ga matan da mazansu suka mutu, waɗanda a gaskiya ba su da kowa. 4 Idan mace da mijinta ya mutu tana da 'ya'ya ko jikoki, to, sai su fara koyon yin ayyukan addininsu ga danginsu, don ta haka su ma za su mayar wa iyayensu taimakon da suka samu daga gare su. Gama Allah yana jin daɗin wannan. 5 Mace wadda mijinta ya mutu, wadda ba ta da kowa da zai taimake ta, za ta sa zuciyarta ga Allah ke nan, tana roƙo da addu'o'i dare da rana zuwa gare shi don taimako. 6 Amma mace wadda mijinta ya mutu, wadda kuma take rayuwar son jin daɗin kanta kawai, ta riga ta mutu ko da yake a raye take. 7 Ka ba su waɗannan umarnai don su kasance waɗanda ba su da abin zargi a gaban mutane. 8 Duk wanda ba ya kula da danginsa, musamman iyalin gidansa, ya ƙaryata bangaskiyarsa ke nan kuma ya fi wanda yake marar ba da gaskiya muni.

9 Mace da mijinta ya mutu ba ta isa a ƙirga ta ɗaya daga cikin matan da mazansu suka mutu ba, sai dai shekarunta sun kai sittin, kuma lokacin da mijin yake da rai ta kasance mace mai aminci gare shi.[e] 10 Ta kuma kasance wadda aka san ayyukanta masu kyau ne. Wato, ta zama wadda ta yi renon 'ya'yanta da kyau, tana karɓan baƙi, tana yi wa masu bi hidima, tana taimakon waɗanda suke cikin damuwa, kuma ta kowace hanya tana miƙa kanta ga yin abubuwan kirki.

[e] **5.9 ta kasance mai aminci:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne, "Ta kasance mai miji ɗaya."

11 Amma kada ka sa mata masu ƙuruciya da mazansu suka
mutu cikin wannan lissafi, domin sa'ad da sha'awar jikinsu ta
raba hankalinsu daga Almasihu sukan so su yi aure. 12 Ta haka
suna jawo wa kansu hukunci, don sun ƙarye alkawarinsu na fari.
13 Ban da haka ma, sukan koyi zaman banza, suna shige-shigen
gidajen mutane. Ba ma zaman banza suke yi kawai ba, amma
har da gulma ma, suna kai da kawowa suna maganganu da ba
su kamata ba. 14 Na fi so mata masu ƙuruciyar da mazansu suka
mutu su yi aure, su haifi 'ya'ya, su bi da sha'anin gidajensu,
don kada a ba abokan gābanmu damar yin mugayen maganganu
a kanmu. 15 Gama waɗansu sun riga sun juye suna bin Shaiɗan.
16 Idan akwai mace mai bi wadda cikin danginsu akwai matan
da mazansu suka mutu, to, sai ta taimake su, kada a sa wa
jama'ar masu bi nauyi. Ta haka jama'ar masu bi za ta sami
damar taimakon ainihin waɗanda mazansu suka mutu, kuma da
ba su da kowa.

17 A ba da girma ga dattiban da suna hidimarsu yadda ya
kamata, musamman waɗanda suke fama cikin wa'azi da koyarwa.
18 Gama Rubutaccen Maganar Allah ya ce, "Ba za a rufe bakin
bijimi sa'ad da yake sussuka ba", da kuma "Mai aiki ya cancanci
ladansa". 19 Kada ka yarda da wata ƙara da an kawo a kan wani
dattijon jama'ar masu bi sai da shaidu biyu ko uku. 20 Game da
waɗanda suke cikin zunubi, ka tsawata musu a gaban jama'a, don
sauran su ji tsoro. 21 A gaban Allah da Almasihu Yesu da kuma
mala'ikun da aka zaɓa, ina maka gargaɗi ka bi waɗannan umarnai
ban da sonkai ko nuna cewa ka fi son wani fiye da sauran. 22 Kada
ka yi saurin sa wa wani hannun albarka, kuma kada ka sa kanka
a zunubi na waɗansu. Amma ka keɓe kanka da tsarki.

23 Kada ka dinga shan ruwa kaɗai, amma ka sha ruwan inabi
mai tsami kaɗan saboda ciwon cikinka da kuma yawan rashin
lafiyarka. 24 Zunuban waɗansu mutane suna nan a fili, kuma
zunubansu sukan riga bayyana kafin a hukunta su. Amma
waɗansu daga baya ne zunubansu sukan bayyana a fili. 25 Haka
kuma ayyuka masu kyau a fili suke, ko ba ma a fili suke ba, ba
sa iya kasance a ɓoye.

6 1 Duk waɗanda suke ƙarƙashin bauta, su ba iyayengijinsu
cikakkiyar bangirma wadda ta dace, don kada a zargi sunan
Allah tare da koyarwarmu. 2 Kada bayi waɗanda iyayengijinsu
masu bi ne su yi musu rashin biyayya, a kan cewa su iyayengijinsu

---

5.18: M. Sh 25.4; Mat 10.10; Luk 10.7 **5.19**: M. Sh 17.6; 19.15

'yan'uwa ne cikin bi. A maimakon haka, sai su ƙara ƙoƙari tun da yake iyayengijinsu, waɗanda suke samun amfanin aikinsu masu bi ne, kuma waɗanda ake ƙauna.

Gargaɗi game da Koyarwar Karya

Lallai ne ka koyar ka kuma yi gargaɗi a kan waɗannan abubuwa. 3 Duk wanda yana da wata koyarwa dabam wanda bai kuma yarda da ainihin maganar Ubangijinmu Yesu Almasihu da kuma koyarwa wadda take bisa ga bin Allah ba, 4 wannan yana cike da ɗaga kai, kuma bai san kome ba. Wannan kuma yana rikɗe da mugun halin son gardama da mahawara game da kalmomi. Ai, wannan ne yake kawo kishi, da rikici, da zage-zage da mugayen zace-zace, 5 da yawan gardama tare da waɗanda tunaninsu ya zama banza, gaskiya kuma ta guje musu. Waɗannan suna ganin bin Allah wata hanya ce ta samun arziki. 6 Babu shakka! Akwai arziki sosai a bin Allah ga wanda yake da kwanciyar rai ga abin da yake da shi. 7 Don ba mu shigo cikin duniya da kome ba, haka ma ba za mu iya fita cikinta da kome ba. 8 Idan dai muna da abinci da rigunan sawa, wannan ma ya isa. 9 Amma waɗanda suke marmarin yin arziki sukan fāɗi cikin jarraba, cikin tarko na mugayen sha'awace-sha'awace iri-iri na banza, da na cutar da sukan sha kansu su ja su zuwa ga lalacewa da halaka. 10 Gama ƙaunar kuɗi ita ce tushen kowace irin mugunta. A cikin son yin arziki da sauri waɗansu sun kauce daga bangaskiyarsu har suka jawo wa kansu baƙin ciki mai yawa.

Gargaɗi ga Timoti

11 Amma ya kai mutumin Allah, ka guje wa dukan waɗannan abubuwa, ka sa kai ga neman adalci, da kasancewa da hali irin na Allah, da bangaskiya, da ƙauna, da jimrewa, da kuma tawali'u. 12 Ka yi kyakkyawar tseren nan, wato, tsere na bangaskiya. Ka karɓi lada na rai madawwami wanda ta dalilinsa ne aka kira ka, a lokacin da ka yi kyakkyawar shaida a gaban shaidu masu yawa. 13 Ina umarce ka a gaban Allah wanda yake ba da rai ga dukan kome, da kuma Almasihu Yesu wanda a cikin shaidarsa a gaban Buntus Bilatus ya yi kyakkyawar shaida, 14 ka kiyaye dokan nan ba tare da abin zargi ko laifi ba har sai Ubangijinmu Yesu Almasihu ya bayyana. 15 Wannan bayyanuwar kuwa Allah zai sa ta kasance a daidai lokaci. Allah wanda shi ne Mai albarka, kuma shi ne kaɗai Mai iko duka, Sarkin sarakuna, da Ubangijin

6.13: Yoh 18.37

iyayengiji. 16 Shi ne kaɗai marar mutuwa, mai kasancewa a cikin
hasken da ba wanda yana iya kusa da shi. Shi ne wanda babu
wani da ya taɓa gani, ko ya iya gani. A gare shi girma, da mulki
marar ƙarewa su tabbata. Amin.

Masu Bin Yesu da Suke Masu Arziki

17 Ka umarci waɗanda suke da arziki a duniyan nan cewa
kada su ɗaga kai ko su sa zuciyarsu a kan arziki wanda ba ya
jimawa. Amma su sa zuciyarsu ga Allah wanda yake ba mu kome
hannu sake don jin daɗin kanmu. 18 Ka umarce su su nuna alheri,
su ƙara yin ayyuka masu kyau, su kasance masu bayarwa hannu
sake, suna taimakon waɗansu. 19 Ta haka za su yi wa kansu ajiya
wadda za ta zama tushen rayuwa mai zuwa, saboda su sami rai
wanda shi ne ainihin rai.

Maganar Karshe

20 Timoti, ka lura da abin nan da aka ba ka amana. Ka ware
kanka daga maganganun banza na maganar reni ga Allah, da
koyarwar da take cike da gardamar da ake ɗauka wai ilimi ne
amma ƙarya ne. 21 Ta bin wannan koyarwa waɗansu mutane sun
riga sun kauce wa hanyar bangaskiya.

Alheri yă kasance tare da ku.

WASIKAR BULUS TA BIYU ZUWA GA
TIMOTI

Gabatarwa

Wannan wasiƙa ita ce ta biyu wadda Manzo Bulus ya rubuta wa Timoti, ɗansa cikin bangaskiya. Ya rubuta ta yayin da yake a kurkuku a Roma (1.8, 16-17, 2.9) a ƙarshen aikinsa, dab kuma da mutuwarsa a A.D. 67 ko 68.

Manufar wasiƙar ita ce don a gargaɗi Timoti a kuma ƙarfafa shi yă jimre a fuskar wahala, yă kuma ci gaba da aikin da Bulus ya yi saboda Almasihu.

Da farko, wasiƙar ta ƙarfafa Timoti yă kula da koyarwar da ya samu sosai (1.14). Da kuma kada yă ji tsoro shan wuya (1.8; 2.3-7), amma yă guji koyarwar ƙarya (2.14-19). Ta kuma gargaɗe shi game da kwanakin ƙarshe (3.1-17).

Bulus ya kammala wasiƙar cikin farin ciki da sa zuciya cewa Ubangiji zai fitar da shi daga kowane irin mugunta yă kuma kiyaye shi har zuwa mulkinsa (4.18).

Abubuwan da Suke Ciki

Gaisuwa 1.1-2
Yabo da ƙarfafawa 1.3—2.13
Gargaɗi da shawara 2.14—4.5
Halin da Bulus yake ciki 4.6-18
Maganar ƙarshe 4.19-22

Gaisuwa

1 [1] Daga Bulus manzon Almasihu Yesu bisa ga umarnin Allah.
Allah ya aike ni in sanar da alkawarin rai wanda yake cikin Almasihu Yesu.

2 Zuwa ga Timoti ɗana wanda nake ƙauna. Alheri, da jinƙai, da salama daga Allah Uba da Almasihu Yesu Ubangijinmu su kasance tare da kai.

Godiya da Karfafawa

3 Ina gode wa Allah wanda nake masa hidima da tunanin da yake tabbatar mini ba ni da laifi kamar yadda kakannina suka yi, sa'ad da nake tunawa da kai kullum dare da rana cikin addu'o'ina.

1.2: A. M. 16.1

4 Sa'ad da na tuna da hawayenka, sai in ji marmarin ganinka, don
dai in cika da farin ciki. 5 Na tuna da bangaskiyan nan taka ta
gaske, bangaskiya ta kasance a cikin kakarka Loyis, da kuma
mamarka Yunis, wadda kuma na tabbata kake da ita. 6 Shi ya sa
ina tuna maka ka inganta baiwan nan wadda take cikinka, wadda
Allah ya ba ka sa'ad da na sa maka hannun albarka. 7 Gama
Ruhun da Allah ya ba mu bai mai da mu masu tsoro ba, sai dai
masu iko, da ƙauna, da kuma natsuwa.

8 Domin haka kada ka ji kunyar shaidar Ubangijinmu, ko
kunyata da aka ɗaure dominsa, amma mu jimre cikin shan wahala
tare saboda Labari Mai Daɗin nan, ta wurin ikon Allah. 9 Shi ne
kuma ya cece mu, ya kira mu mu zama masu tsarki. Wannan kira
ba bisa ga ayyuka na samun lada ba ne, amma bisa ga nufinsa
da alherinsa. Wannan alheri an ba mu ne ta wurin Almasihu Yesu
kafin kafuwar duniya, 10 amma yanzu an bayyana mana shi ta
wurin zuwan Mai cetonmu Almasihu Yesu. Shi ya kawar da
mutuwa kuma ta wurin bishara ya bayyana mana rayuwan nan
marar ƙarewa a fili.

11 Saboda wannan Labari Mai Daɗi ne aka naɗa ni mai
wa'azi, da manzo, da kuma malami. 12 Don haka ne kuma ina
shan wahala kamar yadda nake sha ko a yanzu. Amma duk da
haka ba na jin kunya domin na san ga wane ne na ba da gaskiya,
kuma na tabbata zai lura da dukan abin da ya ba ni amanarsa,[a]
har zuwa Ranan nan.

13 Ka riƙe koyarwan nan ta gaskiya, wadda ka ji daga wurina
sosai, ka kuma yi koyi da ita. Ka kasance cikin bangaskiya da
ƙaunar da suke namu cikin Almasihu Yesu. 14 Ta wurin taimakon
Ruhu Mai Tsarkin da yake zaune cikinmu, ka kula da wannan
koyarwa ta gaskiyar da aka ba ka amanarta.

15 Ka san cewa kowa a Asiya ya juya mini baya, har da
Faijelus da Hamojenis. 16 Bari Ubangiji yă nuna jinƙai ga iyalin
gidan Onesiforus, don kullum yakan ƙarfafa ni, kuma bai ji kunya
wai ni ɗan kurkuku ne ba. 17 A maimakon haka da ya iso Roma,
ya neme ni ba da ɓata lokaci ba, sai da ya same ni. 18 Bari Ubangiji
yă sa a Ranan nan Onesiforus yă sami jinƙai daga wurinsa! Ai,
kai ma ka sani sarai irin hidimar da ya yi mini a Afisa.

1.5: A. M. 16.1 1.11: 1 Tim 2.7

[a] **1.12 Zai lura da dukan abin da ya ba ni amanarsa:** Wani juyi na wadannan kalmomi shi ne, "Zai lura da dukan abin da na ba shi amanarsa".

Soja Mai Aminci na Almasihu

2 [1] Kai kuma ɗana, ka yi ƙarfi ta wurin alherin da yake namu
cikin Almasihu Yesu. [2] Duk abin da ka ji daga gare ni a gaban
shaidu masu yawa ka koya wa mutane masu aminci waɗanda su
ma za su iya koya wa waɗansu.

3 Ka jimre tare da mu cikin shan wahala kamar soja mai
kyau na Almasihu Yesu. [4] Ai, babu sojan da yake a kan aiki da
zai sa kansa cikin al'amuran duniya, gama niyyar soja shi ne
yă sa shugabansa yă ji daɗi. [5] A sha'anin wasan guje-guje da
tsalle-tsalle kuwa, ba wanda yake samun lada sai dai ya bi
dokokin wasan. [6] Ai, manomin da ya yi aikinsa sosai shi ne ya
kamata yă fara samun rabon amfanin gona. [7] Ka yi tunani a kan
abin da na faɗa maka, don Ubangiji zai ba ka ganewa cikin
dukan kome.

8 Ka tuna da Yesu Almasihu wanda an ta da shi daga matattu,
wanda kuma yake zuriyar Dawuda, kamar yadda Labari Mai
Daɗin da nake shelarsa ya koyar. [9] Saboda shelar Labari Mai
Daɗin nan ne nake shan wahala, har zuwa ga ɗauri da sarƙa kamar
wanda ya yi laifi. Amma dai ba wanda zai iya ɗaura maganar
Allah. [10] Domin haka na jimre da kome saboda waɗanda aka zaɓa,
don su ma su sami ceton nan wanda yake ta wurin Almasihu
Yesu, su kuma sami shiga madawwamiyar ɗaukaka. [11] Wannan
magana tabbatacciya ce, mai cewa;

Idan mun mutu tare da shi,
za mu rayu tare da shi;
[12] Idan mun jimre,
za mu yi mulki tare da shi.
Idan mun yi mūsun saninsa,
shi ma zai yi mūsun saninmu;
[13] Idan ba mu da aminci,
shi mai aminci ne,
don ba za ya iya yin mūsun kansa ba.

Ma'aikacin da Allah Ya Yarda da Shi

14 Ka riƙa tuna musu waɗannan abubuwa, ka kuma gargaɗe
su a gaban Ubangiji cewa kada su yi gardama a kan kalmomi,
domin ba ta da amfani sai dai ta ɓata waɗanda suke jinta. [15] Ka
yi iyakacin ƙoƙarinka ka sami cikakkiyar yarda a gaban Allah.
Ka kasance ma'aikacin da ba shi da kunya game da aikinsa, kana

---

2.12: Mat 10.33; Luk 12.9

kuma koyar da kalmar gaskiya daidai. 16 Ka guje wa maganganun banza na maganar reni ga Allah, don sukan ja mutane zuwa ga rayuwa ta rashin kasancewa da hali irin na Allah. 17 Maganarsu kuwa tana bazu kamar babban miki mai cin naman jiki. A cikinsu akwai Himeniyus da Filetus, 18 waɗanda sun bar hanyar gaskiya da cewa, ai, an riga an yi tashin matattu. Suna ta ɓata bangaskiyar waɗansu. 19 Amma zaunannen tushen nan da Allah ya kafa, yana nan daram da hatimin da aka buga a kansa cewa, "Allah ya san waɗanda suke nasa" kuma "Duk wanda yake cewa shi na Ubangiji ne bari yă yi nesa da mugun aiki."

20 A cikin babban gida ba kayan zinariya da na azurfa ne kaɗai suke ciki ba, akwai ma na itace da na yumɓu, waɗansu domin aiki mai daraja, waɗansu kuma don aiki marar daraja. 21 Duk wanda yake tsarkake kansa daga abubuwa marasa darajan nan, zai zama abin da aka keɓe don aiki na musamman ga Maigidan, shiryayye kuma don kowane irin aiki mai kyau.

22 Ka guji mugayen sha'awace-sha'awace na matasa, ka sa kai ga neman adalci, da bangaskiya, da ƙauna, da kuma salama, tare da waɗanda suke kira ga Ubangiji da zuciya mai tsabta. 23 Kada wani abu ya haɗa ka da gardandamin banza marasa kan gado; kai ma ka san yadda suke jawo yawan hayaniya. 24 Kada mai hidimar Ubangiji yă zama mai yawan hayaniya, amma dai yă zama mai kirki ga kowa, yă kasance mai iya koyarwa, da mai haƙuri. 25 Sa'an nan kuma a cikin saukin kai yă gargaɗi masu gāba da koyarwarsa, ko watakila Allah zai ba su dama su tuba su kai ga sanin gaskiya. 26 Sa'an nan bayan sun koma cikin hankalinsu, sai su sami kuɓuta daga tarkon da Shaiɗan ya kama su da shi don su bi nufinsa.

Rayuwar Kwanakin Karshe

3 1 Ka sani fa, a kwanakin ƙarshe za a sha wuya sosai. 2 Domin mutane za su zama masu sonkansu, masu son kuɗi, masu taƙama, masu girmankai, masu zage-zage, marasa biyayya ga iyayensu, marasa godiya, marasa tsoron Allah, 3 marasa ƙauna, masu riƙe juna a zuciya, masu ɓata sunayen waɗansu, marasa kame kansu, masu ƙeta, masu gāba da duk abin da yake mai kyau, 4 masu cin amana, marasa hankali, waɗanda sun cika da ɗaga kai, masu son jin daɗin kansu fiye da son Allah, 5 a waje suna nuna halin addini, amma kuma ta wurin rayuwarsu suna mūsun ainihin ikonsa. Ka guje wa irin mutanen nan. 6 A cikinsu kuwa akwai

2.19: L. Kiɗ 16.5.

wadanda sukan nemi hanya su shiga cikin gidajen mutane su rinjayi mata marasa wayo wadanda zunubi ya sha kansu, kuma mugayen sha'awace-sha'awace iri-iri suna ta yawo da hankalinsu. 7 Wadannan ne matan da kullum suna kan koyo, amma duk da haka ba sa kaiwa ga sanin gaskiya. 8 Kamar yadda Jenis da Jambras[b] suka yi gāba da Musa, haka ma wadannan mutane suna gāba da gaskiya, hankalinsu kuma ya ɓace, bangaskiyarsu kuwa ta banza ce. 9 Amma ba za su kai da nisa ba, don da sauri za a gane da wautarsu a fili kamar yadda aka yi da na Jenis da Jambras.

Umarnai na Karshe

10 Yanzu ka riga ka bi koyarwata, da halina, da manufata ta rayuwa, da bangaskiyata, da hakurina, da ƙaunata, da kuma jimrewata. 11 Ka kuma sani tsanani da wahalar da suka same ni a Antakiya, da Ikoniya da Listira. Duk da haka, Allah ya cece ni daga cikinsu. 12 Lallai, duk wanda yake so yă yi rayuwa da hali irin na Allah a cikin Almasihu Yesu zai sha tsanani. 13 Amma mugayen mutane da masu rudu halinsu na mugunta zai ƙara muni gaba-gaba, suna rudîn mutane, su kuma ana rudînsu. 14 Amma kai kuwa, ka ci gaba da abin da ka koya, ka kuma ba da gaskiya sosai a kansa, domin kana sane da wadanda ka koya daga gare su. 15 Ka tuna yadda tun kana ƙaramin yaro ka riga ka san Rubutattun Maganar Allah masu tsarki wadanda suna iya koya maka hanyar samun ceto ta wurin bangaskiya cikin Almasihu Yesu. 16 Duk Rubutaccen Maganar Allah hurarre ne daga wurinsa, yana kuma da amfani[6] wajen koyarwa, da tsawatarwa, da gyaran hali, da kuma horarwa cikin adalci, 17 don duk wanda yake mutumin Allah yă zama cikakke, yana a shirye kuma domin kowane irin aiki mai kyau.

4 1 Ina umarce ka a gaban Allah da Almasihu Yesu, wanda zai hukunta masu rai da matattu, kuma zai dawo yă kafa mulkinsa, 2 ka nace cikin wa'azin maganar Allah ko da zarafi ko ba zarafi. Ka ja hankalin mutane, ka tsawata musu, ka kuma ƙarfafasu tare da iyakacin hakuri da koyarwa. 3 Gama lokaci yana zuwa da mutane ba za su so jin koyarwa ta gaskiya ba, a

3.8: Fit 7.11 **3.11**: A. M. 13.14-52; 14.1-20

[b] **3.8 Jenis da Jambras**: Babu wadannan sunayen a Tsohon Alkawari, amma bisa ga masanan tarihin Yahudawa, mutanen nan su ne bokayen nan biyu na ƙasar Masar da suka yi gāba da Musa lokacin da ya so yă fitar da 'ya'yan Isra'ila daga ƙasar Masar (Dubi Fit 7.11,22; 9.11).

[6] **3.16 Duk Rubutaccen Maganar Allah hurarre ne daga wurinsa, yana kuma da amfani**: Wata juyi na wadannan kalmomi shi ne, "Duk Rubutaccen Maganar da Allah ne ya huro yana da amfani."

maimakon haka don bin abin da zuciyarsu yake so da kuma ƙaiƙayin da kunnuwarsu suke yi za su kai kansu wajen malaman da za su ƙafa musu irin abin da suke so su ji. 4 Mutane za su ƙi bin gaskiya su mai da hankalinsu ga jin tatsuniyoyi. 5 Amma kai dai ka natsu cikin kowane hali, ka jimre cikin wahala, ka yi aikin mai bishara, ka cika hidimarka na zaman bawan Allah.

6 Gama lokacin da za a miƙa ni kamar hadaya, wato, lokacin da zan bar wannan rayuwa ya yi. 7 Na yi tseren nan mai kyau, na kammala tserena, na kuma riƙe amanar bangaskiyar da aka ba ni. 8 Yanzu an shirya mini lada na aikin adalci, wanda Ubangijin da yake alƙali mai adalci zai ba ni a Ranan nan. Ba ni kaɗai ba, amma ga dukan waɗanda suke jira cikin ƙauna su ga bayyanuwarsa.

Maganar Karshe

9 Ka yi iyakacin ƙoƙarinka ka zo wurina da sauri, 10 domin Dimas ya ƙyale ni saboda ƙaunar duniyan nan, ya tafi Tasalonika, Kirzens ya tafi Galatiya, Titus kuma ya tafi Dalmatiya. 11 Luka ne kaɗai yana tare da ni. Ka nemi Markus ka zo tare da shi, saboda yana da amfani sosai gare ni cikin aikina. 12 Na aiki Tikikus zuwa Afisa. 13 Sa'ad da za ka zo ka kawo mini rigar sanyin da na bari a hannun Karbus a Toruwas, da littattafan nan, musamman fatun nan na rubutu.[c] 14 Alekzanda maƙerin tagullan nan ya cuce ni sosai. Ubangiji zai saka masa gwargwadon abin da ya yi. 15 Kai ma ka lura da shi gama ya yi gāba sosai da saƙonmu.

16 A farkon kāre kaina da na yi a gaban masu shari'a ba wanda ya rufa mini baya, kowa ya guje ni. Kada dai Allah yă lissafta wannan a kansu. 17 Amma Ubangiji ya kasance da ni ya ba ni ƙarfi, don ta wurina wannan saƙo zai sami cikakkiyar shela har dukan waɗanda ba Yahudawa ba su ji. Kuma ya fitar da ni daga bakin zaki wato, hukuncin mutuwa. 18 Ubangiji zai fitar da ni daga kowane irin mugun abu, zai kuma kiyaye ni, yă kai ni mulkinsa na sama. A gare shi bari ɗaukaka ta tabbata har abada abadin! Amin.

4.10: Kol 4.14; Fil 24; 2 Kor 8.23; Gal 2.3; Tit 1.4
4.11: Kol 4.14; Fil 24; A. M. 12.12,25; 13.13; 15.37-39; Kol 4.10
4.12: A. M. 20.4; Afi 6.21-22; Kol 4.7-8 **4.13**: A. M. 20.6
4.14: 1 Tim 1.20; Zab 62.13; Rom 2.6

[c] **4.13 fatun nan na rubutu**: A zamanin Bulus ana rubutu a kan fatu ne.

Gaisuwar Karshe

19 Ka gai mini da Biriskila da Akila da kuma iyalin gidan
Onesiforus. 20 Arastus yana nan har yanzu a Korinti, kuma na bar
Turofimus cikin rashin lafiya a Militus. 21 Ka yi iyakacin
ƙoƙarinka ka zo kafin a fara damina. Yubulus da Fudens, da
Lainus, da Kalaudiya da dukan sauran 'yan'uwa suna gaisuwa.
22 Ubangiji yă kasance da ruhunku. Alherinsa kuma yă
kasance tare da ku.

WASIKAR BULUS ZUWA GA
TITUS

Gabatarwa

Manzo Bulus ne ya rubuta wannan *Wasika zuwa ga Titus* zuwa ga Titus abokin aikinsa da yake a Kirit. Ana zato Bulus ya rubuta ta a Makidoniya ne, lokacin da yake a hanyarsa zuwa Nikafolis a yankin Akaya a shekara ta A.D. 65.

Da farko an tuna wa Titus irin halin da ya kamata shugabannin jama'ar masu bi su kasance da shi wanda ya bambanta sosai da irin mugun halin da mutanen Kirit suke da shi. An shawarci Titus yadda zai koyar da mutane dabam-dabam a bisa ga shekarunsu a cikin jama'ar masu bi. A ƙarshe kuma an shawarce shi game da yadda masu bi za su yi rayuwarsu.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-4
Ma'aikatan jama'ar masu bi 1.5-16
Ayyuka na ƙungiyoyi dabam-dabam cikin jama'ar masu bi
2.1-15
Gargadî 3.1-11
Maganar Karshe 3.12-15

4.19: A. M. 18.2; 2 Tim 1.16-17 **4.20**: A. M. 19.22; Rom 16.23; A. M. 20.4; 21.29

Gaisuwa

1 [1] Daga Bulus bawan Allah kuma manzon Yesu Almasihu. An
mai da ni manzo don in ƙarfafa bangaskiyar waɗanda Allah
ya zaɓa, domin in taimake su su san gaskiyar da ta dace da bin
Allah, [2] ta wurin sa zuciya ga rai madawwami. Allah shi da ba
ya ƙarya ya yi alkawarin wannan rai madawwami tun kafin
farawar zamanai. [3] Sa'an nan a daidai lokaci ya bayyana shi a
cikin saƙonsa wanda nake wa'azi, wanda kuma aka ba ni
amanarsa ta wurin umarnin Allah Mai Cetonmu.

4 Zuwa ga Titus ɗana na gaske cikin bangaskiya da muke da
ita dukanmu.

Alheri da salama daga Allah Uba, da Almasihu Yesu Mai
Cetonmu su kasance tare da kai.

Aikin Titus a Kirit

5 Na bar ka a Kirit don ka kammala abin da ya rage a yi,
ka kuma naɗa dattibai a kowane gari, kamar yadda na umarce
ka. [6] Dattijo[a] yă kasance marar laifi a gaban mutane, mai mace
guda,[b] wanda kuma yaransa sun ba da gaskiya ga Yesu.
Yaransa su zama waɗanda ba a san su da halin iskanci ko ƙin
ji ba. [7] Tun da yake shugaban jama'ar masu bi mai hidimar
Allah ne, dole ne yă kasance ba shi da laifi ga kowa. Kada yă
zama mai ɗaga kai ko mai saurin fushi, ko mashayi, ko mai
rikici, ko kuwa mai kwaɗayin kuɗi. [8] A maimakon haka yă
kasance mai karɓan baƙi, mai cika son yin abu mai kyau, kuma
mai natsuwa sosai, mai adalci, mai tsarki, wanda kuma yake
kame kansa. [9] Shugaba yă zama wanda yana riƙe da maganar
saƙon Allah ta gaske kankan daidai kamar yadda ake koyarwa,
domin yă ƙarfafa waɗansu ta wurin wa'azi da koyarwa na
ƙwarai, yă kuma iya fallasa kuskuren waɗanda suke gāba da
koyarwarsa.

10 Akwai 'yan tawaye da yawa, masu maganganu marar kan
gado, masu ruɗu, musamman cikin Yahudawan da suka zama
masu bi. [11] Dole ne a tsawata musu su yi shiru, tun da yake suna
ta da hankalin iyalai da yawa ta hanyar koyar da abin da bai
kamata ba don neman ƙazamar riba. [12] Ai, mutumin Kirit ne,
kuma ɗaya daga cikin annabawansu, ya faɗa cewa;

1.4: 2 Kor 8.23; Gal 2.3; 2 Tim 4.10 **1.6-9:** 1 Tim 3.2-7

[a] **1.6-9 Dattijo:** Wato, shugaban jama'ar masu bi ke nan.

[b] **1.6 mace guda:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "Wanda ya yi aure sau ɗaya kawai".

"Kiritawa kullum masu ƙarya ne, mugayen dabbobi, 'yan ƙyuya masu yawan cin abinci". 13 Wannan shaida gaskiya ce.
Saboda haka ka tsawata musu sosai, don su kai ga bangaskiya ta
gaskiya, 14 don su daina sauraron tatsuniyoyin Yahudawa, da bin
dokokin mutane waɗanda suka ƙi gaskiya. 15 Kome mai tsabta ne
ga waɗanda suke da tsabtar zuciya. Amma ba abin da yake da
tsabta ga waɗanda ba su ba da gaskiya ba ko tsabtar zuciya saboda
ainihin lamirinsu da hankalinsu marar tsabta ne. 16 Da baki suna
cewa sun san Allah, amma ta ayyukansu suna mūsun saninsa. Sun
zama abin ƙyama, marasa biyayya, kuma ba su ma isa su yi aiki
mai kyau ba.

Yin Koyarwa ta Gaskiya

2 1 Amma kai dai, dole ka koyar da abin da yake daidai da
koyarwa ta gaskiya. 2 Ka koyar da tsofaffin maza su kame
kansu, su yi ƙwazo, su kuma natsu, su tsaya sosai cikin
bangaskiya, da ƙauna da kuma jimrewa.

3 Haka kuma ka koyar da tsofaffin mata su yi rayuwar da ta
dace da mata da suke masu bi, ba masu yin ƙarya a kan waɗansu
ba, ko waɗanda shaye-shaye sun sha ƙarfinsu. Sai su koyar da
abin da yake da kyau, 4 don su koya wa mata masu ƙuruciya su
ƙaunaci mazansu da 'ya'yansu, 5 su zama masu kame kansu, masu
tsabtar rai, masu iya kula da iyalansu, masu hankali, masu biyayya
ga mazansu, don kada a rena maganar Allah.

6 Haka kuma ka gargaɗi samari su kame kansu. 7 A cikin
dukan kome ka nuna kanka mutum ne mai aikin nagari, wanda
ya isa abin koyi. Ka yi koyarwarka da gaske tare da ƙwazo, 8 da
kuma magana mai ma'ana wadda ba za a iya samun abin zargi a
cikinta ba. Ta haka za ka ba wa abokan gābanka kunya yayin da
sun rasa mugun abin da za su faɗa a kanmu. 9 Ka umarci bayi su
yi biyayya ga iyayengijinsu cikin kome, su kuma sa a ji daɗinsu.
Kada su amsa musu magana da magana, 10 ko su yi musu sata.
A maimakon haka su nuna cewa su masu kirki ne da masu aminci,
don a cikin dukan kome su kawo girmamawa ga koyarwan nan
da take game da Allah Mai Cetonmu.

11 Gama Allah ya bayyana alherinsa domin ceton dukan
mutane. 12 Alherin nan yana koya mana mu bar rayuwa marar
hali irin na Allah, da sha'awace-sha'awacen duniya, mu kame
kanmu, mu zama masu adalci, muna masu hali irin na Allah a
wannan duniya. 13 Mu yi zaman haka yayin da muke zaman jira
da sa zuciya ga albarkan nan mai zuwa, wato, bayyanuwar

ɗaukakar Allahnmu mai girma da Mai Ceto Yesu Almasihu.[6]
14 Yesu ne ya bayar da kansa domin yă fanshe mu daga dukan
mugunta, don yă tsarkake wa kansa mutanen da za su zama nasa
waɗanda suna da marmarin yin ayyukan nagari.

15 Ka koyar da waɗannan abubuwa, ka ƙarfafa masu jinka,
ka kuma tsawata musu da dukan iko. Kada ka yarda wani yă
rena ka.

Rayuwar da ta Dace da Masu Bi

3 1 Ka tuna wa mutanenka su riƙa biyayya ga shugabanni da
kuma masu mulki, su yi musu ladabi, su kuma kasance a
shirye don yin kowane irin aiki mai kyau. 2 Kada su yi wa wani
mugun magana, kuma su zauna cikin salama, su kuma kasance
da saukinkai, su nuna hali mai kyau ga kowa. 3 Gama mu ma a
dā wawaye ne, marasa biyayya, aka kuwa ruɗe mu. Sha'awace-
sha'awace da kwaɗayi iri-iri suka ɗaure mu, muka kuma yi
rayuwarmu cikin kishi da riƙe juna a zuciya. Mutane suka ƙi mu,
mu kuma muka ƙi su.

4 Amma a sa'ad da aka bayyana alheri da ƙaunar Allah Mai
Cetonmu, 5 sai Allah ya cece mu. Wannan kuwa ya yi ba don
mun yi waɗansu ayyuka na adalci ba, amma bisa ga jinƙansa ne
ya cece mu ta wurin wankan nan na Ruhu Mai Tsarki wanda ya
ba mu sabon haihuwa da sabon rai. 6 Ruhu Mai Tsarkin nan ne
aka zubo a yalwace a kanmu ta wurin Yesu Almasihu Mai
Cetonmu. 7 Ya yi wannan domin ta wurin alherinsa mu sami
zaman marasa laifi a gaban Allah, kuma mu zama waɗanda za
su gāji rai madawwamin nan da muka sa zuciya a kai. 8 Maganan
nan tabbatacciya ce.

Ina so ka ƙarfafa waɗannan abubuwa sosai, don waɗanda
sun ba da gaskiya ga Allah su nace yin amfani da su wajen yin
aikin da yake mai kyau. Waɗannan abubuwa kuwa suna da kyau
ainu, kuma suna da amfani ga kowa. 9 Amma ka guje wa
gardandamin banza, da lissafin sunayen kakanni, da jayayya,
da kuma yawan gardama game da Doka, saboda ba su da amfani
kuma banza ne. 10 Amma ga mutum mai rigima, bayan ka
gargaɗe shi da farko da na biyu, sai ka rabu da shi. 11 Ka sani
cewa irin mutumin nan ya ɓace, kuma zunubansa sun riga sun
hukunta shi.

2.14: Zab 130.8; Fit 19.5; M. Sh 4.20; 7.6; 14.2; 1 Bit 2.9

[6] **2.13 Allahnmu mai girma da Mai Ceto Yesu Almasihu:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "Mai girman nan Allah Mai Cetonmu."

Gargadi na Karshe

12 Sa'ad da na aika Artimas ko Tikikus wurinka, sai ka yi
iyakacin ƙokarinka ka zo wurina a Nikafolis, don ina da niyya
cin damina a can. 13 Ka kuma yi iyakacin ƙokarinka ka taimaki
Zenas lauyan nan, da Afolos su kama hanya. Ka kuma tabbata
cewa ba su rasa kome ba. 14 Dole mutanenmu su rika koya mika
kansu ga aikata ayyuka nagari, domin su iya taimakawa wajen
biyan muhimman bukatu. Kada su yi rayuwa marar amfani.

15 Duk wadanda suke tare da ni suna gaishe ka. Ka gai da
wadanda suke ƙaunarmu, wadanda muke tare da su cikin
bangaskiya.

Alherin Allah yă kasance tare da ku duka.

WASIKAR BULUS ZUWA GA
FILIMON

Gabatarwa

Manzo Bulus ne ya rubuta wannan wasika zuwa ga Filimon a madadin Onisimus wanda shi bawan Filimon ne. Ana zato an rubutata a tsakanin shekara ta A.D. 61-63 a lokacin da Bulus yake a kurkuku ne.

An rubuta wannan wasika domin a shirya tsakanin Filimon da bawansa Onisimus domin Onisimus ya yi wa Filimon laifi wanda ana zato ya hada da sata.

Abubuwan da Suke Ciki

Gaisuwa 1-3
Bangaskiya da ƙaunar Filimon 4-7
Roko a madadin Onisimus 8-22
Gaisuwa da fatan alheri 23-25

Gaisuwa

1 Daga Bulus, ni da aka kulle a kurkuku saboda aikin da na
yi domin Almasihu Yesu, da kuma daga ɗan'uwanmu Timoti,
zuwa ga Filimon abokinmu da muke ƙauna da abokin aikinmu,
2 da kuma zuwa ga jama'ar masu bi da take a gidanka, da kuma
Afiya 'yar'uwarmu da Arkibus ɗan'uwanmu cikin fama.
3 Alheri da salama daga Allah Ubanmu da Ubangiji Yesu
Almasihu su kasance tare da ku.

Kauna da Bangaskiyar Filimon

4 Nakan gode wa Allah kullum dominka sa'ad da nake
addu'o'ina. 5 Gama ina jin labarin bangaskiyarka cikin Ubangiji
Yesu da kuma ƙaunar da kake nuna wa dukan tsarkaka. 6 Ina
addu'a zumuncin da yake tsakaninmu saboda bangaskiyarmu yă
kai ga zurfin ganewa game da dukan abubuwan masu kyau da
suke namu cikin Almasihu.
7 Ɗan'uwana, ƙaunarka ta kawo mini farin ciki ainu da kuma
ƙarfafawa sosai. Gama zukatan tsarkaka sun sami ƙarfafawa ta
wurinka.

Roƙo domin Onisimus

8 Saboda yadda kake ƙaunar masu bi, ina iya yin ƙarfin hali
cikin Almasihu in umarce ka ka yi abin da ya kamata ka yi.
9 Amma saboda ina ƙaunarka, nafi so in roƙe ka ni Bulus, ni
da nake tsoho [a] yanzu kuma ina a kulle cikin kurkuku saboda
Almasihu Yesu. 10 Ina roƙonka a madadin ɗana Onisimus
wanda na zama kamar baba a gare shi sa'ad da nake a kurkuku.
11 A dā ba shi da amfani [b] a gare ka, amma yanzu ya zama mai
amfani a gare ka da kuma gare ni.
12 Ina aike shi yanzu yă koma gare ka, shi wanda zuciyata
duka take a kansa. 13 Yayin da nake a nan kurkuku saboda
bishara, na so in bar shi tare da ni don yă riƙa yin mini hidima
a madadinka. 14 Amma dai ba na so in yi wani abu ba tare da
na sami yardarka ba, don kada alherinka yă zama kamar na tilas
ne, ba na ganin dama ba.

1.2: Kol 4.17 1.10: Kol 4.9

[a] 1.9 **ni Bulus da nake tsoho**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Ni Bulus da nake Jakada na Almasihu." Wannan ya zama haka ne don "tsoho" da "Jakada" kalma iri ɗaya ce a Helenanci.

[b] 1.11 **amfani**: Ma'anar sunan Onisimus da Helenanci ita ce "Amfani."

15 Wataƙila Onisimus ya rabu da kai na ɗan lokaci kaɗan ne
domin ka sāke karɓe shi ga zama na har abada. 16 Ba wai ka karɓe
shi a matsayin bawa ba, amma har fiye da haka, wato, ka karɓe
shi a matsayin ɗan'uwan da ake ƙauna. Ina ƙaunarsa sosai balle
ma kai, ai, za ka ƙaunace shi fiye da haka, a matsayinsa na bawa
da kuma na wanda ya ba da gaskiya ga Ubangiji! 17 Don haka
idan ni abokin aiki ne a gare ka, to, ka karɓe shi daidai yadda za
ka karɓe ni. 18 Idan ma Onisimus ya yi maka laifi, ko yana riƙe
da bashinka, ka lissafta duka a kaina. 19 Ni Bulus nake rubuta
wannan da hannuna cewa ni zan biya ka. (Kada ma in yi zancen
sabon rai nan da ka samu ta wurina.)[6] 20 Don haka ɗan'uwana,
na roƙi arzikinka game da wannan alheri saboda Ubangiji. Ka
faranta mini rai cikin Almasihu!

21 Na tabbata za ka yi biyayya; shi ya sa na rubuta wannan
da sanin cewa za ka aikata fiye da yadda na faɗa. 22 Har wa yau,
ina so ka shirya mini ɗakin da zan sauka, don ina sa rai ta wurin
addu'o'inku Allah zai mayar da ni gare ku.

Gaisuwar Karshe

23 Abafaras wanda yake cikin kurkuku tare da ni saboda
Almasihu Yesu yana gaishe ka. 24 Markus, da Aristarkus, da
Dimas, da kuma Luka waɗanda su duk abokan aikina ne, su ma
suna gaishe ka.

25 Alherin Ubangiji Yesu Almasihu yă kasance tare da
ruhunku.

1.23: Kol 1.7; 4.12
1.24: A. M. 12.12,25; 13.13; 15.37-39; 19.29; 27.2; Kol 4.10, 14; 2 Tim 4.10,11
[6] **1.19 Kada ma in yi zancen sabon rai nan da ka samu ta wurina:** Da Helenanci an rubuta "Ba lallai in tunashe ka yadda kake kamar bashi ne a gare ni ba."

WASIKA ZUWA GA
IBRANIYAWA

Gabatarwa

Ba a tabbatar da wanda ya rubuta wannan littafin ba. Ana zato an rubuta ta kafin rushewar haikali a Urushalima a shekara ta A.D. 70, musamman don marubucin ya yi magana game da haikalin.

An rubuta wasiƙar a lokacin da waɗansu a cikin jama'ar masu bi, musamman Yahudawa, suka soma nuna wani hali kamar ana jan hankalinsu ga barin bangaskiyarsu. Mai yiwuwa suna fuskanta waɗansu wahaloli. An rubuta wannan wasiƙar domin a ƙarfafa irin waɗannan mutane, ta wurin nuna cewa Yesu Almasihu ne ya cika duk alkawura da shirye-shiryen da Allah ya yi tun daga farko.

Littafin yana ba da tabbaci cewa ɗaukakar Yesu da ikonsa sun fi na mala'iku, da na annabawa, da na manyan firistoci na Tsohon Alkawari (1.1-4, 13). Aikin ceton da Allah ya cika ta mutuwar Yesu shi ne ainihin hanyar ceton da Allah ya shirya tun daga farko. Hadayu da baye-baye na Tsohon Alkawari duk misalai ne kawai game da mutuwar Yesu (4.14—7.28). Bisa ga zuwan Yesu kuma an kawo Sabon Alkawari wanda shi ne mafi kyau (8.1—10.18). A ƙarshe kuma wasiƙar ta yi wa masu bi gargaɗi su riƙe bangaskiyarsu da ƙarfi sosai (10.19—13.25) kamar yadda jarumawan bangaskiya na cikin tarihin Isra'ilawa suka yi.

Abubuwan da Suke Ciki

Yesu ya bayyana Allah 1.1-3
Yesu ya fi mala'iku 1.4—2.18
Yesu ya fi annabawa 3.1—4.13
Tsarin firist na Yesu ya fi na Haruna 4.14—7.28
Sabon alkawari ya fi tsohon 8.1—10.18
Muhimmincin bangaskiya 10.19—12.29
Maganar ƙarshe 13.1-25

Yesu Shi Ne Ya Bayyana Allah

1 [1] A dā, Allah ya yi wa kakanninmu magana ta hanyoyi iri-iri
da kuma a lokatai dabam-dabam ta wurin annabawa. [2] Amma
a waɗannan kwanakin ƙarshe ya yi mana magana ta wurin Ɗansa.
Ta wurin Ɗan ne Allah ya halicci kome da kome. Shi ne kuma
aka zaɓa domin kome yă zama nasa. [3] Shi ne hasken ɗaukakar
Allah da kuma ainihin kamannin Allah. Daidai yake kuma da

Allah. Yana rike da dukkan kome ta wurin maganarsa mai iko.
Bayan ya tsarkake mu daga zunubanmu, sai ya zauna a sama a
hannun daman Mai Daukaka duka.

Yadda Yesu Ya Fi Mala'iku

4 Ta haka nan kuma ya sami matsayin da ya fi na mala'iku
kamar yadda sunan da aka ba shi ya fi nasu girma.
5 Gama babu wani mala'ikan da Allah ya taba ce masa,
"Kai Dana ne,
yau na zama Ubanka."
Ko kuwa wani da aka ce masa,
"Zan zama Ubansa,
shi kuwa yă zama Dana."
6 Amma da zai aiki Dansa na fari cikin duniya, ya ce,
"Bari dukan mala'ikun Allah su yi masa sujada."
7 Game da mala'iku, Allah ya ce,
"Allah yakan sa mala'ikunsa su zama kamar iska,
masu hidimarsa kuma kamar harshen wuta."
8 Amma game da Dan ya ce,
"Mulkinka, ya Allah, na har abada abadin ne,
Adalci shi ne sandan da za ka yi mulki da shi.
9 Aikin adalci ne kake so, mugunta kuma ka ki sam!
Saboda haka Allah, wato Allahnka, ya shafe ka da man
farin ciki,
ya kuma girmama ka fiye da abokanka."
10 Ya kuma ce,
"Tun daga farko, ya Ubangiji, kai ka kafa tushen duniya,
sammai kuma ayyukan hannayenka ne.
11 Za su shude, amma kai kana nan;
za su tsufa kamar riga.
12 Za ka nade su kamar yadi;
za a canza su yadda ake canza zane.
Amma kai ba ka canzawa,
shekarunka marar karewa ne."
13 Ba wani a cikin mala'ikunsa da Allah ya taba ce masa,
"Zauna a hannun damana har in sa masu gāba da kai a
karkashin kafafunka
har in sa ka tattaka su."
14 Hakika, dukan mala'iku ruhohin hidima ne. Allah yakan
aike su domin su taimaki wadanda za su ci gādon ceto.

1.5: Zab 2.7; 2 Sam 7.14; 1 Tar 17.13 **1.6**: M. Sh. 32.43 **1.7**: Zab 104.4
1.8-9: Zab 45.7-8 **1.9**: Zab 45.6,7 **1.10-12**: Zab 102.25-27 **1.13**: Zab 110.1

Kasa Kunne ga Maganar Allah

2 [1] Saboda haka, ya kamata mu mai da hankali ga abubuwan
da muka ji, domin kada a ja hankalinmu ga barin hanya.
[2] Saƙon da aka ba mu ta bakin mala'iku[a] ya sami tabbaci, kuma
duk wanda ya ƙi jinsa, ko ya yi rashin biyayya da shi, ya sami
hukuncin da ya kamata. [3] Ta yaya za mu tsira idan mun ƙyale
irin wannan babban ceto wanda Ubangiji ne da kansa ya fara
sanar da shi? Waɗanda suka ji maganarsa kuma sun tabbatar
mana cewa wannan gaskiya ne. [4] Sa'an nan Allah ya ƙara nasa
shaida a kan tasu ta wurin alamu, da abubuwan ban mamaki,
da al'ajabai iri-iri, da baye-baye waɗanda aka rarraba ta wurin
Ruhu Mai Tsarki bisa ga nufinsa.

Yesu Ya Zama Kamar 'Yan'uwansa

5 Wannan zamani mai zuwa, wanda muke magana a kai yanzu,
ai, ba mala'iku ne Allah ya sa su yi mulkinsa ba. [6] A maimakon
haka, wani ya shaida a wani wuri a cikin Rubutaccen Maganar
Allah cewa,

"Mene ne mutum, ya Allah, har da kana sa shi a
tunaninka,
Mene ne mutum, har da kana lura da shi haka?
[7] Ka sa shi a matsayin da yake ƙasa da na mala'iku a ɗan
lokaci kaɗan;
ka naɗa shi da ɗaukaka da girma,
[8] Ka sa kome a ƙarƙashin ikonsa."

Da Allah ya sa kome a ƙarƙashin ikon mutum, ba wani abin da
bai ba mutum iko a kai ba. Ko da yake, yanzu haka, ba ma gani
yadda mutum yake yin mulki a kan dukkan abubuwa. [9] Amma
abin da muke gani dai shi ne Yesu wanda a ɗan lokaci kaɗan an
sa shi a matsayin da yake ƙasa da na mala'iku. Yanzu kam, an
naɗa shi da ɗaukaka da girma saboda ya sha wahalar mutuwa a
madadin dukan mutane, bisa ga alherin Allah.

10 Allah ne ya halicci kome, shi ne kuma yakan lura da kome.
Saboda haka, idan Allah zai kawo 'ya'yansa masu yawa ga samun
ɗaukaka, ya kyautu ne yă kyautata shugaban cetonsu. Ya yi haka
ta wurin wahalar da Yesu ya sha.

2.6-8: Zab 8.4-6

[a] **2.2 Saƙon da aka ba mu ta bakin mala'iku:** Wato, dokokin Allah waɗanda mala'iku suka ba wa Musa.

11 Gama da shi mai tsarkake mutane, da su waɗanda aka
tsarkake su kuma, duk suna da Uba ɗaya. Shi ya sa Yesu ba ya
jin kunya yă ce da su 'yan'uwansa. 12 Ya ce wa Allah,
"Zan yi shelar sunanka ga 'yan'uwana;
A gaban taron mutanenka zan rera yabonka."
13 Ya kuma ce,
"Ni ma zan dogara ga Allah."
Ya kuma sāke cewa,
"Ga ni nan tare da 'ya'yan da Allah ya ba ni."
14 Tun da yake 'ya'yan nan mutane ne masu nama da jini, sai
ya zama ɗaya da su cikin jiki. Ya yi haka domin ta wurin
mutuwarsa, yă halakar da wanda yake riƙe da ikon mutuwa, wato
Shaiɗan. 15 Sa'an nan kuma yă kunce duk waɗanda tsoron mutuwa
ya ɗaure su, kuma har tsoron ya mai da su bayi dukan rayuwarsu.
16 Lallai ba mala'iku ne yake musu taimako ba, amma 'ya'yan
Ibrahim ne yake musu taimako. 17 Shi ya sa aka mai da shi kamar
'yan'uwansa ta kowace hanya, domin yă zama babban firist mai
aminci, mai jinƙai kuma a cikin hidimarsa ga Allah. Ta haka
kuma Allah zai gafarta zunuban mutane. 18 Da yake shi da kansa
ya sha wahala a lokacin gwadawarsa, ya isa yă taimaki duk
waɗanda ake gwada su.

Yadda Yesu Ya Fi Musa

3 1 Saboda haka, 'yan'uwana tsarkaka, ku da kuka sami kiran
nan na sama ku ma, ku yi tunani a kan Yesu wanda shi ne
Manzo da Babban Firist na saƙon da muke shaida. 2 Yesu ya yi
aminci ga wanda ya zaɓe shi, kamar yadda Musa ya yi aminci
a aikinsa a cikin jama'ar Allah. 3 Mutumin da ya gina gida ya
fi gidan daraja. Haka kuma Yesu ya isa a ɗaukaka shi fiye da
Musa. 4 Gama kowane gida yana da wanda ya gina shi, amma
Allah ne ya gina kome. 5 Musa ya yi aminci a aikinsa na bawa
a cikin jama'ar Allah, ya kuma yi shaida game da abubuwan
da za a faɗa nan gaba. 6 Amma Almasihu ya yi aminci a kan
shi Ɗa ne wanda an ba shi iko a kan dukan jama'ar Allah. Mu
ne kuma jama'an nan tasa idan mun ci gaba da ƙarfin
zuciyarmu, muna kuma sa zuciya ga abubuwan da muke bege
a kansu.

Gargaɗi a kan Rashin Bangaskiya

7 Saboda haka, kamar yadda Ruhu Mai Tsarki ya ce,

2.12: Zab 22.22 **2.13:** Ish 8.17,18 **3.2:** L. Kid 12.7

"Yau, idan kun ji muryar Allah,
8 kada ku yi taurin zuciya kamar yadda kuka yi a lokacin
tawayen nan,
kamar ranar da aka gwada ni a daji.
9 A can ne kakanninku suka gwada ni,
ko da yake sun ga ayyukan da na yi ta yi har shekara
arba'in.
10 Shi ya sa na yi fushi da wancan zamani,
sai na ce, 'Kullum suna ƙina a zuciyarsu,
ba su kuwa san hanyoyina ba.'
11 Sai na yi fushi na yi rantsuwa cewa,
'Ba za su shiga hutuna ba sam.' "

12 'Yan'uwana, ku tabbata cewa ba wani a cikinku wanda zunubi da rashin bangaskiya a zuciyarsa sun sa shi yă juye baya ga Allah mai rai. 13 Amma ku riƙa ƙarfafa juna kowace rana. Ku yi amfani da kowane zarafi wanda ake ce da shi "Yau", domin kada ko ɗayanku yă zama mai taurin zuciya ta wurin ruɗu na zunubi. 14 Mu masu tarayya da Almasihu ne idan mun riƙe bangaskiyarmu da ƙarfi daga farko har zuwa ƙarshe. 15 Kamar yadda aka ce,

"Yau, idan kun ji muryar Allah,
kada ku yi taurin zuciya kamar yadda kuka yi a lokacin
tawayen nan."

16 Su wane ne waɗanda suka ji muryar Allah, duk da haka, suka yi masa tawaye? Ai, su ne dukan mutanen da Musa ya bi da su daga ƙasar Masar. 17 Su wane ne waɗanda Allah ya yi fushi da su har shekara arba'in? Ai, su ne waɗanda suka yi zunubi, suka fāɗi suka mutu a daji. 18 Su wane ne waɗanda Allah ya yi rantsuwa a kansu cewa ba za su shiga hutunsa ba sam? Ai, su ne waɗanda suka ƙi yin biyayya. 19 Saboda haka mun ga cewa rashin bangaskiya ne ya sa ba su iya shiga hutun nan ba.

Hutu domin Mutanen Allah

4 1 Da yake alkawarin shiga hutunsa[b] yana nan har yanzu, bari mu yi hankali sosai kada wani daga cikinku yă kāsa shiga. 2 Gama mun riga mun ji wa'azin Labari Mai Daɗi kamar yadda su ma suka ji. Amma saƙon bisharan nan da suka ji bai yi musu wani amfani ba, domin ba su karɓe shi da bangaskiya ba. 3 Amma

---

3.7-11: Zab 95.7-11 **3.15:** Zab 95.7-8 **3.16-18:** L. Kid 14.1-35

[b] **4.1 hutunsa:** Wato, ceto ke nan.

mu da muka ba da gaskiya, mu ne masu shiga hutun nan. Mu rika tuna da maganar Allah nan mai cewa,

"Sai na yi fushi na yi rantsuwa, na ce,
'Ba za su shiga hutuna ba sam.' "

Allah ya fada haka ko da yake ya riga ya gama aikinsa tun lokacin da ya halicci duniya.

4 Gama a wani wuri a cikin Rubutaccen Maganar Allah an yi magana game da rana ta bakwai cewa, "A rana ta bakwai Allah ya huta daga dukan aikinsa." 5 Amma har yanzu an sāke yi wannan zance cewa, "Ba za su shiga hutuna ba sam." 6 A dā an yi wa'azin Labari Mai Dadi game da hutun nan, amma wadanda aka yi musu wa'azin ba su shiga ba saboda rashin bangaskiya. To, yanzu haka, akwai zarafi don wadansu su shiga hutun ke nan. 7 Ga shi kuwa Allah ya sāke shirya wata rana, wadda ya kira, "Yau". Ya yi magana game da ranar ne, bayan shekaru masu yawa ta bakin Dawuda, kamar yadda Rubutaccen Maganar Allah ya fada a dā,

"Yau, idan kun ji muryar Allah,
kada ku yi taurin zuciya."

8 Da a ce Joshuwa ya ba wa mutanen Allah hutun nan da Allah bai yi magana daga baya a kan wata rana dabam ba. 9 Wannan ya nuna cewa har yanzu akwai hutu irin na rana ta bakwai domin mutanen Allah. 10 Gama duk wadanda suka shiga hutun Allah sukan huta daga ayyukansu kamar yadda Allah ya huta daga nasa. 11 Don haka bari mu yi iyakacin ƙoƙarinmu mu shiga hutun nan. Kada kowa ya kāsa shiga saboda bin misalin wadanda suka yi rashin biyayya.

Ikon Maganar Allah

12 Hakika, maganar Allah tana da rai, tana da ƙarfin aiki kuma. Kaifinta ya fi na kowane takobi mai baki biyu. Tana sara har ciki-cikin mutum, ta raba ruhu da rai, da kuma gaɓoɓi da ɓargo. Har ma tana gane duk tunani da nufin da suke cikin zuciya. 13 Ba wani abu a dukan halitta da yake a ɓoye ga Allah. Kome da kome yana nan a bude, a fili kuma, a gaban idonsa. Shi ne kuma wanda za mu ba shi lissafi game da rayuwarmu.

4.3: Zab 95.11 **4.4**: Far 2.2 **4.5**: Zab 95.11 **4.7**: Zab 95.7,8
4.8: M. Sh 31.7; Josh 22.4 **4.10**: Far 2.2

Yesu Shi Ne Babban Firist Mai Girma

14 To, tun da yake muna da babban firist mai girma, wato,
Yesu Ɗan Allah wanda ya je sama har gaban Allah, bari mu riƙe
bangaskiyarmu da ƙarfi sosai. 15 Gama babban firist nan namu ba
wani ne wanda bai damu da kāsawarmu ba. A'a, shi mutum ne
wanda aka gwada shi ta kowace hanyar da akan gwada mu, amma
fa bai yi wani zunubi ba. 16 Saboda haka, bari mu yi ƙarfin zuciya,
mu zo kusa da kursiyin Allah, wato, wurin alheri, domin mu karɓi
jinƙai, mu kuma sami alheri wanda zai taimake mu a lokacin
bukata.

5 1 Akan zaɓi kowane babban firist daga cikin 'yan'uwansa ne
domin yă yi wa Allah hidima a madadin sauran mutane. Shi
ne mai miƙa baye-baye da hadayu saboda zunubai. 2 Tun da yake
shi da kansa yana da nasa kāsawa, yana iya yă bi da masu rashin
sani da masu kauce hanya a hankali. 3 Saboda kāsawan nan nasa,
ya zama tilas yă miƙa hadayu, ba saboda zunuban jama'a kaɗai
ba, amma saboda nasa zunuban ma.

4 Ba wanda zai zaɓa wa kansa aikin nan mai daraja. Mutum
yakan zama babban firist ne bisa ga kiran Allah, kamar yadda
aka kira Haruna. 5 Haka kuma Almasihu bai ɗaukaka kansa yă
zama babban firist ba. A maimakon haka, Allah ya ce masa,

"Kai Ɗana ne,
yau na zama Ubanka."

6 Ya sāke yin magana a wani wuri ya ce,

"Kai firist ne na har abada,
bisa ga tsarin Malkizadek."

7 A lokacin da Yesu yake cikin duniya, ya miƙa addu'o'i da
roƙe-roƙe tare da kuka mai tsanani da hawaye. Ya kuwa miƙa
addu'o'insa ga Allah wanda yana iya cece shi daga mutuwa.
Domin shi mai biyayya ne cikin tsoron Allah, Allah ya karɓi
roƙonsa. 8 Ko da yake Yesu Ɗan Allah ne, ya koyi yin biyayya
ta hanyar azabar da ya sha. 9 Bayan ya kai ga zaman cikakke, sai
ya zama tushen ceto na har abada ga duk masu yi masa biyayya.
10 Ta haka kuma Allah ya naɗa shi babban firist bisa ga tsarin
Malkizadek.

Gargaɗi a kan Juya Baya

11 Muna da abubuwa da yawa da muke so mu faɗa game da
wannan zancen, amma yana da wuya mu bayyana muku, domin

5.3: L. Fir 9.7 **5.4**: Fit 28.1 **5.5**: Zab 2.7 **5.6**: Zab 110.4
5.7: Mat 26.36-46; Mar 14.32-42; Luk 22.39-46

ba ku da saurin ganewa. 12 Yanzu haka ya kamata da kun zama
masu koyarwa, amma har yanzu kuna bukatar wani yă sāke
maimaita muku koyarwa mai saukī ta maganar Allah. Ba ku isa
cin abinci mai kauri[6] ba, sai shan nono kawai! 13 Duk wanda nono
ne abincinsa, shi jariri ne; bai kuwa san kome game da koyarwa
ta adalci ba. 14 Amma abinci mai kauri shi ne na waɗanda suka
yi girma. Waɗannan su ne masu ƙoƙarin yin amfani da hankalinsu
kullum, har ma suna iya bambanta nagarta da mugunta.

6 1 Saboda haka, bari mu ci gaba a kan koyarwan nan ta farko
da muka karɓa game da Almasihu, domin mu zama masu
cikakken ganewa. Kada yă zama cewa har yanzu muna kafa
tushen koyarwa a kan ba da gaskiya ga Allah, da ta tuba daga
ayyukan da za su kai ga halaka,[c] 2 da koyarwa a kan baftisma,[d]
da ta sa hannun albarka, da ta tashin matattu, da ta shari'ar ranar
ƙarshe. 3 Cin gaba kam za mu yi, idan Allah ya yarda.

4 Gama waɗanda suka juya baya daga bangaskiyarsu, ba zai
yiwu a sa su su sāke tuba ba. Waɗannan dai an taɓa kawo su
cikin hasken Allah, sun mori baye-baye irin na sama, sun sami
rabonsu cikin Ruhu Mai Tsarki, 5 sun kuma ɗanɗana daɗin
maganar Allah da kuma ikon zamani mai zuwa. 6 Duk da haka,
sun juya baya daga bangaskiyarsu! Ba zai yiwu a sa su su sāke
tuba ba, domin suna sāke gicciye Ɗan Allah ne, suna kuwa ba
shi kunya a fili.

7 Ƙasar da take shan ruwan sama da yakan fādi a kanta
kullum, tana kuma ba da tsire-tsire masu amfani ga waɗanda suke
nomanta, wannan ƙasa ce mai karɓar albarkar Allah. 8 Amma idan
ƙasa tana fitar da ƙaya da muguwar ciyawa, ba ta da amfani ke
nan. Wannan ƙasar kuwa Allah ya kusa yă la'anta ta. A ƙarshe
kuma ƙone ta za a yi.

9 'Yan'uwanmu, ko da yake muna irin wannan magana, ba
mu da shakka a kan cewa ku kam kun karɓi albarku mafi kyau
waɗanda suke na cetonku. 10 Allah ba marar adalci ba ne. Ba zai
ƙyale ayyukanku da kuka yi ba, da ƙaunar da kuka nuna masa
sa'ad da kuke taimakon masu bi ba, kamar yadda kuke yi har
yanzu. 11 Muna so kowannenku ya ci gaba da yin ƙwazo haka har

---

5.12-13: 1 Kor 3.2 **6.8:** Far 3.17-18

[6] **5.12 abinci mai kauri:** Wato, koyarwa mai zurfi ke nan.

[c] **6.1 ayyukan da za su kai ga halaka:** Wata fassara ta waɗannan kalmomi ita ce, "al'adun wofi" ko kuwa "ayyukan banza".

[d] **6.2 baftisma:** Mai yiwuwa baftismar da ake magana a nan ita ce ta wankan baftisma wadda Yahudawa sukan yi, ko kuwa baftisma irin ta Yohanna, ko kuwa baftisma irin ta Kirista.

zuwa ƙarshe, domin ku sami cikawar abubuwan nan da kuka sa
zuciya a kansu. 12 Kada ku zama masu ƙyuya, amma ku bi misalin
waɗanda suka ba da gaskiya, suka yi haƙuri har suka karɓi abin
da Allah ya yi alkawari zai ba su.

Tabbacin Alkawarin Allah

13 A lokacin da Allah ya yi wa Ibrahim alkawari, ya yi
alkawarinsa tare da rantsuwa. Ya yi rantsuwar da sunansa tun da
yake ba wanin da ya fi Allah girma da Allah zai rantse da shi.
14 Allah ya ce, "Lallai ne zan sa maka albarka, zan kuma sa
zuriyarka ta zama mai yawa sosai." 15 Bayan Ibrahim ya jimre da
haƙuri sosai, sai ya karɓi abin da aka yi masa alkawari. 16 Mutane
sukan yi rantsuwa ne bisa ga wanda ya fi su girma. Rantsuwar
kuwa takan tabbatar da alkawarin ta wurin hana yin mūsu. 17 Haka
kuma, da Allah ya so yă nuna wa waɗanda za su gāji alkawarinsa
cewa, ba shakka, nufinsa marar canzawa ne, sai ya tabbatar da
alkawarinsa ta wurin rantsuwa. 18 To, akwai abubuwan nan guda
biyu waɗanda suke marar canzawa, waɗanda ba zai yiwu Allah
ya yi rashin aminci game da su ba. Da yake wannan abin ƙarfafa
zuciya sosai ne gare mu, mu da muka gudu zuwa mafaka, ya
kamata mu riƙe abin nan da muka sa zuciya a kai da ƙarfi sosai.
19 Wannan sa zuciyan nan tamu ita ce take tsayar da hankalinmu
ba tare da jin tsoro ko yin shakka ba. Ita ce take shiga ciki-ciki,
har bayan labulen nan na haikalin sama.[d] 20 Yesu kuwa wanda
shi ne na farkon da ya shiga wannan wurin, ya shiga a
madadinmu, ya kuma zama babban firist na har abada bisa ga
tsarin Malkizadek.

Tsarin Firist na Malkizadek

7 1 Wannan Malkizadek shi sarkin Salim ne, da kuma firist na
Allah Maɗaukaki. Ya sadu da Ibrahim a lokacin da Ibrahim
yake dawowa bayan ya ci nasara a yaƙin da ya yi da waɗansu
sarakuna. Da suka sadu, Malkizadek ya sa wa Ibrahim albarka,
2 Ibrahim kuwa ya ba shi kashi ɗaya bisa goma na kome. Da farko
dai, ma'anar sunan Malkizadek ita ce "Sarkin Adalci." Sa'an nan
kuma shi sarkin Salim[e] ne, wato, "Sarkin Salama." 3 Malkizadek

---

6.14: Far 22.16-17 **6.19:** L. Fir 16.2 **6.20:** Zab 110.4 **7.1:** Far 14.18-20

[d] **6.19 bayan labulen nan na haikalin sama:** Wato, ainihin wurin kasancewar Allah ke nan.

[e] **7.2 Salim:** Wato, Urushalima ke nan. A lokacin da Malkizadek yake mulkinsa, Urushalima tana hannun waɗanda ba Yahudawa ba, Isra'ila ba ta samu kasancewa ba tukuna.

kuwa ba shi da baba ko mama ko asali. Ba shi da ranar haihuwa ko ranar mutuwa. Amma kamar Ɗan Allah, shi firist ne har abada.

4 Ku dubi irin girman mutumin nan. Har Ibrahim kakan kakanninmu ya ba shi kashi ɗaya bisa goma na kayan da shi Ibrahim ya ƙwace a yaƙin da ya ci. 5 Bisa ga Doka, duk zuriyar Lawi waɗanda su firist ne sukan karɓa kashi ɗaya bisa goma daga hannun jama'a, wato, daga hannun 'yan'uwansu, ko da yake su ma zuriyar Ibrahim ne. 6 Amma Malkizadek, wanda asalinsa ba ɗaya ba ne da nasu, ya karɓi kashi ɗaya bisa goma a hannun Ibrahim, ya kuma albarkaci Ibrahim wanda shi ne aka yi masa alkawuran. 7 Ba shakka wanda yake sa albarka ya fi wanda yake karɓar albarka girma. 8 Ga shi ma firistoci na zuriyar Lawi, ko da yake su masu mutuwa ne, sukan karɓi kashi ɗaya bisa goma daga hannun mutane. Amma game da Malkizadek, wanda ya karɓi kashi ɗaya bisa goma a hannun Ibrahim, an ba da shaida cewa yana da rai. 9 Har ma ana iya ce Lawi da kansa, wanda zuriyarsa ce mai karɓar kashi ɗaya bisa goma, ya ba da nasa kashin ta hannun Ibrahim. 10 Ana iya faɗa haka domin a lokacin da Ibrahim ya sadu da Malkizadek ba a riga an haifi Lawi ba tukuna, amma yana cikin jikin kakansa.

Yesu Firist Ne bisa ga Tsarin Malkizadek

11 Ga shi, tsarin firistoci irin na zuriyar Lawi ya zo tare da Dokar da aka ba wa Isra'ilawa. Da a ce aikin firistoci na zuriyar Lawi yana iya kawo zaman cikakke, ai, da ba dalilin da wani firist dabam zai sāke zuwa, wanda yake bisa ga tsarin Malkizadek, ba bisa ga tsarin Harunaf ba. 12 Domin idan an canza tsarin firistoci, dole ne a canza dokar ma. 13 Shi wanda ake faɗa waɗannan abubuwan a kansa, wato, Ubangijinmu, ya fito daga wata kabila ne dabam. Ba ko ɗaya daga kabilarsa da ya taɓa yin hidima a matsayin firist. 14 Lallai Ubangijinmu ya fito daga kabilar Yahuda ne, wadda Musa, bai yi wani zance a kanta ba lokacin da yake magana game da firistoci.

15 Wannan magana ta ƙara fita a fili sosai sa'ad da wani firist dabam ya bayyana, wanda yake kamar Malkizadek. 16 Wannan kuwa ya zama firist ba bisa ga wata doka ko ƙa'ida game da zuriya ba, amma bisa ga ikon rai marar ƙarewa. 17 Gama an yi shaida game da shi cewa,

"Kai firist ne na har abada,

7.1-2: Far 14.17-20 7.5: L. Kid 18.21

f7.11 **Haruna:** Shi ne ɗan Lawi da ya zama firist na farì na Yahudawa.

bisa ga tsarin Malkizadek."

18 An ajiye Doka ta dā a gefe ke nan, domin ita marar iko da
marar amfani ce. 19 Dokar Musa ba ta isa ta sa wani abu yă zama
cikakke ba. Shi ya sa aka shirya abu mafi kyau wanda za mu sa
zuciya a kai domin mu matso kusa da Allah.

20 Allah ya tabbatar da wannan shirin tare da rantsuwa.
Sauran firistocin sukan shiga aikinsu ba tare da rantsuwa ba.
21 Amma wannan ya zama firist ne tare da rantsuwar da Allah
ya yi cewa,

"Ubangiji ya riga ya rantse,
ba zai kuma canza nufinsa ba,
'Kai firist ne na har abada.' "

22 Bisa ga wannan rantsuwar ne kuma Yesu ya zama mai tabbatar
da alkawari mafi kyau.

23 Firistoci irin na dā sun yi yawa domin mutuwa takan hana
su cin gaba da aikinsu. 24 Amma Yesu yana riƙe da matsayin
firist na har abada, domin shi da kansa yana nan har abada.
25 Saboda haka ya iya, yau da kullum, yă ceci[g] duk waɗanda
suke matsowa kusa da Allah ta wurinsa, domin yana nan da rai
har abada, yana kuma cin gaba da yin roƙo ga Allah saboda su.

26 Irin wannan babban firist ne muke bukata. Shi kuwa mai
tsarki ne, marar laifi ko zunubi, an keɓe daga masu zunubi, an
ɗaukaka kuma fiye da kome a sama. 27 Shi ba kamar waɗancan
manyan firistocin ba ne. Ba ya bukata yă riƙa miƙa hadaya
kullum, wato, yă fara miƙa saboda nasa zunubai kafin yă miƙa
saboda zunuban jama'a. Shi kam ya miƙa nasa hadaya sau ɗaya
tak, a lokacin da ya miƙa kansa. 28 Gama bisa ga Dokar Musa
akan zaɓe babban firist a tsakanin mutane masu kāsawa ne.
Amma alkawarin nan da Allah ya yi tare da rantsuwa, ya iso
ne bayan an ba da Doka. Bisa ga alkawarin nan ne aka naɗa
Dan wanda an mai da shi cikakke har abada.

Yesu Firist Ne na Alkawari Mafi Kyau

8 1 Kan maganarmu duka shi ne muna da babban firist wanda
yake zaune a hannun daman kursiyin Maɗaukaki a can sama.
2 Wannan babban firist kuwa yana hidimarsa a Wuri Mafi Tsarki,
a ainihin wurin kasancewar Allah wanda Ubangiji da kansa ne
ya kafa, ba mutum ba.

7.17: Zab 110.4 **7.21:** Zab 110.4 **7.27:** L. Fir 9.7 **8.1:** Zab 110.1

[g] **7.25 yau da kullum, yă ceci:** Wata fassara ta waɗannan kalmomi ita ce "cikakken ceto."

3 Akan naɗa kowane babban firist ne domin yă miƙa
baye-baye da hadayu. Haka kuma ya dace babban firist nan namu
yă kasance da abin da zai miƙa. 4 Da a ce yana nan a duniya ne
da bai zama firist ba ko kaɗan, domin dā ma akwai firistoci
waɗanda sukan miƙa baye-baye bisa ga umarnin Doka.
5 Firistocin nan kuwa sukan yi hidimarsu a cikin Wuri Mai Tsarki
wanda yake kamanni ne da kwatanci na wanda yake a sama.
Gama a lokacin da Musa zai kafa rumfan nan ta kasancewar
Allah, an yi masa gargaɗi cewa, "Ka tabbatar cewa ka shirya
kome da kome bisa ga kamannin da aka nuna maka a kan dutsen."
6 Amma yanzu an ba Yesu aikin firist wanda yake mafi kyau
kamar yadda alkawarin nan, wanda Yesu ne ya shirya a tsakanin
Allah da mutane, yake mafi kyau. Alkawarin nan kuwa mafi kyau
ne domin an kafa shi a kan abubuwan da sun fi kyau.

7 Da a ce alkawari na farko ba shi da kāsawa, ai, da ba dalili
a nemi wani mai biye da shi.8 Amma Allah ya gan laifin
mutanensa[h] da ya ce,

"Lokaci yana zuwa, in ji Ubangiji,
da zan shirya sabon alkawari da jama'ar Isra'ila tare da
jama'ar Yahuda.
9 Wannan ba zai zama kamar alkawarin da na yi da
kakanninsu ba,
a lokacin da na kama su a hannu na bi da su daga ƙasar
Masar.
Domin ba su yi aminci da alkawarina ba,
sai na ƴyale su, in ji Ubangiji.
10 Ga alkawarin da zan yi da jama'ar Isra'ila bayan lokacin
nan,
in ji Ubangiji.
Zan sa dokokina a cikin hankalinsu,
zan kuma rubuta su a zuciyarsu.
Zan zama Allahnsu,
su kuwa su zama mutanena.
11 Ba za su bukaci su koya wa juna ba,
ko kuwa wani ya ce wa ɗan'uwansa,
'Ka san Ubangiji,'
domin dukansu za su san ni,
daga mafi ƙanƙantansu zuwa mafi girma.

8.5: Fit 25.40

[h] **8.8 laifin mutanensa:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Ya ga laifi sai ya ce wa mutanensa" ne a nan.

12 Gama zan yafe laifofinsu,
ba zan kuwa ƙara tuna da zunubansu ba."

13 Da Allah ya yi magana haka game da sabon alkawari, ya mai da na farkon tsoho ke nan. Kuma kowane abin da yake iri na dā, da yake tsufa kuma, zai shuɗe ba da daɗewa ba.

Shirin Hadaya Irin na Tsohon Alkawari

9 1 To, alkawari na farko yana da ƙa'idodinsa na yin sujada,
da kuma wurin yin sujada wanda mutum ne ya shirya. 2 An
kafa rumfa wadda take da sashi na farko inda aka sa fitila, da
tebur, da burodin da aka keɓe. Wannan sashi kuwa shi ne ake ce
da shi Wuri Mai Tsarki. 3 Bayan labule na biyu[i] kuma akwai
sashin da ake ce da shi Wuri Mafi Tsarki. 4 A cikin wannan sashin
kuwa akwai bagaden da akan ƙona turare mai ƙamshi a kai, da
kuma akwatin alkawari. Waɗannan abu biyu kuwa an shafe su da
zinariya. A cikin akwatin nan na alkawari kuwa akwai kwanon
zinariya da manna a ciki, da sandan Haruna wanda ya fitar da
fure, da allunan dutse biyu na alkawari. 5 A bisan akwatin nan
kuwa akwai kerubobi na nuna ɗaukakar Allah,[j] waɗanda kuma
suke inuwantar da inda ake ce da shi wurin jinƙai.[k] Amma a
yanzu haka ba za mu iya yin magana dalla-dalla game da wannan
batu ba.

6 Bayan an shirya kome haka, sai firistoci kullum su riƙa
shiga a sashi na farko na rumfar, suna yin hidimarsu. 7 Amma
babban firist ne kaɗai yakan shiga sashi na biyun, yana kuma
shiga wannan wurin sau ɗaya tak a shekara.[ƙ] Ba ya shigowa sai
tare da jinin da zai miƙa saboda nasa zunubai, da kuma saboda
zunuban da jama'a suka aikata ba tare da saninsu ba. 8 Ta haka
Ruhu Mai Tsarki yana nuna cewa hanyar shiga ainihin Wuri
Mafi Tsarki bai buɗu ba tukuna muddin wancan wurin sujada
na farko yana nan tsaye. 9 Wannan kwatanci ne ga wannan

8.8-12: Irm 31.31-34 **9.2:** Fit 26.1-30; 25.23-40 **9.3:** Fit 26.31-33
9.4: Fit 30.1-6; 25.10-16; 16.33; L. Kid 17.8-10; Fit 25.16; M. Sh 10.3-5
9.5: Fit 25.18-22 **9.6:** L. Kid 18.2-6

[i] **9.3 Bayan labule na biyu:** An kira wannan haka domin akwai labule na farko wanda yake a sashi na farko.

[j] **9.5 kerubobi na nuna ɗaukakar Allah:** Waɗannan siffa biyu ne waɗanda aka yi su da kamannin mala'iku. Kowannensu yana da fikafikai biyu (Dubi Fit 25.18-20).

[k] **9.5 wurin jinƙai:** Wannan shi ne wurin da akan yafa jinin hadaya a Ranar Fansa. (Dubi L. Fir 16.14,15). A nan ne ɗaukakar Allah takan kasance (Dubi Fit 25.17-22).

[ƙ] **9.7 sau ɗaya tak a shekara:** Wato, a ranar Bikin Fansar da zunubai (Dubi L. Fir 16.29, 34).

zamani. Yana nuna cewa baye-baye da hadayu da akan miƙa ba
su isa su wanke zukatan masu sujada daga zunubansu ba.
10 Waɗannan sun shafi maganar ci da sha, da wanke-wanke iri-iri
ne, na al'adu. Su kuwa dokoki na halin jiki ne waɗanda aka
shimfiɗa kafin lokacin sabon tsari.

Jinin Almasihu Ne Isasshen Hadaya

11 Almasihu ya riga ya zo a matsayin babban firist, ya kawo
tsari mai kyau da muke da shi yanzu.[l] Ya shiga cikin rumfa mafi
girma, mafi kyau kuma, wadda ba mutum ne ya gina ba, wato,
ba irin ta wannan halitta ba. 12 Ya shiga wannan Wuri Mafi Tsarki
sau ɗaya tak. Bai shiga da jinin awaki ko na 'ya'yan shanu ba,
amma da nasa jini ne, wanda ya samo mana ceto na har abada.
13 Jinin awaki, da na bijimai, da tokar 'yar saniya da aka yayyafa
duk suna iya mai da masu rashin tsabta bisa ga al'ada su zama
da tsabta a jikinsu, 14 balle jikin Almasihu? Shi wanda ba shi da
wani zunubi, ya miƙa kansa ga Allah ta wurin Ruhun nan na har
abada, ai, ƙaramin abu ne jininsa yă iya wanke zukatanmu mu
bar al'adu marasa amfani domin mu bauta wa Allah mai rai.

An Cika Sabon Alkawari ta Mutuwar Yesu

15 Saboda haka Almasihu shi ne mai yin sulhu na sabon
alkawari[m] domin waɗanda aka kira su su karɓi gādo na har abada
wanda Allah ya yi alkawari. Wannan ya yiwu ne domin an riga
an yi mutuwa wadda take 'yantar da mutane daga zunuban da
suka yi a zamanin alkawari na farko. 16 Idan wani ya yi alkawari
game da gādonsa, dole ne a tabbatar da mutuwar wanda ya yi
alkawarin tukuna. 17 Domin alkawarin gādo ba shi da iko sai an
mutu, wato, ba ya ba da izni yayin da mai yinsa yana da rai.
18 Shi ya sa alkawarin nan na farko bai zama da iko ba sai da aka
zub da jini. 19 Bayan Musa ya sanar wa dukan jama'a kowane
umarnin da yake cikin Doka, sai ya ɗauki jinin 'ya'yan shanu, da
na awaki, ya haɗa da ruwa. Sa'an nan ya ɗauki ganyen izob tare
da jan gashin tumaki ya yayyafa jinin a kan littafin Doka da kuma
a kan dukan jama'a. 20 Sai ya ce, "Wannan shi ne jinin alkawari
wanda Allah ya umarce ku ku kiyaye." 21 Haka kuma ya yayyafa
jinin a kan rumfan nan, da kuma a kan dukan kayayyakin da akan

9.13: L. Fir 16.15-16; L. Kiɗ 19.9; 17-19 **9.19-20:** Fit 24.6-8

[l] **9.11 da muke da shi yanzu:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "mai zuwa" ne a nan.

[m] **9.15 mai yin sulhu na sabon alkawari:** Wato, mai shirya tsakanin mutane da Allah ke nan.

mora domin yin hidima. 22 Lallai, bisa ga Doka, kusan kowane
abu ne akan tsarkake da jini. Idan ba tare da zub da jini ba kuwa,
ba yadda za a gafarta zunubai.

23 Ya zama dole waɗannan al'adu su kasance haka don
tsarkakewar waɗannan abubuwa na duniya. Gama su kamannin
abubuwan da suke a sama ne. Ainihin abubuwa na sama kuwa
suna bukata hadayar da ta fi ta farkon kyau. 24 Gama Almasihu
bai shiga Wuri Mai Tsarki wanda mutum ne ya gina ba, wanda
yake kamanni ne kawai na ainihin wurin; a'a, sama ne da kansa
ya shiga, domin yă bayyana a gaban Allah a yanzu saboda mu.
25 Ba kuma wai ya shiga cikin sama domin ya riƙa miƙa kansa
a kullum ba, kamar yadda babban firist yakan shiga Wuri Mafi
Tsarki kowace shekara da jinin da ba nasa ba. 26 In da haka ne,
ai, da Yesu yana kan shan wuya kullum ke nan, tun daga lokacin
da aka halicci duniya. Ga shi kuwa ya bayyana sau ɗaya tak a
wannan ƙarshen zamani domin yă kawar da zunubai ta wurin
miƙa kansa. 27 Kamar yadda aka shirya wa ɗan Adam yă mutu
sau ɗaya tak, bayan haka sai shari'ar Allah, 28 haka kuma an
miƙa Almasihu sau ɗaya tak domin yă ɗauki zunuban mutane
da yawa. Shi kuwa zai sāke bayyana sau na biyu, ba domin yă
ɗauki zunubai ba, amma domin yă kawo ceto ga duk waɗanda
suke marmarin dawowarsa.

Alkawari Mafi Girma, Mafi Kyau

10 1 Doka kuwa kwatanci ce kawai na abubuwa masu kyau
waɗanda suke a gaba; ba ita ce ainihin abubuwan nan ba.
Shi ya sa ba ta isa ba, ta sa duk masu matsowa kusa da Allah su
zama daidai yadda Allah yake so bisa ga hadayun nan da akan
ci gaba da bayarwa shekara biye da shekara. 2 Da a ce Dokar tana
da iko ne, ai, da an daina miƙa hadayun nan, domin masu miƙa
su za su sami tsarkakewa gaba ɗaya, zuciyarsu kuwa ba za ta riƙa
dame su game da zunubansu ba. 3 Amma hadayun nan kuwa
hanyar tunawa da zunubi ne, shekara biye da shekara. 4 Gama ba
yadda zai yiwu jinin bijimai da na awaki yă kawar da zunubai.

5 Saboda haka, da Almasihu zai shigo duniya, ya ce:
"Hadayu da baye-baye kam ba ka so,
amma jiki ne ka shirya mini.
6 Hadayar ƙonawa da hadayar kawar da zunubai kuwa ba
ka jin daɗinsu.
7 Sai na ce, 'Ga ni nan, ya Allah, na zo in aikata nufinka,

9.21: L. Fir 8.15 9.22: L. Fir 17.11 9.28: Ish 53.12

kamar yadda yake a rubuce game da ni a Rubutaccen
Maganar Allah.' "

8 Da farko ya ce, "Hadayu, da baye-baye, da hadayar ƙonawa, da hadayar kawar da zunubai kam ba ka so, ba ka kuwa jin daɗinsu." Ya faɗa haka ko da yake Doka ce ta ce a kiyaye waɗannan umarnai. 9 Ya sāke cewa, "Ga ni nan, na zo in aikata nufinka." Wato, an ajiye tsari na farko a gefe ke nan domin a kafa na biyun. 10 Bisa ga nufin Allah kuma an mai da mu tsarkaka ta wurin hadayar jikinsa da Yesu Almasihu ya miƙa sau ɗaya tak ba ƙari.

11 Kowace rana kowane firist yakan tsaya yana yin hidimarsa, yakan yi ta miƙa irin wannan hadaya wadda ba ta da ikon kawar da zunubai. 12 Amma da Almasihu ya miƙa hadaya guda ta har abada saboda zunubai, sai ya zauna a hannun dama na Allah. 13 Tun lokacin nan kuwa yana jira ne a sa abokan gābansa a ƙarƙashin ƙafafunsa domin yă tattaka su. 14 Bisa ga hadayan nan guda ɗaya kuwa, ya mai da waɗanda aka tsarkake su zama cikakku har abada.

15 Ruhu Mai Tsarki ya ba mu shaida game da wannan. Da farko, ya ce,

16 "Ga alkawarin da zan yi da su,
bayan lokacin nan, in ji Ubangiji.
Zan sa dokokina a cikin zuciyarsu,
zan kuma rubuta su a hankalinsu."

17 Ya kuma ƙara da cewa,
"Ba zan sāke tuna da zunubansu ko laifofinsu ba."

18 Sa'ad da an gafarta zunubai kuwa, ba wata bukatar hadaya saboda zunubi.

Matsowa Kusa da Allah

19 Saboda haka, 'yan'uwana, muna da cikakken 'yanci mu shiga Wuri Mafi Tsarki bisa ga jinin Yesu. 20 Shi kuwa ya buɗe mana sabuwar hanya, hanya mai rai kuma, ta labulen nan, wato, jikinsa.

21 Muna kuma da babban firist wanda dukan jama'ar Allah take a hannunsa. 22 Saboda haka bari mu matso kusa da Allah da zuciya mai gaskiya, da bangaskiya marar shakka. Mu matso da zuciya wadda aka tsarkake daga alhakin zunubi, da jikin da aka wanke da ruwa mai tsabta. 23 Bari mu tsaya a kan sa zuciyan nan

10.5-7: Zab 40.6-8 **10.11:** Fit 29.38 **10.12-13:** Zab 110.1 **10.16:** Irm 31.33 **10.17:** Irm 31.34 **10.22:** L. Fir 8.30; Ez 36.25



Hoton Labulen da ya yage (10.20)

tamu, wadda muke shaida, da ƙarfi sosai domin shi wanda ya yi
mana alkawari mai aminci ne. 24 Mu lura da juna ta yadda za mu
iza juna ga nuna ƙauna da yin aikin nagarta. 25 Kada mu ƙyale
yin taron sujada, kamar yadda waɗansu sun saba yi. A maimakon
haka mu riƙa ƙarfafa juna, mu kuma ƙara yin haka saboda kuna
ganin cewa Ranan nan[n] tana kusatowa.

26 Ba wata sauran hadayar da za ta ɗauke zunubi idan mun
ci gaba da yin zunubi da gangan bayan mun sami sanin gaskiya.
27 A maimakon haka akwai hukuncin nan mai ban tsoro da wuta
mai tsananin zafi wadda za ta cinye masu ƙin Allah. 28 Duk wanda
ya ƙetare Dokar Musa akan kashe shi, ba tausayi, bisa ga shaidar
mutum biyu ko uku, 29 balle ma wanda ya rena Ɗan Allah, ya yi
banza da jinin alkawarin nan wanda ya tsarkake shi, ya kuma
zargi Ruhu Mai Tsarki! Wane irin hukunci mai tsanani ne kuke
tsammani ya yi daidai a yi wa wannan mutum? 30 Domin mun
san wanda ya ce, "Ramuwa tawa ce; ni zan rama." Ya sāke cewa,
"Ubangiji zai yi shari'ar mutanensa." 31 Abin ban tsoro ne fa
mutum yă fāɗa cikin hannayen Allah mai rai.

10.27: Ish 26.11 **10.28:** M. Sh 17.6; 19.15 **10.29:** Fit 24.8

[n] **10.25 Ranan nan:** Wato, ranar dawowar Ubangiji (Dubi 1 Tas 5.2,4; 2 Tas 1.10; 2.2; 2 Bit 3.10).

Masu Jimrewa Za Su Sami Lada

32 Ku tuna fa da kwanakin dā. Bayan da kuka sami ganin
hasken Allah, kun jimre sosai, kuna kokawa da wahaloli. 33 Wani
lokaci ana zaginku a fili, ana tsananta muku a gaban jama'a; wani
lokaci kuma kuna yarda ku haɗa kai da waɗanda suke shan irin
waɗannan wahaloli. 34 Gama kun nuna tausayi ga waɗanda suke
a kulle a kurkuku, kun kuma nuna farin ciki bayan an ƙwace
muku kaya, domin kun san cewa kuna da arziki mafi kyau da zai
dawwama har abada. 35 Saboda haka kada ku yar da ƙarfin
zuciyarku, domin zai kawo muku babban lada. 36 Ya kamata ku
jimre, domin ta yin haka ne za ku aikata nufin Allah, bayan haka
kuma ku karɓi abin da aka yi alkawari.

37 "Gama ba da daɗewa ba,
mai zuwan nan zai zo,
ba zai yi jinkiri ba.
38 Mutumina mai adalci zai rayu
ta hanyar bangaskiya,
Amma idan ya ja da baya,
raina ba zai ji daɗinsa ba."

39 Mu kam ba irin masu ja da baya zuwa ga halaka ba ne, mu dai
masu ba da gaskiya zuwa ga samun ceto ne.

Ma'anar Bangaskiya

11 1 Bangaskiya ita ce yin tabbaci a kan abin da muka sa
zuciya a kai, ita ce kuma kasancewa da tabbaci a kan abin
da ba ma iya gani. 2 Ta bangaskiya ne mutanen dā suka sami
yardar Allah. 3 Ta bangaskiya mun gane cewa bisa ga faɗin Allah
ne aka halicci dukan duniya, abin da ake gani kuwa ya fito ne
daga abin da ba a iya gani.

Jarumawan Bangaskiya

4 Ta bangaskiya ne Habila ya miƙa wa Allah hadayar da ta fi
ta Kayinu kyau. Ta yin haka ya sami yardar Allah cewa shi mai
adalci ne, domin Allah ya karɓi bayarwarsa. Habila kuwa ya
mutu, amma saboda bangaskiyarsa yana magana har yanzu.

5 Ta bangaskiya ne aka ɗauki Enok, shi kuwa bai mutu ba.
Ba a kuwa same shi ba, domin Allah ya riga ya ɗauke shi. Kafin
a ɗauke shi an ba da shaida cewa ya sami yardar Allah. 6 In ba
tare da bangaskiya ba, ba ya yiwuwa a sami yardar Allah, domin

---

10.30: M. Sh 32.35-36 **10.37-38:** Hab 2.3-4 **11.3:** Far 1.1; Zab 33.6,9; Yoh 1.3
11.4: Far 4.3-10 **11.5:** Far 5.21-24

dole ne duk mai matsowa kusa da Allah yă ba da gaskiya cewa Allah yana nan, yana kuma ba da lada ga duk waɗanda suke nemansa.

7 Ta bangaskiya ne Nuhu, bayan Allah ya yi masa gargaɗi a kan abubuwan da ba a gani ba tukuna, ya yi biyayya, ya shirya jirgin ruwa saboda ceton iyalinsa. Ta haka, ya sa an hukunta duniya, shi kuwa ya zama mai gādon adalci wanda yake samuwa ta bangaskiya.

8 Ta bangaskiya ne Ibrahim ya yi biyayya ya kama hanya zuwa wata ƙasa wadda aka yi masa alkawari cewa zai karɓi gādonta. Shi kuwa ya kama hanya ko da yake bai san inda za shi ba. 9 Ta bangaskiya ya zauna kamar baƙo a ƙasan nan da Allah ya yi masa alkawari. Yana zama a cikin rumfa, shi da Ishaku da Yakubu, waɗanda suka gāji alkawarin nan tare da shi. 10 Ya yi irin wannan zaman ne domin ya sa zuciya a kan birnin nan wanda yake da tushe, wanda Allah ne mai shirya, shi ne kuma mai gina shi.

11 Ta bangaskiya ne Ibrahim ya haifi ɗa, ko da yake ya tsufa sosai a lokacin, Saratu kuwa ba ta haihuwa.[o] Ya ba da gaskiya cewa Allah mai aminci ne cikin alkawarinsa. 12 Saboda haka, daga mutum ɗaya, wanda ya tsufa har ya kai ga bakin mutuwa, aka haifi zuriya masu yawa kamar taurarin sama, ko kuwa kamar yashi a bakin teku waɗanda suka gagari ƙirga.

13 Duk waɗannan sun mutu a cikin bangaskiyarsu. Ba su karɓi abubuwan da Allah ya yi alkawari ba, amma sun hangi abubuwan nan daga nesa, sun ji daɗi da ganinsu, sun kuma ba da shaida a fili cewa su baƙi ne, ba 'yan ƙasa ba, a duniya. 14 Waɗanda suna ba da irin wannan shaida suna nuna a fili ke nan cewa suna neman ƙasa ta kansu. 15 Da a ce suna ta tunani ne a kan ƙasar da suka bari a baya, ai, sun sami zarafin komawa. 16 Amma sun sa zuciya a kan ƙasa mafi kyau, wato ta sama, shi ya sa ba abin kunya ba ne ga Allah a ce da shi Allahnsu. Hakika, ya shirya birni saboda su.

17 Ta bangaskiya ne Ibrahim, a lokacin da aka gwada shi, ya miƙa Ishaku hadaya. Wato, yana a shirye yă miƙa makaɗaici ɗansa, 18 ko da yake ya karɓi alkawari cewa, "Ta wurin Ishaku

11.7: Far 6.13-22 **11.8:** Far 12.1-5 **11.9:** Far 35.27 **11.11:** Far 18.11-14; 21.2 **11.12:** Far 15.5; 22.17; 32.12 **11.13:** Far 23.4; 1 Tar 29.15; Zab 39.13 **11.17:** Far 22.1-14

[o] **11.11 Saratu kuwa ba ta iya haihuwa:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Bisa ga bangaskiya ne Saratu da kanta, ko da yake lokacin haihuwarta ya wuce, ta iya ta haifi 'ya'ya domin ta . . ."

ne za a lissafta zuriyarka." 19 Ibrahim kuwa ya yi tunani cewa
lallai ne Allah yana iya ta da matattu. Har ma, bisa ga misali,
muna iya cewa ya karɓi Ishaku daga matattu ne.
20 Ta wurin bangaskiya ne Ishaku ya albarkaci Yakubu da
Isuwa game da abubuwa masu zuwa.
21 Ta bangaskiya ne Yakubu, a lokacin da zai mutu, ya sa wa
kowane yaron Yusufu albarka, ya kuma yi sujada ga Allah yayin
da yake jingine a kan sandansa.
22 Ta bangaskiya ne Yusufu, a lokacin da ya kusa mutuwa,
ya yi magana game da fitowar Isra'ilawa daga ƙasar Masar, ya
kuma ba da umarni game da ƙasusuwansa.
23 Ta bangaskiya ne iyayen Musa suka ɓoye shi har wata uku
bayan haihuwarsa. Sun yi haka domin sun ga cewa yaron
kyakkyawa ne, ba su kuma ji tsoro game da umarnin sarki ba.
24 Ta bangaskiya ne Musa, da ya yi girma, ya ƙi a ce da shi
ɗan 'yar Fir'auna. 25 Ya zaɓi yă sha wahala tare da mutanen Allah
a maimakon yă ji daɗin zunubi na ɗan lokaci. 26 Domin yana sa
ido ga ladan da yake a gaba, ya ɗauka cewa cin mutuncin da aka
yi masa saboda Almasihu abu mai kyau ne fiye da dukiyar Masar.
27 Ta bangaskiya ne ya bar ƙasar Masar, ba tare da jin tsoron
fushin sarki ba. Ya tsaya da ƙarfi domin yana ganin wanda ido
ba ya iya gani. 28 Ta bangaskiya ne Musa ya kafa Bikin Ketarewa,
ya kuma yayyafa jini domin kada mai halakar da 'ya'yan farin
nan yă taɓa Isra'ilawa.
29 Ta bangaskiya ne Isra'ilawa suka ƙetare Jan Tekun nan, a
kan busasshiyar ƙasa. Amma da Masarawa suka yi ƙoƙari su haye,
sai ruwa ya kwashe su.
30 Ta bangaskiya ne katangar birnin Jeriko ta fāɗi bayan an
yi ta kewaye ta har kwana bakwai. 31 Ta bangaskiya ne Rahab
karuwan nan, ba ta halaka tare da marasa bangaskiya ba, domin
ta karɓi 'yan leƙen asirin ƙasan nan kamar abokai.
32 Me kuma zan ƙara cewa? Ba ni da zarafi in yi zance a kan
Gidiyon, da Barak, da Samsin, da Jefta, da Dawuda, da Sama'ila,
da kuma annabawa. 33 Ta bangaskiya ne waɗannan suka ci nasara
a kan mulkoki, suka aikata adalci, suka karɓi abubuwan da aka
yi alkawari, suka rurrufe bakunan zakuna, 34 suka tsai da ikon
wuta, suka tsere kaifin takuba. Suka mai da rashin ƙarfi yă zama

11.18: Far 21.12 **11.20:** Far 27.27-29,39-40 **11.21:** Far 47.31—48.20
11.22: Far 50.24-25; Fit 13.19 **11.23:** Fit 2.2; 1.22 **11.24:** Fit 2.10-12
11.27: Fit 2.15 **11.28:** Fit 12.21-30 **11.29:** Fit 14.21-31 **11.30:** Josh 6.12-21
11.31: Josh 2.1-21; 6.22-25 **11.32:** L. Mah 6.11—8.32; 4.6—5.31; 13.2—16.31;
11.1—12.7; 1 Sam 16.1—1 Sar 2.11; 1 Sam 1.1—25.1 **11.33:** Dan 6.1-27

da ƙarfi a gare su. Suka kori sojojin ƙasashe dabam-dabam.
35 Mata suka karɓi matattunsu waɗanda aka ta da su da rai. Aka
gwada wa waɗansu azaba, su kuwa suka ƙi a sake su, domin suna
nema su tashi daga matattu cikin rayuwa mafi kyau. 36 Waɗansu
suka sha ba'a da bulala, waɗansu kuwa suka sha ɗauri da sarƙa,
waɗansu aka jefa su a kurkuku. 37 Aka jejjefe su da duwatsu,[r]
aka yanka su kashi biyu da zarto aka kuma kakkashe su da takobi.
Fatun raguna da na awaki ne sukan sa, suna ta yawo. Suka yi
zama cikin rashi da tsanani da wulaƙanci. 38 Har ma duniya ba ta
isa su zauna cikinta ba. Sun yi ta yawo a wuraren da ba kowa,
da kuma kan duwatsu; suna kwana cikin kogwannin duwatsu, da
kuma cikin ramummukan da suke ƙarƙashin ƙasa.

39 Duk waɗannan Allah ya ba da shaida mai kyau game da
bangaskiyarsu, amma duk da haka ba su karɓi abin da aka yi
alkawari ba. 40 Allah dai ya shirya abu mafi kyau dominmu.
Nufinsa kuwa shi ne kada a kai su ga zaman cikakke idan ba tare
da mu ba.

Kafa Ido ga Yesu

12 1 Saboda haka, da yake taron shaidu masu yawa ƙwarai
sun kewaye mu, bari mu yar da dukan abin da zai hana
mu, da kuma kowane zunubin da ya riƙe mu kankan, bari kuma
mu yi tseren nan da yake a gabanmu tare da ƙarfin zuciya. 2 Mu
kafa ido ga Yesu wanda shi ne tushen bangaskiyarmu, da kuma
mai sa bangaskiyarmu ta zama cikakkiya. Saboda farin cikin da
aka sa a gabansa, ya jimre wa gicciye bai kuwa mai da shi wani
abin kunya ba, a yanzu kuma yana zaune a hannun daman
kursiyin Allah. 3 Ku lura fa da wannan mutumin da ya yi haƙuri
da irin ƙiyayyar da masu zunubi suka yi masa, don kada ku gaji,
ko kuwa ku fid da zuciya.

Horon Ubangiji Abin Amfani Ne

4 A cikin kokawar da kuke yi da zunubi bai kai yadda za ku
zub da jininku ba tukuna. 5 Ko kun mance ne da maganar
ƙarfafawa wadda Allah ya yi, wadda kuma take ce da ku
'ya'yansa?

"Ya ɗana, kada ka mai da horon Ubangiji abin banza,
kada ka fid da zuciya idan yana kwaɓe ka.

11.34: Dan 3.1-30 **11.35:** 1 Sar 17.17-24; 2 Sar 4.25-37
11.36: 1 Sar 22.26-27; 2 Tar 18.25-26; Irm 20.2; 37.15; 38.6. **11.37:** 2 Tar 24.21
[r] **11.37** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā sun ƙara "aka gwada su" a nan.

6 Domin Ubangiji yakan hori duk wadanda yake kauna,
yakan kuma hori duk dan da ya karba."

7 Ku jimre da wuyar da kuke sha, domin ana amfani da wuya
don horo ne. Ta haka, Allah yana yi da ku kamar 'ya'yansa ke
nan. Wane da ne babansa ba ya yi masa horo? 8 Idan ba a yi muku
horon nan da ake yi wa dukan 'ya'yan Allah ba, to, ku shegu ne
ke nan, ba 'ya'yan gida ba. 9 Ban da haka ma, muna da ubanninmu
na jiki wadanda suke yi mana horo, mu kuwa muna girmama su.
Ashe, ba za mu fi yarda da horon Ubanmu na ruhaniya, domin
mu rayu ba? 10 Ubanninmu na jiki sun yi mana horo na dan lokaci
ta hanyar da ta fi kyau a ganinsu, amma Allah yana yi mana horo
saboda amfaninmu ne, domin mu sami rabonmu cikin tsarkinsa.
11 Duk horon da akan yi mana yakan kawo zafi a lokacin, ba jin
dadi ba. Amma daga baya yakan kawo ribar adalci da salama ga
duk wadanda suka yi koyi da horon.

Gargadi a kan Kin Alherin Allah

12 Saboda haka, ku mike hannayenku da suka gaji, ku kuma
karfafa gwiwoyinku marasa karfi. 13 Ku bi hanyoyi masu kyau
domin kada kafafunku masu ciwo su dafa gurgunta, maimakon
su warke.

14 Ku yi iyakacin kokari ku zauna lafiya da kowa, ku kuma
zama da tsarki, domin ba wanda zai gan Ubangiji idan ba tare da
tsarki ba. 15 Ku lura fa kada kowa yă kāsa samun alherin Allah.
Ku yi hankali kada wani yă zama kamar tushen dacin rai wanda
yakan kawo barna, yă kuma lalatar da mutane da yawa. 16 Ku lura
fa kada kowa yă zama mai lalata, ko marar tsoron Allah kamar
Isuwa wanda ya sayar da gādonsa na dan fari saboda kwarya daya
tak na abinci. 17 Daga baya, kamar yadda kun sani, da ya so yă
karbi albarkan nan, sai aka ki shi; bai kuwa sami zarafin yin gyara
ba, ko da yake ya nemi albarkan nan da hawaye.

18 Ba ku zo ga Dutsen Sinai[5] wanda ana iya tabawa ba, ko
ga wuta mai ci sosai, ko ga duhu baki kirin, ko hadori, 19 ko
busar kaho, ko kuwa murya mai yin magana. Murya mai
maganan nan ta sa masu jinta suka yi roko cewa kada a ci gaba
da yin musu maganar. 20 Sun yi rokon ne domin ba su iya jimre
wa umarnin nan da aka bayar ba, cewa, "Ko dabba ce ta taba

12.5-6: Ayu 5.17; K. Mag 3.11-12 **12.12:** Ish 35.3 **12.13:** K. Mag 4.26
12.15: M. Sh 29.18 **12.16:** Far 25.29-34 **12.17:** Far 27.30-40
12.18-19: Fit 19.16-22; 20.18-21; M. Sh 4.11-12; 5.22-27

[5] **12.18 Dutsen Sinai:** Wato, inda Allah ya ba wa annabi Musa dokoki domin Isra'ilawa.

dutsen, sai a jejjefe ta har ta mutu." 21 Wannan abin da suka
gani ya zama abin ban tsoro ƙwarai, har ma Musa ya ce, "Jikina
yana rawa saboda tsoro."

22 Amma kun zo ga Dutsen Sihiyona[t] ne, da birnin Allah mai
rai, wato Urushalima ta sama, da taron farin ciki na mala'iku
masu ɗumbun yawa. 23 Kun zo ga jama'ar masu bi 'ya'yan fari
waɗanda sunayensu suna a rubuce a sama. Kun zo wurin Allah
wanda shi ne mai yi wa kowa shari'a, da wurin ruhohin mutane
masu adalci waɗanda aka mai da su cikakku. 24 Kun zo wurin
Yesu wanda shi ne mai yin sulhu na sabon alkawari, da kuma
wurin jinin nan da aka yayyafa wanda yake yin magana mafi kyau
fiye da jinin Habila.

25 Ku lura fa kada ku ƙi shi wanda yake magana. Ku sani, su
waɗanda suka ƙi su karɓi wanda ya yi musu gargaɗi a nan duniya
ba su tsira ba, balle fa mu! Ta yaya mu za mu tsira idan mun ƙi
wanda yake yi mana gargaɗi daga sama? 26 A lokacin kuwa
muryar Allah ta girgiza duniya. Amma yanzu ya yi alkawari cewa,
"Zan girgiza duniya sau ɗaya kuma, ba duniya kaɗai ba, amma
har da sama ma." 27 Wannan magana, "Sau ɗaya kuma," ta nuna
za a kawar da abin da aka girgiza, wato, za a kawar da abubuwan
da aka halitta, domin abubuwan da ba za a iya girgiza su ba su
kasance. 28 To, da yake za mu shiga mulkin da ba za a iya girgiza
ba, bari mu yi godiya, mu kuma miƙa wa Allah irin bautar da
yake so, a cikin tsoro da ban girma, 29 domin Allahnmu wuta ne
mai cinyewa.

Abubuwan da Allah Yake So

13 1 Ku ci gaba da nuna wa junanku ƙauna irin ta 'yan'uwa.
2 Kada ku daina yin alheri ga baƙi, domin ta yin haka
waɗansu suka yi wa mala'iku hidima, ba da saninsu ba. 3 Ku tuna
da waɗanda suke a ɗaure a kurkuku, kamar kuna a ɗaure tare da
su ne. Ku kuma tuna da waɗanda ake ba su wuya, kamar ku da
kanku ne kuke shan wuyar.

4 Zaman aure yă zama abin daraja gare ku duka. Alkawarin
aurenku yă tsaya da tsarki, domin Allah zai hukunta masu yin
zina da masu yin lalata. 5 Ku yi nesa da halin son kuɗi, kuma bari
abin da kuke da shi yă ishe ku. Ga shi kuwa Allah ya ce,

"Har abada ba zan bar ka ba,

12.20: Fit 19.12-13 **12.21**: M. Sh 9.19 **12.24**: Far 4.10 **12.25**: Fit 20.22
12.26: Hag 2.6 **12.29**: M. Sh 4.24 **13.2**: Far 18.1-8; 19.1-3

[t]**12.22 Dutsen Sihiyona**: Wannan wani suna ne na Urushalima.

sam-sam ba zan yar da kai ba."
6 Shi ya sa, ba tare da shakka ba, muna iya cewa,
"Ubangiji shi ne mai taimakona;
ba zan ji tsoro ba.
Mene ne mutum zai iya yi mini?"

7 Ku tuna da shugabanninku waɗanda suka yi muku maganar Allah. Ku dubi yadda suka yi rayuwarsu, da yadda ƙarshensu ya zama, ku kuma bi misalin bangaskiyarsu. 8 Yesu Almasihu kuwa ba ya canzawa, yadda yake jiya, haka yake yau, haka kuma zai zama har abada. 9 Kada sababbin koyarwa iri-iri su kwashe muku hankali. Ya dace ku sami ƙarfafawar zuciya bisa ga alherin Allah, ba ta wurin al'adu iri-iri na cin abinci ba. Waɗannan kam ba su da amfani ga masu kiyaye su.

10 Mu kuwa muna da wurin hadaya wanda firistocin rumfar sujada ta duniyan nan ba su da izni su ci daga bisansa. 11 Babban firist yakan kai jinin dabbobi zuwa Wuri Mafi Tsarki domin yă miƙa shi hadaya saboda zunubai, amma naman dabbobin nan kuwa akan ƙone ne a bayan gari. 12 Haka kuma Yesu ya sha azaba a bayan gari domin yă tsarkake mutane ta wurin nasa jini. 13 Saboda haka sai mu fita zuwa wurinsa a bayan gari, domin mu jimre da irin wulaƙancin da ya jimre da shi. 14 Domin ba mu da birni marar shuɗewa a nan duniya, amma mun dai sa ido ga birni wanda yake kan zuwa. 15 Bari kuma mu miƙa miƙa hadayar yabo ga Allah ta wurin Yesu. Yabonmu kuwa yă zama maganganu masu ba da shaida ga sunan Allah. 16 Kada ku daina yin alheri da taimakon juna, domin irin hadayun da Allah yakan ji daɗinsu ke nan.

17 Ku yi wa shugabanninku biyayya, ku kiyaye umarnansu kuma, domin su ne suke kula da rayukanku kamar waɗanda za su ba da lissafin aikinsu. Ku yi musu biyayya yadda zai sa aikinsu yă zama da farin ciki, ba da nauyin zuciya ba, domin wannan ba zai kawo muku wani amfani ba.

Bukatar Addu'a

18 Ku yi addu'a saboda mu. Mun tabbata cewa zuciyarmu ba ta damunmu game da wani laifi. Nufinmu shi ne mu aikata halin kirki cikin ayyukanmu duka. 19 Ina roƙonku musamman ku yi addu'a domin Allah ya sa in koma gare ku ba da daɗewa ba.

13.5: M. Sh 31.6,8; Josh 1.5 **13.6**: Zab 118.6 **13.11**: L. Fir 16.27

Karshen Magana

20-21 Allah ya ta da Yesu Ubangijinmu daga matattu ta wurin jinin alkawarin nan na har abada. Ta haka kuwa, Yesu ya zama Makiyayi Mai Girma na tumaki. Ina roƙon Allah mai ba da salama yă cika ku da kowane abu mai kyau domin ku yi nufinsa, yă kuma riƙa aikata abin da yake so a cikinku ta wurin Yesu Almasihu. Daukaka ta tabbata ga Almasihu har abada abadin. Amin.

22 Ina roƙonku, 'yan'uwana, ku yi haƙuri da wannan gargaɗina, domin ba wata doguwar magana ce na rubuta muku ba.

23 Ina so ku sani cewa an sake ɗan'uwanmu Timoti daga kurkuku. Idan ya zo da wuri, zan zo tare da shi in gan ku.

24 Ku gai da dukan shugabanninku, da dukan tsarkaka. 'Yan'uwanmu daga Italiya suna gaishe ku.

25 Alherin Allah yă tabbata a gare ku duka.

WASIKA TA YAKUBU

Gabatarwa

Yakubu shi ne marubucin wannan wasika (1.1). Ana tsammani ya rubuta ta tsakanin shekara ta A.D. 45 da 50 ne. A Sabon Alkawari akwai mutane masu sunan Yakubu har hudu, amma bincike ya nuna Yakubu da ya rubuta wannan wasikar shi ne Yakubu ɗan'uwan Yesu (Mat 13.35; Mar 6.3). Wannan Yakubu dabam ne da Yakubu ɗan Zabadi ɗaya daga cikin sha biyun nan wanda sarki Hiridus ya kashe a shekara ta A.D. 44 (A.M. 12.2). Yakubu ya zama shugaban jama'ar masu bi a Urushalima (A.M. 12.17; 15.13; 21.18; Gal 1.9, 12). A ƙarshe aka kashe shi a shekara ta A.D. 64.

Wasika ta Yakubu tana bayyana yadda ya kamata rayuwar masu bi ta yau da kullum ta kasance. Ta bayyana dangantakar da take tsakanin bangaskiya da ayyuka. Ta nuna yadda bangaskiya ta ainihi takan haifar da ayyuka da kuma halaye masu kyau. Ta kuma tsawata a kan ɓarnar harshe da kuma nunan bambanci. Wasikar ta bayyana cewa zaman abokin duniya gāba ce da Ubangiji. A ƙarshe ta ƙarfafa masu bi su rika haƙuri suna kuma addu'a a cikin kome.

Abubuwan da Suke Ciki

Gaisuwa 1.1
Bangaskiya da hikima 1.2-8
Arziki da talauci 1.9-11
Wahala da jarrabawa 1.12-18
Ji da aikata maganar Allah 1.19-27
Tsawatawa a kan nunan bambanci 2.1-13
Bangaskiya da ayyuka 2.14-26
Mai bi da harshensa 3.1-18
Zaman abokin duniya 4.1—5.6
Wadansu gargadi 5.7-20

Gaisuwa

1 [1] Daga Yakubu bawan Allah da kuma na Ubangiji Yesu Almasihu, zuwa ga kabila goma sha biyun nan da suka bazu ko'ina cikin duniya. Gaisuwa mai yawa.

1.1: Mat 13.55; Mar 6.3; A.M 15.13; Gal 1.19

Bangaskiya da Hikima

2 'Yan'uwa, ku mai da kowace irin wahalar[a] da ta same ku
abin farin ciki, 3 gama kun san wahalan nan takan gwada
bangaskiyarku ne, don ta sa ku ku cika da haƙuri. 4 Sai ku bar
haƙurinku yă cika aikinsa, ya kai ku ga zaman natsatsu da cikakku
har kada ku rasa kome. 5 In waninku yana bukatar hikima, sai yă
roƙi Allah wanda yake ba wa kowa hannu sake ba tare da gori
ba, zai kuwa ba shi. 6 Amma sai yă roƙa da bangaskiya, ban da
shakka, don duk mai shakka yana kama da raƙuman ruwan teku
wadanda iska take hurawa tana jujjuyesu ta ko'ina. 7-8 Kada irin
mutumin nan da yake mai zuciya biyu wanda ba ya ajiye
hankalinsa waje ɗaya a cikin dukan ayyukansa yă yi tsammani
zai sami wani abu daga wurin Ubangiji.

Arziki da Talauci

9 Bari ɗan'uwan da yake matalauci yă yi taƙama a kan cewa
Allah ya ɗaukaka shi. 10 Haka ma wanda yake mai arziki yă yi
taƙama a kan cewa Allah ya ƙasƙanta shi. Gama mai arziki zai
bushe kamar furen ciyawa. 11 Gama in rana ta fito ta yi zafi
ƙwarai, takan sa ciyawa ta bushe, sai furenta yă fadi, kyanta kuma
ta ɓace. Haka ma mai arziki zai mutu cikin kai da kawowarsa na
kasuwanci.

Wahala da Jarabawa

12 Mai albarka ne mutumin da ya jimre cikin wahalarsa, domin
zai karɓi lada na rai madawwami[b] wanda Allah ya yi alkawari zai
ba wa dukan masu ƙaunarsa. 13 Idan jaraba ta same mutum, kada
yă ce, Allah ne ya jarrabce shi. Domin Allah ba ya jarabtar kowa
da mugunta, kuma ba ya yiwuwa a jarabce shi. 14 Mutum dai yakan
fāɗi cikin jaraba sa'ad da mugun kwaɗayinsa ya rude shi, ya kuma
sha kansa. 15 Mugun kwaɗayi kuwa in ya yi ciki yakan haifi zunubi.
Zunubi in ya yi girma yakan haifi mutuwa.

16 'Yan'uwana wadanda nake ƙauna, kada ku yarda a rude
ku. 17 Kowace baiwa mai kyau, da kowace cikakkiyar kyauta daga
sama suke. Sun sauko ne daga wurin Allah Uba wanda ya halicci
rana, da wata, da taurari duka[6]. Shi kuwa ba ya canzawa, babu

1.10-11: Ish 40.6-7

[a] **1.2 kowace irin wahala:** Da Helenanci an rubuta "Abin da kuna fāɗi a ciki" ne a nan.

[b] **1.12 lada na rai madawwami:** Da Helenanci an rubuta "kambin rai" ne a nan.

[6] **1.17 Allah Uba wanda ya halicci rana, da wata, da taurari duka:** Da Helenanci an rubuta "Uban Haskoki" ne a nan.

kuma alamar duhu gare shi.[c] 18 Bisa ga nufinsa Allah ya ba mu
rai ta wurin maganarsa mai gaskiya domin yă sa mu a matsayi
mafi daraja cikin halittarsa.

Ji da Aikata Maganar Allah

19 'Yan'uwana, wadanda nake ƙauna, ku sani fa ya kamata
kowa yă kasance mai saurin ji, amma ba mai saurin magana ko
mai saurin fushi ba. 20 Saboda fushin mutum ba ya kai shi ga
aikata abubuwa masu kyan da Allah yake so. 21 Sai ku watsar da
ƙazamin halin nan na zunubi da kuma kowace irin mugunta. Sa'an
nan a cikin saukinkai ku karɓi maganan nan da aka shuka a
zuciyarku, wadda kuma tana iya kai ku ga ceto.

22 Kada ku rudi kanku, kuna jin maganar Allah kawai; a
maimakon haka, ku zama masu aikatawa kuma. 23 Domin duk
wanda yake jin maganar kawai amma ba ya aikatawa yana kama
da mutumin da ya dubi fuskarsa a madubi; 24 bayan ya tashi daga
wurin, nan da nan sai yă manta da yadda fuskarsa take. 25 Amma
mutumin da ya mai da hankalinsa wajen bincike koyarwar bishara
wadda ita ce cikakkiyar ƙa'idan nan mai kawo 'yanci, har bai zama
mai ji kawai yă manta ba, amma ya zama mai yi wanda ya nace
yana aikatawa, za a sa masa albarka cikin komen da yake yi.

Addini na Gaskiya

26 Idan wani yana tsammani shi mai addini ne sosai, amma
ba ya kame bakinsa, to, yana rudin kansa ne, addininsa kuma
banza ne. 27 Addinin da Allah Uba ya tabbatar mai tsarki, kuma
na gaske, shi ne: a kula da matan da mazansu suka mutu, da kuma
marayu cikin shan wuyarsu, a kuma kebe kai daga muguwar
rayuwa ta duniya.

Tsawatawa a kan Nunan Bambanci

2 1 'Yan'uwana, kada ku nuna bambanci a tsakaninku, da yake
kun sa bangaskiyarku ga Ubangijinmu Yesu Almasihu,
wanda yake Ubangiji Madaukaki. 2 Misali, idan wani mai arziki
ya shigo cikin taronku yana sanye da zoben zinariya, da kuma
riguna masu daraja, sa'an nan kuma wani matalauci ya shigo da
riga da ta yayyage, 3 za ku fi ba wa mai arzikin nan girma ku ce
masa, "Ga kujera mai kyau ka zauna," amma ku ce wa matalaucin
nan, "Ka tsaya can," ko kuma "Ka zauna a ƙasa"? 4 Ai, bambanci

[c] **1.17 Babu kuma alamar duhu gare shi:** Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "ba ya kawo duhu ta dalilin juyawa" ne a nan.

ke nan kuke nuna wa junanku, kuna kuma yanke hukunci da mugayen tunani.

5 Ku ji, 'yan'uwana waɗanda nake ƙauna! Ashe, Allah bai zaɓi matalautan duniyan nan su zama masu arziki cikin bangaskiya ba? Ba su ne kuma za su gāji mulkin nan wanda ya yi wa waɗanda suke ƙaunarsa alkawari ba? 6 Amma ku, kukan rena matalauta. Ashe, ba masu arziki ne suke wulaƙanta ku ba? Ba su ne suke jan ku zuwa gaban kotu ba? 7 Ba su ne kuma suke maganar reni a kan sunan nan mai daraja da aka san ku da shi ba?

8 Zai yi kyau idan kun yi biyayya da dokan nan ta mulkin Allah da take a rubuce cikin Rubutaccen Maganar Allah cewa, "Ka ƙaunaci abokin zamanka kamar kanka." 9 Amma idan kuna nuna bambanci a tsakaninku, wannan zunubi ne. Bisa ga Dokar Musa kun zama masu karye doka. 10 Don duk wanda ya kiyaye dokoki duka amma ya karye ɗaya, to, ya karye dukansu ke nan. 11 Domin shi wanda ya ce, "Kada ka yi zina" shi ne kuma ya ce, "Kada ka yi kisankai." Idan ba ka yi zina ba, amma ka kashe wani, to, ka riga ka zama mai karye dokar Allah ke nan. 12 Ku yi maganarku da aikinku ta hanyar da zai nuna cewa ku mutane ne da za a yi musu shari'a bisa ga ƙa'ida mai ba da 'yanci. 13 Gama a lokacin hukunci, Allah ba zai nuna jinƙai ga mutum marar jinƙai ba. Amma jinƙai za ta yi nasara a kan hukunci.

Bangaskiya marar Ayyuka Banza Ce

14 'Yan'uwa, ina amfani wani yă ce yana da bangaskiya idan ayyukansa ba su nuna haka ba? Anya! Wannan bangaskiyarsa za ta iya cece shi kuwa? 15 Misali, waɗansu 'yan'uwa maza ko mata ba su da riga da abinci na yau da kullum, 16 sai waninku ya ce musu, "Ku sauka lafiya, Allah ya ba ku abinci da abin sutura," amma bai yi kome game da bukatarsu nan ta jiki ba. To, ina amfanin wannan? 17 Haka kuma bangaskiya wadda ba ta da ayyukan da suke tabbatar da ita, banza ce.

18 Wani zai iya cewa, "Ai, kai kana da bangaskiya, ni kuma ina da ayyuka ne." To, nuna mini bangaskiyarka marar ayyuka, ni kuma zan nuna maka bangaskiyata ta wajen ayyukana. 19 Ka gaskata Allah ɗaya ne? To madalla. Ai, ko aljanu ma sun gaskata haka, har ma da rawar jiki. 20 Kai wawa! Ko kana bukata har yanzu in gaya maka yadda bangaskiya marar ayyuka banza ce? 21 Sa'ad da kakanmu Ibrahim ya bayar da ɗansa Ishaku a kan bagaden hadaya, ba saboda

2.8: L. Fir 19.18 **2.11:** Fit 20.13,14; M. Sh 5.17,18 **2.19:** M. Sh 16.4

ayyukansa ne aka shaida shi mai adalci ba? 22To, ka gani yadda
bangaskiyarsa tana tafiya tare da ayyukansa, kuma bangaskiyarsa
ta zama cikakkiya ta wajen ayyukansa. 23A nan aka cika
Rubutaccen Maganar Allah cewa, "Ibrahim ya gaskata da Allah,
kuma saboda bangaskiyarsa Allah ya lissafta shi mai adalci." Ta
dalilin haka kuwa aka ce da Ibrahim abokin Allah. 24Kun gani,
ashe, mutum yana samun zaman marar laifi a gaban Allah saboda
ayyukansa ne, ba saboda bangaskiya ita kadai ba.

25 Haka yake kuma da karuwan nan Rahab a lokacin da ta
6oye 'yan leken asirim kasan nan, ta kuma taimake su sun tsira
ta wata hanya dabam. Ba ta wurin ayyuka ne ta zama mai adalci
ba? 26Saboda haka kamar yadda jikin mutumin da ba shi da rai
gawa ne, haka bangaskiya marar ayyuka take daidai da gawa.

Mai Bi da Harshensa

3 1 'Yan'uwana, kada yawancinku su so zaman masu koyarwa,
domin kun san cewa mu da muke koyarwa za a yi mana
shari'a mafi tsanani fiye da ta sauran mutane. 2Don dukanmu
mukan yi kuskure da yawa. Idan kuwa wani ba ya kuskure a
maganarsa, to, lallai shi cikakke ne, mai iya lura da jikinsa gaba
daya. 3Mukan sa wa doki linzami a baki don yă yi biyayya da
mu. Ta haka mukan iya bi da shi zuwa inda muke so.



Hoton doki da linzami a baki (3.3)

2.21: Far 22.1-14 **2.23:** Far 15.6; 2 Tar 20.7; Ish 41.8 **2.25:** Josh 2.1-21

4 Ku duba jiragen ruwa ku gani. Ko da yake su manya ne,
kuma iska mai ƙarfi ce take tafiyar da su, duk da haka da ɗan
ƙaramin sandan tuƙi ne mai tuƙan jirgin yakan iya juya jirgin
zuwa ko'ina da yake so. 5 Haka ma harshen mutum yake. Ko da
yake shi ɗan ƙarami ne cikin gaɓoɓin jiki duk da haka yana cike
da buri a kan manyan abubuwa.

Ku dubi yadda ƙankanuwar wuta takan iya ƙone daji ƙurmus!
6 Ai, harshen mutum wuta ne, duniya ne na mugunta cikin
jikinmu! Yana kuma ɓata mutum gaba ɗaya. Harshe kuma yakan
lalatar da mutum a cikin dukan hanyar rayuwarsa. Shi kuwa,
gidan wuta ne yake zuga shi. 7 Mutum yana iya shan kan kowace
dabba, har ma ya riga ya sha kan dabbobi. Wannan ya haɗa da
namomin daji, da tsuntsaye, da namomi masu rarrafe, da kuma
kifaye. 8 Amma ba wanda ya taɓa iya shan kan harshensa. Harshe
mugun abu ne marar hutu, kuma yana cike da dafi mai kashewa.
9 Da shi muke yabon Ubangijinmu wanda yake Ubanmu, da shi
kuma muke zagin mutane waɗanda Allah ya yi cikin kamanninsa.
10 Da baki guda muke yabo, da shi kuma muke zagi. Haba,
'yan'uwana! Ai, bai kamata yă kasance haka ba. 11 Ko rijiya ɗaya
za ta iya ba da ruwa mai daɗi tare da ruwa mai ɗaci daga wuri
guda? 12 'Yan'uwana, itacen ɓaure zai iya ba da 'ya'yan zaitun,
ko itacen inabi yă ba da 'ya'yan ɓaure? Ta haka kuma rijiya mai
ba da ruwan gishiri ba zai ɓullo da ruwa mai daɗi ba.

Hikima ta Gaske

13 Wane ne mai hikima da ganewa a cikinku? Sai yă nuna ta
ta wajen yin rayuwa mai kyau, da kuma aiki mai kyan da yake
yi cikin saukinkai da ake samu ta wurin hikima. 14 Amma idan a
zuciyarku kuna da tsananin kishi da ƙiyayya da kuma sonkai, to,
ku bar yin yanga kuna danne gaskiya. 15 Wannan hikima ba irin
wadda take saukowa daga sama ba ce, ta duniya ce. Kuma ba ta
ruhaniya ba ce, amma ta Shaiɗan ce. 16 Gama duk inda ake kishi
da sonkai, to, akwai kowace irin rigima da mugunta a wurin.
17 Amma hikimar da take daga wurin Allah, da farko dai mai
tsarki ce, kuma mai kawo salama ce, mai hankali ce, mai saukin
kai ce, mai yawan tausayi ce, mai yawan alheri ce. Ba ta nuna
bambanci ko munafunci. 18 Rayuwa mai kyau ita ce amfanin da
akan girbe daga irin da masu kawo salama sukan shuka cikin
salama.

3.9: Far 1.26

Zama Abokin Duniya

4 [1] Mene ne yake kawo faɗa da jayayya tsakaninku? Ba shakka suna zuwa ne ta dalilin kwaɗayi iri-irin da suke yaƙi a cikinku. [2] Kukan nemi abu ku rasa, sai ku yi kisankai. Kukan nemi abu da tsanani, ku kāsa samu, sai ku shiga faɗa da jayayya. Ai, ba kwa samun abin da kuke nema saboda ba kwa addu'a ne. [3] Kuma lokacin da kukan roƙa ba kwa samu don kukan roƙa da mugun nufi. Kuna so ku kashe abin da kun samu a kan ayyukan banza na jin daɗin jikinku ne. [4] Ku marasa aminci! Ba ku sani ba cewa zama abokin duniya yana daidai da gāba da Allah? Gama duk mai ƙaunar duniya, ya mai da kansa mai gāba da Allah ke nan. [5] Ko kuna tsammani a banza ne Rubutaccen Maganar Allah ya ce, "Allah yana cike da tsananin kishi[d] a kan ruhun da ya sa a cikinmu?" [6] Amma Allah yana ƙara mana alherinsa mai yawa, shi ya sa maganarsa ta ce, "Allah yana ƙin mai girmankai, amma yana yin alheri ga wanda ya ƙasƙantar da kansa."

7 Don haka sai ku miƙa kanku ɗungum ga Allah. Ku ƙi Shaiɗan, shi kuwa zai guje muku. [8] Ku yi kusa da Allah, shi kuwa zai yi kusa da ku. Ya ku masu zunubi, ku gyara ayyukanku[d] su zama da tsarki. Ku munafukai kuma, ku tsarkake zukatanku. [9] Ku yi baƙin ciki, ku yi kuka, ku yi hawaye. Bari dariyarku ta koma kuka, farin cikinku kuma yă koma baƙin ciki. [10] Ku ƙasƙantar da kanku a gaban Ubangiji, shi kuwa zai ɗaukaka ku.

Kada A Ɗora wa Ɗan'uwa Laifi

11 'Yan'uwa, ku bar yin wa juna zargi. Saboda duk wanda yake zargin ɗan'uwansa mai bi, ko kuwa yana ɗora masa laifi, yana zargin Dokar Allah ke nan, yana kuma ɗora wa Dokar Allah laifi ne. Gama idan ka zargi Dokar Allah ka zama marar biyayya da ita ke nan. Sa'an nan kuma ka mai da kanka mai ɗora mata laifi. [12] Allah ne kaɗai mai ba da doka, shi ne kuma mai yin shari'a. Shi kaɗai yake ba da ceto, kuma shi yake da iko yă halaka. Saboda haka, wane ne kai da har ka isa ka ɗora wa ɗan'uwanka laifi?

4.6: K. Mag 3.34

[d] **4.5** Waɗansu littattafai suna da wannan ayar kamar haka "Ruhun da Allah ya sa a cikinmu yana cike da soyayya mai tsanani." Waɗansu kuma suna da "Ruhu Mai Tsarkin da Allah ya sa a cikinmu yana cike da ƙaunarmu sosai."

[d] **4.8 ku gyara ayyukanku:** Da Helenanci an rubuta "Ku tsabtace hannayenku" ne a nan.

Kada A Yi Taƙama da Gobe

13 Ku saurara, ku da kuke cewa, "Yau ko gobe za mu tafi
gari kaza, mu yi shekara guda muna ta kasuwanci muna cin riba."
14 Ga shi nan kuwa ba ku ma san me zai faru gobe ba. Shin, wai
mene ne ma ranku? Ai, abu ne kamar hazo wanda yake bayyana
a ɗan lokaci kaɗan sa'an nan yă ɓace. 15 Ya kamata ku ce, "Idan
Allah ya yarda, idan kuma muna cikin masu rai, za mu yi kaza
da kaza." 16 Amma ga shi yanzu kuna ɗaga kai, kuna yanga. Ai,
wannan irin ɗaga kai ba shi da kyau.
17 Saboda haka duk wanda ya san abin da ya kamata ya yi
amma ya ƙi yi, wannan zunubi ne gare shi.

An Tsawata wa Masu Arziki

5 1 To, ku saurara ku masu arziki! Ku yi kuka da ihu saboda
azaba da take zuwa kanku. 2 Arzikinku duka zai ruɓa, kuma
ƙwari za su cinye tufafinku. 3 Zinariyarku da azurfarku sun yi
tsatsa. Tsatsan nan da suka yi ita ce za ta zama shaida a kanku,
wadda za ta cinye ku kamar wuta. Kun dai tara wa kanku dukiya[e]
a kwanakin nan, waɗanda suke kwanakin ƙarshe. 4 Gama albashin
ma'aikatan gonakinku, waɗanda kuka ƙi biyansu saboda halin
cutarku, yana kuka ga Allah. Haka nan kukan masu yin muku
girbi a gonakinku ya kai wurin Allah, Ubangiji Mai iko duka.
5 Kun yi zama a duniya cikin jin daɗi, kuna ci da sha na ganin
dama. To, kun yi wa kanku kiwo ne kuna zaman jira ranar yanka.
6 Kun hukunta marasa laifi, kuka kuma kashe su ba su kuwa yi
gāba da ku ba.

Haƙuri da Addu'a

7 Saboda wannan, 'yan'uwa, ku yi zaman haƙuri har sai
Ubangiji ya dawo. Ku dubi irin haƙurin da manomi yakan yi
lokacin da yake jira gonarsa ta ba da amfani mai kyau. Da
yawan haƙuri yakan jira ruwan shuki da na baya. 8 Sai ku ma
ku zauna da haƙuri. Ku ƙarfafa zuciyarku, domin zuwan
Ubangiji ya yi kusa.
9 'Yan'uwa, ku bar yin gunaguni da juna, don kada a
hukunta ku. Ga shi mai hukunci ya kusan zuwa, har yana a
bakin ƙofa. 10 'Yan'uwa, ku bi gurbin annabawan da suka yi
magana da sunan Ubangiji. Ku yi koyi da jimrewarsu cikin

4.13-14: K. Mag 27.1 **5.2-3:** Mat 6.19 **5.4:** M. Sh 24.14-15

[e] **5.3 Kun dai tara wa kanku dukiya:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "Za ta ci naman jikinku, tun da yake kun tara wuta" ne a nan.

wahala. 11 Gama mukan ce da waɗanda suka jimre masu murna ne. Kun dai ji irin haƙuri na Ayuba, kun kuma san yadda Ubangiji ya albarkace shi a ƙarshe. Saboda shi Ubangiji mai jinƙai ne, mai yawan tausayi kuma.

12 Fiye da kome dai, 'yan'uwana, kada ku yi rantsuwa ko kaɗan in kuna yin alkawari. Kada ku yi rantsuwa da sama, ko da ƙasa, ko a kan wani abu. Sai dai ku ce, "I" kawai, in kuna nufin "I", ko kuwa ku ce, "A'a" kawai, in kuna nufin "A'a" don kada ku shiga hukuncin Allah.

13 Ko akwai wani a cikinku wanda yana cikin wata wahala? To, sai yă yi addu'a. Ko akwai wani mai murna? To, sai yă yi waƙoƙin yabo. 14 Akwai mai rashin lafiya a cikinku? Sai yă kira dattiban jama'ar masu bi su yi masa addu'a, suna shafe shi da mai a cikin sunan Ubangiji. 15 Irin wannan addu'ar da aka yi cikin bangaskiya za ta warkar da marar lafiyar. Ubangiji kuma zai warkar da shi. In kuma ya yi zunubi, za a gafarta masa.

16 Saboda haka ku dinga faɗa wa juna laifofinku, kuna wa juna addu'a, domin a warkar da ku. Addu'ar mai adalci tana aiki da iko sosai. 17 Iliya mutum ne kamar mu. Ya nace sosai cikin addu'a kada a yi ruwan sama , sai kuwa ba a yi ruwa a ƙasar ba har shekara uku da wata shida. 18 Bayan haka ya sāke yin addu'a, sai ruwa ya fādī daga sama, ƙasa kuma ta ba da amfani.

19 'Yan'uwana, idan ɗaya daga cikinku ya bar hanyar gaskiya, sai waninku ya dawo da shi kan hanya, 20 sai yă sani fa duk wanda ya dawo da mai zunubi a kan hanya ya ceci ran mai zunubin daga mutuwa, kuma zai zama hanyar gafarta zunubai masu ɗumbun yawa.

5.11: Ayu 1.21-22; 2.10; Zab 103.8 **5.12:** Mat 5.34-37 **5.14:** Mar 6.13
5.17: 1 Sar 17.1; 18.1 **5.18:** 1 Sar 18.42-45 **5.20:** K. Mag 10.12; 1 Bit 4.8

WASIKA TA FARKO TA

BITRUS

Gabatarwa

Manzo Bitrus ne ya rubuta wannan wasiƙar a tsakanin shekara ta A.D. 60-69, zuwa ga masu bi waɗanda suke a warwatse a wurare dabam-dabam saboda tsananin da suka sha daga hannun wani sarkin Roma mai suna Kaisar Nero.

An rubuta wannan wasiƙa domin a gargaɗe masu bi su tsaya da ƙarfi sosai, su kuma yi haƙuri cikin wahalolinsu.

Wasiƙar tana koyarwa cewa ya kamata masu bi su yi zaman adalci, su kuma sa zuciyarsu a kan Yesu, komene ne ya same su ta hannun 'yan Adam (2.20-21). Su kasance da tsarki, su riƙe bangaskiyarsu sosai ko cikin daɗi ko cikin wahala. Wasiƙar ta kuma nuna yadda ya kamata masu bi su kasance da halin tawali'u da yin hidima ga Allah da kuma junansu.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-2
Ceton Allah a lokacin wahala 1.3-12
A kasance da tsarki 1.13—2.10
Zaman masu bi a lokacin azaba 2.11—4.19
Halin tawali'u da yin hidima 5.1-11
Maganar ƙarshe 5.12-14

Gaisuwa

1 [1] Daga Bitrus, manzon Yesu Almasihu, zuwa ga mutanen Allah waɗanda ya zaɓa, waɗanda suke zaman baƙunci, a warwatse kuma, a ƙasashen Fontus, da Galatiya, da Kafadokiya, da Asiya, da kuma Bitiniya, [2] wato, ku da Allah Uba ne ya zaɓe ku bisa ga shirinsa; ya kuma keɓe ku ta wurin tsarkakewa na Ruhu Mai Tsarki. Nufinsa ne ku yi wa Yesu Almasihu biyayya, ku kuma sami amfanin yafawar jininsa.[a]

Bari Allah yă ƙara muku alheri da kwanciyar rai a yalwace.

---

[a] **1.2 ku kuma sami amfanin yafawar jininsa:** Da Helenancin an rubuta: "Ta wurin yafawar jininsa" ne a nan.

Allah Ya Ba da Abin Sa Zuciya

3 Bari mu gode wa Allah wanda shi ne Uban Ubangijinmu
Yesu Almasihu! Shi ne ya ji tausayinmu sosai, ya sāke rayar da
mu ta wurin tashin Yesu Almasihu daga matattu. Wannan ya sa
muna da rayayyiyar sa zuciya. 4 Ta haka muna sa rai ga samun
abin da Ubangiji ya ajiye a sama don 'ya'yansa. Ajiyan nan kuwa
ba za ta lalace ba, ba za ta ɓaci ba, ba za ta kuwa shuɗe ba.
5 Gādonku ke nan, ku da Allah cikin ikonsa yana kiyaye ku ta
wurin bangaskiya. Nufinsa ne ku kai ga ceton nan da ya shirya
zai bayyana a ƙarshen zamani.

6 A kan wannan dai, ku yi farin ciki sosai, ko da yake yanzu
cikin ɗan lokaci kaɗan kuna da baƙin ciki domin gwaje-gwaje
iri-irin da kuke ciki. 7 Dalilin wannan shi ne don a tabbatar da
bangaskiyarku. A wuta ne mutane sukan gwada zinariya, abu
wanda ya zama mai ƙarewa. Haka ma ana gwada bangaskiyarku
wadda ta fi zinariya daraja. Ta haka bangaskiyarkun nan za ta
jawo muku yabo da girma da daraja a ranar da Yesu Almasihu
zai bayyana. 8 Ko da yake ba ku taɓa ganin Yesu Almasihu ba,
amma duk da haka kuna ƙaunarsa. Ko da yake ba kwa ganinsa
a yanzu, duk da haka kuna ba da gaskiya gare shi, kuna kuma da
farin ciki mai yawa wanda ya fi gaban misali, 9 don kuwa kuna
samun ceton rayukanku wanda shi ne manufar bangaskiyarku.

10 Alherin nan da aka yi muku dai, a dā annabawa sun yi
bincike mai zurfi don su gane manufarsa, sun kuwa yi annabci a
kan wannan ceton da Allah ya shirya. 11 Sun nemi su sani ko
yaushe ne abin nan zai faru, da yadda za a yi shi, sa'ad da Ruhun
Almasihu ya yi magana a zukatansu ya nuna musu yadda
Almasihu zai sha wahala kafin yă kai ga ɗaukakarsa. 12 Allah
kuma ya bayyana musu cewa, lokacin da suke annabci, ba saboda
kansu ne yake ba su maganar ba, amma saboda ku ne. Yanzu
kuwa Ruhu Mai Tsarki wanda Allah ya aiko daga sama, ya sa an
bayyana muku dukan waɗannan abubuwa a cikin Labari Mai Daɗi
na Almasihu wanda aka yi shelarsa a wurinku. Ai, waɗannan
abubuwa, har mala'iku ma suna marmari su duba.

Halin da Ya Yi Kyau ga Masu Bi

13 Don haka sai ku shirya zuciyarku don aiki, ku natsu, ku sa
zuciyarku sosai a kan alherin da za a ba ku a ranar da Yesu
Almasihu zai bayyana. 14 Yanzu da kuke 'ya'ya masu biyayya,
kada ku yarda abubuwan da kuke marmarinsu a dā su ɗauke muku
hankali. A lokacin, ai, kuna zaman duhu ne. 15 Amma da yake

Allah wanda ya kira ku mai tsarki ne, ku ma kanku sai ku zama
da tsarki a cikin dukan ayyukanku. 16 A rubuce yake cewa, "Sai
ku zama masu tsarki, domin ni mai tsarki ne."

17 A lokacin addu'a kukan ce da Allah "Uba". To, sai ku yi
tafiyarku da tsoro har ranar da za ku gama zamanku na baƙunci
a nan duniya. Don shi mai hukunci ne. Shi kuwa ba ya nuna
bambanci tsakanin jama'arsa sa'ad da yake gwada ayyukansu.
18 Gama kun sani an fanshe ku ne daga al'adun banza waɗanda
kakanninku suka bar muku. Ba a fanshe ku da abubuwa masu
lalacewa kamar azurfa da zinariya ba. 19 An fanshe ku ne da jinin
nan mai daraja na Almasihu, wanda ya zama kamar ɗan rago na
hadaya, wanda yake babu ƙazanta ko alamar datti ko tabo, ko
kaɗan. 20 Shi ne Allah ya zaɓa tun kafin a halicci duniya kuma
saboda ku ne aka bayyana shi a zamanin ƙarshe. 21 Ta wurinsa
ne kuka gaskata da Allah wanda ya ta da shi daga matattu, ya
kuma ɗaukaka shi. Ta haka bangaskiyarku da sa zuciyarku sun
kasance ga Allah.

22 Yanzu da yake kun tsarkake ranku ta wurin yin biyayya ga
gaskiya har kuna ƙaunar 'yan'uwanku da zuciya ɗaya, sai ku ci
gaba da irin wannan ƙauna da iyakar ƙoƙarinku. 23 Gama an sāke
haihuwarku da sabuwar haihuwa. Wannan sabon rai naku kuwa,
ba daga mai mutuwa aka samu ba, sai dai daga wanda ba mai
mutuwa ba. Da yake an haife ku ta wurin maganar Allah wadda
take mai rai kuma ba za ta mutu ba. 24 Game da wannan aka
rubuta cewa,

"Duk ɗan Adam kamar ciyawa yake,
duk darajarsa kamar furen ciyawa take.
Ciyawa takan bushe, furen kuma yakan fāɗi.
25 Amma maganar Ubangiji za ta kasance har abada."

Wannan maganar ita ce Labari Mai Daɗin da aka yi muku
wa'azinsa.

Ku Ne Jama'a Mai Tsarki Na Allah

2 1 Saboda haka sai ku rabu da kowane irin mugun hali, da yin
ƙarya, yin munafunci da yin kishi, da kowane irin zage-zage.
2 Maimakon haka, ku zama kamar jarirai waɗanda suke marmarin
shan nonon, haka ku ma ya kamata ku yi marmarin maganar Allah
domin yă sa ku yi girma har ku kai ga samun ceto. 3 Ai, kun riga
kun "ɗanɗana alherin Ubangiji."

1.16: L. Fir 11.44-45; 19.2 **1.24-25**: Ish 40.6-8 **2.3**: Zab 34.8

4 Ku zo wurinsa, shi wanda ya zama dutsen gini mai rai. Shi
ne dutse wanda mutane suka ƙi, amma Allah ya zaɓe shi ya kuma
ɗaukaka shi. 5 Ku kuma, ku zama duwatsu masu rai waɗanda ake
amfani da su don gina gida irin na ruhu. Za ku yi hidima kamar
ƙungiyar firistoci masu tsarki a cikin wannan gida, kuna miƙa
masa hadayu na ruhu irin wanda Allah yake so, ta wurin Yesu
Almasihu. 6 Gama a rubuce yake, cewa,

"Ga shi na zaɓi dutse mai daraja
wanda shi ne tushen gidana.
Na kafa shi a Sihiyona.
Duk mai dogara ga wannan dutsen,
ba zai sha kunya ba, ko kaɗan."

7 Gaskiya ne kuwa, a gare ku, ku da kuka dogara gare shi, wannan
dutse yana da daraja. Amma waɗanda suka ƙi gaskatawa da shi,
za su ga yadda,

"Dutsen da masu gini suka ƙi,
ya zama dutse mai amfani
fiye da sauran duwatsun gini."

8 A rubuce yake kuma cewa,

"Dutse ne mai sa tuntuɓe,
Dutse ne kuma mai kawo fāɗuwa!"

Gaskiya ne kuwa! Mutane sun yi tuntuɓe ne domin sun ƙi yin
biyayya da maganar Allah. Haka kuwa aka shirya musu.

9 Amma ku, ku zuriya ce wadda Allah ne da kansa ya zaɓa.
Ku ƙungiyar firistoci ce ta Babban Sarki. Ku al'umma ce mai
tsarki. Ku jama'ar Allah ce. Shi ne ya zaɓe ku don ku yi shelar
ayyukansa na al'ajabi. Dalilin ke nan da ya kirawo ku daga cikin
duhu ku shiga haskensa mai ban mamaki. 10 A dā, ku jama'a ce
marasa daraja, amma yanzu ku mutanen Allah ne. A dā ku ba ku
sami jinƙan Allah ba, amma yanzu kun samu.

Biyayya ga Kowa

11 Ya ku waɗanda nake ƙauna, tun da yake ku baƙi ne a
wannan duniya, ba ku da gida a nan, ku rabu da halin kwaɗayi
na mutuntaka. Wannan hali yana yaƙi da zuciyarku. 12 Ku zama
dai da halin kirki a cikin mutanen nan da ba su san Allah ba. Ta
haka ko da yake suna kawo kara a kanku, amma ta wurin

2.6: Ish 28.16 **2.7:** Zab 118.22 **2.8:** Ish 8.14-15
2.9: Fit 19.5-6; Ish 43.20-21; M. Sh 4.20; 7.6; 14.2; Tit 2.14; Ish 9.1
2.10: Hos 2.23

ayyukanku masu kyau, za su zo su ɗaukaka Allah a ranar zuwansa.

13 Saboda Ubangiji, ku yi biyayya ga kowace hukuma
wadda take da iko a kan mutane. Ku yi wa babban sarki
biyayya, don yana mulki bisa kowa. 14 Ku kuma yi wa
gwamnoni biyayya, da yake sarki ne ya ɓe su don horon masu
laifi, su kuma yabi masu aikata abin da yake daidai. 15 Gama
nufin Allah ne cewa ku aikata adalci a gaban mutane marasa
wayo, domin ku toshe maganar da suke faɗa cikin jahilcinsu.
16 Ku yi zaman 'yanci, amma kada ku mai da wannan 'yanci
yă zama hanyar yin abin da bai yi daidai ba. Amma ku yi zaman
da zai nuna ku bayin Allah ne. 17 Ku ba da girma ga kowa, ku
ƙaunaci ƙungiyar masu bin Yesu. Ku ji tsoron Allah. Ku ba da
girma ga babban sarki.

Biyayya cikin Aikin Bauta

18 Ku masu hidima a gidaje, ku yi biyayya ga masu gidanku
da ban girma a kowane lokaci, ba ga masu kirki da masu saukin
kai kawai ba, har ma da masu zafin rai. 19 Ai, wanda ya sha
wahala a kan abin da ba laifinsa ba, in ya yi shi saboda yana
tunanin nufin Allah ne, abin yabo ne. 20 Amma idan an yi muku
bulala domin wani laifi, kome jimrewarku ai, ba wata riba a
wurinku. Amma in kun yi aiki mai kyau, sa'an nan kun sha
wahala a kansa, kun kuma haƙura, to, shi ne abin karɓa ga Allah.
21 Gama don irin wannan wahala ne Ubangiji ya kira ku.
Almasihu ma ya sha wuya dominku. Ta haka ya bar muku gurbi
domin ku bi bayansa. 22 Shi bai taɓa yin laifi ba ko kaɗan. Bai
taɓa yin ƙarya ba. 23 Sa'ad da mutane suka zage shi, bai mai da
zagin ba. Sa'ad da ya sha wahala, bai ce zai rama ba. Sai dai
ya dogara ga Allah wanda yake yin hukunci bisa gaskiya. 24 Mun
yi zunubi, amma shi ya ɗauki zunubanmu a jikinsa sa'ad da aka
gicciye shi a kan gungumen itace. Ya yi haka domin ta wurin
mutuwarsa mu rabu da zunubanmu, [b] mu yi zamanmu da adalci.
Kamar yadda aka rubuta, "Ta wurin ciwon da aka ji masa ne
kun sami warkarwa."

25 A dā kun ɓace kamar tumaki, amma yanzu kun dawo ga
Makiyayi da Mai Kula da rayukanku.

2.22: Ish 53.9 **2.23:** Ish 53.7 **2.24:** Ish 53.5 **2.25:** Ish 53.6

[b] **2.24 mu rabu da zunubanmu:** Da Helenanci an rubuta "Mu mutu ga zunubi" ne a nan.

Zaman Aure

3 [1] Haka kuma, ku matan aure ku yi biyayya ga mazanku. Don idan akwai waɗansu mazan da ba su gaskata da maganar Allah ba, mai yiwuwa ta wurin hali mai kyau na matansu, Allah zai jawo su, ko ba a yi musu magana ba. [2] Za su ga halinku mai tsabta da kuma ladabinku, su juyo. [3] Kada adon da kuke yi yă zama na jiki kawai, kamar su kitso, da kayan zinariya, da tufafi masu tsada. [4] A maimakon haka bari adonku yă zama na zuciya, wato, adonku na saukinkai da kuma natsuwa, wanda ba ya ƙarewa, wanda yake da muhimmin daraja a wurin Allah. [5] Gama a dā haka mata masu tsoron Allah, masu sa zuciya gare shi kuma sukan yi wa kansu ado. Wannan ado ne aka gani a wurin matan jama'ar Allah a dā, sukan kuma yi biyayya ga mazansu. [6] Misali, Saratu ta yi wa mijinta Ibrahim biyayya, har tana kiransa ubangijinta. Ku kuma, 'ya'yanta ne na gaske idan kun yi aiki mai kyau, idan kuma ba ku ji tsoro ba.

7 Haka kuma ku maza, sai ku yi zamanku da matanku tare da tunani. Ku girmama su, da yake su ba su da ƙarfi kamar ku. Gama da ku da matanku duka, kun karɓi alherin Allah tare. Ku yi haka don kada wani abu yă hana addu'o'inku.

Shan Wuya don Adalci

8 A ƙarshe kuma, bari dukanku ku haɗa tunaninku yă zama ɗaya. Kuna jin tausayin juna, kuna kuma ƙaunar 'yan'uwa, kuna nuna halin taimakon juna ba tare da ɗaga kai ba. [9] Kada ku rama mugunta da mugunta, ko zagi da zagi. Ku rama dai da albarka; ai don irin wannan ne musamman Allah ya kira ku. Nufinsa ne ku da kanku ku sami albarka. [10] A rubuce yake cewa,

"Wanda yake so yă ji daɗin rayuwa
wanda kuma yake so yă daɗe a duniya
sai yă rabu da mugun magana,
yă kuma daina ƙarya.
[11] Sai yă bar yin mugunta,
yă aikata adalci.
Sai yă yi ta neman salama,
yă neme ta da zuciya ɗaya.
[12] Gama Ubangiji yana lura da masu aikata adalci.
Yana jin roƙonsu kowane lokaci.
Amma yana gāba da masu aikata mugunta."

3.1: Afi 5.22; Kol 3.18 **3.3**: 1 Tim 2.9 **3.6**: Far 18.12 **3.7**: Afi 5.25; Kol 3.19
3.10-12: Zab 34.13-17

13 To, in kuna ƙoƙarin yin abin da yake daidai, ba wanda zai
yi muku wani abu. 14 Amma ko kun sha wuya saboda aikata abin
da yake daidai, Allah zai albarkace ku. Don haka kada ku ji tsoron
masu yi muku mugunta, kada kuma ku damu da su. 15 Sai dai ku
dogara ga Almasihu. Ku yarda masa yă zama Ubangiji a
zukatanku. Ku kuma zauna a shirye kullum ku bayyana wa duk
wanda ya tambaye ku dalilin da ya sa kuka sa zuciya ga bin
Almasihu. Amma ku yi shi da saukinkai da ban girma. 16 Har
yanzu, kullum ku yi kome da zuciya mai gaskiya domin in an
zage ku, waɗanda suka zage ku saboda halayenku masu kyau
cikin Almasihu, su sha kunya. 17 Gama zai fi kyau, idan Allah ne
ya shirya haka ku sha wuya a kan abin da yake daidai, da ku sha
wuya a kan abin da ba daidai ba. 18 Haka yake da Almasihu. Shi
mai adalci ya mutu saboda mu marasa adalci, ya mutu sau ɗaya
ne tak ba ƙari domin ya kai mu ga Allah. An kashe shi a jiki,
amma an rayar da shi a ruhu. 19 A cikin ruhu ne kuma ya je wurin
ruhohin da suke cikin kurkuku, ya yi musu wa'azi. 20 Ruhohin
nan dai su ne waɗanda a dā ba su yi biyayya ga Allah ba, wato,
a zamanin Nuhu. Ba su yi biyayya ba ko da yake Allah ya yi
haƙuri da su a lokacin da Nuhu yake sassaƙa jirgin. A lokacin
mutane kaɗan ne suka tsira ta wurin ruwa, wato, mutane takwas.
21 Ruwan kuwa kwatanci ne na wankan baftismar da muke yi. Ku
kuwa kuna tsira ta wurin ruwan baftisma. Amma tsiran da muka
yi kuwa ba saboda an fitar da datti daga jikinmu ba ne. Mun tsira
ne saboda mun roƙi Allah da zuciya ɗaya, da kuma saboda tashin
Yesu Almasihu daga matattu. 22 Almasihu dai ya tafi sama. Yana
wurin mai daraja na Allah, inda yake da iko bisa ga manyan
mala'iku da sauran masu mulkin sararin sama.

Rayuwar Masu Bin Almasihu

4 1 Tun da yake Almasihu ya sha wuya a jiki, sai ku ma ku
ɗauki halinsa ku shirya zukatanku don ku dage a cikin shan
wahala. Ai, duk wanda ya sha wuya a jiki, ya rabu da aikata
zunubi ke nan. 2 Nan gaba, tun yana da rai a jiki, abin da zai bi
da shi, shi ne nufin Allah, ba sha'awar jiki ba. 3 Kun riga kun
ɓata lokaci sosai a kan zaman da kuka yi a dā, wato, zama irin
wanda marasa sanin Allah suke jin daɗinsa. Kun yi ta yin lalata,
da sha'awa iri-iri ta jiki, da buguwa, da iskanci, da shaye-shaye,
har da bautar gumaka, wanda ya zama abin ƙyama. 4 Yanzu kuwa
abokanku na dā suna mamaki yadda ba kwa haɗa kai da su cikin

3.13: Luk 12.4 **3.14-15:** Mat 5.10; Ish 8.12-13 **3.20:** Far 6.1—7.24

yin mugayen abubuwan nan kamar dā, har ma suna zaginku.
5 Amma Ubangiji a shirye yake don yă hukunta masu rai da
matattu. Za su kuwa ba da lissafin kansu a gabansa. 6 Ta dalilin
wannan ne ma aka yi wa'azin Labari Mai Dadi ga matattu, domin
ko da yake an yanke musu hukunci cikin jiki kamar sauran
mutane, suna iya rayuwa cikin ruhu kamar Allah.

Halin da Ya Yi Kyau ga Masu Bin Almasihu

7 Karshen dukan abu ya yi kusa. Saboda haka sai ku lura, ku
kame kai. Idan ba haka ba, ba za ku iya yin addu'a ba. 8 Fiye da
kome kuma sai ku ƙaunaci juna da zuciya ɗaya. Don ƙauna takan
sa a gafarta laifofi da yawa. 9 Ku riƙa karɓar juna a cikin
gidajenku, ba tare da gunaguni ba. 10 Allah ya ba kowa baiwar
yin wani abu. Don haka, sai mu yi amfani da ita ga kyautata wa
'yan'uwanmu, domin ku zama masu rikon amanar abubuwa
dabam-daba da Allah ya danka muku cikin alherinsa. 11 Duk
wanda baiwarsa yin wa'azi ce, to, sai yă yi ta yin wa'azinsa sai
ka ce Allah ne da kansa yake magana ta wurinsa. Idan kuwa
baiwarsa ta yin hidima ce, to, sai yă yi ta yin hidimar da dukan
ƙarfin da Allah ya ba shi. A yi haka don a girmama Allah ta
wurin Yesu Almasihu. Shi ne da ɗaukaka da mulki har abada
abadin. Amin.

Yadda za a Haƙura cikin Wahala

12 'Yan'uwana waɗanda nake ƙauna, kada ku yi mamaki a
kan wahaloli masu zafin da suke samunku domin gwada ku. Kada
ku ɗauka cewa wani bakon abu ne yake faruwa a gare ku. 13 A
maimakon haka, sai ku yi farin ciki, da yake kuna tarayya da
Almasihu cikin shan wahalarsa, domin ku yi farin ciki da murna
marar iyaka a sa'ad da za a bayyana ɗaukakarsa. 14 Ko an zage
ku don cewa ku na Almasihu ne, ai, masu albarka ne ku, saboda
wannan ya tabbatar da cewa Ruhu mai ɗaukaka, wato Ruhun
Allah ne yake tare da ku. 15 Amma ku kula dai, don kada wani a
cikinku yă sha wuya a kan shi mai kisankai ne, ko mai sata, ko
wani mugun abu haka, ko mai karambani. 16 Amma in wani ya
sha wuya a kan shi Kirista ne, to, kada yă ji kunya, sai dai yă
ɗaukaka Allah saboda an ɗauke shi a matsayin mai bin Almasihu.

17 Lokaci ya yi da za a fara yi wa mutane shari'a. Waɗanda
za a fara da su, su ne mutanen Allah. To, idan da mu ne za a
fara shari'a, yaya ne zai zama da waɗanda suka ƙi jin Labari

4.8: K. Mag 10.12

Mai Dadin da ya fito daga wurin Allah? 18 Kamar yadda aka
rubuta a dā,
"Idan da kyar mutanen kirki za su tsira,
to, me zai faru da marasa jin tsoron Allah da masu
zunubi?"
19 Saboda haka, waɗanda suke shan wuya bisa ga nufin Allah,
sai su rika yin abin da yake daidai. Su sa ransu a hannun Allah
mahaliccinsu shi wanda ba ya karya alkawari.

A Yi Kiwon Garken Almasihu

5 1 Ni da nake dattijo ne kamar ku, ina yi wa dattiban jama'ar
masu bin da take a cikinku gargadi. Da idanuna na ga shan
wuyar Almasihu, kuma nan gaba zan sami rabona cikin
daukakarsa a ranar zuwansa. 2 Ina rokonku, ku yi kiwon garken
Allah da aka danka muku amanarsa. Kada ku ga kamar ana sa
ku tilas ne, amma ku yi shi da yardar ranku yadda Allah yake so.
Kada ku yi wannan aiki don kudi, amma ku yi don kuna da niyyar
yin aikin. 3 Kada ku zama masu nuna iko ga mutanen da Allah
ya ba ku, amma ku zama gurbin da garken nan za su yi koyi da
shi. 4 Ta haka, a ranar da Almasihu wanda shi ne Babban
Makiyayin garken zai bayyana, zai ba ku rawani wanda zai zama
da daraja marar karewa.

5 Haka nan kuma ku samari ku yi biyayya ga dattibai.
Dukanku, ku kasƙantar da kanku ku yi wa juna hidima, gama a
rubuce yake cewa, "Allah yana gāba da masu girmankai, amma
yana yi wa masu tawali'u alheri." 6 Don haka sai ku kasƙantar da
kanku ga Allah Mai Iko, domin a lokacin da ya ga dama yă
daukaka ku. 7 Ku danka masa dukan abin da yake damunku,
domin shi ne mai lura da ku.

8 Ku kame kanku, ku zauna da shiri. Ga shi abokin gābanku
Shaidan yana yawo yana ruri kamar zaki mai jin yunwa. Yana
neman wanda zai cinye. 9 Kada ku ba shi dama. Ku tsaya da karfi
cikin bangaskiyarku, da yake kun sani 'yan'uwanku masu bi
ko'ina cikin duniya, su ma, an danka musu shan wahala haka.
10 Bayan kun sha wuya na dan lokaci kadan, Allah mai alheri
duka, shi wanda ta wurin Almasihu ya riga ya kira ku zuwa ga
zama mai daraja tare da shi har abada, shi zai mai da ku cikakku,
zai kafa ku, zai kuma karfafa ku. 11 Mulki yă tabbata a gare shi
har abada abadin. Amin.

4.18: K. Mag 11.31 **5.2**: Yoh 21.15-17 **5.5**: K. Mag 3.34
5.6: Mat 23.12; Luk 14.11; 18.14

Gaisuwar Karshe

12 Na rubuta muku wannan 'yar wasiƙa da taimakon Silbanus,
wanda a ganina ya isa a ce da shi ɗan'uwa mai aminci. Nufina
ne, in ƙarfafa ku, in kuma faɗa muku a fili yadda gaskiyar alherin
Allah take. Saboda haka, ku tsaya da ƙarfi a kan wannan alherin
Allah ɗin. 13 Ita jama'ar masu bin da take a nan Babila,[6] wadda
ita ma Allah ya zaɓa kamar ku, tana gaishe ku. Ɗana Markus,
shi ma yana gaisuwa. 14 Ku gai da juna da gaisuwar ƙauna. Salama
ta kasance a gare ku duka, ku da kuke cikin Almasihu.

WASIKA TA BIYU TA
BITRUS

Gabatarwa

Manzo Bitrus ne ya rubuta wannan wasiƙa a tsakanin shekara ta A.D. 65-68.

Bitrus ya rubuta wasiƙar don yă koya wa masu bi yadda za su yi da malaman ƙarya da mugayen da suka shiga cikin jama'ar masu bi. Bitrus a matsayinsa na makiyayin garken Ubangiji ya nemi yă yi cikakken ƙarfafawa a kan bangaskiya da duk ainihin abin da ya shafi aiki da rayuwar mai bi.

Wasiƙar ta kasu ƙashi uku. Da farko wasiƙar ta zuga masu bi su ƙara girma cikin ruhaniya. Biye da wannan ta gargaɗe masu bi su tsaya su yi yaƙi da koyarwar ƙarya. A ƙarshe ta ƙarfafa su su yi zama da shiri saboda tabbacin dawowar Almasihu.

Abubuwan da Suke Ciki

Gaisuwa 1.1-2
Kira da rayuwa mai bi 1.3-21
Malaman ƙarya 2.1-22
Dawowar Yesu na biyu 3.1-18

5.12: A. M. 15.22,40 **5.13**: A. M. 12.12,25; 13.13; 15.37-39; Kol 4.10; Filib 1.24
[6] **5.13 Babila**: Mai yiwuwa Roma ne ake nufi.

Gaisuwa

1 [1] Daga Siman Bitrus, bawan Yesu Almasihu, da manzonsa kuma, zuwa ga waɗanda suka sami bangaskiya mai daraja kamar yadda mu ma muka samu, ta wurin adalcin Allahnmu kuma Mai Cetonmu Yesu Almasihu.

2 Bari Allah yă ƙara muku alheri da salama sosai cikin sanin Allah da Yesu Ubangijinmu.

Zaman da Ya Dace ga Masu Bin Almasihu

3 Allah cikin ikonsa ya ba mu dukan abin da muke bukata domin mu yi zamanmu irin na masu tsoron Allah. Dukan waɗannan abubuwan namu ne domin mun san Almasihu sosai. Ya kira mu zuwa ga yin tarayya da shi cikin darajarsa da nagartarsa. [4] Ta wurin abubuwan nan ya ba mu manyan alkawaransa masu daraja, saboda ta wurinsu, ku iya tarayya da shi cikin Allahntakarsa, ku kuma tsira daga muguntar da take a duniya wadda mugayen sha'awace-sha'awace suke jawowa. [5] Saboda haka, sai ku yi iyakar ƙoƙarinku ku ƙara a kan abin da kuka fara da shi. Wato, a kan bangaskiyarku ku ƙara da ayyukan kirki. A kan ayyukan kirki dîn sai ku ƙara da sanin abubuwan Allah. [6] A kan sanin abubuwan Allah kuma sai ku ƙara da kamunkai. A kan kamunkai kuma sai ku ƙara da jimrewa. A kan jimrewa kuma, sai ku ƙara da halin bin Allah. [7] A kan halin bin Allah kuma sai ku ƙara da son 'yan'uwa. A kan son 'yan'uwa kuma, sai ku ƙara da ƙauna. [8] Idan kuna da irin waɗannan halaye a yalwace, sanin Ubangijinmu Yesu Almasihu da kuke da shi zai sa ku zama masu ƙwazo, da masu amfani kumă. [9] Domin duk wanda ya rasa halayen nan, ba ya gani sosai, shi makaho ne. Ya kuma manta da ceton da aka yi masa daga zunubansa na dā.

10 Saboda haka, ya ku 'yan'uwa, ku ƙara ƙoƙarinku ku tabbatar da kiranku da zaɓenku da Allah ya yi muku. Idan kun yi haka ba za ku taɓa fādî ba ko kaɗan. [11] Ta haka kuma za a ba ku cikakken 'yanci ku shiga cikin madawwamin mulki na Ubangijinmu Yesu Almasihu Mai Cetonmu.

12 Don haka, zan riƙa tuna muku da waɗannan abubuwa, ko da yake kun riga kun san su, kun kafu sosai cikin maganar gaskiya da kuka karɓa. [13] A ganina, daidai ne, muddin ina da rai, in fadakar da ku ta wurin tuna muku, [14] da yake na sani kwanakina a wannan duniya sun kusan ƙarewa, kamar yadda Ubangijinmu Yesu Almasihu ya nuna mini. [15] Don haka zan yi iyakacin

ƙokarina in ga cewa kun riƙe waɗannan abubuwa cikin zukatanku kowane lokaci ko ma bayan na bar duniyan nan.

Masu Ganin Daukakar Almasihu

16 Ai, a lokacin da muka faɗa muku labarin yadda
Ubangijinmu Yesu Almasihu ya bayyana da iko,[a] ba tatsuniyoyin
da aka ƙaga da wayo muka bi ba. A'a! Da idonmu ne muka ga
ɗaukakarsa. 17 A sa'ad da ya karɓi girma da daraja daga wurin
Allah Uba kuma, muna nan a wurin. Mun ji muryar Allah Mai
Matuƙar Daraja tana cewa, "Wannan Dana ne da nake ƙauna.
Zuciyata tana jin daɗinsa ƙwarai." 18 Mun ji muryan nan daga
sama da yake muna tare da shi a kan dutsen nan mai tsarki.

19 Waɗannan abubuwa duk sun goyi bayan maganar annabawa na dā game da shi.[b] Ya kyautu fa ku mai da hankali ga wannan magana saboda ta zama kamar fitila mai haskakawa a wuri mai duhu har zuwa wayewar gari, lokacin da hasken tauraro na safe ya ɓullo muku a zuciya. 20 Amma da fari dai, ya kamata ku gane da wannan cewa, dukan maganganun annabawan da aka rubuta a littattafai, ba za a iya fassarar su ta wurin hikimar mutum kawai ba. 21 Gama maganar annabci ba ta taɓa zuwa ta hikimar mutum ba. Ruhun Allah ne ya shiga zukatan mutane ya sa su su faɗa abin da suka karɓa daga wurin Allah.

Annabawan Karya da Malaman Karya
(Yahu 3-16)

2 1 Amma fa, a dā annabawa masu rudî sun fito daga cikin
mutanen Allah. To, haka ma, waɗansu malaman ƙarya za su
fito daga cikinku. Za su kawo wata koyarwa a ɓoye, su koya wa
mutane ƙaryar da za ta ɓata su. Har za su ƙi Ubangiji, wanda ya
fanshi ransu. Yin haka kuwa zai jawo musu halaka ba da daɗewa
ba. 2 Mutane da yawa kuwa za su bi halayensu na lalata. Ta
dalilinsu kuwa waɗansu mutane za su rena hanyar gaskiya. 3 Cikin
kwaɗayinsu za su yi ƙokarin yin riba a kanku da maganganun
ƙarya. Amma dai tun da daɗewa an riga an yanke musu shari'a.
Kuma hukuncinsu yana nan yana jiransu.

---

[a] **1.16-18 Ubangijinmu Yesu Almasihu ya bayyana da iko:** An ɗauki wannan cewa Bitrus yana maganar lokacin da jikin Yesu ya yi walƙiya a kan dutse (Dubi Mat 17.1-13, Mar 9.2-13, Luk 9.18-36). Amma bisa ga fassarar waɗansu, Bitrus yana magana a kan dawowar Yesu a ranar ƙarshe.

[b] **1.19 Waɗannan abubuwa sun goyi bayan maganar annabawa:** Wani juyi na waɗannan kalmomi shi ne "Mun ƙara gaskata da maganar annabawa na dā."

4 Ko mala'iku, a dā sa'ad da suka yi laifi, Allah bai ƙyale su
ba, amma ya jefa su a ramin wuta. Ya ɗaure su a cikin ramuka
masu zurfi inda ba haske sai duhu. Suna jiran ranar hukunci.
5 Kuma a zamanin dā, mutanen da suka yi mugunta ma, Allah bai
bar su ba. Ta wurin babban ruwa, wato ruwan tsufana, Allah ya
halaka mutane waɗanda ba su yi masa biyayya ba. Sai Nuhu kaɗai
mai wa'azin adalci, tare da waɗannan mutane guda bakwai, su
ne Allah ya kiyaye su daga babban ruwan nan da aka yi wa
duniya. 6 Kuma Allah ya halakar da biranen Sodom da Gomora
har ya mai da su toka. Wannan misali ne na irin abin da zai yi
wa waɗanda ba sa tsoronsa. 7 Ya kuma ceci Lutu, wato, mai
adalcin nan. Lutu ya damu ƙwarai game da irin mugayen ayyuka
na mutanen Sodom marasa bin doka. 8 Ko da yake wannan mutum
mai adalci ne, amma yana zaune cikin mugayen mutane, yana ta
ganin muguntarsu kowace rana, yana kuma jin irin munanan
maganganunsu, har ransa ya yi ta ɓacewa ƙwarai a kansu saboda
sun ƙi bin doka. 9 To, ta wurin irin waɗannan misalai ne muka
sani cewa lallai Allah yana iya ceton masu binsa daga cikin
gwaje-gwajensu. Allah ya san kuma yadda zai tsare masu
mugunta har zuwa ranar hukunci. 10 Hukuncin nan dai zai fi zafi
a kan masu bin mugun sha'awar jikinsu, da kuma waɗanda suke
rena masu mulki.

Waɗannan malamai masu ƙarya dai, ba su da kunya sam!
Girmankai gare su. Ba sa jin tsoron kome, har suna zargin
mala'ikun Allah. 11 Amma kuwa, su mala'iku da kansu, ko da
yake sun fi waɗannan malamai ƙarfi da iko, duk da haka ba sa
ɗora musu laifi haɗe da zage-zage a gaban Ubangiji. 12 Amma
waɗannan mutane, suna maganar reni wa Allah a kan abubuwan
da ba su gāne ba. Suna nan kamar dabbobin daji marasa hankali,
waɗanda suke bin abin da jikinsu yake sha'awarsa ne kawai. An
haife su ne don a kama su a kashe kawai. Ai, za su halaka kamar
dabbobin daji! *6* 13 Kuma kamar yadda suka wahalar da waɗansu
mutane, haka su ma za a wahalar da su. Sun ɗauka abin jin daɗi
ne su yi shaye-shaye da iskanci da rana tsaka. Zamansu a cikinku
abin kunya ne, abin muni ne kuma. Suna ci, suna sha tare da ku,
amma a bayanku suna aikata abin da suka ga dama. 14 Neman
mata shi ne tunaninsu a kullum, har ma ba sa gajiya da yin zunubi.
Suna kuwa rudin marasa ƙarfi cikin bangaskiya. Sun gwaninta a

2.5: Far 6.1—7.24 2.6: Far 19.24 2.7: Far 19.1-16

6 **2.12 Ai, za su halaka kamar dabbobin daji:** Da Helenanci an rubuta "A cikin halakarsu za a halaka".

kan kwaɗayi. Irinsu Allah zai hukunta su babu shakka. 15 Sun bar
hanyar gaskiya, suna bin hanyar Balaam ɗan Beyor. Shi ne, garin
neman kuɗi, yake jin daɗin aikata mugunta. 16 Amma an tsawata
masa a kan laifinsa, har jaki, wanda bai taɓa yin magana ba, ya
yi masa magana da murya irin ta mutum, don yă hana annabin
nan yin ɓarnarsa.

17 Waɗannan masu ƙaryar suna kama da rafi wanda ya bushe.
Suna nan kamar hazo wanda iska takan kora. Hakika Allah ya
shirya musu wurin zama cikin baƙin duhu. 18 Mutanen nan dai,
ta wurin surutu da maganganun banza suna nuna girmankansu.
Ta wurin irin halinsu na lalata kuma, suna ƙoƙarin jawo waɗanda
suka kuɓuta ba da daɗewa ba daga cikin mutane masu rayuwa
cikin zunubi. 19 Suna yi musu alkawarin samun 'yanci, amma su
da kansu bayi ne ga aikata lalata. Don mutum bawa ne ga dukan
abin da ya kwashe masa hankalinsa. 20 Idan har mutum ya gane
cewa Ubangijinmu Yesu Almasihu shi ne Mai Cetonmu, kuma
har ya sami tsira daga ayyuka masu ɓata mutanen duniyan nan,
sa'an nan daga baya kuma, ya sāke shiga cikin waɗannan
munanan abubuwa, har sun sha kansa, lallai wannan mutum
zamansa na ƙarshe ya fi na farko muni ainu. 21 Da a ce irin
waɗannan mutane ba su taɓa sanin hanyar adalci ba tun da farko,
da ya fi musu. Amma ga shi, bayan da suka san hanyar, sa'an
nan suka koma da baya suka bar bin umarnin nan mai tsarki
wanda aka ba su. 22 Ai, abin da suka aikata ɗin nan ya yi daidai
da karin maganan nan da ake faɗa cewa, "Kare ya yi amai sa'an
nan ya koma ya lashe amansa," da kuma wanda ake cewa,
"Aladen da aka yi wa wanka ya koma ya yi birgima cikin taɓo."

Alkawarin Dawowar Yesu

3 1 'Yan'uwa waɗanda nake ƙauna, wannan ita ce wasiƙata ta
biyu zuwa gare ku. A cikin dukansu biyu kuwa ina tuna muku
da waɗannan abubuwa domin in fadakar da ku ku bi Allah da
zuciya ɗaya.[c] 2 Ina so kuma ku tuna da abubuwan da annabawa
masu tsarki na dā suka faɗa, da kuma umarnin da Ubangiji Mai
Ceto ya faɗa ta bakin manzannin da ya aiko wurinku. 3 Da farko
dai, ku gane da wannan cewa, a ƙarshen zamani waɗansu mutane
masu ba'a za su fito suna bin sha'awace-sha'awacensu. Za su yi
muku dariya, 4 za su ce, "Ashe, ba Yesu ya yi muku alkawari

2.15-16: L. Kid 22.4-35 **2.22**: K. Mag 26.11 **3.3**: Yahu 18

[c] **3.1 ku bi Allah da zuciya ɗaya:** Da Helenanci an rubuta "Ina yi muku tuni domin in tashe ku ku yi tunani sosai."

cewa zai sāke dawowa ba? To, ina yake? Kakanninmu sun bar
duniya tun tuni, amma dukan kome ya ci gaba ba sākewa tun
farkon halitta." 5 Masu fadin haka dai, da gangan suke ɓin kula
da cewa ta wurin umarnin Allah ne a dā, sama da ɓasa suka
kasance. Ta wurin ruwa ne kuwa ya siffata ɓasa, ɓasa kuwa ta
kasance a tsakiyar ruwa. 6 Ta wurin ruwa ne kuwa ya halaka
duniya a wancan zamani, lokacin da babban ruwa ya zo ya sha
kanta. 7 Ta wurin umarnin Allah kuwa, sama da ɓasa wadanda
muke gani yanzu, suna jira a halaka su da wuta. Allah ya ajiye
su har zuwa ranar da za a yi wa marasa tsoron Allah hukunci, a
halaka su.

8 Amma ya ku 'yan'uwa wadanda nake ɓauna, abu ɗaya
wanda ba na so ku manta da shi, shi ne kwana ɗaya a gun Ubangiji
kamar shekara dubu yake, shekaru dubu kuma kamar kwana ɗaya
ne. 9 Wadansu suna cewa Ubangiji yana jan jiki game da cika
alkawarinsa. Ai, ba haka ba ne. Haƙuri yake yi da ku. Ba ya so
kowa yă halaka, sai dai kowa yă zo yă tuba. 10 Duk da haka,
Ranar Ubangiji za ta zo babu shakka. Za ta zo kuwa kamar
ɓarawo, ba labari. A lokacin za a ji ɓara mai ɓarfi sa'an nan
sararin sama zai ɓace. Dukan abubuwan da aka ɗauka aka yi sama
da ɓasa da su za su ɓone su halaka. Duniya da dukan abin da
yake a cikinta za su ɓace.[d] 11 Tun da yake duk abubuwan nan za
a halaka su haka, wane irin zama ya kamata ku yi?[d'] Sai ku yi
rayuwa mai tsarki, kuna miƙa kanku ga Allah cikin kome. 12 Ku
yi zama kuna marmarin zuwan Ranar Allah, har kuna ƙoƙari ku
hanzarta zuwan Ranan nan, wato, Ranar da sama za ta ɓone cikin
wuta, za ta kuma ɓace gaba ɗaya, har abubuwan da aka yi sama
da ɓasa da su za su narke cikin wuta. 13 Amma bisa ga alkawarin
Allah mu muna jiran sabuwar sama da sabuwar ɓasa, inda adalci
zai kasance kullum.

14 Saboda haka, 'yan'uwa wadanda nake ɓauna, da yake kuna
jiran zuwan Ranar, sai ku yi iyakacin ƙoƙarinku ku yi zamanku
a gaban Allah ba tare da wani abin zargi ko laifi ba. Ku yi zama
a gabansa da salama. 15 Ku tuna cewa dalilin da ya sa
Ubangijinmu yake haƙuri shi ne don mutane su sami ceto. Haka

3.5: Far 1.6-9 **3.6**: Far 7.11 **3.8**: Zab 90.4
3.10: Mat 24.43; Luk 12.39; 1 Tas 5.2; R. Yoh 16.15
3.13: Ish 65.17; 66.22; R. Yoh 21.1

[d] **3.10 za su ɓace**: Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Za su ci wuta" ne a nan.

[d'] **3.11 wane irin zama ya kamata ku yi?**: Da Helenanci an rubuta "Wadanne irin mutane ne ya kamata ku zama?"

ma ɗan'uwanmu Bulus wanda muke ƙauna ya riga ya rubuta muku bisa ga hikimar da Allah ya ba shi. 16 Kullum yana magana a kan irin waɗannan abubuwa a cikin dukan wasiƙunsa. A cikin wasiƙunsa kuwa akwai waɗansu abubuwan da suke da wuyar ganewa. Su ne abubuwan da waɗansu mutane masu rashin ganewa, marasa ƙarfi cikin bangaskiya, suke juya ma'anarsu. Ai, suna jawo wa kansu halaka ne. Haka ma suke yi da sauran Rubutattun Maganar Allah.

17 Don haka, ya ku 'yan'uwa waɗanda nake ƙauna, da yake kun riga kun gane da waɗannan, sai ku lura da irin waɗannan mutanen da suka bar bin Allah, kada koyarwarsu ta ƙarya ta kwashe hankalinku, har ku ƒāɗī daga matsayinku. 18 A maimakon haka, sai ku yi ta yin girma cikin alherin Ubangijinmu Yesu Almasihu Mai Cetonmu, ku kuma ƙaru cikin saninsa kowane lokaci. Daukaka ta tabbata a gare shi a yanzu da kuma har abada. Amin.

WASIKA TA FARKO TA
YOHANNA

Gabatarwa

Manzo Yohanna ne ya rubuta wasiƙan nan a tsakanin shekara ta A.D. 85 da A.D. 95 a birnin Afisa. Tun da yake ba a ambaci sunan wani a cikin wasiƙar ba, wannan ya nuna cewa an rubuta ta da nufin a rarraba wa jama'un masu bin da suke a wurare dabam-dabam ne.

An rubuta wasiƙar ne don a ƙarfafa masu bi su yi zumunci da Allah ta wurin Ɗansa Yesu Almasihu. Wasiƙar ta yi gargaɗi game da koyarwar ƙaryan da yake ƙoƙarin rushe zumuncin nan. Bisa ga koyarwar ƙaryan nan, Yesu bai shigo duniyan nan da ainihin jiki irin na mutum ba, wato, Yesu ba mutum ba ne kamar sauran 'yan Adam. An kuma rubuta wasiƙar ne domin a ƙarfafa masu bi su sami tabbaci sosai game da bangaskiyarsu su kuma ƙaunaci juna kamar yadda Allah ya ƙaunace su.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-4
Haske da duhu 1.5—2.29
'Ya'yan Allah da 'ya'yan Shaiɗan 3.1-24
A gwada ruhohi 4.1-6
Allah ƙauna ne 4.7-21
Yin nasara da duniya 5.1-21

Kalman Rai

1 [1] Muna sanar muku ne yanzu game da wanda tun daga farko
yana nan, wanda muka ji, muka gani da idanunmu, muka
duba, muka kuma taɓa da hannayenmu. Muna rubuta muku ne
game da Kalma mai ba da Rai. [2] Wannan rai kuwa an bayyana
mana shi, mun kuma gan shi. A kansa ne muke ba da shaida
muna kuma sanar muku cewa shi ne Mai Rai na har abada.
Yana tare da Uba tun dā, aka kuwa bayyana mana shi. [3] Muna
sanar muku da abin da muka ji, muka kuma gani ne, domin
muna so ku ma ku yi zumunta tare da mu. Zumuntarmu kuwa
tana tare da Allah Uba, da kuma Ɗansa Yesu Almasihu. [4] Muna

---

1.1: Yoh 1.1 **1.2:** Yoh 1.14

kuma rubuta muku wannan ne domin farin cikinmu[a] yă zama cikakke.

Rayuwa cikin Haske

5 Wannan shi ne sakon da muka ji daga wurin Dansa cewa,
Allah haske ne, kuma a cikinsa babu duhu ko kadan. To, sakon
da muke sanar muku ke nan. 6 Saboda haka in mun ce muna
zumunci da Allah, amma kuma muna cin gaba da rayuwa cikin
duhu, to, muna karya ke nan, kuma ba ma bin gaskiya. 7 Amma
in muna rayuwa cikin haske kamar yadda Allah yake cikin haske,
muna zumunta da juna ke nan. Sa'an nan jinin Yesu Dansa yana
wanke mu daga dukkan zunubi.

8 In mun ce ba mu da zunubi, rudin kanmu muke yi, gaskiya
kuwa ba ta cikinmu. 9 Amma in mun fada wa Allah zunubanmu,
ai, shi mai cika alkawari ne, mai gaskiya kuma, zai kuma gafarta
mana zunubanmu, yă kuma wanke mu daga dukkan rashin
adalcinmu. 10 In mun ce ba mu yi zunubi ba, mun mai da Allah
mai karya ke nan, kuma maganarsa ba ta a zuciyarmu.

Almasihu Ne Mai Taimakonmu

2 1 Ya ku 'ya'yana kanana, ina rubuta muku wannan ne domin
kada ku yi zunubi. Amma in har wani ya yi zunubi, to, muna
da mai taimako a gaban Uba, wato, Yesu Almasihu mai adalci.
2 Shi ne hadayar da ta gafarta zunubanmu, ba ma namu kadai ba
amma har da na dukkan mutanen duniya.

3 In mun yi biyayya da umarnin Allah, to, wannan zai tabbatar
mana cewa mun san shi. 4 Duk wanda ya ce, "Ai, na san Allah,"
amma bai yi biyayya da umarnin Allah ba, to, wannan mutumin
mai karya ne, kuma ba gaskiya a cikinsa. 5 Amma wanda ya yi
biyayya da maganar Allah, to, ai, kaunar Allah ta zama cikakkiya
ke nan a cikinsa. Ta haka ne za mu san cewa muna rayuwa cikin
Allah. 6 Duk wanda ya ce yana rayuwa cikin Allah, dole ne yă yi
zama kamar yadda Yesu Almasihu ya yi.

Sabon Umarni

7 Ya ku wadanda nake kauna, ba domin in ba ku sabon umarni
nake rubuta muku ba. Ai, umarni na dā ne wanda kuke da shi
tun daga farko. Umarnin nan na dā kuwa shi ne sakon da kun
riga kun ji. 8 Amma duk da haka ina rubuta muku sabon umarni

[a] **1.4 farin cikinmu**: Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "farin cikinku" ne a nan.

ne. Almasihu ma ya nuna mana cewa wannan umarnin gaskiya ne, har ku ma kun nuna haka. Ai, duhu yana ƙarewa, hasken gaskiya kuma ya riga ya fara haskakawa.

9 Wanda ya ce yana cikin haske, amma yana ƙin ɗan'uwansa, to, har yanzu yana cikin duhu ke nan. 10 Amma duk wanda yake ƙaunar ɗan'uwansa, to, yana rayuwa cikin haske ke nan, kuma ba zai zama dalilin tuntuɓen wani ba.[b] 11 Wanda yake ƙin ɗan'uwansa yana cikin duhu, kuma yana tafiya cikin duhu ne, bai kuwa san inda za shi ba, domin duhun ya mai da shi makaho.

12 Ya ku 'ya'yana ƙanana, na rubuta muku ne domin an yafe muku zunubanku saboda sunan Yesu.

13 Ya ku ubanni, na rubuta muku ne domin kun
san shi wanda yake tun daga farko.
Ya ku samari, na rubuta muku ne domin kun ci nasara a
kan Mugun nan.
Ya ku 'yan yara, na rubuta muku ne domin kun san Uba.
14 Ya ku ubanni, na rubuta muku ne domin kun
san shi wanda yake tun daga farko.
Ya ku samari, na rubuta muku ne domin kuna da ƙarfi,
kuma maganar Allah tana zaune a cikin zuciyarku,
kun kuma ci nasara a kan Mugun nan.

15 Kada ku ƙaunaci duniya, ko abubuwan da suke cikinta. Duk wanda yake ƙaunar duniya, to, babu ƙaunar Uban a cikinsa. 16 Gama dukan abubuwan da suke a duniya, kamar: neman biyan sha'awarmu ta jiki, da kwaɗayin ido, da kuma taƙama da abubuwan da muke da su. Waɗannan dai ba daga wurin Uba suka fito ba, amma daga duniya ne suka fito. 17 Duniya da dukan muguwar sha'awarta suna wucewa, amma wanda yake yin abin da Allah ya ce a yi, zai rayu har abada.

Mai Gāba da Almasihu

18 Ya ku 'ya'yana, waɗannan su ne kwanakin ƙarshe. Kamar yadda kuka riga kuka ji cewa, mai ƙin Almasihu yana zuwa, to, yanzu ma masu gāba da Almasihu da yawa sun riga sun zo. Shi ya sa muka san cewa muna a kwanakin ƙarshe. 19 Waɗannan masu gāba da Almasihu suna cikinmu a dā, amma sun bar mu, don tun dā ma su ba namu ba ne. Ai, da su namu ne, da har yanzu suna

2.7: Yoh 13.34 **2.7-9**: L. Fir 19.18

[b] **2.10 ba zai zama dalilin tuntuɓen wani ba**: Ko kuwa "Ba abin da zai sa yă yi tuntuɓe."

tare da mu. Amma sun bar mu, wannan kuma ya nuna a fili cewa dukansu ba namu ba ne.

20 Amma ku kam, Mai Tsarkin nan ya shafe ku. Saboda haka dukanku kun san gaskiya.[6] 21 Ban rubuta muku saboda ba ku san gaskiya ba, amma saboda kun san ta. Kun kuma san cewa gaskiya ba ta haihuwar ƙarya. 22 Wane ne wannan mai ƙarya? Ai, shi ne wanda ya ƙi yarda cewa Yesu ne Almasihu. Mutumin da ya ƙi karɓar Uban da Ɗan, to, shi ne mai ƙin Almasihu. 23 Duk wanda ya ƙi karɓar Ɗan, to, ya ƙi Uban ma ke nan. Amma duk wanda ya karɓi Ɗan, ya karɓi Uban ma ke nan.

24 Ku ci gaba da bin koyarwar da kuka ji tun daga farko. Idan koyarwar da kuka samu tun daga farko ta zauna a zuciyarku, to, ku ma za ku zauna a cikin Ɗan da kuma cikin Uban. 25 Kuma wannan shi ne alkawarin da Ɗan ya yi mana wato, rai na har abada.

26 Na rubuta muku wannan ne game da waɗanda suke ƙoƙari su ruɗe ku. 27 Amma Almasihu ya ba ku Ruhu Mai Tsarki wanda yake cikinku, don haka ba kwa bukata wani malami dabam. Ruhun da ya bayar yana koya muku kome da kome; kuma koyarwarsa gaskiya ce, ba ƙarya ba. Saboda haka ku ci gaba da zama cikin Yesu kamar dai yadda Ruhu ya koya muku.

28 Yanzu, ya ku 'ya'yana ƙanana, sai ku zauna cikin Almasihu domin a ranar da zai dawo mu kasance babu tsoro ko kunya a gabansa. 29 Idan kun san cewa Almasihu mai adalci ne, za ku tabbata cewa duk wanda yake yin abin da yake daidai shi ɗan Allah ne.

'Ya'yan Allah

3 1 Ku dubi yadda Uba ya ƙaunace mu sosai har ana ce da mu 'ya'yan Allah, haka kuwa muke. Mutanen duniya ba su san mu ba don ba su san shi ba. 2 Ya ku waɗanda nake ƙauna, yanzu mu 'ya'yan Allah ne. Ba a nuna mana abin da za mu zama nan gaba ba tukuna. Amma mun san cewa in Almasihu ya sāke dawowa za mu zama kamarsa, don za mu gan shi daidai yadda yake. 3 Duk wanda yake sa zuciya a kan Almasihu haka yakan tsarkake kansa don yă zama kamarsa, don shi mai tsarki ne.

4 Duk wanda yake yin zunubi yana karyar dokar Allah ke nan. Zunubi shi ne karyar dokar Allah. 5 Kun dai san cewa Yesu ya

---

3.1: Yoh 1.12

[6] **2.20 kun san gaskiya:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "kun san kome da kome" ne a nan.

zo ne domin yă ɗauke zunubai, kuma babu zunubi a cikinsa.
6 Saboda haka duk wanda yake zama cikin Almasihu ba ya cin
gaba da yin zunubi. Duk wanda ya ci gaba da yin zunubi, to, bai
taɓa ganin Yesu ba, bai ma taɓa saninsa ba.

7 Ya ku 'ya'yana ƙanana, kada fa kowa ya ruɗe ku. Duk wanda
yana aikata gaskiya shi ne mai adalci kamar yadda Almasihu yake
mai adalci. 8 Tun farko Shaiɗan mai zunubi ne, saboda haka duk
wanda ya ci gaba da yin zunubi shi na Shaiɗan ne. Dalilin da ya
sa Ɗan Allah ya zo duniya shi ne don yă rushe ayyukan Shaiɗan.

9 Duk wanda yake ɗan Allah ba ya cin gaba da yin zunubi,
domin sabon rai daga wurin Allah[c] yana cikinsa. Ba zai iya ci
gaba da yin zunubi ba domin ya zama ɗan Allah. 10 Ga yadda za
a gane waɗanda suke 'ya'yan Allah, da kuma waɗanda suke
'ya'yan Shaiɗan. Duk wanda ba ya yin abin da yake daidai, shi
ba ɗan Allah ba ne, kuma wanda ba ya ƙaunar ɗan'uwansa, shi
ba ɗan Allah ba ne.

Kaunaci Juna

11 Wannan shi ne saƙon da kuka ji tun daga farko, cewa mu
ƙaunaci juna. 12 Kada fa ku zama kamar Kayinu wanda ya zama
na Shaiɗan har ma ya kashe ɗan'uwansa. Don me ya kashe
ɗan'uwansa? Ya kashe shi domin ayyukansa mugaye ne, amma
na ɗan'uwansa masu kyau ne. 13 Ya ku 'yan'uwa, kada ku yi
mamaki idan mutanen duniya suna ƙinku. 14 Mu kam, mun tabbata
mun riga mun wuce daga mutuwa zuwa rai don muna ƙaunar
'yan'uwa. Amma wanda ba ya ƙaunar 'yan'uwa, har yanzu yana
ƙarƙashin mutuwa ke nan. 15 Duk wanda yake ƙin ɗan'uwansa,
shi mai kisankai ne. Kuma kun sani cewa ba mai kisankai wanda
yake da rai na har abada a cikinsa. 16 Ga yadda muka san yadda
ƙauna take: Yesu ya ba da ransa saboda mu. Ya kamata mu ma
mu ba da ranmu saboda 'yan'uwanmu. 17 Idan mai arziki ya ga
ɗan'uwansa a cikin rashi sa'an nan ya ƙi ya taimake shi, anya,
ƙaunar Allah tana a cikinsa kuwa? 18 Ya ku 'ya'yana ƙanana kada
ku nuna ƙaunarku ta wurin surutun baki kawai, amma ku nuna
ƙaunarku ta wurin aikatawa da kuma gaskiya.

19 Idan mun ƙaunaci juna, to, mun san cewa muna da gaskiya
ke nan, kuma za mu iya tsaya a gaban Allah ba tare da rawan
jiki ba. 20 Idan zuciyarmu ta nuna mana muna da laifi, mun san
cewa Allah ya fi zuciyarmu ya kuma san dukan kome. 21 Ya ku

3.5: Yoh 1.29 **3.11:** Yoh 13.34 **3.12:** Far 4.8 **3.14:** Yoh 5.24

[c] **3.9 Sabon rai daga wurin Allah:** Da Helenanci an rubuta "irinsa" ne a nan.

wadanda nake kauna, idan zuciyarmu ba ta nuna mana muna da laifi ba, to, muna da karfin zuciyar da za mu tsaya a gaban Allah ke nan. 22 Mukan kuwa sami duk abin da muka roka daga wurinsa, domin muna biyayya da umarninsa, muna kuma yin abin da yake so. 23 Abin da Allah ya umarta shi ne mu ba da gaskiya ga Dansa Yesu Almasihu, mu kuma kaunaci juna kamar yadda Almasihu ya umarce mu. 24 Duk masu bin umarninsa suna zama cikinsa, shi kuma a cikinsu. Ga yadda muka tabbata yana a cikinmu: Mun tabbatar da haka saboda Ruhun da ya ba mu.

A Gwada Ruhohi

4 1 Ya ku wadanda nake kauna, kada ku yarda da duk wanda ya ce yana da Ruhun Allah, amma ku gwada ruhohi duka don ku gani ko daga wurin Allah suke. Gama annabawan karya sun bazu ko'ina a duniya. 2 Ga yadda za ku gane ko mutum yana da Ruhun Allah: Duk mutumin da ya shaida cewa Yesu Almasihu ya zo cikin jiki, kuma ya fito daga wurin Allah ne, mutumin nan yana da Ruhun Allah. 3 Amma duk mutumin da bai shaida haka a kan Yesu ba, to, ruhun da yake da shi ba daga wurin Allah ba ne. Wannan ruhun da yake da shi na mai gāba da Almasihu ne wanda kuka ji cewa zai zo, ai, yanzu ma ya riga ya shigo duniya. 4 Ya ku 'ya'yana kanana, ku kam na Allah ne, kun kuma ci nasara a kan annabawan karyan nan, domin Ruhun Allah da yake cikinku ya fi ruhun da yake cikin mutanen da suke na duniya. 5 Tun dā ma su na duniya ne, saboda haka duk abin da suka fada daga duniya ne; duniya kuwa tana jinsu. 6 Amma mu, na Allah ne. Wadanda sun san Allah sukan ji mu, wadanda kuma ba su san Allah ba, ba sa jinmu. To, ta haka ne muka san mutumin da yake da Ruhun gaskiya da mutumin da yake da ruhun karya.

Allah Kauna Ne

7 Ya ku wadanda nake kauna, sai mu kaunaci juna domin kauna tana zuwa ne daga wurin Allah. Duk mai nuna kauna shi dan Allah ne, ya kuma san Allah. 8 Duk wanda ba ya nuna kauna, bai san Allah ba sam, domin Allah shi ne kauna. 9 Yadda Allah ya nuna mana kaunarsa shi ne, ya aiko da makadaici Dansa zuwa cikin duniya domin mu sami rai ta wurinsa. 10 Ga yadda kauna ta gaskiya take, wato, ba mu ne muka kaunaci Allah ba, sai dai shi ne ya kaunace mu, har ya aiko da Dansa don yă zama hadaya ta gafarar zunubanmu.

3.23: Yoh 13.34; 15.12,17

11 Ya ku waɗanda nake ƙauna, tun da yake Allah ya ƙaunace
mu haka, ya kamata mu ma mu ƙaunaci juna ke nan. 12 Ba
mutumin da ya taɓa ganin Allah sam, amma in muna ƙaunar juna,
Allah yana zama a cikinmu ke nan, ƙaunarsa kuma ta zama
cikakkiya ke nan a cikinmu.

13 Ta haka muka tabbata muna zama a cikinsa, shi kuma a
cikinmu, saboda Ruhunsa da ya ba mu. 14 Mun duba, muna kuma
ba da shaida cewa Uban ya aiko Ɗansa yă zama Mai Ceton
duniya. 15 Duk wanda ya buɗe baki ya yarda cewa Yesu Ɗan
Allah ne, to, yana cikin Allah, Allah kuma yana cikinsa. 16 Gama
mu da kanmu mun sani mun kuma ba da gaskiya ga ƙaunar da
Allah yake nuna mana.

Allah ƙauna ne, duk wanda yake nuna ƙauna yana zama cikin
Allah ne, Allah kuma yana zama a cikinsa. 17 Kaunarsa ta zama
cikakkiya a cikinmu domin kada mu kasance da tsoro a Ranar da
Allah zai yi mana shari'a. Gama kamar yadda Almasihu yake,
haka muke a duniyan nan. 18 Inda ƙaunar Allah take, babu tsoro,
domin cikakkiyar ƙauna takan kori tsoro. Horo ne yake sa mutum
tsoro. Wannan ya nuna cewa mutumin da yake da tsoro ba shi
da cikakkiyar ƙauna.

19 Muna ƙauna domin Allah ne ya fara ƙaunace mu. 20 Amma
idan wani ya ce, "Ai, ina ƙaunar Allah," sa'an nan yana ƙin
ɗan'uwansa, to, wannan mutumin yana ƙarya ne. Don duk wanda
ba ya ƙaunar ɗan'uwansa wanda yake gani, ba zai iya ƙaunaci
Allahn da bai taɓa gani ba. 21 Almasihu kuma ya ba mu doka
cewa, duk mai ƙaunar Allah, dole ne yă ƙaunaci ɗan'uwansa
kuma.

Hanyar Yin Nasara da Duniya

5 1 Duk mutumin da ya ba da gaskiya cewa Yesu ne Almasihu,
mutumin nan ɗan Allah ne. Duk mai ƙaunar Uban yaro zai
ƙaunaci yaron ma. 2 Yadda za mu sani muna ƙaunar 'ya'yan Allah
shi ne in muna ƙaunar Allah, muna yin abin da ya ce mu yi.
3 Gama ƙaunarmu ga Allah ita ce, mu yi abin da Allah ya ce mu
yi, kuma umarnansa ba su da wuya, 4 domin kowane ɗan Allah
yana da iko yă ci nasara da duniya. Bangaskiyarmu cikin
Almasihu ita ce take ba mu wannan nasara. 5 Wane ne zai iya cin
nasara da duniya? Sai wanda ya ba da gaskiya cewa Yesu Ɗan
Allah ne.

4.12: Yoh 1.18 5.3: Yoh 14.15

Shaida Game da Dan Allah

6 Shi Yesu Almasihun nan ya zo duniya, ya kuma zo duniya
da alamar ruwa da jini. Ba da ruwa kaɗai ya zo ba, amma har da
jini kuma. Ruhu kuma ya shaida mana cewa waɗannan abubuwan
gaskiya ne, domin Ruhun gaskiya ne. 7 Akwai abubuwa uku
waɗanda suke shaida cewa Yesu Dan Allah ne. 8 Wato, su ne
Ruhun Allah, ruwan baftisma da jininsa wanda ya zubar saboda
mu. Waɗannan abubuwa uku kuwa suna faɗin abu ɗaya ne.[d]
9 Idan mutane suka shaida abubuwan da suka gani, mukan yarda
da abin da suka ce. To, shaidar Allah ta fi shaidar mutane ƙarfi,
kuma shi ne ya shaidi waɗannan abubuwan a kan Dansa.
10 Saboda haka duk mutumin da ya ba da gaskiya ga Dan Allah,
yana da waɗannan shaidu waɗanda suke zuwa daga wurin Allah,
a zuciyarsa. Amma duk mutumin da bai gaskata da Allah ba, ya
mai da Allah mai yin ƙarya ke nan, da yake ya ƙi yă ba da gaskiya
ga shaidar da Allah ya yi a kan Dansa. 11 Wannan kuma ita ce
shaidar cewa Allah ya ba mu rai na har abada, wannan rai kuwa
ya zo ne daga wurin Dansa. 12 Duk wanda yana da Dan, yana da
rai. Amma duk wanda ba shi da Dan Allah, ba shi da rai.

Rai na har Abada

13 Ku masu ba da gaskiya cikin Dan Allah, na rubuta muku
waɗannan abubuwan duka ne don ku san kuna da rai na har
abada. 14 Muna da ƙarfin zuciya mu tsaya a gabansa, domin
mun san cewa yana jinmu kullum idan muka roƙe shi kome
bisa ga nufinsa. 15 Da yake mun san yana jinmu kowane lokacin
da muka roƙe shi wani abu, mun san cewa za mu sami abin da
muka roƙe shi ke nan.

16 Idan wani ya ga ɗan'uwansa yana yin zunubin da ba ya kai
ga mutuwa, bari mutumin nan yă yi wa mai zunubin nan addu'a.
Saboda mai addu'an nan kuwa Allah zai ba mai zunubin nan rai.
Amma dai, in abin nan da ya yi irin zunubin da yake kai mutane
mutuwa ne, ban ce a yi addu'a game da wannan ba. 17 Duk rashin
adalci zunubi ne, amma akwai waɗansu zunubai da ba sa kai ga
mutuwa.

5.11: Yoh 3.36

[d] **5.7,8** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da aya 7 kamar haka;
"Akwai abubuwa uku da sun shaida daga sama, Uba, Ƙalma da kuma Ruhu
Mai Tsarki, kuma dukan waɗannan ɗaya ne. 8 kuma akwai abubuwa uku da
sun ba da shaida a duniya . . ."

18 Mun san cewa duk 'ya'yan Allah, ba sa cin gaba da yin
zunubi, domin Ɗan Allah yana tsare su, don kada Shaiɗan yă
taɓa su.
19 Mun sani mu 'ya'yan Allah ne, ko da yake duniya duka
tana hannun Shaiɗan.
20 Mun san cewa Ɗan Allah ya zo duniya, ya kuma ba mu
ganewa domin mu san shi wanda yake na gaskiya. Mu kuwa muna
cikinsa, shi da yake Allah na gaskiya wato, cikin Ɗansa Yesu
Almasihu. Shi ne Allah na gaskiya da kuma rai na har abada.
21 Ya ku 'ya'yana ƙanana, ina gaya muku ku lura da kanku
don kada ku bi gumaka.

WASIKA TA BIYU TA
YOHANNA

Gabatarwa

Yohanna ya rubuta wasiƙan nan ta biyu tsakanin shekara ta A.D.85
da 95 domin yă gargaɗi masu bin da suke sauraron malamai masu
yawo suna koyarwa. Wasiƙar ta nuna cewa a cikin malaman nan akwai
masu koyarwar gaskiya da masu koyarwar ƙarya. Ta ce dole su yarda
cewa Almasihu ya zo duniya cikin jiki. Wasiƙar kuma ta yi magana
game da muhimmincin ƙauna a cikin rayuwar masu bi. Ta nuna a fili
cewa gaskiya da ƙauna suna tafiya tare.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1-3
Muhimmincin ƙauna 4-6
Jan kunne game da malaman ƙarya 7-11
Maganar ƙarshe 12-13

Gaisuwa

1 Daga dattijon nan zuwa ga uwargida wadda Allah ya zaɓa
da kuma 'ya'yanta, waɗanda nake ƙauna ƙwarai da gaske. Ba ni

kaɗai nake ƙaunarku ba, har ma da dukan mutanen da suka san gaskiyan nan ta Allah. 2 Wato, muna ƙaunarku saboda gaskiyan nan da take cikin zuciyarmu, kuma za ta zauna da mu har abada. 3 Alheri, da jinƙai, da salama daga wurin Allah Uba da Yesu Almasihu, Ɗan Uban, za su kasance tare da mu cikin gaskiya da ƙauna.

Bin Koyarwar Almasihu

4 Na yi farin ciki sosai da na ga cewa waɗansu a cikin 'ya'yanku suna bin gaskiyan nan, kamar yadda Allah Ubanmu ya ce mu yi. 5 Yanzu kuma ina roƙonki, uwargida, mu ƙaunaci juna duka. Wannan ba wani sabon umarni ba ne, umarnin da muke da shi ne tun daga farko. 6 Ainihin ƙauna ita ce, mu yi abin da Allah ya ce mu yi. Umarnin nan kuma da kuka ji tun daga farko, shi ne ku yi zaman ƙauna.

7 Na cè haka domin mutane da yawa masu ruɗin mutane sun fito, sun bazu ko'ina cikin duniya. Ba su yarda cewa Yesu Almasihu ya zo wannan duniya da jikin mutum ba. Irin mai koyarwan nan shi ne mai ruɗi da mai gāba da Almasihu.

8 Saboda haka ku lura, don kada dukan abin da kuka[a] yi yă zama banza, a maimako sai ku sami cikakken ladanku.

9 Duk mutumin da bai tsaya a kan koyarwar Almasihu ba, amma ya yi ƙari a kanta, mutumin nan ba shi da Allah. Amma wanda ya tsaya a kan koyarwar Almasihu, yana da Uban da kuma Ɗan. 10 Idan wani ya zo yana koyar da wani abu dabam da wannan koyarwar, kada ku karɓe shi, kada ma ku gaishe shi. 11 Domin idan wani ya gai da irin wannan mutumin, yana haɗa kai da mutumin cikin aikin zunubinsa ke nan.

Maganar Karshe

12 Ina da abubuwa da yawa waɗanda nake so in gaya muku, amma ba na so in rubuta su a wasiƙan nan, a maimako, ina fata zan sami dama in zo wurinku don mu tattauna ido da ido, ta haka za mu kasance da cikakken farin ciki. 13 'Ya'yan 'yar'uwanki wadda Allah ya zaɓa, suna gaishe ki.

5: Yoh 13.34; 15.12,17

[a] **1.8 kuka:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "muka" ne a nan.

WASIKA TA UKU TA
YOHANNA

Gabatarwa

Yohanna ya rubuta wasiƙan nan a tsakanin shekara ta A.D. 85 da 95 ne zuwa ga wani shugaban jama'ar masu bi mai suna Gayus. Wasiƙar ta yabi Gayus saboda ayyukan kirkin da yake yi, musamman yadda yakan karɓi malamai na gaskiya waɗanda Yohanna yakan aika. A wasiƙar an lura da wani mai sunan Diyotarifis da yake gāba da masu aikin Ubangiji.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1-4
An yabi Gayus 5-8
Diyotarifis da Dimitiriyus 9-12
Maganar ƙarshe 13-15

Gaisuwa

1 Daga ni dattijon nan zuwa ga Gayus abokina da nake ƙauna,
wanda nake ƙauna kwarai da gaske. 2 Ya abokina wanda nake
ƙauna, ina addu'a ka sami zaman lafiya ta kowace hanya da kuma
lafiyar jiki, kamar yadda ruhunka yake da lafiya. 3 Na yi murna
sosai sa'ad da waɗansu 'yan'uwa suka zo suka ba da shaida game
da yadda kake da aminci cikin gaskiya, da yadda kake bin
gaskiya. 4 Ba abin da ya fi sa ni farin ciki fiye da in ji cewa
'ya'yana suna bin gaskiya.

An Yabi Gayus

5 Ya abokina wanda nake ƙauna, kana da aminci a kan kome
da kake yi a madadin sauran 'yan'uwa, musamman ga waɗanda
ba ka san su ba. 6 Mutanen nan da ka taimake su suna ba da
shaida ga jama'ar masu bin da take a nan a kan irin ƙaunar da
kake yi. Ka ci gaba da taimakon irin mutanen nan a tafiye-
tafiyensu, kamar yadda zai cancanci yin hidima ga Allah.
7 Waɗannan mutanen suna fitowa ne don shelar sunan Almasihu,
ba sa kuma karɓar kome daga waɗanda ba masu bi ba. 8 Saboda

1: A. M. 19.29; Rom 16.23; 1 Kor 1.14

haka yana da kyau mu taimaki irin mutanen nan, don mu zama abokan aiki cikin gaskiya.

Diyotarifis da Dimitiriyus

9 Na rubuta wa jama'ar masu bin da take wurinka 'yar wasiƙa amma Diyotarifis ya ƙi karɓi maganarmu, domin yana neman girma. 10 Idan na zo, zan tona asirinsa, don kowa yă sani yadda yake surutu game da mu, yana baƙar magana a kanmu. Abin da ya fi muni shi ne, shi kansa ya hana masu bin da suka tafi can su zauna da shi, yana kuma hana masu son taimakonsu, har yana korarsu daga jama'ar masu bi.

11 Ya abokina wanda nake ƙauna, kada ka bi mugun hali, a maimako haka, ka bi halin kirki. Mai aikin kirki na Allah ne. Amma mai mugun aiki kuwa bai san Allah ba ko kaɗan. 12 Dimitiriyus dai, yana da shaida mai kyau wurin kowa, har gaskiya kanta ma tana yi masa shaida. Mu ma mun shaide shi, ka kuwa san shaidarmu gaskiya ce.

Maganar Karshe

13 Ina kuma da abubuwa da yawa waɗanda nake so in rubuta maka amma ba na so in rubuta su a wasiƙan nan. 14 Ina sa zuciya cewa zan zo wurinka ba da daɗewa ba, don mu ga juna ido da ido, mu kuma yi magana. 15 Bari salama ta kasance tare da kai. Dukan abokanka a nan suna gaisuwa. Ka kuma gai da duk abokanmu a can, ɗaya-ɗaya.

WASIKA TA
YAHUDA

Gabatarwa

Marubucin *Wasiƙa ta Yahuda* ya gabatar da kansa cewa shi ne Yahuda, ɗan'uwan Yakubu. Ana zato Yahuda ya rubuta wasiƙarsa a tsakanin shekara A.D. 65-67 ne.

Wasiƙar Yahuda da *Wasiƙa ta Biyu ta Bitrus* suna kama da juna sosai. Koyarwarsu tana a kan magana ɗaya, wato, yadda za a guje wa koyarwar ƙarya. Kan maganar wasiƙar Yahuda ya fita a fili sosai inda aka yi gargaɗi cewa, "Ku yi yaƙi sosai domin maganar bangaskiyarmu wadda Allah ya danƙa wa mutanensa, sau ɗaya tak, ba ƙari." An faɗa a cikin wasiƙar cewa dole ne masu bi su ƙi ƙarya, da halayen lalata, su tuna da gargaɗin da manzanni suka yi, su kuma ba da kansu ga bin gurbin Almasihu da kuma taimakon mutanensa.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1-2
Gargaɗi a kan malaman ƙarya 3-16
Gargaɗi da umarnai 17-23
Addu'ar ƙarshe 24-25

Gaisuwa

1 Daga Yahuda[a] bawan Yesu Almasihu, ɗan'uwan Yakubu,
zuwa gare ku, ku waɗanda Allah ya kira, waɗanda Allah Uba
yake ƙauna, waɗanda Yesu Almasihu yake kiyayewa.
2 Bari jinƙai, da salama, da ƙauna su zama naku a yalwace.

Hukuncin Malaman Karya
(2 Bit 2.1-17)

3 Ya ku waɗanda nake ƙauna, na yi marmarin rubuta muku
game da ceton nan namu, amma daga baya na ga ya zama dole
ne in rubuta muku don in gargaɗe ku ku yi yaƙi sosai domin
maganar bangaskiyarmu wadda Allah ya danƙa wa masu binsa,
sau ɗaya tak, ba ƙari. 4 Na faɗa wannan dai don waɗansu mutanen
da suka shiga cikinku a ɓoye. Ba su da tsoron Allah. Sun mai da

---

1: Mat 13.55; Mar 6.3
[a] 1.1 **Yahuda:** Da Helenanci "Yudas" ne; da Ibraniyanci, "Yahuda."

alherin Allah ya zama hanyar yin lalata. Sun yi mūsun Yesu Almasihu wanda shi ne kaɗai Sarkinmu da kuma Ubangijinmu. Ai, tun dā an yi annabci cewa za a hukunta su.

5 Ko da yake kun riga kun sani, ina so in tuna muku yadda Ubangiji ya ceci mutanensa daga ƙasar Masar, amma duk da haka daga baya ya halaka waɗanda ba su ba da gaskiya ba. 6 Ku tuna kuma da mala'ikun da ba su kiyaye matsayinsu na iko ba, amma suka bar wurin zamansu. Waɗannan fa Ubangiji ya tsare su a duhu, ya kuma ɗaure su da sarƙa ta har abada domin shari'a ta babbar Ranan nan. 7 Haka kuma Sodom da Gomora, da garuruwan da suke kewaye da su, su ma sun ba da kansu ga lalata da mummunar sha'awar jiki kamar yadda mala'ikun suka yi. Sun zama misalin waɗanda suke shan horon wuta ta har abada.

8 Haka yake da masu mafarke-mafarken nan gama sukan ƙazantar da jikinsu. Sukan ƙi bin masu mulki, sukan zargi mala'ikun Allah. 9 Ko Mika'ilu, shugaban mala'iku bai yi irin wannan ba. A lokacin da yake gardama da Shaiɗan, suna mūsu a kan gawar Musa, shi Mika'ilu bai yi garajen yi masa zargi da baƙar magana ba. Ya ce kawai, "Ubangiji yă tsawata maka!" 10 Amma waɗannan mutane suna zargin dukan abin da ba su gane ba, kuma waɗannan abubuwan da suka sani bisa ga jiki, kamar dabbobi marasa hankali, irin waɗannan abubuwan ne za su kai su ga halaka.

11 Kaitonsu! Sun bi halin Kayinu. Domin neman riba sun fāɗi cikin kuskure irin na Balaam;[b] sun halaka ta wurin tawaye irin na Kora.[6]

12 Waɗannan mutane, zamansu a cikin taronku na ƙauna mummunan abu ne, suna ciye-ciye ba kunya ba tsoro. Su masu kiwo ne da suke ciyar da kansu kawai. Suna nan kamar hadari wanda iska takan kora, amma ba ruwa a ciki. Suna kamar itatuwa marasa 'ya'ya da rani, ko kamar itatuwan da aka tumɓuke, kuma sun mutu gaba ɗaya. 13 Su kamar raƙuman ruwan teku ne masu tashi sama cikin hauka, suna taƙama da abubuwan kunya waɗanda suke kumfa ne kawai. Su kamar taurari ne masu yawo barkatai,[c] waɗanda aka yi musu ajiyar mummunan duhu na har abada.

5: Fit 12.51; L. Kid 14.29-30 7: Far 19.1-24
9: Dan 10.13,21; 12.1; R. Yoh 12.7; M. Sh 34.6; Zak 3.2 11: Far 4.3-4; 1 Yoh 3.12

[b] **1.11 kuskure irin na Balaam:** Balaam ya karɓi kuɗi don yă yi annabcin ƙarya. (L Kid 22—24; 2 Bit 2.15; R.Yoh 2.14)

[6] 1.11 L. Kid 16.1-35

[c] **1.13 taurari masu yawo barkatai:** A zamanin Yahuda, masu tafiya da jiragen ruwa cikin dare sukan dubi taurari don su san inda za su. Amma idan tauraro bai tsaya a wuri ɗaya ba, ba shi da amfani.

14 Enok[d] ma, wanda yake na bakwai daga Adamu, shi ma ya
yi annabci a kan wadannan mutane cewa, "Duba dai, Ubangiji
yana zuwa da dubban mala'ikunsa, 15 don yă aikata hukuncinsa a
kan kowa. Zai nuna wa marasa bin Allah dukan aikinsu na rashin
bin Allah. Zai tone dukan bakaken maganganun da masu zunubi
marasa bin Allah suka fada game da shi." 16 Wadannan mutane
dai, masu gunaguni ne, kullum suna ganin laifin wadansu.
Muguwar sha'awa kadai ita ce tunaninsu. Sun cika da banzar
magana ta yabon kansu. Suna rudîn mutane da zakin baki don
samun riba ta kansu.

Gargadî da Umarnai

17 Amma ya ku wadanda nake kauna, ku tuna da abin da
manzannin Ubangijinmu Yesu Almasihu suka fada a dā cewa zai
faru. 18 Sun fada muku cewa, "A zamanin karshe za a yi wadansu
mutane masu ba'a, wadanda za su bi irin tasu sha'awa wadda ba
ta Allah ba. 19 Su ne mutane wadanda sukan kawo rabuwa, masu
bin sha'awar jiki. Ba su da Ruhun Allah."

20 Amma ya ku wadanda nake kauna, ku yi ta gina kanku a
kan bangaskiyarku nan mai tsarki. Ku kuma yi addu'a ta ikon
Ruhu Mai Tsarki. 21 Ku zauna cikin kaunar Allah, kuna jiran
Ubangijinmu Yesu Almasihu wanda cikin jinkansa zai kai ku ga
rai na har abada.

22 Ku rika nuna halin tausayi[d] ga wadanda suke shakka. 23 Ku
cece wadansu kamar kuna fizge su daga cikin wuta. Wadansu
kuwa, ku ji tausayinsu, amma tare da tsoro, har ma ku yi kyamar
tufafin da suka ɓata da ayyukansu na jiki.

Addu'ar Yabo

24 To, yabo yă tabbata ga wanda yake da iko yă tsare ku daga
fāduwa, yă kuma mika ku marasa laifi a gaban daukakarsa da
farin ciki sosai. 25 Gare shi kuma, wanda shi kadai yake Allah
mai cetonmu, ta wurin Yesu Almasihu Ubangijinmu: daukaka da
daraja da mulki da iko su zama nasa tun daga farkon zamanai,
da yanzu, da kuma har abada! Amin.

18: 2 Bit 3.3

[d] **1.14 Enok:** Ba Enok na zuriyar Kayinu ba ne (Far 4.17) amma na Set (Far 5.18-24; 1 Tar 1.1-3).

[d] **1.22 Ku rika nuna halin tausayi:** Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "ku rinjayi" ne a nan.

RU'UYAR

DA AKA YI WA YOHANNA

Gabatarwa

Marubucin wannan littafin shi ne wani mai suna Yohanna. Ana zato an gama rubutun wannan littafin kafin shekara A.D. 100 lokacin da masu bi suke shan tsanani daga hannun masu mulki saboda bangaskiyarsu cikin Yesu Almasihu. Marubucin wannan littafin ma ya sha tsanani wanda ya kai har aka kore shi ƙarfi da yaji zuwa tsibirin Batmos. A tsibirin nan ne ya karɓi wannan ru'uya.

An rubuta wannan littafin domin a ƙarfafa masu bi su cika da bege, su kuma kasance da aminci cikin lokacin tsanani.

Littafin ya nuna hoton abin da zai faru a zamanin ƙarshe. Littafin dai ya kasu kashi uku kamar haka: (1) Akwai mugayen ikokin da suke aiki a duniya. Masu bi kuma za su sha wuya har su mutu. (2) Yesu Ubangiji ne, zai kuma ci nasara a kan dukan abin da yake gāba da Allah. (3) Allah zai ba da lada ga dukan mutanensa, waɗanda suka yi aminci.

Abubuwan da Suke Ciki

Gabatarwa 1.1-3
Gaisuwa zuwa ga jama'un masu bi guda bakwai 1.4-8
Ru'uyar Almasihu 1.9-20
Wasiƙu zuwa jama'un masu bi guda bakwai 2.1—3.22
Sujada a sama 4.1-11
Naɗaɗɗen littafi da Ɗan Rago 5.1—8.1
Ƙahoni bakwai 8.2—11.19
Mace da Maciji 12.1-18
Dabbobi biyu 13.1-18
Ru'uyoyi dabam-dabam 14.1—15.8
Kwanoni bakwai na fushin Allah 16.1-21
Nasara a kan masu gāba da Allah 17.1—20.10
Hukunci na ƙarshe 20.11-15
Sabuwar sama, da sabuwar ƙasa, da kuma sabuwar Urushalima 21.1—22.5
Maganar ƙarshe 22.6-21

Gabatarwa

1 [1] Wannan littafin ya ƙunshi ru'uyar da Allah ya ba Yesu
Almasihu domin yă nuna wa bayinsa abin da zai faru ba da
daɗewa ba. Yesu ya aiki mala'ikansa zuwa wurin bawansa Yohanna
yă faɗa masa wannan saƙon. [2] Yohanna ya shaida dukan abin da ya
gani. Wannan shi ne rahotonsa game da saƙon da ya fito daga wurin
Allah da kuma gaskiyan da Yesu Almasihu ya bayyana. [3] Mai
albarka ne mutumin da yake karanta wannan saƙon annabci wanda
ya fito daga wurin Allah, kuma masu farin ciki ne waɗanda suke
ji suke kuma yin biyayya da abin da aka rubuta a cikin littafin nan.
Gama lokacin da waɗannan abubuwa za su faru ya yi kusa.

Gaisuwa zuwa ga Jama'un Masu Bi guda Bakwai

4 Ni, Yohanna, ina rubuta zuwa ga jama'un masu bi guda
bakwai da suke a yankin ƙasar Asiya.[a]

Alheri da salama su kasance tare da ku daga Allah wanda shi
ne yake a yanzu, shi ne a dā, shi ne kuma mai zuwa, da kuma
daga ruhohi bakwai nan da suke a gaban kursiyin Allah, [5] da kuma
daga Yesu Almasihu, wanda ya bayyana gaskiyan nan a kan Allah
cikin aminci. Shi ne Ɗan fari, wato, na farko cikin waɗanda suka
tashi daga matattu, wanda kuma yake mulki a kan dukan
sarakunan duniya.

Shi ne wanda ya ƙaunace mu, ya cece mu daga zunubanmu
ta wurin zub da jininsa. [6] Shi ne ya mai da mu mu zama masu
mulki da firistoci masu hidimar Allah Ubansa. Saboda haka bari
Yesu Almasihu yă karɓi ɗaukaka da mulki har abada abadin.
Amin.

7 Ga shi, zai zo a cikin girgije, kowa kuwa zai gan shi, har
da waɗanda suka ƙashe shi. Dukan kabilun duniya kuma za su yi
kuka a kansa. Hakika! Wannan haka yake, Amin.

8 "Ni ne farko da kuma ƙarshe," in ji Ubangiji Allah Mai Iko
duka, wanda shi ne yake a yanzu, shi ne a dā, shi ne kuma mai
zuwa.

Ru'uyar Almasihu

9 Ni Yohanna ɗan'uwanku da kuma abokin tarayyarku ne
cikin tsanani da mulki da haƙurin jimrewa waɗanda suke namu

1.4: Fit 3.14; R. Yoh 4.5 **1.5:** Ish 55.4; Zab 89.27 **1.6:** Fit 19.6; R. Yoh 5.10
1.7: Dan 7.13; Mat 24.30; Mar 13.26; Luk 21.27;
1 Tas 4.7; Zak 12.10; Yoh 19.34,37 **1.8:** Dan 7.13; 10.5

[a] **1.4 ƙasar Asiya:** Yanzu ana ce da wannan ƙasar Turkiya.

cikin Yesu. An yi mini koran dole zuwa can tsibirin da ake ce da shi Batmos don na yi wa'azin maganar Allah da gaskiyar da Yesu ya bayyana. 10 A ranar farko ta mako, da Ruhu ya sauko a kaina, sai na ji wata murya mai ƙara a bayana kamar ta ƙaho, 11 Muryar ta ce, "Rubuta abin da ka gani a littafi, ka aika wa jama'un masu bin nan guda bakwai, wato, ta Afisa, da ta Simirna, da ta Birgamum, da ta Tiyatira, da ta Sardis, da ta Filadelfiya, da kuma ta Lawudikiya."

12 Sai na juya in ga wanda yake mini magana. Da na juya kuwa sai na ga fitilu bakwai na zinariya. 13 A tsakiyar fitilun nan kuwa na ga wani kamar Dan mutum ya sa doguwar riga, ƙirjinsa kuma da ɗamarar zinariya. 14 Kansa da gashinsa sun yi fari fat kamar farin ulu, ko kuwa kamar auduga, idanunsa kamar harshen wuta, 15 ƙafafunsa suna haske kamar tagullar da aka goge, wadda aka tace a maƙera, muryarsa kuma kamar ƙarar ruwaye masu gudu. 16 Yana riƙe da taurari bakwai a hannun damarsa, daga bakinsa kuma takobi mai baki biyu mai ci sosai yana fitowa. Fuskarsa tana haske kamar rana tsaka. 17 Da na gan shi, sai na fāɗi a gabansa kamar gawa. Amma ya sa mini hannunsa na dama, ya ce, "Kada ka ji tsoro. Ni ne na farko, ni ne kuma na ƙarshe. 18 Ni ne Mai Rai! Dā na mutu, amma ga shi yanzu, ina da rai har abada abadin, ina kuwa da iko a kan mutuwa da wurin zaman matattu. 19 Sai ka rubuta abin da kake gani yanzu, da kuma abubuwan da suke shirin faruwa bayan wannan. 20 Ga ma'anar asirin taurari bakwai da ka gani a hannun damana, da kuma ta fitilun zinariya bakwai dīn: Taurari bakwai nan, mala'iku bakwai na jama'un masu bin nan ne, kuma fitilun zinariya bakwai dīn nan ma, jama'un masu bi guda bakwai nan ne.

Saƙo Zuwa ga Afisa

2 1 "Ka rubuta wa mala'ikan jama'ar masu bi na Afisa cewa: "Ga saƙo daga wannan wanda yake riƙe da taurarin nan bakwai a hannun damarsa, wanda kuma yake tafiya cikin fitilun zinariyan nan bakwai.

2 "Na san rayuwarka. Na san faman da ka yi cikin aikin bi da kuma yadda ka yi haƙuri cikin wahaloli. Na san ba za ka iya yin haƙuri da mugayen mutane ba. Ka gwada waɗanda suke ce da kansu manzanni, amma ba haka suke ba, kuma sai ka tarar cewa su na ƙarya ne. 3 Na sani kana haƙuri, kana kuma jimrewa cikin

---

1.13: Dan 7.13; 10.5 **1.14-15**: Dan 7.9; 10.6 **1.15**: Ez 1.24; 43.2
1.17: Ish 44.6; 48.12; R. Yoh 2.8; 22.13

wahala saboda sunana, kuma ba ka gaji ba. 4 Amma ga abin da nake da shi game da kai, dalilin kuwa don ka bar ƙaunar da kake yi tun farko. 5 Ka tuna da matsayinka a dā kafin ka fādi! Ka tuba daga zunubinka ka koma kan rayuwarka ta fari. In ba ka tuba ba kuwa, zan zo wurinka nan da nan in ɗauke fitilarka daga wurin zamanta. 6 Amma a wannan waje kam ka kyauta da ka ƙi ayyukan Nikolatawa kamar yadda ni ma nake ƙinsu.

7 "Duk mai kunnen ji, bari yă ji abin da Ruhu yake ce wa jama'un masu bi! Dukan wanda ya ci nasara, zan ba shi damar cin 'ya'yan itacen rai wanda yake cikin gonar Allah.

Saƙo zuwa ga Simirna

8 "Ka rubuta wa mala'ikan jama'ar masu bi na Simirna cewa:

"Ga saƙo daga wannan da yake na farko da kuma na ƙarshe, wanda ya mutu ya kuma sāke rayuwa. 9 Na san wahalolin da kake ciki. Na kuma san talaucinka, amma kana da arziki na Ruhu. Na san da mugayen maganganun da mutanen nan suke yi maka su waɗanda suke cewa su ne zaɓaɓɓun mutanen Allah, amma kuwa ba haka ba ne, su jama'ar Shaiɗan ne. 10 Kada ka ji tsoron wahalar da za ka sha. Ga shi, Mugun nan zai sa a jefa waɗansunku cikin kurkuku don a gwada ku. Za ka sha tsananin nan na kwana goma. Amma kada ka fid da zuciya cikin bangaskiya ko da za a kashe ka, domin zan ba ka rai wanda shi ne ladan nasararka.

11 "Duk mai kunnen ji, bari yă ji abin da Ruhu yake ce wa jama'un masu bi! Wanda ya ci nasara, mutuwa ta biyu ba za ta shafe shi ba ko kaɗan.

Saƙo zuwa ga Birgamum

12 "Ka rubuta wa mala'ikan jama'ar masu bi na Birgamum cewa:

"Ga saƙo daga wannan wanda yake riƙe da takobi mai baki biyu mai ci sosai. 13 Na san cewa kana zama a inda Shaiɗan yake mulki. Duk da haka ka yi biyayya da ni, kuma ba ka taɓa daina gaskata da ni ba. Ka dage cikin bangaskiya inda Shaiɗan yake mulki har zuwa lokacin da aka kashe Antifas wanda ya shaida ni da aminci a cikinku. 14 Amma ga waɗansu laifofin da ka aikata. Akwai waɗansu mutane a cikinku da suke bin koyarwar Bala'am, wanda ya koya wa Balak yă sa Isra'ilawa su yi laifi, su ci abincin da aka yi wa gumaka hadaya, su kuma yi lalata. 15 Haka ma kake

2.7: Far 2.9; R. Yoh 22.2; Ez 28.13; 31.8 2.8: Ish 44.6; 48.12; R. Yoh 1.17; 22.13
2.11: R. Yoh 20.14; 21.8 2.14: L. Kid 22.5,7; 31.16; M. Sh 23.4; L. Kid 25.1-3

da mutane waɗanda suke bin koyarwar Nikolatawa. 16 Ka tuba yanzu! In ba haka ba kuwa, zan zo maka da sauri in kuma yaƙe su da takobin da yake fitowa daga bakina. 17 Duk mai kunnen ji, bari yă ji abin da Ruhu yake ce wa jama'un masu bi. Duk wanda ya ci nasara, zan ba shi daga manna da aka ɓoye. Zan kuma ba shi farin dutse wanda aka rubuta sabon suna a bisansa wanda babu wani da ya san sunan, sai wanda yake karɓan dutsen."

Saƙo zuwa ga Tiyatira

18 Ka rubuta wa mala'ikan jama'ar masu bi na Tiyatira cewa:

"Ga saƙo daga Ɗan Allah, mai idanu kamar harshen wuta, wanda ƙafafunsa suna haske kamar tagullar da aka goge. 19 Na san rayuwarka, da ƙaunarka da amincinka. Na san hidimarka da jimrewarka. Na san cewa ayyukanka na yanzu sun fi na farko. 20 Amma ga laifin da na same ka da shi, kana haƙuri da macen nan Jezebel, wadda take ce da kanta annabiya. Ta wurin koyarwarta tana rudin bayina su yi lalata su kuma ci abincin da aka miƙa wa gumaka. 21 Na ba ta zarafi don ta tuba daga karuwancinta amma ta ƙi. 22 Ga shi zan sa ta yi mugun ciwo, in kuma sa waɗanda suke zina da ita su sha azaba mai tsanani. Zan yi haka yanzu idan ba su tuba daga mugayen ayyukan da suke yi tare da ita ba. 23 Zan kashe waɗanda suke bin koyarwarta, dukan jama'un masu bi za su sani cewa ni ne mai duba har cikin tunani da zuciyar kowa. Zan hukunta kowa gwargwadon ayyukansa.

24 "Amma sauranku a Tiyatira ba ku bi muguwar koyarwarta ba. Ba ku koyi abin da masu binta suke cewa, 'Asiran Shaiɗan masu zurfi' ba. Ina ce muku, ba zan sa muku wani nauyi ba, 25 sai dai ku riƙe bangaskiyarku sosai sai na sāke dawowa. 26-28 Duka wanda ya ci nasara, ya kuma ci gaba da yin abin da nake so har ƙarshe, zan ba shi iko da na karɓa daga wurin Uba. Zan sa yă yi mulkin al'ummai. Zai yi mulki a kansu da sandan ƙarfe, zai kuma faffashe su kamar yadda ake faffashe tukwanen laka. Zan kuma ba shi tauraron safe. 29 Duk mai kunnen ji, bari yă ji abin da Ruhu yake ce wa jama'un masu bi!

2.17: Fit 16.14-15; 16.33-34; Yoh 6.48-50; Ish 62.2; 65.15
2.20: 1 Sar 16.31; 2 Sar 9.22,30 **2.23:** Zab 7.10; 62.13; Irm 17.10
2.26-27: Zab 2.8-9

Saƙo zuwa ga Sardis

3 [1] "Ka rubuta wa mala'ikan jama'ar masu bi na Sardis cewa:
"Ga saƙo daga wannan da yake mulkin ruhohi bakwai masu
hidimar Allah, wanda kuma yake riƙe da taurarin nan bakwai. Na
san rayuwarka. Ana ganinka kamar kana da rai, amma matacce
ne kai! [2] Na gane cewa rayuwarka ta mai bi ba ta kai matsayin
da Allahna ya tsara ba. Saboda haka, ka farka daga barcinka na
ruhaniya, ka canza, ka kuma ƙarfafa sauran abin nan na halin mai
bi da ya rage, kafin yă mutu gaba ɗaya. [3] Saboda haka sai ka tuna
da gaskiyar da aka koya maka wadda kuma ka ji. Ka tuba daga
zunubinka ka kuma yi biyayya da gaskiyar. Idan kuwa ba ka farka
ba, zan zo babu tsammani, kamar ɓarawo, kuma ba za ka ma san
lokacin da zan zo maka ba. [4] Amma dai har yanzu akwai mutane
kaɗan a cikinku a Sardis waɗanda suka yi rayuwa mai tsabta.[b]
Za su yi tafiya tare da ni sanye da fararen riguna, domin suna da
damar yin haka. [5] Duk wanda ya yi nasara za a sa masa fararen
riguna. Ba zan cire sunansa daga Littafin Rai ba. Sa'ad da nake
tsaye a gaban Ubana da kuma mala'iku masu hidimarsa, zan sanar
cewa wannan mutum nawa ne. [6] Duk mai kunnen ji, bari yă ji
abin da Ruhu yake ce wa jama'un masu bi!

Saƙo zuwa ga Filadelfiya

7 "Ka rubuta wa mala'ikan jama'ar masu bi na Filadelfiya
cewa:
"Ga saƙo daga wannan da yake mai tsarki da mai gaskiya.
Shi ne magajin mabuɗin ikon sarki Dawuda, wanda in ya buɗe
babu mai rufewa, kuma in ya rufe babu mai buɗewa. [8] Na san
rayuwarka. Na kuma san ƙarfinka kaɗan ne. Ka yi biyayya da
maganata, ba ka yi mūsun sanina ba. Ga shi, na buɗe ƙofa a
gabanka wadda ba mai iya rufewa. [9] Ga shi, mutanen nan da
suke na ƙungiyar Shaiɗan, masu cewa su ne zaɓaɓɓun mutanen
Allah amma kuwa ba haka suke ba, suna ƙarya ne. Zan sa su
su zo su yi maka sujada su kwanta da fuskarsu a ƙasa a gabanka
su kuma gane cewa ina ƙaunarka. [10] Da yake ka kiyaye
maganata ta wurin jimrewa da ka yi, zan tsare ka daga lokacin
tsananin nan wanda zai zo wa duniya don a gwada dukkan
mutanen duniya. [11] Ina zuwa nan da nan. Ka riƙe bangaskiyarka

3.3: Mat 24.43-44; Luk 12.39-40; R. Yoh 16.15
3.5: Fit 32.32-33; Zab 69.29; R. Yoh 20.12; Mat 10.32; Luk 12.8
3.7: Ish 22.22; Ayu 12.14 **3.9:** Ish 49.23; 60.14; 43.4

[b] 3.4 **rayuwa mai tsabta:** Da Helenanci an rubuta "ba su ƙazantar da tufafinsu ba" ne a nan.

sosai sosai, domin kada wani yă ƙwace ladan nasararka.[6]
12 Dukan mutumin da ya ci nasara zan mai da shi ginshiƙi a
haikalin Ubana. Wannan mutum ba zai taɓa barin wurin ba. A
kansa zan rubuta sunan Allahna da na sabuwar Urushalima,
wadda take sunan birnin Allahna, wadda za ta sauko daga wurin
Allahna a sama. Zan kuma rubuta sabon sunana a kansa. 13 Duk
mai kunnen ji, bari yă ji abin da Ruhu yake ce wa jama'un
masu bi!

Saƙo zuwa ga Lawudikiya

14 "Ka rubuta wa mala'ikan jama'ar masu bi na Lawudikiya
cewa:

"Ga saƙo daga wannan da ake ce da shi Amin. Shi ya bayyana
gaskiyar Allah da aminci, kuma ta wurinsa ne Allah ya halicci
dukkan abubuwa. 15 Na san rayuwarka, ba sanyi kake ko zafi ba.
Da ma a ce kana da sanyi ko zafi mana! 16 Amma saboda kana
tsaka-tsaka, ba ka a sanyi ko a zafi, zan tofar da kai daga bakina.
17 Gama ka ce, 'Ina da arziki, ina da dukiya, ba na bukatar kome.'
Ashe ba ka sani ba kai matsiyaci ne, abin tausayi! Kai matalauci
ne, kana tsirara, makaho kuma. 18 Saboda haka, ina ba ka shawara
ka sayi zinariya daga gare ni, zinariyar da aka tace da wuta, don
ka sami arziki na ruhaniya, da kuma fararen riguna ka sa wa kanka
domin ka rufe kunyar zaman tsirararka. Ka kuma sayi maganin ido
daga gare ni ka sa a idanunka, domin ka iya gani sosai. 19 Nakan
tsawata in kuma hori wanda nake ƙauna. Saboda haka sai ka ɗauki
niyya sosai ka kuma tuba. 20 Ga ni nan tsaye a bakin ƙofa ina
ƙwaƙwasawa. Duk wanda ya ji muryarta ya kuma buɗe ƙofar, zan
shiga in kuma ci abinci tare da shi, shi kuma tare da ni. 21 Duk
wanda ya ci nasara, zan sa yă zauna tare da ni a kursiyina, kamar
yadda ni ma na ci nasara na zauna tare da Ubana a kursiyinsa.
22 Duk mai kunnen ji, bari yă ji abin da Ruhu yake ce wa jama'un
masu bi!"

Sujada a Sama

4 1 Bayan wannan, na sāke ganin wata ru'uya, na ga wata ƙofa
a buɗe a sama. Muryan nan mai ƙara kamar ƙaho, wadda na
ji da farko ta ce, "Hauro nan, zan nuna maka abin da lallai zai
faru bayan wannan." 2 Nan take sai Ruhu ya sauko a kaina, na

3.12: R. Yoh 21.2; Ish 62.2; 65.15 **3.14:** K. Mag. 8.22
3.19: K. Mag 3.12; Ibr 12.6
[6] **3.11 ladan nasararka:** Da Helenanci an rubuta "Kambi" ne a nan.

kuma ga a can cikin sama wani kursiyi wanda wani yake zama
a kai. 3 Mai zama a kursiyin kuwa yana ƙyalli kamar duwatsu
masu daraja, wato, jasfa da kaneliya. Kewaye da kursiyin kuma
akwai wani bakan gizo mai ƙyalli kamar dutsen zumurrudu.[c]
4 Kewaye da kursiyin kuwa akwai waɗansu kursiyoyi ashirin da
huɗu, waɗanda dattibai ashirin da huɗu suka zauna a kai. Suna
sanye da farare riguna tare da rawanin zinariya a kansu. 5 Sai
walƙiya ake gani tana fitowa daga kursiyin, da ƙararraki da kuma
tsawa. A gaban kursiyin kuwa, akwai fitilu bakwai da suke ci,
waɗanda suke ruhohin nan bakwai masu hidimar Allah. 6 A gaban
kursiyin kuma akwai wani abu mai kamar tafkin gilas, yana ƙyalli
kamar madubi.

Kuma kewaye da kursiyin ta kowane gefe kuwa, akwai halittu
guda huɗu masu rai cike da idanu gaba da baya. 7 Na farkon ya
yi kamar zaki, na biyun ya yi kamar bijimi, na ukun yana da
fuska kamar na mutum, na huɗun kuma ya yi kamar gaggafa mai
firaya. 8 Kowanne daga cikin halittu huɗu nan masu rai suna da
fikafikai shida, dukan kewayen jikinsu idanu ne har da ƙarƙashin
fikafikansu. Dare da rana ba sa daina waƙa cewa:

"Mai Tsarki, Mai Tsarki, Mai Tsarki,
Ubangiji Allah Mai Iko duka!
Shi ne a dā,
shi ne a yanzu,
shi ne kuma mai zuwa."

9 Halittun nan huɗu masu rai, suka rera waƙoƙi ɗaukaka, da
girma, da godiya ga wannan da yake zama a kursiyin, yake
kuma raye har abada abadin. Duk lokacin da suke yin haka,
10 dattibai ashirin da huɗun nan sukan fāɗi a gaban wannan da
yake zama a kursiyin, sukan yi masa sujada shi wanda yake
raye har abada abadin. Sukan ajiye rawunansu a ƙasa a gaban
kursiyin, suna cewa,

11 "Ubangiji Allahnmu, ka cancanci
ka karɓi ɗaukaka, da girma, da iko.
Gama ka halicci kome da kome,
kuma ta wurin nufinka suka kasance
suka kuma rayu."

4.2-3: Ez 1.26-28; 10.1
4.5: Fit 19.16; R. Yoh 8.5; 11.19; 16.18; Ez 1.13; R. Yoh 1.4; Zak 4.2
4.6-7: Ez 1.22,5-10; 10.14 **4.8:** Ez 1.18; 10.12; Ish 6.2-3

[c] **4.3 ƙyalli kamar dutsen zumurrudu:** Da Helenanci an rubuta "mai launin emeral" ne a nan.

Nadaɗɗen Littafi da Dan Rago

5 [1] Na ga nadaɗɗen littafi a hannun dama na wannan da yake
zama a kursiyin. Nadaɗɗen littafin kuwa yana cike da rubutu
a kowane gefe, an kuma rufe shi kankan da hatimai bakwai. [2] Sai
na ga wani ƙaton mala'ika mai ƙarfi, yana shela da babbar murya
yana cewa, "Wa ya cancanci yă ɓalle hatiman nan yă kuma buɗe
littafin?"

3 Babu wani ko a sama, ko a ƙasa, ko a ƙarƙashin ƙasa wanda
ya isa yă buɗe littafin, balle yă karanta. [4] Sai na yi kuka mai zafi
domin ba a sami wanda ya cancanci yă buɗe littafin ko yă karanta
shi ba. [5] Sai ɗaya daga cikin dattiban nan ya ce mini, "Kada ka
yi kuka! Duba! Zakin nan, daga kabilar Yahuda, tushen Dawuda[d]
ya riga ya ci nasara. Yana da iko yă ɓalle hatiman nan bakwai
yă kuma buɗe littafin."

6 Sai na ga wani Dan Rago[d] yana tsaye kusa da kursiyin da
halittun nan huɗu masu rai. Dattiban nan kuwa sun kewaye su. Dan
Ragon kuwa yana tsaye kamar an yanka shi. Yana da ƙaho bakwai
da idanu bakwai, waɗanda suke ruhohi bakwai masu hidimar Allah
da aka aika a dukkan duniya. [7] Sai Dan Ragon ya je ya karɓi
nadaɗɗen littafin daga hannun dama na wannan da yake zama a
kursiyin. [8] Da ya karɓa, sai halittun nan huɗu masu rai tare da
dattibai ashirin da huɗun nan suka faɗi a gaban Dan Ragon.
Kowanne a cikinsu yana riƙe da molo da kwanon zinariya cike da
turare mai ƙamshi, waɗanda suke addu'o'in tsarkaka. [9] Suka rera
sabuwar waƙa, suna cewa,

"Ka cancanci ka karɓi nadaɗɗen littafin
ka kuma ɓalle hatimansa.
Domin dā an kashe ka,
kuma ta wurin mutuwarka ta hadaya
ka fanso wa Allah mutane daga kowace kabila, da
harshe, da jama'a, da al'umma.
[10] Ka mai da su su zama masu mulki da firistoci masu
hidimar Allahnmu,
kuma za su yi mulki a kan duniya."

11 Da na duba, sai na ji muryoyin mala'iku da sun wuce dubu
dubbai kan dubu dubbai. Suna tsaye kewaye da kursiyin, da
halittun nan huɗu masu rai, da kuma dattiban nan,

5.1: Ez 2.9-10; Ish 29.11 **5.5**: Far 49.9; Ish 11.1,10 **5.6**: Ish 53.7; Zak 4.10
5.8: Zab 141.2 **5.9**: Zab 33.3; 98.1; Ish 42.10 **5.10**: Fit 19.6; R. Yoh 1.6

[d] **5.5 Zakin nan, . . . tushen Dawuda**: Wato, Almasihu ke nan.

[d] **5.6 Dan Rago**: Wato, Almasihu ke nan.



Hoton nadadden littafi (5.11)

12 suna rerawa da babban murya suna cewa,
"Dan Ragon da aka kashe,
ya cancanci yă karɓi iko, da arziki,
da hikima, da ƙarfi, da girma,
da ɗaukaka, da yabo!"
13 Na kuma ji kowace halitta a cikin sama da ƙasa, da kuma
a ƙarƙashin ƙasa, da cikin teku, dukkan abubuwa masu rai da
suke cikinsu suna rerawa,
"Yabo, da girma, da ɗaukaka, da iko, su tabbata
ga wannan da yake zama a kursiyi,
da kuma Dan Ragon, har abada abadin!"
14 Sai halittun nan huɗu masu rai suka amsa, "Amin!" Kuma
dattiban nan suka fāɗi suka yi sujada.

Dan Ragon Ya Balle Hatiman Littafin

6 1 Sa'an nan na ga sa'ad da Dan Ragon nan ya ɓalle ɗaya
daga cikin hatiman nan bakwai. Sai na ji ɗaya daga cikin
halittun nan huɗu masu rai ya ta da wata murya mai kama da
tsawa ya ce, "Zo!" 2 Da na duba sai ga wani farin doki. Mai
hawansa yana riƙe da baka, aka kuma ba shi rawani. Ya kuma
fita kamar mai nasara domin yă ƙara cin nasara.

5.11: Dan 7.10 **6.2:** Zak 1.8; 6.3,6

3 Da Ɗan Ragon ya ɓalle hatimi na biyu, sai na ji halittar ta
biyu daga cikin halittun nan huɗu masu rai ta ce, "Zo!" 4 Sai wani
doki ya fito ja wur. Aka ba mai hawansa iko yă kawar da salama
daga duniya, don mutane su kashe juna. Aka kuma ba shi babban
takobi.

5 Da Ɗan Ragon ya ɓalle hatimi na uku, sai na ji halittar ta
uku daga cikin halittun nan huɗu masu rai ta ce, "Zo!" Da na
duba, sai na ga wani baƙin doki. Mai hawansa yana riƙe da
ma'auni a hannunsa. 6 Sai na ji wani abu mai kama da murya tana
fitowa daga cikin halittun nan huɗu masu rai tana cewa, "Mudun
garin alkama na yawan kuɗin da lebura zai samu na aiki yini
guda,[e] mudu uku na garin hatsin bale na yawan kuɗin da lebura
zai sami na aiki yini guda, amma fa kada ka lalace man zaitun
da kuma ruwan inabi!"

7 Da Ɗan Ragon ya ɓalle hatimi na huɗu, sai na ji halittar ta
huɗu daga cikin halittun nan huɗu masu rai ta ce, "Zo!" 8 Sai na
duba na ga wani doki da launinsa ya koɗe. Sunan mai hawansa
kuwa Mutuwa ce, wurin zaman matattu[f] kuma yana biye da shi.
Aka ba su iko a kan kashi ɗaya bisa huɗu na mazaunan duniya,
don su kashe su ta yin amfani da takobi, da yunwa, da annoba,
da kuma namomin daji.

9 Da Ɗan Ragon ya ɓalle hatimi na biyar, sai na ga a ƙarƙashin
bagaden rayukan waɗanda aka kashe domin sun sanar da maganar
Allah cikin aminci. 10 Sai suka ta da murya da ƙarfi suka ce, "Ya
Ubangiji Mai Iko duka, mai tsarki da kuma mai gaskiya, sai
yaushe za ka shari'anta mutanen wannan duniya, ka kuma
hukunta su saboda sun kashe mu?" 11 Sai aka ba kowannensu
farar riga, aka kuma faɗa musu su huta kaɗan sai an cika lambar
abokan aikinsu, wato, 'yan'uwansu waɗanda za a kashe kamar
yadda su ma aka kashe su.

12 Sa'an nan na kuma ga Ɗan Ragon ya ɓalle hatimi na
shida. Sai aka yi wata babbar rawar ƙasa, rana kuma ta koma
baƙa, kamar gwado na gashi, wata kuma gaba ɗaya ya juya ja
wur kamar jini. 13 Taurari kuma suka faffāɗi a ƙasa kamar yadda
'ya'yan ɓauren da ba su nuna ba suke fāɗuwa daga itace idan
iska mai ƙarfi ta hura shi. 14 Sai sararin sama ya ɓace kamar

6.4: Zak 1.8; 6.2 **6.5:** Zak 6.2,6 **6.8:** Ez 14.21
6.12: R. Yoh 11.13; 16.18; Ish 13.10;
Jow 2.10; 3.4; 4.15; Mat 24.29; Mar 13.24-25; Luk 21.25 **6.13-14:** Ish 34.4

[e] **6.6 yawan kuɗin da lebura zai samu na aiki yini guda:** Da Helenanci an rubuta "dinari ne a nan."

[f] **6.8 wurin zaman matattu:** Wato, wurin zaman waɗanda suka mutu ke nan.

yadda ake nadin tabarma,[g] aka kuma cire kowane dutse da
kowane tsibiri daga wurin da yake. 15 Sai sarakunan duniya da
masu mulki, da manyan sojoji, da masu arziki, da masu iko, da
dukkan sauran mutane, bayi da wadanda ba bayi ba, suka boye
cikin kogwanni, da kuma karkarshin duwatsu. 16 Suna kira
duwatsu suna ce musu, "Ku fado a kanmu ku kuma rufe mu
daga fuskar wannan da yake zama a kursiyi, da kuma daga
fushin Dan Ragon. 17 Gama babbar ranar fushinsu ta zo, wane
ne kuwa zai iya tsayawa?"

Mutane dubu dari da dubu arba'in da hudu (144,000) na Isra'ila

7 1 Bayan wannan, sai na ga mala'iku hudu suna tsaye a
kusurwa hudu na duniya, suka hana iskokin hudun nan na
duniya hurawa a kan kasa, ko a kan teku, ko a kan wani itace.
2 Sai na ga wani mala'ika yana hawa daga gabas, yana rike da
hatimi na Allah mai rai. Da murya mai karfi ya kira mala'ikun
nan hudu wadanda Allah ya ba su iko su lalatar da duniya, da
kuma teku. 3 Mala'ikan ya ce, "Kada ku lalatar da duniya, ko
teku, ko itatuwa, sai mun sa wa bayin Allah lambar shaida a
goshinsu."

4 Sai na ji yawan wadanda aka sa musu lambar shaida, sun
kai dubu dari da dubu arba'in da hudu[h]. Su kuwa daga kabilu
goma sha biyu na Isra'ila ne.

5 An yi wa dubu goma sha biyu daga kabilar Yahuda,
dubu goma sha biyu daga kabilar Ruben,
dubu goma sha biyu daga kabilar Gad,
6 dubu goma sha biyu daga kabilar Asher,
dubu goma sha biyu daga kabilar Naftali,
dubu goma sha biyu daga kabilar Manasse,
7 dubu goma sha biyu daga kabilar Simiyon,
dubu goma sha biyu daga kabilar Lawi,
dubu goma sha biyu daga kabilar Issakar,
8 dubu goma sha biyu daga kabilar Zebulun,
dubu goma sha biyu daga kabilar Yusufu, da kuma
dubu goma sha biyu daga kabilar Benjamin.

6.14: R. Yoh 16.20 **6.15:** Ish 2.19,21 **6.16:** Hos 10.8; Luk 23.30
6.17: Jow 2.11; Mal 3.2 **7.1:** Irm 49.36; Dan 7.2; Zak 6.5 **7.3:** Ez 9.4,6

[g] **6.14 tabarma:** Da Helenanci an rubuta "littafi" ne a nan.

[h] **7.4 dubu dari da dubu arba'in da hudu:** Wannan lambar tana kwatanta dukan wadanda suka ba da gaskiya ga Almasihu ne.

Babban Taron Tsarkaka a Sama

9 Bayan wannan, na duba sai na ga wani babban taro na
tsarkaka da yawa da ya wuce gaban ƙirge. Sun fito daga kowace
al'umma, da kabila, da jama'a, da harshe, suna tsaye a gaban
kursiyin da kuma a gaban Ɗan Ragon. Suna sanye da fararen
riguna, kuma suna riƙe da reshen itacen dabino a hannunsu.
10 Suka ta da murya da ƙarfi suna cewa, "Ceto ya fito daga wurin
Allahnmu ne, wannan da yake zama a kursiyi da kuma daga wurin
Ɗan Ragon!" 11 Dukan mala'ikun kuwa suka tsaya kewaye da
kursiyin, da dattiban, da kuma halittun nan huɗu masu rai. Sai
suka ƒāɗi a gaban kursiyin, suka yi wa Allah sujada, 12 suna cewa,
"Amin! Yabo, da ɗaukaka, da hikima, da godiya, da girma, da
iko, da ƙarfi su tabbata ga Allahnmu har abada abadin! Amin!"
13 Sa'an nan ɗaya daga cikin dattiban ya tambaye ni ya ce,
"Waɗanne ne suna sanye da fararen riguna haka? Kuma daga ina
suka fito?" 14 Sai na ce masa, "Kai ka sani, mai girma." Sai ya ce
mini, "Waɗannan mutane su ne suka fito daga tsananin wahala. Sun
wanke rigunansu da jinin Ɗan Ragon, suka zama farare. 15 Shi ya
sa suke tsaye a gaban kursiyin Allah, kuma suna yin masa hidima
dare da rana a cikin haikalinsa. Shi da yake zama a kan kursiyin
zai kasance tare da su yă kuma tsare su. 16 Ba za su ƙara jin yunwa
ba, ba za su ƙara jin ƙishi ba, ba za su ƙara jin zafin rana ko wani
ƙuna ba sam, 17 domin Ɗan Ragon da yake wajen kursiyin zai zama
makiyayinsu, kuma zai bi da su zuwa maɓuɓɓugan ruwan rai. Allah
kuma zai share musu dukan hawaye."

Hatimi na Bakwai

8 1 Da Ɗan Ragon ya ɓalle hatimi na bakwai, sai aka yi shiru a
sama kamar rabin awa guda. 2 Sa'an nan na ga mala'iku guda
bakwai da suke tsaye a gaban Allah, aka ba su ƙaho guda bakwai.
3 Ga kuma wani mala'ika wanda yake riƙe da ɗan kwanon zinariya
na turare mai ƙamshi ya zo ya tsaya a gaban bagaden. Aka ba shi
turare mai yawa domin yă haɗa da addu'o'i na dukkan tsarkakan
Allah, yă kuma miƙa shi a kan bagaden zinariyar da yake gaban
kursiyin. 4 Hayaƙi na turaren kuwa tare da addu'o'in tsarkaka suka
tashi daga hannun mala'ikan, suka hau zuwa gaban Allah. 5 Sai
mala'ikan ya ɗauki ɗan kwanon turaren, ya cika shi da wuta daga
bagaden, ya jefar da shi a duniya. Sai aka yi tsawa, da ƙararraki,
da walƙiya, da kuma rawar ƙasa.

7.14: Dan 12.1; Mat 24.21; Mar 13.19 **7.16:** Ish 49.10
7.17: Zab 23.1; Ez 34.23; Zab 23.2; Ish 49.10; 25.8 **8.3:** Amos 9.1; Fit 30.1,3

Kahoni Huɗu na Farko

6 Sa'an nan mala'ikun nan bakwai masu ƙahonin nan suka yi
shiri su busa su.

7 Mala'ika na farko ya busa ƙahonsa. Sai ga ƙanƙara da wuta,
gauraye da jini aka zubar da su a duniya. Wutar kuma ta cinye
kashi ɗaya bisa uku na duniyan, ta kuma cinye kashi ɗaya bisa
uku na itatuwa na wannan sashe da tsire-tsirensa.

8 Mala'ika na biyu ya busa ƙahonsa, sai ga wani abu mai kama
da babban tsauni mai tsawo, mai cin wuta, an jefar da shi cikin
teku. Sashi ɗaya bisa uku na tekun ya juya ya zama jini, 9 kashi
ɗaya bisa uku na halittu masu rai na wannan sashi tekun suka mutu,
kuma kashi ɗaya bisa uku na jiragen ruwan da suke a wurin suka
halaka.

10 Sa'an nan mala'ika na uku ya busa ƙahonsa. Sai ga wani
babban tauraro mai cin wuta kamar cukwima ya sauko daga sama,
ya fāɗi a kan kashi ɗaya bisa uku na koguna da kuma a kan
maɓuɓɓugan ruwa.

11 Sunan tauraron nan kuwa "Ɗaci" ne. Kashi ɗaya bisa uku
na ruwan ya juya ya zama da ɗaci, mutane da yawa da suka sha
ruwan suka mutu, don ɗacinsa.

12 Daga nan sai mala'ika na huɗu ya busa ƙahonsa. Sai aka bugi
sashi ɗaya bisa uku na rana, sashi ɗaya bisa uku na wata, da kuma
sashi ɗaya bisa uku na taurari, har sashi ɗaya bisa uku na haskensu
ya zama duhu. Ta haka sai ya zama babu haske a kashi ɗaya bisa
uku na yini, haka kuma kashi ɗaya bisa uku na dare.

13 Sa'an nan da na duba, sai na ji wata gaggafa wadda take
firaya a tsakiyar sararin sama tana kuka da ƙarfi, tana cewa,
"Kaito! Kaito! Kaito, ga dukan waɗanda suke zama a duniya,
sa'ad da an busa sauran ƙahonin nan da mala'ikun nan uku suke
shirin busawa!"

Kaho na Biyar

9 1 Mala'ika na biyar ya busa ƙahonsa. Sai na ga tauraro ya
fāɗo daga sama har ƙasa, aka kuma ba shi mabuɗin marufin
rami mai zurfin nan.[i] 2 Tauraron kuwa ya buɗe ramin, sai wani
hayaƙi ya fito kamar wanda yake daga babbar matoya, har
hayaƙin ya sa rana da sararin sama suka yi duhu. 3 Sai fāri

8.5: L. Fir 16.12; Ez 10.2; Fit 19.16; R. Yoh 11.19; 16.18
8.7: Fit 9.23-25; Ez 38.22 **8.10**: Ish 14.12 **8.11**: Irm 9.14
8.12: Ish 13.10; Ez 32.7; Jow 2.10; 3.4; 4.15 **9.2**: Far 19.28

[i] **9.1 rami mai zurfin nan**: Wato, cikin ramin inda aka kulle aljanu sai ran da za a yi musu hukunci na ƙarshe.

suka fito daga cikin hayaƙin, suka sauko duniya, aka kuma ba su irin iko na harbi daidai da na kunamai. 4 Aka umarce su kada su yi wa ciyawa ɓarna, ko itatuwa, ko kuma wani tsiro, sai dai mutane waɗanda ba su da lambar shaida ta Allah a goshinsu. 5 Ba a ba su damar kashe mutanen nan ba, sai dai su gwada musu azaba na wata biyar. Zafin wannan azabar ya yi kama da zafin harbin kunama. 6 Cikin waɗannan watanni biyar kuwa mutane za su so su mutu, amma ba za su samu ba, za su yi marmarin mutuwa, amma mutuwa za ta ƙi zuwa.

7 Fārin sun yi kamar dawakan da aka shirya don yaƙi, suna da wani abu kamar rawanin zinariya a kansu, kuma fuskokinsu sun yi kama da na mutane. 8 Gashinsu ya yi kama da na kan mata, haƙoransu sun yi kama da na zaki. 9 An rufe ƙirjinsu da wani abu mai kama da rigunan ƙarfe, fikafikansu suna ƙara kamar surutun dawakai masu karusai da suke rugawa a guje zuwa yaƙi. 10 Suna da wutsiya, suna harbi kamar kunamai, suna da ikon jin wa mutane ciwo har wata biyar. Wannan ikon kuwa a wutsiyarsu yake. 11 Suna da sarkin da yake mulki a kansu, shi ne mala'ikan nan da aka ba shi iko a kan ramin mai zurfin nan. Sunansa da Ibraniyanci "Abaddon" ne, da Helenanci kuwa "Afolliyon" wato, "Mai Ɓarna".

12 Bala'i, na farko ya wuce, bayan wannan akwai saura guda biyu masu zuwa.

Kaho na Shida

13 Sa'an nan mala'ika na shida ya busa ƙahonsa. Sai na ji murya tana fitowa daga kusurwa huɗu na bagaden zinariyar da yake a gaban Allah. 14 Muryar ta ce wa mala'ika na shida nan, "Ka saki mala'iku guda huɗun nan da suke a ɗaure a babban kogin Yuferitis!" 15 Sai aka saki mala'iku huɗun nan waɗanda aka shirya domin wannan awar na wannan ranar na wannan watan da kuma na wannan shekarar domin su kashe kashi ɗaya bisa uku na dukan 'yan Adam. 16 Sai ga sojoji masu yawa a kan dawakai. An sanar da ni yawan sojojin nan, sun kai miliyan ɗari biyu. 17 A cikin ru'uyata kuma, na ga dawakai da kuma masu hawansu, suna sanye da rigunan ƙarfe masu launin ja wur kamar wuta, da shuɗi da kuma ruwan rawaya kamar farin wuta. Kowane doki kuwa yana da kai kamar na zaki, wuta kuma da hayaƙi da farin wuta suna fitowa daga bakinsu. 18 Da waɗannan bala'i uku aka kashe

9.3: Fit 10.12-15 **9.4:** Ez 9.4 **9.6:** Ayu 3.21; Irm 8.3 **9.7:** Jow 2.4 **9.8:** Jow 1.6 **9.9:** Jow 2.5 **9.13:** Fit 30.1-3

kashi ɗaya bisa uku na 'yan Adam, wato, da wuta, da hayaƙi, da kuma farin wutan da yake fitowa daga bakin dawakan nan. 19 Gama ikon dawakan nan yana a bakinsu ne da kuma wutsiyarsu. Wutsiyarsu kamar macizai masu kai ne, suna kuma yin amfani da su don su ji wa mutane ciwo.

20 Sauran 'yan Adam da ba a kashe da waɗannan bala'i ba kuwa, ba su tuba sun rabu da abubuwan da suka yi da hannunsu ba. Wato, ba su daina yi wa aljanu sujada ba, ba su kuwa daina yin sujada wa gumakar da aka yi da zinariya, ko azurfa, ko tagulla, ko dutse, ko itace ba, waɗanda ba sa iya gani, ko su ji, ko su yi tafiya. 21 Ba su kuma tuba daga kisankai da suke yi ba, ko sihirinsu, ko halayen lalatarsu, ko sace-sacensu ba.

Mala'ika da Dan Karamin Littafi

10 1 Sa'an nan na sāke ganin wani ƙaton mala'ika mai ƙarfi yana saukowa daga sama. An lulluɓe shi cikin girgije, yana kuma da bakan gizo a kansa, fuskarsa ta yi kamar rana, ƙafafunsa kuma kamar ginshiƙai na wuta. 2 Yana da wani ɗan ƙaramin littafi wanda yake a buɗe a hannunsa. Ya sa ƙafarsa ta dama a kan teku, ƙafarsa ta hagu kuwa a kan ƙasa. 3 Ya yi kira da murya mai ƙarfi wadda ta yi ƙara kamar kukan zaki. Bayan ya yi kiran, sai tsawa bakwai suka amsa da babban ƙara. 4 Da tsawa bakwai nan suka yi ƙara, na yi shiri in rubuta, amma sai na ji murya ta yi magana daga sama ta ce, "Abin da tsawa bakwai nan suka faɗa asiri ne! Kada ka rubuta shi!"

5 Sa'an nan mala'ikan nan da na gani a tsaye a kan teku da kuma a kan ƙasa ya ɗaga hannun damarsa sama, 6 ya rantse da sunan wannan da yake raye har abada abadin, wanda ya halicci sama da dukan abin da yake cikinsa, da ƙasa da dukan abin da yake cikinta, da teku da dukan abin da yake cikinsa. Mala'ikan ya ce, "Babu sauran ɓata lokaci kuma! 7 Amma a lokacin da mala'ika na bakwai zai busa ƙahonsa ne za a cika asirin nan na Allah, kamar yadda ya sanar wa bayinsa annabawa."

8 Sa'an nan na ji muryan nan da dā na ji daga sama ta sāke yi mini magana cewa, "Je ka, ka karɓi littafin nan da yake buɗe a hannun mala'ikan da yake tsaye a kan teku da kuma a kan ƙasa." 9 Sai na je wurin mala'ikan na ce masa yă ba ni ɗan littafin. Shi kuwa ya ce mini, "Ka karɓa ka ci; zai zama da ɗaci a cikinka, amma a bakinka zai zama da zaƙi kamar zuma."

9.20: Zab 115.4-7; 135.15-17; Dan 5.23
10.5-7: Fit 20.11; M. Sh 32.40; Dan 12.7; Amos 3.7

10 Sai na karɓi ɗan ƙaramin littafin daga hannunsa, na cinye. Sai ya yi zaƙi kamar zuma a bakina, amma bayan da na hadiye, sai ya koma ɗaci a cikina. 11 Sa'an nan aka sāke faɗa mini cewa, "Dole ne kuma ka yi annabci game da jama'a iri-iri, da al'ummai masu yawa, da harsuna dabam-dabam, da kuma sarakuna masu yawa."

Shaidu Biyu na Allah

11 1 Sa'an nan aka ba ni wani ma'auni kamar sanda, aka kuma ce mini, "Je ka auna haikalin Allah da bagaden, ka kuma ƙirga waɗanda suke sujada a ciki. 2 Amma kada ka auna fili na farko na haikalin, ka ƙyale shi domin an ba da su ga waɗanda ba su san Allah ba waɗanda za su tsananta wa birnin nan mai tsarki har watanni arba'in da biyu. 3 Zan aiko da shaiduna guda biyu sanye da rigunan makoki, za su kuma yi shelar maganata har kwana dubu ɗaya da ɗari biyu da sittin."

4 Waɗannan shaidu biyun kuwa su ne itatuwan zaitun ɗin nan guda biyu da fitilun nan biyu da suke tsaye a gaban Ubangiji na dukan duniya. 5 Idan wani ya yi ƙoƙarin halaka su, wuta za ta fito daga bakinsu ta halaka masu gāba da su; ta haka ne dukan mai niyyar halaka su za a kashe shi. 6 An ba su iko su kulle sararin sama don kada a yi ruwan sama a kwanakin da suke shelar maganata. Suna da iko kuma a kan maɓuɓɓugan ruwa, su mai da su jini; suna kuma da iko su kawo wa duniya kowane irin bala'i, a duk lokacin da suke so.

7 Bayan sun gama sanar da saƙonsu, wata dabba mai fitowa daga rami mai zurfin nan za ta yaƙe su. Dabbar kuwa za ta ci nasara a kansu, ta kuma kashe su. 8 Za a bar gawawwakinsu a kan titin babban birnin nan da aka gicciye Ubangijinsu. Ana kwatanta birnin nan da suna Sodom, ko Masar. 9 Jama'a da kabilu, da harsuna da al'ummai za su zuba wa gawawwakin ido har kwana uku da rabi, su kuwa hana a binne su. 10 Mutanen duniya za su yi murna saboda mutuwar shaidu biyun nan. Za su yi biki, suna a'aika wa juna kyautai domin annabawa biyun nan da sun kawo wa mazaunan duniya wahala. 11 Amma bayan kwana uku da rabi ɗin, sai numfashi mai ba da rai ya zo daga wurin Allah ya shiga cikinsu, sai suka tashi tsaye. Tsoro mai yawa ya kama waɗanda suka gan su. 12 Sai annabawan nan biyu suka ji wata murya mai ƙarfi ta yi musu magana daga sama ta

---

10.8-10: Ez 2.8—3.3 **11.1** Ez 40.3; Zak 2.5-6 **11.2** Luk 21.24
11.4: Zak 4.3,11-14 **11.6:** 1 Sar 17.1; Fit 7.17-19; 1 Sam 4.8
11.7: Dan 7.7,21; R. Yoh 13.5-7; 17.8 **11.8:** Ish 1.9-10 **11.11:** Ez 37.10

ce, "Ku hauro nan!" Sai suka tafi sama cikin girgije, abokan gābansu suna gani. 13 Nan take sai aka yi wata babbar rawar ƙasa, sai kashi ɗaya bisa goma na garin ya nutse, aka kashe mutum dubu bakwai. Sauran mutanen kuwa suka ji tsoro ƙwarai, suka ɗaukaka Allah na sama.

14 Bala'i na biyu ya wuce, ga kuma bala'i na uku yana zuwa nan da nan.

Kaho na Bakwai

15 Sai mala'ika na bakwai ya busa ƙahonsa, sai aka ji muryoyi masu ƙarfi a sama suna cewa, "Ikon mulki a kan duniya yanzu ya zama na Ubangijinmu da Almasihunsa, zai kuma yi mulki har abada abadin!" 16 Sai dattibai ashirin da huɗun nan da suke zaune a kursiyinsu a gabansa suka fāɗi a gaban Allah, suka yi sujada,

17 suna cewa,

"Mun gode maka, ya Ubangiji Allah Mai Iko duka,
wanda kake a yanzu,
kai ne kuma a dā,
saboda ka ɗauki ikonka mai girma
kana mulki.

18 Waɗanda ba su san Allah ba sun cika da fushi,
domin lokacin fushinka ya zo,
lokaci ya yi da za a yi wa matattu shari'a,
a kuma ba da lada ga bayinka,
annabawa da tsarkaka da kuma dukan mutanen da suka
girmama ka,
babba da yaro.
Lokaci ya yi da za a halaka
waɗanda suka halaka duniya!"

19 Sai aka buɗe haikalin Allah a sama, sa'an nan aka ga akwatin alkawarinsa a cikin haikalin. Sai aka yi walƙiya, da ƙararraki, da tsawa, da rawar ƙasa, da manyan ƙanƙara.

Wata Mace da Maciji

12 1 Sai aka ga wata babbar alama mai ban mamaki a sama, wata mace wadda aka ɗauki rana aka lulluɓe ta, wata kuma yana ƙarƙashin tafin ƙafarta, a kanta kuwa akwai rawanin taurari goma sha biyu. 2 Tana da ciki, tana kuma kukan haihuwa saboda azabar zafin haihuwa.

11.12: 2 Sar 2.11 11.13: R. Yoh 6.12; 16.18 11.15: Fit 15.18; Dan 2.44; 7.14,27
11.18: Zab 2.5; 110.5; 115.13 11.19: R. Yoh 8.5; 16.18,21

3 Sai aka kuma ga wata alama mai ban mamaki a sama, ga
kuwa wani ƙaton jan Maciji mai kawuna bakwai da ƙahoni goma,
da rawani a kowane kansa. 4 Sai wutsiyarsa ta ja kashi ɗaya bisa
uku na taurari ta fid da su daga sama, ta jifar da su a ƙasa. Sa'an
nan Macijin ya tsaya a gaban macen, da nufin idan ta haihu yă
cinye ɗanta. 5 Ta kuwa haifi ɗanta namiji, wanda zai yi mulkin
dukan al'ummai da sandan ƙarfe. Amma aka fizge ɗan aka kai
shi a wurin Allah da kursiyinsa. 6 Macen kuwa ta gudu zuwa daji,
zuwa wani wurin da Allah ya shirya mata, inda za a lura da ita
har kwana dubu ɗaya da ɗari biyu da sittin.

7 Sai yaƙi ya tashi a sama. Mika'ilu tare da mala'ikunsa suka
yaƙi Macijin, Macijin kuma tare da mala'ikunsa suka yi ta yaƙi.
8 Amma aka ci Macijin da yaƙi, aka kori mala'ikunsa, aka kuma
hana su zama a sama daga wannan lokaci. 9 Sai aka jefa ƙaton
Macijin nan ƙasa, wato, Macijin nan na tun dā, wanda ake ce da
shi Mugun, ko kuma Shaiɗan, wanda ya ruɗe dukan duniya. Aka
jefa shi ƙasa a duniya tare da mala'ikunsa.

10 Sai na ji wata babbar murya a sama tana cewa, "Yanzu
fa, ceto, da iko, da mulki na Allahnmu, da kuma ikon
Almasihunsa sun bayyana. Domin an jefar da wannan abokin
gāban 'yan'uwanmu ƙasa, shi da yake zargin 'yan'uwanmu a
gaban Allahnmu dare da rana. 11 Sun kuwa yi nasara a kansa
ta wurin jinin Ɗan Ragon nan da kuma ta wurin gaskiyar da
suka shaida, domin sun yarda su ba da ransu har ga mutuwa.
12 Saboda haka sai ku yi farin ciki, ya ku sammai da dukan masu
zama a ciki! Amma kaitonku duniya da teku! Domin Mugun
nan ya sauko muku, kuma ya cika da fushi domin ya san cewa
lokacinsa ya rage kaɗan."

13 Da Macijin ya gane cewa an jefa shi ƙasa, sai ya fara bin
macen nan da ta haifi ɗa namiji. 14 Amma aka ba macen nan
fikafikai biyu na babbar gaggafa domin ta tashi sama ta rabu da
macijin nan, ta je cikin daji inda aka shirya za a lura da ita har
shekara uku da rabi. 15 Sai Macijin nan ya fitar da ruwa daga
bakinsa kamar kogi bayan matar, wai don ruwan yă tafi da ita.
16 Amma ƙasa ta taimaki macen. Kasar ta buɗe bakinta ta shanye
ruwan da ya fito daga bakin macijin. 17 Sai Macijin ya ji fushin
macen ƙwarai, ya taso yă yi faɗa da sauran zuriyar macen, wato,
dukan waɗanda suke biyayya da dokokin Allah, suna kuma

12.3: Dan 7.7 12.4: Dan 8.10 12.5: Ish 66.7; Zab 2.9
12.7: Dan 10.13,21; 12.1; Yahu 9 12.9: Far 3.1; Luk 10.18
12.10: Ayu 1.9-11; Zak 3.1 12.14: Dan 7.25; 12.7

aminci da gaskiyan nan da Yesu ya bayyana. 18 Sai Macijin ya tsaya[j] a kan yashi na bakin teku.

Dabbobi Biyu Din

13 1 Sai na ga wata dabba tana fitowa daga cikin teku. Dabbar tana da ƙahoni goma, da kuma kai bakwai. A kowane ƙaho kuwa akwai rawani, kuma a kowane kai, akwai sunan da yake na reni ne ga Allah. 2 Dabbar da na gani ta yi kama da damisa, amma tana da manyan ƙafafu masu gashi sosai da dogaye kumba kamar na wata naman daji da ake ce da ita beyar, bakinta kuma ya yi kamar na zaki. Macijin kuwa ya ba dabbar ƙarfinsa, da kursiyinsa, da kuma ikonsa mai girma.

3 Daya daga cikin kawunan wannan dabba, kamar an yi masa wani rauni da zai iya kashe shi, amma raunin ya riga ya warke. Sai dabbar ta ɗauke wa dukan duniya hankali, suna ta mamaki suna binta. 4 Mutane suka yi wa Macijin nan sujada domin ya ba wa wannan dabbar ikonsa. Suka yi wa dabbar ma sujada, suna cewa, "Wa ya yi kamar wannan dabbar? Wa zai iya yaƙi da ita?"



Hoton beyar (13.2)

13.1: Dan 7.3; R. Yoh 17.3; 7-12 **13.2:** Dan 7.4-6

[j] **12.18 Sai macijin ya tsaya:** Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Sai na tsaya" ne a nan.

5 Aka ƙyale dabban nan tana ɗaga kai da maganganun reni ga
Allah, aka kuma yarda mata ta sami ikon yin mulki har watanni
arba'in da biyu. 6 Sai ta buɗe bakinta ta soma zagin Allah tana zagin
sunansa, da inda yake zama, da kuma dukan waɗanda suke zama
a cikin sama. 7 Aka ƙyale ta ta yaƙi mutanen Allah ta kuma ci nasara
a kansu. Aka kuma ba ta iko a kan kowace kabila, da jama'a, da
harshe, da al'umma. 8 Dukan mutanen da suke zama a duniya za
su yi wa dabbar sujada, sai dai waɗanda tun kafin kafawar duniya
an rubuta sunayensu a littafin rai na Dan Ragon da aka yanka.

9 "Duk mai kunne ji, bari yă ji! 10 Kowa da an nufe shi da
bauta, ga bauta za a kai shi. Kowa kuma da aka nufa a kashe da
takobi, da takobi za a kashe shi. Wannan yana bukata dagewa da
kuma sa zuciya na masu bin Allah."

11 Sai na ga wata dabbar kuma, wadda ta fito daga ƙasa.
Tana da ƙahoni biyu kamar na ɗan rago, ta kuma yi magana
kamar Macijin. 12 Ta yi amfani da dukan ikon wannan dabba
ta farko a idon dabbar. Ta sa duniya da dukan masu zama a
cikinta su yi wa dabbar ta farko sujada, wato, wannan da
rauninta ya riga ya warke. 13 Wannan dabbar ta biyu ta yi
manyan abubuwan ban mamaki, har ma ta sa wuta ta sauko
daga sama ta zuba a ƙasa a idon kowa. 14 Sai ta ruɗe dukan
mutanen da suke zama a duniya da abubuwan ban mamakin
nan da aka yarda mata ta yi a idon dabba ta farkon. Dabbar ta
ce musu su gina wata siffa don girmama wannan dabbar da aka
ji mata rauni da takobin nan kuma duk da haka ta rayu. 15 Aka
yarda wa wannan dabba ta biyu ta ba da numfashin rai ga
wannan siffar ta dabba ta farko, har siffar ta iya yin magana,
ta kuma kashe dukan waɗanda suka ƙi yi mata sujada.
16 Wannan dabba ta biyu ta sa a yi wa dukan mutane lamba a
hannunsu na dama ko a goshinsu, babba da ƙarami, mai arziki
da talaka, bawa da mai 'yanci. 17 Ta yi haka don kada wani yă
saya ko yă sayar in ba shi da lamba, wato, sunan dabbar ko
kuwa lambar sunanta. 18 Wannan abin fa yana bukata hikima.
Kowa da yake da ganewa zai iya fito da ma'anar lambar wannan
dabba, domin lambar ta sunan wani mutum ce. Lambar kuwa
ita ce 666.

13.5-6: Dan 7.8,25; 11.36 **13.7**: Dan 7.21 **13.8**: Zab 69.29
13.10: Irm 15.2; 43.11

Wakar Wadanda Suka Sami Ceto

14 [1] Sa'an nan na duba, sai na ga Ɗan Ragon yana tsaye a
kan Dutsen Sihiyona da mutanen nan dubu ɗari da dubu
arba'in da hudu, tare da shi wadanda aka rubuta sunan Ɗan Ragon
da na Ubansa a goshinsu. [2] Sai kuma na ji wata murya daga sama
mai ƙara kamar ruwa mai gudu, kamar tsawa mai ƙara sosai.
Muryar da na ji kuwa kamar masu molo ne suna kidi. [3] Suna rera
wata sabuwar waka a gaban kursiyin, a gaban halittun nan hudu
masu rai, da kuma a gaban dattiban. Babu wani da zai iya koyi
wannan waka sai mutane dubu ɗari da dubu arba'in da hudu ɗin
nan kawai, wadanda suka sami ceto daga duniya. [4] Wadannan
mutanen ne ba su taɓa ƙazantar da kansu ta wurin kwana da mata
ba, domin sun yi zaman tsabta. Su ne suke bin Ɗan Ragon ko'ina
za shi. Wadannan ne an fanshe su daga sauran mutane, su ne
kuma kamar nunan fari na amfanin gonar da za a miƙa ga Allah
da kuma Ɗan Ragon. [5] Ba a taɓa jin ƙarya a bakinsu ba, domin
su marasa laifi ne.

Sakon Mala'iku Uku

6 Sai na ga wani mala'ika yana firaya a tsakiyar sararin
sama, yana riƙe da madawwamin saƙo na Labari Mai Dadi
domin yă sanar wa mutanen duniya, wato, ga kowace al'umma,
da kabila, da harshe, da jama'a. [7] Sai ya ɗaga murya mai ƙarfi
ya ce, "Ku girmama Allah, ku kuma yabi sunansa mai girma!
Gama yanzu lokaci ya yi don yă hukunta dukan mutane. Ku yi
masa sujada, shi da ya yi sama, da ƙasa, da teku, da kuma
maɓuɓɓugan ruwa!"

8 Sai wani mala'ika, na biyu, ya bi na farkon, yana cewa, "Ta
fāɗi, Babila mai girma ta fāɗi! Ita da ta zuga dukan al'ummai
suka bugu da ruwan inabi na tsananin lalatarta!"

9 Sai kuma wani mala'ika na uku, ya biyo wadannan biyu ɗin.
Mala'ikan yana cewa da murya mai ƙarfi, "Duk wanda ya yi wa
wannan dabba da siffarta sujada, ya kuma karɓa lamba a goshinsa,
ko kuwa a hannunsa, [10] shi zai sha ruwan inabi na fushin Allah,
wanda aka shirya da duk ƙarfinsa a cikin kwaf na fushin Allah.
Za a kuwa ba shi wuya sosai da wuta, da farin wuta, a gaban
mala'iku masu tsarki da kuma a gaban Ɗan Ragon. [11] Hayakin
wutar da ake ba su wuya da shi, ya dinga tashin sama har abada
abadin. Babu sauƙi dare da rana ga wadanda suka yi wa wannan

14.1 Ez 9.4; R. Yoh 7.3 **14.5**: Zaf 3.13 **14.8**: Ish 21.9; Irm 51.8; R. Yoh 18.2
14.10: Ish 51.17; Far 19.24; Ez 38.22

dabba da siffarta sujada, da kuma dukan waɗanda aka yi musu lambar sunanta."

12 Wannan yana bukata dagewar tsarkaka, waɗanda suke biyayya da dokokin Allah, suke kuma aminci cikin bangaskiyarsu ga Yesu.

13 Sai na sāke jin wata murya daga sama tana cewa, "Rubuta wannan. Masu albarka ne waɗanda za su mutu cikin hidimar Ubangiji daga yanzu!" Ruhu ya ce, "Hakika! Za su huta daga wahalarsu, saboda sakamakon aikinsu yana bin su!"

Girben Duniya

14 Sa'an nan na duba, sai ga wani farin girgije, da wani kamar Dan mutum yana zama a kan girgijen, yana da rawanin zinariya a kansa, yana kuma da lauje mai ci sosai a hannunsa. 15 Sai wani mala'ika ya fito daga haikalin ya yi kira da murya mai ƙarfi ga wannan da yake zama a kan girgijen, yana cewa, "Ka miƙa laujenka, ka fara girbi, domin lokacin girbi ya yi, amfanin duniya ya nuna sarai." 16 Sai wannan da yake zama a kan girgijen ya wurga laujensa a kan duniya, aka kuma girbe amfanin duniya.

17 Sai wani mala'ika ya fito daga haikali a sama, shi ma yana da lauje mai ci sosai. 18 Sa'an nan wani mala'ika har yanzu, wanda yake lura da wutan bagaden ya fito daga bagaden. Ya yi kira da murya mai ƙarfi wa wancan mala'ika mai lauje, ya ce masa, "Ka miƙa laujenka ka yanka inabin daga gonar inabin duniya, domin 'ya'yansa sun nuna." 19 Sai mala'ikan ya wurga laujensa duniya, ya yanke 'ya'yan inabin daga itacen, ya jefa su cikin babbar ramin matsin inabi na fushin Allah. 20 Aka matse inabin a ramin a bayan gari, jini ya riƙa fitowa daga ramin, ya kai nisan kilomita ɗari uku, kuma zurfinsa ya kai kamar mita ɗaya da rabi.

Mala'iku bakwai da Bala'i Bakwai na Karshe

15 1 Sai na ga wata alama a sama, mai girma, mai ban mamaki kuma. Mala'iku bakwai suna nan da bala'i bakwai, waɗanda su ne na ƙarshe, domin da su ne za a bayyana fushin Allah na ƙarshe.

2 Sai na ga wani abu kamar tafkin gilas, gauraye da wuta. Na kuma ga waɗanda suka ci nasara a kan dabbar da siffarta, da kuma lambar sunanta, suna tsayawa a bakin tafkin gilas ɗin, suna

---

14.11: Ish 34.10 **14.14**: Dan 7.13 **14.15** Jow 4.13
14.20: Ish 63.3; Mak 1.15; R. Yoh 19.15

rike da molaye wadanda Allah ya ba su. 3 Suna rera wakar Musa,
bawan Allah, da kuma wakar Dan Ragon, suna cewa,
"Ayyukanka da girma suke, masu ban mamaki ya Ubangiji
Allah Mai Iko duka!
Hanyoyinka masu adalci ne,
na gaskiya kuma, ya Sarkin al'ummai! k
4 Wane ne ba zai ji tsoronka ba,
ya Ubangiji? Wane ne ba zai daukaka girmanka ba?
Kai kadai ne mai tsarki.
Dukan al'ummai za su zo,
su yi maka sujada domin kowa yana ganin hukuncinka
mai adalci."

5 Bayan wannan, sai na ga an bude Tentin Shaida, wato,
haikali a sama. 6 Mala'iku bakwai masu bala'i bakwai din nan
suka fito daga cikin haikalin, sanye da yadin lili mai tsabta da
yake haske, da kuma damarar zinariya a kirjinsu. 7 Sai daya daga
cikin halittun nan hudu masu rai ya ba wa mala'iku bakwai din
nan kwanonin zinariya bakwai cike da fushin Allah, wanda yake
raye har abada abadin. 8 Sai haikalin ya cika da hayaki da yake
fitowa daga daukakar Allah da ikonsa. Babu kuwa wanin da ya
iya shiga cikin haikalin nan sai da bala'in nan bakwai na mala'iku
bakwai din nan suka kare.

Kwanoni Bakwai na Fushin Allah

16 1 Sai na ji wata murya mai karfi tana magana daga
haikalin, tana gaya wa mala'iku bakwai din nan cewa, "Ku
je ku juye wa duniya wadannan kwanoni bakwai na fushin Allah."

2 Daga nan mala'ika na farko ya je ya juya abin da yake a
kwanonsa a kan duniya. Sai wadansu mugayen miki masu zafi
sosai suka fito a jikin mutanen da suke da lambar wannan dabba,
wadanda suka kuma yi wa siffarta sujada.

3 Mala'ika na biyu ya juye abin da yake cikin kwanonsa a kan
teku. Ruwan ya juye ya zama kamar jinin mutumin da ya mutu,
sai dukan halittu masu rai da suke cikin teku suka mutu. 4 Sai
mala'ika na uku ya juye abin da yake cikin kwanonsa a kan
koguna da maɓuɓɓugan ruwa, sai suka zama jini. 5 Na kuwa ji
mala'ikan ruwa ya ce, "Kai mai adalci ne a hukuncin nan naka

15.3: Fit 15.1 **15.4:** Irm 10.7; Zab 86.9 **15.5:** Fit 38.21
15.8: Fit 40.34; 1 Sar 8.10-11; 2 Tar 5.13-14; Ish 6.4 **16.2:** Fit 9.10
16.4: Fit 7.17-21; Zab 78.44

k **15.3 sarkin al'ummai:** Wadansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "Sarkin zamanai" ne a nan.

ya Mai Tsarki, wanda kake a yanzu, kake kuma a dā. 6 Gama
mutane sun zub da jinin tsarkaka da na annabawa, ga shi yanzu
ka ba su jini su sha. Suna samun abin da ya yi daidai da su ke
nan!" 7 Sai na ji murya daga bagaden tana cewa, "Ubangiji Allah
Mai Iko duka! Hukuncinka mai gaskiya ne, mai adalci ne kuma."

8 Daga nan sai mala'ika na huɗu ya juye abin da yake cikin
kwanonsa a kan rana, aka kuwa yarda mata ta ƙone mutane da
tsananin zafi. 9 Sai tsananin zafin nan ya ƙone mutane, har suka
zagi sunan Allah, shi da yake da iko a kan waɗannan bala'i.
Amma ba su tuba sun ɗaukaka girmansa ba.

10 Sai mala'ika na biyar ya juye abin da yake cikin kwanonsa
a kan kursiyin wannan dabba. Sai duhu ya rufe mulkin dabbar,
mutane kuwa suka ciji harshensu saboda azaba, 11 suka kuma zagi
Allah na sama saboda azabarsu da mikinsu. Amma ba su tuba
daga mugayen ayyukan ba.

12 Mala'ika na shida ya juye abin da yake cikin kwanonsa a
kan kogin Yuferitis mai girma. Sai kogin ya bushe, don a shirya
hanya wa sarakunan da za su zo daga gabas. 13 Sai na ga aljanu
uku waɗanda suka yi kama da kwaɗi. Daya yana fitowa daga
bakin Macijin nan, ɗaya kuma daga bakin wannan dabba, ɗaya
kuma daga bakin annabin nan na ƙarya. 14 Su aljanun nan ruhohi
ne da suke yi abubuwan ban mamaki. Waɗannan aljanu uku kuwa
su suke zuwa wurin dukan sarakunan duniya, su tattara su domin
yaƙi a wannan babbar rana ta Allah Mai Iko duka.

15 "Ga ni ina zuwa kamar ɓarawo! Mai albarka ne duk wanda
yake tsaro, yake kuma sanye da rigunansa, don kada yă yi tafiya
tsirara, yă ji kunya a cikin jama'a!"

16 Sai aljanun suka tattaro sarakunan nan wuri ɗaya, a wurin
da ake ce da shi Armageddon[ƙ] da yaren Ibraniyawa.

17 Mala'ika na bakwai ya juye abin da yake cikin kwanonsa
a sarari sama. Sai wata murya mai ƙarfi ta fito daga kursiyin a
cikin haikalin, tana cewa, "An gama!" 18 Sai aka yi walƙiya, da
ƙararraki, da tsawa, da kuma muguwar rawar ƙasa irin da ba a
taɓa yi ba tun halittar mutum. Babbar rawar ƙasar ce kuwa ƙwarai.
19 Babban birnin nan kuwa ya rabu kashi uku, biranen dukan
al'ummai kuwa suka rushe. Sai Allah ya tuna da Babila mai
girma, ya kuma sa ta sha daga kwaf na fushinsa mai tsananin

16.10: Fit 10.21 **16.12:** Ish 11.15 **16.15:** Mat 24.43-44; Luk 12.39-40; R. Yoh 3.3
16.16: 2 Sar 23.29; Zak 12.11 **16.18:** R. Yoh 8.5; 11.13,19

[ƙ] **16.16 Armageddon:** Ma'anar wannan suna ita ce, "Dutsen Megiddo." (Dubi L Mah 5.19; 2 Sar 23.29-30).

gaske. 20 Kowane tsibiri ya nutse, manyan tsaunuka kuma ba a ƙara ganinsu ba. 21 Manyan ƙanƙara, masu nauyi da gaske, suka fāɗo daga sama a kan mutane har mutane suka zagi Allah saboda bala'in ƙanƙara, domin bala'in ya yi muni ƙwarai!

Babbar Karuwa da wata Dabba

17 1 Sai ɗaya daga cikin mala'iku bakwai masu kwanonin bakwai ɗin nan ya zo wurina ya ce, "Zo, zan nuna maka yadda za a hukunta wannan babbar karuwa, wadda ita ce babban birnin da aka gina kusa da inda akwai ruwa mai yawa. 2 Sarakunan duniya sun yi lalata da ita, mutanen duniya kuma sukan zama kamar waɗanda sun bugu da ruwan inabi na lalatar da suka yi da ita." 3 Sai Ruhu ya sauko a kaina, mala'ikan ya ɗauke ni zuwa cikin daji. A can na ga wata mace zaune a kan wata jar dabba. Dabbar kuwa tana da sunaye na zagin Allah da aka rubuta a jikinta. Tana kuma da kawuna bakwai da ƙahoni goma. 4 Macen nan ta sa kaya masu launin jan garura, da kuma ja wur, ta ci ado da kayan zinariya, da na duwatsu masu daraja, da lu'ulu'ai. Tana riƙe da kwaf na zinariya cike da abubuwan ƙyama na lalatarta. 5 A goshinta kuwa an rubuta sunan da yake da ma'ana ta asiri, "Babila Mai Girma, mamar dukan karuwai, mamar abubuwan ban ƙyama na duniya kuma." 6 Na kuma ga macen ta bugu da jinin tsarkaka da kuma jinin waɗanda aka kashe saboda shaidarsu game da Yesu.

Da na gan ta, sai mamaki ya kama ni ƙwarai. 7 Amma mala'ikan ya tambaye ni ya ce, "Don me kake mamaki? Zan faɗa maka asirin ma'anar wannan mace, da kuma na wannan dabbar da take ɗaukarta, wannan dabba mai kawuna bakwai da ƙahoni goma. 8 Wannan dabbar da ka gani, ta taɓa rayuwa a dā, amma yanzu ba ta rayuwa, za ta haura daga rami mai zurfin nan zuwa inda za a halaka ta. Mutanen da suke zama a duniya, waɗanda tun kafin halitta ba a rubuta sunayensu cikin littafin masu rai ba, duka za su yi mamakin ganin dabbar, domin dā ta taɓa rayuwa, yanzu kuma ba ta rayuwa, amma za ta sāke dawowa.

9 "Wannan abu fa yana bukata hikima da ganewa. Kawuna bakwai ɗin nan kuwa tudu bakwai ne, waɗanda macen take zama a kai. 10 Kawuna bakwai ɗin nan kuma su ne sarakunan nan bakwai, waɗanda biyar daga cikinsu sun mutu, ɗaya yana nan,

---

16.19: Ish 51.17 **16.20:** R. Yoh 6.14 **16.21:** Fit 9.23; R. Yoh 11.19
17.1: Irm 51.13 **17.2:** Ish 23.17; Irm 51.7 **17.3:** R. Yoh 13.1 **17.4:** Irm 51.7
17.8: Dan 7.7; R. Yoh 11.7; Zab 69.29

ɗayan bai zo ba tukuna. Sa'ad da ya zo kuwa dole yă yi mulki na ɗan ƙanƙanin lokaci. 11 Dabbar da ta taɓa rayuwa a dā, yanzu kuwa ba ta rayuwa, ita ce ta takwas, kuma daga cikin bakwai ɗin ta fito, kuma tana tafiya zuwa inda za ta halaka.

12 "Kahoni goma da ka gani, su ne sarakunan nan goma da ba su riga sun karɓi ikon mulki ba tukuna, amma za a naɗa su su yi mulki na awa ɗaya tare da dabbar. 13 Waɗannan goma ɗin kuwa nufinsu ɗaya ne, kuma sun ba wa wannan dabba ikonsu da sarautarsu. 14 Za su yi yaƙi da Ɗan Ragon. Amma Ɗan Ragon tare da waɗanda ya kira, da zaɓaɓɓunsa, da waɗanda suke bïnsa cikin aminci, za su ci nasara a kan sarakunan nan domin shi ne Ubangiji na iyayengiji da kuma Sarkin sarakuna."

15 Sai mala'ikan ya ce mini, "Ruwan nan da ka gani, inda wannan karuwa take zama, jama'a ce iri-iri, da taro masu yawa, da al'ummai, da harsuna. 16 Kahoni goma da ka gani, su da dabbar za su ƙi ganin wannan karuwa, za su ƙwace kome da take da shi su kuma bar ta tsirara, za su cinye naman jikinta, su kuma ƙone ta da wuta. 17 Gama Allah ya nufe su su aikata nufinsa, su zama da ra'ayi ɗaya, su ba wa wannan dabba ikonsu don ta yi mulki har sai maganar Allah ta cika. 18 Macen nan kuwa da ka gani, ita ce babban birnin nan, wanda yake mulki a kan sarakunan duniya."

Fāɗuwar Birnin Babila

18 1 Bayan wannan, na ga wani mala'ika yana saukowa daga sama. Yana da iko mai girma, kuma ɗaukakarsa ta haskaka duniya duka. 2 Ya kira da murya mai ƙarfi ya ce, "Ta fāɗi, Babila mai girma ta fāɗi! Ta zama wurin zaman aljanu da iskoki da kowane irin ƙazamin tsuntsu, mai ban ƙyama. 3 Don dukan al'ummai sun sha[1] ruwan ïnabin lalatarta. Sarakunan duniya kuma sun yi lalata da ita. 'Yan kasuwan duniya suka yi arziki ta wurin muguwar sha'awarta."

4 Sai na ji wata murya daga sama tana cewa,
"Ku fito, mutanena daga gare ta!
Don kada zunubanta su shafe ku,
don kada bala'inta ya same ku.
5 Gama zunubanta sun yi tsayi har sun kai sama.
Allah kuma ya tuna da muguntarta.

17.12: Dan 7.24 **18.2**: Ish 13.21; 21.9; Irm 50.39; 51.8; R. Yoh 14.8
18.3: Ish 23.17; Irm 51.7 **18.4**: Ish 48.20; Irm 50.8; 51.6,45
18.5: Far 18.20-21; Irm 51.9

[1] **18.3 sun sha**: Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "ta sa dukan al'ummai suna sha" ne a nan.

6 Ku yi da ita daidai yadda ta yi da ku,
duk abubuwan da ta yi muku,
ku saka mata har sau biyu.
Cikin kwaf da ta dama muku ruwan inabinta da shi ku
kuma ku dama mata sau biyu
7 Ku gwada mata azaba da baƙin ciki gwargwadon
ɗaukaka da jin dadîn da ta yi wa kanta.
Gama ta kan ce wa kanta, 'Ni sarauniya ce,
a zaune nake a kursiyita!
Ni ba matar da mijinta ya mutu ba ce,
kuma ba zan taɓa yin baƙin ciki ba!'
8 Don haka, cikin kwana ɗaya
za a buge ta da bala'i na ciwo,
da na baƙin ciki, da na yunwa.
Za a kuma ƙone ta da wuta,
gama Ubangiji Allah, mai iko ne.
Shi ne kuwa mai hukunta ta."

9 Sarakunan duniya kuma da suka yi lalata, suka kuma yi muguwar sha'awa da ita. Za su yi kuka da kururuwa a kanta, sa'ad da suka ga hayaƙin wutan da yake cinta. 10 Za su tsaya da nisa domin suna jin tsoro kada su sha wahala tare da ita. Suna cewa, "Kaitonki! Kaitonki, ya ke babban birnin Babila! Ya ke babban birnin Babila! Cikin awa guda an hukunta ke!"

11 'Yan kasuwan duniya kuma suna mata kuka suna baƙin ciki, domin ba wanda yake saya kayansu kuma. 12 Ba wanda yake saya zinariyarsu, da azurfarsu, da duwatsunsu masu daraja, da kuma lu'ulu'ansu, da yadunan lilinsu masu kyau, da zane mai launin shuni, da siliki, da zane mai launin jan garura, da itatuwan ƙamshi iri-iri, da kayan hauren giwa iri-iri, da dukan abubuwan da aka sassaƙa da itace mai tsada, da kayan tagulla, da kayan ƙarfe, da kayan dutse mai sheƙi, 13 da kayansu na sinamon, da kayan yaji, da na turaren wuta, da mur, da lubban, da ruwan inabi, da mai, da garin alkama, da tsaban alkama, da shanu, da tumaki, da dawaki, da kekunan doki, da kuma bayi, wato, rayukan 'yan adam. 14 'Yan kasuwan suka ce mata, "Dukan abubuwa masu kyau da kika sa rai a kai sun ɓace, kuma dukan arzikinki da kayan adonki sun ɓace. Ba za ki ƙara samunsu kuma ba!" 15 'Yan kasuwa waɗanda suka yi arziki ta wurin kasuwanci da ita, za su tsaya da nisa, domin suna tsoro kada a haɗa su cikin azaba da za

18.6: Zab 137.8; Irm 50.29 **18.7-8**: Ish 47.7-9 **18.9-10**: Ez 26.16-17
18.11: Ez 27.31,36 **18.12-13**: Ez 27.12-13,22

ta sha. Suna kuka, suna baƙin ciki, 16 suna cewa, "Kaito! Kaiton babban birnin nan! Wanda dā yakan sa zanen lilin mai kyau, da riga mai launin jan garura da kuma riga mai launi ja wur, yakan kuma ci ado da kayan zinariya, da duwatsu masu daraja da kuma lu'ulu'ai! 17 Amma cikin awa guda dukan arzikinta ya halaka!"

Sai dukan masu manyan jiragen ruwa da masu shigansu, da masu tuƙin da kuma dukan sauran waɗanda suke samun biyan bukatarsu ta ciniki a teku, suka tsaya da nisa. 18 Suka yi kuka, sa'ad da suka ga hayaƙin wutan da ya cinye birnin, suna cewa, "Ba a taɓa yin wani birni irin wannan babban birnin ba!" 19 Sai suka zuba ƙura a kansu suna ta kuka, suna baƙin ciki, suna kururuwa, suna cewa, "Kaito! Kaiton babban birnin nan! Birnin da dukan masu manyan jiragen ruwa suka yi arziki daga dukiyarsa! Amma a cikin awa guda kome ya halaka!"

20 Ku yi farin ciki, ya ku da kuke zama a sama, ku yi farin ciki ku tsarkaka, da manzanni da annabawa, domin Allah ya riga ya hukunta Babila a kan abin da ta yi muku!

21 Sa'an nan wani ƙaton mala'ika mai ƙarfi ya ɗauki wani dutse wanda girmansa ya kai na babban dutsen niƙa, ya jefa cikin teku, yana cewa, "Haka za a jefar da Babila babban birni, da ƙarfi, ba za a kuwa ƙara ganinta ba. 22 Ba za a ƙara jin kidin molo, da mawaƙa, da masu busa, da masu huran ƙaho a cikinki ba. Ba kuwa za a ƙara ganin mai kowace irin sana'a a cikinki ba. Ba kuwa za a ƙara jin ana niƙa a cikinki ba! 23 Fitila ba za ta ƙara haskaka a cikinki ba. Ba kuwa za a ƙara jin muryar ango da amarya a cikinki ba, don dā 'yan kasuwanki su ne masu iko a dukan duniya, kin kuma ruɗe dukkan al'ummai da sihirinki!"

24 Haka aka hukunta Babila saboda jinin annabawa da na tsarkakan da aka sami a kanta, har ma da jinin sauran waɗanda aka kashe a duniya.

An Yabi Allah a Sama

19 1 Bayan wannan sai na ji wani abu kamar murya mai ƙarfi ta babban taro a sama, suna ihu suna cewa, "Halleluya! Ceto, da ɗaukaka, da iko, sun tabbata ga Allahnmu. 2 Gama hukuncinsa daidai ne, na adalci kuma. Ya hukunta wannan babbar karuwa wadda ta ɓata duniya da halin lalatarta. Allah ya hukunta

---

18.15: Ez 27.31,36 **18.17:** Ish 23.14; Ez 27.26-30 **18.18:** Ez 27.32
18.19: Ez 27.30-34 **18.20:** M. Sh 32.43; Irm 51.48 **18.21:** Irm 51.63-64; Ez 26.21
18.22: Ez 26.13; Ish 24.8 **18.22-23:** Irm 7.34; 25.10 **18.24:** Irm 51.49

ta domin ta kashe bayinsa." 3 Sai suka sāke yin ihu, suna cewa,
"Halleluya! Hayaƙin da yake fitowa daga wutan da ya cinye
babban birnin yana tashi har abada abadin." 4 Sai dattibai ashirin
da huɗun nan tare da halittun nan huɗu masu rai suka fāɗi, suka
yi wa Allah sujada, wannan da yake zama a kursiyin. Suna cewa,
"Amin! Halleluya!" 5 Sai aka ji wata murya daga kursiyin tana
cewa, "Ku yabi Allahnmu, ya ku bayinsa, Ku da kuke girmama
shi, babba da yaro."

Bikin Auren Ɗan Rago

6 Sa'an nan na ji murya kamar ta babban taro, kamar motsin
ruwa mai yawa da yake gudu, kamar tsawa mai ƙara. Na ji suna
cewa,

"Halleluya! Gama Ubangijinmu Allah Mai Iko duka shi ne
yake mulki! 7 Mu yi farin ciki, mu yi murna, mu ɗaukaka shi!
Gama lokaci ya yi na auren Ɗan Ragon. Amaryarsa kuma ta yi
shiri. 8 An ba ta yadin lili mai tsabtar da yake ɗaukar ido, ta sa."
Yadin lilin ɗin nan shi ne ayyuka masu kyau na tsarkaka.

9 Sai mala'ikan ya ce mini, "Rubuta wannan. Masu albarka
ne waɗanda aka gayyace su zuwa bikin auren Ɗan Ragon nan."
Ya kuma ce, "Wannan ita ce maganar Allah ta gaskiya." 10 Sai
na fāɗi a gabansa na yi masa sujada, amma ya ce mini, "Kada
ka yi haka! Ni ma abokin bautarku ne, kai da 'yan'uwanka,
waɗanda suke shaida gaskiyan da Yesu ya bayyana. Allah za ka
yi wa sujada!"

Domin gaskiyar da Yesu ya bayyana ita ce ta ba da ikon yin
annabci.

Wani a Kan Farin Doki

11 Sai na ga sama a buɗe, sai ga wani farin doki. Ana ce
da mai hawansa Mai Aminci da Mai Gaskiya. Cikin adalci ne
yake hukunci da kuma yaƙi. 12 Idanunsa sun yi kamar harshen
wuta, a kansa kuwa akwai rawani da yawa. Yana kuma da wani
suna a rubuce, sunan da babu wanda ya sani sai shi. 13 Rigar
da ya sa kuwa an jiƙa ta da jini. Sunansa kuwa "Kalman Allah."
14 Rundunar masu yaƙi na sama suka bi shi, sanye da fararen
yadin lili masu tsabta a kan fararen dawaki. 15 Daga bakinsa
wani takobi mai ci sosai ya fito. Da takobin nan ne zai ci nasara

19.2: M. Sh. 32.43; 2 Sar 9.7 **19.3:** Ish 34.10 **19.5:** Zab 115.13
19.6: Ez 1.24; Zab 93.1; 97.1; 99.1 **19.9:** Mat 22.2-3
19.11: Ez 1.1; Zab 96.13; Ish 11.4 **19.12:** Dan 10.6

a kan al'ummai. Zai kuma yi mulki a kansu da sandan ƙarfe,
zai kuma tattake 'ya'yan inabi cikin ramin matsar inabi na
tsananin fushin Allah Mai Iko duka. 16 A rigarsa, da kuma a
cinyarsa an rubuta wannan suna, "Sarkin sarakuna, da kuma
Ubangiji iyayengiji."

17 Sai na ga wani mala'ika yana tsaye a rana. Da murya mai
ƙarfi ya kira dukan tsuntsayen da suke firaya a tsakiyar sararin sama
ya ce, "Ku zo, ku taru wurin babban bikin nan na Allah. 18 Ku zo
ku cinye naman sarakunan nan, da na manyan sojoji, da na
jarumawa, da na dawaki, da na masu hawansu, da kuma naman
dukan mutane, bayi da masu 'yanci, babba da yaro!" 19 Sai na ga
wannan dabba da kuma sarakunan duniya da sojojinsu sun taru, don
su yi yaƙi da wannan da yake zama a kan dokin, shi da sojojinsa.
20 Sai aka kama dabbar tare da wannan annabin ƙarya wanda ya yi
abubuwan ban mamaki a dabbar. Ta wurin waɗannan abubuwan
ban mamakin ne ya ruɗe waɗanda suke da lambar wannan dabba,
da kuma waɗanda suka yi wa siffarta sujada. Aka kama wannan
dabba tare da annabin nan na ƙarya aka jefa su da rai cikin tafkin
wuta mai ƙuna da farin wuta. 21 Aka kashe sojojinsu da takobi da
ya fito daga bakin wannan da yake zama a kan dokin. Dukan
tsuntsaye kuwa suka ci namansu iyaka yadda za su iya ci.

Shekaru Dubu

20 1 Sa'an nan na ga wani mala'ika yana saukowa daga sama,
yana riƙe da mabuɗi na rami mai zurfin nan, da wata
babbar sarƙa a hannunsa. 2 Sai ya kama Macijin, wannan Maciji
na tun dā, wanda shi ne Mugun nan, ko kuma Shaiɗan, ya ɗaure
shi da sarƙa har na shekaru dubu. 3 Mala'ikan ya jefa shi cikin
wannan ramin mai zurfin nan, ya rufe ramin, ya kuma kulle shi
ya kuma buga hatimi, don kada yă ƙara rudin al'ummai kuma,
sai bayan shekaru dubun nan sun wuce. Bayan haka za a sake shi
na ɗan lokaci.

4 Sa'an nan na ga kursiyai, da waɗanda aka ba su ikon hukunci
suna zama a kai. Na kuma ga rayukan waɗanda aka yanka musu
kawuna saboda sun shaidi Yesu, da kuma maganar Allah. Su ne ba
su yi wa wannan dabbar sujada ba, ko su yi wa siffarta. Ba su kuwa
karɓi wannan lambar dabba a goshinsu ko a hannunsu ba. Sun sāke
rayuwa, suka yi mulki tare da Almasihu har shekaru dubu. 5 Sauran
waɗanda suka mutu ba su sāke rayuwa ba, sai bayan shekaru dubun

---

19.15: Zab 2.9; Ish 63.3; Jow 4.13; R. Yoh 14.20 **19.17-18**: Ez 39.17-20
19.20: R. Yoh 13.1-18 **20.2**: Far 3.1 **20.4**: Dan 7.9,22

nan suka wuce. Wannan fa shi ne farkon tashin matattu. 6 Masu albarka ne wadanda suke da rabo cikin wannan farkon tashin matattu don su tsarkaka ne. Mutuwa ta biyu ba ta da iko a kansu, za su zama firistocin Allah da na Almasihu, za su kuma yi mulki tare da shi har shekaru dubu.

Nasara a kan Shaidan

7 Bayan shekara dubun nan sun wuce, za a saki Shaidan daga inda aka kulle shi, 8 zai kuma fito yă rudi al'umman da suke a warwatse cikin dukan duniya, wato, Gog da Magog. Shaidan zai tattara su don yaki, yawansu kuwa ya yi kamar yashi a bakin teku. 9 Suka bazu a duniya, suka kewaye birnin da Allah yake kauna, wato, sansanin tsarkakansa. Amma wuta ta sauko daga sama ta kone su. 10 Mugun nan kuwa da ya rude su, aka jefa shi cikin tafkin wuta mai kuna da farin wuta, inda aka jefar da wannan dabba tare da annabin nan na karya. A can za su sha wuya dare da rana, har abada abadin.

Hukunci na Karshe

11 Sa'an nan na ga wani babban farin kursiyi, da wanda yake zama a kai. Sai sama da kasa suka gudu daga gabansa, ba a kuwa kara ganinsu ba. 12 Sai na ga matattu, babba da karami, suna tsaye a gaban kursiyin. Aka bude littattafai, sa'an nan aka bude wani littafi, wato, littafi na masu rai. Aka hukunta matattun bisa ga abin da suka yi, kamar yadda yake a rubuce a cikin littattafan. 13 Sai teku ya fid da wadanda suka mutu a cikinsa. Mutuwa da wurin zaman matattu, su ma suka ba da matattunsu. Sai aka hukunta kowa bisa ga abin da ya aikata.

14 Sa'an nan aka jefa Mutuwa tare da wurin zaman matattu a cikin tafkin wuta. Wannan tafkin wutan, shi ne mutuwa ta biyu. 15 Duk wanda sunansa bai fito a rubuce a cikin littafin nan na masu rai ba, an jefar da shi cikin tafkin wutan nan.

Sabon Sama da Sabuwar Kasa

21 1 Sa'an nan na ga sabon sama da sabuwar kasa. Sama na farko da kasa ta farko duk sun gudu, babu kuma teku. 2 Na kuma ga Birnin nan Mai Tsarki, wato, sabuwar Urushalima, tana saukowa daga sama daga wurin Allah. An shirya ta kamar amaryar da ta ci ado saboda mijinta. 3 Na kuma ji murya mai

---

20.8: Ez 7.2; 38.2,9,15 **20.11-12:** Dan 7.9-10 **21.1:** Ish 65.17; 66.22; 2 Bit 3.13
21.2: Ish 52.1; 61.10; R. Yoh 3.12

ƙarfi tana magana daga kursiyin tana cewa, "Ga shi wurin zaman
Allah yana tare da mutane! Zai zauna tare da su, za su kuma
zama jama'arsa. Allah kuwa da kansa zai kasance da su, yă kuma
zama Allahnsu.[m] 4 Zai share musu dukan hawaye daga idanunsu.
Babu sauran mutuwa, ko baƙin ciki, ko kuka, ko azaba. Don
abubuwan dā sun wuce."

5 Sai wannan da yake zama a kursiyin ya ce, "Yanzu zan
yi dukan kome sabo!" Ya kuma ce mini, "Rubuta wannan,
domin wannan maganar gaskiya ce, kuma tabbatacciya." 6 Ya
kuma ce, "An gama! Ni ne farko da kuma ƙarshe, mafari da
kuma matuƙa. Ga duk mai jin ƙishin ruwa, zan ba shi izni yă
sha daga maɓuɓɓugan ruwan rai kyauta. 7 Duk wanda ya ci
nasara zai karɓi gādo daga wurina, zan zama Allahnsa, shi kuma
zai zama ɗana. 8 Amma masu tsoro, da masu cin amana, da
masu aikin ƙyama, da masu kisankai, da masu halin lalata, da
masu sihiri, da masu bautar gumaka, da kuma dukan masu yin
ƙarya, duk rabonsu yana cikin wannan tafkin wuta mai ƙuna da
farin wuta, wanda yake shi ne mutuwa ta biyu."

Sabuwar Urushalima

9 Sai ɗaya daga cikin mala'iku bakwai ɗin nan masu
kwanonin da aka cika da bala'i bakwai ɗin nan na ƙarshe ya
zo wurina ya ce, "Zo, in nuna maka amarya, matar Ɗan Ragon."
10 Sai Ruhu ya sauko a kaina, mala'ikan ya ɗauke ni zuwa kan
wani tsauni mai tsawo sosai, ya nuna mini Urushalima, Birnin
Mai Tsarki tana saukowa daga sama daga wurin Allah. 11 Birnin
kuwa yana haske da ɗaukakar Allah, haskensa ya yi kamar dutse
mai daraja, kamar jasfa, yana ƙyalli kamar madubi. 12 Yana da
babban katanga mai tsawo, da ƙofofi goma sha biyu, da
mala'iku goma sha biyu masu lura da ƙofofin. An rubuta
sunayen kabilu goma sha biyu na mutanen Isra'ila a kan
ƙofofin. 13 A kowane gefe kuwa akwai ƙofofi uku, uku a gabas,
uku a kudu, uku a arewa, uku kuma a yamma. 14 Aka kuma
gina tushen birnin a kan duwatsu goma sha biyu, inda aka
rubuta sunayen almajirai goma sha biyu na Ɗan Ragon.
15 Mala'ikan da ya yi mini magana kuwa yana da sandan awon
da aka yi da zinariya wanda zai auna birnin, da ƙofofinsa, da

21.3: Ez 37.27; L. Fir 26.11-12 **21.4:** Ish 25.8; 35.10; 65.19 **21.6:** Ish 55.1
21.7: 2 Sam 7.14; Zab 89.27-28 **21.10:** Ez 40.2 **21.12-13:** Ez 48.30-35

[m] **21.3 yă kuma zama Allahnsu:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da wannan.

kuma katangarsa. 16 Birnin nan kuwa kowane gefensa daidai
ne da sauran. Tsawonsa da fãdinsa kuma daidai suke. Sai
mala'ikan ya auna birnin da sandansa na awo, ya sami kilomita
dubu biyu da ɗari huɗu, tsawonsa, da fãdinsa, da tsayinsa duka
daidai suke. 17 Mala'ikan ya kuma auna katangar, ya sami
tsayinta[n] ta kai mita sittin da shida, bisa ga cikakke abin awo
wanda mutane suke amfani da shi. 18 An gina katangan nan da
wani dutse mai daraja da ake ce da shi jasfa, aka kuma gina
birnin da zinariya zalla, yana kuma ƙyalli kamar madubi. 19 An
kuma yi wa tushen katangar birnin ado da kowane irin dutse
mai daraja. Jasfa ne dutse na farko a tushen ginin, na biyu
saffaya, na uku agat, na huɗu zumurrudu, 20 na biyar onis, na
shida karneliyan, na bakwai kirisolat, na takwas beril, na tara
tofas, na goma kirisofuras, na sha ɗaya jasin, na sha biyu
ametis. 21 Ƙofofi sha biyun nan kuwa lu'ulu'ai sha biyu ne, an
yi kowace ƙofa da lu'ulu'u guda ɗaya. An yi titin birnin da
zinariya zalla, yana kuma ƙyalli kamar madubi.

22 Ban ga haikali a birnin nan ba, domin Ubangiji Allah Mai
Iko duka da Ɗan Ragon su ne haikalin birnin. 23 Birnin ba ya
bukatar rana, ko wata su haskaka shi, domin ɗaukakar Allah ita
ce take haskaka shi, Ɗan ragon kuma shi ne fitilar birnin.
24 Mutanen duniya za su yi tafiya a cikin hasken birnin,
sarakunan duniya kuma za su kawo wa birnin dukiyarsu. 25 Ba
za a kulle ƙofofin birnin da rana ba har abada ba kuwa za a yi
dare a can ba. 26 Za a kuma kawo abubuwan masu kyau da kuma
dukan arzikin mutanen duniya cikin birnin. 27 Amma abu marar
tsarki ba zai taɓa shiga cikin birnin nan ba, ko kuma wani mai
yin abin ƙyama, ko mai ƙarya. Sai dai waɗanda sunayensu suna
a rubuce cikin littafi na masu rai na Ɗan Ragon, su ne za su
shiga birnin.

22 1 Sa'an nan mala'ikan ya nuna mini kogin ruwan rai, mai
ƙyalli kamar madubi, yana gudu daga kursiyi na Allah da
Ɗan Ragon, 2 yana gudu ta tsakiyar titin birnin kuma. A kowane
gefen kogin kuwa akwai itacen[o] rai mai haihuwar 'ya'ya sau
goma sha biyu a shekara, yana haihuwa sau ɗaya kowane wata.
Ganyen itacen kuwa domin warkar da dukan al'ummai ne. 3 Ba
za a sami wani abu da Allah ya la'anta a birnin nan ba. Kursiyi

---

21.15: Ez 40.3 **21.18-21:** Ish 54.11-12 **21.23:** Ish 60.19-20 **21.24:** Ish 60.3
21.25-26: Ish 60.11 **22.1** Ez 47.1; Zak 14.8 **22.2:** Far 2.9; Ez 47.12

[n] **21.17 tsayinta:** Wani juyi na wannan kalmar shi ne "kaurinsa."

[o] **22.2 itacen:** Da Helenanci kalman nan na iya zama "Itatuwa."

na Allah da Dan Ragon zai kasance a cikin birnin. Bayinsa kuma za su yi masa sujada. 4 Za su ga fuskarsa, za su kasance da sunansa a rubuce a goshinsu. 5 Babu sauran dare, ba kuwa za su bukaci fitilu ko hasken rana ba, domin Ubangiji Allah ne zai zama haskensu. Za su kuwa yi mulki har abada abadin.

Yesu Yana Zuwa

6 Sai mala'ikan ya ce mini, "Wannan magana gaskiya ce, tabbatacciya ce kuma. Ubangiji Allah, wanda ya ba wa annabawa Ruhunsa, ya aiko da mala'ikansa yă nuna wa bayinsa abin da zai faru ba da daɗewa ba."

7 "Ga shi kuwa, ina zuwa da wuri! Masu albarka ne waɗanda suke biyayya da maganar annabcin littafin nan."

8 Ni, Yohanna, na ji, na kuma ga waɗannan abubuwan. Da na gama jinsu da kuma ganinsu, sai na fāɗi a gaban mala'ikan da ya nuna mini waɗannan abubuwan, domin in yi masa sujada. 9 Amma ya ce mini, "Kada ka yi haka! Ni abokin bautarku ne, kai da 'yan'uwanka annabawa, da kuma dukan waɗanda suke biyayya da maganar littafin nan. Ka yi wa Allah sujada!" 10 Ya kuma ce mini, "Kada ka ɓoye maganar annabcin nan, domin lokaci ya yi kusa da dukan waɗannan abubuwan za su faru. 11 Duk mai yin mugunta yă ci gaba da yin mugunta, kuma duk mai yin abin ƙyama, yă ci gaba da yin abin ƙyama. Duk mai yin abu mai kyau, yă ci gaba da yin abu mai kyau, duk kuwa mai tsarki yă ci gaba da zamansa na tsarki."

12 "Ga shi, ina zuwa da wuri! Zan zo tare da ladana, in ba kowa bisa ga abin da ya yi. 13 Ni ne farko da kuma ƙarshe, mafari da kuma matuƙa."

14 Masu albarka ne waɗanda suka wanke rigunansu, domin su sami iznin ci daga itacen rai, su kuma shiga birnin ta ƙofa. 15 Amma waɗanda suke waje kuwa su ne masu ƙazantar da kansu, da masu yin sihiri, da masu halayen lalata, da masu kisankai, da masu bautar gumaka, da kuma masu ƙarya cikin maganarsu da ayyukansu duka.

16 "Ni, Yesu, na aiko da mala'ikana don yă sanar muku waɗannan abubuwan cikin jama'un masu bi. Ni ne tushen Dawuda, zuriyarsa kuma. Ni ne tauraron safe, mai haske."

17 Ruhu da Amarya suna cewa,

22.3: Zak 14.11 **22.5:** Ish 60.19; Dan 7.18 **22.11:** Dan 12.10
22.12: Ish 40.10; 62.11; Zab 28.4; Irm 17.10
22.13: R. Yoh 1.8,17; 2.8; Ish 44.6; 48.12 **22.14:** Far 2.9; 3.22 **22.16:** Ish 11.1,10

"Zo!"
Duk kuwa wanda ya ji wannan, shi ma yă ce,
"Zo!"
Duk mai jin ƙishin ruwa yă zo, duk mai bukata yă karɓi
ruwan rai kyauta.

Maganar Karshe

18 Ni, Yohanna, ina jan kunnen duk mai jin maganar annabcin
littafin nan cewa, in wani ya yi ƙari a kanta, Allah zai ƙara masa
bala'in da aka rubuta a littafin nan. 19 In kuma ya yi wani ragi a
maganar annabcin littafin nan, Allah zai karɓa rabonsa na 'ya'yan
itacen rai, da na birni mai tsarki kamar yadda aka bayyana a cikin
wannan littafin.

20 Shi da ya shaida waɗannan abubuwan duka ya ce, "Hakika,
ina zuwa da wuri!"

Amin. Zo, Ubangiji Yesu!

21 Bari alherin Ubangiji Yesu yă kasance tare da ku duka.[r]
Amin![s]

22.17: Ish 55.1 **22.18-19**: M. Sh 4.2; 12.32

[r] **22.21 ku duka:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da "tsarkaka duka" ne a nan.

[s] **22.21 Amin:** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da wannan.